DA SO KAMANE

Cikin rayuwa da akwae abubuwa daban daban ita rayuwa ana tsarata bisa ga yarda Allah ya rubutawa bawansa saidai kashh!! A cikin irin wannan rayuwa mai ciki da darasi daban daban abubuwa na faruwa wasu na shudewa duk yarda Allah ya tsarawa bawanshi toh hakan ke faruwa dashi to amma abun dubawa ana shine wani irin abu muke aikatawa shi haramci abun ne wanda Mahalicinmu ya Hana miyasa muke kokarin jawoshi jikin ? Miye laifin mai fada maka gaskiya miye mai baka shawara Akan daidai? Miye laifin wanda ke sonka tsakani ga Allah?

Duk A cikin rayuwar nan babu abunda ke tabbas, Allah shine masanin daidai.

DA SO KAMA LITTAFINE WANDA WATA BAIWAR ALLAH TA RUBUTA SHI DOMIN ALLAH DOMIN FADAKARWA NISHADANTARWA

Ban fara rubutun littafin nan ba sai dana tabbatar inada interest akai littafi wanda marbuciyarshi da kanta bata san iyakar inda labarin zai tsaya bah labari wanda gama su fahimta da son kara sanin makama da darasin rayuwa Sam bazasu gajiya dashi bah saidai Allah yasani banyi alkawarin typing kullum bah

Kubiyo ni domin ji abunda ke kunshi A labarin

Bismillahir rahamanur rahim

ADAMAWA YOLA

Kamar yarda kowa yasan adamawa ta kasance babbar jaha a Nigeria inda mutane masu banbancin yare kabilu da addinai suke rayuwa tamkar abu guda a jahar haka zalika mutane masu kudi da akasin haka ke rayuwa. G.R.A

Anguwa ci da ta hada mutane yan siyasa da kuma yan kasuwa inda mafi yawa daga ciki masu hannu da shuni sun fi rayuwa a anguwa kasancewar lokaci ne na sanya ko ina shuru yake babu kara ko sautin komai face precious air dake kadawa a ko wani road na anguwr wani babban mansion house ne wanda tsayawa fadin tsaruwar gidan kan iya zama wani babban aiki gareni but iyakar kudi an kashe zabarsu wajen kira ginin gidan tamkar ba a mutuwa mutunan dake tsaye sanyi da white iron uniform yayi hanzarin wangale babban mint green din gadin yah illahi warabul ka’abah zanyi yarda da cewa alummar dake cikin wannan gida basu taba sanin cewa da akawai wani bil adam dake kwana bai da kwayar hatsi ta sama cikin shi bah domin kuwa ko nayi rantsuwa babu batun kaffara cewa ginin gida zayi irin ginin White House na kasar UNITED STATE (America USA) hankali nake bin jerin motocin dake pake a parking lot din gidan sunyi 30 kowace aka baka zata isheka karasa rayuwar duniya da yarda Allah (gamu talakawa kenan)

Babban parlor ne wanda ke cike da abun duniya wanda za,a iya kira da aljannar duniya wata mashiyar mace ce zaune cikin daya daga cikin cushions din parlor kallo daya nayi take bakina ya furta kamalar tsarki ya kara tabbata ga Allah daya halice wannan halitar sanyi take cikin wata dakakiyar sequences atampha ash and maroon dinki kaftan sosai dinki ya karbi jikinta kasancewarta fara irin farin nan mai haske mai daukar ido wanda hutune kawai ke magana wurin duk dacewa shekarun ta zasuyi

talatin da tara zuwa arba’in hakan bai hana zalar kyau da haibatar bayana bah yarda take sarafa waya zaka iya cewa her life depends on it wani irin sirin kamshi ke fita daga jikinta wanda ya haade da kamshin turaran wutar dake fita daga cikin burner hade da dumin da room heater tasa parlor ya dauka sosai ta shagala da kallon pictures din Kayan da tayi order daga Cyprus wanda aka turo ma ta su turo mail dinta tana kallo rising head dinta tayi so masha Allah manya white eyes dinta sun sha kajal a hankali take motsa bakinta tana karanto addua kafin ta mike tsaya nabi bayanta da kallo yarda take tafiya kace jinin saurata ce tsayawa tayi daidai kofar wani daki dake tsakiyar jerin dakunan har ta kai white fingers dinta kan handle din sai kuma tafasa ta nufi hanyar dakin ta toilet tashiga tayi tafito jikinta da lema alamar sallarh zatayi carpet ta shimfida ta kabara sallarh cikin natsuwa takeyi har ta kammala zuhur prayer tayi azkar ringing din da wayar tayi yasa ta maida hankali kan wayar lumshe ido tayi tareda murmushi wanda har saida beauty points dinta ya luma cikin sanyi murya tareda natsar da kanta ta dauka daga can ajiyar zuciya aka sauke wannan na daya daga cikin halayan da yasa yake son zarah saboda duk fadan ta indae kanshi ne maida kanta take wata irin kamila salaha amincin Allah ya tabbata a gareki tare dakai ta amsa tana mai fitar da sautin murmushinta Ina daughter na kira wayarta switch off while so nake na fada mata munyi waya da dr Sam yace resumption din su next week ajiyar zuciya ta sauke tare da kira sunanshi ABBAN BABY daga bangaran shima cewa yayi OUMMUN BABY cigaba da magana tayi abban baby ina bukatar ka dawo cikin gagawa please domin kullum AYDAH abunta gaba yakeyi please do it for my sake ta fada tare mayar da muryar ta zuwa harshen da tafi kwarewa wato Arab cus she is Arab woman while ABBAN ayda bafulatani ne na asali tafiye tafiyen kasuwancin shi ya hada shi da ita a kasar sudan kullum ayda kara salon take wurin tozarta rayuwar na kasa da ita wanda kasani nasani cewa ubangijin sammai da kassai ya karrama bil ADAM amma Sam ayda bata gani ko fahimtar haka lokaci yayi da ya kamata ta shiga hankalinta cikin fushi da gajiyar dayayi na complain din oummun aydah kanta yace enough zarah just be quite wae miyasa kike neman takurawa rayuwar baby she is still young habah har ynx bata san what’s wrong or what’s right bah habah cikin zallar mamaki oummun aydah ta waro ido tace man anya kasan abunda bakin ka ke furtawa aydah you just called her a kid kokuwa my eyes had that? Man kasan age din aydah ynx aydah is 22 pah and you are calling her a teen yarinya da ta isa aure ta isa daukar ciki har ka ke kiranta da young murmushi tayi mai ciwo tace it wouldn’t hurts me anymore cus duk abunda aydah tayi gaada tayi man aydah duk wasu halaya naka ta dauko cikin tsawa yace zarahhhhhhh ya isa haka let it be billahi don’t treat my

gurl wrong if not kit ya kashe wayar ba karamin tashi hankalin hajiya zarah yayi bah yau Alhaji habib ne ke fada mata irin wannan hurts words din kan yarsu yar cikinsu yar dasu ka haifa with loads of love with much caring tsakanin su inalilahi wa'ina illahil raj'iun da wani yafada mata akwai ranar da habib zai daga mata murya har haka bazata taba yarda bah amma gashi yau da kunnan ta taji yarda yake mata mgn saboda soyayyar yarinya shi ganin tunani bazai haifar mata da komai bah kuma ko rantsuwa tayi bazata yi kaffara bah aydah batayi sallarh bah tashi tayi ta nufi hanyar dakin aydah anan ta hadu maids nata jiran fitowar ta cus sun gama lunch kuma su fada mata still aydah bata fito bah dakatar dasu tayi tare da basu umarnin an gama komai zasu iya komawa part dinsu su huta godiya sukayi mata tareda juyawa suka fita direct dakin ayda tashiga.

Babban bedroom ne mai dauke da closet da toilet aciki mai na bedroom din sky blue ne da baby pink bakaramin kyau dakin yayi bah komai na daki killace yake a wurin daya dace dashi ga kamshin wasu mayun oud na tashi a dakin babu abunda ke tashi dakin sai sounds din girgiza anklet da mamalakiyar dakin keyi zaune ta a kan sofa ta tayi crossing white legs dinta masu matukar kyau da daukar ido sanye right leg dinta take da wasu hadadun gold chain anklets masu stone mai masifar haske sai shining yake duba na nakai zuwa fuskarta OMG this lady fine finish Allahuma this innocent gurl ake faman magana kan halinta she is that much beauty tafi kyawu kyau sanyi take da red long sleeve shirt da milk palazzo dasauri ta mike ganin yarda oum ke jifarta dawani kallo she is well shaped lady yah illahi mace wadda ko a cikin thousandths of ladies babu irinta sosai ta tsorata da ganin Oum haka cikin nuna umarni oum tace aydah ki tashi kiyi sallarh kuma ina jiranki down stairs hope u get gyada kai ayda tayi har Oum ta juya tace words aydah nasha fada maki kar ina maki magana kina man body language jikin ki zai gaya maki dasauri tace toh tana turo baki tayi hanyar toilet zame hular kanta tayi nan take long black silk hair dinta ya bayana tsawon shi har gadon baya shafa shafa tayi ta fito cikin three minutes ta gama sallarh zuhur (fake fake kenan lol) ko hijab din bata cire bah ta nufi hanyar dining

Duniya na dauke abun so da abun ki lokacin da wasu ke cikin daula wasu kuwa kwana suke basu ci bah tunda kofar dan maidaidaicin gidan zaka gane cewa masu wannan gidan masu karamin karfe ne sautin wata irin zakakar muyar wanda sautin ta yayi amsa kuwa ya karade duk harabar karamin gidan dake shafe da cement amon muryar na bin iskan da ke kadawa hakan ya taimaka wurin saurin isar da sakon sautin karatun littafi mai girma da mamalakin muryar ke rerawa sosai yake ba kowani harafi hakkin shi cikin

dakuna uku da ke jera a cikin gidan muryar nan ke fito daga dakin dake karshe wanda duk yafi saura dakuna karanta share yake tass madaidaiciyar katifar na a gyare komai na dakin ya shirye yake kamar ba dakin matashi bah zaune yake saman prayer mat abun mamaki duk karatun nan da akeyi daka akeyin shi sosai na zuba saurayin ido farine tass saje ya zagaye kyakyawar fuskarshi yana cikin irin karfafan mazan nan masu kwar jini game da cikar kamala shekarun shi baza su fi 32 bah yayi nisa a cikin karatun shi duk yarda yake jiyu muryar ummin shi na fama yi ma kannanshi fada saboda makarar da sukayi na tafiya makaranta yasan cewa mudun yafita Allah.

May Allah bless all the ladies

My love for women's is endless ♥

Yafita abun bazaiyi kyau bah domin Allah ya halice shi wani irin murdadan mutun miskilli ne na bugawa a jarida baya raina kowa cus bai son raini talakka ne amma mai wadatar zuciya wani sa'ilin har Abbyn su kan kira shi da mai girman kai tawani bangaran mutun ne shi mai matukar mutunci da son mutane ko da yaushe Faran faran yake most especially idan yana tare da abokananshi yauma kamar kullum bayan ya karasa karatunshi mikewa yayi tareda shirya kanshi cikin wani yadi mai saukin kudi kasancewar tsabta ta zauna jikinshi sosai yadin ya karbi shi sai kamshin oil perfume (real xx ta'iba) bude wata karamar ghana yayi tareda fito da envelope yayi mai dauke da cv shi fita yayi ya tarar da ummi da abby zaune suna magana ganin shi yasa sukayi shiru domin magana ce da tashafi su asirinsu ne baza su so suyi involved yara ciki bah sallama yayi masu ya wuce fatan nasara sukayi mashi ya fice kasancewar gidan ya rage daga ummi sai abby yasa Abby cewa Asiya ba nayi wannan maganar bane da niyyar cewa na yanke wata alaqa dake tsakanina da dan uwana habib bah aaa Sam kawae dai ban san ta inda zan cigaba da rayuwa da mutunan da dan yayi kudi zaiyi watsi dani da mahaifinmu bah mahaifinmu shi kadae ya rage manah amma habib haka ya tsallake shi ya tafi cikin halin ciwo hawayene ke gangarowa daga idon abby girgiza kai yayi tareda da tashi ya shiga daki domin bazai iya cigaba da wannan maganar bah saboda wani irin tsanar habib da halin shi ke nasarar sukar har kasan zuciyar shi.

Bayan fitar ABDULMALIK yayi yawo ma 'aikatu daban daban amma babu inada aka dace ko ina zai je basu daukar mai matakin karatu irin nashi (degree) sosai ya sha bakar wahala a haka yadawo gida kasa domin duk ya karar da kudin shi wajen hau acaba haka yadawo gida kasa shiga ma yayi

yazauna nan bakin dakalin gidan ya mayarda ajiyar zuciya yah Malik sunan shi da aka ambata yasa shi da’go kai ya kai duban shi zuwa fararan yan matan masu kama da shi sosai murmushi yayi masu tare da cewa welcome sister’s aysha tace big broose ya baka shiga gida ba ware manyan idon shi ya tare da tabe fuska yace ummi bata nan kuma baku nan gidan was so bored yarda yayi ba karamin dariya ya basu bah halimai tace oyyah lets enter now little boyyyyyyyyy yarda taja sunan ya sa su sakin dariya sosai suka shiga cikin gidan batareda bata lokaci bah suka zage da aikin gida aysha itace babba sai halimai maryam the lastborn sai shine first born sosai suke son junan su wanda ko ina tare suke zuwa suna da illimi but boko da Islamic uwa uba tarbbiya ko aikin gida zasuyi tareda Malik suke yin shi danwake da salat aysha ta masu cikin tray babba ta zuba suka zagaye duka su hudun suna ci so peaceful cikin haka ne ummi ta dawo har rige rigen mata welcome suke murmushi tayi tare da amsa masu itama abincin ta zuba ta zauna side dinsu suna ci suna fira

My love for women’s is endless ♥

AYDAH

Bayan ta sauko dining din lokacin har Oum tafara cin abincin ya mutsa fuska tayi tareda turo baki tana ma abincin wani irin kallo Oum na kallon ta but bata ce mata kanzil bah daukar warms din abincin tayi ta nufe hanyar waje Oum na kallo tayi mata banza fita tayi tana tak’o tamkar bata son taka kasa sai da ta fito cikin haske naga wannan baiwar kyauwun na ta ya kara bayana har tsoro zata baga kayi tunanin ba mutun baci kasancewar sanyi ne abayar bin jikinta sai karewa take da hannu daya domin a duniya tana mugun Jin kunyar wani yaga surarta ko da Oum ce (akwae da yawa mata da basu san akwae rayuwar aure bah most especially yaran dake sangartawa da kudi da gata uwa uba a Hana su karatun addini ana tura su kasashe domin western education toh Aydah na daya daga ciki) sosai ta daure fuska ganin ta karaso part din maids din cikin daga yar karamar baby voice dinta tace who cooks this? Ba karamin firgici sukayi bah kowa na zullum mata magana Gudun kar kayi laifi cikin dan daga murya tace don’t let me repeat myself da sauri wata mata wace zatayi sa’ar Oum tace nice ASEEYARH (her real name is ASEEYARH) wani irin dauke ta da mari ayda tayi takara mata ta Dayan side din tareda bude warms din jallof spaghetti ta kefa mata a fuska wani irin zabura sukayi kowa shock ya kamashi duk da cewa ba yau ba ne na farko da aydah ta fara irin haka amma bata taba makamancin hakan bah dasauri rufaida da ta kasance aminiyar Oum wadda Oum ta dauke ta kamar kanwa wace suke uwa daya uba daya kasar su daya tun da

tayi aure mahaifin Oum ya hadu su tare domin su basu baka ya sai da mai mata hidima tun suna yara suka saba da Oum cikin yar tsawa tsawa ta ce aydah kina da hankali kuwa aydah da Sam ta zage wurin abunda take yasa rufaida yin saurin nufar part dinsu (ita ba a part din maids take tanadae shiga su gaisa) dasauri ta ware murya tana kiran Oum oummun aydah dasauri Oum ta tashi tace habah ruffyy is this fair da kinsa nafadi pah girgiza kai rufaida tayi tace Aseeyarh zatayi kisan kai lets go kawae zaki ga komai wani irin jiri ke kwasar Oum Allah ne kawae ya kai su part din maids lafiya daidai nan aydah ta kara daga soft smooth hand din ta zata zagba gawa ladi su Oum ta rike idon Oum tamkar zaiyi aman wuta ta dafe saitin zuciyar ta tana wani irin kallon aydah

Cyprus

Zaune yake cikin suit wani babban dakin taro yana sauraron bayanin da wani bature ke masu dangane da kasuwanci su duk sun maida hankali wurin sauraron abunda yake fada Alhaji habib kowa sosai yake jin dadin yarda kayansu ke samon karbowa a lungu da sakon countries kallo daya zaka yi mashi kaga tsananin kamar shi da malik

(To pah Malik ko aydah)

My love for women’s is endless ♥

Yah Allah bless guide protect each and every woman in this world ❤

Kamar su da malik har yabace sosai yake fahimtar abunda suke gudanarwa duk bayan yan seconds sai ya duba wayarshi ko yaga missed call ko sms na oummun aydah amma shiru kasa hakura yayi har saida ya nemi uzuri ya fita ahankali yake sauko wa daga stairs din har ya karaso wani babban Parking lot da motoci ke a fake ajiyar zuciya ya sauke tareda nemo number ta da akayi saving da heart desire ringing take har ta tsinke ba a daga ba sake kwatanta kiran yayi Still no answer lumshe ido yayi tareda shafa kwantaciyar sajen shi a ranshi yana adduar Allah yasa ba fushi zaran shi tayi bah komawa yayi suka daura daga inda aka tsaya

AYDAH

Kallon ta oum keyi cikin tuhuma sosai tasha jini jikinta duk da bata nuna a fuska ba ta daure saboda maids din dake tsaye suna kallon sarautar Allah rufaida tace aydah abunda kikayi kinyi daidai nace kinyi daidai? Habah aydah when where yaushe zaki daina sa mahaifiyarki cikin damuwa yaushe zaki daina halin da alummar duniya zasu dinga zagin parents dinki habah

ASEEYARH abunda kikeyi aldaci ne ko daidai ? Aseeyarh miyasa a kullum baki kokarin ganin kin gyara halinki miyasa a kullum kike son ganin mahaifiyar ki cikin wani hali Aydah idan babanki na da kudi kinada tabbacin cewa zaki kasance cikin arziki har Abadan? Kina da tabbacin cewa zakiyi aure cikin daula? Ki Sani pah ke mace ce aure babu idan bazai kaiki bah aydah bamu san abunda Allah ya tanadar maki bah nan gaba ya kamata ki san ciwon kanki hakan nan aydah shirune ya biyo bayan kaf maganganun da rufaida tayi babu abunda Oum keyi sai ajiyar zuciya saboda sosai hankalinta ke tashi da irin wannan muguwar dabi’a ta aydah Oum nada wani hali duk irin laifin da aydah zata aikata bazata taban yi mata fada bah ko kadan rufaida ce kawae ke iya fito fili tayi wa aydar fada cikin bacin rai aydah tace enough anty rufaida ya isa haka wani irin kallon mamaki gaba daya maids din da rufaida kewa aydah harda Oum kanta duk brain din ya kulle babu abunda zuciyar ta keyi face bugawa da matsanancin karfe da hasaso mata irin hukunci daya dace ta dauka kan tarbiyyar yarta kwaya daya tal domin gudun abunda zai iya faruwa gaba ya kamata aydah ta san miye rayuwa ya kamata ta fuskanci abubuwa biyu dake a duniya wato arziki da talauci amma taya? Yaushe? Ta wace hanya lumshe idonta tayi gam dasuka tara kwalla ta bude su ta zuba su akan mafi soyuwa halita a wurin ta abu mafi kyau da kwarjini a idonta abunda zata iya sayar da rayuwarta wurin ganin rayuwar yarta ta gyaru sosai rufaida ta tausaya mata saboda tasan irin wahala da kuncin data ke ciki aydah kuwa fau tayi kamar zata tashi sama ta nufe hanyar part dinta tana shiga tayi wurge da hijab din direct bedroom dinta ta wuce zuciyar ta na wani irin zafi kwantaciyyar sumar kanta dake nan har gaban kai tayi luf baka sidiq wani watsi ta fara da kayan kan dress mirror kwallaban perfumes sai bada sautin kass kass kass suke kuka take sosai white eyes dinta sunyi reddish hanci ta yi jazur har sai tayi nasarar fasa duk wani abunda ke kan mirror din wanda suka kasance masu matukar kyau da tsada dafe kanta dake masifar sarawa tayi idan akwae abunda ta tsana ya biyo bayan yi mata fada shiyasa a duniya kullum take ganin oum da anty rufaida basa sonta abba kawae ke sonta cikin zallar kuruciya da ta daurawa kanta da sangarta tace wllh swears I most informed abba last time sunyi sun gama ban fada mashi bah Allah this time basuyi wa banza bah ahaka ta cigaba da kukan ta harsai da wayarta ta dau kara tadauka tayi sanin duk duniya daga oum,sai abba da anty rufaida da salma kawae take da number su su kawae ke kiranta tasan cikin su biyun dole daya ne ko salma ko abba ganin saving din world best dady yafito yasa ta jin wani sanyi a ranta wani irin murmushi tayi mai sanyi wanda ya fito da zallar white cute face dinta ta kara kyau dimples dinta suka loma jeren whitewash teethes dinta suka bayana at this time sai naga zamu iya kiran aydah da milky

domin she is beauty beginning dauka tayi tareda turo wannan karamin bakin nata tace abbanah ciki kuwa Alhaji habib yace babynah abba ina wuni yah aiki lpy lau and you hope kinci abinci baby rolling eyes dinta tayi tamkar tana gabanshi dandanan idonta ya cika da kwalla cikin sanyi murya tace abba miyasa Oum da anty rufaida basa sona miyasa kullum suke man fada how dare her ta hadani da wani abu wai shi poor har tana cewa wai zan aure poor man abba ka fada mata ni babu wani auren da zanyi if mah Auran zanyi I will make sure na aure wanda yafi kowa kudin in whole world ko abbanah gyada kai Alhaji habib yayi tamkar yana gaban yace exactly baby ki barni dasu zan koya masu hankali kuma kin natsu ki kwantar da halinki very soon zaki koma school your holiday is over mah self kinji baby ita kuwa rufaida kibar ni da ita dasauri tace wait abba ynx kasan da kace zaka kore anty rufaida oum mah fushi zatayi tace saida su tafi tare kaga lets fine another solution

Abangaran malik kuwa tashi yayi da safe ya fara gudanar duk aiyukan da zama dawaniniyyar shi a gidan har gari ya karasa wayewa jama,a suka fara kai kawo domin gudanar da kasuwancin su Abby ne zaune kan clean mat din radio a gefenshi yanaji morning news su aisha da ummi na ta faman hada break fast wanka yafito dakinshi ya nufa ya kintsa kanshi yayi matukar kyau ya taje sajenshi tareda kafa hular p-cap ta zauna dass a kanshi kusa da abby ya zauna domin yana son magana dashi tare suka cigaba sauraron news din har aka kammala sannan abby yayi gyaran murya yace Malik ina son a kullum ka kasance mutun mai hakuri da juriya da jajircewa akan komai malik duniyar nan ba Komai kake nema kasamu bah kasance mai hakuri a duk idan ka samo kanka kada ka taba cutar da wani wai dan yana karkashin ka cikin gamsuwa da maganar abby malik ya ce in sha Allah abby nagode Allah yasaka da alkhairi yakara girma murmushi yayi sosai wanda sai da naga kamar shi da Alhaji habib har yaso yafi da malik

Ahankali take takawa tamkar wace bata son taka tiles din dakin har ta karasa gaban bedside dinta ta dauke wayar ta yau ne karo na farko a rayuwarta da zata kira salma da kanta ba ita ta kira taba

Ba tare da ita salman ce takirata bah dialing number salman tayi amma har tanuna call ended ba a dauka bah tsaki tayi tareda jefan da wayan

Karo na baadadi oum tasake saukar da ajiyar zuciya tareda fesar da numfashi yanda gabanta ke buguwa har kana iya hangowa tacikin riganta Rufaidah ce tsaye akanta tana tofa mata adduo’in samun sassauci wajan mahalice mikewa tsaye Rufaidah tayi ban tagama yi wa oum dukkan

azikarin datasani wanda zai sa zuciyan ta sanyi kallonta oum tayi tareda kiran sunanta nagaskiya ,Rufaidah ma kallon oum tayi tabbass tasan anzo gabar da yakamata kaddara da kuma gyaruwar alamurra su pah taka rawa a rayuwar aydah hakika anzo lokaci da rayuwar sauyi dakuma gyara ta pa wanzuwa a duniyar aydah mafita daya ce kuma hanya daya tal wanda zaya sa ququwar sauyi da tarbiyya mafi inganci su fara taka tasu rawar a fili dakuma zahiri na rayuwar aydah dukkanin hanaye biyu na oum Rufaidah ta rike cikin natsuwa soyayya irin ta yan uwan asali Rufaidah tafara wa oum magana, Uktieee anzo wajan lokacin yayi amma kafin wanzuwar komai sai kin jure sai kin daure da duk irin matakin da zamu dauka domin shine mafita ta har abada a rayuwar aseeyarh kallon Rufaidah oum keyi cikin tsantsar son jin wannan mafita wanda tasan duk dunia bayan Allah Rufaidah ce kawai zaran dazaya daure mata duk wani matsalanta idanunta dasu kayi laushi ta zubawa Rufaidah tace uktie bana shaka ko kuma fargaba akan duk abunda zaya faru indai abunda muke so zai faru indai abunda muke nema zai samu! Murmushi Rufaidah tayi tace uktieee komai zaya faru yanzu zai zamo sanadin abu guda biyu tunuwa da hakan da oum tayi yasa taji kashi tamanin na damuwanta yarage amma uktieee wani hanzari bah gudu bah abban aydah fa murmushi itama oum tayi tareda cewa wannan mai sauki ne uktieee tashi tsaye Rufaidah tayi tace yau zamu fara duk wani plan namu sosai oum takara samun kwarin gwiwa da kuma karsashin aikata duk abunda ta tsara wanda abu ne wanda zata jifi tsuntsu biyu da dutse guda

Ranar baki daya wunin malik yayi a kwance sanadiyyyar alamu dayafara ji na tasuwar ciwon shi bbu sunayan Allah dari ba daya yake ta faman ambata domin bai ga ranar dawannan ciwo nashi zaizo karshe bah duk wani kokarin da abby ke son yi sam malik bai bari saboda yasan cutarwa ce dakuma cuta ga duk Wani d’a da abby ya haifa saboda a ganin malik din wani karin nauyi ne dakuma dawaniya ga abby din Allah shaidane irin wahalar da cutuwar dayake a duk sanda ciwon ya taso abby ne da ummi kawai ka kwatanta halin dayake shiga wanda bayan Allah su kawai suka san da ciwonshi sai shi da yabar wa kanshi sani bai da abokin daya zamar mashi na jiki kuma aganin shi wannan ba kamar irin normal ciwo bane daya kamata kowa yasani tunanin ne fal aranshi har bacci yayi nasarar kwashe shi .Abby ne zaune kan prayer mat sallarh nafila ya idar wanda shafa adduar shi kenan tun dazu yake lura da ummi ganin kamar akwai magana bakin kasancewar ta ba kasa fai tafiye magana ba har sai idan maganar tazama mai ma ‘ana dakuma amfanin cikin natsuwa da haiba dakuma kamala irin ta dattijan kwarai cike da so yace mata tagari uwa tagari kuma sirika tagari in Allah ya yarda tamkar mashi ya soka mata azuciya kamar wani fami yayi mata a tsohon

ciwon dake ranta tamkar soso mata idan yake mata kyakya yayi har ga Allah wani irin abunda ya dirar mata arai wanda take kwana take tashi da dawainiyyar shi arai hawaye suka fara zarya bisa kuncin ummi wanda ba karamin dagawa abby hankali yayi bah

Kallonta abby yakeyi babu kiftawa shiru yayi tamkar mai nazari kaf kalaman shi baiga idan yayi kuskuran zance ba wanda zai saka zuciya da kuma ran ummi bace ba kallo yake mata irin na mamaki da alajabi kallonta yake har sai da tagaji da kanta tayi shiru gyaran murya yayi tareda da fara magana ahankali tamkar wanda yake kan gabar ban hakuri a laifin daya aikata banyi tunani ko zaton a duk cikin kalamai na akwai wanda zai bata ranki ba ummin malik share hawayenta ummi tayi cikin karaya da tarin rauni tace abbyn malik duniya gudu take kwananki karewa suke abubuwan kullun tsayawa suke babu sauyi har sai yaushi har sai wane lokaci komai zai zamu daidai har sai wani lokaci komai zai dawo bisa mizani rayuwa tazamo manah kamar busar sarewa duk yanda iska ya kada haka sautin fitar busar zaiyi damu tunda tafara maganar yake juya kalaman nata kamar mai bita ko kuma hadda su akai, cikin karfin zuciya da tarin kwarin gwiwa yace ina ji a jikina lokaci yayi ban san ta ina ba ko ta wace hanya bah amma adduar damuke tana gab da karbo wa mu bar wa Allah komai kallonshi kawai ummi keyi bstareda ta amsa ba ko fahimtar kalaman da yake amfani dasu wajan maganar bah hankalinta sam baya tareda dashi.Tashin yayi cike da karfin hali da kuma dauriya sakamakon kira mafi daraja a duniya dayaji kaf massallanta anguwar tasu ta dauka ahankali yake tafiya har yakarasa bakin kofar dakin shi daidai ummi na fitowa daga dakin domin duba jikin nashi kasancewar tasan idan ciwon yafara lafawa bacci ke daukar mai nauyi da nisa hada ido sukayi taga lokaci guda yafada irin fadawar da ciwon ke saka shi yi cike da tausai take jera mashi kalmar sannu da adduan samun sauki kallonta yayi ya amsa mata yana nufar hanyar bayi saida yayi wanka tass sannan ya daura alwalla zuwa yanzu Alhamdulilah jikin nashi da sauki shiryawa yayi cikin cream jallabi mai matukar kyau wanda tafito da ainahin kyauwunshi na hausa fulani karfafan kirar jikin dayahade da tsawon shi wanda ke kara fito da asalin kwarjini da haibar shi takawa yake ahankali da kuma nutsuwa har ya shiga cikin massallaci ko bayan angama sallarh zaunawa yayi ya cigaba da azkar yana jiran lokacin magrib wanda tun farko dabi’ar malik din ce ahaka.

Kasancewar fita suke so suyi cikin sirri hakan yasa oum da kanta driving motar hankali take juyawa fararan yatsun hannunta da suka sha ado da jan lalle dan asalin kasar sudan duk bayan seconds take sauke ajiyar zuciya duk abunda take rufaida tana kallonta wanda itama kusan hakane addua kawai

takeyi Allah yasa matakin dazasu dauka ya zamu silla da kuma sanadin daidaituwar komai har suka karasa anguwar dake dauke da gidaje waenda ke nuni da tsarin anguwar ta masu karamin karfi ce sauka sukayi daidai kofar wani madaidaicin gida hankali suke takawa kowa da abunda yake rayawa a ranshi

Tafiya take tamkar wace wani ke counting steps foot dinta tafiya take cikin nutsuwa aji kamala da kuma tsabar kwarewa a gayu har takai gaban wardrobes dinta wacce ke dauke da tsarin kaya tamkar ana shirin bude boutique wata grey abaya ta fiddo batada hanyani sam amma kuma tayi musulmin kyau komawa tayi bangaran underwears dinta ta fiddo wata black lace form bra tare pants dinta tsaba ta shirya kanta Yah rabbil alameen!

Yah rabbil alameen!A koda yaushe tamkar ana kara fiddo da ainahin kyauwunta ne tamkar ana sake kera hallitar tane kyauwun jiki dana fuska hade fata tamkar rabawa akayi ta zaba gayun da jikin nata ya hadu dashi ke sa duk wani bawan marmarin kallonta ko da sau dayane wanda hakan ba karamin cutar da ita bane sam bata son mutane bata so hayani bata son duk wani abunda ya shafi mutane towards her Mirrow ta maida kallonta tashi tayi tareda sauke ajiyar zuciya fuskarta ta dan bata kadan tareda turo karamin bakinta hannu ta mika tareda daukar uniques perfumes dinta wanda tsabar kudi aka sa aka siya ANGHAM ALHUM,Dhahab Arabiyat sune asalin turaran da take amfani dashi wanda tun daga kan shower gel dinta face cream body cream shampoos soaps toothpaste hand cream dinta duk na company Dhahab dinne shiyasa ni’ima da asalin kamshinta wanda ya cukude da natural skin scent dinta yake bada wani ni’imtacan kamshi mai saukar da nutsuwa game da kantar da hankali tunuwa tayi batayi sallan la’asar bah dasauri tamike tana turo baki saboda tasan yanzu oum zata shigo tafara mata fada baki da sallarh da alwalla basu wuce 3mins har tayi tagama yunwa takeji hakan yasata daura bakin salkakin gashinta da scarf din abayar wasu soft flat shoes ta zira kafar ciki tafito zuwa dining area ko da tasauko babu kowa t.v ce kawai ke nata aikin sai na’urar da sanyi dake aiki hankalin sanyi wajan ya hade da kamshin rosemary air freshener hakan yataimaka matuka wajan fitar da siring kamshin a parlor din bude warms din tayi taga white spaghetti da kayan lanbu anyi slices dinsu in very attractive shape dan bata fuska tayi tabude dayan warmer din itama dai vegetables stew ce taji kayan ciki fresh watermelon juice ne cikin jug din wanda hakan yana daya daga cikin aladar oum baa taba shan wani drinks apart from fresh juice kadan ta zuba tafara ci ahankali tamkar wacce ke ci dan dole ba dan yunwar cikinta bah takai 30mins tanacin abinci da bai fi yaro dan shekara 3 ba zai ci shi kusan rabin hankalinta yakoma kan tunanin

abunda ke jawo mata faduwar gaba duk kwanan bah so take Abba tafada masa haka kawai take jin kamar wani abu na damunta to miye wannan tasamu kanta dayiwa kanta wannan tambayar sam bata san oum bata cikin gidan duk tunanin tana dakinta ko part din auntie rufaideerh karar danna door bell din da akayi shi yaja hankalinta ta mayarda da dubanta kan kofar maids din da aka tanada domin aikin tuni ta tambaye waye tareda bude kofar bayan amsa mata da salma tayi ,masha Allah salma itama bai laifi komai nata daidai bazata wuce shekarun aydar bah koma tawuce sai dai da 1or2 years sanye take cikin dinki fitted gown din atamphar yayi matukar amsar jikinta kasancewar ta mai dan murjajan jiki saidai ko kama kafar aydarh batayi bah wajan kyau da ma surar jiki baki daya ta sallama takarasa dining din iyakar lips kawai aydarh ta amsa sallamar ganin yanda tayi ne yasa salmar tuna ita fa mai laifi ce takirata bata dauka,sannin halin aydarh yasa salma yin murmushi tareda fara ba aydarh dalilin dayasa bata shigo da wuri bah tunda tafara magana aydarh ke kallonta ko kiftawa babu saninin bazata amsa bah yasa salma chanza labarin,aydarh miya faru naga kamar ba yarda nasake ganinki ba wani abu yafaru ne ita dai aydarh batace komai tacigaba da kallon salmar hararta salma keyi tace wait kinga bana son rashin kirki ina maki magana kin mun shiru can tamike tace mata sannu da mamaki salman ke kallonta wannan hali nata bata san ranar chanza ce shi dakinta takoma ta zauna kan sofa daurin datayi ma kanta ne take warwarewa zuba mata ido salma tayi tace aydarh oum pah mutsa bakinta tayi tace she is in room mikewa salman tayi tafita domin gaishe da oum sosai suka saba da oum wacce take ma kallon mahaifiya itama oum na mata kallon diya da sallama ta bude kofar dakin amma shiru babu kowa girgiza kanta tayi tana jinjina irin halin aydarh bata ma san oum bata gidan ba ma girgiza kayi takoma dakin aydarh cikin wannan muryarta ta mai nuna zallar shagwaba da kuma aji tace nakiraki baki daga ba kuma baki tambayeni dalilin kiran salma tayi kasa da murya tace naga dana shigo har fara baki hakuri nayi amma tsabar rainin hankali kika zuba man ido sorry tafada agajarce salma tace to miya faru kika kirani bana kusa ban daga bah nayi kokari nazo gidan kuma kika zuba ido kina kallona kamar wata yar iska tashi tayi tareda daukar wayarta tace babu komai kuma sakin baki salma tayi tana kallonta kamar taga abun mamaki tace hala kanki babu dadi yanzu kuma shiru aydarh tayi har salma tagama masifar tayi shiru tace kingama wani katon bakin ciki ya tsayawa salma a rai ta watsa mata harara bag dinta tadauka tare nufar hanyar kofa cikin masifa take cewa in sha Allah ankusa yi manah maganinki miskilar banza miskilar wofi murmushi tayi kadan ita dai duk nan bataga abun masifa amma dayake salmar ita komai na fada ne da masifa shine har taji haushi wayarta ta dauka tashiga playing games

amma kaf hankalinta na kan faduwar da gaban takeyi runtse idonta tayi tanajin wani yanayi tamkar bada ta lapia tun tashinta yau duk tunanin ta cramps zatayi rau rau tayi da ido gabanta na faduwa domin ba karamin wahala take bah idan tana cramps har allura ake mata sometimes har dayan ciwon nata yake tasowa watau asthma hakanan taji tana so daga curtains din window dinta Allahumma bareek yanayin jikin su aydarh shi ake kira da package shape gyara zip din gaban abayar nata tayi boobs dinta dake cure waje guda suka fitar wani shape mai kyau da daukar hankali fatar wajan tasamu Hutu da tsabata game da kulawa ciza lips dinta take tana takawa ahankali zuwa yanzu ta fahimce ciwon marar ne take komawa tayi ta kwanta kan gado.

Kasancewar garin da alamar hadari yasa ummi fitowa tashiga dakin su aysher zaune suke halime ce ke gyarawa maryam (autarh) kallabar da aysha tayi mata take complain din yayi zafi har aysha ta saba da complain dinsu na zafin hannu da suke cewa tana dashi tun tana biye musu suyi chapter har takoma idan sunyi saidai tayi shiru tana kallonsu gyaran murya ummi tace tau fadan da bai karewar ne kuka dasa koh?takarasa maganar alamar tana tambaya dasauri maryam tace wallahi ummi adda zafin hannunta kullun karuwa yakeyi halimai ta turo baki tace ummi adda pah da gangan takeyi saboda ace ta daina yi kitso daman ai bataso aysha tace ummi ni duk banda lokacin wannan abun nasu abinci zaa daura ne? Eh ummi ta amsa mata tare da bata umarnin abunda zaa daura din ko da ta fito saida tafara shiga dakin malik ta mashi ya jiki tareda tambayar shi ko akwai abunda yake da bukata maida duban shi yayi gareta cikin wannan muryar tashi kamar mai magana dan dole yace mata tea tasan daga wannan babu saura abunda zai ce mata kasa tayi da murya tace wai yayah itama auntie tamu haka kake magana da ita?mugun kallo ya watsa mata da gudu ta fito daga dakin saboda tasan sauran ma ko bayan fitar aysha maganar tace tadawo mashi akai kalmar ‘ auntie’ tana nufin budurwa murmushi yayi yana shafa salkakiyar suman kanshi bakaa sol shi kam bai ga ranar bah ma kan murhun gawaye ta daura mashi ruwan zafin 5mins tagama ta hada mashi ta mika mashi daki idonshi na rufe amma ba bacci yake bah ta ajiye ta fita domin cigaba da aikin girkinsu, oum ta maida dubanta ga rufaidarh ganin cikin plan dinsu wani yazo dasauki domin kau harda gudun zuwa wajan hajajju garesu domin itace zata nuna masu kofar cikan burinsu madaidaicin gidan dake shafe da cement ko ina tsab a gyare gida tsofi ne babu wani hayaniya sam mama Rabi wace matsayin kaka take ga abba ita daya ta rage musu shi da dan uwan nashi kaf dunia amma rashin son zumunci irin na abba dakuma ware

kanshi dayayi tun farko daga lamarin familyn shi tun bayan rasuwar mahaifinsu mahaifiyarsu ta jima da rasu tun suna yara

Wanene dan uwan abba?

Wane irin plan oum da rufaidarh garesu wanda suke ganin zasu jifi tsuntsu biyu da Dutsi daya?

Miya kawo su wajan kanwar kakarsu abba wacce ke matsayin kakarsu?

Salma tace ankusa maganin aydarh wani irin magani?

Mi yajawo kamar da malik keyi da abba?

Tun suna yara cikin tattare kwarin gwiwa da karfin zuciya oum ta fara ma baaba kulu magana tunda ta fara magana hajajju ke kallon oum da baaba kulu da rufaidarh baki daya kallonsu take kamar wasu zararru tana mitsi mitsi da ido tana jiran taji iyakar idan oum zata tsaya cikin sanyi murya game da raunin zuciya da sarewa oum ke magana tunda tafara baaba kulu ke kallonta cikin tausaya da tsabar kauna baaba har yaushe zamu bar cigaban wannan gaba da kiyayya dake tsakanin yan uwa biyu har yaushe zan cigaba da jure ganin ASEEYARH a wannan yanayin baaba fashewa tayi da kuka mai taba rai rufaidarh tacigaba da magana baaba maganar damuka zo ita itace mafita maganar da muka zo ita tace makama itace wukar dazata yanke duk wata damuwa da kowanin muke ciki! cikin gamsuwa da fatan cikar buri baaba tace rufaidarh kuyi saurin fadin abunda ke tafe daku kuyi saurin yin man bayani cikin gagawa kuyi saurin bani haske in sha Allah nayi alkawarin goyan bayan ku,bayanin duk plan dinsu sukayi ma baaba shiru yabiyo bayan rufaidarh takai ayar maganar ta ajiyar zuciya baaba tasauke domin ta yarda ta amince ta gamsu da duk bayanin da rufaidarh tayi mata zata fara magana kenan hajajju ta mike tamkar wacce kunama ta harba salati tagama tamkar wacce aka aiko ma sakon mumunan accident tace hala oum dai kun chanza addini daman ance waennan rubabbun larabawan sudan din ba hankali gareku ba Jama’a kuji wata maganar dauri tayi kasa da murya tace amma dai gaskia kulu baku da imani keda waennan masu zubin abzinawan nijer din haka kawai ku bankawa bayin Allah sharri saboda baku kaunar Allah wai wani saboda a gyara zumunci ita kuma adar ta gyara halinta tau sam babu ni a wannan bakin zunubi wannan sharrin ko a fim sai haka fashewa da kuka tayi tamkar wata tababba cikin daka tsawa da daga murya baaba kulu tace ke wai hajajju mahaukaciyar ina ce ina nan naga basu sa dake ba cikin wannan lamarin kuma saboda sun ga cikin mu guda dake yasa basu ce ke bamu wuri bah,haba dan Allah ki dinga abu kamar

wata zararra ina amfanin wannan abunda kikayi haka tau ba ruwanki idan bazaki goye bayan wannan baiwar Allan ba a wannan sadaukarwa da tsoron Allah nata ba ba’a zage ta ba share hawaye hajajju tayi tareda fesar da majina ta mike tsaye tace tau gaskia kun zama abun tsoro tun zuwana yola nake ganin jafa’i kala kala babu irin mugun abun dake ban gani ba shiru sukayi babu wanda batayi mamaki bah domin a tunaninsu itace mutun ta farko dazata amince ta nuna yardar akan lamari amma har cikin rai rufaidarh tasan hajajju daga baya zata chanza magana ta amince domin idan da sabo kowa yasaba da wannan halin nata sosai baaba kulu ke jinjinawa oum wata irin kauna da soyyayarta na sake karuwa har cikin ranta addua tayi musu sosai da fatan alkhairi dakuma fatan cikar burinsu batare da wata matsala bah hajajju kau daki tashiga tayi zaman dirshan ta cigaba da hada kayanta a ghanan ta yau ban kwana yola gaskia duk idan dare yayi man yau a kano zan kwana ah ni binta ina zan iya zama cikin masu zuciyar kafurai da mugun abu ina zaman zamana wannan tsohuwar ta taso ni wai nazo batada lapia bancin kaddara da mi zai ma kawoni wannan gida nata kamar zuciyar talaka gida ko farin glop babu sai ja kamar dai bamm,Har hajajju tagama hada kayanta su oum na zaune suna cigaba da tautaunawa da baaba kulu fitowa hajajju tayi da katon ghanan ta tashare hawaye ta nemi kujera ta zauna ta mike kafa tayi kasa da murya kamar ba ita tagama kuka yanzu ba tace a gaskia rufida’u ban taba sanin kunada hankali ba irin yau idan bahaka har miya hadaki dasu dazakiyi musu irin wannan halaccin tau ko ni nadake ciki guda da kakarsu habibun bazan iya wannan abunda kikayi bah gaskia kinyi kokari Allah yayi muku albarka ahankali kuma tace amma shi mai zubin yan fim din indiyan ya amince itakuma diyar wurin naki hwa?murmushi oum tayi daman tasan daga karshe hajajju zata sako tace in sha Allah hajajju komai zai zo manah cikin sauki tunda gaki murmushi hajajju tayi tace aikam nasan ta kan tsiya daman tun sauka ta jiya na kira shi audul din nace mashi gani a yola yace zai zo tau nasan wannan bahillatanar uwar tashi zata hana shi zuwa shikuma rubabben ibrahim din daman bana san ran zaizo idan nake saura yaran dama ba fita suke amma ki bari ya shigo sai nasa kulu ta kiraki kituro man ita adar shima habibun ki tada mashi hankali ki nuna wani jafa’i ke shirin faruwa a najeriyar yayi gaggawar dawowa yauwa tunda tafara magana baaba kulu yake murmushi domin tasan halin yar uwarta tsaf saidai ta shirya yarda komai zai tafi daidai daman tasan sai ta amince da zancan daman kowa yasan halinta shiyasa tayi mata wannan gorin.

Karar kiran wayar yasake shigowa a wayar tashi a karo na ba adadi yasan mai kiran kuma ko daya daga bai san abunda zai fada ba bai shirya daukar

darun mai kiran ba shiyasa bai daga ba so yake kawai ya cika alkawari yaje dasafe Idan Allah ya kaimu ummi na lura dashi saboda tasan da maganar sai tayi murmushi tace miyasa ba zaka daga ba? Shafa sumar kanshi yace so nake kawai naje zuwa dasafe in sha Allah,Allah yakaimu tace babu wanda yasake magana acikinsu har kowa yagama cin nasa abinci bayan sun kammala halime ta kwashe plates din tayi kitchen dasu shirin tafiya makarantar dare sukayi amma sai malik din yace su bari saboda har yanzu garin akwai alamun hadari ya yayi musu kari a gida godia sukayi mashi aysha har cikin ranta taji dadi saboda sam bata cika son zuwa makarantar bah saboda malamin su dayafiye takura mata da sunan soyayya har ummi takawo ma zancan tashare ta tareda fadin Allah yakyauta kawai babu abunda tace wajan takwas daidai abby yashigo gidan hannunshi dauke da bakar leda wanda fura ce a ciki da fresh nono mai kyau irin na fulanin adamawa gaishe sa sukayi tareda masa sannun da dawowa tambayar su yayi abunda yahana su zuwa karatun dare maryam tagaya masa bace komai sai shiga daki dayayi gidan a tsabtace yake sai tashin kamshin tsintsiyar tsinke yake abinci shi ummi tashigo mashi dashi tareda wajan dazata dama mashi furar

Zarah bansan abunda yasa kika takurani cewa gobe sai nadawo Nigeria ba ajiyar zuciya oum tasauke tace amma kasan abbyn baby ba karamin abu bane zai sa nace kadawo nigeria zuwa gobe wani tarihi ne na kaddara wani salo ne da tashin zaune tsaye gaskia ce dakuma asalin rayuwar farko zai maimaita kanshi duk bai fahimce kalaman ta ba saidai gaban shi yayi mumunar bugawa har sai da glass cup din dake hannunshi yayi mumunar fashewa kokarin daidai ta kanshi yayi sannan yace zan biyo private jet around 10:00am in sha Allah munyi landing katse wayar yayi batare da ya jira amsawar oum ba sauke wayar tayi daga kunnata ta zubawa wayar ido tamkar mai son gano karafan daakayi amfani dasu wajan kera wayar wasu irin hawaye suka sauko mata bazata iya fasallata yanayin datake ciki ba farin ciki ko bakin ciki sam ta kasa fahimta bad room tanufa tasakar ma kanta shower ko zata samu saukin abunda take ji a ranta shirya tayi cikin v gown tayafa mayafin gown dinta inner cap ta rufe gashin kanta daya sha gyara da ita tayi matukar kyau duk da yanayin da take ciki yasa ta dan fada sai tayi matukar kyau yarintarta tafito kamar bata haifi aydarh bah dakin aydarh tawuce da sallama tashiga tasame ta tsaye jikin window wannan karon ta Chanza kaya tasaka soft gown baby pink tayi matukar karbar jikinta kanta babu dan kwalli amma ta daure shi tsaf da ribbon kasan kai kallonta oum keyi ko kiftawa babu ganin irin kallon da oum keyi mata yasa tayi rau rau da ido ahankali cikin sanyin muryar nan nata tace oum ina wuni

ashe fita kukayi oum banda lapia pah takarasa cikin dan karyar da wuya duk tunanin laifi tayiwa oum dayasa ta tsayawa tana kallonta haka itama oum babu yabo babu fallasa tace

Mafarin faruwar komai kaddara zane ne shikuma tarihi ajiya ne babu gaskiar dake boyuwa duk yanda aka so rufeta shin DA SO KAMANE ba iyakar soyayya zata bayanu a labarin bah faruwa da taushan komai zai fara gudana Allah shine masanin daidai hikima da dabara na iya aiki ne kawai akan abunda Allah yasa zai dawo daidai zai dawo hanya yah rabbi kasa mu ci dukkan kaddarorin dake shimfida a littafin kaddarar mu

Tace mike damunki ?kasa tayi da murya tace cramps ne ta fada tana rau rau da ido kallonta oum keyi ko kiftawa babu tace tun yaushe da yamma nafara ji kuma drugs din duk sun kare sannu oum tayi fita har cikin ranta taji wannan ma wata dama ce duba da yarda cramps din ke wujujuga aydarh numfashi ta fesar tayi hanyar dakin rufaidarh domin sanar da ita halin da aydarh ke cike kasancewar daman duk sanda aydarh ke cramps rufaidarh ce ke dawainiya da ita duk sanda take cramps saboda acewar oum bazata iya da rakin aydarh bah tsaye tasamu rufaidarh tana jera kaya cikin wardrobe dinta kamar ko ina na gidan shima dakin rufaidarh hakan ya kasancewar mai matukar kyau komai a tsare yake daidai da daidai murmushi tayi tace nikam uktiee ko dan gobe abban aydarh zai dawo ne naga kin wani chanza kamar wata yar shekara sha takwas miye sirrin takarasa cikin sigar tsokana tayi sosai oum tayi tace kinga ki koh uktiee miye wani sirri bayan kinsan komai nikam babu wani sirri kuma ma ai wannan ba irin normal zuwa bane zuwa ne mai dalili hakane rufaidarh tafada agajarce sannan tace akwai abunda kike da bukata ne uktiee no babu yarinyar ki ce ba laifi nazo nagaya maki subhanallah mike damunta cramps? gyada kai oum tayi batareda tayi magana murmushi rufaidarh tayi tace Allah maji rokon bawa Allah mai yarda yaso a duk sannda yaga dama kinga hanyoyin nasara na ta zuwa ta ko ina ta hanyar da bamu zato bah koh zama oum tayi kan Italian bed din dakin tace uktiee nadai zullumi ko fargabar wayewar gobe zuciyata ta dake da duk abunda zai faru goben nayi i’mani kuma nayarda da ubangiji in sha Allah komai zai zo yanda muka tsara komai zai zo cikin sauki da yarda Allah ya maganar doctor ashraff salman tayi magana dashi ne eh uktiee salma tace ta tsara duk yarda abun zai kasance kuma bata samo matsala dashi ba wajan fahimtar yanayi domin shi kanshi shaida ne Alhamdulilah oum tace tareda kwanciya sosai kan gadon tana rufe idonta wani irin sanyi ke ratsa dukkan sassan jikinta dukkan wata kafa ta veins dinta sanyi ke ratsawa jini take jikin na kara yawan gudu a cikin veins din so take ta samu bacci sosai kallonta rufaidarh tacigaba dayi tana

tsananin tausan yar uwarta ta hakika ba kowane dan adam bane zai iya aikata abunda oum ba kowane mai rai bane zai iya wannan sadaukarwar ba uktiee bara naje wajan baby kiyi kokari ki samu bacci sosai anan din daidaita gudun Ac tayi tareda sakin duk curtains din dakin kofa taja mata ta fita ko da ta shiga dakin aydarh kwance tasame ta idonta rufe amma tasan ba bacci take ba domin a wannan halin allura kawai ke saka aydarh bacci ahakan ma yanzu da sauki sosai domin kaf Europe countries babu wanda abba bai zagaye ba da aydarh ba saboda case din nan duk da idan asthma ta taso ba karamin wahala take sha ba amma ciwon marar yafi dagawa kowa hankali domin duk rashin tausan ka dole ka ji tausayin aydarh tunda rufaidarh ta zuba mata ido bata dauke ba ji tayi kamar ana kallonta ahankali ta bude ido,idonta dayayi laushi Sosai ba karamin kyau tayi ba duk da tadan fada a wunin hakan sai ya taimaka Sosai wajan fito da asalin zatin fuskar tata kokarin tashi tayi rufaidarh tace no dear kuma ki kwanta no need kamar jira take tafashe da wani shagwababan kuka tamkar wacce aka do’ka ahankali rufaidarh ta taka gaban gadon zaune ta mikar da ita cikin sigar lallashi tace sorry cutie pie maran ne gyada kai tayi ta rike hannun rufaidarh tace second ma gabana faduwa ban san miyasa ba ina jin tsoro I didn’t to be alone please stay Sosai rufaidarh ke jin tausan rungume tayi a jikinta ta cigaba da sauke ajiyar zuciya samun kanta tayi da tambayar zuciya shin ko dai aydarh taji a jikinta akwai alamarin dake shirin faruwa da ita? bata da amsar tambayar tata hakan yasa ta cigaba da tofawa aydarh addua tana shafa bayanta kusan 10mins suna haka sannan rufaidarh tasauka tahadu mata abinci a tray da bottle water marar sanyin ta shigo dakin dashi dakyar tasamu aydarh taci kadan ta turo ganin zatayi amai yasa rufaidarh barinta hakanan magani ta bada tareda gyara mata kwanciya ta rufe da duvet kallonta tacigaba dayi cike da tausayi da kuma kauna kusan 5mins ta bata tana kallon aydarh sannan ta fita tayi bangaran masu maids din gidan saboda akwai abunda take bukata.

Sosai suka ji dadin karin da malik din yayi musu kowa yagane Sosai duk wani kurakuran su sun gyara kuma alhamdulilah Allah yayi masu baiwar fahimta da kuma gane karatu hakan nada nasaba da tarbiyya mai kyau da kuma good background din karatu dasuka samu saida suka sake maida komai mahallinshi a gidan kafin suke shige daki su kwanta (yan uwa a kula dan adinga kauda komai kafin kwanciya bacci kama daga takalmi kwanuka dasauran su saboda mutanan boye dare shine time din hidimomin su kuma suna iya sakar ko wacce kalan cuta a jikin kayan amfanin mu)zaune suke shi da abby da ummi a dakin abby din murmushi abby yayi yace tau ka daure kaje manah tunda dai an zabe ka kamar tumun dare shima murmushi yayi

kadan yace in sha Allah abby zanje ummi tace ahtau kafin kuma ka jawa kowa cikin saboda kasan halin yan kayanka Sosai sun dan bata lokaci suna fira sallama malik yayi musu yawuce daki ko daya shiga dakin sake fitowa yayi waje yayi alwalla domin yana san raya daran yana sallarh,sai wajan 2:30sannan ya kwanta

Gyara daurin kallabin ta tayi tareda matse biredin dake hannunta wanda yaji kwai Sosai ga roman kai dayaji kayan kamshi a gefe sannan tayi kasa da murya kamar mai tsoron wani yaji ta tace wai yaya hof kin fahimce duk yarda na shirya filan dina koma kallonta baaba kulu tayi tace na fahimta hajajju kuma na gamsu Allah yasa komai yatafi daidai Ameen tace sai ta cigaba dacewa wai kuma yaya babu son zuciya da cuta a lamarin nan a ba wannan mutumin auran wannan yar yarinyar ina ji pah yayi talatin biyar zuwa hamsin haka baaba kulu dai tayi mata shiru saboda tasan idan ta biyeta yanzu zata cigaba da maganganu babu kai babu kugu tace ahtau ai maganar gaskia akwai bakin Mugun abu a zuciyar ku daza kuyi wannan abu nidai babu ruwana sabo hwa da Allah babu ruwana tau ni miye hadani ma da lamarin dinku bacin anyi zancan gabana kuma an nuna inda muhimmanci a lamarin da mi zai kaini shiga wannan sabon da shirka ita dai baaba tayi shiru kamar bata dakin cigaba da breakfast dinta tayi ta ba banza ajiyan hajajjun dan ma dan uwa na dan uwa bacin haka mi zai sa nazo gidan mata ta dinga dinki fusa kamar buss din cikin fim daga an bani wani gutun biredi ina ci Allah na tuba da a kano ne iyakar abunda zan ba almajirin makōta kenan still dai baaba bata kulata sai ma kwashe plates din da tagama kalaci da tayi tabarwa hajajju dakin few minutes itama ta fito dauke da kwanukan taci ta koshi sai hada zufa take tamkar babu celling fan a dakin tsabar ci ne yasata zufa ahankali tace tau kina ganin yana shigowa zaa kira ita uwar yarinyar itama ta turo ta ko kuwa ehhh haka zaayi tunda ai dole sai an hadasu waje guda sai ki tura so can gidan shi dan baban yarda kowa zai fi yarda idan aka gansu tare koh?gyada kai hajajju tayi tareda ballar goro tasaka baki tana tauna

Kona 1 minute bai runtsa ba gani yake safiya takiyi yanayin da yake ji da kalaman zarah watau oum sun bada gudunmuwa Sosai wajan rikita tunanin shi yakasa fassara kalamanta da abunda yake ji a jikinshi da zuciyar shi bitar su yake daya bayan daya ganin zai rikitar kanshi da tunaninshi yasa shi shafawa kanshi lapia kiran farko na asuba har yagama shiryawa duk wani abunda zai bukata tun jiya ya shirya shi already yagama da aikin daya kawo shi kasan daman sai karashe karashe P.A dinshi yayi ma handling duk wani abunda ya rage tareda fada mashi kiran gaggawar daya samu daga gida

Daga gida tsaf ya shirya kanshi cikin shadda dinkin kaftani tayi matukar karbar jikinshi yafito bafullatanin usuli cikin sassarfa yafito daga dakin babban hotel din idan driver shi ya ajiye motar ya nufa bai san dalilin dayasa yake ji wannan yanayin ba yaso yake yakira oum yagaya mata yanzu zasu taso amma yafi son kawai gaya mata gashi idan sunyi landing. Ahankali take kurbar ruwan shayin baki daya takarasa jigatuwa rufaidarh ce tsaye akanta bayan ta taimaka mata tayi wanka ta shirya ruwan tea din shine abu nafarko da aka samu zata sha tun wayewar garin kuka take mai karamin sauti domin azabar sake karuwa take tace ma auntie rufaidarh takira mata doctor ashraff tace baya nan yayi tafiya ta daure tasha magananin in sha Allah zataji sauki da sallama oum tashigo dakin tunda tashigo ta zubawa aydarh ido ko kiftawa babu rufaidarh ma dai oum take kallo tasan daurewa kawai take amma ba karamin zafi zuciyarta ke mata ba jurewa kawai take amma Allah kadai yasan halin dake ce a yanzu da fara’a suka gaisawa da rufaidarh tana tambayar ta ya mai jiki Alhamdulilah kawai rufaidarh tace taja bakinta tayi shiru babu yabo babu fallasa oum ta amsawa aydarh gaisuwan da take mata tana tambayar ya jikin nata Alhamdulilah kawai tace tacigaba da kurbar ruwan shayin kallonta oum tayi tana fesar da numfashi tareda laushe ido addua take kasan ranta kafin ta tattaro duk wani kwarin gwiwa da karfin zuciyarta cikin sanyi muryar tace idan kin gama ki shirya ai kinsan idan baaba ko?dan bude ido tayi har gabanta na faduwa tace wace baabarn?harara oum ta watsa mata tace ai kinsan duk fadin Abuja baaba daya kawai ke akwai murmushi rufaidarh tayi tace aaa uktiee ki bita ahankali baby baaba kulu take nufi saukar da ajiyan zuciya aydarh tayi tace yeah I know cigaba oum tayi da magana idan kin gama in the next 10mins ki fit ozan aike ki har cup din hannunta na barazanar faduwa lokaci daya tari ya sarqe ta tace oum wannan anguwa gidan baabarh ni kuma tafada tana nuna kanta saurin girgiza kai tayi tace gaskia oum ba zanje wannan anguwan ba and I didn’t see the reason of going there tafada har cikin ranta domin ita a tunanin iyakar gaskiarta kenan sanin kan oum ne bata zuwa gidan baaba idan ma har taje tau yazama dolene oum ta tirsasa mata su tafi din kuma ko data je ma bata iya zama a gida tsaye take tsayawa har su taho idan kuma suka dawo gida ta dinga tsanar kanta kenan da kayan datayi amfani baki daya ranar duk wani kalan shower gel da turaran dake kan Mirror dinta sai ta yi amfani dasu a jikinta cikin tsawa da daga murya oum tace ASSEEYARH rike ta rufaidarh tayi tace kiyi ahankali uktiee cikin masifa oum tace tau nabaki 10mins ki shirya ki yi driving da kanki saboda ma’aikatan gidan nan baza su cigaba dayi maki bauta kina wulakantasu as if there are your slaves am I cleared saukar da kanta kasa tayi tareda gyadawa oum kai words aydarh shine abunda oum tace,yes ma

juyawa oum tayi tabar dakin fadawa dakinta tayi tafashe da wani irin raunannan kuka mai taba zuciya Allah astagafirrullah Allah ka yafe man Allah kaga zuciyana yah rabbi kaga niyyana yah rabbi ka tafiyar da abunan cikin sauki ya rabbi kabani ikon cinye wannan jarabawar yah rahaman kasa kada muyi duk wannan shirin a wofi yah rabbil alameen kasa ko da ba duka burikan mu kwara biyu ba yah arrahamar rahimin ka cika mun daya kuka tacigaba dayi tamkar anyi mata mutuwa,Tau auntie mi zanyi acan din auntie kiji tausayina ki bata hakuri auntie I hate that area I can't even imagine seeing only me a wurin nan auntie please bazanje bah rage murya rufaidarh tayi tareda jawo aydarh a jikinta cikin sigar lallashi tayi kasa da murya tace baby kiyi hakuri kinji kiyi hakuri kinga mahaifiyarki ta baki umarni kinsan halinta kuma ko ni bazan iya hanata abunda datayi niyya ba and after all aydarh ai kinga bawani zama zakiyi acan din bah hajajju fa ce tazo miki da magani tace kuma dole sai ke da kanki zakije karba saboda ka'idan maganin ko bakya son ki warke ne?ita dai aydarh bata ce komai kallon rufaidarh kawai take kamar mai son gano gaskiyan maganar tunda oum tace taje gidan baaba kulu gabanta ya cigaba da bugawa kamar ana buga mata guduma,amma auntie ba zan iya driving ba nasani aydarh daurewa zakiyi ai daga yau in sha Allah keda wannan ciwon kuma shikenan still aydarh was so confused tau miyasa sai ita zataje karban maganin tau kuma ance dokan maganin kenan can kuma ta bata fuska tareda dan tabe baki tace auntie gaskia bana son maganin while nama san traditional herbal ne girgiza kai rufaidarh tayi tasan halin aydarh zuma ce saida wuta tace mata no normal magani ne bana son sake jin komai tashi kije ganin itama auntie rufaidarh ta daure yasa aydarh tashi anhankali kamar bata son taka kasa dangeshi take domin har yanzu kafaffun ta da maranta azaban ciwo suke gaban mirror ta tsaya tana kallon kanta tasake fresh amma duk tafada closet tabude ta dauko wata mad dubai abaya magenta ta chanza inner wears magenta wani hadaddan soft lace form brassiere tasaka tareda pant da undie duk magenta din tabarakallah, fitowa tayi ta kalli rufaidarh sannan tace uhm auntie ina key din mota yake murmushi rufaidarh tayi ganin irin yanda aydarh ke ba'bata rai tace yana wajan oum bara naje nakarbo maki ki karasa shirya kiyi sauri amma kafin 10mins din yakarasa cika toh tace ta dauki lights perfume masu fitar da musulmin scent ta fesa a abayar tareda saka lipgloss kadan a kananun lips dinta sai qyali suke, fizgar mota tayi mai gadin gidan nasu naganin itace yayi saurin bude mata gate yana mai mata adduar shiriya ga yarinyar har yarinya ko alarabawa da wuya asamu mai zubin ta Allah yayi halitta a wajan nan ina ma ace Allah yay ini mai kudi da babu abunda zai hanani auran yarinya kai idan na aureta ko fita waje nagama yi habu,habu yace ni ji nake ina ma kullun zan dinga kallonta da angama man

komai a rayuwa tahada komai amma saidai kash wannan halin nata na wulakanta dan adam yafi komai cim un tuwo a kwarya sule mai gadi yace hmm habu ke nan yarinyar duk abunda tayi tace tayi kuma gado girman d’a shi kanshi uban haka yake dandai ance dan gado sai yayi zarra haka suka cigaba da hirar abba da aydarh sunata sakawa oum albarka domin sunce oum mutunce hadda rabin mutun ma .Tagwayan numfashi oum tasauke jin yanda aydarh ta fizge motar ,tace uktiee kinji dai koh naji uktiee in sha Allah komai zai wuce da yardar Allah shirune yabiyo baya kowa da abunda yake juyawa a ranshi.

A gaskiya mutane sun zama abun tsoro a wannan rayuwar tau idan ba abun tsoro bah ace tun shekaranjiya sai fama ake dakai kamar wani rubabbe kazo kazo amma kadauke ni wata abu can daban kasa tayi da murya tace ko dai baka da na napap shiyasa ahtau niba bakuwar tsanina bace sai kayi magana na ara maka dan gaskia bazan iya baka kyauta bah idan bahaka bah kai kamar wani abun arziki sai ka kadama kake zuwa waje shidai malik kallonta kawai yake sannan yace tau yanzu dana zo hala ke kika bani? Ina ce nagaya maki banda lapia gwalo tayi tace haram haramun karya haramun yaushe kace mun baka da lapia ni binta ka gayawa haka saidai koh yaya, baaba kulu da ke ta kallon ikon Allah tace hajajju wai miye haka yaron nan ko gaisuwarsa baki amsa ba amma kin hau shi da masifa kamar dai wanda yayi maki wani laifi sake kasa da murya hajajju tayi tace ma malik tashi kaga mu fita mu gaisa a waje kafin wasu su cigaba da samana baki a magana tunda mutane basu san su ja bakinsu suyi shiru ba idan bada su ake zance bah murmushi malik yayi yana kallon baaba ganin irin duban da take ma hajajju da ta mike tsaye fita sukayi ita da malik dayan dakin baaba suka zauna ta kawo masa shayi da irish tace ga naka muna iya wuni nan tsohuwar gidan bata damu da bamu abinci ba shidai bai ce komai ba yazauna yafara cin irish din can hajajju ta mike tace jirani ina zuwa,wai yaya Adar ta taho ne?gyada kai baaba tayi tace ehh uwar tace yanzu haka ma ta kusa zama hajajju tayi ta dinga dariya kamar sabon kamun hauka inda sabo baaba yasaba da halin hajajju batace mata komai ba har ta tsaya da dariyan tace yau akwai hada bamm a Nigeria wooo yau zasu ga fim ganin idonsu kowa sai ya girgiza da lamarin shekara 22 biyu ba wasa bah zumunci gaskia da tarihin gaskia zai fallaso Allah yakawo ta lapia Ameen baaba tace,har ta kai bakin kofa ta juyo tace tau shi dan karunar pah ya taho gyada kai baaba tayi da tunani kala kala aranta, wai audul kasan wasu a kano girgiza kai malik yayi yace aa gaskia ni sau daya ma nataba zuwa kuma naga shima gidanki idan baki manta bah

Naga kuma gidanki ne naje ko? Ehhh hakane audul gidana ne kaje shiru tayi tana ta girgiza kafa can malik yace miyasa kika tambaya,kallonshi hajajju tayi sannan tayi kasa da murya tana kallon kofa tace aa babu komai gani nayi matar gidan na man wani gani gani kamar wata yar hau,murmushi malik yayi yace ke dai kika fadi haka kowa pah hakuri yake dake a cikinmu wani irin kallo hajajju tayi ma malik tace tau da nayi niyyar kawo ma komai cikin sauki amma saboda baka kaunar Allah filan dina kanka zaka sha mamaki!kallonta malik yake ko kiftawa babu yace plan kuma na mi?shiru tayi bata sake yi mashi magana ba shima malik din shiru yayi saboda yasan halin hajajju sometimes hakanan take magana babu kai babu kugu.Duk yanda taso ta daure ta gano direction din gidan baaba batare da magana yahada ta kowa na anguwar ba ta kasa irin gudun da take da motar tamkar zata ta shi sama yaran da manya na anguwar sai sauka suke a hanya domin ko da ganin zubin motar ko bigeka mamallakin motan yayi babu abunda zai faru,duk bayan seconds sai ta fitar da sautin tsaki cikin kwarewa da sanyi take tsakin ji take duniyar tayi mata duhu gabanta tsananta faduwa yake duk da ba komai tasani na illimin dunia bah zama a iya cewa cikin kashi dari na illimin zaman duniya tau aydarh kashi talatin tasani saura saba’in din bata sani ba kuma bata damu da tasani din bah(iyaye dan Allah duk yanda yakai da gata da son dakuke wa yaranku ai kokari ana daura su kan hanya ba kamar yaran mu mata basu san idan zasu riski kansu ba misali gidan miji d.s.s) takasa gane gidan hakan yasa ta nemi wuri tayi parking sauke glass din motar tayi tareda mai black shade dinta a ido tana kallon wani mutun dake tsaye kusa da wani gida cikin sanyi da izgili da isa tace tambaya nake waiwayo yayi yana dubanta sakin baki yayi yana kallonta mamaki yake yarda har ta iya hausa,sake motsa bakin ta tayi kamar taga abun kyama tace are you dumb?washe baki yayi yace hajia Allah yasa nasani bata ma san inda zata ce tana nema bah aka yasata yi mashi nuni da hannu batareda tayi magana ba,hajiya ai ko shaidan bai san nuni da hannu ba balle ni kallonshi tayi domin bata fahimce abunda yake fadi ba and yasan yarda take ji a zuciyan ta tsayawa datayi tana mashi magana ba karamin kokari tayi ba saboda yanda take jin har kanta na juyawa gani tayi idan zasu kwana anan wannan mutunan ba zai taba fahimta bay asa tace gidan baabarh shiru tayi kamar mai tunani can tace baabarh kulu sake gyara tsayuwa yayi yace Allahu akbar ai kin zo ma da baki tsaya kika bamu wahala ba daraat kinyi magana, kinga wannan gidan dake kallonki tau nan ne gidan hajiya baabarh bata tunanin zata iya masa godiya dan bata ma saba da hakan ba bata ga amfanin hakan ba domin a tunanin ta when you are rich you deserves anything in this life kudi ta kwaso wanda ita kanta bata san ko nawa bane ta wurga mashi ta window ta kwashe motar tayi gaba washe baki yayi ya

tsugunna ya kwashe kudin tass aran shi yana cewa shashasha yoo ni Allah na tuba miye damuwa na idan ma a fuska kika watsa man indai kudi ne (Allah ya kyauta) daidai kofar gidan tayi parking bin gidan take da kallo kamar mai son gano maginin gidan relaxing tayi kan driver sit din da take maida numfashi take tareda laushe idonta takai 10mins ahaka kafin ta dauke hadaddan luxury mini bag dinta wacce zata kai almost 500 thousands (na ga wasu a ig suna nuna manah ita 😂tau kunyi kokari dai dakuka siya)ahankali ta zira kafanta waje yah rabbi wani mad flat shoe ne a kafan sunyi matukar karban kafan sosai ahankali take tafiyan kaman mai counting steps har ta tura madaidaicin kofan wani irin yankewa gabanta yayi yafadi har sai da taji kanta na sarawa,Salati hajajju ke kwadawa ta gwalo ido tana karewa aydarh kallo kafin ta buda murya da karfi tana kiran baaba yaya yaya fito kingani dasauri baaba ta fito har tana tuntube da ghanan hajajju dake bakin kofar daki ,tana fitowa tayi ido hudu da aydarh murmushi tayi tareda karasawa gaban aydarh ta kamo hannunta tace Aseeyarh mi yahanaki karasowa ciki kallonta aydarh tayi tace babu komai ji take kamar zata fasa kara ji take kamar ta kwasa da gudu .hajajju dai na tsaye ta makale jikin bango tana kallon ikon Allah can taga baaba zata shiga tareda aydarh cikin daki dasauri tace yaaya mike damunki daga gani mata zaki shiga daki da ita minene haka baki tsayawa ma a tambaye a ji daga wace kasar aka aiko ta zata ki kama hannunta ku shiga ciki kallonta baaba tayi tace bana son shirme Aseeyarh ce fa,kankance ido tayi tace wacece kuma Asiya?ko dai itace adar? Baaba ta gyada mata kai tace ehh itace baki gane ta ba washe baki hajajju tayi tace billahi ban gane ta ba kiji yarinya kamar ana kara zana ta Allah mai halitta sai kuma ta fashe da kuka tace tau abunda zanyi saidai Allah ya yafe man amma dole tasani da kuma matan dasuka sak ani gaba sai kuma tayi shiru tace tau bismillah ada mu shiga daga ciki ita dai aydarh kallonta kawai take ,karasa shiga dakin su kai malik na zaune yana kallon t.v dasauri hajajju tarika su shigowa kamar an jifo ta ,ta zauna kusa da malik ta daure fuska kamar bai ta ba daidai sanda ta shigo daidai lokacin gabanshi yawani irin fadi har saida yadan dafa kirji yana mai karanto addua zaunar da ita baaba tayi a kujera kallo daya malik yayi mata ya dauke ido karamin tsaki yayi a ranshi domin tacika parlor da kamshi a tsarin shi baya son macen da take ado da kamshi da fizgar hankalin namiji yasan yanada kyau sisters dinshi na dakyau amma wannan nata yayi yawa tsaki yakara saki yana mai kwabar kanshi da gulmanta dayayi azuciyan shi,ko kallon inda yake batayi ba domin bata masan da wanzuwar shi a dakin ba,duk a takure take she is eager su bata abunda ta zo karba ta wuce bata gaishe da kowa cikin su ba domin gaisuwa ba halinta bane still bata cire shade dinta da yakasance black kanta na kasa tana juya

black stone English gold din hannunta baaba tace Aseeyarh bara a kawo abinci ko?girgiza kai tayi alamar aa batareda tayi magana ba hajajju da ta hade rai ta mike tsaye tace yaya bismillah inada magana tayi hanyar fita baaba ta mara mata baya suka shiga dayan dakin hajajju tace yaya baa bori da sanyin jiki kwara ayi komai kafin yamma koh?

Ummi shine yah malik yatafi bai jirani bah?auta ce mai maganar tana wani bata fuska cikin shagwaba tana turo baki halime tace tau hala mu ba mutane bane da bamuyu complain ba da yatafi yabarmu? Aysha tace rabo da ita maybe she is only human being here autarh dai batace masu komai ba tayi shiru taji haushi da yatafi wajan hajajjun yabarta,mikewa ummi tayi tace sai kuyi hakuri ai kwa je gobe idan Allah yakaimu kafin ta koma kusan dai hajajju ba ta ban kwana,dariya aysha tayi tace hajajju ikon Allah ni da abby zai yarda da wallahi bin ta zanyi ina son zuwa kano da sauri halime tace idan abby ya yarda yah malik fa? Kuma fa dariya autarh tayi tace ahtau dole dai mutun ya zauna adamawa har aysha ta mike zata kwade ta ummi tace ba fa na son shirme ku tashi ku kama aikin gabanku da alamar hadari a garin nan ,yauwa ummi daman so nake mu juya tsarin dakinmu cewar halime,Maryam ta kwabe fuska tace ku kullun da aikin da za ku dinga jawo manah babu wanda ya tan ka ta cikin ,Abbyn malik ga ruwan can na kai bayi idan sanyi baiyi ba sai nasake sirka shi mikewa yayi yakamo hannunta yace Allah yayi maki albarka yabiya ki da gidan aljanna murmushi ummi tayi tace Ameen yah rabbi miji nagari .

Rufaidarh tace amma dai uktiee duk da halin da ake ciki yakamata ko saloon ne kije sharp sharp ayi maki sabo fa da Allah mutunan ya saba duk tafiyan da zaiyi yadawo zai tarar dake kal kamar amarya wannan karon kuma yazaayi kibari yadawo ya tarar dake babu lalle babu gyaran kai oum batace komai sai warware salkaqiyar sumar kanta baka sosai har gadon baya tashafa tace yanzu uktiee gashin nan fa babu abunda yayi and kuma na fiso yazo ya tarar dani ahakan domin tun kafin wanzuwar komai yasan akwai matsala ,hakane fa uktiee wannan ma wani tsarin ne saboda shi kanshi zaiyi mamakin ranshi gyaran naki,can kuma tayi murmushi tace uktiee n isai naga ramar nan dakikayi kamar ba wannan damuwan bane kawai anya uktiee tafada tana sake rike dariyar zaro ido oum tayi tace anya mi? Babu komai rufaidarh tace sannan tace ko dai aydarh zaa wa kanni ko kanwa ban sani bah hararar wasa oum ta ballawa rufaidarh tace saidai ke idan kin amince da doctor Ahmad sai kiyi mata amma nikam badani ba dariya rufaidarh tayi tace uhm ni kwana biyu ma ya hakuri ko waya bama yi oum tace ai laifinki shi pa gani yake kamar takura maki yakeyi shiru

rufaidarh tayi domin bata shirya kare kanta wajan oum ba kan korafin ta kan doctor Ahmad din,oum tace uktiee nagani nake lokaci bai gudu kamar komai bazai faru a ya uba gyara zama rufaidarh tayi ta kamo hannun oum tace ki kwantar da hankalinki uktiee in sha Allah Komai zai tafi daidai karar ringtone din wayanta ke tashi tana dubawa taga abba ne da number shi ta Nigeria that means sunyi landing kyarma jikinta yakama kirjinta na lukude yana dugan tara tara cikin sanyin da jikinta yayi ta amsa wayar tamkar mai jin bacci ko wace take fama da kasala kuma agajiye sallama tayi daga can ya amsa tareda sanar da ita yana airport basai tazo ba tabar driver yataho kawai ya daukeshi da tau ta amsa tare mikewa tsaye duk wani nutsuwa ta, ta tanema ta rasa sai kai kawo take har rufaidarh ta fadawa drive sakon ta dawo oum ta tsaye zaunar da ita rufaidarh tayi tace uktiee ki nutsu ki kwantar da hankalinki nasan abba aydarh bai daukar komai dasauki amma in sha Allah abunda mu ka saka ma ranmu shima shine hukuncin shi Allah yasa uktiee Allah ya amince Ameen rufaidarh tace sannan tawuce kitchen domin karasa girkin da suke ita oum da kansu domin abba bayace girkin kowa idan ba na oum ba inhar yana kasar.
Zama hajajju tayi tace am audul tashi zakayi ka dauke ni da ada mu tafi can gidan naku ai Ibrahin nan koh? Kallonta malik keyi ko kiftawa babu yace wacece haka? Sake daure fuska hajajju tayi wai ita ala dole taci serious tace zaka tashi ko sai na zab zabga ma mari,aydarh sam bata fahimtar su zufa ke tsatsafu mata a goshi da hanci zuwa yanzu har tayi ja ba karamin dauriya take ba amma marar kamar zata fito tsananin azabar da take mata duk baaba kulu na lura da yanayin ta cikin sanyin murya tace Aseeyarh ta shi ki bisu ki bashi key din motar naki ku tafi can gidan su sai ki karbi sakon ki wuce gida tau kawai aydarh tace tareda mikewa tabar key din kan kujera domin bazata iya mika mashi ba da hannunta bacin bazata iya driving da kanta ba kuma rufaidarh tace mata da ta karbo maganin shikenan ba amma da babu abunda zai sa tabar su ,su shiga motan ta ba ganin key din da tabari kan kujera yasa baaba dauka tamikawa malik bai ce komai ba yakarba yayi gaba shima.Bayan fitar malik da aydarh hajajju tayi kasa da murya tace yaya muna fita kema ki rufe wannan kurkukun ki tafi can gidan habibun zuwa yanzu ya sauka ku jirani acan kar ku damu zanyi komai kan tsari in sha Allah baaba tace tareda zama tana jiran tashin motar su sannan itama ta shirya tafita, back sit ta bude ta shiga tana hade rai ganin yanda yake wani shan kamshi yana wani isa trash shine abunda tace can kasa yanda babu wanda ma zai ji ta hajajju tafito da wata katuwar jikka da uban mayafi ta bude front sit ta hakimce sai daurewa take babu wanda ta tan kamawa cikin su shidai malik bai ce mata Komai ba duk da ya lura da daurewar da hajajjun keyi cikin kwarewa nutsuwa kamala yake driving

yanda motar tayi fitting dinshi kana iya rantsewa kace tasa ce har suka isa anguwarsu babu wanda yayi magana cikin su ukun bin anguwar da kallo aydarh tayi kusan iri day ace da anguwarsu baabarh sai dai wannan gidan yafi gidan baabarh girma da kadan ko Parking bai gama ba hajajju tasako ta bude baya tace ma aydarh tasako ahankali aydarh tasako yau kam angama da rayuwarta zuciyarta har dace take ganin irin anguyoyin da oum tasaka ta zuwa a yau din gani take tamkar rashin aldalci ne mahaifiyarta tayi mata,hajajju ta katse mata tunani lokacin dake cewa malik tau dan cifil sifense kazama ba'a sani ba komai kawani tokare jikin kofa kamar wani rubabbe ba zaka kwankwasa a abude manah ba shidai kallonta yake he was speechless ganin lokaci daya hajajju ta juye tana ta masifa kamar ba ita tagama wasa da dariya ba dazo,knocking yayi halime ta bude.

Halime ta bude ganin hajajju tsaye kamar wata yar wrestling sai faman hura hanci take yasa ta washe baki tace yau tsofaffin kano ne a yola kenan?wata muguwar harara hajajju ta watsawa halime tace yau dai anbani muna ganin jafa'I kala kala bacin maganar da dan uwanki ya kwaso sai kin tsaya a kaina kina kallona kamar wata rubabba, shidai malik kallon hajajju yake sam ya gaza fahimtar abunda hajajju ke nufi to waye dan uwan nasu shi ko wa?to mi yayi? Kama hannun aydarh hajajju tayi suka shiga gidan aydarh sai bin ta take da kallo suna shiga hajajju tasaki aydarh,Ta fadi kasa kamar mai aljannu ta dinga kwarara ihu kamar wata tababba da sauri ummi da abby suka fito daga cikin daki suna kallon sarautar Allah ummi dai takasa cewa hajajju komai sai kallon aydarh take da mamaki domin har abada bazata taba mance fuskar da kamanin oum ba ko tayi rantsuwa babu batun kaffara wannan jinin habib da zarah ce to amma miya kawo ta gidan wannan wacce kala sabuwar kaddarar ce takasa ba kanta amsar ko wace tambaya a ciki yasa ta mara wa abby baya suka doshi inda hajajju ke ta zabga ihu tana kuka, mun shiga uku mun lalace wannan wace kalar rayuwa ce ibrahin kana zaman zamanka an yayo ma jafa'I an yayo ma bala'I ,abby was shock har kusan 5 mins abby da ummi na kallonta babu wanda yayi kokarin hanata domin sun kasa fahimtar komai sun shiga matukar rudani ganin aydarh da hajajju a gidan ga kuma malik tsaye ya zuba hannu a aljihu yana kallon ikon Allah,halime maryam da aysha suma duk sun tsore babu wanda yasan abunda ke faruwa sai kallon aydarh suke lokaci daya suka ji tayi mugun shiga ransu.shiru hajajju tayi ta goge idonta tass ta kalli abby tace ai batsaye za kuyi kamar matattu ba shiryawa zakuyi mu tafi aje asan yarda za muji da wannan bala'in ummi tayi karfin halin cewa hajajju mike faru ne? Shiru hajajju tayi sannan tayi mitsi mitsi da ido tace idan mukaje can kwa ji komai ,abby yayi ma ummi alamar datayi shiru sannan ya juya ya shiga daki

binshi ummi tayi domin kaf ji take hankalinta da tunaninta baza su iya daukar duk abunda ke faruwa ba ,ajiyar zuciya abby yayi cikin sanyi murya yace Aseiyarh kisaka hijab dinki mu bi hajajju domin ni kaina a cikin rudani nake.Tafiya suke cikin mota babu wanda ke magana cikin su biyar din sai hajajju dake ta rusa kuka babu sararawa wallahi daza'a bude zuciya aydarh ji take kamar zata mutu wannan wasan kwaikwayon yayi mata yawa a kai daga karban magani sai wahalan da rayuwarta ake what's all this? Hajajju tayi shiru tace tau ada yazaki barmu munata walagigi kan hanya bazaki gaya manah anguwar ba ?aydarh da bata fahimce tambayar da hajajju tayi mata ba tunda suka shigo motar da abby da ummi ta saukar da kanta kasa takasa hada ido dasu gabanta cigaba da faduwa yake sosai batasan dalili ba ga ciwon maran nata kamar kara karuwa yake tunda tafarawa malik kwatancan gidansu gaban abby ya yanke yafadi gidan habib? Shine tambayar dayayi wa hajajju shiru hajajju tayi kamar bata ji shi ba ummi dai kamar bata cikin motar tsabar yanda hankalinta yakasa kwanciya da tafiyar tarasa yanayi da zata saka Lamarin jujuya maganar hajajju take , tsaki malik yayi cikin ranshi yace wai wannan wace kalar yarinya ce komai nata kamar ba mutun ba who is she yasake jan dogon tsaki kasa da murya hajajju tayi tace Allah na tuba wannan abu dami yayi kama ibrahin ni bakina ma yayi nauyi wajan fadin wannan masifar sai kuma tasake fashewa da kuka,duk yanda aydarh ke faman riqe ciki tana zufa duk da sanyin a.c na kadawa ummi na lura da yanayinta kallo daya tayi mata tagane tabbas itace to amma mike faruwa ?mike shirin faruwa ? Wannan wane irin rikitaccan al'amari ne mai wuyar fassarawa yah rabbi kasa duk abunda zai faru yazama alkhairi tafada tana lumshe ido , sannu shine kalmar da ummi tacewa aydarh duk da bata gaishe su bata ko daga ido takalle su ba amma wani irin yanayi ummi taji game da ita lokaci daya yarinya ta kwanta mata rai,gyada kai aydarh tayi batareda ta amsa ummi ba still kanta na kasa bata dago ba abby da hankalinshi sam bai jikinshi sam bai ga abunda yafaru ba kuma bai ma kalli aydarh ba balle yasan wacece tunda bama sanin nata yayi ba.

Welcome sir tafada cikin sanyi da kuma raunin murya hugging dinta yayi sosai dukkansu ajiyar zuciya suka dinga saukewa zuciyoyinsu na musayyar bugawa kamshin jikinsu dana fatarsu na aikawa kowa sako cikin su ahankali ya zare ta daga cikin jikinshi yazaunar da ita kan sofa dake bedroom din nashi wanda yanayi bedroom din kamar show room shima kan sofa ya zauna tareda jawo ta ya kwantar da kanta akan shoulder dinsa yana shafa sumar kanta ta cikin Jersey veil din da tayane kanta dashi ,Zarahhhhhh yanda yaja sunanta sai da gabanta yafadi bata amsa ba sai ma kara riqe hannunshi

datayi sake maimaita sunanta yayi yace zuciyata na bani akwai abunda ke faruwa wanda kike boye mun cikin sauri ta dago kanta ta zuba mashi ido kallonta yayi yace yes zarah akwai abunda ke faruwa kuma kin barni a cikin duhu girgiza kai tayi cikin sauri tana kokarin tsayar da hawayanta tace babu komai abban baby idan ma akwai ni kaina bansan ta yarda zan fara ma bayani ba kallonta yake ko kiftawa babu yace zarahhhhhhhh da dan karfi saukar da kanta kasa tayi batareda tayi magana ba zuciyarta bugawa take da sauri numfashin ta tsananta fita yake yah rabbi kaine mai kowa yah rabbi kaine mai komai yah rahaman ka gyara al'amarin nan shidai abba kallonta kawai yake ba haka yasaba ganinta ba duk sanda yayi tafiya yadawo ba yasaba riskar ta cikin walwala da annushuwar ganin shi wannan karon kuma tamkar ma bata da lapia tamkar wacce ke cikin matsananciyar damuwa da takura duk ta rame tayi haske asalin kyauwun fuskarta yasake fito tarr kamar lokacin da take shekarun kuruciyarta to mike faruwa? Mike shirin faruwa?shi kanshi yanajin wani yanayi na daban inalilahi waina illahil rajiun shine kalmar dayake maimaitawa a zuciyarshi yarasa gane kan oum sam duk yanda yaso ya lallashi ta amma abun yace tura kuka kawai take mai tsananin ban tausai zuwa yanzu hankalin shi yagama tashi yarasa ta idan zai fara mikewa yayi tsaye tareda kwantar da ita flat kan sofa yayi hanyar kofa da sallama yashiga parlor part din oum wanda yasan anan ne zai tarar da rufaidarh ko daya shigo bai ganta ba ya tambaye oum tana ina bata bashi amsa ba as well ya tambayeta ina aydarh nan ma tayi shiru sai aikin kuka take mashi duk da tasan duk dunia babu abunda ke daga masa hankali irin ganin hawayanta shi kanshi bai san iya adadin son dakewa zarah ba amma he knows that words will never enough to express his feelings on her,Mikewa tsaye rufaidarh tayi tare da fadadda fara 'ar fuskarta tace ah masha Allah yallabai sannu dazuwa ya hanya anzo lapia? Duk tambayar da take mashi bai amsa kallon baabah dake sallarh kawai yakeyi zuwa yanzu kuma bai masan yanayin da zai kamanta abunda ke faruwa ba zama yayi cikin daya daga cikin cushion din parlor yana amsawa rufaidarh gaisuwar da tayi mashi yana tambayar su yasuke lapia lau alhamdulilah daga nan babu wanda sake magana cikin,zama yayi har baaba ta karasa sallarh murmushi tayi domin rabon data ganshi kila anyi 15yrs sam habib wani kalar mutun ne wanda shine tushe kuma shine silar faruwar komai a ahalin baki daya babu yabo babu fallasa suka gaisa duk da ba karamin nauyi da kunyar baabar ya keji ba shi kanshi yasan duk abunda ke faruwa amma sam bai damu ba shirune yabiyo bayan gaisawar dasukayi da abban kowa da yake sakawa a ranshi.
Nikam adda aysha wai wacece wannan wadda suke tareda hajajju da yah malik? Naga duk a tare mu ka gansu koh tau amma adda mike faruwa ne

hajajju na ta kuka kuma naga ummi da abby sun bisu tareda yah malik , ajiyar zuciya aysha tasauke tace dan Allah ku rabo dani kawai kuyi adduar Allah yasa komai lafiya Ameen suka amsa can maryam tace nikam daman na kara ganin ta ta burgeni Sosai ta iya gayu wallahi kallonta halime tayi tace nima haka wallahi aysha dai murmushi kawai take so take ta tuna idan tasan fuskar amma takasa.
Wata irin zabura hajajju tayi gani gidan dasuka kazo da sauri ta kalli malik sannan ta juya ta kalli aydarh tace inalilahi waina illahil rajiun yau naga abunda ya isheni bai ishe Allahnah nan kuma ina ne jama'a ? Babu wanda ya tanka mata cikin su aydarh har wani ajiyar zuciya ta sauke ganin sun dawo gida kamar kan kaya take a cikinsu duk da babu wani datti ko alamar wahala a tattare dasu amma sam ta kasa nutsuwa cikin su cilla motar yayi cikin gidan yana mai tambayar kanshi tau miya faru miyasa zasu zo gidansu? Babu mai bashi amsar tambayar shi har ya paka motar cikin jerin motocin dake jere a parking space din aydarh da kamar jira take dasauri ta fita daga cikin motar kamar jira take tafita marar ta tawani irin murda har sai da ta saki siririyar kara dasauri ummi tace subhanallah tare da rike ta,wani irin murmushi hajajju tayi tace tau riketa mu karasa still malik bai fito daga motar ba yana ta kallon ikon Allah shi kam yau mamaki kala kala yake Sha, tsawa hajajju ta daka masa tace kai da baza ka fito ba hala wani abu yasami kafar ta ka ? Shidai bai ce mata komai ba yasa kafa yafito daga motar ya mara masu baya yana bin tsarin gidan da kallo tsaki yaja ganin yar ummi ke ta lallaba yarinyar kamar kwai itakuma sai wani narkewa take kamar wacce ke ciwon mutuwa. Wani irin harbawa zuciya abba tayi iya gigita ya gigita cikin wani irin yanayi yake binsu da kallo musamman malik dayake iya ganin zallar tsananin kamarsu dashi Abby yakasa saka kafarshi ma cikin parlor wani irin iska ke kada duk illahirin jikin shi wani sanyi ke ratsa zuciyarshi da ruhin shi,hajajju takaraso tane mi kujera ta zauna kusa da baaba da oum rufaidarh ma karasawa tayi ta taho da ummi dake rike da aydarh ganin yarda ta tsaya tsaye kamar babu numfashi a jikinta tsabar yanayin da ta shiga still bata saki aydarh ba ahaka suka zauna itama aydarh bata nemi hakan ba domin wata nutsuwa ke bin jikinta har cikin veins dinta wani sanyi ke ratsawa duk abunan abba bai lura da aydarh dake jikin ummi ba oum kau tun shigowar su tazuba masu ido tana jin wani rahama ta ko 'ina to mi hajajju tayi haka dayasa komai ya cika tamkar gaske? Hannu abba ya daga yana nuna abby cikin rawar murya da tsoro yake furta ya..y...yarh ya...y..yarh kaine ko idona ne daman yayah kana adamawa har yanzu? Malik dake kallon su tamkar idonshi zasu fado yarasa gane kan komai hankalinshi da tunaninshi baki daya sun gaza fahimtar komai anan tsaye yake ko zama yakasa haka shima abby a tsaye yake yana

jinjina girman da kuma ikon Allah wacce kaddara ke son tadawo baya wacce gaskia ke son bayanna kanta ashe suna da rabon sake ganin juna a duniyar nan Duk da yasha mafarkin hakan kuma kullun cikin ba ummi kwarin gwiwar faruwar hakan yake amma sam baiyi tunani yanzu ba baiyi tunanin kwana ku saba,Mikewa tsaye hajajju tayi tare da gyaran murya tace duk ku tsaya kowa sai wani gwale gwalan ido yakeyi ku da ko abunda yakawo mu nan din baayi ba har kun fara wani yan sane sane ku zauna kuji abunda yatara mu nan kafin ku cigaba da wannan ya tunane tunane ahtau ku tsaya kuji jafa'in da yaran ku suka kwaso zama sukayi kowa na mamakin maganganunta cikin abby da abba da ummi baki dayansu ta daure masu kai wasu yaran nasu?oum dai kanta na kasa itama rufaidarh haka while baaba hajajju take kallo tareda yi mata alamar datayi shiru ita zatayi magana dasauri hajajju tafashe da kuka tace aaa yayah wllh aaa dole nayi magana ki daina hanani dole nayi magana kowa ita yake kallo cikin su,kafin takira sunan abba tace habibu kaga wannan sai sannan abba yakalli direction din ummi da aydarh da hajajju ke nuna mashi, nagani hajajju kiyi magana manah kin sani a duhu mitsi mitsi da ido hajajju tayi tareda gyara zama tace tau tunda ga farko har karshe zan zayyana duk abunda yafaru domin niba'a munafurci dani ba oum kadai ba hatta rufaidarh da baaba saidai da hankalinsu ya tashi sun san halin hajajju tsaf zata iya watsa duk wani shiri nasu ta fadi gaskia amma kau da sunyi dana sanin involving dinta a case din sake fashewa da kuka tayi cikin muryar dattako abby dasai yanzu yayi magana tunda suka shiga yace hajiya kamata yayi kuyi magana ba ku dinga kuka ba duk kun bar mu a cikin duhu wani abu ya farune mutuwa akayi ko mai? Yoo Allah na tuba ibrahin ba kwara mutuwa ba da zagin da yaran nan suke shirin jawo manah.

Jawo manah ba still dakin babu wanda yayi magana kowa kallon hajajju yake banda rufaidarh oum da baaba da gaban su ke ta lugude hantar cikinsu na kadawa jiran jin abunda hajajju za tace, suke. tana matsar kwalla Takai 5mins ahaka sai tayi kasa da murya tace tau Alhamdulilah haka naso kuma haka na bukata mu hadu baki daya pameli domin mu yanke hukunci tare na'am shine abunda abby yace tare da gyara zama yana kallon hajajju gyaran murya tayi "tace tau saidai fa kuyi hakuri ita zuciya bata da kashi yara ne ka haife su baka haifi halinsu zamani ne yazo da haka habibu mai mace kuma kullun mai mace shi ake cuta kai zaka lallaba ka rufawa kanka da rayuwar ka asiri ka zubda makaman yakinka ka bada hadin kai abba dai bace komai duk a birkice yake sauraran bayanan hajajju, "sai kuma ta kalli abby tayi kasa da murya tace kai kuma sai ka goye bayan gaskia kayi adalci "zuwa yanzu jikin abby yagama yin sanyi yace in sha Allah hajajju zan

zamo mai adalci a duk hukunci da zaa yanke,wayar ta fiddo daga cikin katuwar jikkarta keypad ce anyi mata mugun daure da rubber bands bugu daya tayi aka daga sannan tace bismillah ku shigo,within 2mins sai ga salma da doctor ashraff sun shigo gaishe da kowa na parlor sukayi sannan doctor ashraff yafara magana cikin nutsuwa Alhaji ayi hakuri I didn't wish abubuwa su zo ahaka I have no other option but to spared the truth a min afuwa cikin tsawa abba yace doctor just talk "daidai ta nutsuwar shi doctor ashraff yayi yace last week nayi ma aydarh medical checkups abunda nagani ba karamin daga mun hankali yayi ba nasamu salma nayi mata bayanin komai duk cikinmu babu wanda yasan abun yi yasa muka sami hajia rufaidarh da maganar da kuma ita oum, will you just go straight to the point doctor shiru doctor yayi can yace am sorry sir but I found out aydarh is pregnant for almost two months wani irin zabura aydarh tayi kanta nawani irin juyewa tasan abunda yake nufi tasan mi kalmar ke nufi da yare kala kala da turanci hausa larabci da kuma fulanci,malik kau tsaki yayi a ranshi daman yasan wannan yarinya salihan cin karya take (nikau nace kabari rabo yazo kanka) Ummi ta rike ta sosai ganin yarda tayi din. Da wani irin mugun speed abba ya mike tsaye yayi ma doctor ashraff wani irin mugun kallo yace did you know what you just said doctor kasan abunda ka fadi kuwa? Baby? This is serious ina tunanin baka san waka ke magana kai ba girgiza kai doctor ashraff yayi yace nasan abunda nake fadi ga result din ma ka duba sir yafada yana fiddo paper daga pocket din suit dinshi ya mikawa abba hannu na rawa abba yakarbi takardar ya bude kallo daya yayi ma paper ya maida ta kan kujera banda yana namiji yanada karfin zuciya da tuni zuciyarshi ta buga maganar da hajajju tayi yasa shi dawowa daga shock din daya shiga "tace tau ai komai yazo da sauki tunda cikin ba rayayye bane Allah yakarbi abinshi yanzu haka ibrahin kafin mu zo gidan naka daga asibiti muke nida yarinya dashi uban cikin audul gashi nan zaune ya sadda kai kamar wani waliyye alhalin shine mai laifin, da wani irin duba ummi ta kalli hajajju domin bata ma gane abunda take fadi ba malik uban dan as how? Ganin haka yasa hajajju cewa kwarai da gaske asiya audul shine uban cikin dan ya gantalle yau kuma ga shaida nan naga ke ma kika rike yarinyar kamar kinsan danki yacuce ta ya zalinceta! da zaa auna jinin ummi kila yakai trillion 100 wannan wacce irin kaddara ce wannan wani sabon bala'In ne ya kunno kai inalilahi waina illahil rajiun adduar samun sauki daga wurin ubangiji kawai ummi ke domin dakin juya mata take komai biyu biyu take gani and still yanda take rike da aydarh bata sake taba duk da yanzu kusan hali daya suka shiga ita da aydarh ,kokowa aydarh tashiga yi da numfashin ta alamar asthma ta ke nima tashi " tunda yazo dunia bai taba shiga tashin hankalin da yashiga yau ba bai masan yanayin dazai fassara kanshi ba

shidai yasan rabi rai rabi mutuwa haka yake ji, wasu irin hawaye masu zafi ke sauka daga.

Idon abby bai taba tunani faruwar komai ta haka ba bai taba kawo ma ranshi malik zai aikata abu irin haka bai san adadin lokacin da ya dauka ba zuciya sa na juya zancan hankalin sa ya gaza auna lamarin ji yake kamar mafarki ko almara ABDOOLMALIK ne yayi ma wata ciki watan ma diyar dan uwanshi uwa daya uba daya wanda duk duniya su biyu iyayansu kawai suka haifa “son zuciya da kuma son duniya irin na dan uwan nasa yaraba su da juna tsawan shekara ashirin da biyu wannan wacce irin kaddara ce mike shirin faruwa da rayuwar su? Oum kau wani irin ajiyar zuciya ta sauke rufe idonta tayi ruf tana jiran ji karashan zaman, ummi da har yanzu bata dawo daidai ba ji take kamar duk duniya babu wanda ake jarabta kamar ita ashe kuka rahama ne ashe,ashe wani lokaci dadi ke sa ayi kuka . Hajajju tace tau nan da kuke ta wani yan kuke kuke abunda dai yafaru ya riga faru kuma dai iyakar yamu yamu kawai muka sani kunga kwara asan yarda zaayi kafin wasu rubabbun su sani su samu a bakin duniya yanzu ma fita day ace tattara su a hadasu “AURE”kalmar auran da tafito daga bakin hajajju sai yazamo tamkar wani miki ne ta famo a azuciyar ummi harbawa zuciyar tayi tana barazanar fitowa waje bazata zamo marar aldaci ba bazata so kanta da zuciyarta ba ko itace a wannan matsayin da wani yayi wa yar ciki karshan hukunci da zata yanke mashi kenan shiyasa taji wani kalar yanayi farin ciki ko bakin ciki (bakin cikin dai)ba karamin karfin hali abba yayi ba wajan sauraran maganganun su bai taba tunanin abu mai haka da wannan ba zai faru a rayuwarshi ashe duk wayon ka duk dabarar ka Sai Allah ya jarabceka mutanan dayayi nisa dasu mutanan dayayi kaura daga rayuwarsu mutanan daya binne gaskiar dangantaka tsakanin su ashe zanan gudun kaddara su atare suke ashe gudun kaddara guzirin iske ta ne inalilahi waina illahil rajiun zufar dake keto masa tamkar yana cikin oven tamkar bai taba shiga inuwa ba,aydarh dake ma salma wani irin kallo hawaye ke zuba a idonta sosai ko da bata taba tunanin salma da doctor ashraff zasuyi mata abu irin haka ba kuma da wanda ma batasan ko waye ba kuka take sosai a jikin ummi, oum tamike ta nufi abba ta durkusa ta rike kafanshi cikin kuka “tace abban aydarh kar son zuciya ya rude ka kasa zatar da hunkunci ka dubi rayuwar ka ka dubi rayuwarmu ka yi abunda musulunci yace tunda har bataji kunyar yi manah haka nima a matsayin mahaifiyarta na yafe ta wani irin kuka ta fashe dashi ,dasauri hajajju ta mike tace aaa zara’u yoo Allah natuba babu katon da ya isa hana wannan mutuman auran yarinyar nan sai kuma tayi kasa da murya tace tau tunda bai ji kunyar taba masu diya ba mu ma ai bamu jin kunyar aurar masa da ita,malik ya mike tsaye yana girgiza

kai yace enough hajajju ya isa haka mi nayi maki dakike kokari bata rayuwa ta mi nayi maki da kika zabi yi mun wannan sharrin ?’wani wawan mari abby ya dauke shi dashi kamar jira ummi take ta taro shi ta dayan side din cikin kuka ummi tace wallahi duk duniya idan gatanka ne sai ka aure yarinyar nan mugu azzalumi marar tsoron Allah indai ni ce mahaifiyarka sai ka aure yarinyar dabas ta zauna kasa ta fara wani irin kuka,zuwa yanzu aydarh mutuwar ta kawai take jira ciki! Aure! Kalaman da suka zautar da tunaninta bin kowa take da kallo domin batasan abun fadi bakoo abun yi sauraran yanda numfashi ta ke fita da yarda zuciyarta ke over racing kawai take.Baaba tace kuyi hakuri shi daman duk yanda bawa ke kokarin gujewa kaddararshi sai ta riski shi wannan wani ikon ne daga Allah wayau ko dabarar bazata iya kwatar mu ba daga rubutatciyar kaddara ba “Don haka a matsayi na na babba a kaf ahalin nan nake umartar ku da kuyi hakuri ku hadda auran yaran nan ya yanzu kuma a take! Abba daya lula duniyar tunani sai yanzu ya dago kai ya zubawa aydarh ido kallonta yake irin kallon kin ban kunya kinbani mamaki,aydarh da bata fahimtar komai batasan ma irin kallon da abban ke mata ba,Abby yayi gyaran murya yace habib ina neman alfarma ka yafewa abdool abunda yayi na biyu ka yarda mu hada auran su suyi nesa damu domin ganin su a kusa damu ba karamin ciwo zai jawa zuciyoyin mu ba musamman kai abby ya karasa maganar yana Kafe abba da waennan manya idanun nashi,har ga Allah lokaci daya abba yaji ba aure ba komai ya cancanci yayiwa aydarh bai taba tunanin zatayi mashi wannan tabon ba kuma ma a mutanan daya dauka mafi kaskantatu a rayuwar shi mutanan daya guda saboda a ganinshi abun kunyarshi ne yayi kudi kuma mutane su sam asalinshi talaka bane tsawon shekara 22 ba taba tunanin akwai ranar da zasu dawo rayuwarshi ba,mikewa tsaye yayi yace ni Alhaji habib nabawa yaron wurinka auran Aseeyarh akan sadaki mafi kankanci sannan matsayi na mahaifinta na yafe ta har…. Dasauri baaba tace aaa habibu kar ka karasa hakan ma ya isa zasuyi nesa daga gareku in sha Allah har sai zuciyoyin ku sunyi sanyi,Abby ya fiddo 20k daga aljihun shi ya mikawa rufaidarh yace taba aydarh sadakin ta ne sannan ta kira limamin massalacin gidan yazama waliyyin aydarh! .cikin yan mutunan liman yakara so aka farad uk wani abunda musulunci ya shar’anta kafin daurin aure gaban duk wanda ke parlor aka daura auran ABDOOLMALIK IBRAHIM MAIDO DA ASEEYA HABIB MAIDO kan sadaki naira dubu ashirin wani irin sanyayan ajiyar zuciya oum tasauke bata taba tunanin abun zai faru duk yanda suka shirya ba hajajju kau wani irin arna smile tayi irin boss din nan rufaidarh kau ga farin ciki ga tausai dukka sun hade mata ,salma dai kanta na kasa.Doctor ashraff yayi bankwana yatafi abba bai jira komai ba ya mike yanufi part dinshi oum ta bishi da ido tasan yau akwai aikin lallashi koma

miye mai sauki ne tasan yarda zata saita mijinta abby ma godiya yayi wa oum ya sake bata hakuri kan abunda yafaru yayi mata sallama yafita,ahankali ummi tamike ta rike hannu aydarh da still takasa tsayawa tsaye tace mungode fatima Allah yayi albarka oum itama godia tayiwa ummi ta bisu da ido zuciyarta na tsinkewa aydarh kau da batasan duk abunda ke faruwa ba sai bin su take kamar status da sauri rufaidarh ta mara musu baya domin yi musu rakiya hajajju ma jikkarta ta diba tana cewa oum zuwa gobe zata zo ta karasa hutun nata anan,wata irin faduwa aydarh da jiri ke kwasarta tayi daidai kofar fita parlor oum na ganin haka ta juya dasauri tay hanyar part dinta kukan dake cin ranta na kufcewa dasauri ummi tayi kanta ganin yarda ta fadi kamar ba rai tsawa tayi wa malik tace yadauke su tafi “kamar bazai tabata ba ya dai daure ya dauke ta yanufi hanyar waje hajajju ta gwalo ido ta kalli rufaidarh tace anya kau ba mutuwa tayi ba?rufaidarh tashare hawayenta tace aa hajajju ina tunani rudun da tashiga ne in sha Allah zata tashi tau Allah yasa dai mudai bara mutafi sai kuma tayi kasa da murya tace yau dan dole kawai zai sa na kwana wannan kuturun gida na ibrahin gashi audul din dake siyo man abubuwan da bazaa rasaba yau ko bindiga aka bashi ni zai harba yoo Allah natuba daga taimako sai abu yadawo kai na shi hwa taimakon shi nayi dana sa aka bashi yarinyar ita dai rufaidarh kallon hajajju kawai take batayi magana ba dasauri hajajju ta bi bayan ummi. Babu yarda rufaidarh batayi ba su bari driver ya mayar dasu abby yace babu komai sun gode zasu samu dan sahu, hajajju da bata so haka ba tayi mitsi mitsi da ido tace kai kuji tababbe tau a ina kaga alamar dan sahu anan anguwar salon aganmu cikin dan sahu kamar wasu yan iska ace manah mayu yan kwakwa munzo maula kamar wasu zararru ina dalili da kyar dai aka shawo kan hajajju suka samu napep suka tafi ummi da abby suka shiga daya Malik dake dauke da aydarh kamar baby a kirji wanda riqe ta dayayi yanayin shi ya chanza bai fahimce komai abun dunia ya taru yayi mashi yawa tare suka shiga da hajajju,fuskar nan tashi kamar hadari dinki tsab idonshi kamar zaiyi aman wuta turaranta ya takurawa rayuwar shi. Assalam babyn habeebe’s nace bara na gaya muku ina yan mata? Ina haddadun mata?ina manya mata?ina yan gayu? Da zawarawa baki daya nesa ta zo kusa kina neman musulmin turare mai kamshin rahama turare mai musulmin kamshi wanda zai sa duk idan kikaje a kalli ki domin kamshin shi cikin nutsuwa yake fita tau nesa tazo kusa come one ☝ come all to real scent perfumes nake gaya muku karshan kamshi ake magana just dm me and purchased yours ☺muna da air fresheners masu kamshin oud

Turaranta ya takurawa rayuwar shi, hajajju ta kauda fuska tace uhm “ tau banda ma neman bala’I irin na ibrahin mi yayi zafi daga wannan dan abun sai ya danna maka auran yarinya “tayi kasa da murya tace tau wai da kake ta wani daura fuska kamar wani afta mi zakayi aure ne an riga an cuce ka an Baka ma yarinya ,ga yarinya kuma ba lafiyaya ba , Allah na tuba ita kuma asiya ta dauka da zafi tasaka gaba da masifa kamar wani dan iska shidai malik bai ce komai ba domin bai ma da abun cewa , hajajju tace ohh dan ka daukeni zararra ina ta magana kayi shiru kana ta bina da ido kamar wata tababba Still malik was quite da tasan yanda yakeji da bata dameshi da wannan surutun nata ba marar kan gado ba da tasan yarda yake ji datayi shiru, har suka sauka gida hajajju na mashi masifa wai tana magana yayi mata shiru, suka sukayi abby ya biya masu keken kudinsu ko gida bai shiga ba ya wuce masallaci ba lokacin sallarh bane amma yana bukatar dayaje ko yasamu nutsuwa ‘ko kallon shi ummi batayi batace ya wuce ya kai aydarh dakinta aysha da su halime kallon ikon Allah kawai suke sun rasa abunda ke faruwa Yarinyar da suka zo dazo da hajajju ce tau ya akayi yayansu ya dauke ta miye hadani su da ita dazo ta shigo da kafanta yanzu kuma an kawo ta? Basu san wanda zasu tambaya ba hakan ya sa suka zubawa ikon Allah ido , ummi da still idonta ke jawur ta kalli aysha tace daura man ruwan zafi yanzu ta sa kai tashiga dakin kan gado ya kwantar da aydarh har yanzu kuma bata bude ido ba! Ummi ta cire hijabinta ta linke ajiyar zuciya ta sauke har yanzu bata gama dawowa daga shock din da ta shiga ba abu ne wanda ya faru tamkar a flim lalle Allah abun tsoro ne shike juya alamari a duk yarda ya so ,ahankali taje kusa da aydarh tana kare mata kallo batasan sanda murmushi ya kufce mata ba hawaye ke zuba a idonta tana kallon yarinya wani irin kaunar ta ke bin duk wani sashen jikin ummin bata so hukunci ya kasance hadda na nesa dasu da abby yace ba amma babu yarda zatayi dole tabari a nuna masu kuskuran su dole taba zuciyarta hakuri a hukunta malik din. Ahankali take buda idonta kanta yayi mata nauyi sosai jikinta kamar ba nata ba zuwa yanzu tafara jin sassaucin ciwon da maran ke mata,wata irin ajiyar zuciya tasauke tana tuno yarda komai yafaru gata kuma a wani daki na daban wani irin azababban kuka tafashe dashi da sauri ummi ta riketa kallonta take batasan ta inda zata fara mata magana shiru tayi tana kallonta , kuka kawai take har sai da ummi ta lura da yarda take wahalar da kanta ga numfashin ta na janyewa yasa ta fara lallashinta yau ne karo na farko da ta zauna da wata mace babba bayan oum da rufaidarh kuma yau ne karo na farko dataji tanajin masifar nauyi da kuma kunyar wata hallitta batasan miyasa ba batasan ya akayi ba yi shiru kawai da ummi ta ce mata sai taji kamar wani abu aka hura mata a zuciya. Zuwa yanzu tagama saddakar da kanta tagama sallama ma rayuwa bata dawani saurin

gata ba abbanta ba oum ba auntie rufaidarh babu salma Komai kallonshi take bako a rayuwarta duk yanda tak'I gidajan talakawa duk yarda take kyamar gidaje irin haka wannan sam bataji komai game dashi bata ma da nutsuwar fahimtar komai , da sallama aysha tashigo tana kallon aydarh ita dai aydarh ko sanin shigowar aysha ma batayi ba,aysha tace ummi nagama " ki zuba a bocket ki kawo shi toilet din dakin nan da to aysha ta amsa sannan ta fita. Ummi ta taimaka mata tayi wanka domin sam jikinta ba kwari bata da kayan da zata chanza kuma ka'idan ta ne idan tayi wanka ba ta mayar da kayan da ta cire ,ummi takalle ta tace al'ada kike? Sunkuyar da kanta kasa tayi domin bata fahimce abunda ummi tace ba ganin hakan yasa ummi cewa mp kike ? Ahankali ta gyadawa ummi kai batareda da tace komai ba ta share hawayan dake zuba a idonta, mamaki ne yakama ummi period kuma? Mi zai kawo mata period yanzu a halinta da take ciki wannan wani alamari ne mai wuyar ganewa? Duk iya tunani ummi takasa gane komai hakan yasa ta mikewa ta fita. Hajajju tayi shiru tace wllh kun dai ji tau Allah na tuba ai daman abunda yadace ayi masu kenan a kori yan banza daga cikin mu baki daya nan da shekara hamsin haka sai su dawo,aysha was so confused the three of them are speechless kallon hajajju kawai suke babu ko dauke ido can halime tamike tace yanzu hajajju kun yarda duk anyi hakan gaskia yayah bazai wannan abun ba,hajajju ta kankace ido tace minene kuma yayah tau shi audul din wanene zaayi mashi sharri kai kuji wata rubabba nan tau dan uwwaki haka akayi yanzu haka anbaka masu aure kuma ance su kwasa subar cikin mu,Allah sarki audul ko wacce duniyar zai kwashe ta su shiga oho ta karasa maganar tana tafa hannu,ni tsorona Allah tsorona karsu shiga cikin mutane ayi tunanin daga wata kasar aka watsu su ahtau yara kamar su aka tara ma kenn dunia to kila daga ni sai su dai akayi ma wannan kyautar , Maryam dai so take kawai taje wajan aydarh bakaramin dadi taji bai to amma taga su aysha da halime duk sun wani damu duk da babu dadi amma ai ance cikin ya bare kuma ma har an daura masu aure babu wanda yasan ma da zancan cikin haushin ta daya da akace wai zasu tafi subar Adamawa tau ina zasu,daga haka babu wanda yasake magana cikinsu hajajju kwanciya tayi taba su baya "ummi tace tau tsayawa zanyi jiranki bazakiyi sauri ki kira shi ba? Da sauri halime tayi hanyar dakin malik,shiga tayi ta iske shi kwance idonshi a rufe ahankali tace yayah yayah yayah har sai da takira shi sau uku sannan ya bude runanni idonshi ya zuba mata su sai data tsorata ganin shi ahaka sannan tace ummi nakira ka bata jira amsar shi tafita domin tasan bazai ma amsa din ba. Da sallama yashiga dakin kasa hada ido yayi da ummi itama ummin bata kalleshi ba kallo daya yayi ma aydarh dake kwance cikin bargo ta nade kamar wata baby tsaki yayi ya dauke ido still ummi bata kalleshi ba kuma

batayi mashi magana ba “can tace bakin layi zakaje kasiyo mata pants biyu da sanitary guda daya kasan maganin daya dace da ita ai daga haka bata sake kallon inda yake ba ta dauke ido domin wani irin zafi da quna take ji da har wai ta haifi dan dazai iya cin zarafin mace inalilahi waina illahil rajiun! Har yanzu maganar na mata yawo a kai babu wani adalci ko rahama da malik din yacancanta daga gareta shiyasa har kagara take gari yawaye ya dauke aydarh su tafi ko taji sauki da sassauci har ga Allah har cikin ranta take son yarinya har cikin ranta take tausayinta ba karamin mamaki abun ke bata daga malik din har aydarh babu wanda yayi kama da abunda akace sun aikata din amma miye dalilin waenda suka bada shaida akan abun nayi musu sharri bata ga dalilin yin hakan ba shiyasa ko tana so ko bata so sai ta amince ko kadan bata ga laifin aydarh batasan babu abunda ya isa yayi forcing malik ya aikata abunda baiyi niyya babu kudi ko mutanan dasuka isa su sa shi yin abunda baiyi niyya ba, wani irin haushi da daci take ji kan abunda malik din yayi.shagon yashiga suka gaisa sama sama daman kuma wannan halinshi ne sam bai dasakin fuska saboda baya son raini 2k ne kaf kudin shi bai san nawa kayan suke ba hakan yasa shi yin shiru yana nazari kafin yace Malam musa dan Allah pants nake so na mata guda biyu sai sanitary pad kwara daya shi kanshi wani irin nauyi da kunya yaji sadda yayi maganar shidai kam yaga rayuwa baya siyin irin waennan abubuwan ,, su aysha na tambayar shi kudi sometimes idan yana da shi zai basu da kansu su fito bakin layin su siya yana iya cewa tun dayayi wayau bai taba,taba pants ko pad na mata ba ,washe baki malam musa yayi yace tau malam abdul yanzu kam in sha Allah amma sai naga kamar wani abu nadamunka ko ,cikin tsare gida malik ya girgiza kai yace babu komai sauri nake packing malam musa yayi mashi ya lissafa mashi kudin 1500 ne daidai 2k yamika mashi yabashi chanjin 500h sai da yatsaya chemist nan ma tunani yafara yi wani magani zai siyan mata hasashe yayi kawai yafadi wanda zaa bashi yasiya yafito. Yana shiga ya iske hajajju da abby zaune a tabarma da alama magana suke suna ganinshi sukayi shiru kanshi na kasa ya wuce dakin shi maryam ce a dakin ta na gyara mika mata ledar yayi yace takai ma ummi amsa tayi ta wuce dakin ummin,”sadda tashiga ummi na toilet sai aydarh kawai da yanzu a zaune take ta jingina bayan ta da karfen gado kallonta maryam tayi,tayi murmushi tace mata hello tayi tana mata waving hannu ,ahankali aydarh ta daga ido komai ciwo yake mata a jikinta bata masan abunda take ji yanzu haka bai dan aka cemata zuciyarta ta goce daga kirjinta bazatayi gardama ba cikin sanyin murya dakuma muryar da taci kuka tace mata hey , batayi niyyar amsawa ba domin bama halinta bane magana da mutane amma sai taji sam bazata iya kyale maryam din ba can kasa da murya maryam tace you are damn cute sis ‘ kalma ce wanda bayau

bane ba farko bata masan ranar da za’a daina gaya mata hakan ba murmushi tayi kadan wanda bai nuna ba domin bazaka iya gane cewa baki ya motsa ba a murmushin, Maryam tace ina ummi? Shiru aydarh tayi yanzu domin tagaji da surutun maryam din kafin tasake wata tambayar ummi tafito daga toilet , ummi gashi inji yayah yace na kawo maki amsa tayi batareda tace komai ba “”maryam tace ummi anan zata zauna? Wani irin kallo ummi tayi wa Maryam daya sata fita da sauri daga dakin (masu sunan mu pah Akwai tambaya da surutu) ASEEYA tashi ki shiga sai kin chanza bara na kawo maki Abinci karba aydarh tayi kanta na kasa ta wuce toilet din fess yake bawani dirty white broken tiles ne a toilet din aydarh dai sai kallon karamin toilet din take tana mamaki sai data bata 30 mins a bayin tana sake gyara jikinta zuwa yanzu jirin da take ji ya ragu saidai abunda baa rasa ba, ummi tashigo rike da plate din abinci da pure water biyu a plate ta ajeye gaban aydarh tace mata bismillah kici abinci sai ki sha magani ki kwanta, kallon abincin da ummi ta miko mata tayi spaghetti ce da kifi sai ganye sai kamshi abinci yake karba tayi ta ajeye domin bata jin zata iya ci ba wai saboda abinci ba aaa saboda halin datake ciki ne. Fita ummi tayi har tadawo dakin abincin na yarda yake , aydarh kuma yanzu a kwance take wani side daban take kallo da alamar har yanzu bata hayacinta wani irin tausan ta yakama ummi har ruwan kwalla ya taru a idonta dasauri tashare, cikin dattako tace ASEEYA kitashi kici abincin sai ki sha magani Nakoshi aydarh tace,”aaaa Aseeya ki daure ki ci sai ki sha magani kinji; ummi ta taimaka mata tazauna ko five spoons batayi ta ture tace ma ummi ta koshi amai zatayi idan ta sake ci kuma, hakan ma yayi ummi tace tareda ballar mata maganin ta bata.Duk wani kala take ji domin da pant din har pad bata san su ba batasan company pad din ba (daman yazaki sanshi irin namu ne na yaku bayi) pant din ma tasan bak alar company data ke using bane domin wannan yayi mata wani kala (ai pah yanzu maganar company yakare 😂😭) ganin damuwar datake ciki and yanzu ba ma ta wannan take ba so take tasan su waye waennan mutane hajajju kawai tasani a cikinsu amma dazo kafin hankalinta ya gushe taji abba nace yan uwa wannan shine damuwar ta dakuma sanin dalilin salma da Doctor ashraff nayi mata haka, bata san amsar duk tambayoyin ta bah akan yasa ta zame ta kwanta ta rufe ido. Hajajju tace wai ibrahin wane gari zaka kadasu wannan rashin tsoron Allah har ina? Abby yace rashin tsoron Allah hajiya rashin tsoron Allah fa kuka ce tau hajiya shi bai ji tsoron Allah ba ya aikata abunda yake so sa ini ne zan ji tsoron Allah wajen hukunta shi duk garin daza shi ma yatafi ban damu ba hajiya shi yaja ma kanshi! Hajajju takalli ummi da kanta ke kasa sannan tace kuma fa da gaskiar ka ibrahin tunda bai ji kunyar dauko ma magana ba kaima karka ji kunyar hukunta shi kwara suyi nesa damu idan

hankalin kowa ya kwanta sai su dawo still ummi batayi magana ba domin bata da abun cewa komai akayi ma malik din a ganin ta daidai ne domin shi yaja wa kanshi! Abby yayi gyaran murya yace gobe zasu bar garin su tafi duk idan yayi masu daga ya tashi ya fice daga gidan, hajajju kalli ummi tace ahhh asiya wai daman haka ibrahin din yazama ko dai duk talaucin ne ahtau talauci manah dan ka daka haifa kake kora kamar wani kare daga shaidan yayi mai kirari anya ibrahin mai taamalli da kwayoyi da ko kuma dai kila yana bankar wiwi? Ummi dai batace komai ta tashiga ta wuce kitchen ta turo kofar so take tayi ma aydarh abu mai ruwa wa wanda zai mata dadi a baki yakuma gasa mata ciki already akwai grind groundnut a wani clean white bocket dauko shi tayi ta daura ruwan zafi a kan murhun gawayin da ke kunne, jin ta a kitchen yasa aysha shigowa kitchen din tace ummi ki kawo bara nakarasa maki aaa ummi tace zatayi da kanta basa jayayya ko musu da ummi abby dakuma malik hakan yasata bar ma ummi aikin tacigaba da tsayuwa dai so take ta yi magana da ummi ganin yanayin ummin yasata jan bakinta tayi shiru.40mins ta dauka wajan yi ma aydarh kunun gyadar da yaji madara mai kyau ta garri yayi haske da kyau sosai kasancewar ummin ba baya bace wajan iya girki a flasks ta juye shi saboda tasan ko ta kaiwa aydarh yanzu bazata iya sha ba, a cup ta zuba ta mikawa aysha tace ta kai ma hajajju, sannan ta turo maryam da halime su karbo mata cat fish,

Wani irin sanyanya kamshi ke fita daga jikinta wata simple Turkish abaya ce white a jikinta ta cusa sumar kanta dake nata kamshin dinaar oily tasks a cikin siririn mayafin abayar babu komai a fuskar ta sai Expensive powder da take amfani sai kajal da lips shinner wallahi baza ka taba cewa oum tayi 30 yrs ba balle ka kira mata 39 dayake shekarunta idan ana neman real definition of gayu aji,tsari” tau oum ce shiyasa babu abunda aydarh tabaro daga gayun oum sai ma karawa datayi, Ahankali ta tura kofar bedroom din kamshin ta kawai ya saukar mashi da nutsuwa kuma yasanar mashi da iso warta waya yake amsawa kuma still ganinta bai hanashi cigaba da magana a wayar ba kusan 10mins da shigowar ta bai aje wayar ba kuma alamu sun nuna mata kamar wani horo yake mata ta hakan tasan ranshi a bace yake shiyasa zatayi duk yarda zatayi ta boye ta ta damuwar tayi maganin tashi,kasa cigaba da juriya tayi idonta yakawo kwalla,fadawa jikinshi tayi tareda zare wayar ta kashe tafashe wani irin kuka ta kankameshi kamar wani zai kwace mata abban shima hakan ne wani sanyi yaji da rahama yakasa yin komai yakasa lallashin ta kanta kawai ya iya shafawa duk girman laifi ko abunda oum zatayi mashi bai ga ranar da zai iya yin fushin da zai kasa kallonta ba hade.

Hade bakinsu oum tayi ta bashi wani irin passionately kiss he can’t hold it but to kisses her back kusan 3mins suna ahaka kafin yadago ya rike fuskanta yace zarah! Dan faduwa gabanta yayi cikin sanyin jiki ta dago kai ta zuba mashi raunanin idonta hannunta yakama yace zarah! Miyasa kika zabi yi mun haka? miyasa kika zabi boye mun komai zarah why?? Zarah kina ina abubuwa duk suka faru ahaka zarah kina ina har aka samu wani ya ketare iyaka kina ina har wani ya ci zarafin aydarh? Hawaye ke zuba a idon oum ba karamin tausayin abba taji ba ko ita da tashirya komai gabanta yankewa yake yana faduwa duk sanda ta tuno faruwar alamarin! Kayi hakuri zawjjjjjj kayi hakuri yah roohi am critical sorry ABBANARH ban san tayarda zan fara kare kaina ba bansan ta inda zan fara ma bayani ba “shiru tayi tana mashi wani irin kallo har cikin veins din shi yake jin kallon “lumshe idonshi yayi ya bude yace zarah ya akaiyi aydarh tasan yaron can ya akaiyi iyalan ibrahim suka dawo rayuwar mu bayan shekara 22 da barin su rayuwarmu,tafiyar wata biyu kawai nayi abubuwa suka dame haka ;ciki fa aydarh kuma inalilahi waina illahil rajiun hawaye abban keyi ,bakaramin tashi hankalin oum yayi abunda bata saba gani bane gamai da abban kwantar da kanshi yayi a kirjin oum yanda yakeji a ranshi tamkar an zare mashi wani hope na rayuwa ya tsora ta da dunia ya tsorata da rayuwa ashe babu karyar dake dadewa a rufe ashe duk iyakar ginin da aka ginawa gaskia guguwar kaddara na iya rushe shi , Allah shine masanin daidai Allah shi ke iko da zartar da komai a duk yarda yaso hakika sai yau yake ganin iya kuskuran dayayi a rayuwa babu abunda oum bata gaya mashi kan abunda ya aikata tayi kukan tayi rokon tayi fushin amma sam abba yayi kunnan uwar shegu da ita,tun kan halin aydarh oum ke fama dashi amma sam bai taba kawo wa oum gaskia take gaya mashi ba,cikin su babu wanda ke da abun fada kowa da abunda yake sakawa a ranshi.still yana kan kirjinta shafa mashi kai take har bacci yasamu nasarar daukanshi jin yanayin ajiyan zuciyarshi ta sauya yasa oum fahimtar bacci yadauke shi,ahankali ta kwantar dashi kan gadon tareda rufe shi da duvet zuba masa ido tayi tana kallonshi ko zatayi karya kan komai banda soyayyar dake wa habib wani irin so take mashi wanda ita kanta basan adadin shi ba , har yanzu kallon yarinya yake mata ko dawasa bai taba hada ta dawata mace ba a rayuwarshi duk girman kai izza wulakanci dakuma isa ta abba idan yana gabanta komawa yake tamkar yaro ganin yarda yake bacci da alama sam baya jin dadin shi yasata zare veil din da ta daure kanta ta ajiye kwanciya tayi saman gadon itama ta shigewa jikin shi.

7:35 daidai ummi ta kammala pepperoni catfish din da kewa aydarh yaji kayan kamshi sosai sai kamshi yake a warmer ta juye mata shi ta kwashe

sauran a plate ta hada da bread aka mikawa hajajju, hajajju dai sai kallon ikon Allah take can takalli aysha dake warware mata ledar bread din tayi kasa da murya tace ahhh gaskia a Lamarin asiya akwai gyara mamadin ta tayi ma ita yarinyar horon yunwa shine ta dage ta rasa inda zata tsoma rayuwarta tun dazo ta daura waccan ta sauke waccan an mayarda gida kamar rastaurans Ahh tau mu dai ba ruwanmu iyaka a dafa a debar manah namu rabon ahtau aysha batace komai ba har tagama warware mata bread din ta ajiye ta tashi bin bayan aysha da harara hajajju tayi tana kallon maryam,tace duk cikin su naga ke kadai ce kawai ba tababba ba ,hala a mutanan gidan akwai mai sasirikat din hauka Allah natuba bai dan ba zararru ba kana magana kowa ya dinga ma shiru, dariya kawai maryam keyi batace komai ba tace tau minene wani sasirikat? Certificate fa ake cewa kuma ma naga ke ina ruwanki ba an dafa an baki kinci ba miye wani abun complain ? Hajajju dai abunda ke gabanta tacigaba da ci bata sake bin ta kan maryam ba. Ummi tace zauna ahankali ASEEYA ki daure ki ci ko kadan ne bayan spaghetti din nan dakikayi cokali biyar babu abunda fa kika ci aydarh dai kanta na kasa bata sha’awar cin komai domin cikinta ma cunkushe yake can ummi tabude flasks din ta tsiyaya kunun a cup tamikawa aydarh karba aydarh tayi Still bata sha ba sai kallon kunun take ummi tace daure ki sha zaki ji dadin jikin ki, ahankali ta kafa cup din a bakinta tayi sipping kunun har cikin ranta taji zafin kunun yayi mata dadi Sosai a baki ba i ta ta ajiye ba har sai da tasha rabin cup kafin ta ture sannu ummi tayi mata tareda mika mata bowl din da ta zuba mata pepperoni a ciki shima dai bata ci dayawa ba ta ture, kallonta ummi keyi ko kiftawa babu da alama dai halinta ne na kin abinci bata takura mata ba da dole sa ta cinye ta rabu da ita, so take suyi magana so take ta fahimce wani abu daga bakin aydarh amma bata san taya ba a ganinta yakamata a bar aydarh ta huta da taso mata maganar amma idan tayi shiru kila wannan ne dama nakarshe dazata sake samun irin wannan lokacin ita da aydarh hakan yasa ummi fara magana cikin hikima da dattako tace ASEEYA! Aydarh bata dago ba kanta na kasa kuma bata amsa ba ummi na lura da ita a wunin dasukayi tare ta fuskance abubuwa da dama daga halin aydarh, “”hakan yasa ummi cigaba da magana “” bansan kaddarar da ke sake bibiyar rayuwarmu ba basan ta yarda komai yafaru ba a wannan karon kila wannan ce hanyar da muka jima muna addua akai,a kullun adduar mu shine daidaito da kuma gyaruwar tarwatsewar da ahalinmu yayi ,sai sannan aydarh ta dago kai ta kalli oum dasauri kuma ta mayar da kanta kasa wani irin nauyi da kunyar ummin take ji,ganin abunda datayi yasa ummi kamo hannunta tace Allah shike kaddara duk abunda zai faru da bawa tun kafin fitowar shi daga cikin-cikin mahaifiyar shi duk abunda yafaru yau da ma wanda zai faru har abada yana

cikin littafin rayuwarmu,wani birkitacan alamari ne mai wuyar fassarawa nayarda da kaddara nasan cewa wannan wani hanyar ce Allah ya billo manah dashi domin mu karyata tunaninmu da kanmu domin ya nuna manah iyakar mu akan zunubin da mahaifinki ya saka mu,mukuma mu kabada hadin kai wajan aiwatar dashi ZUMUNCI ba abun wasa bane amma ahaka muka sa kafa muka ruguza mafarkin kakanin ku! Hawaye ke zuba a idon ummi,share su tayi tacigaba dacewa ASEEYA nasan baki san suwaye mu ba a cikin mu bayan ABDOOLMALIK sai hajajju kawai kika sani, ni nice mahaifiyar ABDOOLMALIK Wanda kika ganmu tare shine mahaifin shi kuma yayan naki mahaifin uwa daya uba daya wani irin zabura aydarh tayi tareda mikewa tsaye hankali tashi tace yayan abbana kuma? Daman abbana ba da wani dan uwa? Zaunar da ita ummi tayi tace ki kwantar da hankalinki ASEEYA yanzu ba lokacin sanin komai bane na fada maki wannan maganar ne domin kinsan waye malik a wurinki domin ki san su waye mu, aydarh was shock and speechless at thesame time iyakar abubuwan da zasu firgita mata tunani ba wanda bata gani ba a yau har zuciyarta ma ta kai da bushewa ta riga da ta sallama komai na rayuwa a yau din nan shiru tayi kawai tana cigaba da sauraron ummi. Malik yayi shiru yana sauraron hajajju har takai aya tace tau sai kayi hakuri ka rungume kaddara ka yafe man amma kaji duk yarda akaiyi sannan ta fashe da kuka tace tau bacin ma ba kaunar Allah ni miye laifina dan matan can sun gaya man abunda kayi nikuma na gayawa ubanka an daura muku aure da yarinyar sai kuma tayi kasa da murya tace wai kau kaga kenn yarinyar da zaka dinga bakin rai kana irin wannan mugun abu dan Allah yataimake ka na shige maka gaba an baka auranta ? Yanzu taimako daya zanyi ma nagaya maka garin dazaka ku dinga istigifari Allah ya yafe muku,tashi yayi ya fita domin bazai iya cigaba da sauraron hajajju ba “daidai zai shiga daki yaga ummi tafito rike da hannun aydarh wace ke tafi ahankali tamkar bata son taka kasa, yarasa miya aiko ta cikin rayuwarshi ya rasa hadin kaddara da yahada shi da ita kalmar ciki yamaimaita a ranshi wai yayi mata ciki har ya zube an kuma daura masu aure a yanzu haka wai fa matar shi ce !! Da sauri yashige daki ganin ummi na kokarin juyuwa abunda bai sani ba shine tunda yafara kallon su ummi ta lura da shi . Shiga sukayi dakin hajajju tamike tsaye ta dafa kirji tace wacece wannan? Ummi dai tayi shiru ahankali ta zaunar da aydarh kan cushion din dake cikin dakin tace barka da dare , hajajju tayi shiru tayi kamar bataji ba tace tau waennan rubbbun dasuka samu gaba suna kwala manah idanun kamar larabawan daji bazaki sallamai su ba ki kirawo ibrahin da audul din ba? Fita su halime sukayi kafin ma ummi tayi masu magana malik tasa aysha takira mata sannan ta tafi dakanta kiran abby, tsaye yayi kamm bakin kofa ya sukunyar da kanshi kasa, can sai ga ummi tashigo abby

na biye da ita duk zama sukayi abby nama hajajju barka da dare fuskar nan tashi babu yabo babu fallasa kallo daya yayiwa aydarh yadauke ido takure take zaune a dakin kamar wata baby ta lafe jikin cushion din alamar zazzabi da kuma tasowar asthma dinta take ji daurewa kawai take amma ita kadai tasan halin da take ciki,hajajju takalli malik da kauda kai still a tsaye yake bai zauna bas ai kanshi da har yanzu na akasa “Tace ibrahin akwai wani bawan Allah can a kano a rimin auxunawa yake aikin gini yake shine nake rokon alfarma ka taimaka kabar audul ya dauke matar tashi su tafi can kano din yabashi aiki da dan kuturun gida su zauna suyi rayuwar su a can babu wanda yaji babu wanda yagani sai kuma tayi kasa da murya tace saidai ayi mai wonin kafin su tafi kar aje can yarabu da yar mutane a shiga uku saboda gaskia habibu ba yarda zaiyi ba wannan karon dai nasamu na tankwara shi ya hakuri da yanzu duk muna can muna zance da karkata kai a caji opus,bayan abby yagama sauraron hajajju tass sannan yace tau ba laifi hajiya ko 5 seconds bai kara ba ya tashi ya fita,hajajju ummi ta bishi da kallo , tarin da aydarh keyi ahankali yasa shi dagowa ya zuba mata lion eyes dinsa ko kiftawa babu wannan ne karon farko da ya tsaya yana kare mata kallo dasauri ummi ta nufeta tana mata sannu domin ganin yarda take rike kirjinta, hajajju tace tau nan daka tsaya kamar dan karota kana kare mata kallo baza ka iya taimaka manah da komai ba ko duk abunda kuka yi bai.

So babyn habeebe’kuna neman uniques turaran wuta,turaran dana kaya baki daya? Tau faduwa tazo daidai dazama □□come one come all to real scent ,haddadun mata,manya mata,yan mata da zawarawa baki daya kuzo mu hadaku ku dinga musulmin kamshi,kamshi marar tadda hankali kamshi mai kwantar da hankalin bawa and munada room fresheners masu kamshin oud just dm me and purchased urs ❤

Duk abunda kukayi bai ishe ku ba sai ka dinga zuba mata ido kana kallo shidai bai ce komai ba ya juya ya fita daga dakin, sannu ummi ke ta jera ma ta ba karamin tausayin ta ummin ke jib a tasan tunda take bata taba shiga irin wannan yanayin ba “taga kokarin yarinyar sosai, har tarin ya lafa hajajju na gefe tana wurga ido,can tace tau wai wannan wani irin tari ne ko daman bayan anyi bari tari na biyo baya? Ummi dai batace komai still tana kan aydarh ta jata jikinta tana shafa mata baya kusan 7mins kafin ummi takama hannunta suka koma dakin ummi, sannu ASEEYA kinada asthma ne? Gyada kai aydarh tayi batare da ta amsa ummin ba,gyara mata kwanciya ummi tayi still tana kallonta, addua tashafa mata kafin tashiga toilet ta dauro alwalla.
Kiran sallarh asuba yasa ta bude idonta ahankali tana bin fuskar abba da kallo,yatsanta daya ta daura kan lips dinshi tana zagayewa ahankali shima

yake buda idonshi har sai da ya bude su tarr a kanta wani irin cute smile tayi mashi shima ya mayar mata,batace mashi komai ba tayi hanyar toilet shima toilet din yashiga,tare sukayi wanka tareda dauro alwalla,sharp sharp oum tashirya shi cikin light blue jallabi zubin kasar sudan turare ta fesa mashi tareda da daukar pray mat ta bashi murmushi yayi yace Allah yasaka maki da alhamdulilah zarah , 3mins yakaishi mosque din dake cikin gidan “Bayan fitar abba cikin sauri oum ta gyara gadon dakin tareda daidai hasken dakin ,fita tayi zuwa dakinta na Part din abban towel din jikinta ta zare ta shafa cream din da take amfani dashi duk san da abba ke kasar few minutes ta dauka kafin ta saka hijabi ta kalle alkibila, tunda ta hau abun sallarh tunanin aydarh ya hanata sakat takasa sukuni tunanin halin da aydarh ta ke ciki kawai takeyi tasan babu abunda zai faru da ita ta hango tsananin sonta a idon ummi taga tsananin kaunarta a idon ummi da abby baki daya iya zaman da sukayi da ummi tana mutuniyar kirki ce tasan in sha Allah zata samu abunda take so daga wurin ummi da malik in sha Allah wannan shine silar kawo karshan komai bata san iyakar adadin kwanakin ba batasan iyakar adadin watannin ba batasan iyakar adadin shekarun ba amma tasan in sha Allah komai zai daidaitu in sha Allah. Hajajju ta matse kwala tace”yanzu ibrahin dama dai dagaske kake sai ka kada yaran nan sun bar garin? Abby dai na tsaye shigowar shi kenan daga masallaci yace ma ummi tasa aydarh ta shirya yanzu zasu tafi malik dai na tsaye kanshi a kasa he is out of control, he is out of mine bai san abunyi ba zuciyarshi ta dake ganin komai yake tamkar a mafarki bai san tunanin dazaiyi bai idan ma yace zaiyi tunanin wani abun zuciyarshi na iya fashewa.ummi ta kalli aydarh da ta fito wanka yanzu tace “ya kike jin jikin yanzu? Cikin sanyi murya tace Da sauki amma kaina na ciwo ta karasa muryarta na karyewa alamar kuka take son yi, ummi ta mike tsaye tafita daga dakin, tana fitowa hajajju ta bita da kallo ganin ta shiga kitchen yasa ta shiga kitchen din itama,har kasa ummi ta durkusa ta gaisheta, hajajju tace niba wannan ba yarinya nan haka zaa kadasu babu kaya babu ko tabarma kwanciya ke baki ga abun yayi Kamar ba kan gado ba? Ummi tace aaa ai naga idan yaje can aiki zaiyi sai ya siyan masu, ta maida hankalin ta kan tea din da take hadawa aydarh, hajajju dai ta juya ta fita tana magana kasa kasa, ummi tace sha sai ki sha maganin ,Kusan rabin cup tasha ummi ta kalli tace har ya isheki kuma naga baki ci bread din ba,”goge kwallarta tayi tace na koshi,maganin ummi ta ballar mata taba ta tasha.bude wardrobe ummi tayi tafido wata sabuwar hijab baby pink da sabon tirmin atampha tasaka cikin wata jikka tareda dayan pant din da malik ya siyo mata sai sauran pads dinta daya rage ta maida bag din ta rufe. Aysha tace ummi anya batayi mata kadan ba ummi dai batace komai tacigaba da daga

atamphar chiganvy ce sabowa dal dinki yayi masifar kyau free straight ce atamphar red anyi mata leafs da grey dinki aysha ne da akayi mata na saukar su da zaayi, grey din hijabi ta hada shima sabuwa na saukar taso,Maryam tace ummi wannan kayan pa sunyi mata kadan tafi adda jiki fita ummi tayi ta koma daki duk kansu suka bita da ido,halime tace ni wllh yah malik tausayi yake bani duk yazama wani kala,aysha ta sauki ajiyar zuciya tace ni kaina tausayin shi nake sosai yama kasa ko cin abinci pa ,Maryam na tsaye dai bata ce komai bas ai can tace adda wai ita wannan din nan bata magana ne komai? Aysha tace wai ke miye ruwanki da ita ne haba duk kin dame mu da ita zan bata maki rai fa maryam haba kibar mu,muji da abunda ke damun mu haba,halime tayi kasa da murya tace adda nima da haka zan ci maki wallahi ni so nake nafita muyi bankwana da ita tana birgeni sosai,aysha dai baki bude take kallonsu.Allahumma bareek shine kalmar da yafito daga bakin ummi lokacin da aydarh ta saka rigar tayi kyau sosai rigan yayi mugun karban ta cuteness body ta yafida shape cikin rigan, babu breast's cuff a rigar amma boobs dinta sun cure wuri daya masha Allah,"tadan fada kadan sai wani haske datayi sosai mai milky milky "karba hijabin tayi tasaka har yanzu jikinta babu kwari sam, Maryam tashigo ta kalli aydarh tace good morning auntie " aydarh kanta nakasa ta dago kadan tace morning " ummi ta kalli maryam tace linke wannan rigan ga kallabinta nan a gado rigar da tazo da ita ummi tasa maryam din linkewa tasaka a cikin bag din da ummi ta zubawa aydarh kayan.

Babu yabo babu fallasa ummi ta amsawa malik gaisuwar da yake mata ya risina kasa yace ummi nasa ko zan dafa Qurani taba yarda da babu abunda na aikata ba Amma ummi ina roqanki wannan alfarma ummi kar ki bari natafi batare da kin yafe man ummi babban musifa ce fushi gareni, tau nan dakikayi shiru kina kallonshi bazaki ce mashi komai ba? Abby da tuni domin yasan bazai iya jurar bankwana tsakanin su ba komai yake cikin karfin hali yakeyin shi kudi yadauka 20k yace hajajju ta ba malik din. "" ummi tace babu yafe tsakanina da kai abunda kayi! ABDOOLMALIK ga ASEEYA nan duniya da lahira batada kowa bayan kai a yanzu kai ne komai na rayuwarta duk ranar da ka zalince ta Allah ya isa ban yafe duk ranar dakayi tunanin rabuwa da ita kasa ma ranka baka da wata mahaifiya a duniyar nan girman amanar nan ,dana baka shine ticket din yafiyar da zanyi maka, ummi tajawo aydarh tace Allah yayi maki albarka ASEEYA , batasan dalili ba batasan ya akayi ba kawai tasamu kanta da fashewa da kukan da tarike na awa 24 har cikin ranshi yaji kuka yasa shi dago ido yazuba mata ganin yarda take kuka jikin ummi itama ummin hawaye ke bin kuncinta yasa shi shagala yana kallon su sosai aydarh ke kuka kamar zata

shide dakyar ummi ta lallashe ta,hajajju dai na gefe da katuwar jikkarta sai raba ido take tana kallonsu can tace Aaa gaskia asiya baki kaunar Allah ahtau bacin haka miye wani abun kama yarinya kuna ta wasu koke koke kamar wani ya mutu miye wani abun kama sirika kuna kuka kamar dai wasu marar sa alkibila nipah bana son wannan abun yaran kar su rasa mota a tasha ina jiya ibrahin yace duk abunda ake karfe bakwai su tarkata su tafi inda zasu , shine kika wani tsaya akansu kina wani zuba mashi umarni kamar dai wani yaro ita kuma bazakiyi mata nasihar ba tayi biyayyar aure? Ummi tayi shiru tana kallon hajajju, hajajju ta bude jikkarta ta fido kudin da abby yabata da wayarta tace tau ga wannan inji ibrahin, wannan kuma waya tace zaka ga ansa isah magini ka kwafi number kuna sauka kano ka kirashi kace kun sauka zamuyi waya dashi nayi mashi bayanin komai karba malik yayi ,yayi yarda hajajju tace masa, Maryam ta mika masa jikkarta da ummi ta hadawa aydarh hannu yasa ya amsa ya juya ya fita daga dakin hajajju ma takama hannun aydarh tace tau asiya nima daga can gidan habibu zan koma kinsan nabaro kano har abada tun ina can watse ba dangin uwa ba na uba, tunda wanda ya kaini yabar duniar ma baki, ummi dai batace Komai ba domin wani zafi take ji a zuciyarta bazata iya jure ganin tafiyar tasu ba. Har suka shigo tashar babu wanda yayi ma wani magana cikin su yau ne karo na biyu data shiga keke a rayuwarta.

Here is a piece of advice please □□

For you to blackmail someone it will not take you a time? Idan ke kin zubar da mutuncinki or something like that dole sai kinyi ma wata sharri? Mi za ku samu ko mi zaku karo dashi a yi ma wani sharri dan girman Allah? Ai wance yar iska wance bin maza take! Baku da wani shaida ko hujja amma duk idan kika zauna sai kin kira sunan wata kince tayi kaza ai kaza take, and bara na dawo kan matan aure wasu daga cikin su kenan ba kowa ba □ke sarkin kishi ke masipapa ai mijina take bi ai mijina take dating to hell with you and your miji , wallahi billahi idan nice wata ke bi mun miji bazan ma bari asani ba tau that means nayi lacking wani abu da har zan bari a san mijina natare da wata awaje,Da wai har wannan darajar take da mutunci igiyar auranki zaki tari yarinya a titi ki nemeta da fada da hayagaga .Bara kiji yar uwa ke daraja da mutuncin auranki zai bare a titi wata kila mijin ma yaji haushi kin fito kamar karya kina hauka a titi da auranshi kanki kinga duk matakin da ya dauka kanki ke kika sani,Dan Allah muji tsoron Allah mu daina blackmailing mutane saboda wani dalili namu na daba,Allah ya shiryamu yashirya manah zuri'a Ameen❤

Yaune karo na biyu a rayuwarta da tashiga keke, har sai da mai keken ya juyo yace“malan ko ba nan tashar ba? Sai sannan malik yasauka tare da maida duban shi kanta, idonta lumshe yake bakinta yayi pink yarr ya tattare wuri daya kamar bata da lapia, girgiza kai yayi sannan cikin wannan muryar tashi kamar boss yace sauko, bata bude idonta ba kuma bata sauko ba kallonta yake ko kiftawa babu baya son raini kowa yasan shi da wannan halin amma ya lura ita kamar girman kai gareta da raini ,bai sake maimaita mata ba har yagama daukar jikkarta da ummi tahada mata da tashi back bag din daya zuba kayanshi basu fi kala shidda ba, sallamar mai keken yayi sannan ya zagayo side dinta yasa hannu ya rike soft hand dinta da sauri ta bude idonta ta watsa su tarr a kanshi shima ita yake kallo ko kiftawa babu kaifin idonshi da kwarjinin shi yasa ta dauke nata idon tare da kokarin janye hannunta daga nashi ,duk da ba rokon kirki yayi mata ba amma tasaka kwarta hannun nata shima bai saki bah, har sai da suka zo gaban motar kano sannan ya rabu da hannun nata, wanda ke lodin motar malik yayi ma magana ya gaya masu garin dazasu ,washe baki yayi yace tau masha Allahu daman wajan mutun biyu kawai ya rage ku shiga sai a dau hanya, kallonta malik yayi sai bin tashar da dakallo take she never come across suchs place ko commercial market bata taba zuwa ba ,in taje super market ma tau wani karamin abu taje purchasing yawanci komai nata na order ne daga wani kasa, Bai ce mata komai ba still hannunta yakama suka shiga motar. Hajajju na kallon rufaidarh tace tau daman wannan kuturun gida na ibrahin ai bazan iya zama ba Allah na tuba, rufaidarh tayi murmushi tace hajajju ai gaki nan yanzu a nan din ko, hajajju tace niba wannan ba cikina babu komai kawo man kalaci nayi, fita rufaidarh tayi ta shiga kitchen oum na tsaye tana slicing fruits da murmushi rufaidarh tayi takalli oum tace,”yan mata ba zama miji nagari yau sai wani jin kanki kike oum tace shin ba dole ba sai kuma ta marairaice fuska tace har yanzu fa abun na damunshi wallahi ban san yarda zanyi ba rufaidarh ta dafa kafadar oum tace ki kwantar da hankalinki uktiee kiyi kokarin sa shi manta komai mu ma kanmu uktiee mu daina tunanin abun a ranmu, in sha Allah uktiee zanyi duk yanda kikace in sha Allah, few minutes suka dauke ta shirya komai a kan wani hadaddan tray komai na abba oum tsaye take kanshi. Cup din shayi rufaidarh tahadawa hajajju ga irish plate guda tayi mata fraying 5 eggs da uban bread hajajju dai sai zufa take hadawa can ta kalli rufaidarh tace yaran nan fa ko waya wannan babu ahannunsu bamu ma san idan zasu sauka a kano ba nikaina lambar wanda na bashi bansan ko mutumin na nan ba ko ya mutu daman dai ya jima yana jinya, tunda tafara magana rufaidarh ta zuba mata ido tana kallo, rufaidarh tace hajajju daman baki san mutunmin ba kika ce kin san sa? Hajajju tayi mitsi mitsi da ido tace tau nan dakika zuba man

waennan idanun naki kina kallona Kamar wadda tayi ma sarki karya fa, daga taimako sai abu yazama jafa’I ina nan naga saboda hankalin yaron ya kwanta yasa nace mashi akwai wanda zai tarar a can kanon koh? Rufaidarh dai tayi shiru batace komai domin so take baki daya su yakice tunanin aransu su bar addua da rokon Allahn dasukayi yayi aiki.
Wani irin numfashi ya shaka ya fesar sauyin yanayi sauyin rayuwa da rubutaciyar kaddarar dake kudin littafinsu komai ya fara daga yanzu , babu abunda ke mashi amsa kuwa a kunne irin maganar oum ta karshe, amanaci nabaka idan kaci ka manta dacewa kana da wata mahaifiya a duniyar nan. Nan take yaji wani irin kwarin gwiwa da karfin zuciya yayi tawakalli yayi imani da kaddararshi kuma yasa ma ranshi daukar wannan kaddarar,zuwa yanzu jikinta yayi weak da yawa ahankali take tafiya jiri taji yana kokarin debar ta kasan bishiyar dasu ke tsaye tayi luu zata fada cikin zafin nama ya taro ta,tafada jikinshi wuri ya nema yazauna Still tana jikin shi cikin wata irin raunannar murya tace sanyi nake ji , dasauri ya cire rigan sanyin jikinshi ya yafa mata,baisan ta inda zai fara ba baisan yarda zayi ba yana jin duk yanda take kankame jikinta saboda .

Saboda tsananin sanyin da take ji , yarasa makama da abunyi, cigaba da zuba mata ido yayi yana kallonta har sannan idonta na rufe bata ma san a jikin da take ba, Assalam matar tace cikin dan yin kasa da murya amsa mata sallaman malik yayi cikin wannan muryar tashi, cike da barikanci matar tace am tun cikin mota nake lura daku kamar batada lapia koh? Tunda tafara magana malik bai dago balle tasa ran zai kalleta har ya amsa, kara gyara tsayuwar ta tayi tace naga kuma Kamar baqi ne ko? wace anguwar zaku, ganin maganar nata yayi yawa yasa malik ce mata “ina zan samu chemists? Indai kemis ne bakada matsala akwai wani babban kilinik nan baya dan anguwarmu ne mai kilinik din, “ kallon aydarh yayi yaga yarda fuskar ta tayi wani sharr kamar batada jini lashes dinta sun tattare waje daya he can’t express how he feels on her shidai yasan baya jin haushin ta kuma shi dai yasan bata burgeshi rainin yarinya yayi yawa and the worst part ma taje tayi abun kunya an laqa masa sharrin da ma yakasa fassara abun sam karamin tsaki yayi azuciyarshi ahankali ya furta I will put common sense into your head idiot(miye abun zagi kuma 😂) gajiya tayi da tsayuwa can tace yallabai ko dai bakaji mi na fada ba? Sai sannan ya tuno da wanzuwar ta a gun, can yace ina ne clinic din? Washe baki tayi tace can babu nisa zata iya tafiya ko na kama ta, Ahankali yace bara na dauke jikkar sai ki taimaka ki kamatan mu je “ ahankali ta bude ido wani irin banzan kallo tayi masa shi da matar dayake cewa ta daga ta su tafi ai ko mutuwa zatayi sai dai ta mutu da dai wannan ta kama ta baisan iya adadin dauriyar

da take kenan ba bai san iya adadin karfin zuciyar datakeyi ba wajan duk abubunwa dake faruwa ba tasan babu yarda zatayi ,tasan bata da wani sauran gata a duniya shiyasa ta yarda da ummi lokaci daya taji wani irin kaunar ummin aranta,,”dasauri ta dauke idonta ganin shima ya zuba mata ido yana mata more than kallon datake masu shi da matar dake tsaye a kansu “ this is the second time da tayi abun da ya mugun bata masa rai a tafiyarsu baya son raini bai raina kanshi and yatsani mutun mai irin wannan halin “ cikin isa izza dakuma kwarjini irin nashi da dakakiyar muryar sa yace mata stand up and follow her! Wani irin abun ya tsarga mata a rai kamar tsoro shakka ko mai kenan batasan ya akai ba batasan mi akai ba samun kanta tayi da kokarin mikewa tsaye amma takasa kwata kwata jikinta kamar ba nata ba still kokarin ganin ma ta saisaita numfashin ta take amma ta gaza yin hakan, kamar jira matar take tayi karaf ta kamata, shi kuma malik ya dauki jikkar shi data ta yayi gaba, kamshin jikinta kawai matar ke shaka duk da ba normal turaranta ta fesa ba kuma ba ma kayan ta bane amma pefume din da skin scent din ta nan a jikinta. Wani karamin building suka shiga babu hayaniyar komai sai wasu few mutane dake zaune kan wasu rubber chairs da alama dai wajan reception ne wata nurse ce zaune kan kujera tana attending wani patient, tunda suka shigo ake binsu da kallo duk da wurin bai wuce mutun biyar ba amma hakan ba karamin damun malik yayi basai karamin tsaki yake saki, kowa kallonsu yake da mamaki basu saba ganin mutane irin su ba tau ko daga wata kasar suke oho “malik ya kalli matar ya dauke ido yace ina zan ga doctor? Kallon nurse din da ta saki baki ta maida hankalinta wajan kallon aydarh matar tayi tace ina dr ibrahin din yake marar lapia ce dashi baqi ne naga matar bata da lapia nace masa yazo mu kawo ta nan, murmushi nurse din tayi tace Allah sarki yana ciki yana duba wasu amma ku jira shi kadan, kallonta malik yayi yace it’s emergency asthma ke kokarin tashi ga jikinta is very weak can you talk to him? Tashi nurse din tayi ta nufi office din Doctor,:shiga tayi office din da sallama a bakinta wani matashi ne da bazai wuce shekarun malik ba ya amsa mata dogo ne baki da ka ganshi kaga very decent mutun, kallonta yayi yace is there any problem saratu? Yes sir wani ne ya kawo matarshi and it’s emergency shiyasa nashigo, okay muje “” fita sukayi lokacin malik na zaune yasaukar da kanshi kasa, aydarh dake zaune kan daya daga cikinsu kujerun itama nata idon a lumshe yake,matar da tarako su mai su na’ima itama zaune take tana ta kallon malik shi bai masan tanayi ba, taba shi doctor yayi sannan ya dago kanshi ya mike tsaye gaisawa sukayi “Doctor yace kai ka kawo patient din? Malik yace eh “Doctor yace wacece a cikinsu malik yanuna aydarh, nurse din tashiga da aydarh dakin da Doctor yana nuna mata, kusan 30 minutes kafin doctor yafito da murmushi ya kalli malik yace

bismillah muje office yallabai “Doctor ya kalli malik yace matar kace yallabai? Gyada kai malik yayi duk da yaji abun wani kala haka ya daure yace masa ehhh, Doctor yace bawani serious sickness bane kawai damuwa ce dakuma kamar akwai abunda yasa ta shock saboda yanayin ta ya nuna hakan ‘’shidai malik kallon Doctor yake yayi shiru Doctor yace nayi mata allurar bacci saboda mu samu tasamu nutsuwa tana bukatar hutu sosai ,malik yayi masa godiya kafin ya mike zai fita “har yakai bakin kofar Doctor yace yallabai idan badamuwa inda tambaya, malik yadawo ya zauna , Doctor yace amma yallabai ku baqi ne ko? AJiyar zuciya malik yayi ahankali cikin kamala yafara magana yace masa eh mu baki ne cus ban masan kowa a garin nan ba, Doctor yace Allah sarki , ina ne masaukin ku? Malik ya girgiza kai yace daga tasha sai nan kawai muka yo bamu kai da samun masauki ba, Doctor yace oh Allah ya bata lapia Ameen malik yace sannan ya mike yace ma Doctor zaiyi excusing kansa yayi sallarh akwain masallaci a kusa, tare da Doctor suka tafi har masallacin sai jan shi da fira Doctor yake shidai daga eh sai aa idan abun dariya ne yayi wannan miskilin murmushin nasa.

Sannu ya jikin? Na’ima tace mata , bata kaunar kallo ta lura kuma tun bayan farkawar ta daga bacci na’ima ke zuba ido tana kallonta duk sai taji ta uncomfortable pad din dake jikinta duk yabace batasan kuma yarda zatayi bak o wanda zata tambaya ba, ga wanka tana son kawa isai ji tayi hawaye na bin kuncinta, har yanzu gani take kamar a mafarki komai ke faruwa, har yanzu bata amsar tambayar na’ima ba kuma Still idon na’ima na kanta kamar tasamu t.v ganin tana hawaye yasa na’ima cewa asha kam sannu wallahi indai taipot ne haka yake mugun ciwo ne taipot wllh daurewa zakiyi ko maigidan naki zan kira maki ko kina bukatar wani abun bata jira amsar aydarh ba ta tashi tafita.”a office ta tarar da malik da Doctor ibrahim zuwa yanzu malik ya dan sake dashi suna fira akan abunda yashafi halin da kasar ke ciki , washe baki tayi tace sannunku yallabai ta farka naga kamar tana bukatar wani abu shiyasa nace bara nayi maka magana, Doctor ibrahim yace oh ta farka kenan, Bayan san son san halin da suke ciki hakan yasa shi daukar bags dinsu ya nufi dakin data ke ciki, can kasa yayi sallamar ko da hankalinta wajan yake ba lallai taji sa ba balle sam hankalinta baya tareda ita, cikin few seconds yakare mata kallo shekarun ta kwata kwata bazasu wuce na maryam autarsu ba amma sam yarda yanayi jikin su ba daya ba, jin alamar tsayuwar mutun akanta yasata dago idonta ta sace kallon shi batace mashi komai ba shima bai ce mata ba, kusan 10 minutes sunyi shiru babu mai magana sai celling fan dake nata aikin kawai ka ke jin sautin, duk ta takura ga wani irin fitsari da take ji kamar zai fito, ganin ba

tada mafita ga kunya takeji ta ce mashi tana son pad ko zatayi wanka, sai taji daman tayi ma na’ima maganar, kwata kwata tasan bakinta bama zai iya furta ma mutun kamar na’ima ko da kalma daya ce ba,duk ta zama abun tausai kallo daya zakayi mata kasan batada lapia ba karamin gayu da hutu suka samu muhalli da waje a jikinta ba real definition of beauty classy ce aydarh “kallonta kawai ya ishe ka jin wani abun a rai, still kanshi nakasa idonshi na rufe , kamar zatayi kuka muryar ta tamkar sarewa zallar shagwabar hallita da kuma gata dasuka samu mazauni a murya game da rashin sabo da kuka sanin ta yarda zata furta maganar, tace tau ai ummi ta hada mun kaya ,shiru tayi kuma kamar wace aka daka ta fashe da kuka, wallahi shi mamaki ma tabashi baisan ma mi zai ce mata ba amma ya jinjina zallar yarintar ta sai yanzu ma yakara fahimtar wannan tamkar raino ne ma aka bashi, bai ce mata komai kamar yarda itama ba tasake magana sai kukan da tacigaba dayi kasa kasa, daukar bag din yayi ya dire a gabanta sannan ya juya yafita, nurse din yayi ma magana ta shiga ta taimaka mata ta shirya.

Ahankali take shafa masa oily rublet hair din a kai kamar wacce ke shafa ma jariri abu haka take bi ahankali tana tafiyar da hannunta a sumar gently take rubbing mashi man, sanye take cikin wata mad dubai abaya yellow mai haske tayi matukar karbar jikinta sosai kanta babu kallabi sai wani hadaddan hair style da tayi akan,, kamshin jikinta dana jikinshi dana dakin baki daya hadin gwiwa da a.c dake fitar da kwantacan sanyi yahade wajan bada kamshi na musamman mai kwantar da hankali dasa nutsuwa, ahankali ya fesar da iska a bakin shi tareda tashi zaune ya maido ta zauna sosai kan cinyarshi, yadan fada kadan domin har yanzu da sauran tunani abun a ranshi duk da oum tana son mantar dashi komai amma yakasa ,cikin salihar murya cike da tausai kauna dakuma soyayya yace.

Yace zarah ina son mu bar Nigeria cus zamana a Nigeria zai haifar man da mumunan ciwo a zuciya na yakarasa maganar yana zuba mata idonshi, ajiyar zuciya oum ta sauke tareda yi ma kanta masauki a kirjin shi tace, babu damuwa abba “duk yarda kace haka zaayi bani da fahimta ni kaina duk abunda yafaru bada son raina ba,bansan ta yarda komai yafaru ba “Amma hakan na nuni da wani iko ne na ubangiji, wani darasi ne na rayuwar dakuma bayanar da gaskia da na shekara sama da 22 ina kokarin nuna ma,amma kayi watsi da hakan, shiru tayi tana sauraron yarda bugun zuciyarshi ke fita, kusan 3mins bai ce komai ba ahankali ta dago kanta tace Abba nasan bayan mu dasu yayah babu wanda yasan abunda yafaru mi zai hana ka fahimce gaskia mai zai hana ka gyara laifin da ka aikata baka ganin Allah ne yaso ka da rahama a faruwar wannan alamarin, tun anan dunia

yabaka damar gyara abunda ka aikata! Still Abba was quite sauraron ta kawai yake amma har cikin ranshi sam duk da faruwar wannan alamarin babu abunda ya chanza a zuciyar shi game da yayah ibrahim din da ahalin shi baki day abaya son duk wani labari ko tarihin da zai nuna tsohon asalin shi baya son alaqar da kuma zumunci da zai nuna yan'uwartakar su da abby sam yasa kafa yayi kwallo da alaqar dake tsakanin su yasa cleaner yayi cleaning tarihin da zai nuna asalin ko shi waye, tuni dunia tayi naam da shaharar shi a matsayin mai kudi dan mai kudi jikkan mai kudi kuma jinin mai kudi, tau taya suke tunanin zai iya fallasa gaskiyar tarihin sa?its unbelievable! Ita kanta oum shaida ce baya son abunda yashafi talauci baya kaunar sunan baya kaunar talaka duk abunda aydarh key i akan talaka duk hudubar shi ce duk tarbiyyar sa ce babu yarda oum ta iya said ai kallon ikon Allah, Kamar tasan abunda ke mashi yawo a kai kamar tasan abunda yake rayawa a zuciyarshi yasa ta cewa ABBANARH lokaci yayi dazaka…… da dan karfi ya kira sunanta zarahhhh bygone should be bygone please ! Daga karki sake yi man magana kalar wannan and get ready we are leaving tomorrow ! Bai jira amsarta ba yayi hanyar fita "oum ta bishi da kallo tana jin wani iri a zuciyarta , mike shirin faruwa?ta tambaye kanta duk wani efforts dinsu ita da rufaidarh yatafi a banza kenan? Inalilahi waina illahil rajiun shine kalmar da ta ambata a fili, wannan kuma wata sabuwar kaddarar ce ko mai? Wata zuciya ta gargadeta " lumshe ido tayi ta bude kafin tace yah rabbil alameen kace man burina yah rahaman kasa nayi nasara kan abunda na shirya yah arrahamar rahimin kasa malik yazamo garkuwa haske da kuma madubi a rayuwar aydarh ya rabbi ka bashi iko da juriyar daukar duk wani kuruciya da shirme nata, yah azeez kasan yarda nake son gyaruwar komai yah rabbil arshi kasa komai ya gyaru cikin hikima da dabarar ka yah Allah.

Nurse din ta sake kallon aydarh wannan karon kanta a kasa yake idonta rufe amma ba bacci take ba tayi wanka duk a takure take jin ta har wani kyankyanmin jikinta take ji (ah□abun naki yayi yawa aydarh) asalin abayar ta ce da tafito daga gida tun farko ta mayar domin tak'I mayarda wanda ta cire, ta fada sosai sai asalin kyauwun fuskarta yafito tarr gashin gabanta kanta yayi luff luff kasancewar veil din abayar da ta daure kanta yayi baya " can nurse din tace please can I asked you ma'am? Bude idonta tayi kamar bata taba kuka dasu ba wani irin haske da kyau garesu mai matukar daukar hankali da fizga, washe baki nurse Saratu tayi tace dan Allah daga Qatar kuke ko Egypt ni nakasa gane da yan wace kasar larabawan kukayi kama wallahi kunada mugun kyau ke da mijinki kai har kama ma kukeyi auran zumunci ne hala? Aydarh dai tayi shiru domin surutun nurse saratu ya dameta ko gane abunda take fada ma batayi,ganin aydarh bata amsa bay

asa nurse saratu tace ko dai ke bakya jin hausa amma naji shi mijin naki hausa raddam a bakinsa wallahi daman baya son yawan magana, still aydarh was quite ganin bazata amsa ta bay asa nurse saratu kama kanta tayi shiru tace mata zan fita idan kina bukatar wani abu sai ki kirawo ni bara nayi ma maigidan naki magana yasamu maki abunda zaki ci, daga haka ta juya ta fita, sai sannan aydarh ta bude ido tana bin dakin da kallo. Dr ibrahim yayi murmushi yace kai kam baka son magana sam sai muna labari sai ka fada tunani, ko dai duk halin da mai dakin naka ke ciki ke damun ka nagaya maka babu wani damu ko zuwa gobe ma zamuyi iya sallaman ku, dan murmushi malik yayi yace tau Allah yakaimu “nurse saratu ce tashigo da sallama office din cikin girmamawa takalli malik tace yallabai asamo ma madam abunda zata ci zuwa yanzu alluran sun sake ta nasan ta isa tafara jin yunwa, kallonta yay isai kuma yace tau a ina zan samu wurin siyarda abinci? Da sauri dr ibrahim yace aa abokina bara nayi waya yanzu a ba yaro yakawo muku daga gida “ kallonshi malik yayi zaiyi magana dr ibrahim ya girgiza kai yace aaa babu komai gidan ai babu nisa kuma ance bakon ka annabin ka duk da ba wajena kazo ba amma ai garin mu kazo, murmushi malik yayi tareda shafa sumar kansa yayi kasa da murya yace tau angode Allah yasaka, Ameen dr ibrahim yace tareda fido android phone dinshi yayi dialing contact din da yayi Saving da iya, bugu biyu aka daga cikin nutsuwa yayi sallama daga can bangaran aka amsa mashi yace iya idan rabi’ah na nan a bata abinci takawo mun yanzu, amsa mashi akayi sannan yayi godiya ya katse wayar, Ko 12mins ba ayi bas ai ga wata matashiyar yarinya kamar aysharsu tashigo da warmer abinci kwara biyu cikin leda sai jug da cups biyu a hannu, tana tsananin kama da dr ibrahim koba a fada maka bak asan sister shi ce ta kalli malik ta gaishe sa ya amsa ta, tace yaya ga abinci amsa yayi yace mata sannu, yauwa tace tana satar kallon malik dayayi kamar bai office din dan ko motsi bayayi, duk abunda take dr ibrahim na kallonta. Kallon malik yayi yace gashi sai kaje ku ci don kaima tunda kuka zo banga ka kai komai bakin ka bah, hannu yasa ya dauki kayan abinci yafita zuwa dakin da take. Bayan fitar malik rabi’ah takalli dr ibrahim tace yaya a ina kasan shi please? Wannan ba balarabe bane kam? Ibrahim ya kalleta yace aaa ba indiye ne karewa! Wait miye hadinki da shi? Girgiza kai tayi ta mike tace ni natafi sai ka taso “:bata jira amsar shi ba ta phecee daga office din yaraka bayanta da harara, bayan sun dawo sallarh malik ya kalli dr yace dan Allah a ina ake samun gidajan haya? Shiru Doctor yayi sai can yace idan ba damuwa akwai wani gida can kasan anguwar nan babu nisa gidan mai clinic din ne da a ciki yake zaune kafin a mayar dashi kaduna aiki compound ne sauran parts din akwai mutane wannan ne kawai babu idan ya tashi da yace nashiga na zauna baya son barin shi hakanan tau yanzu tunda ga ka sai

muje ka gani idan yayi maka, malik was speechless he is out of words tun haduwar shi da dr ibrahim yake masa kirki kala kala……..

Dr ibrahim yace zuwa gobe dasafe kafin a sallameta sai muje tare ka ga gidan daga nan din zuwa can 200 ake zuwa a keke, malik yace tau shknn Doctor Allah yakaimu nagode “ dr ibrahim yace babu komai yanzu lokacin tashi na yayi daman bama kwana a nan din mu uku ne kawai ke aiki a nan din sai shi mai clinic din da ai chemist ne sai kuma mayarda wurin clinic ,malik ya danyi murmushi zuwa yanzu har yasaba da surutun Doctor ibrahim din. Sai da yafara shiga dakin da aydarh ke kwance ya sake gwada bp ta kafin suyi sallama da malik nurse saratu da 8 tayi take tafi sai dayar ita Doctor ce ita kawai ke kwana itama ba kullun saidai in har akwai patient din da aka kwantar basu ma cika kwantar da mutane ba a clinic din, Akwai wadatacan haske a clinic din, da sallama mai gadin clinic din yashigo hannu shi rike da tabarma dakuma prayer mat sai bargo da pillow mikawa malik yayi dake zaune a reception ,” da mamaki malik ke bin mai gadi da kallo shima mai gadin kallon malik yake kamar yasamu t.v bai taba ganin mai irin Kamar shi a zahiri ba saidai a indian flim “ ganin yarda yake kallonshi ko kiftawa babu yasaki baki yasa malik mikewa tsaye, yace lafiya dai? Sai sannan mai gadin ya washe baki yace aaaa lafiya lau yallabai dakta ibrahim ne yace a kawo maku wannan hannu malik yasa yakarba yana jinjina kirki irin na Doctor ibrahim, mai gadin yace ina waje ranka ya dade idan akwai abunda ake bukata ayi man magana “ko rufe baki bai yi su kaji takon tafiya a bayansu mai gadin ne ya waiwaya yace ahh barka da zuwa dakta yanzu nake zancan ki a raina nace ko dai dakta ibrahim bai gaya maki da marar sa lafiya bam asu kwana “dan murmushi wacce yakira Doctor din tayi tace aaa ya fadamun ina hanya bana jin dadin jikina ne sam ,cikin jimami yace Asha kam Allah yabada lafiya,Ameen kawai tace tayi gaba ko kallonta malik baiyi ba ya kwashe kayan da Doctor ibrahim ya aiko masa yashige dakin. Ahankali ya tura dakin ta takure kanta waje daya bacci take amma a wahale da alama ma sanyin damuna da akeyi garin na damun ta domin ta kudundene kanta cikin hijabi kallonta yayi for few seconds yadauke kanshi ya ajiye kayan, bargon yasha jiki amma duk da haka fess yake a wanke sai kamshin klin yake “ warware shi yayi tass sannan ahankali ya matsa kusa da gadon karamin tsaki yasaki kafin yasa hannu gently ya kwashe hijabin, dasauri ya dauke kanshi ganin yarda zip din abayar jikinta ya dan bude har kana iya ganin whitest boobs dinta wanda skin din ke kamar madara har wani shining yake , tsaki yasaki a fili kafin ya yafa mata bargon “komawa yayi ya zauna kan rubber chair dake dakin yayi alkawarin mantawa da komai yayi alkawarin karbar kaddararshi shiyasa ko kadan baya son sake

tuna komai. Without making any sound ya buda warm din yana kallon abinci bazai iya tuna when last yaci abinci ba irin mutanan ne shi wanda sam basa wasa da cikin su amma yau gashi baya son ko kallon abinci, white rice ce da stew sai kifi cikin jug din kuma zobo ne still akwai ice a ciki batayi melting ba kadan yaci abincin ,yana tuna yarda take cin Abinci dazo kamar magani batayi three spoon ba ta aje, girgiza kanshi a ranshi yana tunanin ita din amanace a wajanshi ita din ticket ce ta yafiyar da mahaifiyarshi zatayi masa kan laifin da bai aikata ba “cike da kwarin gwiwa yayi ma kanshi alkawarin fuskantar sabuwar rayuwar shi da kuma gogaya tsakanin shi da kaddararshi.

Tabarmar ya shimfida yasaka pillow ya kwanta sam baya jin bacci amma wata irin gajiya ke tattare dashi, Almost thirty minutes yana ahaka idonshi rufe amma ba bacci yake ba,knocking kofar akayi ahankali yamike yace who’s that? Daga waje Doctor hafsa tace Doctor ce zan duba ko drip din yakare, “bude kofar yayi tareda bata hanya tashigo zata kai saar shi koma tafishi, ahankali tace ina wuni ya mai jikin? Lapia, da sauki kawai yace ya koma kan kujerar ya zauna ,duba drip din tayi taga still da saura, sannan ta dan yaye bargon kadan tashafa goshin aydarh taji temperature din jikinta normal normal kafin ta mayarda da bargon ta rufe ta, tunda Doctor hafsa tayi knocking ta farka taki buda idonta tana sauraron duk abunda ke faruwa, Doctor hafsa ta kalli malik tayi murmushi ahankali ta saukar da muryar kamar mai tsoron yin magana tace is she your sister or your wife sir? Malik yayi shiru har ta fidda ran zai amsata can yace “both” Dr hafsa tace Allah sarki Allah yabata lapia ,anan anguwar kuke ne? Malik ya girgiza kai yace aaaa , dr hafsa tace alright idan drip din yakare please let me know am in the office, Alright yace “daga haka Doctor hafsa ta juya ta fita. Har wajan 12 na dare malik ya nemi bacci yarasa itama aydarh sam ba bacci take kasancewar kadan kadan drip din ke sauka shiyasa har yanzu bai kare ba, har yanzu idonta rufe yake and bata fito da fuskar ta waje ba,ganin ya kasa bacci hakan yasa shi shiga toilet ya daura alwalla ya fito ya shimfida prayer mat din ya kabara sallarh, sai wajan one kafin drip din yakare lokacin malik ya sallame sallarh, sai sannan ya tuna da zancan kiran dr hafsa idan drip din yakare mikewa yayi tsaye ya matsa kusa da gadon yaga drip din yakare,without making any sound ya buda kofar yafita zuwa office din dr hafsa sai da yayi knocking sau uku sannan cikin muryar bacci dr hafsa tace am coming, bai sake cewa komai ba ya juya ya koma dakin, Dr hafsa ta kalli aydarh tace ko zaki shiga toilet din? ahankali ta gyada mata kai sai kuma tayi kasa da murya kamar zatayi kuka tace I need to change kuma ina son warm water,ita dai Doctor hafsa kallonta take ko kiftawa babu ganin yarda take magana cike da shegen shagwaba da tsananin izza da

kuma aji gauraye a muryan ta kar ma aje batun kyau wannan zata ce tunda Allah ya hallice ta she never meet a beautiful persons irin aydarh da malik duk da bata da lapia amma asalin gayu ya bayyana a jikinta asalin hutu yanuna ajikinta babu abun da take kallo a sai diamond rings din dake hannun aydarh masu masifar kyau da daukar ido, murmushi dr hafsa tayi tace alright am coming, bayan fitar ta shima malik ya tashi ya kasake kabara sallarh ita dai aydarh har yanzu bata yarda ta sake hada ido dashi ba . Dr hafsa tadawo dauke da flask a hannunta ta wuce toilet ta hada ruwan toilet din is very neat daman bawani amfani ake dashi ba, fitowa tayi tace muje na hada, bata ce mata komai ba ta tashi ahankali tana wannan tafiyan nata mai daukar hankali,dr hafsa dai sai kallonta take yah rabbi duk shape din nata ne ko na ciko ne this girl fine finish Allahumma bareek, fitsari tayi dr hafsa ta mika mata pad da pant duk malik na kallon su bayan ya sallame sallarh har su kagama sannan dr hafsa ta kalli malik tace yallabai sai dasafe,sannan ta juya ta kalli aydarh itama tayi mata murmushi tace sai dasafe madam Allah yakara sauki aydarh bata ce komai ba, sai malik ne yace angode kwarai Allah yasaka , babu komai dr hafsa tace sannan ta fita ta ja musu kofa, Malik ya kalleta bai san sunan da ya dace ya kirata ba, Ahankali yace how was your body? Shiru tayi kanta na kasa tace fine, babu wanda yasake magana cikin su.
Hajajju ta kalli oum tace to pah, wanene abba? Oum ta gyara tsayuwar ta tace habib, hajajju tace shi habibun yace zaku tafi can kasar din? Oum tace ehh ba jimawa zamuyi ba , hajajju tayi kasa da murya tace tau nidai ina nan bazan koma wannan kuturun gidan na yaya ba gaskia,oum tayi murmushi tace tau shknn nima na fi son ki zauna nan din tunda rufaidarh na nan itama hajajju dai tayi shiru bata ce komai ba oum tace tau idan gari ya waye ma karasa maganar tau Allah yakaimu hajajju tace,oum ta fita. Wajan karfe 10 flight dinsu ya tashi zuwa kasar spain hajajju dai hada kukanta,tace Allah sarki rayuwa famelin Habibu duk sun yaye sun barmu daga mu sai halin ko awani hali yaran can ke ciki Allah kawai yasani andai cuce su an cuce rayuwar su ita yarinya an banka mata aure da wannan basamudan mutumin, shikuma an lika mashi yarinya ga ba isassar lafiya Allah dai yasaka masu, rufaidarh dai sai kallon hajajju take inda sabo har tasaba da halin hajajjun. Hajajju tashiga kitchen ta iske daya daga cikin maids din gidan tsaye tana goge kitchen cabinet.

Hajajju tayi mitsi mitsi da ido tace hup dai an gaya maku matsayina a gidan tau idan baku sani ba daga yau kusani daga yanzu har su habibu su dawo nice zan dinga bada umarnin duk abunda zaayi a gidan nan , ita dai mai aikin na tsaye da dan karamin towel a hannunta tana kallon hajajju, ko

kiftawa babu “can hajajju tayi kasa da murya tace wai ita waccan dayar balarabiyar ita bata da mai so ne komai? Allah na tuba tunda nasanta ban taba jin labarin wani na neman auranta ba gaskia, mai aikin tace wacce balarabiyar ? Hajajju ta juya ta juyo Kamar mai gudun wani ya ganta tace waccan abun manah watake yauwa rufaidarh, “mai aikin ta girgiza kai tace aaa mama tanada masu so sosai amma kila ita ce dai bata bada fuska”hajajju tayi shiru can kuma tace kai kuji rubabba yoo Allah na tuba bata ga ita yar uwar ba ma da auranta kuma tafita komai ma,amma sai ita tau nidai ba ruwana bara nakama bakina nayi shiru kingan ni nan babu abunda yashafe ni da rayuwar mutune, ni ko maganar mutane bana son ana mun, shiyasa kullun nake zamana lapia,kema ga shawara ki kama bakinki ba ruwanki da maganar bil’adama “ ta sake kasa da murya tace kinga habibu duk cikin mu shine kawai ba rubabbe ba da kudinshi tau sai ni din nan dakika gani tsaye a gabanki famelin mu duk sun yaye sun rasu daga ni sai wata mata da muke uwa daya uba daya muka rage sai kuma ibrahin da ya’yanshi “ ta gyara tsayuwar ta tace wai fa shine dan tsoron Allah da kaunar ma’aiki da yanzu ba ‘ayi za a hadani da jafa’I wai wani abu na koma kuturun gidan matar da zama “ita a wa?ita ame? Da zasu hadani da zama waje daya da ita babu iskan kirki gidan ba kai babu kugu haka take rayuwa ba da ba jikah daman mu famelin mu munada tsari bama sakin jiki mu dinga zazaga yara kamar tsuma shiyasa kikaga bamu da yawa ma “ ita dai mai aikin har ta gaji da sauraron hajajju she see no reason da zata dinga mata wannan zubar, bata ce mata komai ba har tayi shiru “sannan tace tau Allah ya kyauta mama”hajajju tace haram haram badani ba aikata wannan baqin kantameman zunubin miye wani mama, sau biyu ina zuwa makkah fa wanda a famelin mu bayan ni sai habibu da wannan matar tasa dakuma diyarsu wanda a halin yanzu bamu san inda suke ba, still dai maid din she is eager hajajju tafita takarasa aikinta tun tana bata dariya har labarin yafara fita kanta nan fa take ce mata ita bata maganar mutane amma tun dazu take bata labarin abunda bai shafe ta ba “ can wani dabara ya fado mata tace am hajiya mi kike bukata na kumallo “hajajju ta washe baki tace daman tun jiya rabo na da sa ma cikina wani abu tashin hankali ya hanani sakat billahi “maid din tace Allah sarki, hajajju tace shayi zaki hadaman ki suya dankali da kwai takwas sai sabon biredi da farfesu yanzu ina jiranki ,maid din tace tau shknn hajiya dana gama sai na kawo maki a nan dining hajajju bata ce komai ba ta juya tafita.

Doctor hafsa ta kalli malik tace ya jikin nata tasamu bacci kuwa? Sai da malik ya sace kallon aydarh dake zaune ta rabe waje guda kamar marainiya kallo daya zakayi mata kaga alamar tana cikin damuwa sosai she is helpless

and she’s alone,can ya kalli dr hafsa yace jiki da sauki alhamdulilah amma ina ga gaskia batayi bacci ba, duk maganar da suke aydarh na jinsu ko kallo basu ishe ta ba,ahankali dr hafsa ta taka kusa da ita tace good morning ma’am how was your body? Kamar bazata magana ba kamar batagane da yaran da dr hafsa ke tambayan ta ba , bata motsa ba kuma bata dago kanta ba jikinta na cure waje daya daidai numfashinta ahankali take shakar sa take kuma fidda shi, dr hafsa dake kallonta ko kiftawa babu bata gaji ba tasake maimaita tambayar da take mata, kusan 2mins lokacin dakin yayi shiru malik kau bakin ciki kamar ya kashe shi ji yake kamar ya rufeta da duka ganin irin yarda ta maida dr hafsa kamar wata shashasha tana tambayar ta tayi mata shiru, dr hafsa tayi murmushi ta girgiza kai tace Allah yakara sauki bara na hada mata ruwa tayi wanka malik yace tau nagode,daga haka dr hafsa ta fita zata dago flask din ruwan zafi data sa aka kawo mata daga gida “kallo daya yayi mata ya dauke idonshi sannan ya mike tsaye baya son raini baya kuma wulakanta mutane duk halin san e rashin son magana amma idan har yazo wajan fagen kulawa yana nuna juriya da hakuri akan kowace tambaya dakuma amsarta ita amana ce wajan shi da kuma alaqar dake tsakanin su na yan uwa bayajin zai bar tarbiyyarta da rayuwarta su cigaba da wanzuwa ahaka ba, yana cikin jerin mutanan masu saurin karantar halin dan adam tsaf ya karanci girman kai izza izgili dakuma raini a tattare da ita, yarda yayi alkawarin karbar wannan kaddarar ahaka yayi alkawarin rike amanar da hallita mafi daraja da ki’ma a idonshi mafi koluluwar soyayyya a idonshi ta basa, bayajin sonta ko diko a ranshi kwata kwata halinta baya cikin jerin matan dayake son zama dasu matsayin matar aure tanada amfani da kyau wajan raina duk wani bil’adam shikuma bazai dauki hakan bah, wata zuciya tace masa tau wannan ai ba aure bane kamar kowane! “Cikin tsananin tsara gida ya kalle ta yace,she is not your mate she’s older than you so don’t take for granted, yasa kai yafice,kallonshi take ko janye ido babu batasan miyasa ba take wani jin shakku mai kama da tsoro idan yayi mata magana ba har faduwa gabanta keyi idan yayi mata magana wasu irin kwalla taji masu masifan zafi na bin kuncinta ta she can’t hold it but cry, kuka tafa rerawa kamar karamar yarinya har cikin ranta take jin babu wanda yayi saura a rayuwarta wani irin zafin oum da abba take ji har cikin ranta ko tuno bata son yi (subhanallah) Dr hafsa ce tashigo tasame aydarh na kuka kallonta tayi ahankali tayi dropping flask din kan med-drower ,kallonta takeyi batasan abunda zata ce mata saboda bata son kan mi take kukan bah almost five minutes suna haka ,sannan dr hafsa tace you are sick komai yafaru ki bar isai kinji sauki sannan ki ji da duk wani damun wanki for now dai keep anything aside recovered first,daga haka dr hafsa ta hada mata ruwa a toilet,sai da tayi

wanka tass Doctor ta taimaka mata tashirya babu kayan da zata chanza illa rigar da ta kwana dashi hakan yasa ta jin kamar zatayi kuka dr hafsa na kula da ita bata ce mata komai ba tana son ta wanke mata pant din datacire ganin yayi stain amma gani take kamar batada wannan hurumin domin ta fuskanci daga matar har mijin bahagwaye ne gashi babu yarda zaayi ita aydarh ta wanke kasancewar da abu a hannunta, fitowa tayi daga toilet din tasame ta kwance ta rufe dukkan jikinta ruf, a reception ta iske malik da Doctor ibrahim cikin Fara'a suka gaisa sannan ya tambayeta ya mai jiki dasauki alhamdulilah Doctor ya aikin? Doctor ibrahim yace mata Alhamdulilah sannan yace tunda nazo sai ki tafi maybe yau ma ayi discharging dinsu tunda jikinta dasauki right?dr hafsa tayi murmushi tace ehh Alhamdulilah daman jira nake kazo sai na wuce nima,sai ta kalli malik tace ehen yallabai akwai abu a toilet nasaka a bucket akwai detergent sai ka wanke mata, then a nemo mata abunda zatace, tunda tafara magana malik bai ce komai ma sai da tagama sannan yace "thanks".Bayan tafiyar dr hafsa suka cigaba da maganar dasuke shida dr ibrahim kan gidan dazasu zauna yana fada masa ai makwabta mane su da dr hafsa itama a anguwar take, Yau ma kamar jiya rabi'ah ce rike da food flask tasaha well ironed hijab dinta sai baza kamshin turaranta mai saukin kudi take,sai satar kallon malik tace bata taba ganin mutun mai kyaun shi ba,ko a indiyan flim din ma mamakin yarda yake da wannan mugun kwarjinin take bata ma iya kallonshi face face ko da ta gaishe sa ya amsa bata kallesa ba,taji yayan nata yace matar sa ce ba lafiya ita kam tana son ganin matar tasa taga ya take da har wannan mai zubin larabawan zai aureta,hakan yasa da dr ibrahim ke shirin karbar food flask din hannunta ya mikawa malik tayi karaf tace aaa yayah barsa kawai bara na shiga najiye sai na duba ta da jiki ma, dr ibrahim yace tau shknn, bude kofar dakin tayi ahankali tashiga "har numfashin ta sai dayayi barazanar daukewa, a kallo daya datayi ma aydarh Yah rabbil alameen, tau daga wace kasar suke tasamu kanta da wannan tambayar a zuciyarta,wani abu taji mai kama da bakin ciki hassada ya darso a ranta ganin aydarh da tayi ahankali ta ajiye food flask duk sai taji ta muzanta ashe karyar body structure suke ashe karyar kyau suke ashe karyar skin care suke ashe yar ubansu karyar body scent suke, warabul ka'aba she never imagined this type of beauty in the whole world? A gadon asibiti kenan fa tasamu zancan a zuciyarta bazata manta ba sun taba ganin hoton rigar jikin aydarh a wayar siyama kawarta itama a instagram ta gani wai three hundred k a lokacin mamaki suke wasu kalan kudi mutun zaiyi dazai siye wannan rigan sai yau taganshi jikin aydarh, ahankali tace mata ya jikin ki? Kallonta tayi lokaci daya taji wani irin bata ji haka ba kan dr hafsa da nurse saratu , sam ji tayi zuciyar ta tayi mata wani kala ganin rabi'ah ta bin ta da

kallo kamar mayya, duk sun suna kallonta amma na rabi’ah yafi bata mata rai, rabi’ah tace daman yayah ne yace akawo maki breakfast,

Akawo maki breakfast, aydarh ko kallon rabi’ah batayi ba balle tasa ran amsata “ rabi’ah dai natsaye ta zuba ma aydarh idon ta namata wani irin kallo, can tasake cewa magana nake maki malama ko baki jina ne ? cikin dan daga murya rabi’ah tayi maganar, Wani irin duba aydarh tayi ma rabi’ah cikin few seconds ta dauke kanta batace mata komai ba sai rufe ma fuskanta datayi da veil din kanta “ta bar rabi’ah nan tsaye kamar status “wani irin haushi ya kama rabi’ah watau yar iska ta mayarda da ita kenan marar lissafi da zata dinga mata magana tayi shiru “ juyawa rabi’ah tayi ta rufe kofar da mugun karfi har sai da aydarh ta mike tana kallon kofar wani irin harara tabi kofar dashi kamar idonta zai fado taja siririn tsaki, duk wani kala take ji amfani da riga daya dakuma brassiere daya datakeyi “she wish all this was dream ba reality bane, duk wani kala take jinta kamar wata daban ba ita ba she is totally lose take ji, ita salmarh da Doctor ashraff sukayi wa sharri irin haka “and without any investigation kuma suka saka aka koreta ba koran kawai ba hadda daura mata aure da waccan mutumin da bata ma sani ba, she didn’t have anyway to go “bata dakowa a duniyar batasan yanzu idan ta gudu daga wurin shi ina zata kuma ba she promise herself bazata sake komawa gida ba , she has no other option but to stay!” Zuciyar ta,tasake maimaita kalamanta na karshe, hawaye sharr suka zubo daga idonta.Tare suka shigo da Doctor ibrahim bayan sun dawo daga ganin gidan, ahankali ya turo dakin da sallama Doctor ibrahim na mara masa baya “ kuka take fuskar ta tayi jawur eyelashes dinta sun jiqe sun tattare waje daya hakan yaba idon damar fito da asalin kyawu da girman da Allah yabasa “ Doctor ibrahim yakalleta cikin few seconds ya dauke idonshi sannan ya juya ya kalli malik dake jingine a kofar dakin shima kallonta yakeyi ko dauke ido babu cikin wannan yanayin fuskan nashi ba yabo ba fallasa, duk da suna shigowa ta saukar da kanta kasa hakan bai hanata jin kamar ana kallonta ba, bayan hannu tasa tashare hawayenta tass sai sauke ajiyar zuciya take, Doctor ibrahim bai ce komai bah aka shima malik din duk shiru sukayi Doctor ibrahim a zuciyarsa yake tambaya tau mi yaakayi mata na kuka?baya son zagewa a lamarin su shiyasa yaja bakinsa yayi shiru, sake dubu bugun zuciyarta yayi yaga komai daidai, file dinta ya bude tare da dubawa ya rubuta masu takarda sallama.

Malik ya sai ke kallon Doctor ibrahim yace taya Doctor zaka ce basai nayi biya ba naga nan din private clinic ne, kuma kace mun bana ka bane “dr ibrahim yayi murmushi yace babu komai wllh nasan da haka idan wata yayi sai a fidda a salary na, Malik dai hakan sam bai mashi dadi ba domin ya lura

shima dr ibrahim kamar bawani hali garesu ba “idan kau suna da hali bazai yiyuwa ba ace da kwallin shi na degree kuma ma medicine ya karanta ace yatsaya yana aiki anan din dake kamar chemist,” Malik yace nagode Allah yasaka maka da alkhairi “ dr ibrahim yace babu komai yanzu kaje ku shirya sai na tare mai keke ya kaiku can gidan, in sha Allah da magrib sai nashigo akwai sakon da zan kawo maku,malik yace sako kuma dr sako nami?dr ibrahim ya girgiza kai yace kawai dai sai nashigo, fita malik yayi yashiga dakin “zaune take tacire veil din kanta fever dake jikinta ta sauka sai ciwon kai kadan kadan zafi takeji hakan yasata cire veil din, kanta datayi parking a keya daga gaba an rabashi biyu yayi wani musulmin kyau sai shining yake kamar wace tafito daga shagon saloon yanzu , jin alamar shigowar shi yasata saurin mayarda veil din a kanta tana cusa kanta tsakanin kafafunta ita ala dole bata son ko ganinsa, toilet ya wuce direct dan bai manta maganar Doctor hafsa ba to miye abun da tace tajika a bayi, taba kofar toilet din dayayi yasa aydarh saurin dago kanta domin ta san pant dinta na ciki,wani irin yankewa gabanta yayi yafadi to ya idan yaga pant din ta fa kuma jikinshi hadda stain,ko a gida rufaidarh ce kawai ke wanke mata pant shima sai idan ciwon nata yaci karfin ta duk ranar da oum ta taba mata pant kau dasunan wankewa kunya take wuni ji domin bata son kowa yaga private abunta abunda tsani wani gaya jikinta ko daoum ce kau har ta da rufaidarh ko bata da lapia saidai a taimaka mata akama ta taje toilet din ko ta shirya shi ma saidai adinga mika mata abubuwa, har yasa kai zai shiga,yace wannan soft muryan nata na baby’s ahankali kamar bata so na waje yajita tace “stop” tsayawa yayi bakin kofar bai juyu ba kuma bai ce komai ba almost 1min suna haka ganin baza tayi magana bayasa juyuwa cikin husky voice din sa yace didn’t you need anything? Bata dago kanta ba ta girgiza kai, shima mamaki ma take bashi fa hakan yasa shi folding hannunshi a kirji this time around kaf waennan idon nashi na kanta yakafe ta dasu ko janyewa babu,ahankali ta sauko daga kan gado ta saka flat shoe din ta tun wanda ta fito dashi daga gida, shidai kallonta yake ko kiftawa babu ta gyara zaman veil dinta, tana tafiya kamar bata son taka tiles din dakin jikinta sam babu kware ga duk yau bata sa ma cikin ta komai ba, har tazo inda yake tsaye ba dauke idonshi kanta ba, kanta na kasa kamar mai tsoron taba handle din kofar toilet dinta tasa ahannu ta murda ahankali ta shiga, sannan ta mayarda kofar ta rufe,ajiyar zuciya ya sauke sannan ya koma kan kujera ya zauna babu abunda suka bata Ko abunda zai shirya bags din su ne kwara biyu kacal kuma hade suke waje daya, pillow da bargo da tabarma da warmer din duk na dr ibrahim ne yasan zai sa a kwasa a mayar gida, kwata kwata jikinta is weak ahaka ta daure ta wanke pant din tass da detergent ta dauraye shi ta shanya saman wani karfe na toilet din, Ahankali take takowa

cikin dakin tafiya take kamar da gaya tafiya take without making any sound, kafafunta yake kallo so yake ko sau daya ne yaga ta hanyar da zai shaida cewa bataji ko zata iya aikata abunda akace tayi kuma shine uban dan “kafin su sauka kano ya yarda ya amince amma zaman da sukayi na kwana daya ya karance halinta tsaf bata da sakin jiki Ko fuskar dazata bada damar faruwar hakan, kawai dai yasake tabattar dacewa kaddara ce kawai ta rayuwar su ahaka.

Miyasa baki ci abinci ba yafada yana tsare ta da idonshi da babu alamar wasa fuskar nan tasa a daure, hannu tasa ta goge hawayen fuskar ta ahankali tace na koshi,bai sake kallonta ba yabude “warmer din yazuba mata white rice da stew ya mika mata” bata karba ba ya dire abinci kan gado sannan yace eat! Ahankali tasa hannu ta dauki abinci tafara ci kamar tana shan magani tanayi tana goge kananun kwallar dake sauka a idon,yana kallonta bai ce mata komai shima abinci yasa yafara ci domin yayi alkawarin mance duk wani damuwa a ransa sosai yaci abincin , har yanzu bata ci ko rabi ba, shidai Malik ya cigaba da ninke ma dr ibrahim bargon sa, can ya kalleta yace kisaka hijab dinki idan baza k ici abinci ba mu wuce, ture plate din abincin tayi kamar tana jira, dr ibrahim yayi ma dan sahun kwatancan idan zai kaisu yazaro 1k a pocket dinsa yabashi malik zuwa yanzu har bai iya irga a dadin alkhairin da dr ibrahim yayi masu har yagaji dayi masa godiya, yace Doctor ga bargon can da pillow da tabarma sai acewa iya mungode Allah yasaka da alkhairi, dr ibrahim yace aaa fa malik ai na kune nason kuna bukatar su,malik yace aaaa Doctor iyakar abunda kayi manah mungode dan Allah ka barshi, dr ibrahim yace ma mai dan sahun tada babur din ku wuce, madam nasan tana da bukatar hutu anjima zan shigo Allah yakara sauki, daga haka mai keke ya ja suka tafi.Anguwar sam babu hayaniya duk dacewa anguwar masu karamin karfi ce sosai kasancewar gini anguwar kusan duk unfinished buildings new asu sa plasta babu shafe balle paint wasu kuma ko kofar kirki babu “kofar wani gida ya tsaya duk layin shine babba duk dacewa gidan kofa ce amma kallo daya zakayi mashi kasan cewa cikin gidan compound ne, sauke kayan malik yayi yana kallon aydarh da yanzu fuskarta babu hawaye amma kallon daya zakayi mata kasan she is sick domin babu walwalla sam a fuskarta duk tazama kamar wata marainiya, ahankali yace mata sauko. Da sallama suka shiga cikin gidan apartments biyar ne a gidan ko wane akwai dan space tsakanin shi da dayan, da kallo waenda ke zaune tsakar gidan suka bisu suna kafe su da ido Kamar mayu,gaishe su malik yayi dasauri suka amsa ita dai aydarh kanta nakasa ko iskan da ya kwaso su bata kalla bad uk kanta nakasa hakan bai hana matan dake tsakar gidan kare ma hallita kallo ba tunda malik yashigo

wata budurwa take tsaye kallon shi take kamar tsohuwar mayya, har kofar dakin yayi dropping kayan dake hannun shi yafido ke.

Babban parlor ne yaji tiles sai bedroom daya da kitchen sai toilet a bedroom din dakuma wani a parlor, parlor babu komai sai karamin carpet a tsakiyar parlor " babu kura ko kadan wajan tass yake,Tunda ta tsaya bakin kofar dakin bata motsa ba kamar wacce aka dasa,kayan dake hannunshi yasauke tareda saukar da ajiyar zuciya mai karfi ahankali yake tafiya zuwa bedroom din dashi ma kofar shi ke a rufe sake fido key yayi daga aljihun shi ya bude dakin sai dayayi sallama kafin ya shiga , bedroom din dan madaidaici da katifa akasa nan ma akwai carpet da wardrobe like a bangon dakin taga dayace da plain ash curtains a both kofan da tagan, babu bedsheet a katifa sai rigar katifar kawai da pillow kwara biyu, "kallon dakin yake ko kiftawa babu anan kuma rayuwa ta kawo su anan kuma rayuwa ta maido su anan kuma zanan kaddarar su zata cigaba da kudana Yah rabbi ya furta ahankali tare buda kofar ya dawo parlor "idan take tsaye tun shigowar su anan take ta gaji da tsayuwar domin jikinta sam babu kwari amma bata jin zata iya zama sai lumshe idonta datayi ta jinginar da keyarta a bango tana sauke ajiyar zuciya ahankali da gani kasan bata son tsayuwar da take "kallonta yayi cikin few seconds ya dauke idonshi yayi kasa da kanshi tun tahowar su this is the first time data bashi wani irin mugun tausai haka nan yaji yana tausayin ta dagani kasan deep inside she is hurt, bayan dogon nazari dayayi ya fuskance abubuwa dayawa game da ita, Ahankali yake matsawa towards her "cikin wannan muryar tashi but this time can kasa yayi maganar yace ki shigo , bata ce komai bas ai buda idonta datayi tana kallon parlor, duvet din da pillow ya dauka ya juya yasake cewa follow me " koda suka shiga bedroom din nan ma dakin take kallo ko dauke ido babu "yana lura da duk wani motsin ta bags dinsu ya aje , ya daura duvet din kan katifar da pillow dake hannunshi " mikewa yayi ya kalleta yace come and have a set " shiru tayi Kamar bataji shi ba kusan 2mins bai sake magana ba sai can ahankali kamar tana taka garwashi ta zauna kan katifar ahankali tana takure kanta cikin hijabin dake jikinta " fita yayi ya koma parlor ya jinginar da tabarmar a bango kafin yabude kitchen din yashiga dan karami ne kitchen din babu komai ciki sai camping gas karami da pot a gefe da alama dai mai gidan daya tashi tafiya duk ya barsu. Kusan 1hr tana kwance babu ko alamar bacci a idonta tun dazu take kanannun hawaye takasa jurewa takasa mantawa so take kawai ta mutu domin duniyar ta isheta,knocking yayi ahankali kafin ya tura kofar dakin yashigo kwance take ta ba kofar baya

yarda take curewa waje daya yana bashi mamaki kamar bata da k'ashi da sallama yashigo dakin bata amsa ba domin Hankalinta sam baya jikinta kallon bayan nata yake kamar zai gano wani abu a bayan ' kusan 3mins yana ahaka ahankali kuma ya matsa kusada da katifar da take kwance ganin bata ji motsin shi ba ko alamar tasan dashigowar sa dakin hakan yasa shi yin gyaran murya "dasauri ta tashi zaune ganin mutun tsaye a kanta idonta yayi raurau alamar zatayi kuka don ta tsorata kallonta yayi ya dauke ido " yace sannu ya jikinki? Fuskar nan kamar za shi yak'I batace mashi komai bas ai sa bayan hannunta datayi ta goge fuskarta shima bai sake magana ba yabude bag dinshi yafido kudin da abby yabasa 20k ne cif domin baa cikin su yataba kudin mota bay ana son ya fita ya siyo abubuwan amfani amma bai san inda zaije ba hakan yasashi tunani zuwa clinic wajan dr ibrahim duk yace mashi zai shigo da,daddare amma kafin daran sun bukaci wani abun kamar bockets sponge toothpaste da sauran su, har yakai kofa zai fita yajuyo ya kalleta yace stay here don't out I will not stay long "aydarh batace masa komai ta koma ta kwanta,

Dr ibrahim ya kalli malik yace amma ai akwai gas da tukunya a kitchen din ba? Malik ya gyada kai sannan yace masa eh akwai, dr ibrahim yace tau Alhamdulilah yanzu bara lokacin tashina yakarasa sai mu shiga kasuwa mu siyo dan abunda ba'a rasa ba wanda zaku nema right? Malik yace eh hakane ina jiranka tau. Keke suka hau har central market din garin babu nisa Sosai daga clinic zuwa kasuwan cikin few minutes suka karasa, zanin gado suka fara yanka aka dinka musu da four pillows kamar yarda malik din yace babu bata lokaci aka gama suka karba suka wuce, bockets suka siya na wanka kwara biyu sai plate 6 spoon 6 cups ma haka sai knife da container karama daya babba daya sai warmer masu kwara uku kanana masu saukin kudi nan yabiya suka wuce wani shago yasiya soaps detergent da kuma sponges sai toothpaste da Vaseline babba daya sai karami daya, nan malik ya mika kudi "dr ibrahim yakalle shi yaso yayi shiru amma yakasa sai yace ka manta baka siyan ma madam perfume ba koh? Shaf ma ya manta a ranshi yace ka kasan kamshin datakeyi da baza kayi magana ba,baice komai ya koma ya daukar mata wani medium perfume body splash ne bai da karfi sosai yabiya kudin suka kwashe kayan suka fice fira suke ammar abin da kwatan firan dr ibrahim ke yinshi shidai malik daga um sai aa idan kuma abun dariya ne yayi wannan miskilin murmushi nasa " malik yace please ina zamu samu abinci nasiyan mata? Dr ibrahim ya girgiza yace aaa bara mu fara biyawa gidan sai a karbar mata wajan iya kafin taji sauki tafara girki,malik yace aaa Doctor dawainiyan yayi yawa kuma " mu dai sami inda ake siyarwa ko da restaurant ne sai muyi takeaway "Dr ibrahim yace na lura har yanzu baka

daukeni yarda na dauke bah? Malik yayi kasa da murya yace aaa sam bahaka bane kawai dai naga anyi wahala damu dayawa ne “dr ibrahim yace indai ka daukeni yarda na dauke ka muje mu karbar mata abincin can wajan iyan, keke su ka hau har kofar madaidaicin gidan, sallamar shi sukayi suka kwashe kayan suka shiga gidan dasu dakun ne kwara biyu a jere sai wata rufa da nan ma daki ne sai filin tsakar gida da kitchen da toilet a dakin koi na shafe yake cement anshare gidan kwal,kamshin turaran tsinke da aka kunna a daki har tsakar gidan, da sallama dr ibrahim yasaka kai yashiga rumfar malik na biye dashi baya dauke da ledojin siyayyar dasukayi a hannun sa,daga cikin dakin aka amsar sallamar dare bada izinin shigowa “babbar mace ce zaune kallo tayi saar ummi kallo daya zakayi mata kasan mahaifiyar Doctor ibrahim ce saboda tsananin kama dasukayi dashi cikin ladabi malik ya gaishe ta cike da kamala da fara’a ta amsa bata gane shi ba hakan yasa ta cema dr ibrahim bako mukayi ne? Gyada kai yayi yace eh iya ABDOOLMALIK ne wanda nake baki labarin sa, ohh Allah sarki tasake fadada fara’arta tace Abdul sannu ina gajiya ya mai jikin takara ji? Da sauki alhamdulilah iya,iya tace tau madallah Allah yakara sauki,Ameen suka amsa atare dr ibrahim yace iya ina yaran gidan suke su hadawa ABDOOLMALIK abinci a warmer ,iya tace duk sun tafi wajan biki nan baya bara natashi na hada da kaina bata jira amsar su,ba ta mike “a kula biyu ta hada masu lafiyayan tuwo da miyar danyan kubewa dayasha naman karamin dabba da man shanu sai kamshi yake “ sallama sukayi da iya tareda yi ma malik alkawarin zasu shigo su duba jikin aydarh in sha Allah Sosai yayi mata godiya har cikin ranshi yaji iya kamar umminsa. Saidai ya shirya duk abunda suka siyo a muhallinsa tun can daman yana taya su aysha aiki shiyasa duk wani aikin gida ya iyasu babu abunda yake basa wahala, toilet din dake parlor yashiga yayi wanka” wani cotton yard yasaka black duk da ya kwana biyu amma yayi masifar karban jikinshi kamar wani baindiye,shiga yayi dakin har yanzu bata ci abincin daya zuba mata ,kallonta yayi ya dauke ido bai ce mata komai ba yawuce bathroom din sai dayasa detergent ya wanke bayin duk da babu wani dirty a ciki fitowa yayi tareda komawa kitchen yana tunanin inda zai je ayi mashi refeling gas, yasan bazata iya sakawa jikinta ruwan sanyi ba.kallonshi take ko kiftawa babu gani irin kallon dake mashi yasa bata ranshi yana jan karamin tsaki a ransa har zai gota ta yawuce cike da iyayi tace hey handsome ina zuwa haka? Bai ce mata komai ya wuceta bin shi tayi a baya har yafita kofar gida, Daga murya tayi tace bawan Allah magana fa nake.

Malik dai sai wage wage yake yana neman wanda zai tambaya yayi masa kwantancan inda ake siyar da gas, budurwa dake tsaye mai suna

ramlah,takasa shiru sai magana take masa wanda ya maida ta da ita da banza duk daya “gajiya yayi da maganar da take masa,ya juya yayi tafiyarsa, dasauri ta like jingin bangon dan karamin gidan nata da parker rike a hannu da alama dai shara ta zubar sai faman sababi take ganin malik yasata likewa jin bango tace “wa’inahu min sulaimanu wa’inahu bismillahil rahamanin rahim,sai gwale ido take tana kallonshi kamar taga mutuwa shi mamaki ma tabasa yatsaya yana kallon ikon Allah,ganin yarda take yasa shi ajiye gas din hannun sa ya matsa kusa da ita, kara shigewa tayi jikin bangon tana rufe idon zuwa yanzu malik yarasa abunyi hakan yasa shi cewa baba lafiya? Har sai daya maimaita sau uku sannan tsohuwar ta bude idonta,tana kallonshi murmushi yayi mata yace ina wuni? Inna dai bata amsa bas ai kankance ido datayi ,malik yace baki da lapia ne baba? Sai sannan ina ta sauke ajiyar zuciya tace ohh ashe daman mutun ne kai ka razana ni hakan nan? Yanzu fa Ko Allah ya isa na banka sai ta bika ahtau wannan abunda kayi man tunda nazo duniya ba ataba firgita ni irin haka ba,malik was confused and speechless at the same time “ ya firgita takuma ta ina?shida ko magana baiyi mata ba and tafiya yakeyi lafiya lau he see nothing wrong kaf a jikinshi da zai firgita ta “bai ce komai bas ai gyara tsayuwar shi dayayi sannan yace Tau ayi hakuri “ inna tayi kasa da murya tace daga wace duniyar kake, kuma naji kana hausa anya yaro? Malik yashafa sumar kanshin nan kamar ta irin yan gayun larabawa yace daga sama ta bakwai inna ta tabe baki tayi shiru “kallo daya malik yayi mata kawai ta tuna masa da hajajju saboda har kama suke kuma ma kusan shekarun su daya,”Sake daukar gas dinsa yayi yace yanzu kiga ni bak’o baa nan nake ba zanje na saka gas ban san kuma inda ake sawa bak o zaki hadani da yaro sai yarakani,dafe kirji tayi tare da kwada wani irin salati tace wasu yagagun yaran na isa dasu a fadin anguwar nan dazanyi wani neman suna nasa su raka ka wanene wanda ya fada maka a nan akwai yaron dana isa dashi nasa ya raka ka,daga su har iyayansu ya’yan Allah bani ne woo tau nidai gaskiya ba ruwana bana shiga harkan kowa a fadin kano shiyasa kagani zamana , yanzu ka sakar ma mata fuska ta dinga kwaso ma yara suna shigo maka gida a zuba ma cuta suna tafe daudaa na zuba,shiyasa kaga babu mai shigowa waje na dagani sa ini idan takama dole ma sai mutun yazo wajena ko wanene saidai ya tsaya waje na fito nasame shi saboda bana kaunar azaba ni a dinga cutar mutane da wari ahtau, shidai malik sauraron ta yakeyi har tayi shiru bai ce komai ba, tace jirani yanzu na dauko mayafi sai naraka, malik yace tau “nagode “fitowa tayi da katon mayafinta da jikka tasa makulli ta rufe gidan tace yawwa muje tau tayi gaba malik yabita baya suna tafiya sai surutu take ko shiru babu shidai malik yayi shiru yana sauraron ta ,Tace wai kai daga wacce duniyar ma kake? Malik yayi murmushi yace adamawa “tayi shiru

tace minene kuma Adamawa? Yola ko Ina? Yace ehh can tayi kasa da murya tace tau wa ya aiko ka kano kuma kai? Malik yace ba kowa, tayi mitsi mitsi da ido tace kai dawa kazo? Yace mata nida matata,inna takalleshi tace tau Allah ya kyauta babu wanda yasake magana cikinsu har suka isa bakin hanya inda ake siyar da gas din babu wani tafiya sosai daga gidansu zuwa nan din,3kg yake dauka sai da aka cika sa yabada kudin suka tafi, inna tace tau kaga gidana nan ka gaishe da mai dakin naka,malik yafiddo 1k yamikawa inna yace tau gashi babu yawwa in sha Allah naga gidan ai zan shigo ko nima dai saidai mu tsaya kofar gida kar nashigo inna tace, injiwa kai da ba rubabbe ba miye wani abun nace kar kashigo mung ida amma dai bara nasa maka lambata sai ka gayaman karka cuceni ka shigo man gidan ban shirya bah ,shidai malik dariya yayi ,yayi mata sallama ya wuce.Ramlah na tsaye kofar gidan wannan karon ta chanza kaya fitted gown ce ta atampha Jikinta bakin nan yasha lipstick kamar tashafa rubber guda astagfirullah ga bakin kamar filin jirgi washe shi tayi tana karya jiki kamar kara jikin nan kau bleaching yayi gardama “shi Malik ma wllh kyamar ta yake cikin five seconds yakalleta amma yaji sam batayi masa ba “barka da zuwa yallabai tafada tana kashe kanannun idonta kamar Chinese ko kallonta side din datake baiyi ba yashige cikin gidan” part dinsu ya nufa ya fiddo key dinsa ya bude,da sallama yashiga yawuce kitchen ya hada gas din cikin few seconds ya cika tukunyar ya daura mata ruwan zafin da zatayi wanka kafin ahankali yashiga dakin , zaune take amma ta cusa kanta tsakanin kafanta ta takure kanta wuri daya kamar mai jin sanyi,plate din daya saka mata tuwo yabi da kallo tace dan kadan ko rabin malmala baiyi basai pure water daya aje mata shima tasha kusan rabi duk da she cannot recall when last ta sha pure water a rayuwarta, zama yayi ahankali kan carpet din dakin ya bude ledan dake da maganin ta yana dubawa, babu alamar duk yau tasha, maidawa yayi ya aje bai ce mata komai ba itama bata dago kanta ba duk da taje shigowarsa,kusan six minutes babu wanda yayi ma wani magana, tashi yayi “yashiga toilet yadauko sabon bocket din daya siyo kasuwa yafito dashi yashiga kitchen ya juye ruwan da har sun tafasa kashe gas din yayi sannan yarufu kofan kitchen din, ruwan yakaimata already yashirya sponge da soap din tare da toothpaste da brush din daya siyan mata tunda aka kwantar da ita asibiti,har yanzu tana yarda take saidai yanzu ta saussauta curewan datayi wa jikinta, jikkarsa yabude ya dauko wani pink clean toilet babba, ya ajiye kusa da kafanta, sannan yace ki tashi ki shiga kiyi wanka, bai jira amsarta ba ya fice daga dakin zuwa parlor kwantawa yayi kasan carpet yana son yayi bacci kona two hours ne.

Spain >

Bakaramin haduwa gidan yayi ba duk da ba wani babban bane amma yasha wani hadaddun flowers masu kyau da daukan ido wani red blocks akayi amfani wajan ginin gidan, oum ce zaune saman wata mad Expensive sofa tayi bala'In kyau cikin atampha normal riga da zani tayi wani ubansu daure ta fito da gashinta da tayi packing can kasan keya irin daurin ture kaga tsiyan nan amma tsabar gayu da iya ado salon daurin daban yake karamin bowl ne rike a hannunta da wuka tana slicing green apple wanda ke very fresh dagani yanzu a tsinko su,karo na ba dadi abba yakalleta ,kasa hakuri yayi yace nifa kamar da gayya kike sliced din apple din nan ahankali,murmushi tayi wanda zallar kyanta ya fito tace nifa babu wani abunda kayi mun dan kun gaisa da ita ai ni bana cewai dole kuna da affairs tsakani ba kawai dai bana son yarda kake sakewa da mata nidai gaskia,takarasa maganar tana raurau da ido "abba yayi murmushi yace tau shknn your majesty daga yau angama, dariya yabata yarda yayi kamar wani indian hadda dafa kirjinsa ya ware dayan hannun kamar zaiyi worshipping dinta, kallon shi tayi tace tunda muka sauka ban kira rufaidarh ba , bara nakirata definitely nasan yanzu tana can tana tunanin mu a ranta, abba yace ohh eh yakamata gaskia kiji ya wannan tsohuwar ma,tunowa da hajajju yasa oum yin murmushi har tafara missing magana da ita.

Rufaidarh tace mutanan spain, tun dazu nake tunanin kiranku tau danaji shiru baki kirani ba shiyasa nayi tunani ko bakuyi landing ba ko kuma kun tsaya wani wajan tafa sautin murmushi na fita a muryanta "oum tace aaa fah kawai dai agajiye muka sauka sai da muka huta kafin" gaisawa sukayi da rufaidarh "tana tambayar ta ina hajajju "rufaidarh ta sauke ajiyar zuciya tace hmmm hajiya na kasa wajan maids ai yau labari sai wanda ta manta kawai ke bata basu ba, kiji fa "nidai har na gaji da jiran ta dawo saman ma inga dai bin ta zanyi na dawo da ita tabar su su huta suma "oum tayi dariya tace ai hajiya halinta sai ita ki gaisheta tau and kibi ta ahankali kafin takare maki tanadi kinsan ta, dariya rufaidarh tayi tace ba ko wuya "can kuma tayi kasa da murya tace yallabai dai ya nutsu yafara dawowa daga damuwan right?oum ta lumshe ido cikin sanyin murya tace uktiee saidai idan bana duniyar nan zai zauna cikin damuwa amma tuni ya saki waccan tunani 'rufaidarh ta washe baki tace tau alhamdulilah nasan baki da wasa uktiee,ayo manah tsaraban twins daga spain tafada tana kwashewa da dariya tayi maza tana rufe baki kamar tana gaban oum, bata jira amsar da oum ke bata ba tayi saurin kashe kiran .Zan kwanta , bana son kowa yasan ina garin nan domin bazan ma je company ba oum tayi kasa da murya tace tau shknn ni bara naje muyi dinner karkayi bacci amma saboda yamma yayi,murmushi yayi yana gyada kai yace in sha Allah "

Juyawa yayi yafita,sosai take son tayi wanka amma tana tsoron ace ruwan sanyi ne,daurewa tayi ta tashi, ahankali take wannan tafiyan nata kamar tana yi da gayya , Kamar mai tsoron kofar haka takarasa wajanta duk da a rufe take amma sai da ta jinjina ta tabbatar domin bata son yashigo dakin, kayanta tacire kafin tasa hannu ta dauke pink clean towel din ta daura kamar dan ita akayi towel din kamar dan fatan ta aka saka zaran towel din hannu tasa ta zare ribbon din kanta yah rabbil alameen “hair dinta har wuce kafada, sanyi take ji haka yasata daukar hijabi tanufi toilet din,koina very need ta kalli bucket din da alama ruwan zafi ne a ciki bata wanka da bucket hakan yasa ta jin wani kala”pampo yayi mata wani kala duk da ba local pampo bane amma ita bata saba amfani da irin wannan ba ,sirka ruwan tayi daidai yanda take so wanka tayi,tayi brush tareda wanke pant din da tacire, ahankali ta bude kofar toilet din ta fito har sai da gabanta yafadi ganin shi zaune cikin dakin kallo daya yayi mata ya janye ido kamar ma bai ganta ba da sauri ta koma toilet din,tana tura kofar idonta cike da kwalla ta tsani wani ya ganta haka ko dasu oum ne kau, duk da towel din babba ne hijab din ma har kusan kneels dinta hakan bai hanashi jin wani kala ba domin ko su aysha baya gani haka,mamaki tabashi har sai da ya girgiza kai ahankali yamike ya fice daga dakin da dan karfi ya mayarda kofar ya rufe,saboda taji yafita tafito, cikin few seconds takare ma Vaseline din kallo hawaye ke bin idonta shikenan yanzu bata da gata itama talakka ce yanzu kenan? Da irin waenan abubuwan zata cigaba da amfani sanyi takeji tana bukatar shafa Vaseline din hakan yasata fara shafawa kamar mai tsoron fatan jikinta haka take shafa man, kusan 15 minutes tabata tana shafa Vaseline din,kallon bag din tayi ahankali ta bude ta fido pant din da ta wanke a asibiti bai bushe ba taje ta shanya shi a karfen datayi hanging wanda ta wanke yanzu, dayan ta dauka da pad tasaka kallon rigan da tacire da brassiere ta tayi bata jin zata iya kara sa su, duk da body scent din ta na nan perfumes dinta irin masu kama fatar jiki ne saboda ko da bata shafa ba kamshin na nan makalle da ita Amma sai take jin kanta wani irin tunuwa datayi bata dashi yanzu, kallon kwalban take ko dauke ido babu body splash aka rubuta jiki tasan perfume ne ,kamshin sa kadan hakan yasa tafesa kadan komawa tayi can karshan katifar ta koma ta cure kanta waje daya ta rufe da duvet, tunani kala kala a ranta, Sai da yagama sallar la’asar kafin ya tashi ya koma dakin, ledan maganin ta yabude yafido su hankali yace “tashi ki sha magani,shiru tayi kamar bata ji shi ba, bai sake maimaitawa ba sai ruwa daya fito ya dauko mata a kitchen, yace take “sai sannan ta tashi ahankali tana rike duvet din ala dole kar ya ganta da towel da hijab yarda take shan magani kadai zai nuna maka irin rashin kaunar dake tsakaninta da magani, saida tasha kowane kafin ya kwashe ya mayar a leda, kallonta yake can yace wear up

your cloth akwai sanyin, kamar zatayi kuka ta saukar da kanta kasa tace babu “sai kuma tayi shiru shi fa har mamaki take basa komai na kuka ne wai “bai fahimce abunda take fada ba hakan yasa shi cewa babu mi? Tace kayan, bai sake ce mata komai ba itama bata sake magana ba, sai bude bag dinta dayayi ya fiddo dayan rigan atamphar da ummi ta bata da kallabi , abayar da take nan wajan katifar da veil din daukar abayar yayi dawani irin speed ta sa hannu ta dauke brassiere dake nan kasan rigan ,ta boye yaga abunda tayi tsaf Ko kallonta baiyi ba yashiga bathroom din dakin sai da yabi manyan pants din ta da kallo yayi saurin dauke kai pampo yabude ya tari ruwa a bucket ya yazuba detergent kadan yasaka sabulu yafara wanke mata kayan, saidai ya wanke su tass ko kadan babu dirty a kayan sai kamshinta daya adabe masa rayuwa kamar time din tafesa perfume din .fitowa yayi rike da bucket din daya dauraye kayan a hannu, Ko kallonshi batayi ba ta dauke kai shima bai ce mata komai ba yayi ficewar sa. Ramlah na tsaye a ventilation dinsu wanda yake opposite da part din su malik din wayarta a saman building din daya zagaye part din normal android ce ta yayi,wanda cikin samarinta irinta ya siya mata,tiktok take tana wani karya jiki kamar wata macijiya, ganin yafito tayi maza ta bi bayansa “cikin kissa tace barka da yammaci yallabai ina wuni “iya saman lips ya amsata yayi gaba idan Doctor ibrahim ya nuna masa ta bayan parts dinsu dake zagaye anan ke da igiya daure ya shanya mata kayan ko wane part haka yake da igiyarsu. Warming miyar yayi ya rufe, wayarsa tayi ringing yana dubawa yaga dr ibrahim ne ,gaisawa sukayi yace hala madam dince tahana ka fitowa dariya malik yayi yace karka jawa yarinya sharri babu ruwanta gajiya ne kawai ke damuna dr ibrahim yayi kasa da yace kaidai kasa hakuri zakayi ta warke shiyasa kake ta dakon ta, murmushi malik yayi yace idan ma hakan ne ai ba laifi bane, dr ibrahim yace kwarai dagaske amma dai a dinga jin tsoron Allah ana tausayi, malik bai ce Komai ba sai cewa yayi kaji dashi dai, dr ibrahim yace tau na biyo maka zakaje kallon ball din ko kuwa? Malik yayi shiru sai can kuma yace aaa gaskia sai mai jikin ta karasa warwarewa zuwa next week sai na dinga bin gwaraye yawon dare, dr ibrahim daga can ya rike baki yace naji magana saukin ma dai nima bai fi two months ba,dariya malik yayi sukayi sallama.ko daya dawo daga salar isha backyard din ya zagaya domin kwaso shanyar yasan zuwa yanzu sun bushe ga kuma alamar tasowar hadari domin har walkiya akeyi tun dasuka zo gidan akwai nepa ko sau daya bata kifta ba daman dr ibrahim yagaya masa anguwar bakasa fai ake dauke nepa ba, Ahankali ta sake curtain din window this Time bai dauke idonshi ba akanta maganar dr ibrahim yadawo masa a rai dayace masa wai suna kama da ita kallonta yakeyi sosai shidai baiga kaman ba maybe ko dan itama tana da manyan ido ne oho ganin kallon dayake mata

duk sai taji bata sake ba towel din daure yake a kirjinta sai hijabin da ta dauko waccan doguwar har kasa gani take kamar yasan babu bra a jikinta, kayan hannunsa yabuda wardrobe din yasaka mata tareda jikkar ta baki daya , har yakai kofa ya juyo yace mata ki saka rigan bara na kawo maki abinci, harara taraka bayansa dashi ahankali taja karamin tsaki tace who's he? Sai wani jin kansa yake.

Sharp sharp tabude wardrobe din ta dauko abayar daya wanke mata tass tasaka ta maida hijab din, saida ya dan bata lokaci kafin yadawo dakin saboda yabata daman shiryawa "ko daya shigo zaune ya iske ta saman katifa ta jinginar da Bayanta a pillow bai ce mata komai ba ya aje abinci ya juya ya fita " bin plate din ta dinga yi da kallo same abincin daya kawo mata da rana ne ya sake kawo mata yanzu, ahankali ta dauki plate din tafara cin abincin kaman tana taunar magani bata ci wani dayawa ba ta ture ta sha ruwa, bacci ne sosai a idonta baccin da ta mance when last tayi sa " Ahankali ta zame ta kwanta tana rufe idonta. Har sai da gari yayi haske kafin yashigo daga sallar asuba, babu motsin kowa a gidan" bude kofar yayi ya shiga, har yanzu akwai wuta tun jiyan basu dauke ba "har yakai hannu zai bude kofar bedroom din ta sai kuma yafasa ya koma nan parlor inda yasa bargo ya kwanta sai da gari yayi haske sosai kafin ya tashi "toilet din nan parlor ya shiga duk irin sanyi dake akwai na damuna bai dame sa ba ahaka yayi wanka da ruwan sanyi yafito kayan jikinsa ya maida kafin ya bude kofar bedroom din without making any sound har ya bude wardrobe inda yasa jikkar shi ya fido black jeans ne da T shirt itama black yafido Vaseline da perfume din sa ya dauko sai comb fita yayi ya koma parlor tsaf ya shirya yayi matukar kyau, " kitchen ya shiga ya kunna gas ya daura mata ruwan zafi, tunanin abunda zasuyi break dashi yake hakan yasa shi yanke shawaran fita shagon daya gani ya siyo musu indomie.indomie yasiyo manya kwara uku da yellow label sai sugar,masu cefanan daya gani ya tsaya wajan su yasiyo vegetables da pepper sai kifi wanda aka gasa, zuwa yanzu mutane duk sun fito masu hadahadar tafiya office,nayi masu tafiya kasuwa da masana'antu nayi tun zuwan shi garin ya fahimce kowa anan din ta kansa yakeyi,daidai kofar shiga gidan ya hadu da daya daga cikin yan gidan namiji tun zuwansa gidan bai ga namiji ko daya ba sai yanzu "mutunmin ya washe baki ya tsaya yana kallon malik,hannu malik ya basa suka gaisa "mutunmin yace Allah sarki malan ashe kai ne wanda kuka tare inda dakta ya tashi,malik yace eh nine,mutunmin yace tau ni sunana malan sabo nima anan nake zaune da iyalina mata ta daya sai yaranmu biyu duk kananane,Kamar yarda kagani gidaje hudu ne anan din kowa da matarsa yake zaune dayan ba mazauni bane matar shi daya da yarinyarsu daya

Ramlah mutunmin kirki ne kwarai dagaske saidai kash “wllh bai yi saar mata ba da diya abar dai kaza cikin gashinta, dayan kuma sabon aure ne Auwalu ko wata ba a cika ba shagon siyar da kayan shafe shafe garesa na mata a kwari, malik dai surutun malan sabo ya ishe sa,murmushi yayi yace Allah sarki daga haka malik yayi masa sallama ya wuce ciki.karshe ya kai wutan gas din hakan yasa akayi daidai toni sanda yashigo ruwan na tafasa yau ma kamar jiya a bucket ya juye mata ya kai mata bathroom din already towel din daya fiddo mata yana nan rataye a kofar toilet din Sai da yasa detergents ya wanke toilet din kal duk da babu dirty ko kadan a toilet din “duk motsin da yake tana jinsa amma ko da wasa bata motsa ba har yagama yafita, kusan 5 minutes kafin ta tashi ta sawa kofar dakin key ta cire kayanta ta daura towel din tashiga bayin kusan 20mins ta bata kafin ta fito toilet din ba karamin kyau raman datayi yayi mata ba, Zama tayi gefen katifar sanyi take ji kadan kadan stain kadan tagani jikin pad dinta a pant din ma babu” shiryawa tayi tasaka rigan atamphar daura kallabin tayi simple style tayi wani irin kyau,bata saka brassiere ba amma zaka iya rantsewa da Allah akwai bra a jikinta saboda yarda breastcuff din ya zauna mata dass a jikinta, toilet din ta koma ta wanke bra din ta data shanya tass tayi hanging dinta a inda tayi hanging pants dinta, sun bushe hakan yasa ta kwaso su ta bude wardrobe din ta saka a ciki kallon bag dinsa dayasa a dayan gidan wardrobe din tayi ta dauke kai tana sakin karamin tsaki, Alhamdulilah yau tanajin saukin jikinta sosai babu abunda ke mata ciwo kawai dai har yanzu abun na mata yawo a kai yana kuma yi mata ciwo a zuciya, komawa tayi ta zauna kan katifar ta zubawa waje daya ido, duk wani abu nata mai muhimmanci shikenan fa yanzu?tambayar data samu kanta dayi ma kanta kenan sai ga kwala ya cika mata ido tayi maza ta goge kamar mai tsoron wani ya ganta tana kuka. Yarda yayi shaping vegetables din kamar wata mace ba karamin mamaki zai baka ba cikin nutsuwa yake girkin Kamar yadda wata hadadiyar chef din zatayi saidai indomie ta kusa yi kafin ya zare kayar kifin tass ya zuba, kamshin ne ya cika gidan ko ina 15 minutes ya dauke sa dafa indomie da ruwan Lipton a plate ya zuba mata daidai daidai ba dayawa ba,saboda yasan ko yazuba da yawa din asaran shi zaayi ba ci zatayi ba shima ruwan Lipton din half cup yazuba mata ya saka sugar kadan kafin ya dauka yashiga dakin da sallama,baiji ta amsa masa ba,kuma bazai iya cewa bata amsa din ba shidai yashiga kawai ajiye kayan hannunsa yayi bai ce mata komai ba itama ko kallon sa batayi ba” ledar maganin ta ya dauko ya ajiye mata tareda pure water ya juya yafita yana tafiya kamar wani boss “ sai daya cika plate da indomie yazuba ruwan Lipton din kafin ya zuba sauran da ta rage a warmer ya rufe ya koma parlor kan shimfidar dayayi ya kwana domin bai dauke ba” tafara samun appetite hakan yasata cin almost

half of the plate ba karamin dadi indomie tayi mata ba ruwan zafin ma tasha ba laifi saidai bata shanye ba raurau tayi da ido sadda tana ballar maganin ta tsani magani miye ma abun ya dinga ajiye mata magani while ta warke , da kyar dai tasha magani ta ture ledar. Agogon wayarsa ya kalla 10:00am daidai tashi yayi Sai da yafara kwashe shimfidar daya kwanta akai kafin ya share parlor tass, kitchen din yashiga ya share yayi arranging abubuwa dayayi amfani dasu kafin ya hada wanda ya bata wuri daya, fitowa yayi ya dauke bargon da bedsheets din da pillow ba waenda yasiyo bane duk a gidan yasame su, dakin yashiga yanzu ma da sallama,can ciki ta amsa shi sai dayayi da gaske kafin yaji ta amsa din bargon hannunsa ya buda wardrobe ya saka can gidan kasa inda babu komai da bedsheet din da pillow, ahankali yabude ledar magani sai da ya tabbatar da tasha din kafin da dauki plate din da cup din ko ina ta rage, ya wuce kitchen ya wanke 2 plates din da few kwanunin, ko ‘ina a parts din nasu looks very neat and tidy babu dirty ko’ina saboda baya son kazanta tun can mutun ne shi mai son tsafta, zama yayi yana ta juya wayarsa babu number ko ciki sai ta dr ibrahim tun bayan tahowar su daga adamawa ya fida sim din ya yar ya siyi sabo a tasha dialing number dr ibrahim din yayi bugu biyu ya daga cike da barkwanci Doctor ibrahim yace balarabe mijin balarabiya, dariya sosai dr ibrahim yaba malik, yace wai waye balaraben kai yanzu fisabillah idan larabawa suka ji ka ai sai su sa akamani, dr ibrahim yace a kama ka sukoma da kai kasar su ko? Daman can Daga can din ka gudu “ malik bai sake cewa komai ba “ dr ibrahim yace ai nayi tunanin duk kamar yanzu baka tashi ba ,malik ya girgiza kai yace aa ni ai bana ranar bacci da asuba tayi shikenan da anga nayi ranar bacci tau a tabbata banda lapia gaskia “dr ibrahim yace kace kai ma iri na ne, malik yace naji kamar ma ba ka fita aiki ba lapia dai ko? Dr ibrahim yace lapia lau alhamdulilah am off today kasan daga karshan month din nan ma zan dauki hutu sai kuma bayan biki “malik ya ware idonshi yace no kabari dai sai can irin ya rage one week haka amma kace tun ending this month kusan wata daya da sati daya fa zakayi kana hutu “ hakane kuma tau shikenan yallabai na dauki shawarar ka malik yayi murmushi yace tau nagode “ ya mai jikin takara ji? Da sauki alhamdulilah dr ibrahim yace tau masha Allah in sha Allah nan da 20mins zan shigo gidan naka, malik yace tau Allah yasa daga haka ya kashe kiran. Dr ibrahim sai bin parlor da kallo yake koina tsaf tsaf sai kamshin turaran tsinke yake,kasa hakuri yayi har sai da yace wai har taji saukin fara gyaran gidan malik dai yayi shiru kamar bai ji sa ba, kitchen ya shiga ya zuba mashi sauran indomie da yasaka a warmer cikin plate ruwan Lipton din daya dafa ya huce saboda babu flask a cikin tukunya ya barshi hakan ya daura masa pure water biyu a wani plate ya kawo masa “ dr ibrahim yace sannu kace rabon naci dadi

yasani zuwa gidan nan dawuri fara cin indomie yayi,can yayi kasa da murya yace kai fa abokina Allah yabaka wannan iya girki haka ko dai a catering tayi degree ne,shidai malik murmushi kawai yayi kafin yace kadai kar ace santi ne ya ruda ka,Kaci abinci kawai malam,tass dr ibrahim yacinye indomie bai rage ko kadan ba sunyi suna fira, har wajan 12:00pm dr ibrahim bai ko ji motsin aydarh ba “kuma bai ji malik yayi zancanta ba, kasa hakuri yayi yace ma malik,yallabai wai ina mai jikin ne ko bacci take sai sannan malik ya tuno ma da ita danshi sam ma ya mance da ita, malik yace kasan cikin drugs dinta kamar akwai na bacci , tunda tasha na safe bayan mun gama breakfast take bacci gashi yanayin garin akwai sanyi damuna kwara ta zauna a cikin dakin saboda yanayin lafiyanta kasan masu asthma “dr ibrahim daya gama sauraron malik yace “sure”fira suka cigaba dayi kamar waenda sukayi shekara 30 da sanin juna wannan ne karo na farko a rayuwar malik daya taba wani irin dama da matsayin daya ba dr ibrahim lokaci daya yaji ya yarda dashi kuma bugu da kari ma jinin su ya hadu;Dr ibrahim yace like I was saying before clinic din nan da chemist ne ahankali ya mayarda wurin clinic nida dr hafsa mun riga da mun san juna tun muna yara babana Allah yajikan sa malik yace Ameen ,da babanta tight friends ne a tare suke komai na rayuwa tare da ita mukayi primary school har sai da muka kai secondary kafin ita aka kaita boarding school ni kuma aka bar ni day,malik yace Allah sarki, dr ibrahim yacigaba dacewa Bayan munyi graduation ne daga secondary government ta dauki scholarship ciki har da sunayen mu ni da ita , saboda parents din mu daman sunyi kokarin ganin mun samu din saboda basu dawani karfin daukar nauyin mu,munyi jami’i anan BUK mukayi medicine kafin na karasa babana ya rasu itakuma bayan graduation dinmu da month daya mahaifinta da mahaifiyarta suka rasu yanzu haka tana zaune da kakarta inna daga nan gida daya ne tsakanin ku da gidansu,dr ibrahim na fadin sunan inna malik ya tuno da tsohuwar da ta rakasa siyan gas jiya sai sannan ya tuna daya ce mata zai shigo yau ma da basuyi wannan firan ba ya manta ma da zancan ta, malik yace indai innan dakake nufi ne jiya mun hadu da ita a kofar gidan nata har ta rakani siyan gas, Dr ibrahim yace kai haba? Malik yace am serious,dr ibrahim yace lallai kam ajiqa ka asha innar da kowa hakuri yake da ita,ita kanta dr hafsa dan bata biyeta da tuni kowa ya kama gabansa fa,malik yayi murmushi yace nima a jiyan na fahimce haka, dr ibrahim yace kasan yanzu government din aiki wahala yake sai idan akwai wanda ke tsaya maka, malik yace hakane, dr ibrahim yace wannan bawan Allah mai clinic din shine yayi employing dinmu nida ita duk karshan wata ana biyanmu 30k nurse saratu kuma yarinyan wani abokinsa ce diploma ne da ita a chew 20k ne salary duk month dan dai kawai kar mu zauna ba aiki amma mutumin dake da degree a med yafi

karfin 30k as salary malik yayi murmushi yace in sha Allah komai mai wucewa ne, dr ibrahim yace tunda dai madam tak'I farkawa na duba jikinta bara na wuce akwai inda zani daga nan din, malik yace tau shikenan dr muje na taka ma nagode Allah yasaka " dr ibrahim yace babu komai ai an zama daya har kofar gida ya rakasa anan suka tsaya dayake center ce har yasamu keke yawuce, har ya juya zai shiga gida yaji ana tafa hannu ga salati ana rabkawa,juyuwa yayi suka hada ido da inna dake tsaye da katuwar jikkarta da uban mayafinta da alama daga anguwa take,malik yashafa kansa yayi murmushi yace ina wuni, inna tayi mitsi mitsi da ido tace aaa haram aaa haramun miye wani ina wuni bayan baka kaunar Allah ina zaman zamana kace mun zaka zo hadda saman lambarka a waya dana kira lamba yan kamfani suka ce man layin waje ne bana najeriya ba,bacin ina tsoron Allah karya ba halina bane ai da yanzu nace daman baka da gaskiya,nagaya ma hafsa yarda akayi tayi banza dani kamar wata tababba daman can niba shiga harkanta nake ba tunda na lura babu Allah a ranta tak'I fito da miji tayi aure ina jin fa yanzu zata iya 50 zuwa hamsin da,samari duk wanda yazo sai ta koresa tau irin wannan mi zai sa ka dinga shiga harkar mutun? Malik yace babu gaskia,inna tace tau nan da kake ta sauri daman dai ba kayi niyyar zuwa gidan nawa ba kenan? Malik ya girgiza kai yace aa fa daman dai da yamma nayi niyya zanzo aie, inna tace tau shikenan amma yanzu sake sa man lambar sai ka kirani gabana naji kar ka sake sa wata kuma na kira ama kulle layin baki daya ka cuceni, malik yayi murmushi yace tau shikenan,sabowar number shi yasaka ya kira sai da tayi ringing inna ta yarda kafin ya kashe tace tau yi man sebin yace tau mi zan saka?tace rubuta audu kawai da manyan baki daman hafsa ce ke gano man, itama dai sai ahankali ba yarda nake da itama ba,sai kuma tayi kasa da murya tace inaga itama fa ba wani iyawa tayi ba karatun nan Amma kafin tagano man lambar mutane sai nashiga ukku shidai malik yayi shiru bai ce komai ba,inna tace tau sai anjima sai kazo ka gaishe da mai dakin naka,bata jira amsar sa ba tayi gaba. Suna fitowa daga sallar azahar shago ya wuce yasiyo flour da yaji dakake a rubber sai groundnut oil da star kwai yasiya kwara 4 yabiya kudin yatsaya wajan mai cefanan daya siya dazu suka gaisa dashi dan ya gane sa,fresh tomatoes ya siya da albassa anan yake tambayar mai cefanan idan zai siyi kuka da kanwa mai cefanan yace masa yaba yaron sa yashiga gidan dake kusa dasu ana siyarwa ya siyo masa,10mins sai ga yaron yadawo yasiyo godia yayi ya karba ya wuce, ruwa ya tara ya daura kafin ya kwaba flour danwake zaiyi wanda favorite food din sa ne ya iya danwake sosai abubuwan da bai iya ba kadan ne a girki yana tafasa ya jefa dan waken 30mins ya dauka yagama ya wanke tukunyar tunda kwara dayace Bayan ya juye danwaken a warmer ya mayarda da tukunyan ya wanke kwan ya saka

kafin ya yanka tomotoes din da albassan kanana yarda yaga ummi nayi idan anyi dan wake tass ya hada komai kafin ya zubawa aydarh a plate ya bare kwai kwara uku ya zuba mata a nata plate din,zaune take kan carpet, kallonta yayi ya dauke ido kafin ya aje mata plate din agabanta bata dago ba kanta nakasa amma taga abunda ke cikin plate din, this time ma kamar dazu ledan drugs dinta ya kawo mata kafin yaje kitchen ya dauko mata ruwa .

Inna tace oyoyo ga audu ga audu ga audu maraba, ganin har angama la’asar baka shigo ba nayi tunanin ma baka zuwan,malik yace aaa zan shigo daman barin nayi yamma tayi kafin nazo, daki tashiga ta sai gata da jug da cup a hannu fura ce ciki mai kyau tasha Nono sai kamshin kayan yaji ke tashi ta zuba masa a cup tace gashi kasha daman kai na dama ma ita,karba malik yayi yabi furar da kallo yace nagode kwarai inna, da sallama dr hafsa tashigo cikin shigarta tsaf da lab coat sai jikkarta da wayanta a hannu masa mata malik yayi inna ta tsaya tana kallonta ko kiftawa babu, sai ta dauke kai,dr hafsa tayi murmushi daman dr ibrahim yabata labarin komai itama kanta ba karamin mamaki tayi ba jin wai har inna taraka malik din siyan gas,tace yallabai ashe dai anguwarmu daya,ina wuni ya mai jikin?shima malik dan sakin fuskar sa yayi yace Alhamdulilah Doctor,inna tace wacece wannan kuma, sai kuma tayi kasa da murya tace ina kasan wannan kuma? ita fa haka take a duniya burinta taga nasan wani itama tace tasan shi,malik yayi murmushi yace a asibitin su aka kwantar da mai dakina,inna tace ohh ,sai kuma ta kalli Doctor hafsa da ta daure fuska tace nan dakika tsaya kamar wata yar sanda bazaki shigo ba komi? Doctor hafsa batace komai ba tawuce tashiga daki “inna tasake kasa da murya tace itace nake gaya maka dazu nidai ba ruwana jikata ce diyar babban dana ce daya rasu,nake riko Malik yace Allahu akbar Allah yayi masa rahama inna tace Amin, babu ruwanka da ita rashin mutunci wanda ta mance ne kawai ke bata mun ga girman kai,kaii hakuri nake kawai billahi amma daya yanzu na kai kaina gidan marayu na bar mata nan din, malik yayi murmushi yace bazaayi haka ba ai. Inna tace yanzu fa nan da ta shiga kafin ta fito sai wani iko daga Allah, malik yace hutawa take kinsan gajiyar aiki “inna ta bi malik da kallo kafin ta kalli kofan dakin dr hafsa tace tau mutun idan iko da sarauta yake ji ai sai yatafi can gidan sa yayi “Amma babu katuwar da ta isa ta dinga man mulki a gida “malik dai yayi shiru yana sauraron inna,mikewa tsaye tayi tashiga daki,can sai gata ta fito hannunta rike da kula da kuma jug “tayi kasa da murya tace bara nashiga na kai mata abinci saboda idan bani na kai mata ba saidai fa yunwa ta kashe ta wallahi bazata fito ta dauka ba,malik dai nata kallon drama inna, inna ta kalli dr hafsa tace nasan daman dawuri

zaki taso shiyasa nace bara nayi kokarin gama girkin da wuri ita dai dr hafsa bata kalli inna ba ta cigaba da linke lab coat dinta, inna tayi kasa da murya ta kalli kofa tace wai zararra ce ni ko mi ina magana kinyi shiru kin maidani kamar wata yar iska dai, dr hafsa tace wai ba naga bak'o gareki ba? Ki fita ki same sa manah abinci ne dai kin kawo kuma nagode, sai nafara yin wanka kafin,inna ta tsuke bakin ta tace tau Allah yabaki hakuri bara na fita kafin ki zage ni kuma",tana fitowa tace yawa daman ai na gaya maka nice daidai da ita, malik yace ayi hakuri dai ni bara na koma naga magrib ta kusa, inna ta washe baki tace tau ba laifi ka gaishe da mai dakin naka nima nasamu lokaci sai nashigo na dubata, har kofar gidan inna ta rako sa labari kau kamar kar yatafi inna takasa shiru. 6:00pm daidai yashigo gidan ,Ramlah na zaune a ventilation dinsu ita da mahaifiyar ta sai dayar matar part din fadila da yaranta biyu maza da mata, su biyar ne wurin amma kamar mutun dari fada suke sosai kan Ramlah ta bige yaron fadila musa aiken sa tayi bai je ba tayi magana yace bazaije aiken karuwa ba,ta dakesa uwarsa tace bazata yarda ba ai gaskia ya fada, shine suke faman wannan masifar, ko kallon su bai yi ba yayi wucewar shi part dinsa, dawani irin mayyan kallo Ramlah ta bisa ta mance ma shaf da abunda sukeyi, har sai daya shige building din part dinsa ta daina hango shi domin an zagaye ma kowa ventilation dinsa, fadila tayi gyaran murya tace haka fa aka yi, Ramlah ta maka mata wata wani shegen harara tace tau uban miye yayi ruwanki da ni?maman Ramlah tace duk ba wannan ba kuyi shiru, tayi kasa da murya tace ma fadila " shin fadila kinga abunda nake gani kam? Fadila data saki baki tana kallon maman Ramlah tace nagani tun jiya abun ke ci na hakuri nayi kawai banyi magana ba wallahi, maman Ramlah tace tau wai balarabe ne ko mi wannan din? Fadila tace wallahi tun jiya dana ganshi nake tambayar kai na tau baki nan shiyasa na ja bakina nayi shiru (kamar basu bane ke fada yanzu) Ramlah ta tabe baki tace ba fa balarabe bane kawai dai haka yake, maman Ramlah tace ki bari baban musa yadawo kila ma ji magana daga wurin shi,fadila tace in sha Allahu saidai idan basu hadu dashi ba amma nasan sai ya tambaye shi wayeshi,kin fa san halin sabo, Ramlah tace ku kwantar da hankalin ku zan binciko maku komai ni fa ai naga miji wurin nan, fadila ta tabe baki tace ko makaho yasan wutsiyar ragumi tayi nesa da wuyan zakara " maman Ramlah tace aa fadila mi kike nufi?fadila tace babu komai bara na tafi kafin sabo ya shigo,

Sai daya fara shiga kitchen ya daura ruwan zafi kafin ya fito knocking yayi saboda ya taba kofar yaji ta a rufe, sai dayayi almost 8mins atsaye yana knocking kafin a bude kofar ahankali ta bude masa kofar ta juya ciki, bin ta yayi da kallo ganin abunda tayi masa a rayuwa baya son raini ya tsani

rashin kunya,bai ce mata komai ba itama hakan ko kallon sa batayi ba kanta na kasa tana wasa da Expensive diamond ring din hannunta,plates din daya kawo mata abinci yabi da kallo ba laifi taci sosai saidai ga yajin nan gefe guda da alama bata son yaji dan bata ma taba shi ba saidai star din kawai eggs din kuma daya kawai tace ga sauran two din nan danwaken ma gashi nan ledan maganin ta ya dauka yanzu ma tasha daga yau ya kare daman na 3days ne kawai, kallonta yake ko kiftawa babu so yake ta dago idonta yayi mata concrete warning kan rashin sallama amma tak'I baya jin kuma sai iya yi mata magana tayi shiru ta kyale sa saboda ko saar maryam auta bata wuce ba bazaiyi tolerating shits ba, bai ce komai ba ya kwashe plate din ya fita dasu da harara ta bi bayansa a ranta tayi karamin tsaki , kwanciya tayi ta rufe idonta daman can bata saba zama cikin mutane ba ,shiyasa bata jin kadaici 'Ko a gida sai ta wuni bata fito ba,a can school Cyprus daman idan ba lectures zatayi attending ba bata fita daga campus dinta, her life is always private bata da friends bata jin magana ya hada ta ko sau uku ne dawani a school din tun zuwan ta duk da yanda school din yake akwai yara masu yawa yaran masu hali ne,amma bata gani akwai wanda zata iya zama dashi balle har a kai da wani abu wai friendship.sai da ruwan yatafasa kafin ya dauko bucket ya juye mata, this time ma bata amsa sallaman shi ba, bai ce komai basai da ya kai ruwan toilet yafito ya zuba mata ido mistakenly ta bude idonta suka hada ido dashi wani irin fadi gabanta yayi tayi maza ta saukar da kanta kasa, ya kafe ta da waennan idon nashi , cikin tsare gida da muryan nan tasa babu alamun wasa yace "baki iya amsa sallama ba hala ? Sai taji wani iri da tambayar tasa abun yazo mata wani kala,shiru tayi batace komai ba, yace "daga yau kar nasake sallama naji kinyi shiru " bai jira amsarta ba yayi ficewar sa daga dakin, sai time din ta dago kanta idonta cike da kwalla , umarni yake bata kenan? Ita yake ba umarni ? Saboda yaga bata da kowa sai shi babu inda zata je sai wajan shi? Who is he? Mi yake daukar kanshi? Mi ma yake nufi da ita ne wai? Tayi ma kanta tambaya kusan goma amma bata da amsar ko daya,hawayen ta tasa bayan hannu ta share tass tayi ma kanta alkawarin baza ta sake takura kanta ba ko daura ma kanta damuwa,kuma shima bai isa ya daura mata damuwa ba ko ya juya ta,idan girman kai yake ji dashi ta fisa idan izzgili yake ji dashi ta fisa, hararar datayi ma kofan dakin sai ka rantse da Allah malik ne tsaye a gabanta, toilet ta shiga nan taga bucket din ruwan zafin da ya ajiye mata, kallon bucket din take ko kiftawa babu ita yakawo ma wa kenan? Tunda taga shi baya using da wannan toilet din,tsaki ta saki kafin ta fito cikin dakin ta cire kayanta ta dauki towel ta daura, Sai da tayi wanka tsarki dan tagama period kafin tayi wanka ta fito, kamar dazu yanzu ma Vaseline da tashafa da perfume din abayar ta mayar ta koma ta kwanta. Daga masallaci

daya fito garin dinke yake da hadari tunanin abunda zai yi masu na dinner yake mai awaran daya gani a gefen gidan su kawai ya yanke shawaran siyan masu,sallama yayi yarinya ta amsa wurin a share yake tass da alama awaran na da tsafta na 500h yasiyan musu ya wuce. Kofar dakin ya tura this Time bata saka key ba sallama yayi yaji shiru bata amsa ba,karasa shiga dakin yayi ya ganta tana salla,murmushi yayi iya lips dinsa yafice daga dakin a plate ya saka mata awaran kafin ya zuba tasa a warmer , sallama yayi ta amsa sa can kasan makoshi kamar wace throat din ta ke ciwo mamakin halin yarinyar yake,ta idar da sallan still kuma tana zaune kan prayer mat din “ bata tashi ba ajiye plate din yayi ya fita.

TWO WEEKS LATER

Zuwa yanzu malik ba karamin sabo yayi da inna ba sosai suka saba kullun ne da yamma sai yashiga gidan indai kau baije baya tare da dr ibrahim suka fita wanda yanzu ya zamar masa kamar wani dan uwa tsakanin sa da aydarh har yanzu babu mai ma dan uwansa magana, kullun ne sai yadafa ma ruwan wanka ya kai mata abinci kau babu fashi kullun sai ya girki duk wani gyaran gida shi yakeyi,ya fuskanci abubuwa dayawa game da ita,wani lokacin idan tayi wani abun dariya take ba sa akwai ranar da inna ta matsa mashi sai sunje ta ga mai dakin sa, suka tafi tare shiga yayi daki yasame ta tsaye inda take tsayuwa kullun tana kallon mutanan gidan,bai san mi zai ce mata ba kawai yasa shi cewa ga innata nan zaku gaisa batayi magana ba dan batasan wace inna ba. Kayan ta kala biyu ne daga gown din atampha sai abayar ta wllh ta gaji da saka su bra daya take using idan tayi wanka ta wanke sai ta zauna haka har sai ta bushe sannan ta mayarda,abayar ce jikinta ta daura kallabin akai fita parlor tayi wanda bata cika zama a nan din bas ai idan baya nan ko kuma an dauke nepa tazo ta tukure kanta waje daya shidai yana ganin abunda takeyi baya tankata ya fahimce yarda take tsoron duhu hakan yasa shi siyan mata torchlight indai babu nepa ta dinga haske haske kenan, Ahankali take tafiya har ta iso cikin parlor kasancewar yamma ce akwai nepa hasken globs din parlor sun haske fuskarta tarr kullun kara kyau take sometimes malik har mamakin ta yake yakan tambayi kansa wai mata haka suke ko kuwa? Wani lokacin dr ibrahim neke yawon kawo masa zancan mata da zamantakewar aure har wani zakewa yakeyi shima yakusa shigo daga ciki yaji abunda suke ji, shidai malik saidai yayi murmushi kawai har mamakin dr ibrahim yakeyi shi baya kunyar ko wace magana “. Murmushi kadan a fuskar ta,ta zauna kan carpet din parlor tana gaishe da inna dake ta faman zara ido kamar wacce aka tsikara haka inna ta mike tsaye tana kallon malik da aydarh tasake bude idonta sosai kafin ta koma ta zauna tace Allah mai halitta sai kuma ta kalli malik tayi kasa da murya tace

audu ashe kafini gaskia danace boyun matarka kake ashe dole ka boyeta, masha Allahu sai kuma ta washe baki tace tsali yo Allah na tuba audu ku wannan kamar dai ku aka hada ma wa, sai kuma taja bakinta tayi shiru tace ah babu ruwana balle ace nayi sabo amma wannan dai wannan dai sai kuma tayi shiru,shidai malik sai kallon inna yake aydarh ma tarasa abunda zata ce mata, inna tace ya sunan ta kace?ahankali malik yace ASSIEYERH yarda yafadi sunan kamar da larabci yasa inna kasa fahimta yarda yafada , zata sake magana akayi knocking kofan part din nasu malik yace waye muryar dr hafsa suka ji tana fadan ita ce, bude mata malik yayi inna tadafe kirji tana kallonta tace yanzu kuma haka kika zama ni hajara nabani, tayi kasa da murya tana kallon aydarh tace kiji bala'I daga taji labarin nazo nan har ta biyo ni, dr hafsa dake gaisawa da malik ko ta kan inna bata bi ba, ta kalli aydarh tace patient daga rana ban sake ganinki ba kuma saidai yallabai murmushi aydarh tayi tace ina wuni dr hafsa ta amsa tana tambayar ta ya jiki, labari sukeyi duk da inna ce mai labarin ita dai aydarh murmushi ne nata,malik kau da har yasaba fira da inna biye mata yayi suna fira, ana labari da dr hafsa tayi magana sai inna ta kwale ta sai wajan six suka yi sallama zasu tafi har waje suka rako su dr hafsa da ta daga waya tayi gaba sai inna a bayanta aydarh a bayan inna malik ke can bayan su, har suka fito building din parts dinsu inna batayi shiru ba, ganin tana neman fita yasa shi jawo……

Kallonta yake ko kiftawa babu itama ido cikin ido take kallansa ,kasa yayi da murya cikin tsare gida yace duk ranar da kika kara kokarin fita a haka babu hijab sai na karya ki,yasake ta yafice "anan tsaye yabar ta mamaki ya cikata har kofan gida ya raka inna sannan yadawo, bata parlor yasan cikin daki ta koma, hakan yasa shi yin zaman shi a parlor kwana biyun nan kudin hannunshi sun kusa karewa,shiyasa yake so idan anjima suyi shawara da dr ibrahim kan abunda zaiyi.Dakin yashigo ko kallansa batayi ba yana tsaye kanta "ta turo baki "tace nan da ka tsaya mun akai fa? Malik mamaki ne ya cikasa, sai yaji kamar bai ji da kyau ba, yace dani kike duk yarda gabanta ke faduwa na masifan tsoron shi da yanzu ta yarda tanayi bai hanata ,mikewa tsaye ba tace erh, bai ce mata komai ba ya fice daga daki " . Kallonshi yakeyi har sai da yayi shiru yace tau shknn na fahimta Allah yakaimu lapia, dr ibrahim yace Ameen "shiru ya biyo baya dr ibrahim yamike tsaye yace bara na fita na jira ka kar time ya wuce,malik ya kalli watch din hannunsa yace har na kusa mantawa ma fa ashe yau ana wasa " dr ibrahim yace sure kayi sauri mu tafi, fita dr ibrahim yayi kofan gida,shi kuma malik ya juya yashiga kitchen indomie daya dafa masu ya zuba mata a plate sauran tasa kuma ya zuba a warmer, salla take sai da yatsaya kallonta yake ko dauke

ido babu,ganin yarda take salla ajiyar zuciya ya sauke tareda girgiza kai kwata kwata ba a daidai take sallan ba hakan na nufi bata iya ba ko mi? Har tagama kafin ajiye plate din hannunsa yace ki kashe globs kuma din kafin ki kwanta bazan dawo da wuri ba, batace komai ba shima daman baiyi tunanin zata ce din ba,yayi ficewar sa, kusan five minutes tana kallon plate din indomie hawaye yazo mata a ido tashare ashe zata iya saba wa ahaka ashe zata iya rayuwa dasu ashe zata iya cin cimar su?zuwan inna yau sai ya wanke mata kashi ashirin cikin dari na damuwan ta ashe suma suna rayuwa cikin farin ciki, kullun sai ta tsaya bakin window bedroom dinta tana hangen yarda yan cikin gidan ke shiga da fice zuwa yanzu ma tasan fuskokin su,sau dayawa zataji suna fada wanda kullun ma cikin haniya suke, share hawayen ta tayi ta jawo plate din tafara cin abincin kaman bata so, halinta ne rashin cin abinci shiyasa bata ci dayawa ba ta mayar kitchen ta rufe kamar yarda taga yanayi, shimfidar shi da ya fito ta bi da kallo tana karamin tsaki ta shige daki haka kawai taji bazata yi abunda yace din bas ai taga yarda zaiyi, a ranta tace shi kullun Kamar wani force ya dinga daure fuska yana magana Kamar baya so, trash tafada kasa kasa, ta je ta kwanta kasa bacci tayi domin ba ta iya bacci cikin haske ka’ida ne shi ke kashe mata glob,yau kuma daya sata kashewar bazata kashe ba so take ya dawo taga abunda zaiyi tunda shi komai na masifa ne bala’i’a kawai ta fada kasan ranta. Bayan yagama duk wani aiki da shi keyi na gidan ya kai mata ruwan wanka tayi, sai da yabari ta shirya kafin ya shiga dakin ya jingina da kofa yayi folding hannunshi a kirji straightly yake kallonta da waennan idon nashi , kanta na kasa bata dago ta kalle sa ba tana dai jiran abunda zai ce, babu wasa a muryar shi yace I asked you to off the globs yesterday and you refused to do sures why, wani banzan kallo tayi mashi sai kuma tayi saurin janye idonta ta juya masa kai, tace I can’t “ wallahi banda umarnin ummi ba yarda yake da zuciyar nan baya son raini da rashin kunya da yau kam sai ya balla yarinyar nan,shiru yayi yana cigaba da kallonta still bata juyo ba tana yarda take,takawa yake ahankali kan carpet har ya kusa zuwa inda take,dawani irin mugun speed ta mike ta manne a can karshan wall din dakin tace wallahi’bada kai nake ba don’t beat yarda jikinta ke shaking yagane ba karamin tsorata tayi ba amma rashin kunya bata hanata murguda masa baki ba, sai dayazo towards her sun kure ma juna sosai numfashin ta na barazanar fita ta rufe idonta gam yana iya hango yarda gaban ke over racing kirjinta na dagawa sama da kasa,wannan bakaramin daman kare mata kallo yabashi ba kallonta yakeyi ko kiftawa babu yah rabbi,dasauri ya dauke idonshi,yace this should be the last time da zanna saki abu bakiyi ba I will surely deal with you and your mate ko kuma na kai ki can wurin wanda yayi maki cikin aka like mun sharri sai ki cigaba da mashi ranshi kunyar

bani ba idiot, wallahi har cikin ranta taji zafin kalmar dandanan idonta ya kada yayi ja bude ido tayi fuskanta har yayi ja kuka na kwace mata cikin wannan shagwababiyar innocent voice din nata da dan karfi take maganar tace ni babu wanda yayi mun ciki ban san kan abunda suke magana ba kuma duk wanda yasake ce mun wannan abun ban yafe masa ba kafin ta fashe da wani irin kuka tana silalewa kasa kan tiles ta hade kanta da gwiwa tana kuka mai shegen karfi numfashin ta har sama sama yake,daga yarda tayi maganar kawai yasa kan malik sarawa he cannot lie or deny anything yaga tsabar gaskiya a idonta inalilahi waina illahil rajiun wannan wane kalar alamari ne, kusan 10minutes bai tashi ba ita kuma batayi shiru ba har sannan kukan take,hankalinsa baya jikin shi tunani ne kala kala aransa, can yaji tana wani kalar numfashi kamar tana kokowa ma da numfashin, dasauri yasa hannu ya dago kanta fuskar tayi ja sosai idonta yayi bala'In reddish sun fito waje ,ahankali take fadin inhelar baya jin ta da kyau amma ko baa fadi masa bay asan asthma ce da wani irin sauri yakira dr ibrahim yace masa yana asibiti eh kawai yatsaya dr ibrahim din yace ya kashe wayar bai tsaya jin sauran maganar da dr ibrahim din ke fadi ba ya kashe wayar, hijab yasaka mata, kafin ya kamata ko tsayuwa da kyau bata iyawa dakin ya jawo, yarda ya rike ta kamar baby ba guntuwa bace amma tsawon su ma bai hadu ya kere ta sosai, kofan parts din nasu ya rufe yataho da ita rike a jikinshi "kaf yan gidan na zaune a a tsakar gidan kowa na harkan gabanshi suna fitowa ido ya koma kansu kamar zasu cinye su da kallo, Ramlah kau kamar zatayi hauka,yana fita yasamu keke suka shiga. Cikin few minutes dr ibrahim da taimakon dr hafsa sukayi kokarin daidai ta numfashin nata allura akayi mata saboda ta huta, Dr ibrahim yace malik yarinyar nan na shan wahala asthma nata chronic ne, malik yasauke ajiyar zuciya yace Ya jikin nata? Dr ibrahim yace she is getting better dr hafsa ma tayi mata allura, zuwa anjima zaku iya tafiya idan ta farka, malik yakalli dr ibrahim yace idan badamuwa dr hafsa zata iya mata p test? Dr ibrahim yayi murmushi yace awwww tun farko Malam kayi magana amma ka wani tsaya kwana kwana,bara ta farka tau.

Kallon paper dake hannunshi yake ko kiftawa babu mamaki ne sosai a ranshi duk da dr ibrahim yayi masa bayani amma bawai ya yarda bane sai da ya gani da kansa, dr ibrahim yace sai fa kawai hakuri this time bakayi nasara ba,atari gaba,malik yayi murmushi yace tau wani yace maka na kagara ne,dr ibrahim yayi kasa da murya yace tau miye nasawa ayi mata awo,malik yamike tsaye yace sai anjima zan fito sai na tarar dakai gida muje wajan tare dr ibrahim yace tau ba damuwa sai munyi magana tace ma dr hafsa da inhelar take amfani an bata,malik yace tau shknn nawane bill din

dr ibrahim yace nabiya ai,malik ya kalleshi bai ce komai ba ya wuce.Haka kawai yaji bai kyauta mata ba shine silan faruwan komai har tayi kukan da asthman ta taso ko da yashiga dakin zaune take hijab din ta rike a hannu fuskanta tayi wani kala, she is fine,she fine,she is damn cute,and cool in body structure ,sannu yace mata batace mashi komai ba,kafin yace saka hijab din mu tafi yayi gaba bai jira amsarta ba.Ramlah ta kalli mamansu da fadila dake tsaye tace wallahi mama nake gaya muku fa ba larabawa bane, maman Ramlah tace wai ya'yan waye a kasar Ramlah ta tabe baki tace da yaran wasu ne sunzo su kama haya a wannan compound din ina kuma kullun kuna nan baku ga wani alamar ansa furnitures ba fadila tace hakane amma ranar dana ga sun rako inna wallahi abayar jikinta dana ganshi a wayar maman boy data zo kitso wajena yakusa dubu dari biyu maman Ramlah tazaro ido tace ke fadila!fadila tace sai kiyi kuma ai ita Ramlah tasani,Ramlah tace mama idan ma bata fi ba,maman Ramlah tace ni ba wannan ba kyan jiki da haduwar yarinya ke kamar haddadun yaran masu kudin larabawa fa, fadila tace ni haushi na mijin ko gaisuwa da kyar yake amsawa ita bata ma fitowa balle mu ga fuskar mata magana,Ramlah ta mike tsaye tana wani kashe dauri tace ai wallahi ko ma miye sai munyi soyayya dashi,fadila tac eke Ramlah baki da tsoro wai?ina laifin ki tsaya akan auwal din,Ramlah tace minene kuma auwal ana maganar mutane wannan yar iska siyamar daman danayi maganin ta naga tana wani dauke manah kai a gidan nan siyasa ma na nuna ina sonsa duk da hakan kuma har yanzu babu ruwanta damu bata shiga harkar mu shiyasa na rabu da ita,nidai na fita maman Ramlah ta washe baki tace a dawo lafiya diyar albarka ita dai fadila na kallon ikon Allah tafa san inda zata je shine hadda wani addua take mata. Sai daya shimfida mata zanin gadon daya wanke kafin ta kwanta sai bacci,parlor yadawo yana cigaba da tunanin abunda ya faru yau , without making any sound yashiga bedroom din yabude wardrobe ya fiddo turmin atamphar da ummi taba ta kudi yagani a kasan atamphar kallon kudin yake ko kiftawa babu tunuwa yayi da 20k sadakin ta yasa shi yin murmushi ya girgiza kai yasan ummi ce tasaka mata kudin tunda kudin ta ne ai sadakin ta ne,Bakan leda ya saka atamphar kafin ya rage fankar dakin yasa duvet yarufe ta she is sleeping so tight kamar yar baby kallonta yayi few seconds kafin ya juya da ledar atamphar a hannu ya fita, "Gidan yashiga tana zaune gidan nan kal kamar a zuba abinci ka ci kan cement din da aka shafe tsakan gidan dashi,tana ganinshi ta washe baki tace yanzu fa nake labarin ka araina nace yau shiru ko kana ina zama yayi kan tabarman da take yace asibiti mukaje bata jin dadi ina wuni inna?tace asha kam Allah yasawwake,malik yace Ameen kafin yace dr hafsa fa?inna tayi mitsi mitsi da ido tace wacece kuma haka? Malik yace hafsa nake nufi tace ohh wannan

matar zaka ce,nidai tun safe datasa wannan farar rigar ta fice har yanzu bata dawo ba,malik yace eh asibiti muka baro ta ai nayi tunanin ta dawo inna tace aaaa wallahi bata dawo ba,tayi kasa da murya tace audu ko dai yaron ciki ne ke gana mata wannan azabar?malik yace aaa inna asthma gare ta, inna tace Allah ya kyauta ciwon lumfashi baiyi ba sam, malik yace yawwa inna ga wannan atamphar idan hafsa ta dawo a bata sai ta kawai mai mata dinki ,a dinkawa ASSEIYARH inna tace tau shknn daga haka suka cigaba da fira da malik kafin yayi mata sallama ya wuce. A kofar gidansu suka hadu da dr ibrahim dake tsaye yana waya da murjanatu matar da zai aura wata mai zuwa bayan ya kashe ya kalli malik yace ya mai jikin?malik yace dasauki bacci ma take mutafi kawai basai na shiga gidan ba akasa suka cigaba da tafiya har wani babban gida,dialing number mai gidan dr ibrahim yayi yace masu su shigo " parlor daidai cikin mutunci suka gaisa dashi, Allh musa yace ma malik nasan Ibrahim yayi ma bayanin komai shiyasa nace kazo sai naji daga bakin ka malik yace eh , babu damuwa Allh musa yace to daga gobe in sha Allah zaa fara aikin site din kaine babban engineer malik yayi godiya kafin Allh musa ya fiddo 5k yabasa yace transports ne.plate din chips yasiya kwara biyu shi daya ita daya tun kofar gidan Allh musa suka rabu da dr ibrahim kasancewar akwai inda zaije ,yasiya man mata fresh green apple sai water melon yahau keke ya dawo gida,a plate ya juye kafin yayi sliced din apple din da kankanan dakin yashiga da sallama,can kasa ta amsa sa yashigo.

Zaune take ta jinginan da kanta a wall,ahankali take breathing kallo daya zaka mata kasan she is sick fuskan nan tayi karkar kaman madara,idonta ya dan fada ciki ahankali take rufe idon tana budewa kaman wani yasata, kallonta yake ko kiftawa babu kafin ya dauke ido,ahankali ya ajiye plates din hannunshi dukka biyun " murya can kasa yace how are you feeling now? Kaman bazata ce komai ba,tace better daga nan taja bakinta tayi shiru shima shirun yayi kafin yace "sit" tashi tayi ta zauna ahankali kanta kasa plate din chips ya dauka ya daura matakan laps dinta kafin straightly yace "eat" hannunta yabi da kallo yanda take juya fork din a mugun gayence rings din hannunta masu masifan kyau da daukar ido bakaramin karama hannun nata kyau yayi babu digon lalle ko kadan, chips din data ci bai fi 8 ba egg din ma rabi taci,ta ture 'plate din chips din ya dauka yasake mayar mata a cinya kafin yace eat it all! Kallonshi tayi kadan kafin ta kalli plate din tayi raurau da ido alaman kuka zatayi kafin ta girgiza kai,muryanta irin masu gaf dayin kuka taci na koshi ai " baisake cewa komai ba ya kwashe plate din chips din ya fidda a warmer yazuba sa, sannan ya dawo ,ko baiyi magana tasan abunda yake nufi,ahankali ta dauki sliced din apple daya tana

tauna kadan kadan ba laifi tace kusan 4sliced kankanan ma taci kusan uku satar kallonshi tayi kafin ta ajiye plate din, kusan 10mins suna zaune a haka babu wanda yayiwa daya magana,mikewa yayi ya zuba mata ido yace akwai abunda kike so kuma?batayi magana ba sai gyada masa kai kadan datayi alamar babu fita yayi daga dakin ya koma parlor. Inna dake tsaye bakin ventilation din su da katuwar jikkanta sai gwada sallama dake,jin ana sallama kuma da alama na ne yasa shi ajiye tsintsiyar dake hannunsa ya nufi kofan part din inna yagani tsaye,murmushi yayi ya shafa kai yace inna sannu da zuwa ina kwana? Inna tace na ma fayi tunanin hala cutar kurumtaka yasame ka ace na kusa tanminid ina banka sallama amma shiru baa amsa ba kuma baa zo aka bude ba,malik yace ina can ciki fa yanzu shigo, shigowa tayi ta zauna kan carpet din ta ajiye jikkarta gefenta malik ma ya zauna yace inna ina kwana?ya gidan mun tashi lapia?inna tace lahiya lau audu ya kwanan mai jikin kuma?yace Alhamdulilah “tashi yayi yashiga kitchen sauran fruits din daya siyo mata ya ma inna slicing ya kawo mata yasan ko ya kawo mata abinci bazata ci ba ma, inna ta bi fruits din da kallo kafin tace ohhni hajara banda kai daga nashigo dubiya kuma sai ahadani da kayan karin ciwo ni dana zo dubiya,malik yace babu komai fa inna,yawwa inna nace jiya an bawa hafsa kayan?inna ta juya kai ta kalli kofa kamar mai tsoron magana ta dauki kankana daya ta sa baki tana sha,kafin tace eh ta karba tau Allah natuba audu miye wani abun bawa hafsa ta kai wa matarka dinki ita kanta ba fa wani masu dinki arziki ta sani a kanon nan ba wallahi,dan dai babu ruwana amma da jiyan nan nace kabani na kai idan ake man nawa dinki,malik can’t hold it but to laugh dariya yake irin wace yajima baiyi kalar ta ba hadda rike ciki,inna ta ajiye slice din apple din data dauko tana kallonshi ko kiftawa babu “ idan tana kallon malik sai ya dinga tuno mata dawasu mutane a rayuwarta amma har yau ta kasa fahimtar su waye,saida yayi shiru kafin inna ta dawo daga tunanin data tafi,yace tau inna ai da hakane tun jiyan da baki ba ita hafsa din ba,inna tawani daure fuska tace dariyan dakakeyi nabari kagama kafin nayi ma bayanin waya wayar da hafsa din,malik da har yanzu dariya ke cin sa yace yanzu dai duk abar wannan zancan amma ai kowa yasan wacece ke wajan gayu inna tawani tabe baki irin kai ma kafada din nan, Dasauri ta ture plate din tace astagafirrillahi nabani ni hajara,dubiya fa nazo ina matar dabata da lahiyan,malik yace ai surutu ma yasa kin manta abunda yakawo ki bara nakira ta”,Baiyi knocking ba ahankali ya tura kofan da sallama can kasan throat,ko kadan bataji motsi ko alamar shigowan sa ba tsaye take ta fito wanka ta baza gashinta data wanke da shampoo din da maman dr ibrahim tasa ya kawo mata ko daya fada mata bata gane wa yake nufi ba ya ajiye dai kawai, tana son wanke kanta saboda she forget when last taje saloon tun

tana adamawa wanda ka’ida ne duk two weeks ake mata gyaran gashi duk da bata so amma rashin son kazanta ke sata zama a wanke mata dakuma fadan da oum keyi idan bata wanke ba,pink towel din nan ke daure a kugunta bra dinta nan kwara daya tagama sawa yanzu wanda ta fito a toilet wanke tass tana ta kamshin detergents daba ya wasa wajan siya a ajiye mata a toilet tagama sa bra din tana kokarin mayarda towel din a kirji ya karasa shigowa baki da daya bataji motsin sa ba still,wallahi saura kadan numfashin sa yafita jikinsa bayanta yabi da kallo this is the forst time daya taba ganin wata diya mace ahaka,bai san magnet din dake jan idonshi wajan kallon bayan nata ba yarda bra din ya zauna a haddadan bayan nata da yarda milky clean skin dinta da babu spot ko wani stain ko daya ke mahaukacin glowing yaraina girmanta gani yake yar karama ce amma yau sai yasamu kanshi da karyata hakan, ahankali ta juya tana daga hannunta dukka biyun zatayi parking gashinta still towel din na a wrist dinta tana juyuwa kallo daya yayiwa boobs din yawani irin dauke kai kamar zai karya wuyan shi ,saura kadan bata suma ba yarda ta tsorata dawani irin speed ta jawo duvet ta rufe jikinta baki daya hawaye na zarya a kumatun ta, kafin tafashe da kuka yagama da ita yagama da rayuwarta, how long yake tsaye a wajan inalilahi waina illahil rajiun shi kansa malik din duk ya rude bai san miya yaja sa ya tsaya yana mata irin wannan kallon ba,juyawa yayi dasauri har yakai kofa kafin ahankali,yace inna ce tazo dubaki “bai jira amsarta ba yafice ya ja kofan,Time din daya dawo parlor inna har ta shanye fruits din tass zama yayi kanshi a kasa yace,wanka ta fito shiryawa take yanzu zata fito inna tace Allah sarki, fira suka cigaba dayi duk da yau innar ce kawai ke zuba surutun ta malik abunda yafaru yanzu duk yasa shi jin wani iri,Bude kofar akayi ta fito kanta kasa kamar marar gaskia tana wannan tafiyan ta ta,kallo daya yayi mata ya dauke idonshi ko ganin sa ma batayi ba kanta kasa,ahankali ta zauna kafin ta gaishe da inna,inna ta washe baki ita ko kadan bata lura da mood din aydarh ba tace lahiya lau diyar nan ya karfin jiki?ashe baki ji dadi ba?Aydarh tace Alhamdulilah,bata sake magana ba domin ji take kamar zatayi hauka zama inda yake yana sata jin girman laifin daya aikata mata, inna dai sai zuba take ko shiru babu jefi jefi malik na biyeta, Ahankali cikin voice din ta dayayi kasa sosai innocently tace inna nagode sai anjima,inna tace nima tafi zanyi bara kigani mikewa inna tayi ta maka jikkarta a kafada tayi masu bankwana malik yatafi ya rakata,aydarh tayi saurin shiga bedroom tafada kan katifa kuka take sosai iya karfinta pillows din dake kan katifan ta dinga watsar wa hatta da duvet din da bedsheet din sai data watsa kasa,malik dai natsaye jikin kofan da bata rufe ba yadaga curtain yana ta kallonta baki daya rayuwarta abun tausai ce ansaba mata da irin dabi’ar turawa na watsar da abubuwa idan suna cikin

kunci,parlor yadawo bai shiga bedroom din ba,tunanin ta inda zai fara billowa lamarin ta yakeyi,wata zuciya tace masa wannan duk mai sauki ne ka fara aikin tukunan da haka ya yanke shawara yakasa manta abunda yafaru dazu daya juya sai ya tuno hakan yasa shi daukar al”Qurani dake nan ajiye a parlor ya bude muryan shi yana rera karatu baki daya part din babu inda sautin muryan shi baiyi amsa kuwa ba,Har cikin jikinta karatun ke shiga wani sanyi take ji a zuciyarta wanda bata san daga inda yake ba ahaka har bacci ya dauke ta,yayi spending almost 2hrs yana karatu kafin ya rufe ganin time din lunch ya kusa saboda lokacin azahar dake kunnu kai.Yau ma kamar kullun sai datayi masa magana amma Ko kallonta baiyi ba, har tana tuntube ta bi sa har waje, bata gaji ba har wajan inda zaiyi cefane ta bisa bai tanka ta ba dan yi yayi kamar bai san da wanzuwar ta a wajan ba kayan miya yasiya na 300h kafin yasiya salad na dari sai da beef na 500h kafin ya mika kudin har ta riga ta bayar sanin ko wacece ita yasa mai cefanan cewa hajiya Ramlah shine yasaki?tana taunar chewing gum irin na kwararun yan barikin nan papa (Sosai) tace miyayi ruwanka kudinka ne biya ka ka rike sauran change din, mai cefane dai yasaki baki yana bin ta da kallo,wani kaskantacan kallo malik yabi Ramlah dashi kafin ya sake daura fuskar nan kamar hadari,wallahi Ramlah idan tana kallonsa har loosing control take, daura fuskar nan dayake ba karamin tafiya yake da ita ba haka ranar da taga suna dariya shida dr ibrahim a kofan gidansu har mutuwan tsaye tayi,bai ce komai ba cikin wannan isan nashi ya Zaro 1k ya mikawa mai cefane mai cefane baiyi musu ba dauki 200h yabashi chanji,juyawa yayi yatafi bai kara bin ta ita ba, ko kadan abunda yayi mata bai dameta ba ko taji kunyar abunda yafaru ganin akwai mutane sai ma kara gyara calaban attachment din kanta blue and green tayi gaba mai cefane yace kudin hala kin bar mun?wata banzar harara ta watsa masa tace kaine dan wahala ai sai ka rike ta juya ta tafi mai cefanan ya daga murya yace gaki nan yar wahala yar asara ma Allah ya shiryaki matasan dake tsaye wajan suka sa baki,dayan yace ai wannan yarinyar yar wahala ce kullun fa ina nan kusan ko yaushe sai ta biyo balaraben nan shi kau ko ta ita baiyi ni bana ganin ma yana shiga harkan kowa a anguwar nan, mai cefane yace ai baya ma fitowa cikin layin nan indai kagansa waje tau gidan hajiya inna zai shiga sai kau wani abokinsa dake zuwa wajansa mutunmin ma dabaya magana kamar jinin sarauta kullun anan yake cefane gaisuwa kawai ke shiga tsakanin mu yasiya abunda zai siya yayi gaba.sai daya shiga provision shop yasiya spices da maggi ya siya kwai kafin ya koma gida, yana shiga kitchen yafara yashiga yadaura ruwan da zai dafa shinkafa kiran sallarh akayi ya rage wutan gas din yafita massallaci,white rice ya dafa da stew ya yanka salad yayi boiling 3 eggs din da ya siyo tsaf ya shirya mata a plate,kudin hannunshi sun kare

tass ga abincin daya siyan masu yakare daman ba mai yawa bane shinkafa ne tiya daya sai macaroni biyu taliya hudu da indomie six,bakaramin dadi yakeji bi idan ya tuno da maganar aikin daya samu bazai taba mantawa da dr ibrahim ba a rayuwar sa domin yayi mashi hallacin da har abada bazai iya mantawa ba, pure water ya daura mata a plate wanda bag daya yake siyowa ya ajiye kan tiles din kitchen sanyi damuna ke dan cooling ruwan, da sallama yashiga dakin tana jinsa tayi maza ta rufe idonta,yaga abunda tayi bai ce komai ya ajiye plates din hannunsa yace stand up and eat”kafin ya juya yayi ficewar sa

Dr hafsa ta juya atamphar kafin ta mayar a leda,tabi inna da kallo tace shi yakawo a kai a dinkawa Asseeyan?inna tace wacece kuma asiya?dr hafsa tace matar tashi inna tayi ma dr hafsa wani kallo tace tau uban waye wanda yace maki sunanta haka?dr hafsa dake kallon inna da mamaki tace tau ai sai kibata wani sunan idan ba sunanta haka ba,inna tace aaaa gaskia katuwar karya kike daman dai kowa yasan ke ba kaunar Allah kike ba,amma shi audu bah aka yake fadi ba sunan ma da kamar da larabci yake fadinsa “dr hafsa tamike tsaye ta dauki handbag din da wayar ta sai ledan atamphar kafin tace sai kiyi kuma kawai dais hi haka yake fadan sunan ne sai kiji kamar larabci amma dai sunan ta Asseeyah ni nafita,daga haka dr hafsa ta juya tayi tafiyan ta, inna data kasa shiru tace kai amma gaskia audu bai kaunar Allah ashe duk zaman nan damuke sunan matar nan asiya yaja bana kiran sunanta saboda kar na fada a raina ni ban iya ba, ni fa idan naji yafada sai nayi tunani sunan larabawa ne ashe duk kwarewa ce,sai kuma tayi shiru ta tabe baki tace tau dan kanshi.Jin knocking din da akeyi yayi yawa yasata fara tunani ko dai shine yafita kofan ta rufe,sai kuma ta tabe baki ta juya sake buga kofan akayi ahankali ta tashi ta bude veil din abayar ta tayafa bude kofan bedroom din tayi taga bai parlor ga kofar kitchen din a rufe tau kodai shine tasamu kanta da tambayar kanta,ahankali tasa hannunta kan Handle din kofar kamar kuma mai tsoron bude kofan tace waye?dr hafsa da har tagaji da tsayuwa zata juya a tunaninta ko basa nan tace nice,Kamar taso tagane waye amma kawa isai da bude tsaf tagane dr hafsa,murmushi dr hafsa tayi tace da har zan juya nayi tunanin ba kwa nan ai,aydarh tayi murmushi kadan tace ina wuni?sannu,dr hafsa ta amsa mata,anan parlor suka zauna babu wanda yakara magana cikin su,so take ta tuno abunda malik keyi idan anyi guest,kitchen tashiga ta dinga bin koi na da kallo pure water tagani asaka biyu ta dauka ta daura a plate takawo wa dr hafsa din kafin ta koma ta bude warmer da ta gani a kitchen din abinci daya dafa ne da rana white din ta zuba a plate tasaka mata stew kadan sai salad takawo wa dr hafsa,dr hafsa na murmushi tace lah ai da baki kawo abinci ba yanzu

naci abinci kafin na fito kuma ma sauri nake,aydarh tace aa fa sai kici ko kadan ne “kanta akasa tana wasa da zuben hannunta kadan kadan dr hafsa ke mata fira murmushi kawai ne nata dan bata cewa komai itama dr hafsa din bawai tafiye surutu ba, ba laifi taci abincin tasha ruwa,ta kalli aydarh tace mai gidan baya nan ne?tsaf aydarh tagane wanda take nufi hakan yasata cewa erh”dr hafsa tace kinga sauri nake jiya ne yakai wa inna wannan atamphar yace tabani na kai maki dinki, so bansan measuring din ba,aydarh tayi shiru kafin can tace kawai ayi tunda ban san style din ba,dr hafsa tace aaa ga styles nan kala kala sai wanda kika zaba, murmushi tayi tace aa ayi kawai,dr hafsa tace no kafin tayi unlocking wayanta tashiga photos screenshots din styles din dinki ta nuna mata wanda tayi a ig, ita dai aydarh sai bin dinkuna da kallo take, bata wanda zata ce yayi mata ba amma hakan nan ta zabi wani free straight yayi kyau sosai, dr hafsa tace kuma zai maki kyau sosai masha Allah, miye measuring din nan aydarh tagaya mata domin komai nata tasani kuma bata mantawa,har kofar part din ta rako dr hafsa din tayi mata godiya ta wuce, tana dawowa ta kwashe plates din ta kai kitchen ta jawo takalman sa slippers dake nan bakin kofar toilet din ta bi da kallo ta dauke ido tana tsakin siririn tsaki iya lips dinta, hakanan taji tana son zama parlor sosai taji dadin zuwan dr hafsa ashe mutun rahama ne,duk sai taji bata ji wani damuwa Sosai, yau din nan, nan kan carpet ta zauna ta kura wa wuri daya ido,kara knocking kofar akai tanaji har sai da akayi sau uku kafin ta mike taje ta bude, Ramlah ce tsaye sai wani taunar chewing gum take kamshin karamin perfume dinta kalar na yan bori duk ya cika ma aydarh hanci babu alamar wasa ko wani murmushi a fuskanta ta koma real aydarh ta na can baya take kallon Ramlah da kusa shidewa wajan kallonta batayi tunani takai haka ba domin bata taba yi mata kallon gab da gab ba, maganar da aydarh tayi yasata dawowa cikin hayacinta,tace lapia? Ramlah ta aro jarumta domin kwarjinin aydarh yasata firgita daidai nutsuwan ta tayi kafin tace lafiyan kenan yayah malik nake nema idan yana kije ki ce masa gani nan nazo,kallonta tayi sama da kasa kamar taga wani abun kyama.

Ganin irin kallon datake binta shi yasa Ramlah gyara tsayuwar ta, Aydarh bata ce komai ba tajuya ta koma ciki tayi banging door din a fuskar Ramlah,wani irin mugun ashar Ramlah tayi “ kamar zatayi hauka a inda take tsaye ita tayi ma wannan rashin mutuncin tau wallahi bazata yarda ba.fadila tayi shiru tace umm ni wallahi baki birgeni ba da baki tatakata a wajan ba tau wacece ita haka?maman Ramlah datayi shiru tace nidai ku bi komai ahankali kar fa ace mutanan batar da sahu sukayi ,kuyi masu rashin mutunci ayaye ku a daure wallahi,fadila tayi kasa da murya tace wallahi fa

maman Ramlah ni har tsoro suke bani daka gansu fa kaga kudi da mulki kar fa dai yaran sarkin makka ne?ramlah tayi wani uban tsaki tana hararar fadila da maman tasu baki daya tace ku fa matsalana da ku har yanzu kanku a duhu yake kauyawa ne ku wallahi bacin haka miye wani abu danganta su da wani sarkin makka miye ma tau zai kawo su nan in har hakane?kawai da wallahi abunda tayi mun sai narama shine kawai,duk shiru sukayi babu wanda ya tanka ta cikin su. Ko data koma daki tunanin ramlah ta yakasa barin ranta,tau wacece wannan kazamiyar da zata zo neman sa kuma,sai kuma taja dogon tsaki tace miye ruwanki dashi, nan take abunda yafaru da inna tazo yadawo mata a rai tayi tsaki yafi a irga,kwanciya tayi tana ta juye juye idonta ya sauka kan wani karamin littafi na azkar na shi ya manta shi a carpet din dakin jiya,ahankali ta mike ta dauka budawa tayi tana dubawa sosai ta maida hankalinta wajan duba littafin bai fi addua biyar tasani a ciki ba tunuwa tayi da yarda yake raira karatun al quraani dazu ,wannan ne karon farko a rayuwanta dataji tana so sanin wani abu game da addini bayan wanda tasani wannan ne first time datayi hawayen kin tsayawa tasan abubuwa game da addini babu yarda oum batayi ba rufaidarh ma haka amma tasamu daurin kugu wajan abba nakin tsayawa ta koya din,abubuwa dayawa gasu rubuce a littafin amma bata iya karantawa da hausa sai kuma larabci akayi rubutun,ta iya ranta hausa tsaf amma batasan ma’anan adduo’in ba.Ba karamin gajiya yayi ba a yau din nan aiki ne wanda bai saba dashi ba duk da yanda ya taso amma kwata kwata jikinsa ba mai son wahala bane,aiki ne wanda bai taba yin irinsa ba shiyasa ya sha wahala duk da matsayin shi na babba a wurin yanada hutawa amma dai yayi wahala sosai,jikinshi duk yabaci da cement haka kayanshi duk sunyi kura kadan bayan sun tashi aikin kowa ake basa 2500 cash a hannu,duk da kudin babu yawa he appreciate tunda dole ya bukaci kudi ko dan saboda aydarh ko dan saboda yanayin rashin lafiyan ta,yana shiga kitchen kawai yawuce ya daura ruwa a gas yasan batayi wanka rana ba tunda bai nan balle ya dafa mata ruwan wanka,sai da ya daura kafin yashiga toilet dinshi nan parlor yayi wanka tass kayan jikin shi ya mayar yashiga dakin da sallama kallonta yake ko kiftawa babu har yanzu littafin ke hannunta tana karantawa duk da ba fahimta take ba,abunda yakawo shi dakin yayi ya fita, sai dayashirya ya jika kayan da ya cire a bucket kafin ya duba ruwan,bucket din toilet din ta ya dauko yajuye mata yafita,Sosai ya ci abinci kafin ya koma toilet ya wanke kayan shi tass ya fita ya shanya dan kwanciya yayi kadan kafin a kira sallarh magrib.Awara yasiya masu yashiga gida domin ba karamin gajiya yayi yau din nan ba kuma kwana biyu ma sai ahankali yake jin shi kamar zaiyi fever,

AFTER A WEEK

Alhamdulilah malik yanzu har ma yasaba da aikin ginin dasuke ga ta gefe guda wani irin kirki Allh musa yake masa kamar irin ya jima da sanin shin nan yana matukar jin dadin aiki dashi Sosai.kallon shi yake ko kiftawa babu har yayi shiru kafin malik yace har fa kwana biyu kace dr ibrahim ya gyara zaman sa a kujeran clinic yace eh kwana biyu zamuyi can nasarawan tunda kai ne babban aboki kaga dole mutafi tare,malik yayi shiru can yace tau Allah yakaimu “dr ibrahim yace Ameen kafin yace ya aikin?malik yace aiki Alhamdulilah,dr Ibrahim ya saukan da ajiyar zuciya yace take heart malik in sha Allah zamu samu wanda yafi wannan nasan baka saba ba nasan daurewa kawai ka ke kayi hakuri in sha Allah zaa samu wanda yafi wannan ,malik yayi murmushi yashafa kanshi yace kaga tashi muje gidan inna zan karbawa ASSEIYARH dinki gun dr hafsa dr Ibrahim yace tau badamuwa muje nima kwana biyun bamu gaisa da innan ba.inna ta kalli dr Ibrahim tace daga ina kai kuma? Lahiya dai ko?ko rashin tsoron Allah yasa wata katuwa taje tace maka banda lahiya aaa wallahi lahiya ta lau tambaye audu gashi nan shi ai yasan gaskia,dr Ibrahim dayake kallonta yasaba da halin ta basa shiri sam kullun idan yazo sai sunyi fada “yace tau ke dakika ga nashigo daga gaisuwa kinga nace maki wani abu ne?inna dai tayi banza ta kyale shi ta tashi ta shiga cikin daki , hadaddan kwadon zogale day asha kuli da kayan hade ta fido cikin kula, tace tun dazu nayi maka audu tau da nayi tunanin baza ka zo ba ,har ina cewa yamma tayi na kai ma matar ta aje maka, malik ya karbi kular yace tau shknn inna nagode shidai dr Ibrahim bai ce komai bas ai danna wayarsa yake, dr hafsa ta fito hannunta rike da dinki aydarh gaisawa sukayi cikin mutunci “ tana tsokanar shi ango ango dr Ibrahim yayi murmushi yace fadi ki kara,inna tawani tsuke fuska ta kalli malik kafin tayi kasa da murya tace kaji wani jafa’I bikin da saura kusan kwana sha biyu miye abun wani fara kiran mutun da ango banda neman magana,Allah dai ya kyauta shi dai malik bai ce komai ba yanata kallon inna, dr Ibrahim ya mike tsaye yace ma malik ka tashi mu tafi ni akwai inda zani,inna tasaki baki tayi shiru tana kallon dr Ibrahim tace aaa kai kau ibrahin kazama abun tsoro yanzu kai ina ruwanka da shi wuri daya kuke kwana ko kuma wani neman maganar ne,dr Ibrahim tace ni fa bana son kina yawan saman baki idan ina magana kema ina ruwanki fisabillahi? Malik yayi murmushi yace yanzu duk hakura inna na bara nakai ma jikarki sakon zan dawo in sha Allah,dr hafsa dai tayi shiru batace komai ba. Tsaf ya gyara gidan koi na fess babu abunda ke bukatan gyara, ranar tafara sa dinki Sosai take kallon kanta a mirror din window bedroom din tayi wani irin kyau mai fuzga bakaramin tuno mata da ummi atamphar take ba murmushi tayi

ahankali kafin ta dauke body splash din ta fesa kanta tasamu tayi parking sumar can kasan kan babu saloon amma yayi matukar masifan kyau kallabin ta daura all back kafin ta dauki well iron hijab din sabowan wanda bata cika sawa ba tasaka malik ne ya goge hijab din da iron din da ya siyan masu,a parlor ta iske sa yashirya yana jiranta babu wanda yayi ma wani magana dr hafsa ce tace mata tazo tayi mata calaba daman tana so batasan gidan ba kuma batasan yarda zata ce mata bata sani din ba ,sai gashi malik yace tashirya yarakata gidan inna,har yanzu magana bata shiga tsakanin su duk da a yanzu suna zama parlor tare amma babu wanda ke ma wani Magana.

Sa kai kawai yayi,yafita ganin hakan yasa ta bi bayansa da harara tana tura masa baki " shi yasa key ya rufe kofan part din nasu yana gaba tana biye dashi ba,maman Ramlah dake wanki a can ventilation dinta har ta hango su ,dasauri tanuna ma,fadila dake nan tsaye tana sanaar surutu kamar mai cutan dimi, itama kallon tabi su dashi kamar zata hadiye su, cikinsu babu wanda ya juyu balle ya kalli iskan daya kwaso su,tafiya yake kamar wani boss sai sauri yakeyi fita sukayi kofan gida,ya tarar musu keke kallonshi take ko kiftawa babu bata shiga napep din ba, bai lura da bata shiga dan shi har yashiga ya zauna ,can ya lura da ita da kallon datake masa, ahankali yayi kasa da murya yawani kafe da ido yace ko komawa zaki ni natafi? Tawani juyan da kai ta balla masa harara kafin tace ina fa inna tacemun anan anguwan suke?bai ce komai sai yayi shiru ya saako daga napep din side din datake tsaye yaje yakama hannunta tawani zaro ido tana kallonsa bai ko kalleta ba ya turata napep din shima ya zagayo yashiga yace wa mai keke sutafi har suka isa kasuwan babu wanda yayi ma wani magana cikin su suna sauka yafido kudi yabiya mai keken ganin yasauka yasa itama ta sauka tanata kallon inda suke ko kiftawa babu kamar tana tsoron wani abu haka tayi raurau da ido tace masa ina ne nan? Gaba yayi batare da ya kalle ta bayace siyar dake zanyi,duk da abun datake ji bai hanata hararar shi ba yana juyuwa karaf suka hada ido yaganta tsaf bai ce mata komai ba dan wannan bashi bane first time daya taba kamata tana hararan shi ba,duk inda yasa kafanshi sai tasa nata kamar wani zai dauke ta indan ta daina binsa,kanta ta saukar kasa ganin irin kallon da mutane ke binsu dashi, wani babban shago suka shiga babu abunda ake siyarwa sai inner wears Abayas da kuma bubu gown pure cotton, gaisawa sukayi da mai shagon mace ce wata hadadadiyar Hajiya tasha atampha vilisco taci uban gayu,sannu da zuwa tayi masu hadda wurin zama shagon sai kamshin turaran wuta yake da khumra kasancewar duk tana siyarwa, tambayar su abunda suke bukata tayi ya kalli aydarh sannan ya mayar da kallonsa kan matar yace inner wears zata zaba daga nan bai sake magana ba ya saukan da kanshi kasa

yana latsa wayanshi, mata tace Hajiya mi da mi zan dauko maki?sai da ta dago kai taga bai kallonta kafin ta yi ma matar nuni da hannu wasu classic brassiere ta nuna mata masu tsada saboda hakan ma yasa ta fidda su gefe guda foreign ne matar tayi murmushi tace tau size nawa aydarh tafada mata cikin wannan voice din nata, matar ta bi aydarh da kallo a ranta tana mamakin size din da ta gaya mata anya bai mata yawa ba,batace komai ba ta dauko mata wani hadaddan black lace form bra sai baby pink dark green da kuma red aydarh tabi su da kallo imagination din nata ne na gida, tasan price dinsu bai kai natan ba,amma duk da haka sunada kyau pants tasa aka dauko mata this time matar kasa shiru tayi sai datace diyata anya size din daidai kika fade sa?aydarh tayi kasa da kai sannan ta gyada mata kai malik najin duk abunda ke faruwa amma ya ki dago kansa balle ya kalle su ita dai aydarh takagara agama su tafi bata son ya dago kansa yagani,shima pants din kwara hudu ta dauko mata kowani irin bra din, matar ta tambaye ta hadda undies aydarh ta girgiza kai kafin tace aa sai sannan malik ya dago kai yace shima a saka kwara hudun,bai jira amsar matar ba dan yasan ma aydarh bazata ce komai ba ya fita kofar shagon, wani bubu gown ya dauko light purple mai haske Sosai duk jikinshi sai flowers din jiki black har zip din gaban gown din purple ne da black mai shining ba karamin kyau tayi irin ta yan gayu na sosai da sosai yashigo dashi rike ahannu babu wanda ya kalla cikin su ya ajiye ya koma inda yake zaune ya zauna matar tayi packaging rigan da mayafinta babba ne ba laifi tana yabon zaben dayayi kafin tace tau ranka ya dade an mance da inner caps suma muna siyarwa na lura matar taka bata son kana wahalar kashe kudi, malik yayi murmushi kadan yace tau ba damuwa hajiya a dauko guda hudu shima aydarh najin su dai batace komai ba matar ta dauko wani karamin basket cike da plain inner caps yards din masu kyau masu tsada, ta ajiye gaban malik tace zabi”sai daya kalli aydarh kafin ya maida duban shi a basket din light purple yafara daukan mata sai ya dauki black da pink sai wata kamar ash kamar grey, duk kayan ta hada masu cikin ledan shagon ta lissafa masa kudin ya fido 35k daidai yace ta bata turaran na 5k matar ta washe baki tace tau shknn turaran kaya dana jiki ta dauko ma aydarh masu dadin kamshi Sosai tayi packaging din a tasu leda kafin ta hada su waje daya cikin ledan kayan godiya matar tayi masu sukayi bankwana har zasu fita kafin tace yawa ranka ya dade dan Allah zan iya samun number madam ko naka idan kuna son gyaran jiki ko lalle duk ina yi har kayan sawa na maza ina siyarwa, kafin ta rufe baki aydarh tace “no”shidai malik baki bude yake bin aydarh da ta tsare shi da ido da kallo tawani hada fuska kamar irin yaji tsoron ta kar yayi din nan, sai ya juya ya kalli matar yace sorry Hajiya zamu dawo wata rana ai in sha Allah ,matar tayi murmushi tace babu komai Allah yatsare,suna fita

tace wai bansan mi ma yahanani tambayar su daga wani kasar suke ba wallahi sai kuma tace umm ina fuskar hakan cikinsu kowa kamar sarki duk sun tsare gida babu sakin fuska amma akwai dan banzan kyau wai Allah, ji yarinya karama amma ji body structure shiyasa aka ce natural daban yake da artificial mu dake bankar supplement ina zamu hadda kanmu da jikin yarinyar nan. Cikin 50k din da Allh musa yabashi jiya kyautan Allah saura 15k flask yasiya karami mai madaidaicin kudi wanda zai dinga ajiye mata ruwan zafi saboda yanayin aikin shi yanzu kusan sai yamma take wanka idan tayi dasafe mamadin tayi da rana sai yamma ga garin damuna gudun shi kuma sanyi ya kamata, man kitso yasiyan mata da pink oil sai comb da tsinke tunuwa daga nan gidan inna zasu wuce dr hafsa din tayi mata calaba kamar yarda inna ke gaya masa dan shi bai sani ba tunda ba wani shiga harkan juna suke ba,plate shoe yasiyan mata masu kyau sai yasiyan ma inna daya itama da sabulu da klin leda daban ya fidda kayan inna ita kuma yabar mata nata wuri daya babu abunda ya siyar ma kanshi,napep ya tarar masu suka isa har kofar gidan inna yabiya mai keken kudi kafin ya mika mata ledar kayan da yasiyawa inna da man kitso comb da tsinke din kallon shi tana turo baki tace ina kaima shiga zakayi ? Hannushi daya yasa cikin Aljihu yawani daure fuska yace eh shiga zanyi amma ke zaki rike wannan din,bata sake cewa komai ba tayi gaba ta bar masa kayansa a nan tashige gidan inna dasauri,bin ta ya dinga yi da kallo bata magana batada hayaniya amma akwai taurin kai da rashin kunya bakar magana kam sai wacce ta manta kawai ke bata gaya mashi girgiza kai yayi ya dauki kayan yabita baya inna nagani shigowar su ta mike tsaye tace kai kai kai kune tafe oyoyo asiya sannu da zuwa aydarh tayi murmushi ta dukar da kai kafin ta russuna tace ina wuni? Inna ta washe baki tace lahiya lau asiya ya gidan da audu baki daya?aydarh tace Alhamdulilah,malik ya bata fuska yace ni sai na koma ai,inna tayi kasa da murya tace ash eke dashi kuka zo aydarh dai kanta nakasa batace ma inna komai ba,inna ta kalli malik tace indai ba aikin sintiri kasamu ba yaci ace kashigo tunda kuka zo,inna takama hannun aydarh suka shiga cikin daki aka bar malik nan tsaye,inna ta kalli aydarh tace wallahi nake gaya maki tau bayan ma ba kaunar Allah yake ba tun farko basai ya gayaman sunanki haka ba fisabillahi,aydarh dake murmushi ta gyada wa inna kai,inna tacigaba dacewa “tau bai fada bas ai dai naji ya kira wani suna da larabci nidai ba fahimtan sunan nake bas ai fa ranar matar dake zaune nan gidan,wa take da suna ma hafsa ita ke fada mun sunan naki nidai ba ma yarda nake da maganar ta ba,sai dana tambayi shi audun da kanshi yake ce man ai sunanki haka aydarh dai sai murmushi take,malik yace ma dr hafsa suna ciki ni tafiya zanyi yau inna bata ni take ba daman kuma ba zama zanyi ba dr hafsa tayi murmushi tace tau kashiga sai kuyi bankwana da innar “da

sallama yashiga dakin inna ta amsa masa kafin yace ga wannan babu yawa inna,inna tabi ledar da kallo kafin tace Allahu akbar audu nagode sosai Allah yasaka maka da alkhairi Allah yakawo zuri’a ya dayaba Amin dan nabiyyu rahamati malik yashafa kai yace Ameen inna ni bara na wuce idan anjima sai nadawo in sha Allah,inna tace tau Allahu yasha, ledar man kitso da pink oil din ya bar mata sai comb da tsinke tunda yasan dasu zaayi amfani babba leda kayan nata da turare ya dauka yafita dash isai dayayi enough cefane wanda zai ishe su “kafin yatsaya shago yasiya macaroni da pasta rabin cartons sai shinkafa tiya biyu da kanannun indomie carton daya sai maggi leda leda da spices sauran 15k din tass ya kashe . Sai da ya gyara koi na tsaf yashirya duk abunda yasiyo a muhallinsu inner wears din ma cikin wardrobe yasaka mata perfumes din ma bai fida su a ledan su ba yabar su, kitchen yawuce ya daura jallof din pasta da kifin da yasiyo sai daya gama kafin ya daura mata ruwan wanka sannan ya zuba pasta a plate wanda favorite dinsace ya zuba sauran a warmer, yaci ya shiga yayi wanka ya gaji bacci yake son yi dan akwai nepa sai daya juye mata ruwan zafin a sabon flask din dasuka siyo ya kai mata bedroom kafin ya dan kwanta.

Inna tashirya ta dauki mayafinta da jikka,tasaka sabin takalmin da malik yakawo mata tace tau ni natafi asiya nasan kafin na dawo kun tafi gida in sha Allah gobe na shigo, aydarh tace to inna dr hafsa takalli inna tace tau hala idan kikaje wajan suna can zaki zauna?inna tace ina ruwanki nifa bana so shishigi da neman wajan zama dana tashi fita na kinga nayi magana dake baiwar Allah?dr hafsa tace Allah yabaki hakuri sai kin dawo na daura maki girkin ne kafin ki dawo?inna bata tanka ta ba tasa kai ta fice,dr hafsa tayi murmushi ta kalli aydarh tace haka nake fama da ita amma kullum cikin cewa take hakurin zama nake da ita,aydarh tayi murmushi tace she is really funny,dr hafsa tace ai ina tunanin mijinki ne kawai ke iya zama da ita shima kuma dan dai Allah yasa tanaji dashi ne aydarh batace komai ba dr hafsat ace mu fara ko? Aydarh ta gyada kai tacire hijab da dankwallin kanta tana warware uban tulin gashinta daga cikin ribbon dr hafsa ta dinga bin gashin da kallo tace masha Allah shiyasa bakya son kitso, aydarh tayi raurau da ido damuwa kan fuskanta tace akwai zafi hannunki ko?bakaramin dariya aydarh taba dr hafsa ba yarda tayi maganar kamar wata yarinya she always behaves childish dr hafsa tace no ai calaba bai da zafi ko kadan yallabai ma dan bai iya bane da ko shi ai sai yayi maki calaba aydarh bata fahimci abunda dr hafsa tace ba shiyasa tayi shiru, cikin few minutes aka fara tsagan calaba aydarh dai hadda kanannun kwallan ta a ido tasa bayan hannu tashare su,saboda dariyar da dr hafsa ke mata,dr tace nikam dai aydarh naso naga ranar haihuwanki ai wannan sai Doctors din Nigeria sun

taro a kanki,kice hakanan ma yallaban ya matsu a samu cikin ashe matar tasa ragowa ce, aydarh batasan time din datace shi ne yace haka? Dr hafsa da har yanzu da sauran dariya a fuskarta tace eh cewa yayi nayi maki p-test ashe ashe ba jaruma bace matar tasa,aydarh batace komai a ranta take tunanin time din daba ta da lapia kenan hadda abunda yasa akayi mata kenan?babu mai bata amsa yasata yin shiru tana cigaba sauraron labarin da dr hafsa ke bata,dr hafsa tace wallahi aydarh wasu matan auran sai ahankali aydarh tayi murmushi dr hafsa ta cigaba dacewa wata friend din ace fa suka rabu da mijin kuma fa laifinta ne shiyasa yanzu duk ta zauna labarin sa takeyi,aydarh dai na sauraron dr hafsa tana fahimta labarin amma batasan ma’anar labarin ba dr hafsa tace kiji fa a zamanin nan wane namiji ne zai dauke ma shara wanke wanke girki ke hadda fa wankin bayi da kayan sawa,kiji fa ai wallahi indai ba shanye shi tayi ba babu namijin da zai maka irin wannan a yanzu,aydarh dai tayi shiru aranta take juya maganar dr hafsa din yanzu ita malik dakeyi mata duk wannan itama shanyesa tayi tau miye shanye war?sai kuma wata zuciya tace mata aa ai auranku bakalar na kowa bane,dr hafsa tace tau the worst part of it ma abunda yasa har maganar divorcé yashigo ciki fita take bata tambaye sa ba shikuma yaji bazai iya ba,aydarh tayi shiru kafin tace auntie hafsa minene shanyewan? Dr hafsa tayi murmushi tace eh gaskia ke ba lalle bane ki sani idan aka ce mace.

Aydarh dai tayi shiru sai sauraron bayanin da dr hafsa ke mata take, batace komai ba har sai da dr hafsa tayi shiru kafin tace,idan matar ke yin komai fa?shine mijin ya shanye ta dr hafsa tayi wani irin dariya tace wallahi ke ma aydarh tau a normality na alada da addinin musulunci shi ya daurawa mace wannan nauyin na girki shara wanke wanke kula da yara a gida shi kuma mijin ya tafi office Ko wajan sanaar shi yafita ya nemo maku abunda zaku ci da duk wani abubuwa na yau da kullun,aydarh ta sauke wani irin ajiyan zuciya,tau ita miye matsayin auran su da malik shima ai aure tunda tasan aure dole sai da sadaki kuma aie aure aure ne,sai kuma wata zuciya tace mata aaa aurenki dashi ba kalar na kowa bane, bakya sonsa ko kadan sai ma tsoronsa da haushin sa dakike ji shima bakya sonki wannan ai ba aure bane,ta tura baki ahankali can ciki tace Mugu kawai,tunanin ne fal aranta so take dai tasan miye matsayin auran su da malik miye kuma sharudan auran da dr hafsa tace duk macan da bata cika su ba makoman ta wutan jahanama,bakaramin tsoron wuta take ba tun tana yarinya tana iya tuna time din rufaidarh ke gaya mata zafin wutar duniya ba komai bane kan lahira 1%din wutar lahira ne,wani irin yankewa gabanta yayi ya fadi batasan ta yarda zata fara tambayar dr hafsa ba shiyasa tayi shiru,wani irin

kyau calaban keyi ba fatar kan fari tass yarda take fitan da tsagan kamar sai tasaka ruler tayi ta daidaita ita kanta dr hafsa duk zaman ta boarding bata taba sanin ta iya calaba ba kamar yau datayi wa aydarh masha Allah, yi ake yi ake amma gashin kamar ana kara masa yawa,duk da manyace akeyi, tun dasukayi magana da dr hafsa take ta juya zancan a ranta so take ta tambayi dr hafsa amma batasan ta yarda zata tambaye ta ba “can wani dabara ya fado mata a rai,tayi kasa da murya kafin tace auntie sai kuma tayi shiru ganin haka yasa dr hafsa cewa ina jinki aydarh,ajiyar zuciya ta sauki kafin cikin nutsuwa tace daman auntie a can akwai wata friend dina ita da mijinta basa son juna kwata kwata sun tsani juna ko magana ma basa yi kuma duk wani aikin gida shi keyi komai fa har ruwan zafi shi ke dafa mata tayi wanka,idan kinga sunyi magana sai idan batada lapia kawai fa, dr hafsa tace subhanallah amma gaskia wannan bata son ciwon kanta ba wait ba ma wannan miyasa sukayi aure while basa son juna?aydarh ta ware hannu tace nima ban sani ba kawai dai a daura ma su aure babu biki babu komai kawai anan take aka biya sadakin akayi komai a gabansu, dr hafsa tace duk da haka bata da wayo dai ai aure aure ne duk da bata son shi ai aljannarta nakasan kafar sa,kuma aure dole mata tayiwa miji biyayya ko da bata sonsa kinga shi ko da baya sonta alama ya nuna cewa yana tausanta kuma ya rike amanar Allah ita kuma ranar gobe kiyama sai Allah yakamata da laifi,aydarh naji duk abunda dr hafsa ke fada tayi shiru tana tunani tau ita ya zatayi? Har ga Allah bata son ma abunda zai dinga haddata da malik sam,dr hafsa tace tau kuma shi bayan haka baya siya mata komai?aydarh ta girgiza kai tace he is trying his best ya mata abubuwa ,dr hafsa tace kingani ba that’s means shi yasan hakkin aure kenan yasan miye aure ,ita kuma da bata da hankali saboda bata son sa kuma bata neman rahamar ubangiji ai ni atunani duk wani rashin kauna yakare daga ranar da aka daura ma aure da mutun,ba kamar idan yana kyautata maka kamar yarda wannan mijin kawar taki keyi mata shikenan rashin so ya kare ko da bata sonsa tayi hakuri ta dinga sauke hakkin aure yarda ta hakura har tayi biyayyan iyaye haka ya dace ta hakura tayi biyayyan Allah tasauke hakkin mijinta a kanta ta sauke hakkin gidan auranta,ta sauke ajiyar tace tau auntie ita fa batasan komai na aure ba tace,dr hafsa ta saki calaban datakeyi yanzu ta zagayo ta kalli fuskar aydarh tace daman akwai macan da batasan miye zaman aure ba aydarh? Aydarh da gabanta keta bugawa tace nima dai bansani ba amma haka tace batasan komai na aure ba dr hafsa ta dinga salati tace tau bata da yan uwa ke bata da mahaifiya ma forst? Aydarh ta girgiza kai tace bata da yan uwa tanada mahaifiya,dr hafsa tace tau miyasa ba a fada mata ba? aydarh tace itace bata tsayawa ta saurara kullun bata zama inda kowa yake idan ta tafi school shikenan wani time enma har sai tadawo nan kasar

sannan zatayi magana dawani,dr hafsa tace gaskia kam ta cuce rayuwarta bata kyauta ma kanta ba kuma duk mai daure mata kugu tayi wannan abun shima ya cuce ta,ta tubar ma Allah ta fara shirin koyon rayuwa saboda batasan komai ba,aydarh tasauke ajiyar zuciya har zatayi magana sai kuma tayi shiru,can dr hafsa tace yawa mu'amalar aure fa? Aydarh bata gane tambayar da dr hafsa tayi mata bah akan yasata cewa na'am? Tace kina nufin wani abu bai taba shiga tsakanin su ba like sex or something like that? aydarh tawani zaro ido ta daga kanta tana kallon dr hafsa sai kuma tayi maza ta saukar da kanta kafin ta girgiza kai tana wasa da hannunta tace aaa dr hafsa ta rafka salati tace yau mun shiga uku ke yanzu a matsayinki na kawarta kuma ke kinada aure kinsan komai na aure zaki barta tana wannan rashin hankalin da wannan ai hauka ne , aydarh tace ranar ne ma tana shafa yazo yaganta da towel shine fa ta dinga kuka,dr hafsa da bakinciki ya cikata tace tau Allah ya kyauta amma tanaji tana gan isai ya auro wata,ko gwal ce ita ai sai haka wallahi kuma ranar lahira sai Allah yakamata red handed tunda ita shashasha ce wawiya har ga Allah dr hafsa bata kawo aydarh bace tayi tunanin kawar ta tace dagasken,Aydarh dai bata kara magana ba jikinta duk yayi sanyi tau ita yazatayi kenan babu abunda yafi firgita ta irin wutar dazaa sata kamar yarda dr hafsa din tace, gabanta sai faduwa yake tayi lamo dr hafsa ta cigaba da mata calaban babu wanda yasake magana cikin su aydarh hankalin ta baki daya ya koma kan maganar dasukayi da dr hafsa sai saka take da warwara.Da sallama yashigo gidan dr hafsa ta amsa masa,bai san inna bata nan ba kawai yasa kai yashiga dakin dr hafsa tace ahh yallabai sannu da zuwa ina wuni?malik yadanyi murmushi kadan yace lapia hafsa sannu da aiki dr hafsa tayi yar dariya tace yawwa ai dole kamun sannu,haka kuke da gashi tabarakallah,shidai malik murmushi yayi ya dinga bin gashin kanta da kallo calaban tayi mugun kyau masha Allah kamar karya dauke idonshi daga kallon calabar mutun ne shi mai mugun son gashi yana masifan son yaga anyi kitso kuma a da har parking gashinsa yakeyi ko kuma su aysha suyi mashi kitso sai daga bayan nan ne ma yake aski ya ke dan rage ta kadan, can yayi kasa da murya yazuba wa bayan ta ido murya babu wasa yace ko baki ji na shigo ba dabazaki gaishe nib a ko kicemun sannu da zuwa,Kamar daga sama taji maganar sa tayi niyyar daya shigo ta rufe kanta amma bata son dr hafsa ta fahimce komai yasata barin kan aka cigaba da kitson, sai da murda masa baki duk da bata ganin sa kafin ahankali tace in anima baka gaishe niba da kazo ?bai san ranin datayi masa ba har yakai haka ba,yayi tunani zata gaishe sa din ko dan dr hafsa din,bai ce komai ba yayi shiru,sai dr hafsa ce tayi dariya tace tau ai kinsan rijalu su kullun sun fi son ayi masu,aydarh dai tayi shiru,malik din ma bai kara cewa komai ba kuma bai fita ba,har suk agama calaban tass Allahumma bareek

bakaramin kyau calaban yayi ba akayi parking dinshi can kasa tasa hannu tayi mashi wani irin style kafin ta mike ta dauki gashin da ya zuba kadan zata zubar a dustbin sai yanzu dr hafsa taga yarda dinki ya zauna a jikinta sai yanzu ta sake ganin wacece aydarh sai tunanin ta yabata ko dai sake p-test din zasuyi, maybe akwai cikin ko boyewa yayi tunda alama yanuna kamar hips ya shiga da boobs dinta yarda shape din jikinta yafita kallo daya malik yayi mata ya dauke ido yarda take tafiya kamar da gayya yasa shi dauke kai , shigowa dakin tayi ta zauna kusa da dr hafsa idan ta ajiye hijab dinta kallabinta take kokarin daurawa dr hafsa ta kalli malik tace yallabai nace ko sake mata p-test din zaayi naga kamar akwai shi maybe ko shigewa yayi ba? Malik ya shafa kasa yace anya kau ina ganin no need,dr hafsa ta gyara zaman tayi kasa da murya tace aa yallabai kamar fa akwai cikin ko dai shigewa yayi cikin hips da boobs ko kuma ranar ansamu matsala ne aydarh dai kalli malik suka hada ido sai kumayi tayi kasa da kai,malik yace ma dr hafsa tau shknn zamu zo din dahaka ya mike yayi ma dr hafsa godiya yace ki same ni a kofan gida, dr hafsa tayi mata sallama aydarh tace thank you auntie “dr hafsa tace don’t mention aydarh sai anjiman ku,ku gaida gida,a kofan gida ta same sa tsaye yana jiranta yana ganin ta fito yajuya yatafi ta bisa baya daidai kofan shiga gidan suka hadu da Ramlah tsaye ta tare kofan gidan tana ganinshi tawani washe baki cike da bariki tace welcome sir malik yace thanks a takaice yayi hanya zai wuce ta wani sha gabansa wani kalan wawan kallo yayi mata yahada fuskar sa yawani hada giran sama da kasa billahi yarda yayi din kamar zata suma, gathering courage tayi tawani lankwasar da murya tace karar matarka na kawo maka aydarh najin haka tawani hada rai tayi wucewanta tana tafiya kamar batasan taka kasa, batasan raini ita kunyar kanta ma zataji ace ta tsaya tana magana da wannan trash din,malik ya ja da baya ya gyara tsayuwar sa bai ce komai bay ana sauraron ta tace kofan part din ku ta sakar mun a fuska daga naje duba ko kana nan malik bai ce komai ba yayi wucewar sa yabar ta nan tsaye kamar status.

Toilet tashiga tayi alwalla kafin tafito ta chanza kaya ta hau prayer mat ta kabbara sallarh shigowa yayi dakin ganin tana sallarh yasa shi zaunawa kan katifa har sai da ta gama sallan ,yace miyasa kika buga mata kofa a fuska aydarh tawani hada rai ta juyo tana face dinsa sai kuma ta juya kai tace to ita miya hanata ka tambaye ta abunda tamun,shi wallahi dariya ma ta basa yarda tayi din yayi kasa da murya yace ai nasan ita ke da gaskia shiyasa kuma ni naso ma ace ta rama,aydarh ta mike tsaye tace to ai sai ka turo ta tarama din, bata tsaya jin abunda zai fada ba tayi fitan ta parlor ta bar masa

bedroom din.

Kitchen ya shiga ya zuba mata pasta daya dafa a plate yazo parlor ya ajiye mata gabanta without saying a word ya shige toilet din nan parlor yafara wankin kayansa jiya yayi mata nata wankin,bin bayansa tayi da kallo ta kafin ta mayarda idonta kan plate din ahankali take cin abinci cikin nutsuwa har tagama kitchen ta kai plate din ta ajiye ta dinka bin kitchen din da kallo ko dauke ido babu maganar dr hafsa ce ke dawo mata fresh a brain tama rasa kalar tunanin da zatayi,juyawa tayi tafita bedroom din ta koma ta zauna ta zubawa waje daya ido,yanzu haka na nufin ita zata cigaba dayin duk wani aikin dayake yi?sai kuma ta girgiza kai a ranta tace ai Allah bai kamaki da laifi tunda shi keyi bake kika saka shi ba dawannan tunanin ta zame ta kwanta amma sam zuciyanta bai yarda da wannan conclusion din,ahaka har bacci yayi gaba da ita da tunanin a ranta.Tun safe yake jin yanayin jikinsa babu dadi yasan kuma cewa maybe ciwonsa ne zai taso sam sai yabar hakan a ransa ya cigaba da addua domin bai san yarda zaiyi ba idan ciwon nashi yataso a yanzu,ko daya dawo sallan isha’I da kyar ya kwanta kan shimfidar sa dayayi anan parlor wani irin yanko masa zufa keyi lips dinsa har hadewa sukeyi yarda ciwon ke masa a yau sai yaji kamar ransa zai fita he is seriously in pain his condition is much critical babu abunda yake iya furtawa sai inalilahi waina illahil rajiun zuwa wani lokaci he is trying much to breath in and out numfashin sa ya toshe waje daya salatin ma yakasa bakin shi yahade waje daya.So take yashigo ta tambaye sa inda littafin azkar dinsa da take karantawa yake shine kawai abunda takeyi yanzu zuwa yanzu har tafara fahimtan wasu abubuwa daga ciki tafara gyara kura kuranta na sallarh shiru shiru taji sa bai shigo ba yasata bin kofan bedroom din kallo kamar zata hango sa ta kofan tashi tayi ta yafa mayafin abayanta tana tafiya ahankali har tafita parlor ganinsa tayi a kwance yayi facing wall tasan ba bacci yakeyi ba maybe da gangan ya dauke littafin daman dan yasan zata zo nema shine yake wani pretending as if he is sleepy,batace komai ta zaune can karshan parlor tayi raurau da ido kafin murya can kasa tace ni kabani,shiru bai tanka ta ba bakaramin haushi abun yabata ba,bata gaji ba tace ai nidai babu ruwan ka dani tunda bana taba ma abu wallahi,still malik bai tanka ta basai wani irin numfashi da yasaki kamar wanda aka zarewa numfashi gabanta ya yanke yafadi ta mike tsaya batasan abunda yasa yayi numfashin amma numfashin dayayi Kamar wanda ke struggling da breath ensa ahankali ta matsa kusa dashi tana kallon shi,juyuwa yayi jikinsa ya jiqe sharkaf da zufa ganin yanda yake zufa yasata binsa da kallo ahankali ta daga idonsa da kyar yayi mata alama da hannu

nata zo,yarda gabanta ke faduwa kamar zai fito waje yasata bin bango har ta karasa kusa dashi ahankali yake fadin ruwa ruwa bataji da kyau bah akan yasa cewa baka da lapia ne hankalinta a tashe gyada mata kai yayi ahankali kuma yasake buda baki yace ruwa dasauri tashiga kitchen ta dawo hannunta rike da pure water yakasa daga hannunsa balle yakarbi ruwan yasha ganin hakan yasa ta fasawa ta kai ruwan daidai satin bakin sa daga nan kwance tabasa ruwan yama kasa sha sai zubewa yakeyi ta gefen bakinsa, yarda jikinsa yake kyarma bakaramin daga mata hankali yakeyi ba tarasa abunda zatace masa,ahankali tace sannu,hannu yasa ya rike nata hannun tanajin yarda jikinsa yayi mugun zafi he is running temperature ahankali tace sannu mike maka ciwo?kanka ne?you are running temperature mike damunka yarda take maganan muryanta very slow and innocently kamar zatayi kuka ,daurewa kawai yake amma ji yake kamar zaa zare mashi rai cikin shi nawani irin masifar ciwo har yanajin yarda jinin shi ke gudu a veins dinsa ,aydarh dai tarasa yarda zatayi banda bin sa da ido babu abunda take bata son taga wani na ciwo tana da mugun tausai wayar dake flashing light wanda a silent take ta kalla kiransa ake da kamar kar ta dauka sai kuma ta kai hannu ta dauki wayar kallo daya tayiwa sunan mai kiran tagane ko waye sallama akayi cikin sanyin murya ta amsa daga can dr ibrahim yace ahh madam ina wuni,ina wuni tace masa kafin yace baya kusa ne?aydarh ta kalle shi ganin yarda yake kyarma na yanzu yafi na dazu can kasa da murya kamar zata fashe da kuka tace bai da lapia dr ibrahim yayi salati yace subhanallah tun yaushe miyasa me sa?Tace nima bansani ba yanzu ne kawai nasame sa ahaka dr ibrahim yace karki damu ganin zuwa yanzu,15mins sai ga kiran dr ibrahim yasake shigowa tana nan zaune ta zuba masa ido ko daukewa babu hankalinta idan yayi dubu yatashi bata kowa batasan kowa anan ba sai shi,a duniyar ma baki daya yanzu bata da kowa sai shi,daukan kiran tayi yafada mata yana bakin kofan part dinsu dasauri ta koma bedroom tasaka hijab dinta kafin ta bude masa kofan,tun daga bakin kofa ya hango malik din ya hango yarda yake kyarma ga zufa yanayi dasauri yashigo ya durkusa kusa dashi yarda jikin yayi zafi yana zufa ga kyarma ba karamin dagawa dr ibrahim hankali yayi ba dasauri yasaki gudun fan din parlor,yakalli aydarh yace tun yaushe yake haka madam kuma miyasa baki kirani tun dazu ba sai dakika bari abun yayi worst har haka ita dai aydarh batace komai kanta nakasa ko dagowa batayi ba hawayen idonta take gogewa gently ganin bata ma kanshi lokaci yake ga condition din malik fita yayi yatafi pharmarcy yasiyo pain reliever injection yafara yiwa malik din kafin yasamu nutsuwa gano abunda yasami malik din sosai yake kokarin kan malik din amma abun kamar yana so yafi karfin sa duk yahada zufa,juyawa yayi yana kallon aydarh dake tsaye kamar zata

shige jikin wall din parlor da ka kalli fuskanta kasan hankalinta ba a kwance yake ba yace madam ko mutafi asibiti ne naga kamar his condition is getting worst aydarh dai takasa cewa komai sai bin malik da kallo take,ahankali yake bude idonsa kafin yadaga hannunsa ya taba dr ibrahim dr yayi sauri ya matsar da kunnan sa daidai satin bakin malik din murya can kasa malik yake gayawa dr ibrahim alluran da zaya siyo yayi masa,dr ibrahim likitane yasan kalar alluran yasan amfaninta kallon malik din ya dinga yi kafin ya mike yafita pharmacy ya koma yasiyo alluran ya hadu dana bacci yayi masa,cikin good 10 minutes malik yafara sauke ajiyan zuciya numfashin sa yafara daidaituwa sweating din dayake yana bushewa kyarman dayake yana rage da alama alluran baccin na fizgar sa, dr ibrahim ya kalli aydarh yace Alhamdulilah madam he is getting better ,ina ga zan tafi yanzu tunda nayi masa alluran bacci ko zai farka sai cikin dare ko da asuba kuma in sha Allah daya farka shikenan ma,ko ki kamasa ku shiga bedroom kar ya kwana anan dan akwai sanyi sosai aydarh ta gyada sallama sukayi da dr ibrahim kafin taje tasakawa kofan key ta dawo ta kusa 5mins tana kallonsa ko dauke ido babu,yarda yake bacci a matukar wahala zaka san yayi matukan jigatuwa, mikewa tayi ahankali ta bude kofan bedroom din first kafin tadawo ta dinga binsa da kallo to ita ta ina ma zata fara kama sa ina ita ina shi ma? Kuma yace akai sa bedroom saboda sanyi yanzu yazatayi? Dr hafsa ce tafado mata a rai tayi saurin kunna wayarsa takalli time kusan pass ten yanzu girgiza kai tayi aranta tace yazaayi ta taba sa ita da ba matarsa ba ma ai haramune wata zuciya tace mata ke ce matar ke yakamata ki kamasa,da wannan tunanin yasa ta kara gyara zaman hijabin jikinta hankali tasa hannu ta bubbuga pillow dayake kwance akai,baccin nasa bawai yayi nisa ba duk wani motsin datakeyi yana ji amma bazai iya ce mata komai ba hannunta ta mika masa,kallonta yakeyi sosai ita kuma ta saukar da kanta kasa wani irin rahama ke bin duk wani parts na jikinsa har cikin soul dinsa yake jin sallama da nutsuwa sosai yarike hannun nata as if his life’s defenses on her hand kallonta yake cike da tausai da tunanin daban daban sai yanzu ta dago ido takalli kwayar idonsa tayi saurin dauke kai domin wani irin fuzgagen kyau da tagani kwance a sick face dinsa, tunda aka daura auranta dash isai yau yake kallon kaddarar da abunda aure ke nufi ba karamin tausayin kansa yaji ba da ita baki daya a yanzu fa su basu da kowa basuda komai bayan su biyun shikenan yau da ta Allah takasance akansa bai san irin halin da zata shiga ba,yasaba da wannan ciwon amma bai taba jigatuwa irin na yau,tagaji da durkusan datayi ga tafin hannunta da nashi dasuka hade waje daya very soft and clean, hankali muryanta can kasa tace yace nan da sanyi kaje bedroom bai ce mata komai bas ai bin da yake da kallo kafin ahankali ya mayarda da idonsa yarufe yafara motsa bakinsa ahankali kafin yace sai ki

dauke ni ki kaina can din,sai sannan ta bude ido tana kallonsa sosai baki bude kafin tace baka da lapian ma amma sai ka dinga gaya magana “to ni ai bazan iya daukan ka ba wallahi wait did you ever look your self through the mirror?ya girgiza mata kai bakaramin relief yake samu a maganar nan dasukeyi ba tayi kasa da murya kamar mai tsoron abunda zatace tace to wallahi you are very tall and fat takarasa tana kawar da kanta gefe tareda turo baki duk da halin dayake ciki bai hanashi yin murmushi ba dan ba karamin dariya tabashi ba zatayi iya yin kwana biyu batayi magana Amma duk ranar datayi magana sai ta bashi dariya she is very sturbborn and arrogant ga mugun tsoro da raini kuma Allah yaga abunda yagani yayi miskila bai ce mata komai sai kokarin mikewa tsaye dayayi cike da karfin hali yake komai dan he is brave enough duk yarda alluran baccin ke fizgar sa haka ya daure yamike ganin ya mike yasata mikewa itama tana kallonsa hannu yasake mika mata itama ta miko nata hannu da taimakon ta duk da bawani karfin kirki gareta ba har suka isa bedroom din side din datake kwanciya anan yayi ma kansa masauki,wallahi scent din wurin ba karamin dadi yake masa ba hankalinsa nawani masifan kwanciya (ni fa no words can express waye aydarh gareku)komawa tayi can waje wardrobe ta zauna bata jin bacci sam sai ta tura kanta tsakanin laps tun yana kallonta har wani baccin ciwo yayi gaba dashi.Anan inda take tazame ta kwanta bacci barawo yayi gaba da ita,kiran sallan asuban da akayi yayi daidai dawani irin azababan ciwo daya Sake saukar masa wani irin nishi yafara yi wanda yasa ta farkawa daman bata da nauyin bacci sam,jin nishi dayakeyi yasa ta saurin kunna globe din dakin haske tarr tasauke idonta a fuskar sa idonshi yayi wani kala kamar rushin wuta gabanta yawani fadi tama kasa matsawa kusa dashi domin batasan abunda zatayi ba yanzu ma kamar jiya kiran wayan dr ibrahim ne ya shigowa wayan shi daman yabari sai asuban saboda ya daidaici lokacin da zai farka din dasauri tayi accepting call din bata jira jin abunda dr ibrahim ke fadi ba muryanta cike da rauni tace bai fa da lapia har yanzu he is breathing hardly inalilahi waina illahil rajiun shine kawai abunda da dr ibrahim ke fada yace wait kwantan da hankalinki ki bara nakira dr hafsa yanzu tazo ku same ni a clinic kafin yakashe wayan,cikin few minutes taji ana buga kofan part din tajin haka tasan dr hafsa din ce dasauri ta fita ta bude mata hankalinta a tashe kwalla cike a idonta dr hafsa ta kama hannunta tace kiyi hakuri aydarh in sha Allah babu abunda zai same sa kinsan yanzu asuba ne babu masu keke shiyasa na kira yaron neighbor mu shima keke garesa ki shiga sai ku fito mu wuce, komawa dakin kawai aydarh tayi wardrobe ta bude ta fito kudin nan dake cikin bag din ta rike a hannu bazata iya kamasa ba kuma ai bazata ce ma dr hafsa ta kama mata shi ba ahaka tasamu da yarda yake daurewa ta kamo shi dr hafsa ta rufe

part din ta cire key din,titi babu kowa hakan yasa basu hadu dawani traffic ba sosai suka isa clinic din dr ibrahim yanajin tsayawar keke yasan su ne yayi saurin fita zuwa yanzu bakaramin galabaita malik din yayi ba da taimakon mai gadi da dr ibrahim suka shigo da malik din cikin clinic dr ibrahim da dr hafsa ke tsaye akanshi dayawa basu da manya alluran da zai bukata tunda zuwa yanzu su biyu duk sun san abunda ke damun shi,fita dr hafsa tayi tabar dr ibrahim a dakin aydarh ta ganinta ta taso daga inda take zaune kafin dr hafsa tayi magana aydarh tasa bayan hannunta ta goge kwallan idonta kafin ta mika mata kaf kudin dake hannunta 20k babu yanda dr hafsa ta iya haka ta karbi kudin domin suna bukatansu wajan siyo sauran alluran, fita tayi tafido wayanta daga aljihun wando baccin tayi dialing wata number ana daga tace gatanan zuwa mai keken daya kawo su shi yakaita babban pharmarcy din duk wani medications daza su bukata tasiya ta koma dr ibrahim ya dinga binta da kallo ganin data da alluran da maganin basu da lokacin tsayawa tambayoyi kawai ya amsa yacigaba dayi wa malik din duk abunda yadace .

Dr ibrahim dai baice komai ba har sai datayi shiru ,ajiye abunda ke hannunsa yace ni kaina abun yabani mamaki kuma naga miye zai kawo masa wannan ciwon bayan yanada aure?dr hafsa taware hannu tana tabe baki tace ni kaina shi nake tunani dr,dr ibrahim yasauke ajiyan zuciya yace anyway inaga personal life dinsu ne saboda haka there’s no any need muyi involving kanmu a ciki dr hafsa ta sauke ajiyar zuciya tace “gaskia” ta mike tsaye tace bara naje office dina aydarh na can nasan nagaji nima I need to rest dr ibrahim yace tau ba damuwa zuwa anjima idan yafarka sai kice tashiga ta duba sa bacci yake yanzu tace tau.dr hafsa dake kallon aydarh ko kiftawa babu with seriousness a fuskanta tace aydarh am older than you nayi mamakin dakika bari har mijikin na shiga irin wannan condition din, kinsan mi yafi bata mun rai?yarda.

Dr hafsa tace aydarh baki san fushin da mala’ikun rahama zasuyi dake ba kan kusamu sabani da mijinki kin kaurace masa,aydarh are you normal?am highly disappointed on you! wallahi aydarh kina aikinmi zaki bar mijinki kinsan halinsa kinsan yanayin rashin lapian sa amma fushin zuciya yasaki barin sa cikin wannan halin,aydarh dai kanta nakasa sam tarasa abunda dr hafsa ke nufi can ta dago kanta ta goge hawayen dake zuba a kuncinta ta dinga kallon dr hafsa din ta dai yi shiru batace komai ba ahankali dr hafsa tamike ta zagayo inda aydarh ke zaune taja kujera kusa da ita ta zauna,murya can kasa takama hannun aydarh tace nabaki shawara?still aydarh na kallon dr hafsa,dr hafsa tace don’t be silly aydarh you are wise enough take me as your biological sister your eldest sister just feel free let’s

talk mike damunki kika bari har kika aikata abunda yafaru? Aydarh ta sauke kanta kasa kafin tasa bayan hannu ta goge hawayen ta tass” tace Allah babu nidai babu abunda nayi masa wallahi, dr hafsa ta saukar da ajiyan zuciya ta mike tsaye tace anyway aydarh zan jiraki duk lokacin dakika ga yadace you are always welcome ,I will be waiting, Aydarh dai tayi shiru batace komai ba,can ta mike takalli Doctor hafsa tace zanyi sallarh,dr hafsa tace tau shknn ki shiga toilet sai kiyi alwalla akwai prayer mat a bag dina,sai datayi sallarh kafin ta mike,tace auntie zan iya duba sa?tafada tana wasa da gefen hijab dinta kamar mai jin kunyar abunda tafada din,Dr hafsa tayi murmushi ta girgiza kai tace kya ji dashi kibari sai anjima yanzu yana bacci muje gida kiyi wanka kisamu kiyi girkin dazaki kawo masa ki dauko masa kayan da zai sake, Aydarh ta girgiza kai tace ahah zan tsaya anan din babu yarda batayi ba dr hafsa tabar ta amma tace dole sai sunje tayi wanka tayi girki kafin tadawo ba dan taso ba haka tabi dr hafsa din suka wuce cikin gidan tawuce da key din a hannunta ko da tashiga tsakar gidan babu kowa part dinsu ta wuce ta bude tashiga, bedroom din ta wuce tacire hijab din ta linke,few minutes ta dauka tafito a toilet din daure da toilet sai karamin da ta daura akai, Vaseline ta shafa kafin ta dauko sabon bubu gown din dasuka siyo tasaka,plain light purple inner cap din ta tura calaban kanta dake nan ya maida ta kamar kan yaran hadaddun larabawa ba karamin kyau rigan yayi mata ta kwanta a jikinta luff color din rigan yabi skin dinta Side din wardrobe dinsa ta bude ta dinga bin kayan dake nan a wanke tass da kallo faran jallabiya ta daukar masa sai short da singlet dinsa perfumes din dasuka siyo jiya ta dauka tasaka masa a ledan ta yafa mayafin gown din ta fito hannunta rike da ledan,sai sannan gabanta yafadi tunuwa datayi dr hafsa fa tace tayi masa girki ita mi zata dafa masa? Bata taba tunanin rana irin haka zata zo a rayuwarta ba ranar dazatayi regretting duk wani actions dinta na baya bata tsaya ta koyi girki ba duk kokarin oum akan ta koya din kwalla ne a idonta ta gaji da kukan nan she just wants to face the reality now tashirya karban rayuwan da suke a yanzu wata zuciya tace hadda karban shi a matsayin miji? Noo shine ta furta a fili this is the last thing dazanyi a rayuwa na karbansa a matsayin miji bana son sa, knocking kofan da akayi yamaido ta daga dogon tunanin data tafi, ahankali ta ajiye ledan hannunta tanufi kofan ta bude dr hafsa ce tsaye rike da basket a hannu, sanye take da doguwan rigan atampha sai labcot din ta tayafa white jersey veil, murmushi tayi tabi aydarh da kallo kafin ahankali tace Allahumma bareek tabarakallah mrs ABDOOLMALIK you fine die matan malik aydarh tayi murmushi tace thanks dr hafsa tace Allah yasa dai baki daura girkin ba ina shiga gida fa na tuna akwai stew a frigide din inna white spaghetti kawai na dafa,aydarh tayi murmushi kadan tace aa yanzu ne zan daura sai

naji knocking dr Hafsa tace tau Alhamdulilah tunda baki daura ba,sai ki dauko masa kayan mutafi na hada abinci dake nasa baki karya bai dan mukaje can sai ki ci ba?aydarh ta gyada mata kafin ta dauko ledan suka fito tana rufe kofan ne dr hafsa,tace yawwa aydarh har zan manta yanzu naga Ramlah a kofan gida tau kinsan inna bata nan,shine nake fada mata yallabai na asibiti idan innan tadawo sai tashiga tafada mata idan yaso sai ta iske mu can kinsan halin inna,idan baa gaya mata ba rashin mutunci sai wanda ta manta,aydarh da tagama rufe kofan ta kalli dr hafsa tace waye kuma Ramlarh?dr hafsa tace yarinya dake part din can aydarh tagane wacce take nufi tsaf amma bata nuna mata ba ta juya kawai suka wuce, a kofan gidan suka samu keke suka wuce clinic din,a keken dr hafsa takalli aydarh tace wannan perfume din naki yanada masifan dadi kuma kinsan mi yahadu da natural body scent dinki shiyasa yake fitan dawannan kamshin aydarh tayi murmushi tace " Erh" dr hafsa tace ahakan bakiyi lacking komai shine kike nima ki jazawa kanki ko aydarh tafada da alaman tambaya aydarh dai tayi shiru batace komai ba,bakin clinic din mai keken yayi parking dr hafsa ta biyasa suka shiga ciki.Rabiah ce zaune a dakin a kujeran dake kusa da gadon da malik din yake kwance idonsa arufe yake amma ba bacci yake ba,sai wani kallonsa take kamar tasamu t.v dr Ibrahim ne yakira iya yace ta ba rabiah takawo masa ruwan zafi a flask shine tace zata shiga ta duba malik yace mata tau zata iya shiga bara yaje yayi attending wasu patients dasuka zo yanzu, kallo daya aydarh tayi mata ta dauke kai ta ajiye kayan dasuka zo dashi a gefen drawer drugs din dake dakin,dr hafsa ma ta ajiye kayan dake hannunta tace sannu rabiah sai sannan rabiah ta dago tace mata yawwa mun kwana lafiya?dr hafsa tace Alhamdulilah,aydarh ko,ko iskan daya kwaso rabiah bata kalla ba balle har tasa ran zata amsa ta,dr hafsa ta kalli rabiah fuska babu wasa tace rabiah ina ga ki tafi tunda ga mai dakinsa tazo rabiah takalli dr hafsa kafin ta maida kallonta ga aydarh,kallo daya tayi mata gabanta yayi wani irin faduwa wani irin kyau tagani kwance a fuskan aydarh rigan jikinta kamar dan ita akayi ta,batace komai ta mike ta fita daga dakin dr hafsa tabi bayanta da harara, sai da tafita kafin tace aydarh bara naje sai ki tashi sa yayi wanka yace abinci drip din naga ancire masa saura allura daya maybe anjima,ku koma gida,Aydarh tace to, bayan fitan dr hafsa zama tayi a kujeran da tashi wanda tafi kusa da malik din cikin few seconds takare ma fuskansa kallo kafin ta dauke ido karaf yabude idonsa fess a kanta kallonta ko kiftawa babu, ta kalle sa kafin ta saukan da kanta kasa tace how are you feeling? Murya can kasa irin na wanda yayi ciwo yace "fine"batasake magana ba shima bai sake magana basai can yace zanyi wanka, bata tanka sa ba ,ta shiga toilet din dakin very tidy koi na fess kafin tadawo ta dauki flask din ruwan zafin da tagani a gidan tahada masa

kamar yanda yakeyi mata,tadawo ta tsaya atsaye tayi folding hannunta a kirji yarda yake kallonta kamar irin yau dinnan yafara ganinta can ta gaji da tsayuwa tace “ko ba yanzu zakayi wankan ba? This is the first datayi masa magana with full respect mamaki yafara yi anya kau itace? Bai ce komai ba yatashi ahankali dan yanzu sosai yake jin saukin jikin nasa sai dan abunda baa rasa ba, hannu yasa ya dauki ledan dayagani nan kan drawer din komawa tayi ta zauna kan kujera ta zubawa waje daya ido ta ina zata farawa dr hafsa bayani to?mi zatace mata tana son koyo? Idonta tasauke kan basket din abincin dasuka zo dashi yunwa takeji amma bata jin cin komai haka yasata yin lamo ta rufe idonta tanaji bacci kadan kadan yana fizgan ta,sai dayayi spending kusan 20mins kafin yafito shirye cikin jallabiyan sai kamshin perfume din data kawo masa yakeyi yakara jaa sai fadawa dayayi kadan hadda suman kansa ya wanke tayi luff akansa,zaman yayi ya ajiye ledan wanda yazuba kayan da ya cire a drawer kafin yadawo ya zauna kan gadon “murya can kasa yace tau ko bazaki bani abinci ba?batace komai tabude warmer ta zuba masa abinci kafin ta dauko masa bottle water da dr hafsa tasaka a basket din ta ajiye masa a gefensa yadinga bin abincin da kallo kafin yace wannan naki ne?takalle sa ta dauke ido kafin tace ina kai kace zaka ci din”baice komai ba yajuya batare da yadauki plate din ba kallo ta dinga binsa dashi,kafin tace wai bazaka ci bane? Sai sannan malik yace hala baki san ni inada cin abinci ba dazaki saka mun wannan dan abinci kamar dai wani yaro sai sannan ta tuna da ranar data gansa ya zuba abinci a plate kamar zasu ci su hudu yana ci batace komai ta kara masa abinci ta daura masa a cinya,sai daya kusa cinye abinci sannan ya lura da ita bacci take nan kan kujera kallon rigan yayi yarda tayi mata kyau sosai duk yarda creams soap shower gels dinta suka chanza amma kalan fatan ta na nan babu abunda ya rage glowing take sosai,idonta a rufe hakan yasa ya dinga kallon fuskanta gashin gaban kanta yayi luff yadan fito har kana iya ganin calaban kanta yarda hulan yazame,dewdrop ya furta can kasan ranta sai yayi maza kuma yayi shiru saidai day agama cin abinci kafin ahankali ya mike ya ajiye plate din hannunsa yasha ruwan kadan kafin ya matsa kusa da ita yasa hannu yashafa cheeks dinta tayi sauri ta bude idonta, yawani hade fuska kafin yace wake up and eat bana son wannan rashin cin abinci, harara ta watsa masa,yayi sauri yasa yatsa ya buge mata baki wani shegen kara tasake kwalla yakawo idonta ta mike tsaye,wallahi saura kadan yafadi wannan abun datayi, kallonta yake ko dauke ido babu,ita shi take kallo kafin ta dauke ido bai ce mata komai sai juyawa dayayi walking majestically and slow har ya isa gaban basket din yabude yazuba mata abinci daidai yarda take ci ya yadaura mata kan cinya kafin ya koma kan gadon ya kwanta ya rufe idonsa yana sauraron yarda zuciyansa ke bugawa, Abinci take ci cike

da aji da kuma nutsuwa bata ci dayawa ba ta ture ta bude ruwan nan ma kadan tasha tarufe yanajin duk motsin ta har time din data ajiye abinci ta rufe yaji,tashi yayi zaune yace ki kwanta bara naje wajen dr Ibrahim naga kaman bacci zakiyi right? Ahankali tace ahah ni ba bacci nakeji ba,bai sake magana ba yakoma ya kwanta itama kan kujeran ta zauna tayi shiru. Inna da tashigo yanzu ta goge hawayenta tace tau daman banda anyi niyyar audu ya tsane ni ya tsani kayana,sai a rasa matar dazata kirani nadawo daga wurin rubabban sunan nazo asibitin fisabillahi banda rashin kaunar Allah yayi yawa ace yaro tun jiya akawo sa nan ace babu wanda zai kirani ya gayamun sai tasake fashewa dakuka,malik dai yayi shiru can yace kiyi hakuri hajiya inna kinga sai fa da asuba kuma nayi tunanin ma kina gida ko hafsa ta gaya maki,inna ta mike tsaye ta aaaaa haram haramun wacece kuma haka? Matar da kowa yasan bata kaunar Allah, Aydarh dai na zaune batace komai ba inna ta shiga da masifa ta inda take shiga batanan take fita ba wulakanci sai wanda ta manta ke batayi wa dr hafsa ba ita dai tayi shiru batace komai sai danna wayan ta takeyi,malik yace yanzu dai ai nace kiyi hakuri ba?tunda yanzu kinsani kuma har gaki kinzo ai shikenan koh hajiya inna?inna ta goge sauran hawayan fuskar ta tace shikenan audu na hakura ya jikin naka?yace Alhamdulilah dasauki inna tace ai wannan masassara dai baa ji dadinta ba, waenda basuyi taba gaskia basu dayawa,nidai Allah ya tsallakar dani,daga ranar naje anguwa nadawo kaina naciwo sai ga wannan matar da magani waai nasha kila zazzabi ne ni dai dayake nasan ciwon kaina Ko kallonta banyi baita da maganin nata, malik yace Allah ya kyauta,can tayi kasa da murya ta kalli malik tace tare fa nake da ranla ita dayake babu ita a munafukai na, sai gashi tana ganin dawowa ta tashigo take fadamun tace na rufe gidan ma mutafi malik yace Allah sarki,kafin yarufe baki aka turo kofan dakin Ko sallama babu tashigo tasha wani fitted gown na atamphar rubber gawani uban jam baki tasha sai baza kamshin balila ake ga ubansu dauri ankashe anfito da calaban attach blue da green irin na asalin karuwan nan, tana tafiya kamar zata kare shidai malik kallo daya yayi mata ya dauke ido yarasa miyasa bai son yarinya kwata-kwata bayason yarda takenan babu kamun kai,dr hafsa dai sai binta da kallo take tana son taga inda zata da taho hakanan,tun shigowan ta aydarh ta ganta sai ta dauke ido tahade fuska kaman bata taba dariya bai ta Ramlan bata ma lura da aydarh basai said ai baza ido take taga ta ina zata hango ta, ganin malik yasata mance duk wani abu straightly gadon ta nufa tana isa idonta yasauka kan aydarh dake kujera can karshan bangon gadon a zaune kallo daya Ramlah tayi mata ta dauke ido duk sai taji ta muzanta tana san zaran ma bak alar yard din bane ita da aydarh amma ko zatayi yawo tsirara sai malik ya saurareta ko da sau dayane cike da duniyanci ta sace kallon aydarh

taga hankalin ta baya kansu,dan daga murya tayi kafin tawani karyan da kai gefe tace “sorry dear”ya jikin naka,daman tun jiya dasafe na lura da yanayin ka nasan ko nafada ma baka da lafiya ba lallai ka aminci ba,tass aydarh taji abunda tace, saboda yarda take maganar kowa na dakin ma yaji balle ita aydarh dake gefensu shi wallahi ma mamaki abun yabasa bai ce mata komai sai sauraron ikon Allah dayakeyi,jin hakan yasa dr hafsa mikewa bata tolerating shits din yaran nan domin tun ba yau ba tana lura da duk wani movements din Ramlah kan malik bata taba maida hankalin ta ba saboda ba ruwanta dasu amma yanzu gani take kamar cin fuska ne ramlah keyi ma aydarh,hakan yasa cikin tsare gida dr hafsa tace Ramlah kiyi masa ya jiki kawai ki fita babu wanda yatambaye ki wani abu anan so better maintain your dignity here am I cleared? Wani banzan kallo Ramlah tayiwa dr hafsa dan ba bata raina taba shiyasa tayi shiru batace bata komai ba aydarh yi tayi Kamar batasan dasu hallitu ba a dakin baki daya,inna tasake baki tana kallon Ramlah kafin tace inalilahi waina illahil rajiun.

Ta dinga bin Ramlah da kallo kafin tace aaa ranla ke kau kin zaqe dayawa, daga zuwa dubiya Sai ki tsatsallake mu,mu danginsa ki kai har nan ko ita asiyar baki ga inda ta zauna ba balle ke kwashe kwashe ki?Aydarh dai kanta nakasa bata dago ba tana dai jin su,dr hafsa tace fita zamuyi inna mu barsu da matanshi inna ta mike tsaye tace gaskia bara nakoma gida nasamu gayen in kwadawa audun kafin in dawo,dr hafsa tace tau shknn ,inna ta kalli Ramlah kafin tayi mitsi mitsi da ido tace tau ko dai baki ji ne? Matar dake aike wurin tace a fita katti sun zo sun cika daki ina yaro zai warke, dan baa kaunar Allah ai sai a sa masa wani cutan ma Allah natuba, Ramlah ta mike tsaye tana wani bata rai,tace Alright love Allah yabaka lafiya zuwa anjima nadawo, malik dai ya maida idonshi ya rufe bace komai ba inna tabi ta da kallo baki bude dr hafsa ma haka, mamakin Ramlah ya cikata,inna ta dauki jikkatar ta fice,dr hafsa ta kalli aydarh tace muje office kibar sa yayi bacci malik yabude ido yana kallon aydarh kafin yace ki rufan mu duvet din,bata masa komai ba ta warware duvet din gently ta rufa masa,ya’ki dauke ido akanta,hannunta ya kalla kafin ya rike hannu few seconds ya dauka yana kallon hannun kafin yasake ta,dr hafsa dai nagani haka tasa kai ta fice daga dakin, ta ja kofan malik yace “kunsan ba zama zakuyi ba kuma sai kisa ta koran mun budurwa?aydarh ta watsa mashi idonta kafin tace aaaa kasheta nasa tayi ba koranta ba ni miyayi ruwana da ita,put this into her head please am not a mate of a kid whether she is your girlfriend or you wife that’s none of my business am not her type,bana son raini and ta daina kallo na if not I surely deal with her I will deal with the stupidity out of her, kafin ta juya ta fita mamaki tabasa da dariya,yashafa kansa yabita da kallo yasha

kansa ahankali yace masifafa ya lura yarda Ramlah bata birge sa itama haka,amma wannan masifan fa? Girgiza kawai yay isai kuri ga tsoro,sturbborn bae.ko da tashiga office din dr hafsa still bakinta na a tsuke ta hade giran sama da kasa,sallama tayi ta zauna kan kujeran dake facing din dr hafsa,dr hafsa data lura da yanayin aydarh tace miya faru naga fuskan ki a hade,sai sannan ta bude baki cike da tsiwa tace kiji sa fa auntie,wai nasa kin koreta nayi magana ko nasa da ita didn't I even know her existence a dakin ne? Dr hafsa da tagama sauraron aydarh ta girgiza kai tace kiyi hakuri aydarh kuma tun farko laifinki waenan yaran basu da hankali basu da tunanin basu da kamun kai ma,maybe fa ko magana baya hadasu kawai daman opportunity take nema wanda zai hadasu tayi mashi magana sai ga dama tasamu don haka karki damu ba laifinsa bane,kawai kiyi kokari ki sa yafita harkan ta,aike ce matar sa babu fada babu tashin hankali zaki sa ta fita harkan sa,Aydarh dai tayi shiru bata sake cewa komai ba,dr hafsa tace bansan abunda ke damun yarinyar nan ba har ta bata kanta har haka wallahi, definitely nasan shidai yallabai ba shiga harkan ta zai dinga yi ba mutun da kullun fuskar sa nan babu wasa kwarjinin sa ma sai yahana kayi masa magana amma rashin kunya da tsaurin ido irin nata sai da tasamu waje har haka Allah natuba ma banda neman jafa'I irin na Ramlah ina ita ina kishi dake ni wallahi ko mijinki kawai ya rage a rayuwa wallahi aydarh na gwamaci na karasa rayuwana ahaka saboda nasan dai photo kawai na aure,ita dai aydarh sai sauraron dr hafsa take har tayi shiru kafin aydarh murya can kasa tace "why"? Dr hafsa ta gyara zama tace haba aydarh ki dube ki,ki dube Ramlah idan kina wuri har akwai wace ta isa tayi magana? Aydarh ta cigaba da bin dr hafsa da kallo itama dr hafsa din aydarh take kallo, babu wanda yasake magana cikin su ,tunani ne kala kala azuciyan aydarh.

Inna tace sannu ko audu,malik ya amsa mata ta bude samiran data saka kwadon a ciki tace ka daure ka ci ko kadan ne,malik ya dinga bin kwadon da kallo ummi tafado masa a rai yayi murmushi yasaka cokalli yafara cin kwadon ahankali,inna ta kalli aydarh tace tunda nashigo naji ki shiru ko kema ba lahiyar?aydarh ta girgiza kai tace aa inna lapia na lau,inna tace tau ai shikenan bara yaci kwadon idan ya rage kema sai k ici, malik yajuya ya kalli aydarh kafin ya dauki samiran ya daura mata a cinya yace eat batace masa komai ba ta sa cokallin dake ciki tafara ci bakaramin dadi kwadon yayi mata bahakan yasa taci ba laifi shidai sai bin ta yake da kallo duk surutun da inna ke masa sama sama yake amsata,har tagaji tayi shiru bacci ma ya kwashe ta anan kan prayer mat din datake kwance.wajan 6:00pm dr ibrahim yashigo dauke da file ahannu ya kalli malik kafin yayi murmushi

yace giwa tafadi daga ciwo kwana daya har kafada na lura madam ta ma fika dauriyan ciwo wallahi,malik yakalli dr ibrahim kafin yace sallamana zakayi right?yarda yayi maganar bakaramin dariya yaba dr ibrahim ba saboda yasan haushin maganar daya gaya masa ne,dr ibrahim yace aaa gaskia maybe sai zuwa jibi tace kar na sallame ka dan yanzu,malik ya kankance ido yace wayace?dr ibrahim na dariya ya nuna aydarh dake zaune kanta a kasa, karfasa dake saitin kafanta yasa ya taketa da dan karfi taji sare amma ta daure duk dataji zafi, kafin ya kalli side din inna dake bacci yace ni kayi discharging dina idan yaso ita sai ka bata gadon dana sauka tunda zaman bai ishe ta ba,dr ibrahim yace auu haba?naga time din dabata lafiya ko nan da bakin clinic kasa fita kayi saidai ,kaga idan nabata gado kaima zaman ba isheka ba,aydarh dai najin su still kanta na kasa bata dago ba.Kasancewan gidan koi na very neat yake babu wani dirty suna shigo malik yawuce bedroom so yake ya kwanta tunda alright anyi isha'I dr hafsa takalli aydarh tace tau sai dasafe Allah yabashi lafiya Aydarh tace Ameen har bakin kofa ta raka dr hafsa din kafin ta rufe kofan da key tadawo kitchen ta shiga ta dinga bin kayan girkin da kallo bata iya kuna camping gas din bahakan yasata matsawa sosai kusa dashi ta dinga bin rubutun jiki da kallo open/close ashanan data gani nan aje ta dauka tana murda wajan open din ta qasta ashana sai kau wuta tagama murmushi tayi kafin ta tari tukunya ta daura ruwan zafi, parlor tadawo ta zauna few minutes kafin ta koma kitchen din yatafasa yasa takashe gas din successfully wani hadaddan simile tayi kafin ta fita ahankali without making any sound,ta bude kofan bedroom din bacci yake sosai kanshi a waje while ya rufe jikinsa da duvet toilet ta wuce ta dauki bucket kafin ta fito ta koma kitchen din juye ruwan, wanka take son yi amma tana tunanin yarda zatayi wanka gashi a cikin dakin towel da dauka da duk abunda zata bukata tashiga toilet din sai datayi wanka tass kafin ta sake kayan jikinta tafito,zama tayi can karshan dakin kusa ta wardrobe tana shafa Vaseline gently ,tun dazu yafarka yana lura da duk abunda take sai bai nuna ba ,duk da duk bayan seconds sai ta kallesa taga ko ya farka ita yake kallo,dayaga zata juyu din sai yayi maza ya rufe idonshi kamar yana bacci saida tagama komai kafin tasaka hijab ta takure kanta waje har bacci ya dauketa ahaka, yabar jin motsinta hakan yasa shi gane cewa tayi bacci,tashi yayi daga kan katifar,daf ya dauketa kamar baby ji yayi kaman ya dauke paper, baccin ta yayi nisa shiyasa sam bata ji sa ba har ya kwantar da ita kan katifan ahankali yasa hannu ya zare mata hijab din jikinta bin ta yadinga yi da kallo ko dauke ido babu yarda tawani hade fuska duk da bacci take yabashi dariya ya girgiza kai yace troublemaker,bargonsa ya fiddo da pillow sai bedsheet din dayake rufa ya shimfida nan kan carpet ya kwanta.kiran sallarh farko yasa shi bude ido

kallon katifan kafin ya dauke ido ,toilet dinta yashiga har kamshin ta ya kama toilet din,yadinga bin pants dinta da brassieres da kallo sai dayasa soap dinta ya wanke fuska kafin ya dauro alwalla yafito, yana shigo sallan asuba har yanzu bacci take bata farka ba,hannu yasa yataba pillow datake kai, ahankali tabude idonta dasuka koshi da bacci,yace wake up its time subhi batace komai ba ta lumshe ido shi kuma yajuya yafita daga dakin ya koma parlor ya zauna ,ta dinga bin katifan da kallo ta dai san ba nan ta kwanta ba amma ya akayi ta dawo nan din?tabe baki tayi kafin tashiga toilet tayi alwalla tafito sallarh tayi ta koma kan katifan ta rufe ido still da bacci a idonta, 8:00am daidai yafarka daga baccin dayasake daukar sa anan parlor kitchen yashiga ya daura ruwan shayi kasancewar yasiya kayan tea yana saukewa ya mayarda ruwan dazai dafa masu indomie zuwa yanzu yagama jin sauki tass daman haka ciwon yake masa, yajuye ruwan a flask indomie ma yajuye musu a warmer kafin ya wanke few plates din daaka bata baa wanke da tun kafin ya kwanta ciwo sai daya gyara kitchen din tass kafin yadawo parlor nan babu wani dirty shiyasa bai dauke shi long time ba kafin ya karasa yashiga toilet din nan parlor ya wanke shi kal bedroom din yashiga Still tana bacci incense sticks kawai yadauko yazo nan kitchen ya kunna yasaka a parlor kafin nan ruwan zafin daya daura sun tafasa ya shiga yayi wanka ,har sai da yashirya yaci abinci kafin yaji motsinta alaman ta farka, bai shiga bedroom din ba yayi zamansa anan parlor, Tana tashi ta kwashe bargon daya kwana aka isai data ajiye komai a inda yake Kamar yarda taga yanayi kafin ta yaye bedsheet din ta gyara katifan tanaji yaune second time a rayuwanta data gyara gado da kanta yayi kyau babu laifi dan har tafisa iyawa murmushi tayi ganin ta gyara dakin yayi kyau sai taji wani irin dadi,shara ya rage sai mopping shima bara taje ta dauko tayi tasan zata iya,tana buda kofar ta ganshi zaune kan carpet yana kallon satin kofar har zata koma sai kuma tafito kanta a kasa ta nufi hanyar kitchen din mopper day agama goge kitchen da parlor na nan bakin kofan kitchen din bai zuban da ruwan ba hannun tasa ta dauki bucket din da tsintsiya sai Parker yadinga bin ta da kallo tau mi zatayi? Ya dai dinga binta da kallo baice komai ba har tashige daki,yana nan zaune yanata tunanin abunda zatayi da mopper tau ko dai tafara gyaran gidane hakan da zuciyarsa taraya masa bakaramin dadi yaji ba,Ahankali ya furta Alhamdulilah ,komai yafara zuwan mun cikin sauki Allah nagode ma, mikewa yayi tsaye yanufi bedroom din kawai dan ya tabattar yana shiga yaga ta zage tana ta mopping, kafa yasa zai taka tace “hey wait”kafin tawani yi kincin kincin da fuska tace karka takamun, daure fuska yayi yace tau idan ban shigo bai na kike son naje na dauki abunda zan dauka? Tayi kasa da murya tace to basai kajira ya bushe ba kafin ‘ malik yadai dinga bin dakin dake nan gyare tsaf yayi kyau kamar daman tasaba da

gyaran aransa yake tambayar kansa daman ta iya ne? Bai dai ce mata komai ba yaja bakinsa yayi shiru domin yasan halinta koya tambayeta baza mata tanka sa ba, juyawa yayi ya koma parlor Alhamdulilah yake ta furtawa saura girki kenan yanzu islamiyya a can ne yake tunanin kawai zai saka ta a koya mata komai na addini dakuma zamantake ta yau da kullun,da wannan tunani yayi tazama parlor har sai data gama kafin ta fito hannunta rike dasu mopper,kitchen ta shiga ta kunna gas kamar yarda tayi jiya ta daura ruwan dazatayi wanka ,tana fita yashigo kitchen din zuwa yanzu mamaki yakarasa kashe sa how talented she is wai duk a cikin kwana biyu ta iya abubuwa haka? Auu tau daman can rashin koya matan dabayayi ne yasa bata iya ba, kusan 5mins yana nan tsaye a kitchen din kafin yajuya ya koma parlor,fitowa tayi da bucket a hannu tashiga kitchen din, ko da tafito wanka nan ta tarar da plate din indomie da cup din tea sharp sharp tashirya kafin ta zauna tayi breakfast din.
Dr ibrahim dayagama sauraron malik ,yayi shiru yace tau badamuwa ai babu ma nisa daga nan zuwa can iskamiyyan matan aura ina ma da aboki a waja inaga kamar shine headmaster gaskia,malik yace tau yaushe zamuje can din? Dr ibrahim yashafa kansa kafin yace aa bara na tura maka number sa sai ka kirasa kayi masa bayani idan yaso sai yayi muku fixing time kuje can din,Malik yace tau shknn ngd, tura masa number yayi anan take malik yakira mutunmin waya suka gaisa yayi masa bayani mutunmin yace tau shknn idan Allah yakaimu gobe sai ku shigo waja tara nasafe in sha Allah malik yace tau Allah yakaimu, bayan malik yagama wayar dr ibrahim yakalli sa yace maganar tafiya nasarawan fa saura kwana tara yau,malik yayi shiru can kuma yace tau Allah yakaimu yau ina son zuwa wajan aiki bara nashiga gida nashirya,dr yace tau shknn nima clinic zan tafi,idan angama magrib mu hadu a can wajan kallon wasan basai na biyo ta nan ba,malik yace tau shknn. Yana shiga gidan ya tarar da Ramlah nan tsaye kofan part dinsu bai ce mata komai ba yayi wucewar sa da sarsarfa tabi bayansa har wajan kofan shiga parlor bai ko kalle taba yafara knocking ahankali almost 10seconds yana nan tsaye kafin a bude,yana shiga itama Ramlah ta shiga, wani irin banza kallo aydarh dake tsaye tabita dashi kafin ta kalli malik ahankali cikin wannan hadaddan innocent voice dinta tace tell her to walk out I want to shut the door tana fadin haka ta tsare sa da ido fuskanta babu alaman murmushi,wallahi malik kamar wani yaro ko mai jiran umarninta haka yasa shi kallon Ramlah yace mata out, Ramlah kau kamar zata fashe da kuka gawani irin shakkan su,su biyun duk dataji ya diran mata lokaci daya tayi maza tafice kafin aydarh tamaida kofan ta rufe da karfi,har sai da yabita da kallo.

Kallo har sai da tashige daki kafin yabar bakin kofan shima yashigo, tura kofan bedroom din yayi ya sameta tsaye gaban wardrobe tana mayar da kayanta daya wanke ranar,ahankali yace wai miye ruwanki da yarinyar nan? Dawani irin speed aydarh ta juyu har ta manta ma bata ajiye bra din dake hannunta ba, cike da masifa tace kai ma miye ruwanka da ita? Malik ya daure fuska yace mind you she is my gurl,aydarh tawani wara ido ta tabe baki tace your gurl bata masan tayi wani dariya ba,da har saidai ta malik yakasa dauke ido kanta kafin ta wani tabe baki tace ashe mace ce wannan din,ai ni bansani ba, Malik bai sake ce mata komai ba ya juya ya fita, kamar kullun yauma haka suka wuni aiki ‘ wani big mansion suke ginawa a nan anguwarsu Alhaji musan, sai yamma lis ya koma gida ya gaji sosai yau shiyasa ya tsaya wani café ya musu takeway yawuce, yanzu ma kamar dazu ita ta bude masa kofan yayi sallama ta amsa masa kamar an mata dole, kafin ta dinga binsa da kallo har yashiga kitchen yarda jikinsa ya bace da cement yak bata mamaki accident yayi ko faduwa yayi? Tayi shiru tana tunanin abunda yasa mesa,jin takunsa yasa ta saurin dauke idonta ta shige bedroom bin ta yayi da kallo ya girgiza kai yashige bathroom din nan parlor, sai dayayi wanka tass kafin ya mayar da kayan jikinsa ya shiga dakin tana nan zaune kan katifa idonta a rufe duk da ba bacci take ba saboda dayayi sallama ta amsa sa Still kuma Idonta na a rufe,bude wardrobe yayi ya dauki kayansa da Vaseline da perfume sai comb ya dawo parlor sai da yashirya tsaf kafin ya shiga,kitchen yajuye masu chips din a plate kafin yadauki pure watar yatafi bedroom din ya kai mata, bata wani chips din dayawa ba ta ture,sai ana kiran magrib dr ibrahim yakirasa yace yataho kawai bazai biyo ta gidansa ba su hadu kawai a can tau malik yace ya katse kiran,bai dawo ta gidan ba can ya wuce kawai.

Sai wajan ten ya shigo gidan kamar ko da yaushe yau din ma akwai nepa koi na tsaf tsaf har parlor yakama kamshinta saboda yawan zaman da take yawan yi a yanzu,ledan da yashigo da shi yawuce kitchen ya wanke fruits din dake ciki yayi slicing kan plate kafin ya debe nasa ya zuba mata nata a plate da fork, da sallama yashiga bedroom din yaji shiru bata amsa ba,bacci take takure waje daya cikin duvet kamar yar baby hulan kanta ya cire manyan calaban da dr hafsa tayi mata yafara warwarewa duk ya baje kan pillow, sai da ya ajiye plate din hannunsa kafin yazauna can nisa da ita yana binta da kallo kamar mai irga numfashin ta, kusan 5mins yana ahaka sai yau ya lura da kunnata bula ne har uku kowani a jiki akwai hadaddan barima gold bakaramin kyau bariman yake dashi bad uk duniya ya matukan son bula shiyasa a gida ma yake yawan ba su aysha kudi yace su siya earring su saka a bulan su, gajiya yayi da tunanin dakuma binta da kallo dayake faman

yi kuma yana son magana da ita,kafin ahankali ya mike yaje saman kanta yatsaya sai kuma ya duka ya buga pillow datake kai,jin ana buga pillow yasata bude idonta dake cike da bacci ahankali har takarasa bude idonta a kanshi,sai kuma ta juya kafin ta mike tana kallonsa,yace ki daina barin wutan dakin nan kunne batace komai ba tayi maza ta dauki hulan kanta ta mayar, ya dauki plate din fruits din ya daura mata a laps, ta dinga bin kankanan da apple din da kallo can kuma sai ta dauke ido, bata fara shan fruit din ba shima kuma bai tashi ba,kuma baiyi magana ba ya dai dinga kallon waje daya kafin ya mike tsaye ya zuba duk hannunsa biyun a pocket din jeans dinsa yace ki shirya gobe zamu fita dasafe,taji abunda yace haka yasata dago kanta ta zuba masa ido kafin tace, ina kuma zamuje?kamar ba zaiyi magana ba har yakusa fita daga dakin kafin yace, zuwa zanyi na siyar dake,daga haka yafita hararar bayansa tayi ,kafin ta dauki fork din ahankali tafara daukan apple din ta kai baki , tass ta shanye kafin ta dauki plate din walking slowly ta tura kofan kitchen din ta shiga plate din ta dauraye tana mamakin inda yaje don bata gansa a parlor ba, yana shigowa yasa key ya rufe kofan kafin yayi switching off din globs din parlor,tana sa kafa ta fito daga kitchen din ta ga ankashe wutan parlor tasan shine dan har yanzu akwai wuta tana ganin hasken globes din compound din duk da hasken baya shigo har cikin part din nasu, bata son duhu hakan yasata dinga bin bango, lafiyan sa yake hankali kwance dan bai kawo ma ransa tana parlor ba, wani irin karo suka ci dashi har sai da kafanta yayi bending tafadi kasa,the incident cames suddenly shiyasa he can hold it kawai yabita suka fadi itace akasa shine a sama,jinsa kanta yasa hankalinshi yayi masifan tashi bata ma ji zafin faduwan batasa hannu iyakan karfinta ta dinga ture sa tana hawaye yayi mata nauyi sosai har kirjin su daya hadu waje daya nasa numfashin ta yin sama sama,malik kau da bai masan yanayin dayake ciki ba ko gizau bai yi ba jin shi plate a jikinta bakaramin birkita sa ba yayi,yama kasa yin komai he already lose his weight, hankalinsa bai dawo jikinsa ba sai dayaji tasaki wani kara sannan cikin hanzari yayi saurin tashi akanta,ahankali ta mike ko juyuwa batayi ta shige bedroom din kan katifan ta kwanta ta rufe idonta da karfi still hawaye ke ta zuba a idonta,tun daya kwanta yakasa bacci,sai dawo masa abunda yafaru keyi akai.Kallonta yake ko kiftawa babu ta yafa mayafin gown din, still tak’I yarda su hada ido sai kallon waje daban take,yayi kasa da murya babu wasa ko kadan a fuskan sa yace ai da baki yafa mayafin ba ma kin tafi ahaka “ sai yanzu tajuyu ta kallesa batace komai ba ta dauke kanta,ta nufi hanyar kofa,har takusa fita kafin yabude wardrobe ya dauko mata hijab dinta daya goge mata, bai ce mata komai ba ya warware abayan ya mika mata bata karbi abayan ba kuma bata kallesa ba ganin tana bata masa lokaci yasa shi zare mayafin kafin yasaka mata hijab din duk abunan

dayake ko motsawa batayi ba har yagama yafice yabarta nan tsaye ajiyan zuciya kawai ta sauke kafin ta bisa ba,kofan part din ya kulle ya saka mukullin a aljihun wanda yard dinsa yayi matukar karban jikinsa zaka rantse da Allah yaron wani babban ambassador ne ko kuma wani minister kudi duk da yard ne mai karamin kudi ne amma bakaramin haduwa malik din yayi ba cikin yard din, baby pink din hijab din daya saka mata ya hau sosai da touches din flower gown din nata Sosai yahau da gown din, daidai kofan gidansu suka hadu da dr hafsa itama ta fito daga gida tana neman keke zata tafi clinic,murmushi tasake tana kallonsa tace Good morning my couples malik yayi murmushi yace morning dr yah inna?dr hafsa tace inna lafiya lau,aydarh ta kalli dr hafsa kafin tayi wani cute simle tace Good morning auntie,dr hafsa tace morning mrs malik mun tashi lafiya yajikin yallabai? Aydarh tace Alhamdulilah ,dr hafsa tace yau fitan safe za’ayi ba? Aydarh ta kalli malik ta gefen ido hankalin sa na kan keken dake tahowa kafin tace Erh dr hafsa tace wannan kauna haka aydarh dai tayi murmushi ta saukan da kanta kasa dr hafsa tace ni bara na kara gaba maybe nasamu keken a can tunda kila ba hanya damu mukayi ba right?Aydarh taware hannu kafin tace bansan inda zamuje ba,ko ki tambayesa,dr hafsa ta girgiza kai tace aaa fa sai kundawo kawai sallama tayi da malik kafin tawuce, keke suka shiga yayi masa kwatancan inda zasuje,shiga sukayi mai keken ya sauke su har kofan islamiyan da babu wani nisa sosai daga anguwar su, aydarh dai sai bin makaranta take da kallo bayan sun sauka malik yakalleta yace muje ciki, office din Headmaster suka shiga already sunyi waya tun a hanya kafin su iso suna shiga cikin mutunci suka gaisa da malik da headmaster, kafin aydarh ta gaishe sa ya amsa ta batare da ya kalle ta ba, headmaster dake sauraron bayani da malik ke masa yayi shiru kafin yace tau shknn yallabai in sha Allah babu abunda zai gagara nafahimce ka kuma mostly sauran daliban ma duk hakan ne shiyasa ma aka gina islamiyan,malik yace Tau Alhamdulilah,ita dai aydarh tayi shiru sai sauraron su take,nan akayi komai malik yabiya bill din komai kafin ya karbi kalan yard din uniform din kafin sukayi sallama cikin mutunci yafada masa ranar da zata fara zuwa makaranta.saidai sukaje kasuwa anan suka yanke yard din uniform din kafin yatambaye inda ake dinkawa mai siyan da yard din yace anan din ma suna dinkawa hijab aka dinka mata har kasa sai doguwan riga marar hannu,light blue ne uniform din hakan yasa shi siyan mata light blue din inner cap anan shagon har zasu tafi sai ya juyu yace amm a ina ake siyar da nikkab? Mai shagon yahada su da yaron yace yaraka su wajan dake siyarwa, kala biyu ya siyan mata kafin su hau keke suka tafi gida, suna isa gida time din har ankusa azahar,sharp sharp yadaura macaroni fari sai stew already suna da cefane cikin 40mins yagama komai ya juye a warmer kafin

yashiga toilet yadauro alwalla yawuce masallaci, shigowar sa kenan daga masallaci duk yau bai ganta ba sai yanzu ta gefenta yarabe zai shiga cikin gidan tayi saurin tara gabansa, hakanan kawai yaji yau yana son mata warning , chewing gum take chewing irin yarda cikakun mararsa kunyar nan ke ci wani irin baci ransa yayi bai dai ce mata komai yana jiran yaji abunda zatace din, inna ranka dade?ya karfin jiki? Kar ka damu fa kan abunda yarinyar nan tamun jiya ni bai dameni ba sam saboda ni bama da riko ko kadan,malik dake tsaye nan fuskar sa babu alaman wasa cikin isa yace “hey”quiet “ sai da gabanta yafadi yarda sound din muryansa yafita, yace this should be the first and last time dazaki dinga mun irin haukan nan, don’t repeat this mistake again karki sake shiga gabana idan ina tafiya not only me,even my wife she is not your mate, wucewa yayi yabar ta nan tsaye baki bude, yana shiga ya tarar da ita kofar bedroom da alama yanzu tafito, sallama yayi ta amsa kafin kuma ta juya takoma bedroom ,kitchen yashiga ya zuba mata abinci a plate yakawo mata sharp sharp yagama cin nasa abinci daman uzuri ya dauka yace zai je wani waje bazai dawo da wuri ba, yau ma bashi ya gyara mata bedroom din ba ita ta gyara abun ta tsaf kafin kuma ta shiga kitchen ta wanke few plates din da yabata bai tsaya wankewa ba..

Malik yace tau fa bai kai nan ba tun farko ai laifinka ne mi zai sa kace musu zakayi event daga baya kuma ka fasa?dr ibrahim yashafa kansa yace aie ni fa banma san lokacin da nace haka ba , malik yace au haba? Giyan soyayya ya dibeka kenan kayi musu karya,dr ibrahim yayi dariya kafin yace wallahi fa,malik ya gyara zamansa yace tau gashi ai yanzu ta sake ka,kaga dagaske hidiman zaayi dr ibrahim yace wallahi fa,kafin yace ni yanzu ba wannan ba number yarinyar nan zan baka ka kirata please kadan bata hakuri saboda yanzu haka fa fushi take dani,Malik yace aaa ni na aike ka kayi musu karya? Dr ibrahim yayi kasa da murya yace kai fa matsala gareka,ka taimaka please kasan fa yarda auran zumunci yake malik yace nikam taya zan san yarda yake,dr ibrahim yadinga bin malik da kallo baki sake yace ina kaima auran zumuncin ne,malik dai yayi shiru bai ce masa komai ba sai can yace yanzu naji zan kirata nabata hakuri nace mata yau har masu ciwon ido ma allura ka basu, su biyun babu wanda baiyi dariya ba,dr ibrahim yace nidai najib a komai idan zaka bata hakurin, Aydarh tabude kofan bedroom din tafito ahankali har tazo tsakiyan parlor taga dr ibrahim,ahankali tace ina wuni,dr ibrahim yace lafiya lau alhamdulilah madam ya gida ya mai jiki? Aydarh tace Alhamdulilah dr ibrahim yace madallah, malik dake kallonta ko dauke ido babu ya mike tsaye ya kalleta yace nazo ne? Batace komai ba ta girgiza kai murya can kasa tace “inna” yafahimce abunda take nufi mamaki take basa

yarda take abu kamar wata yar yarinya nufinta fa gidan inna zataje, malik bai ce mata komai ba ya juya ya kalli, dr ibrahim yace dr bara na rakata gidan inna ina dawowa yanzu dr ibrahim yayi murmushi yace tau shknn, tunda nan da gidan innan ma bazaka barta taje ita daya ba, malik bai ce masa komai ba yabi bayanta har ta riga tayi gaba,kowa na gidan nan compound din zaune in banda mazajen su, yarda suke kallon su kamar zasu cinye su yasa aydarh saukan da kanta kasa ranta a mugun bace bata son kallo ko dan shi kau malik har yasaba ma ko a jikinsa kallonsu bai dame su ba, yau ma tana nan tsaye bakin kofan tunda suka fito take kallonsu kamar mayya, malik ko sau daya bai daga kai ya kalleta ba daman ko mutuwa zatayi.

Dr hafsa dake kallon aydarh ko dauke ido babu tace tau ke kuma sai kika ce mi?aydarh ta girgiza kai tace say no word I just kept shut lokacin,dr hafsa tayi murmushi tace kamar da baki da kishi aydarh ai idan nice wallahi sai na wanke wannan karamar fuskan nata da mari,aydarh ta kalle dr hafsa bata ce komai ba tayi shiru, kafin dr hafsa ta cigaba da cewa kinsan mi kin birgeni ma da baki yi mata maganan ba tunda dai ke bat saran yin ta bace,waennan dasuka saba da hau a titi kingani babu ruwanki da ita, nan ma dai aydarh tayi shiru, kafin tace he is said wai gurl dinsa ce, nikuma nace there’s none of my business koma wace even if she is his wife I don’t bother care kawai tafita harkana ta daina kallona bana son raini, dr hafsa ta dinga bin aydarh da kallo baki bude, tace anya kau Aydarh kanki daya kuwa? You didn’t care fa kai mace na shiga sabgar mijinki kice baki damu ba,mijinki fa yanmata fa inalilahi, aydarh dai ta dinga kallon dr hafsa ganin ta dauki lamarin babba tau ina ruwanta dan yana magana dawasu,dr hafsa takalli aydarh tace kinsan mi?aydarh ta girgiza kai kafin ahankali tace ah’ah dr hafsa ta cigaba dacewa na lura har yanzu kina fama da yarinta kuma dai aydarh kin kusan 22ko kin mayi kinga ba auran wuri akayi maki ba right? Aydarh ta gyada mata kai,dr hafsa tace tau miyasa kike abu kamar baki kishin yallabai ne? Wait aydarh ko dai kawai auran hadi ne irin wanda akeyi na zumunci? Aydarh tayi shiru gabanta na faduwa don batayi tunanin dr hafsa zata mata wannan tambayar ba,dr hafsa tayi saurin cewa sorry for my questions aydarh kawai dai yarda ke kiyi din ne ke bani mamaki assuming that you love malik baza ki dinga behaving this childish way ba kan shi, feel free aydarh kaman yarda nagaya maki abaya ki daukeni matsayin babbar yayar Am 34 aydarh kinga akwai kusan tazaran 12 years tsakanin mu kinga sai dai nazo daya da malik , Aydarh tayi shiru tana sauraron dr hafsa,bata gaji ba tasake cewa aydarh sai kin maido fa da hankalin ki jikinki, you are not longer a child da idan kina ganinki gaban su mama kina tunanin har

yanzu ke yar yarinya yace noo yanzu komai ya chanza yanzu ke matar aure ce kinada aure nan dawasu months ma idan Allah ya amince sai ki ganki da baby, kinga kau dolene ki chanza wannan halin naki na I didn’t care, namiji bai da tabbas haka sharrin yan matan yanzu ba kamar yarda suke ganin yallaban dayawan su sunyi tunanin balaraben qatar ne yarda suke crushing kansa sai yabaki mamaki dan ma mijin naki neb a wasa kallon sa kawai sai yasa matsoraci fitsari,sai yanzu aydarh tayi murmushi ta sunkuyar da kanta kasa saboda dariya dr hafsa din tabata wai fitsari, dr hafsa tace Aydarh kinga duk yarda kike nan kamar ke kikayi kanki komai naki sai an kusa zagaye Nigeria kafin asamu mace haka ko tau wallahi rawar kan yaran nan na iya dauke maki hankalinta miji, yanzu jira daya rako ki komawa gida yayi Ko wajan aiki yatafi? Aydarh ta girgiza kai tace ah’ah yanada bako a gida, dr ibraheem ne yazo,dr hafsa tace ohh Allah sarki, dr hafsa tace kinga Ko lokacin daya kwanta asibiti naso nayi maki fada amma kawai naga kamar baki son maganar yasa na rabu dake, Aydarh malik yana bala’In kaunarki duk baya nunawa,ko ba a fada ba nasan malik ba wai yanada karfi bane yanzu saboda aikin gini fa kawai yakeyi amma aydarh dube ki dubi kayan dakike sakawa ko wata matan minister haka har yanzu ina mamakin kaddaran daya dawo daku rayuwa cikin mu duk iya lokacin da zaku dauka kuna boye reality ku,alama dakuma kamanin sun nuna ku yaran wasu ne a kasar nan, aydarh dai tayi shiru abba da kullun ke cikin ranta tunanin sa yasake fadu mata arai tana yawan tuna sa, dr hafsa tace tunda bakya son maganar bara na kawo maki abinci nasan inna ma tana hanyar dawowa yanzu, aydarh ta girgiza kai tace ah’ah fa kawai dai bansan abunda zan fada ba ne, dr hafsa tayi murmushi tace na fahimta Allah yakara muku zaman lafiya, kafin tace ehen aydarh natuna miyasa baku dawo aka sake p-test din ba aydarh ta dago kai ta kalli dr hafsa kafin tace babu komai, dr hafsa tace yakamata dai ku dawo saboda wannan kyaun dakike karawa kullun baki da giba amma ko’ina na jikinki na acike gaskia ciki ne,aydarh tayi murmushi tace ai na rame kuma nayi duhu a da bahaka nake ba ,dr hafsa taware ido tace kai haba,aydarh tayi murmushi bata ce komai ba nan dr hafsa ta cigaba da jan ta da fira yawancin firan abunda yashafi zaman aure ne bakaramin catching abubuwa take ba a firan nasu, sosai dr hafsa ta saki baki suna fira da aydarh duk a tunanin aydarh tasan abunda take nufi,wanda a wurin aydarh daga erh ko ah’ah sai idan abun dariya ne tayi murmushi,sosai takaro a firan nasu yamma tayi lis har yanzu inna shiru bata dawo ba,dr hafsa tace yau kinji ni sakat wannan tsohuwar bata nan ba,aydarh tace hajiya inna sarkin labari,bata gaji ma ita,dr hafsa tace wai ahaka fa cewa take bata son mutun yacika surutu ita bata son cutan dimi,aydarh tayi dariya dr hafsa tace yau dai kin wunar manah, Aydarh tace ai daman ina so

nazo kawai Allah ne baiyi ba,dr hafsa tace ko kuma yallabai ke baya son kina fita aydarh tace ah’ah fa babu ruwansa shi dr aah idan ba haka ba ai da kin zo, aydarh tayi shiru, dr hafsat ace bara kiga natashi ko wainan flour sai nayi manah tunda dai kin ki cin tuwo aydarh ta girgiza kai tace ah’ah nagode bana jin yunwa ne, dr hafsa tace no sai fa nayi sharp sharp dr hafsa ta hada komai kafin ta kunna murhun gawaye tafara suyan wainan flour anan tsakar gidan suka zauna tsaf Aydarh ke kallon yarda dr hafsa ke komai na wainan flour sai data mayarda hankalinta kaf ta na kallonta suna yi suna fira kadan kadan duk da dr hafsa ce mai firan, sallama suka ji abakin kofa dr hafsa ta amsa masa yashigo gaisawa sukayi da dr hafsa kafin cikin zolaya dr hafsa tace ai na sha kwana tazo yi manah yayi murmushi yashafa kansa yace sai ki bamu dakinki nida ita din,dr hafsa tayi dariya ta nuna masa kusa da aydarh inda take zaune tace ka zauna sai kayi joining dinmu wainan flour muke, malik ya gyara tsayuwar kafin yace ke keyi dai ita wannan da bata son aiki haka fa take kullun,Aydarh ta kallesa batace komai ba ta dauke kai yayi kasa da murya ya zauna kusa da ita,yace ki tashi mutafi kallonsa tayi kafin tace ina nan kasame ni? Malik yace ehhh shiyasa nace ki tashi mu tafi din duk maganar nan dasuke dr hafsa bata jinsu, Mike wa yayi gently ya kamata hannunta ta kwace tana tura masa baki , baice mata komai ba ya kalli dr hafsa yace tau dr zamu tafi sai Anjima ki gaishe mun da inna idan ta dawo please, dr hafsa tace aaa yallabai kabari na karasa idan yaso sai na zuba muku a warmer please saboda ita fa nayi malik yayi shiru kafin can kuma yace ko da kin bata baci fa zatayi ba nasani, Aydarh tace zan ci “kallonta yayi baki bude dr hafsa dai tayi murmushi kafin tashiga kitchen ta dauko warmer ta juye masu duk wanda ta suya kafin ta samu wani clean rubber ta zuba masu yajin a ciki tamikawa Malik har zai karba aydarh tayi saurin sa hannu ta karbi kulan ya dinga bin ta da kallo kafin tace karki basa abuna ai bana sa bane, dr hafsa tayi murmushi tace yau yallabai ka ja fada fa yashafa kansa yace ba fa ni nasa yarinya ta hararеta ba kuma tabani sako and nagaya wa yarinya fisabillahi hafsa miye laifina yafada yana murmushi dr hafsa ta girgiza kai itama dariyan take ta kalli aydarh tace tau kinji har sakonki yabata ma, Aydarh tayi shiru kafin tace tau ta daina yi masa magana bana so,malik yayi shiru yana ta kallonta har cikin ranshi yaji maganar datayin, ahankali yayi kasa da murya yarda ita kawai zata iya jinsa yace tunda ke bakya kulani kuma kar kowa ya kulani right? Batace masa komai ba sai kallonsa datayi da sauri, ta kuma kawan da kanta gefe, dr hafsa dai ta cigaba da suyan wainan flour ta, Aydarh takalli dr hafsa kafin tace thank you auntie sai anjima, dr hafsat ace don’t mention aydarh ki gaida gida, gaba tayi yana binta baya har suka isa cikin gidan babu wanda yayi ma wani magana cikin su key yasa ya bude kofan part din nasu ta riga

sa shiga ya tsaya nan ya kulle kofan kafin shima ya shiga,da warmer wainan flour ta tashige bedroom din ta ajiye kafin ta shiga toilet ta zuba ruwan zafin flask dinta a bucket dan wanka take son yi ga magrib ta kusa, towel ta daura kafin ta cire kayan ta, sharp sharp tayi wankan tafito Vaseline kawai tashafa sama sama sai perfume still bata cire towel din jikinta ba inners kawai tasaka tabar towel din daure a jikinta, black inner cap dinta kawai tasaka ta zauna kan katifan ta bude warmer kamshin wainan flour yayi mata ta dinga bin wainan flour da kallo kafin ta ware kwara 4 a gefe hakan taji bazata iya hanasa ba kwara 4 din tace tayi dadi sosai Amma ka koshi rufe warmer din tayi tashiga toilet din ta wanke hannunta,ahankali ya tura kofan dakin yashigo da sallama can kasan throat dinsa daidai itama ta fito daga toilet din tana gyara daurin towel dinta, bata lura dashi ba har takara so cikin dakin, sai sannan tagansa ta firgita ta juya babu abunda zatasa ko ta rufe jikinta sai kawai tashige jikin bango tana saukar da kanta kaf size din bra din dasuka siyo yayi mata kadan kusan half din boobs dinta a waje yake yarda tayi daurin towel din har kana iya hangowa,yi yayi kamar bai san abunda take nufi ba kamar bai san da shigan datake ba kallonta yayi kafin ya janye ido kuma ya lumshe su,kamar zatayi kuka kuma a tsoraci tace to ka dauke warmer ka fita manah ni banda kaya fa,yarda tayi maganar yasa shi hade fuska yadinga tahowa towards her har yakawo inda take jikin bangon, kallonsa take a rude ganin yana nufuta har yayi mata rumfa da fadaddan kirjinsa ta rufe idonta kam jikin ko’ ina rawa yake cikin wannan muryan tasa ba wasa yace bazan dauka na fita ba sai kin gaya mun wanda kika raina,kike harara kike gaya ma bakar maganar,girgiza kai tace wallahi Allah ban raina ka ba ni bana hara..ra.nka tafada tana ina ina malik yace idan kinga na fita sai kingaya mun wanda daya mike magana sai kin mayar masa da baka, gabanta faduwa kawai yake hankalinta yayi masifan tashi tace ni dai bakai bane ka yiakuri dan Allah wallahi ba da kai nake ba ka yiakuri malik yace idan kinga na hakura fa sai idan kin gaya mun dawanda kike yafada yana bin da kallo wani irin extraordinarily kyau take dashi yarda baby pink din towel din yabi fatan jikinta haka ma bra din baby pink ce ga towel din dake nan daure ba sosai ba,so yake ta kiyayyesa ta dinga jin tsoron sa ko abubuwan sun zo masa dasauki hakan yasa shi gently ya kai hannunsa kan towel din wllh jin hannunsa a towel din har wani fizga numfashin ta yayi suddenly taji kasancewar idonta a rufe yake shikansa sai dayaji wani kala amma ya daure dai har yana iya jin yarda gabanta ke wani irin faduwa bakaramin tsorata tayi ba, hannunta dake wani irin rawa kamar yarda jikinta keyi tasa tana kokarin cire hannunsa daga wajan tunda ga brain dinsa har tafin kafar sa yaji wani irin abu ya tsarga masa jin hannunsu ya hadu wuri guda wani irin ajiyar zuciya yasauke ahankali yafara ja da baya

sai kuma yayi Saurin fita yabar dakin ,takai kusan 3mins bayan fitan sa bata motsa daga jikin bangon dake ba yarda kirjinta ke over racing kai kaje wasan gudu tayi ahankali ta zame nan kasa ta zauna ta fashe dawani irin kuka har shedewa take takama jikinta ta kankame waje daya kamar irin yayi mata wani abu, har sai dataji numfashin ta nafita da karfi kafin ta saurara daga kukan datake.

Anan kofan gidan yazauna ,yazuba ma waje daya ido babu abunda yakeyi irin tunanin rayuwarsa yanzu haka shi mijin aure ne nauyin ci,sha surutu da kuma tarbiyyar yarinyar na hannunshi,duk ya dauke wannan kuma ai yana yi bakin karfi da ikonsa tunda duk saboda da ita yake duk wani abunda yakeyi, da kuma amanar ta da ummi tabasa ,tunani ne kala kala a ransa tau yanzu idan yasake kamar yarda zuciyar sa ke raya masa fa?idan yabari soyayyar yarinyar da tausayinta yakarasa shiga zuciyarsa da ruhinsa fa? Yasan kiyayyyar da mahaifinta ke ma abby, yasan yarda mahaifinta yake kar ya shimfida rayuwa da ita daga baya mahaifinta yazo ya raba su fa? Duk duniya bai taba jin wata a rai ba bayan ummi dasu aysha sai ita,saukar da ajiyar zuciya yayi ahankali yatashi ya shiga cikin gidan sai da yarufe kofan part din kafin yazauna parlor yana kallon kofan bedroom din ji yake kamar yashiga,amma yafasa. Kasancewan yayi daran bacci shiyasa ya makara sallan asuba ma a gida yayi ta Sai da ya gyara ko ina kafin ya dafa masu indomie sharp sharp yau ko ganinta baiyi ba ko daya shiga daukan kayansa tana toilet,bayan yafita already tayi wanka tashirya ta fito tun dazo take son tafita ta dauko tsintsiya amma bata son ta fita su hadu wani irin girma da kunyarsa take ji gani take babu wani sauran abu kuma daya rage yanzu yariga da ya gama da ita, guntun hawaye tashare kafin ta mike ahankali ta bude kofan dakin tana kallon cikin parlor ya share koi na babu kuma shimfidar shi hakan na nuni daya fita komawa tayi bedroom din ta fiddo warmer jiya takai kitchen tana shiga taga nan ma ya share tass sai warmer nan ajiye tabude taga indomie ce ciki.

Ta dinga bin indomie da kallo kafin ta rufe warmer,Sai da ta gyara bedroom din tass yau hadda toilet ta wanke ,tana aiki yau duk jikinta babu dadi kaman wace batada lafiya,ahankali ta fito daga bedroom din tana tafiya kamar mai counting steps dinta kitchen din tashiga ta ajiye mopper da tsintsiyan kafin ta bude warmer ta dauki plate ta zuba kadan ta fita parlor,bata ci dayawa ba ta ajiye ,kitchen ta mayar da plate din tayi zaune nan parlor, knocking kofan akayi kamar bazata bude ba sai kuma ta tashi,tace waye? Shiru taji ba a amsa ba kuma ba’a sake knocking din ba hannu tasa tabude kofan ahankali, kallonta yake ko kiftawa babu ita dai kanta na kasa kafin kuma ta juya tashige bedroom,bedroom din yashiga

zaune take kan katifa ta zuba ma waje daya ido yayi kasa da murya yace hala baki iya gaisuwa ba? Kaman bazata amsa ba sai kuma ta tuno da abunda yafaru jiya,ahankali bata kallonsa ta juyan da kai gefe kafin tace “ina kwana” bai amsa ba sai bin dakin da kallo da yakama yi,itadai kanta na kasa bata dago ta kallesa ba, can yamike tsaye yace yau bazaki yi sharan ba?ta ware ido ta kallesa tace nan din fa dana gyara ,duk dayaga yarda dakin yayi kyau amma kawai so yake ya tsokaneta, yace nan din ne kika gyara? Ta bata fuska tace nafa gyaraaaaaaaa yanda taja kalaman kamar yar baby yasa shi kallonta, yace tau said ai ki sake gyarawa nan dai babu alaman anyi shara gaskia dai,batace masa komai ba tayi shiru ta kawar da kanta “can ya mike har yakai kofa ya juyu yace,dakin yayi kyau “sai kuma yafita ta dinga bin kofan da kallo kafin tayi murmushi can kasa tace sai kace shima iyawan yayi, yana fito ya wuce wajan dayake yin cefane vegetables yasiyo masu sai nama, dr hafsa ya hango yakarasa in datake,sai sannan ta gansa tayi murmushi tace “ina kwana “yallabai? Malik yace Alhamdulilah ya aiki? Tace Alhamdulilah,kafin yace inna fa? Dr hafsa tayi kasa da murya tace bata da lafiya fa,malik yace subhanallah dr hafsa ta gyara tsayuwanta tace fever take nayi magana k ozan mata allura ta rufe ni da masifa yanzu haka tana can kwance malik yace dasauki ba? Tace ehhh gaskia dasauki kasan dai halin ciwon inna malik yayi murmushi yashafa kansa yace in sha Allah zamu zo shigo idan anjima ki gaishe ta dr hafsa tace in sha Allah. Tana parlor zaune yafito da knife sai karamin rubber da cabbage sai carrot a ciki gawani plate rike a hannunsa,kallon shi tayi sai kuma ta dauke ido bai kalle ta ba ya zauna yafara yanka vegetables din kamar wani hadaddan chef,tunda yafara yanka vegetables din take kallon yarda yake duk abunda takeyi yana lura da ita sai daya kankare carrot din tass kafin yace, “yanka “kamar daga sama taji maganar sa batace komai ba ta sa hannu ta karba yarda yakeyi haka ta dinga bi tana yankawa ahankali, kallonta yake har ya shagala bakaramin kyau tayi masa ba,yarda take hade gira tana yanka carrot din murmushi yayi kadan kafin yayi kasa da murya yace “kin gaji ne? Ta girgiza kai tace ah’ah zanyi, malik yace tau muje kitchen sai mu karasa girkin?ta gyada masa kai kafin tayi wani cute smile tace erh nima zaka koyamun? Malik daya sakankace yana kallonta kamar wani yaro ya gyada kai yace mu tafi ,kitchen suka shiga ya mika mata cubes yace bare wannan kin iya? Tayi kasa da murya kafin tace to ka bude daya sai nagani,kallonta yayi bai ce komai ba ya matso kusa da ita ta matsa kadan tadan bada space a tsakaninsu cube din star daya ya dauka yace look up,ta dago kanta yafara bare maggin kwara daya ya bari kafin yace karbi ki bare sai nagani, fine fingers dinta tasa ta dauki cube daya tafara barewa, yarda take juya hannunta tana barewan yake bi da kallo sosai kananun diamond rings dinta

sunyi ma hannun kyau sosai, tana bare daya ta dago tayi wani hadaddan smile tace,”nayi” malik ma yayi murmushi yace Good job mamana jin sunan daya kirata yasata bin shi da kallo dauke idonsa yayi kafin yacigaba da frying kayan miyan tacigaba da bare maggin har tagama kafin murya can ciki tace “nagama”kallon maggin yayi ya kalleta kafin yayi saluting dinta tayi murmushi kadan har cikin ranta take jin dadin yarda taga tabare maggin sosai take son ta iya girki kusan duk abunda ya dauko zai zuba sai yafada mata ko ya nuna mata duk babu wani dogowan magana amma ahaka take koyon duk abunda ya nuna mata din cikin few minutes suk agama girkin dake ta faman kamshi kallonta yayi itama shi ta kalla sai kuma ta saukar da kanta kasa hannunsa ya zuba a aljihu kafin murya can kasa yace zamuje mu duba inna ,batace komai ba shima bai sake magana cikin warmer da dr hafsa ta ba ta wainan flour jiya yazuba abincin kafin ya juye sauran cikin warmer su jin ana kiran sallarh yasa shi cewa idan nadawo masallaci sai mu tafi,fita yayi a kitchen sharp sharp kasancewan Friday ce yayi wanka wani white shadda yasaka duk da ta kwana biyu amma bakaramin kyau tayi masa ba agogon daya siya black yasaka sai azurfan shi black itama wani ubansu black shade ya kafa a ido yah arrahamar rahimin ya rabbil alameen Malik yafi kyawu kyau yayi wani irin kwantacan musulmin kyau, sai lokacin tafito bayan tagama wanke abunda suka bata wajan girkin bata ko kalli inda yake tsaye ba a parlor yana linke prayer mat zai yafa a shoulder tawuce cikin bedroom din, wanka tashiga ta dauro alwalla kafin ta fito sai datafara yin sallarh kafin ta dauki vaseline tafara shafawa,har zata cire hijab din jikinta sai kuma ta tuno da abunda yafaru jiya yasata barin ta , yau hadda powder tashafa wanda tunda yasiyo ya ajiye ko taba ta batayi ba tayi using kajal da kuma masccara sai lips stick kadan tasa brush ta gyara giran ta, bude wardrobe tayi tafito da black lace foam bra sai wani black pant wanda suka siyo waccan ranan a shagon matannan, kafin tajawo fitted gown din da ummi tabata wanda kullun kayanta na a wanke goge har baya gajiya ma da mata wanki duk da kayan bawani yawa ned asu ba,saidai har yau taki barinsa ko da kallon bra dintayi yayi kar aje ga maganar wankewa ma,shiyasa jiyan nan taji kamar dakin ya tsage ta shige, ko’ina na jikinta sai da tabi sa da perfume as usual, kallabin atamphar ta daura all back irin nasa hijab ,gashin gaban kanta ya kwanta luff kamar na babies, bude kofan dakin tayi tafito tana fitowa ta samesa zaune kan carpet yana cin nasa abinci batace masa komai ba ta dauke kai tayi hanyar kitchen dole sai tabi ta gabansa kafin tashiga kitchen din kafa yasa mata kawai sai ji kayi yaraff, ta fado a cikinsa wani dan banza kara tasaki duk da bawani muguwan faduwa tayi ba ,da karfi tafadar da kirjinta akan laps dinsa saboda yanayin faduwan datayi,murmushi mugunta yayi jin

yarda tayi karan, dasauri tafara kokarin mikewa ta kasa tadinga kallonsa kwalla cike a idonta kafin shi da kansa yasa hannu ya dago ta,ta zauna tasa hannu ta rufe idonta tabare masa baki zatayi kuka yasa karamin yatsa kan mini bakin nata kafin yace this should the first and last dazaki ganin zaune baki gaishe ni ba idan lokacin gaisuwan ne am I cleared yakarasa maganar da alaman tambaya? Tana jin sa Still kuma batayi shiru ba tacigaba da kukan ta wanda yafi kama dana shagwaba,yawani hade rai yace secondly wannan perfume din naki yayi yawa ki daina cikasa hakanan,sai yanzu ta saki hannunta daga kan fuskan ta kafin tace “perfume? Ya gyada mata kai yace kin ji ni aie batasake cewa komai ba kafin ta mike tsaye ta nufi ahanyar kitchen abinci ta zuba kadan kafin ta dauki ruwa ta fita still yana zaune parlor ko style din dayayi nazama bai chanza ba, ita dai tayi wucewan ta bedroom.

Yana gani Ramlah yasace kallon aydarh kanta na kasa har yariga da yasaba ma tafiya da ita ahaka kullun kanta na kasa idan suna tafiya,Ramlah nagani malik dayake zuciyan kare gareta tawani gyara yafin mahayafin abayar ta tawani katon kwan chewing gum din datake chewing ta karasa fita zauran gidan tana jiran isowarsu, shidai malik ko kallon ta bayi ba balle ma ya ga abunda tayi aydarh kau da daman ko zata mutu ba ta ita takeyi ba, hannunshi rike da warmer inna dasuka zuba mata abinci suna zuwa zauran Kamar daga sama sukaji muryar Ramlah tace yallabai kawo a rike maka kulan cike da duniyan ci tayi magana malik ya girgiza kafin ya juya ya kalli aydarh yarda tawani hada rai ta tsuke fuska tana kallon Ramlah yace aaa kibarshi nagode aydarh dAi natsaye tana kallon su.

Tana kallonsu kafin ahankali ta bi ta gefen Ramlah tafice a gidan,kofar gida ta tsaya tana hade fuska kamar wacce rana ke bugu “ tawani bata rai, malik yazo zai wuce ta gabantaa kamar bashi take ma magana yanzu ba,shidai yayi shiru baice mata komai tun dayake a duniya bai taba ganin raini irin haka ba,baisan kalan tsaurin ido kalan na Ramlah shi da ko namiji dan uwansa ke shakkar sa balle ita wannan abun yayi tunanin warning din daya yayi mata jiya ya isa, amma ina kamar ma bayi mata ba,yarda yau tafi shishige ma sa fiye ma da,daa ahankali yake fitowa daga cikin gidan,Still aydarh na nan tsaye, kallonta yakeyi ko kiftawa babu yarda tawani hada rai da ta gansa matsawa yayi kusa da ita kafin yace sorry I keep you waiting ,kinsan halin yarinyan nan bata so taga ina wahala baki ga tace na bata daukan warmer din ba?aydarh ta juyo sai da tafara zubawa kofan gidan harara kafin ta kalli malik ido ido cikin ido,cike da masifa tace “why baka bata warmer? Ai da ka bata,malik ya dinga bin ta da kallo ganin irin masifan datakeyi cike da yarinta shagwaba da tsiwa irin sturbborn girls din

nan,malik yashafa kai kafin yayi kasa da murya yace,”yanzu dakike ta masifa sai kin ja an kallemu ace kina wa mijinki fada?tawani hade kafin tace “to bana ci ta daina kallona ba kuma bata daina din ba malik ya juya yaga babu komai kofan gidan kafin yasa hannu yaja long nose dinta yace ai dole ta kalleki tasan kishiyarta sosai aydarh ta bige masa hannu kafin tace Allah ya kiyayaye waye kishiyanta? Wannan shashashar kake hadawa dani wai kishiyar ta ko ma wacece ni dinta that’s not my business kawai nidai ta daina kallo if not hmm ,Malik yayi murmushi yace if not what? Ai da kin karasa malama, aydarh batace komai ba ta juya tayi gaba ya bi bayanta yace sturbborn bea, har sunyi nisa Ramlah ta sake biyo su baya da sassarfa ta isko malik wanda shine baya yana binta ita tana gaba, Malik dayake bin Ramlah da kallo fuskar nan babu yabo babu fallasa,Ramlah tayi wani tsayuwa irin na yaran nan masu rawan kai kafin tace naga fa gidan inna zakaje nima kuma zanje please ka bani na rike maka, aydarh tawani juya batace komai ko kallan su batayi ba kafin tace give me,kamar wanda aka ja da magnet haka ya mika mata wannan warmer kafin fuskan nan ba wasa ta kallesa murya cike da ba da umarni da isa tace masa let her to go back, wallahi malik kamar wani mai jiran umarnin ta shima ya juya kafin yace ma Ramlah “go back “yabi bayan aydarh suka cigaba da tafiya Ramlah kau ta na nan tsaye ji take da tanada bindiga yau sai ta harbe aydarh har suka shige gidan inna tana nan tsaye kamar an dasa ta.sai da suka gaisa da dr hafsa kafin su shiga dakin inna, sallama sukayi inna dake nan cikin wani katon bargo ta amsa masu Kamar irin wace ta shekara dari tana ciwo nan kwance, Malik yace asha kam sannun inna jikin new ai har yakai haka yafada yana kallon dr hafsa da ta shigo yanzu ko zama bata kai dayi ba, dr hafsa ta sauke ajiyar zuciya kafin ta gyada ma malik kai alaman aaaa ya fahimta bata son yin magana ne saboda tasan halin yan kayan ta, malik ya sake matsawa kusa da inna kafin murya can kasa yace sannu inna,tayi shiru yace yanzu mike maki ciwo nan ma tayi shiru daga aydarh har dr hafsa su dai suna nan zaune sun zubawa sarautan Allah ido ba kamar dr hafsa da taga innan cikin bargo mata da yanzu ta gama Kare mata tanadi har ta fita shine wai yanzu dan taji su malik din sun shigo dubiya ta kwanta,juyin duniya malik yayi inna tayi magana amma tayi shiru bata ce komai,can ya sake dan kasa da murya kafin yace tau inna tashi mutafi asibiti kwara ai allura asa karin ruwa tunda naga jikin yayi kasa kwarai bara mutashi yafada yana kokarin mikewa aikam inna ta riga malik tashi ta na ajiye bargon gefe,kafin tayi mitsi mitsi da ido tace ni fa bana son kiran masifa daga mutun ya kwanta sai a fara kiran wasu bambaman tijara wai karin ruwa wa zaa karawa ruwa banda neman jafa’I aaa tau lahiya ta lau naji sauki Alhamdulilah,aydarh ta dinga murmushi bakaramin dariya inna tabata ba,

malik ma sai dayayi murmushi kafin ya koma inda yake zaune ya zauna, dr hafsa dai batace komai ta fice daga dakin,malik yace tau sannu ai yanzu jikin da sauki koh?inna tace ah dasauki Alhamdulilah ai naji sauki sosai kafin yace tau yanzu ga abinci nan sai ki tashi k ici inna tace tau shknn zuba man abinci daman idan ba kai ba wa zai bani shidai malik bai ce komai ba ya dauki wani clean plate daya gani da spoon nan gefe ya bude warmer ya zuba mata abincin daidai daidai yace tau gashi sai ki daure ki ci,inna ta karbi plate din sai da ta cinye tass kafin ta kalli malik tayi kasa da murya tace tau ita mai dakin naka taci abinci ko baza taci bane? Malik ya girgiza kai yace ehhh taci,inna tace tau madallah ita fa waccan matar fa? Malik yace bara tadawo ai nasan zata zuba, inna ta dinga zuba labari kamar ba ita bace ba marar lafiyan malik na biye mata ita dai aydarh bata cewa komai sai sauraron su take can ta mike,malik yabita da kallo inna bata ma lura ba,bai ce mata komai ba har tafice ta shiga dakin dr hafsa kafin ya dauke kanshi daga kallonta ya maida hankalin shi wajan inna da take ta zuba kamar kanyan da ba dadi, dr hafsa tace naji dadi ma dayake yallabai ne daidai ita baki ga ta mike ba, aydarh tayi murmushi , kafin tace aie yanzu har taci abinci ma dr hafsa tace kai haba,ah anci sa’a ko dayake ma aie inna bata wasa da cikinta, aydarh tace uhm dr hafsa tace kinga fa wata friend dina ce ta haihu kar jibi suna ban samu naje barka ba,aydarh tace oh Allah sarki, dr hafsa tace bari zanyi naje sunan ma baki daya, aydarh tace gaskia dai,kwara ki bari din kije baki daya, dr hafsa tace yallabai da zai barki da sai mu tafi tare ma Aydarh tayi kasa da kai batace komai dr hafsa tace naga kamar baya so kina fita ma ba? Aydarh ta girgiza kai tace ah’ah fa,dr hafsa tace kin fadi gaskia dai,yawwa har zan manta ina mutuniyar mu?aydarh tayi shiru alaman bata gane abunda dr hafsa ke fadi ba,dr hafsa tace Ramlah manah,nan shiru tayi kafin tace waye haka? Dr hafsa tayi dariya domin har tafara sabawa da halin aydarh itama ita dai komai nata unique ne,dr hafsa ta dinga dariya tace kinga kishiyarki nake nufi, sai sannan aydarh ta daga kai tace, ni miye hadani na da wannan, dr hafsa tace ga hadin ki da ita nan kina kokarin sa ido ki bar ta da mijinki kinga aydarh nib a zugaki nake ba amma a matsayina na babba mai hankali bazan so taba barin ki bar shi wannan abun nashige ma rayuwar sa ba,ina ma ace wata macan kirki ce wannan ai yanada daman da zai yi aure ya aure duk wace yake so,aydarh dai ta kasa dauke kanta daga kallon dr hafsa maganar ke shiga har brain dinta batace komai ba dr hafsa tacigaba dacewa yanzu haka fa akwai wani na nan sosai yake sona amma matarsa kamar haukace ma ce gaskia haka na lura,saboda irin cin mutunci da take mun nidai ban iya masifa ba kuma bana son raini wallahi aydarh shiyasa har yanzu nake ta adduar zabin Allah ku dai ku godewa Allah,aydarh kinyi sa’ar miji saidai fatan kuma yara nagari,

aydarh kanta nakasa.malik ya tsaya daga bakin kofa yayi sallama dr hafsa ta amsa masa,kafin yace ta fito mu wuce gida yamma yayi , dr hafsa ta kalli aydarh tace mai gida ya ce ki tashi ku tafi, aydarh ta mike ahankali tace sai anjima auntie “har kofan gida dr hafsa ta rako su.

Ta dinga kallonsa kafin tayi shiru can kuma ta dago kai tace to a ina ne zakuje bikin? Malik bai yi tunanin zata amsa sa ba dayana fada mata shiyasa yayi mamaki, yace mata can nasarawa,tace lafiya? Yace yeah a can ne matar take “aydarh tayi shiru tarasa ma mi zata ce masa, kafin yace yau saura kwana biyu mutafi islamiyan ku ai naga maki na sat sun ne kawai right? Ta gyada masa kai alamar erh, babu wanda yasake magana cikinsu yayi shiru bai ce komai ba, Ahankali ya mike ya bude wardrobe dinta, ya fiddo uniform din kafin ya fito parlor iron ya hada yagoge mata uniform din tass kafin ya kwashe su ya koma bedroom din saida ya mayarda su cikin wardrobe kafin ya jira tafito daga toilet da alama wanka tayi domin fuskan ta da alaman lema sai gashin gaban kanta da ya kwanta luff, kasancewan hijab dinta tayi baya, ya dinga bin fuskan ta da kallo ita dai bata kallonsa kanta nakasa, juyawa yayi har ya kai kofa idan kin gama ki same ni a cikin, kafin yafita ya rufe mata kofa sharp sharp ta shirya bakaramin dadi take ji ba,yarda take koyon abubuwa yanzu abaya tasaka tayi shafa perfume sai inner cap black da tasaka tafita , a kitchen tasame sa kafin su ya daura white macaroni da zaiyi stew dan tagani,cikin nutsuwa da aji suke komai duk da babu wani dogowan magana da ke shiga tsakanin su amma tsaf take koyon komai zuwa yanzu zatayi iya yin stew tadafa farin pasta da kuma macoroni wainan flour dakuma jallof.cikin fe minutes su ka gama kafin ya fita saboda lokacin isha’I ya kusa ita tagyara kitchen din ta kuma wanke duk wani plate dasuka bata, sharp sharp tashiga tayi alwalla tafito tayi sallarh shima sai sannan ya shigo sai datagama sallan tafito a parlor tasame sa zaune kan carpet ga warmer sai plate biyu spoons biyu da serving spoon kan plates din yana gani tafito ya bude macaroni ya zuba mata daidai yarda take ci a plate kafin yasa stew din kadan yasaka mata spoon din a gefe, ya tura mata gabanta kafin shima ya zuba ya sai ta kalli abincin nasa ta gefen ido kafin ta cigaba da cin nata ahankali,shima abinci yake ci babu wanda ke ma wani magana, bata cinye ba ta mike ahankali yana kallonta ta shiga kitchen ta ajiye plate din ta rufe kafin ta dauki ruwa ta sha kafin ta dauki plate ta saka mashi pure water biyu a kai tafito takawo masa kallonta yayi har ta ajiye kafin yace thank you,duk sai taji taji kunya ita bai taba yi mata abu tace masa thank you ba shikam yau ruwa kawai tabasa yace thank you,bata tsaya ba tayi wuce bedroom din ta zauna,littafin dasuka siyo a islamiyan ta dauka tana dubawa kafin ta tashi ta dauki books din ta zuba cikin hadaddan back bag din da

yasiyo mata na zuwa islamiyan, abu biyu ne ya hade mata murna da kuma fargaba,is she eager gari yawaye ta ganta a islamiyan a haka ta kwanta.tass suk agama aikin gidan as usual ta gyara bedroom ta wanke toilet dinta shikuma ya gyara parlor da kitchen ya wanke toilet din nan parlor,sai daya tabbatar da tagama gyaran bedroom din sannan yashiga tana tsaye ta tasaka camesole din uniform din da aka dinka mata sosai rigan ya karbi jikinta kasancewan bata da hannu yasa har kana iya ganin hannu light blue din bra dinta exactly irin uniform din, wanda yabi jikinta ya kwanta luff gashin kanta take kokarin cusawa cikin light blue din inner cap din dayasiyo mata ta dinga sakawa da uniform dakin ya dauki kamshin jikin ta juyuwa tayi ta gansa tsaye jikin kofa , dasauri ta karasa saka hulan ,kafin ya kalleta yayi smile yace yan islamiya an shirya tayi kasa da kai ta gyada mashi kai tace erh yace Alright kafin muyi later kizo sai muyi girki tace alright, ahankali ta biyo bayan sa har kitchen din indomie sukayi sharp sharp sukayi vegetable indomie kafin sukayi frying egg kusan komai ita tayi yau sai dai ya nuna mata,yana kallon yarda takeyin komai ga zufa kadan a goshinta wani irin hadaddan kyau tayi masa a yau din he likes everything in her,her sturbborness ,shiru shiru dinta tsiwa yau din hakan nan sai yaji kansa a matsayin mijin aure shima yarda tagama indomie tayi serving dinsa kadan ta zuba taci kafin ta koma daki abayan tasa ta dauki back bag dinta ta koya kafin tasake fesa perfume kadan nikkab din ta dauka ta dinga bi da kallo bata san yarda zata daura sa ba,Ahankali tafito tajawo dakin rike da nikkab din a hannu kallonta yake ko kiftawa babu kafin yace Tabarakallah, a ranshi takalli sa kafin ta wara ido tana mika masa nikkab din tace gashi ya kalleta yace ni zan saka hala? Tabata fuska tace ahah ban iya sakawa bane aie bai ce komai ba ya bude nikkab din yazo daidai ita duk da ba guntuwa bace amma yayi mata tsawo dayawa ahankali yake daura mata nikkab din har ya gama,Sosai nikkab din yayi mata idonta dayasha kajal yafito tarr , gaba yayi tadinga bins abaya har sai dasuka fita part din kafin yasaka key yarufe, suna fita suka samu keke ya mika su har makarantar, Sai ya tabbatar an ta shiga aji kafin ya wuce wajan aiki. Sit tasamu daga nan gaba babu kowa anan ta zauna kasancewan duk matan aure ne waenda basu samu isa shan illimin addini ba saboda haka aka bude ajin tunda ga farko aka fara karatun lokacin al’quran ne kowa yafito da quranin sa aka fara krt, Sosai aydarh ke fahimta saboda tasa ma ranta karatun ba karamin maida hankali tayi ba .lokacin break ne babu malami sauran students din kowa yacigaba da harkan gaban sa masu surutu nayi masu cin abinci haka masu ba yara abinci ma haka kasancewan dayawan su duk goyo suke ,bata cire nikkab dinta ba kanta nakasa tana duba karatun da mai tajwid yayi masu yanzu sai bin book din take da kallo zata iya maimaita larabcin amma bazata iya

fassara hausan ba,a zuciya tace idan naje gida sai na nuna masa yakoya mun, wasu gang din mata ne zaune a bayan ta dayar takasa hakuri tace maman baffa wai bakuji wani irin kamshin dake fita daga jikin wannan sabuwar zuwan ba?wace aka kira maman baffa tace wani iri ma naji wallahi tana shigowa ai gaban sit dina take, dayar tace niba kamshin ba dan Allah kuji diamond rings a hannunta, maman noor ai ke kinsan diamond ko gasu nan dai kananna kwara biyu a yatsanta nafarko dana can karshe kafin babban yatsa ko? Maman noor data gama bawa yarta nono ta gyara zama tace sosai ma wllh diamond rings ne ko da mukayi zaman malaysia babu yarda banyi da dad noor yasiyan man ko daya bane yace bazai siya ba waye shi, maman baffa ta zara ido tace hadda fa English gold a dayan hannunta gashi can a yatsa na biyu, maman noor ta tabe baki tace wallahi kuma mai shegen tsadar ne saboda yan kanannan can sun fiye tsada, dayar tace ji ma yarda skin dinta kewani milk milk gawani shegen glowing datake,maman baffa tace Allah daya gari banban naso ace babu nikkab a fuskan naga fuskan maman noor tace uhm ni fa duk wannan bai daman ba kamar yarda tazo batayi manah magana ba tayi wani shiru,maman baffa ta rike baki kafin tace kiji maman noor dawani zance saninmu tayi ne kuma wannan duk ma abunda tayi ai takai tayi wallahi maman noor tace tau saura kuma ku da shigen shishigi wata taje tayi mata magana,maman ta mike tsaye tace haram haramun wallahi kau sai nayi mata magana yoo ko da wannan turaran banayi mata magana ba kin kau san yarda baban baffa ke son kamshi kuwa? Maman noor tace haka kuka iya aie da kunga mutun tsab sai ku shige masa ai ni wallahi har yanzu baayi wacce zan shigemawa ba,maman baffa tasaki baki tana kallon Maman noor tace aaa fa maman noor da dai anan ajin dai babu kamarki amma yanzu an kawo wace idan tana wuri baki isa ki nuna kin san komai ba,maman noor tayi mata wani dan iskan kallo kafin tace tau tsaya kafin kije nagaya maki wani abu maman baffa,ko da turaran tabaki kamshinsa kawai zakiyi bazakiyi kamshi irin nata ba saboda ita natural body scent dinta yahade da turare maman baffa tadawo ta zauna tace kai haba da Allah? Maman noor tace wallahi kuwa maman baffa tace tau ke taya kika sani ma? Maman noor tace Maman baffa kenan kamar dai kinta miye sana’ata mudai gyara idan na diya mace babu wanda bamu sani ba wallahi,maman baffa tayi shiru sai can kuma tace gaskia dai ita wannan Allah ya yabata, duk abunda suke cewa tana jinsu ko juyawa batayi ba balle ta kallesu,ta cigaba da abunda takeyi,12:00pm daidai ake tashin su tun 11:40 yazo ya zauna cikin office din headmaster suna fira sama sama kamar irin sun san junan duk kusan headmaster ke yinta,shidai malik na sauraron sa,yana jin an tashe su yayi ma headmaster sallama yafito bakin kofa duk kansu da nikkab wani ya sauke nashi wani kuma ya dage sa

sai fitowa sukeyi wasu da goyo wasu ciki wasu kuma da yara rike a hannun sai baza ido yake yaga ta inda zata fito,Gently take tafiya kamar wacce bata son taka kasan har tafito bakin kofan school din duk inda ta bi sai maman baffa da maman noor sun sa kafar su suma,so suke suyi mata magana;tana dago kai suka daga ido har yanzu fuskanta da nikkab murmushi yayi kadan kafin yayi mata waving hannu hango sa tayi hakan yasa ta tafiya ahankali ta iske shi kafin tadaga nikkab din tace “ka cire mun “ya girgiza kai yace mutafi gida sai nacire maki din tayi kaman zata fashe dakuka tace noo zafi fa “ahankali ya sa hannu ya kwance nikkab din ya rike a hannu, maman noor da maman baffa da tun dazu suke kallonsu, ganin abunda yafaru yasa su hada ido, kafin maman baffa tace yah rabbil alameen maman noor ashe larabawa ne?maman noor tace maman baffa ko dai yayanta neb a mijinta ba kiji kama fa suke dan dau kawai kalar skin dinsu ya bambanta, maman baffa tace aaa gaskia kila dai auran zumunci ne gaskia saboda ai kinga class dinmu ba akawo yan mata,maman noor tace ai gaskia naga kyau yau wai Allah.Malik yace mutafi daga wurin aiki nake ,keke suka samu har gida tare suka shiga kasancewan rana ce babu kowa tsakan gida, suna shiga tawuce bedroom sai datayi wanka tashirya kafin tadawo ta linke uniform dinta ta ajiye,tayi tunani yafita shiyasa ta fito ta shiga kitchen din,tsaye tagansa yana zuba pasta cikin ruwan daya tafasa yanzu, kallonta yayi yace aiki ke akwai Sosai yau zaki iya yin stew da kanki ne?gyada masa kai tayi, yafita yace sai na dawo.

Tsaf tagama girkin kafin ta zuba a warmer already tayi sallan azahar, kitchen din tasake gyarawa kafin ta dawo parlor ta zuba abinci kadan tacit asha ruwa,kafin takoma bedroom ta dauko jikkanta ta bude littafin daaka koya musu yau tadinga bi da kallo tana maimaita karatun daki-daki du kinda ke bata gane bas ai tasaka pen tayi underlining ta niyyar idan yadawo sai ya ta nuna masa ya gyara mata,knocking taji ana yi ta warware veil din ta yafa kafin ta tafi wajan kofan tace waye? Dr hafsa tace nice,aydarh ta bude kofan tayi murmushi tace welcome auntie,dr hafsa ta mayar mata da murmushi tace thanks dear kafin aydarh tabata hanya tashigo anan parlor suka zauna,aydarh tace ina wuni?ya jikin inna?dr hafsa tace lafiya lau aydarh inna taji sauki ta fita ma,aydarh tayi murmushi tace masha Allah kafin tashiga ta zuba mata abinci data dafa sai ruwa kan plate ta kawo mata,dr hafsa ta girgiza kai tace aydarh kullun nazo ko gajiya bakiyi abinci dai abinci dai dana shigo amma ke idan kika zo nabaki kice kin koshe “aydarh tayi murmushi kafin tace “Allah auntie nakoshin ne “dr hafsa ta girgiza kai tace ai dayake ina lura dake baki son cin abinci sam aydarh tayi shiru tana murmushi bata ce komai ba,dr hafsa ta kalli aydarh bayan tagama kallon

books din dake nan ajiye kan carpet kafin tace islamiya kika shiga ne aydarh ta gyada kafin tace erh,dr hafsa tace masha Allah Allah yataimaka,yau kika fara zuwa ne?aydarh tace erh yaune first day dina,dr hafsa tace Allah yabada sa'a aydarh tace "Ameen "babu wanda yasake magana cikin su, dr hafsa ta cigaba cin abinci ta kafin can tace yauwa aydarh so nake ki tambayi yallabai gobe zamuje wajan suna na lura babu inda kike fita sai tare da shi kawai aydarh tayi kafin tace "gobe akwai islamiya kuma "dr hafsa eyyerh karfe nawa kuke tashi ne?aydarh tace twelve ne closing time dinmu,dr hafsat ace ahh Alhamdulilah kinga ai sai wajan four zamu tafi kinga time din ai kun taso har ma kingama girki time din kin huta aydarh tace Allah yakaimu dr hafsat ace Ameen kafin su cigaba da fira sama sama duk labarin friends dinta take bata wani abun dariya wani kuma abun tausayi can dr hafsa tace kinga har naso na manta yau dasafe nafita clinic aka kawo wata zata haihu ,inalilahi waina illahil rajiun aydarh mata na wahala wajan haihu yaron kansa fa yakoma a chest din matar nan gashi yanzu doka ne an hana juyawa saboda ana samun matsala gashi jini ya balle wa matar nan sai bleeding take wallahi abun tausai abun yafi karfin clinic saidai nahada su dawani Doctor a genral da taimakon sa fa muka shiga aiki da ita emergency munyi aiki successfully am the saddest part of the event yaron komawa yayi daga karshe abun ba dadi,aydarh datayi shiru tana sauraron dr hafsa har tayi shiru duk da bawani Sosai ta fahimce abunda labarin ya kunsa ba amma sai data nuna jimamin ta sosai bakaramin tausayi matar taba ta ba da babyn dayarasu,tace babyn ya rasu auntie?dr hafsa ta gyada kai tace ya rasu aydarh ya rasu gyada ta sauke ajiyan zuciya tace Allah yayi masa rahama yaba maman lapia,dr hafsa tace Amin,kafin ta mike tace bara kiga na wuce gida daga general din nake ruwa kawai na watsa na fito so nake nadan samu hutu clinic zan kwana,aydarh tace sorry "dr hafsa tace tau sai anjima ki gaishe da yallaban idan yadawo,aydarh ta gyada kafin ta raka dr hafsa din har kofan part din,ta dawo ta kwashe plates din ta wanke ta ajiye kafin tadawo ta dauki books dinta ta wuce daki.
Wanka yayi kafin ya zuba abinci yaci yana ci yana murmushi bakaramin mamaki take basa ba how sharp her brain is yana sa shi jin tana sake shiga ransa, yarda tayi abinci da yarda ta gyara kitchen din sai ya dinga tuna masa dream din wani abu mai kyau daya tabayi a baya yasha yin mafarkin wanda wani lokacin har murmushi yakeyi shi kadai idan yana tunanin mafarkin har yanzu kuma bawai yadaina ba time to time yana yi girgiza kai yayi kafin ya cigaba da cin abinci har yakarasa kafin ya mayar kitchen, parlor yafito kafin yahada iron ya goge sabon dinki dayayi kala biyu wanda daya kala daya ne shi da ango dr ibrahim wanda zasu saka a ranan daurin aure wani hadaddan ash gezner ne mai azaban kyau da tsada wanda Allh

musa ne yasiya musu shida dr ibrahim din dayan kuma plain yard ne yasiya white aka masa dinkin kafta duk na bikin ne wanda ranan Tuesday zasu tafi su dawo sat bayan angama daurin aure, Sai da ya gama gogan kafin ya dauki kayan yashiga bedroom din ya ajiye kayan a wardrobe ta na nan zaune kan katifa Still hannunta rike da littafin ta tana sake dubawa malik bai ce mata komai ba kamar yarda ita batace masa ba ya ajiye kayan yafita yawuce masallaci bai dawo gidan ba har sai da akayi isha'I ,yana shigo parlor wayarsa tayi ringing yana dubawa yaga dr ibrahim daga wa yayi kafin yayi kasa da murya yace "bad ai basu gama din ba?dr ibrahim ya fizgan da iska yace ina fa basu gama ba waye daman haka hidiman aure yake malik?malik yayi murmushi yace sai kayi hakuri ai ance idan aski yazo gaban goshi yafi zafi,just keep patience remaining just few days komai yawuce in sha Allah yeah,dr ibrahim yace in sha Allah amma wai daman haka kaji kaima?malik yashafa kai kafin yasa key din hannunsa ya dan sosa girar sa yace haka ma kowa yaji ibrahim amma kasan ko da hidiman sa, dr ibrahim yace hakane amma gaskia yau bazan iya fita kallon wasa ba,malik yace likewise ni gaji yau mun sha aiki oga ma yace idan muka dawo nasarawa Akwai maganan dazamuyi dashi dr ibrahim yace tau Allah yasa muji alkhairi abokina malik yace Ameen, ahankali ta bude kofan bedroom din tafito hannunta rike da books din islamiyanta ,yadinga binta da kallo kafin ya zauna itama ta nemi wuri ta zauna can nesa dashi babu wanda yace komai batayi magana ba shima baice komai ba can tayi kasa da murya kafin tace "ga shi nan din inda bangane bane "malik ya karbi book din yakalli inda bata gane ba, yace tau karanta naji book din takarba tana karantawa ya dinga binta da kallo yayi mamakin jin lokaci daya har ta iya rike karatun, inda bata gane din bane yasake maimaita mata lokaci kadan ta rike ta karanta masa tsab,har sai datagama kafin yace masha Allah, tashi tayi har takai wurin kofan bedroom din kafin ta juyu kuma ahankali ta koma ta zauna ta saukan da kanta kasa tace " dazu ne auntie tazo tace mun wai nashirya zamu je wurin suna gobe kuma wai na tambayi ka "malik yayi shiru yana ta kallonta kafin can yace wacece kuma auntie? Aydarh tayi shiru kafin ahankali tace dr hafsa,malik yace itace tace ki tambayi ni cike da yarinta aydarh ta gyada masa kai yace su idan zaku sunan kin san sune ko miye?ta girgiza kai kafin yace idan ta zo kice nace aaa bazaki je ba,aydarh tayi shiru kafin ta daga kai tana kallonsa tace itace fa tace zamuje "malik yace nikuma nace bazaki je am I cleared? Aydarh batace masa komai ta koma bedroom dinta ta zauna tacigaba da juya maganan kamar hadda miyasa ma ta tambaye shi ai da bata tambaye shi ba amma ai ita auntie tace na tambaye sa to yanzu idan tazo yazata ce mata,wata zuciya tace ki gaya masa yarda yace din. Kamar yarda sukayi jiya yau din ma haka har sukaje islamiyan

kafin yace a maida hankali, tana shiga aka fara karatu kaman jiya yarda lokacin break ajin kamar kasuwa yau dai su maman baffa sun samu dama aydarh na zaune tana duba littafinta maman noor tayi mata sallama ahankali ta amsa masu sai da suka hada ido jin yarda aydarh ke magana hausan ma kaman foreign take mai mugun dadi Maman baffa ta washe baki tace ina kwana ya gida ya yara,aydarh tace Alhamdulilah maman noor tace anya dai yara saidai ki tambayi mai gida amma da ganinta amarya ce, maman baffa tace haka fa,zaman sukayi kafin maman baffa tace amma anan anguwarku kuke ne?aydarh tace ah’ah maman noor tace Allah sarki ya sunanki ?aydarh tace ASEYARH maman baffa tace masha Allah auntie asiya nidai sunana farida yara na biyar amma anfi kirana da maman baffa a nan anguwar nake,aydarh tace Allah sarki still bata dauke nikkab din taba,maman noor tace sunana hadiza yarana biyu a malaysia muke nida mijina kafin mu dawo nan kano maman noor ake cemun,Aydarh tace Allah sarki labari suka dinga janta dashi duk bata amsa su,sai kadan kadan wasu daga cikin yan ajin suka taho inda su aydarh suke cike da girmamawa, cike da isa na yarda suke bata girma kanta na girma tace masu lafiya wata tace anty hadiza dan Allah wai turare muke so waccan ya kare nawa dayar ma tace haka maman noor tace tau badamuwa amma gaskia sai zuwa jibi saboda inda abun yi yau da gobe,suka ce tau Allah yakaimu lapia nan fa maman noor ta tsinke tacigaba basu labarin malaysia wanda babu ranar dabazata zaunar dasu tabasu labarin nan ba, bakaramin ganin girmanta sukeyi ba ganin duk tafisu wayewa daga ita sai maman baffa ,dayawan labarin karyane aydarh najinta yawwanci abunda tafada duk karyane kan labarin malaysia,ita kau duk dan ta birge aydarh takeyi duk dan itama tadawo wajanta, ringing bell akayi lokacin komawa break yayi kowa ya koma wajan zaman sa aka cigaba da karatu,yau ma kamar jiya tun kafin twelve yazo daukanta, suna fitowa already ya tsayar da keke suka shiga suka wuce gida, ko gidan bai shiga ba mai keken ya wuce dashi wajan aiki.

Dr hafsa tace babu komai karki damu tunda bai bari ba shikenan wani lokaci idan yabari sai mu fita din aydarh tayi shiru bata ce komai ba amma sai taji duk bata ji dadi ba,dr hafsat ace karki damu fa aydarh babu komai kinji sai nadawo in sha Allah aydarh tace Allah ya tsare,dr hafsat ace Amin thank you aydarh kafin tawuce, tafita kofan ta rufe ta shiga kitchen jallof din pasta tayi masu already yayi cefane hadda cat fish tsab ta yi girkin kafin tayi slicing fruits a plate tashiga tayi wanka ta karasa gyara kitchen din,kadan kadan take jin ciwon maran datake tun dazu na kara karuwa,daurewa take amma ina ta kasa bedroom ta koma ta kwanta a dadafe, yana shigowa toilet yafara shiga yayi wanka jallabiyan sa daya

wanke yazagaya ya dauko yasaka kafin yashiga kitchen yadinga bin abincin da kallo,yarinya nan komai nata nadaban ne abinci yayi dadin da shi kansa ya manta when last daya ci abinci mai dadi irin wannan ummi yatuno, dasu aysha sai yaji hawaye ya taru a idonsa dasauri yasa hannu ya goge he surely missed them words cannot express how he missed them, bayan yagama cin abinci yasha fruits din sosai yadawo parlor ya kwanta tun daya dawo bai ganta ba shiyasa yatashi ahankali ya mike yashiga bedroom din ya tarar da ita kasan carpet zufa yarda take juye juye kawai ya tabattar masa da she is sick hankalinsa tashe yakarasa kusa ita dasauri ya dago ta ya daura ta a jikinsa yace ASSEIYARH kimun magana what's wrong with you tell me mike damunki dakyar ta iya nuna masa maranta dake masifafan ciwo kamar zata rasu gently yasa hannu.

Gently yayi placing hannunshi kan maran wani irin ajiyan zuciya ta sauke,kafin tawani irin rike shi sosai kaman zata shiga jikin shi tsabar azaban datake ji, malik din ma yarasa abunda zaiyi bakaramin daga masa hankali tayi bad uk abunda take sam batasani ba, zufa keta keto ma duk iya kokarin sa na yagane abunda ke damunta yakasa addua kawai ya keta faman tofa mata kafin tayi wani irin yankuri sai data wanke masu jiki kaf da amai zuwa yanzu hankalin malik yakarasa tashi amai take kwara wa kamar zata fito da kayan cikinta, duk ya kara rungumeta a jiki du kaman datake a jikinshi takeyi ,sai da tayi kusan 10mins tana abu daya kafin ya lafa wani irin kuka take naban tausai da kaganta kasan she is in pain duk tabata musu jiki yasa shi tashi ahankali dauke da ita hannu kamar yar baby sam bayajin nauyinta idan ya dauketa kamar paper toilet yashiga da ita kafin ya zaunar da ita nan kan kujeran dake a toilet din bazata iya yin komai ba dan she is in serious pain, hannunsa yakai gaban zip din bubu gown din jikinta wace duk tabata da amai, kafin gently yaja zip din kasa yabude white soft boobs dinta dake cikin black lace foam bra suka bayana, dawani irin speed malik ya dauke idonshi yah rabbil alameen ya furta ahankali yasa hannu yakama shoulder dinta jikinta very warm and soft, yafara cire rigan gently kamar mai tsoron cire mata din har sai daya zo wajan wrist kafin yasa tsaya ganin yarda take wani rufe ido kaman zata suma yasa shi karasa cire mata gown din yasaka gown din a bucket kafin yadawo cikin dakin ya dauki flask din ruwan zafi ya koma karamin towel din datake tsane gashin yadauka ya goge mata jikin tass kafin ya cire nashi rigan shima yasaka a bucket yarda yashiga da ita rike ahaka yadawo da ita daga ita sai bra da undie still inner cap din kanta na akan wasu kayan ya chanza kafin yadawo ya bude duvet din daya rufe ta,ganin yarda take shaking,kafin ahankali dakyar ta iya bude bakinta tace "abdominal pain "jin haka yasa shi tuna farkon haduwar su da

kalan drugs din daya siya mata dasauri yamike ya fita,pharmacy din nan bayan gidansu yashiga yasiya allura da magani sai sanitary babba kwara daya,yarda yabata haka yadawo ya iske ta alluran yahada idonta na a rufe kafin gently yayi bismillah yayi mata dan ya mutsa fuska tayi kafin tasake maida idonta ta rufe gyara mata kwanciyan ta yayi yacigaba da tofa mata addua kusan 5mins kafin yaji numfashin ta na sauka ahankali alaman bacci ya dauke ta sauke ajiyan zuciya yayi kafin yatashi ya shiga toilet din ya wanke rigan ta dana shi ,kafin ya wanke toilet din fess,yafito ya dinga bin ta dakallo yarda ta cure jikinta waje daya,fita yayi parlor kafin yashiga kitchen ya daura ruwan zafi a tukunya yafita oat yasiyo sai madara da sugar,lokacin daya shigo ruwan sun tafasa ya juyu su a flask kafin yafito yakoma dakin Still bacci take daman yasan zatayi baccin carpet din yagoge da detergent kafin yakoma kitchen din yasake daura wasu ruwan masu yawa a tukunya sai dasuka tafasa kafin ya juye a flask yadawo parlor ya zauna. Ahankali take bude idonta sunyi mata nauyi ,ya dinga bin ta da kallo ko kiftawa babu ahankali tafara kokarin mikewa zaune kafin tabi jikinta da kallo babu riga jikinta sai bra da undie wani irin fadi gabanta yayi,yana lura da ita so take ta tashi yasa shi mikewa tsaye yafita daga dakin, har sai da ya rufe kofan kafin tasamu ta tashi walking slowly ta dauki flask din wanka tayi kafin ta wanke pant dinta da undie dasukayi stain kadan ta daura towel wani pant din ta dauka da pad tashiga toilet din sai data shirya kafin ta fito wardrobe tabude ta dauki rigan atampha ta tasaka, ta koma ta zauna kan katifan looking so pale and weak,ga tunanin yarda yacire mata riga daya kasa barin ranta tunda ta farka taganta a haka,bude kofan dakin akayi yashigo tayi saurin sukunyan da kanta kasa, kwalla har ya cika mata ido,fita yayi yakoma kitchen ya hada mata oat,yadawo dakin ahankali yazauna kasan carpet kusa da kafanta kafin yace “take “gently tayi raising head dinta takasa hada ido dashi tasa hannu ta karbi cup din oat din dayake mika mata, hannu ta dinga rike cup din kanta a kasa shima zama yayi nan kan carpet bai sake ce mata komai ba,kusan 3mins yaga bata da niyyar sha kafin yakalleta yace “take it sai ki sha magani “kamar mai jiran umarnin sa haka ta mutsa spoon din dake cikin cup din kafin tasa spoon din ta debo oat din tafara sha ahankali sam bakin ta babu dadi amma ahaka ta daure tasha kusan cup daya ,bai tashi ba har sai datagama shan din kafin yawuce kitchen ya dauko mata ruwa yadawo drugs dinta yabude ya balla mata duk 2din kafin yace take this ta dinga bin maganin da kallo kamar yaune na farko data fara ganin magani,hannu ta miko gently ta karba kafin ta karbi ruwan sai data rufe ido da karfi kafin ta hadiye maganin, kafin ya kalleta yace how are you feeling now?tayi kasa da kai ahankali tace “better “yamike yace sorry yasa kai yafice daga dakin.

Wajan nine yasake shigowa dakin yanzu ba bacci take ba ta farka,kallo daya tayi masa ta dauke kai shikuma kallon yake ko kiftawa babu ciwon datayi na wunin yasata fadawa sai wani milk glow da skin dinta tasake yi calaban kanta ya tsufa still da kyaun sa, sallama yayi ta amsa kafin yace yah jikin? “Tace dasauki “kitchen yashiga ya dauko mata abinci a plate sai apple daya siyo mata yanzu yayi slicing ya daura a plate yadawo ya ajiye mata kafin ya juya ya koma parlor kadan tace Abinci sai apple din data sha,ba laifi tasha dayawa har yanzu jikinta bai dawo nata ba , kwashe plates din tayi tafita zata kai su kitchen bai parlor sai kofan dake bude iska nata daga curtains din parlor kitchen din tashiga ta ajiye plates din kafin sama sama ta dinga jin maganar malik din duk da ba da karfi yake maganan ba amma yanayin voice dinsa irin na boss din nan ke shiga har brain din mutun, tayi shiru har zata koma bedroom sai ta dinga jin maganan wata can kasa kasa,kamar wace magnet ke ja ko kuma wani yace tafito haka ta sa kai ta lika kadan,Ramlah tagani tsaye sai malik dake tsaye ya zuba hannunsa a pocket din jeans dinsa fuskan nan babu yabo babu fallasa ,yarda take wani fari da ido yasa aydarh dauke kai daga duban datayi mata,bata yi magana ba dan shi bai ma lura da ta fito ba,Ramlah kau sarai ta ganta shiyasa tawani kara gyara tsayuwa tana turo kirji kaman allon sha,slippers dinsa dake nan bakin kofan black ta saka akafanta sunyi mata yawa sai sukayi ma kafan wani extraordinarie kyau ahankali tasa kafan ta sauka daga kan step daya dake nan wajan kofan kafin ka sauko ventilation dinsu wani wawan kallo tabi Ramlah dashi kamar taga abun kyama,hannu tasa ta kamo damtsan malik din,kamar daga sama yaji soft tafin hannunta dake warm gashi soft kamar pure cotton tunda ga kafan shi har brain dinsa yaji wani irin abu ya tsarga sa wallahi bakaramin kokari yayi ba wajan controlling kansa,Ramlah kau kamar zata mutu batasan miyasa take bala’In shakkar aydarh ba, malik ya juyu yana kallonta kamar yarda take kallonsa ido cikin ido yarda ta hade rai fuskanta babu alamun wasa bakaramin tafiya da imaninsa tayi ba duk yanda kafin idonsa yayi tasiri a kanta amma ta daure ,Still ta kama hannusa gam ta rike ko shoulder dinsa bata kai ba Wallahi kallonsu da Ramlah keyi ahaka bakaramin firgita ta yayi ba sunyi wani irin azaban kyau atare, aydarh tace “this should be the first and the last time da zaki sake kawo kafanki nan “get out! Shidai malik kaman wani sakarai haka yayi tsaye yakasa cewa komai Ramlah kau haukacewa ne kawai ke batayi ba amma yarda aydarh tayi mata magana bakaramin sosa mata zuciya yayi ba,cike da raini izza wulakanci tayi mata maganar, bata jira ganin tafiyan Ramlah ba tasa hannu taja sa suka shiga Parlor ta maido kofan ta rufe da mugun karfi kafin ta murza key ko kallonsa batayi ba ta juya tayi hanyar bedroom yarda take tafiya kamar wata princess yanda wrist dinta ke kadawa kamar da gayya

take tana tafiya kaman bata son taka tiles da carpet din dakin ta shige bedroom,nan tabarshi tsaye bude da baki kamar wani status haka ya tsaya, tana shiga bedroom din ta zauna kan katifan ta rike kanta she didn't know why she didn't know the reason but she hates Ramlah to the essence that words can express, kusan 5mins yana tsaye kafin walking majestically yabi bayanta zuwa bedroom din kan katifan yasame ta zaune ta rufe ido yadinga binta da kallo yarda numfashin ta ke fita ahankali ahankali ta jinginan da kanta jikin pillow, tana jin alama da motsin shigowan shi amma tak'I bude ido can yayi gyara murya kafin yace "hey" nan ma bata bude ido ba ganin abunda tayi din sai ransa yabace cikin dan daga murya yace open your eyes and sit "yarda yayi maganan in a serious tone yasata bude ido kafin ta tashi ta zauna gently, bai zauna ba ya mayarda hannunshi cikin aljihu,kusan 2mins babu wanda yayi magana "kafin yace "what's your problem with her? Kamar irin tana jiransa ko kuma wace ke jiran tambayar ta mike tsaye cike da tsiwa kafin tayi nesa da shi,tace "you just ask what's my problem with her are you asking or you are trying to explain my problem with her sir? Malik yadinga kallonta ko kiftawa babu hannunta ta daga kafin ta nuna direction din kofa tace go and ask her what's her problem with me first kafin ni kazo ka tambayeni,I passed this to you time without number sir,nace kace tafita harkana ,malik dai dayaki dauke ido kanta yama rasa abunda zai ce mata wallahi, can ganin tayi shiru Still kuma tana a tsaye kaman yarda shima yake a tsaye,yayi kasa da murya yace "kin riga kin bada amsan ai kince ta fita a harkanki naga ko datazo ai wajena tazo tau I see no reason dazaki yi mata wulakanci ba right? Aydarh ta juya kafin tasake juyuwa ta kallesa tace miyasa tazo wajanka din?kamar yana jiranta yace because she is my girl idan kuma kishi kike sai fada naji,wani irin smile tayi kafin tace kishi kishi miye hakan,I just hate the girl kuma I want her to stop going your way malik yayi shiru kafin yace if not?Aydarh tace said ai ka zaba ko ni ko ita din,malik yayi shiru ya dinga kallonta kaman yarda take kallonsa kafin ta janye idonta tayi kasa da kai juyawa yayi yafita daga dakin,komawa tayi ta zauna kan katifa tarasa dalilin dayasa tayi wani mugun tsanar Ramlah,bata so tanayi masa magana, wata zuciya tace ina ruwanki idan tana masa magana tunda ke ai batayi maki? Girgiza kai tayi kafin tace he is your brother and your husband as well,Husband no idan mijin naki ne miya hada ki dashi baki son sa shim abaya sonki miye zai dameki dashi, zama tayi kan katifan kafin ta kwanta,ahaka ahaka har bacci yayi gaba da ita. Da tunanin abun ya kwana a rai yarasa yarda zai juya lamarin, sai day agama duk wani aikin gida irish yake so ya koya mata yanda ake frying amma bai son yi mata magana ganin kaman tana fushi dashi this is the first a rayuwarsa dayaji yayi mahaukacin damuwa dawani

bayan su abby ummi aysha halime da kuma maryam duk duniya bayan su babu wanda yake ji aransa amma yau sai gashi tunaninta yahana shi sakat what does that mean?ko dan tana yar uwarsa shiyasa ko dan tana amana a wurinsa shiyasa?ko daraja girma da martaban ummi kesa sa jinta a ranshi? Ko dan darajar igiyoyin auransa dake kanta, iya zaman su ya fahimce abubuwa dayawa game da ita, saurin kuka,kunya,shagwaba,yarinta, tsoro ga saurin daukar duk wani abu da aka koya mata, maganan tsabta da neatness kamun kanta nutsuwanta is killing him, yarda take magana kawai ya isa kasan how calm she is ga bata son raini rashin son mutane kuma asali yasamu daga home training amma hakan ba halinta bane, sometimes idan yana tuno drama dinta har dariya abun ke basa,wata zuciya tace malik be a man duk yarda kake da rauni kanta try and control your self teach her how you wanted her to be,da wannan yatashi yayi hanyar bedroom din har tayi wanka dakin sai kamshin ta yakeyi ta gyara katifan koi na tass sallama yayi ta amsa kafin straightly yace muje sauri nake yau Monday bata ce komai ba kanta akasa ta bi bayansa har kitchen,bai sha wahala ba ya koya mata kafin yazuba wanda yayi frying a plate yaci yasha sauran oat din jiya kadan kafin yace na fita,shiru tayi har yafita kafin takarasa frying irish din ta kwashe tass ta wanke abunda suka bata kafin ta gyara kitchen din sai da tayi sweeping da mopping bedroom din kafin tadawo parlor tayi Breakfast, ta dauko books dinta tana dubawa,anan parlor bacci yayi gaba data ita ga books din nan kusa da ita.

Kofan bude take bata saka key ba sallama yayi yashigo nan ya ganta kwance parlor, kallonta yake kaman irin yau yafara ganin ta da alama ta jima tana bacci anan din books din ya kwashe ya mayar cikin bag din kafin ya kai bag din bedroom ya fito ahankali ya matsa kusa da ita kafin yakai hannunta gently saman cheeks dinta bude ido tayi suka hada ido kafin ahankali ta tashi zaune yace yamma yayi babu kyau baccin yamma,mikewa tayi tsaye tawuce bedroom shima wanka yayi kafin yashiga kitchen din yabude tukunya first yaga babu alaman tayi girki sai kuma ya bude warmer din irish din ne tun nasafe har yanzu a warmer din that’s means bata mayi girki ba kenan bata ci abinci ba kenan? Girgiza kai yayi yana mamakin halinta na rashin son abinci tun safe daya fita yau wuni sukayi yawo shida dr ibrahim don ganin sun hada komai na tafiyan su gobe shiyasa bai dawo darana ba ganin akwai cefane yayi tunani zatayi girki, yunwa yakeji yasa shi daukan sauran irish din yadawo parlor yaci kafin yakoma kitchen din flask yaduba yaga akwai ruwan zafi a cup ya zuba yasaka mata sauran madara da sugar din daya rage ya dama mata oat,sallama yayi ta amsa masa har tayi wanka tana zaune,ya ajiye cup din oat din kafin yayi kasa da murya yace “you are

fat and u are not use to food “ aydarh ta ware ido kafin tawani Hade rai tace nidai am not fat Allah,malik yace is a lie baki ga yarda kike bane hala baki kallon Mirror? Aydarh ta juyan dakai murya can kasa tace saidai kaine kato bani ba Allah, malik yace waye katon?bata dauka zai ji ba amma dayake snake ears garesa sai daya jita, tace kai manah,yahade rai yace naga ya maki yarda kike ko na barki,dasauri ta gyara zamanta tace erh fada ina ji, malik ya matso kusa da ita yace your tummy is flat and sai kuma yayi shiru ,tace and what tafada kamar zatayi kuka,yace and the rest of your body is very nan ma yayi shiru ,this time har wani kwallan shagwaba yafara taruwa a idonta tace very whatttttt? Shiru yayi Still idonshi na kanta, ko daukewa babu kafin ahankali yace nothing”tahade rai kafin ta juyan da kanta gefe malik yamike ahankali yace ki sha oat din bara nayi girki har yakai kofan tace “sir” sunan datakira shi dashi sai yaji duk wani kala tun jiya yaji takira sa haka sai bai maida hankali kansunan ba sai yanzu datasake kira,juyuwa yayi baice komai basai kuma ta mike tsaye hannunta rike da cup din oat din daya kawo mata kafin tayi kasa da kai tace nima zanyi girkin murmushi yayi he loves how she behaves childish yanzu miye abun jan maganan daga tace zatayi joining dinsa suyi girki bai ce komai ba yafita tabisa da kallo, kafin ta bi bayan sa danwaken flour yake tana tsaye a kitchen din tana kallonsa Still hannunta rike da cup din oat din ta duk abunda yakeyi tana kallonsa tsaf yarda yake jefa dan waken yake burgeta,cup din ajiye kafin tace nima zanyi murmushi yayi kafin yace zaki iya yi? Ta gyada masa kai yace alright sit yanuna mata dayan karamin kujeran dake nan kitchen din kusa da shi hannunta ta wanke kamar yarda tagani yanayi kafin tafara diban kwabin tanayi exactly yarda yakeyi cikin few minutes suk agama jefawa, kafin malik yace yanzu bari zamu sai ya juya sau uku kafin.

Saboda tun dasafe zasu tafi yasa ya siyo mata duk wani abunda zatayi amfani dashi yasan ba lalle ta dinga girki ba ko cin abinci, yasa shi siyo mata chocolates sai cornflakes hadda cabin ma sai madara da sugar yayo cefane kafin ya dauki 5k ya ajiye cikin kayanta, ta dinga kallonsa har ya zuge zip din bag din kafin yace tunda asuba zamu fita shiyasa batace komai ba dai ta dinga kallonsa har ya tashi zai fita sai kuma ya dawo ya zauna yana kallonta yace ko zaki je ki zauna dasu inna ne? Ta girgiza kai kafin murya can ciki tace ah’ah yayi shiru sai kuma yace ko nayi ma dr hafsa magana sai tazo ku dinga kwana tunda inna bata nan tayi tafiya?aydarh ta gyada kai ahankali kafin tace erh “yace tau sa hijab dink isai muje gidan inna yanzu nayiwa dr hafsa din magana yanzu,ta mike tsaye kafin ta bude

wardrobe ta fito da well iron hijab dinta har kasa kafin yayi gaba ta bisa abaya, sai da yarufe kofan part din kafin su fita, kasancewan dare kusan past 9 gidan tsit sai hasken globs tarr ko ina anan zaure suka hadu da Ramlah da,dawowan take nan, ta dinga bin malik da kallo shikam ko lura da ita ma baiyi ba aydarh kam tagan ta amma tayi kaman bata ganta ba wani irin shegen harara Ramlah tabi bayan aydarh dashi kafin tayi kwafa tawuce cikin gida.Dr hafsa tayi murmushi tace Allah sarki babu komai yallabai Allah yadawo daku lafiya, malik yace Ameen dr hafsa tayi murmushi tace ai nayi tunanin ma atare zaku tafi malik ya girgiza kai yace no akwai nisa kwara ta zauna tunda kwana hudu ne kawai zamuyi,dr hafsa tace Allah sarki " malik yamike yace tau dr mungode sosai Allah yasaka sai da safe aydarh ma tamike tace thanks auntie " dr hafsa tayi murmushi tace don't mention aydarh Allah yadawo dasu lafiya sallama sukayi ma dr hafsa,suna fitowa nan kofan gida malik ya kalli wurin daake siyan da nama ga fruits a gefe yakalleta kafin yace tsaya ni anan ina zuwa,ta gyada masa kai kafin ya juya ya tafi wajan masu siyan da fruits din sai daya siya kafin ya siyan musu balango mai kyau , few minutes yayi yadawo ya tarar da ita tazauna kan dakallin dake wajan tana kallon yarda abun hawa ke wucewa, yace "muje"tashi tayi tabisa gida suka shiga har yanzu Ramlah na tsakar gida tana jiran dawowan su duk kansu babu wanda ya kalli inda take sai ita da ta dinga binsu da kallo kamar idonta zai fado waje har suka shige kafin ta dauke idonta ta mike tashige dakinsu. Ya wanke fruits din kafin ya yanka ya jera a plate naman ma a plate yajuye sa ya zuba mata nata shima ya dauki nashi bedroom yakai mata har tayi shirin bacci zaman yayi ya ajiye mata kafin yace, zaki iya zuwa dakanki can din?bata gane abunda yake nufi fa shiyasa tace ina? Yace can islamiyan kafin ta gyada kai tace erh "sai kuma tace bak ace ranan sat zaku dawo ba kuma? Yace ehhh amma maybe aie sai dare,aydarh tayi shiru bata ce komai ba tashi yayi yafita kafin ta sauko kan carpet tafara shan fruits din kafin taci naman kusan yanka 6 kafin ta shiga toilet ta wanke hannunta ta fita da plates din kitchen,shima naman yake ci yabita da kallo har ta fito kafin ya dauke ido.wajan five daidai yagama wankan shi da komai a gida yayi sallan asuba kafin yashiga bedroom din ahankali without making any sound yayi tunanin bacci take sai yaganta zaune sanye da hijab kan katifa kallonta yayi itama shi take kallo kafin murya can ciki tace Good morning yace morning are you alright? Tace yes yace tau miya hanaki bacci ta girgiza kai tace "babu" bude wardrobe din yayi yafito da bag dinsa, kafin yakalleta yace mun tafi, Ta mike tsaye ta bias har bakin kofa batace masa komai ba shima haka baiyi mata magana ba har sai daya kai wajan kofa kafin ya daga mata hannu yace till we came back,hannu tadaga masa tace Allah yatsare yace Ameen bai tafi ba har sai

data koma cikin gida ta rufe kofan part din kafin yawuce yana fito yaga dr ibrahim zaune da uban kaya cikin keke daman shi suke jira “dr ibrahim yayi kasa da murya yace hala dakyar ka iya rabuwa da ita malik yayi shiru bai ce komai ba, dr ibrahim yace hala kewan ne yasaka ciwon rashin magana ko hala ka kurumce ma?sai sannan malik yace ko dai na koma tunda naga kamar baka shirya tafiyan yanzu ba,dr ibrahim yayi shiru bai ce masa komai ba ,ya kalli mai keken kafin yace muje kafin wannan ya koma gida tunda naga bai so yataho yabar matar ba , motor park sukaje basu wani jima sosai ba, moton ta cika suka tashi ,har sai dasuka dauki hanya kafin dr ibrahim ya dauki wayarsa ake ta kira hibba ce matar dazai auran waya su ka dinga yi kamar irin bayana kan hanya zasu inda take din,shidai malik yayi shiru yarasa miyasa yakasa cire tunaninta a ranshi duk wani mins Ko seconds sai ya dinga tuna nata abun kamar magic ma duk iya kkr wajan ganin yadaina kasawa yayi, gari yayi haske sai datagyara koi na kafin tayi breakfast hadda dr hafsa ta hada da niyyar idan tazo sai su ci tare kawai.

Dr hafsa tace kunyi waya ba? Aydarh ta girgiza kai kafin dr hafsa tayi shiru tana kallon aydarh can tace yanzu fa nasan sun isa kuma kice bakuyi waya ba , aydarh tace ai babu waya a hannuna yanzu, dr hafsa tace tau ko na kira sa ai inada numbersa, Aydarh ta girgiza kai tace ah’ah dr hafsa tayi shiru bata sake cewa komai ba kafin ta mike tace clinic babu kowa dr saratu ce kawai tunda dr ibrahim bayanan anjima idan nadawo zan shigo wajan isha’I Aydarh tace to sai kindawo, dr hafsa tace ngd” breakfast din yayi dadi aydarh tayi wani cute smile ,har bakin kofa taraka ta, kafin tadawo kitchen ta koma taciga da wanke abubuwan data bata kafin tafito ta wuce bedroom din hakanan take jin gida duk ba dadi duk da daman tasaba zama ita kadai amma yau duk sai taji shiru, toilet din bedroom ta shiga ta wanke duk da babu wani dirty dayayi kafin ta wanke inners dinta tayi wanka, batasan lokaci yaja haka ba kiran sallarh kawai taji, kafin tadawo nan parlor hannunta rike da jikkan islamiyan ta tacigaba da bude books dinta tana dubawa Sosai karatun ya zauna akanta kusan 2hrs tabata ahaka, tun breakfast din dasukayi dasafe shine a cikinta duk da kadan taji bawani dayawa amma har yanzu batajin yunwa,tunuwa da abunda yace tayi sai kuma tayi murmushi kadan kwashe books din tayi ta wuce bedroom wardrobe din ta bude kafin ta dinga bin chocolates din da kallo kwara daya ta dauka sai biscuit fab! Shima daya tadawo parlor ta ajiye su kan carpet kafin ta shiga kitchen apple daya ta dauka cikin basket din dayake zuba su,wanke shi tayi kafin ta daura knife kan plate tareda apple din tadawo parlor,chocolate din tabare tafara ci ahankali kamar bata son taunawa, tass ta cinye leda daya kafin tafara slicing apple din tana sha kusan 40mins ta

bata wajan shan apple da cin biscuit da chocolate daya, kafin ta dauke ledan da plate din ta mayar kitchen hulan kanta tasake gyarawa kafin tasaka slippers dinsa wanda ke nan bakin kofa ta dauki tsintsiya tafito nan ventilation dinsu tafara sharewa kaman yarda yakeyi, Ramlah ta hango ta da ragan building dinsu daya zagaye part din nasu, tayi tunanin a tare suke da malik din shiyasa tak'I dauke idonta daga kallon wajan ahankali take sharan har ta share wajan tass kasancewan babu dust tiles din saboda asthma, tana gamawa time din la'asar tayi ta koma bedroom ta fito da kayanta zata cire su daga cikin jikka ta mayarda su a wardrobe, tana fitowa dasu sai ga kudi tagani ta dinga juya kudin tarasa ta inda suka shigo ,can ta tuno maybe ko shi yasaka ta tabe baki ta mayarda su cikin bag din ta ajiye,kitchen din tashiga girki take son yi ko dan saboda da dr hafsa, cefane tafara gyarawa cikin nutsuwa take komai har tagama jallof din macaroni wanda ta juye sauran balangon jiya dasuka siyo wanda yazuba a tukunya kasancewan akwai sanyi babu abunda yayi yanka vegetables din a hadaddan shapes tasaka spices bakaramin kyau macaroni yayi ba lokacin datagama har an kira isha'I , sharp sharp ta karasa kafin ta kwaso fruits din dake nan cikin basket apple sai watermelon orange da banana ba dayawa ba,ta yanka su kanana kaman yarda ya koya mata fruits salad sugar ta zuba kadan kafin ta mayar ta rufe ranan hadda ice block suka saka yau kam batasan inda zata samun block ba tunda baya nan, kawai ta dauki tin daya na madara dayasiyo mata ta daya murufin ta juyesa tass a cikin saida tagama tass kafin tayi murmushi,bakaramin dadi take jib a yarda take girkin yanzu, saida tagama komai kafin ta shiga bedroom tayi wanka tafito vaseline kawai tashafa sai perfume tasaka riga ta chanza inner cap baby pink duk da babu komai a fuskan ta Allahumma bareek tayi kyau sosai masha Allah " dakin da gidan baki daya ma yakama scent din jikinta kamshin mai sirin dadi, knocking kofan akeyi,walking slowly ta isa bakin kofan kafin tace "waye? daga can dr hafsa tace nice budewa tayi dr hafsa tsaye sanye da doguwan hijab sai handbag dinta a hannu, aydarh tayi murmushi tace welcome auntie ki shigo nan parlor suka zauna dr hafsa tace kingani sai yanzu ko?Aydarh ta gyada kai dr hafsat ace aikin ne yayi manah yawa yau shiyasa,Aydarh tace eyyerh sorry kafin ta mike tashiga kitchen din tafito da warmer sai plate da spoon da serving spoon ta ajiye kafin ta sake komawa tafito da container data zuba fruit salad din sai cup biyu da spoon biyu tasake komawa ta daura pure water biyu a plate ta ajiye gaban dr hafsa,dr hafsa ta dinga kallon kayan abinci kafin ta kalli aydarh tasauke ajiyan zuciya tace sannu aydarh,Aydarh ta gyada kai dr hafsa tace duk da mai gidan baya nan sai dakikayi wahalan girki? Aydarh batace komai bad ai kanta nakasa ta cigaba da serving dr hafsa, sai data cika mata cup da fruit salad din kafin itama ta

saka half cup,daidai da yanayin cin abinci ta abun sha’awa ne dr hafsa ta fada a ranta , can dr hafsa takalleta tace ke bazaki cin abincin ba naga fruit salad kawai kika sha,aydarh tayi murmushi kafin tace zan ci “ dr hafsa tace tau shknn “ tass ta cinye abinci da fruit din tasha ruwa kafin ta kalli aydarh tace yayi dadi sosai “aydarh batace komai ba amma har cikin ranta taji dadi yabon da dr hafsa din tayi ma abinci, bata karasa shanye fruit salad din ba ta ajiye cup din ta dauke plate ta zuba macaroni kadan dr hafsa dai na binta da ido ganin dan abincin data zuba, duk tana lura da ita almost 15mins yadauke ta cin abincin time din dr hafsa har ta manta ma data ci hankalinta na kan waya tana kallo a ig, can dr hafsa ta dinga kallon hoton tana kallon aydarh har wani zooming take tana kara haske kusan five minutes tana haka, aydarh sam bata lura da abunda takeyi ba saboda hankalinta na kan abinci datake ci ahankali ahankali,can dr hafsa ta kira sunanta ido ta dago dr hafsa tace Wallahi ke ce anan aydarh,aydarh tawara ido kafin tace a ina auntie? Dr hafsa ta mikawa aydarh wayar ko karba batayi gabanta yayi wani irin faduwa tasan ita din ce da kanta kuma a Cyprus wurin wani hadaddan beach take tsaye,tasha wata mad turkey abaya tayi rolling veil din gawani hadaddan Expensive dark shade a idonta zaune tsaye take ta hada rai abba ma ne ya dauke ta photo tayi wani irin kyau marar misali kaman wata jewel, ta dai san bata posting a Instagram page dinta ma private ne, likewise oum bata posting pics dinta abba ma haka daga kai tayi taga sunan mai page din taga an rubuta “salmerh malami” daman tasan salman ce kawai ke posting din pictures dinta a ig duk , shiru tayi kafin ta dauke kai ta mikawa dr hafsa wayar, dr hafsa tace Wallahi ke ce Ko aydarh nayi kwana biyu ban shiga page dinta ba ,shiyasa ganin farko danayi muku sai narasa ina nasanki nan ma aydarh tayi shiru dr hafsa ta cigaba da kallon posts din duk da anyi kusan 6 months dayin post din, wasu a Cyprus wasu a umra wasu kuma tareda abba a nan gidansu adamawa, dr hafsa dai tsoron Allah yakamata batasan kaddarar data kawo su nan din ba daman zuciyanta yajima dabata su wasu ne a kasar nan dr hafsa takasa hakuri ta nuna ma Aydarh wani photon ta ita da oum sai abba a new York cikin wani hadaddan restaurant duk san sha black jacket kana ganin su kasan uwa da diya da baba ne,wani extraordinarie kyau da gayu da kudi kawai magana a photo, dr hafsa da tambayoyi dayawa suka isa a rai tace your parents? Aydarh ta gyada kai sai tasake zooming abba kafin tace wannan amma baban yallabai ne? Aydarh ta girgiza kai kanta kasa tace babana ne, dr hafsa tayi shiru tace amma babanki da babansa gidansu daya ko ? Aydarh ta gyada kai kafin tace erh, dr hafsa ta cigaba da kallon pictures din aydarh wani wuri hadda salmerh duk basu kama amma hakan bai hana tacewa aydarh is she your sister? aydarh tace no she is my only friend, dr hafsa tayi shiru bata sake cewa

komai ba ta cigaba da kallon pictures din aydarh ta mike tsaye ta kwashe plates din takai kitchen kafin ta jingina jikin kofan kitchen tasa hannunta duk biyun a bakinta tafashe dawani irin kuka,kuka take sosai har idonta sai dayayi ja fuskan ta ma haka,babu abunda take tunawa irin ranan da abba yayi chasing dinta out duk yarda abba ke sonta amma haka yayi mata haka kan abunda bata sani ba kuka take har tana buga kanta,jin shiru yayi yawa yasa dr hafsa tashi tanufi hanyar kitchen din har yanzu tunani aydarh da malik fal a ranta ,knocking kofan tayi dasauri aydarh ta goge idonta kafin ta matsa kusa da sink ta bude tap ta wanke fuskanta tass kafin tasa veil dinta ta goge ruwan fuskan ta tabude, murmushi tayi wanda iyakar sa kan lips dinta dr hafsa dai tayi shiru ta dinga binta da kallo batace mata komai ba amma kallo daya tayi mata tagane kuka tayi,girgiza kai dr hafsa tayi wani irin tausayinta taji ahankali ta kama hannunta suka zauna kan carpet kan aydarh nakasa kafin dr hafsa tace bansan su waye ku ba amma lokaci daya naji kun kwanta mun a rai tun kafin nasanki aydarh naji ina wani irin kaunanki duk da a rai nayi tunanin har na koma ga Allah bazan taba ganinki a fili ba domin sama tayiwa yaro nisa aydarh sai gashi yau gani gaki,dr hafsa tayi murmushi tace kinga ikon Allah ba? Still aydarh kanta nakasa batace komai ba saboda tasan datayi magana kuka zai biyo baya bata son kuma tayi kuka gaban dr hafsa din,dr hafsa tasake rike hannun aydarh tace kiyi hakuri aydarh ki mance da komai ki dubi rayuwar auranki kawai da mijinki har lokacin da komai zai wuce ku koma wajan familyn ku sai sannan aydarh taji wani irin kuka, dr hafsa tajawo ta jikin tana patting bayanta har kukan ya lafa.

Duk gajiyan dasukayi na mota basu zauna ba har sai dasuka gama da duk wani abu a ranan, garin fulani ne sosai can cikin lafiya, Sosai aka karama su,dr ibrahim kau yasha tsiya wajan malik shidai bai biye masa ba, saboda yau gashi ga hibba,bazata wuce shekarun aydarh ba,fara ce marar jiki mai kyau da ita masha Allah, sai da suka gaisa da malik tana tambayar sa ya aydarh ai tayi tunani tare zasu taho dr ibrahim yakalle su yayi kasa da murya yace kema dai kingani dakyar fa nasamu yabiyo ni fa yace garin yayi nisa bazai taho da ita bs kar ta wahala, kuma gashi yakasa barin tunaninta shidai malik bai ce masu komai ba saboda ya lura duk halinsu guda, tashi yayi yace dare yayi fa ka rabu da ita, tawuce ciki muma muje mu kwanta nagaji,dr ibrahim yakalli malik yace naga dai babu wanda ya tsayar da kai anan “malik yace au haka kace tau shknn kafin ya kalli hibba dake dariya kasa kasa yace Amarya sai dasafe hibba tayi murmushi tace tau yah Malik Allah ya huta gajiya idan kunyi waya kace mata bayi fushi malik yayi murmushi yashafa kansa kafin yace in sha Allah. Daki daya aka basu shida dr ibrahim kan katifan ya kwanta bayan ya dauro alwalla yasaka jallabiyan

sa ya kwanta, hakan nan yaji ransa na bashi kamar dr hafsa bata zo,duk da yasan kawai maybe tunaninta ne dayayi masa yawa amma sai yaji hankalinsa bai kwanta ba, wayar sa ya fiddo yashiga contacts yayi dialing number dr hafsa anan parlor ta kwanta bayan aydarh tayi tayi da ita su shiga bedroom tace bazata shiga ta kwanta a inda suke kwanciya da malik din ba sai dai tabata bedsheets da pillow ta kwanta anan kan carpet babu yarda aydarh ta iya haka ta dauko mata din, suna nan zaune parlor suna fira sama sama wayar dr hafsa din tafara ringing tana dubawa taga sunan yallabai murmushi tayi kafin ta turawa aydarh wayar tac eke ake nema “aydarh ta dinga bin wayar da kallo kafin tayi tayi accept, Assalam alaikum aydarh murya can kasa ta amsa ma yanajin itace yakoma yayi resting kanshi a pillow, bai sake cewa komai ba itama bata sake magana ba tayi shiru can yace hala baki iya gaisuwa ba?kaman yana gabanta ta wani bude ido kafin ta hade rai murya can cikin throat tace ina wuni “bai amsa ba sai cewa yayi have you eaten? Ta gyada masa kai kaman yana gabanta kafin ahankali tace yes “yace mi kika ci ,tayi shiru sai can tace fruit salad,yace only fruit salad? Yafada kaman irin tayi laifin nan,ta girgiza kai tace ah’ah fa naci abinci bai ce komai bayace sai dasafe ya kashe wayar ta dinga bin wayar da kallo kafin ta ajiye gefen dr hafsa da har tafara bacci, aydarh tamike tace auntie sai dasafe dr hafsa Allah yabamu alkhairi aydarh. Tunda dugu dugu dr hafsa tawuce bayan tashare parlor tayi mopping tass ko da aydarh ta tashi tagama gyara parlor,aydarh tayi mata sannu dr hafsa ta amsa ta,kafin tace bara taje ta gyara gida tayi shirin wucewa clinic,sharp sharp aydarh tagama dafa musu indomie kafin tayi frying egg dr hafsa tashigo yimata sallama zata wuce clinic “aydarh tace nagama breakfast ai bara na kawo kamar ko yaushe kadan taci dr hafsa tayi break dinta kafin ta wuce clinic din, sai da tagyara bedroom ta wanke two toilets din ta gyara kitchen ta wanke plates da warmer din dasuka bata already tana tashi tayi wanka kafin ta dauko books dinta tana dubawa.sai yamma dr hafsa tadawo aydarh na zaune parlor bayan tagama girki, bude mata kofan tayi kafin dr hafsa tayi murmushi tace mrs malik aydarh ta saukan da kanta kasa kafin tace sannu da dawowa dr hafsa tace yauwa y gida? Aydarh tace Alhamdulilah, abinci takawo mata suka ci tare dr hafsa tace aydarh baki son abinci ke kam aydarh ta girgiza kai tace ai nashs fruit,dr hafsa tace fruits ai ba abinci bane, aydarh dai tayi shiru kafin dr hafsa tace wata friend dina ta bude babban salon hadda su spa da lalle baki daya Aydarh tace masha Allah “dr hafsa tace kinga tunda su yallabai ranan Saturday zasu dawo sai muje ranan Friday ayi manah lalle,aydarh tayi shiru kafin tace lalle henna? Dr hafsa tace eh sai muje ayi manah kinga yallabai idan yadawo yaga kafan nan masha Allah yasha lalle ai bazai ganeki ba “aydarh tayi murmushi,dr hafsa

ta kalli wayar ta dake ringing kafin tace gashi mai gidan ne bara naje gida na dauko abu sai nadawo. Malik yayi shiru bayan ya amsa gaisuwan datayi masa,kafin yace ina dr hafsa din aydarh tace taje gida yanzu, yace wake yin girki,Kaman tana jiran tambayar tace ni fa “malik yayi murmushi yace dagaske ta gyada kai kaman yana gabanta tace erh.

Yace tau yau din mikaka girka? Tace fruits salad nayi sai nayi jallof din shape pasta (macaroni) ,yace inyee tau yayi dadi? Tace yayi fa auntie ma tace yayi dadi sosai yace wacece auntie? Tace auntie hafsa yayi murmushi yace kinyi kokari, littafin ki fa kin duba? Ta gyada kai tace erh naduba, Yace tau sai anjima “tace “to” kashe wayan yayi kafin ta ajiye wayan ta mike tsaye tadawo parlor tana jiran dawowan dr hafsa, knocking akayi aydarh tabude tasan dr hafsa ce shiyasa bata ma tsaya tambayar waye din ba, tana budewa taga inna tsaye tasha mayafi ga uban jikka ta rataya aydarh na ganin inna tayi murmushi kafin tace oyoyo inna “andawo lapia ya hanya? Inna tayi shiru bata amsa Aydarh ba kafin aydarh ta bata hanya tace shigo inna “anan parlor suka zauna kafin tace ina wuni sai sannan inna tace lahiya lau asiya, ya gidan? Aydarh tace Alhamdulilah inna dai tayi shiru ta tsuke baki ta zubawa waje daya ido aydarh ta mike tashiga kitchen ta kawo mata ruwa da abinci ta ajiye, inna ta kalli abincin kafin ta dauke ido,aydarh tace inna lapia? Inna tace duniya tazo karshe asiya aydarh tayi shiru tana kallon inna kafin inna tayi kasa da murya tace fisabillahi yanzu ita hafsa miye ruwanta dazuwa na wajan dangi na sabga? Aydarh tayi shiru bata ce komai ba kafin inna tace tau nida yanzu idan audu na nan ki shiga ki kira man shi nakai kararta wajan shi gaskiya,aydarh tace kiyi hakuri inna ita auntie mi tayi maki? Inna tace rashin mutunci da wulakanci sai wanda ta manta kawai ke batayi mun ba ,ina cikin fameli kawai ta kirani wai nataho ruwa zai mun banna, dayake ita kowa yayi shaidar bata kaunar Allah “ina dawowa gidan babu abunda yafaru “Aydarh tace gaskia ba dadi “ inna tayi kasa da murya tace shiyasa kingani bana shiga abunda yashafeta babu ruwana da ita “yanzu tashi ki shiga ki kira mun audu ya bige Mata wonin,babu ruwanta da rayuwata tunda nima bana shiga rayuwarta “Aydarh takalli “inna” tace ki yiakuri baya nan ma “inna tayi shiru kafin tace yana ina shi audun? Aydarh tace sun tafi auran Doctor ibraheem “ inna tace wanene haka kuma?aydarh tace wanda suke aiki clinic daya da auntie hafsa inna tayi shiru tace ibrahin wai? Aydarh tace erh shi, inna bata sake magana ba ta cigaba da cin abinci ta, har tagama kafin ta kalli Aydarh tace hafsa din tazo nan?aydarh tace erh amma yanzu ta tafi zata dawo anjima inna ta tabe fuska tayi yi shiru.malik yace tau ai baki daya zamu tafi ba?dr ibrahim yayi shiru kafin yace eh ai an riga da anyi jere so babu need din kuma ace hadda wasu yan rakiyan

amarya,kawai da ita kawai zamu tafi malik yace tau Allah yakaimu asabar din “dr ibrahim yace Ameen “ , da sallama yaron yashigo hannu shi rike da jug da cups ya ajiye kafin yace ina wunin ku? Dr ibrahim yace lafiya lau malik ma ya amsa, can dr ibrahim yakalli malik yace naji baka kira, ta ba yau malik yayi wani murmushin gefan baki kafin yace ai nasan yanzu safiya ce dr hafsa na clinic ita babu waya hannunta “ dr ibrahim yace eh haka ne dazu nurse saratu ma takirani malik yace ohh, ringing wayar malik tayi number ce ke ta kiransa tun jiya baiyi niyyar dagawa bas ai kuma yadaga yayi sallama daga can aka amsa cike da yanga tace ina wuni ranka dade bai gane mai magana ba hakan yasa shi cewa lafiya, kafin tace ya nasarawan? Yace Alhamdulilah “kafin tace sunana rabi’ah kanwar dr ibrahim abokinka malik ya dage giranshi kafin babu yabo babu fallasa yace oh Allah sarki ykuke? Tace Lafiya lau alhamdulilah kafin yace ga ibrahim din,dasauri rabiah tace aa bashi nake nema ba kai nake nema daman nakiraka naji ko ranar daurin auran dawuri zaku taso saboda ayi muku girki dawuri saboda abokanan ku kamar bai gane tambayar datayi masa ba “ yace okay “ tasake cewa dawurin zaku taso? Ehhh kawai yace mata kafin yakashe wayan tacigaba dacewa hello hello taji shiru takalli bilki tace yafa kashe wayan bilki tace ai Alhamdulilah tunda wahalar mu bata tashi abanza ba daman malan yace ko sau dayane kukayi magana dashi shikenan aikinmu yaci,rabiah tayi wani irin tsalle kafin tace Wayyo dadi waya ga rabiah a matsayin matar bawan Allahn nan kafin ta mike tsaye tayi wani juye tana fari da ido, sai kuma ta zauna tana kallon bilki tace bilki matarsa fa?bilki ta tabe baki tace tau ke miyayi ruwanki da ita? Rabiah tawani zaro ido kafin tace baki da hankali bilki baki da kan gado kin kau san yarda take wannan yarinyar? Wllh ganin kanki zaki dinga yi biri idan kina kallonsa shida matarsa wallahi,kinga duk kyau yayah ibrahim dashi yabiyo iya ko?tau komawa yake wani kwa’do kwa’do bilki ta babake da dariya tace amma fa rabi baki da mutunci yayah ibrahim din?rabiah ta saukan da ajiyan zuciya tace bazaki gane bane bilki wallahi ko a mazan indian flim ban taba ganin mai irin haduwar shi ba kin ga tsawon sa kam?kinga fadin sa kam?ke Wallahi kalan fatar sa ma kawai ya isa ya ruda mutun bama kiran jiki ko kyaun fuska ba wand ani ban ma san yarda zan misilata miki kyaun sa ba, bilki ta saki baki tana zara ido tace kai haba ? Ita fa matar? Rabiah ta tabe baki,kafin tac eke wannan yarinyar fa tsoro zata dinga baki ban taba ganin abu mai kyau irin taba ke billahillazi ban iya ma hada ido da it ani kwarjini take mun ga isa raini hankali da shegen girman kai wai kinji muryarta da yarda take tafiya bala’In nan “bilki dai sai binta takeyi da kallo tace Allah natuba rabiah kuma shine kike son kai kanki inda Allah bai kaiki ba?kiji yanzu fa tsabar girman kai da isa ko sallama bai maki ba ya katse kira ke ko

amsar kirki bai baki ba ‘anya rabiah bazakiyi ma kanki fada ba? Ki fta harkan su kiji yarda kika bani labarin abayan jikinta fa kika ce hannunta hadda diamond rings biyu ga dayan English gold kin kau san ko a can kasar wajan sai babban mai kudi ke siya?rabiah ta mike tsaye tayi ma bilki wani kallo tac eke Wallahi ko ma mi zai faru sai dai yafaru amma idan kika ga baayi auranmu dashi ba sai dai idan mutuwa nayi ko shi ya mutu, bilki ta rike baki tace tauuuuuuuu ban taba sanin abun har yakai haka ba yanzu ki tashi mu wuce kasuwan yarda zamuyu cefanan da wuri har mu hadu ma iya danata wanda zasuyi na wuni,rabiah tace tau shknn mutafi sai mu siyo kayan sobon ma baki daya tunda malan yace a zuba masa maganin a sobo bilki ta dau mayafin ta tace tau mu wuce kinga daga nan ma sai muyi wankin kan a daura man bakin lalle tunda munyi jaa rabiah tace tau shknn mu tafi.

Dr hafsa tace kinga yau nace mata zamu zo,aydarh tace erh ‘dr hafsa tace idan muka je can aka saka miki lallan sai na warware miki calaban a wanke maki gashin right?aydarh ta gyada kai kafin dr hafsa tace tau ki shirya tunda munyi breakfast basai munyi lunch a gida ba a can munyi nima bara na shirya nadawo yanzu inna ta wuce gidan iya,aydarh tace ina ne haka?dr hafsat ace ohh gidansu dr ibrahim wajan biki sai angama biki tadawo nidai sai gobe in sha Allah wuni kawai zanje aydarh tace Allah yakaimu dr hafsa tace Amin kafin ta mike tace sai nadawo kiyi sauri ki shirya kema,aydarh tayi murmushi tace right now auntie dr hafsa tayi murmushi, dr hafsa na fita tashiga tayi wanka kafin ta fito ta shafa vaseline da powder kadan sai kajal a idonta tasaka lipstick kadan shima kafin ta dawo dinki da tabaro gida sanye dashi a jiki yarda fitted gown din ya zauna a jikinta sai taga kamar na yau yafi na kullun kafin ta shafa perfume ta fito da well iron baby pink din hijab dinta ta ajiye kan katifan dan kwallin kayan ta dauka ta daura shi akai masha Allah “ knocking kofan akeyi tayi tunanin dr hafsa ce tafito bata ce waye ba kawai ta bude kofan, tunda ta bude suka zuba mata ido kamar sun samu cartoon kallon su tayi kafin tace ku shigo Wallahi bilki duk tunanin aydarh bata kai kyaun haka ba duk sai taji sun muzanta duk yarda suka taho suna wani yauki, bilki dai takasa dauke idonta akan aydarh ta dinga kallonta ko kiftawa babu ga wani masifan kamshi dake neman zauta su,Rabiah tace sannu kin gane ni ai ko tafada tawani irin fizga kaman irin yan local champions dinnan (yan ghetto idan zasuyi abun yan gayu lol) aydarh tayi wani irin abun da ido cike da isa ta tsaya bakin kofan ta rike Handle din ta girgiza kai bata ce komai ba kafin rabiah tace sunana rabiah kanwar dr ibrahim abokin yayah malik ,aydarh tace ohh ku shigo ta basu wuri takalmin

su suka cire suka shiga yarda aydarh ke tafiya bilki ta dinga bin da kallo duk ta sha jinin jikinta da niyyarsu sai sunyi abunda zai ma aydarh ciwo tun yanzu tasan rabiah naso malik, kitchen aydarh tashiga zata kawo musu ruwan rabiah nata wani tabe baki bilki ta dafe kirji tace rabiah see shape dan Allah wai kinga yarda take tafiya kiji maganar ta fisabillahi,rabiah ta bangawa bilki harara ta dauke kai,fitowa tayi hannunta rike da plate din ruwa sai fruits da tayi musu slicing bilki ta washe baki tace ina wuni bamu gaisa ba babu yabo babu fallasa aydarh tace Alhamdulilah " rabiah dai kamar zata mutu dan bakin ciki,kamar zai kasheta, aydarh tawuce bedroom tayi zamanta,kusan ten minutes suna zaune bilki nat asha kankana ita dai rabiah ko abu daya bata dauka ba, knocking akayi aydarh naji adduan ta daya dr hafsa ce domin haka nan taji batasan zaman su a gidan,fitowa tayi walking slowly ta isa bakin kofan kafin tace waye? Dr hafsa tace nice budewa aydarh tayi kafin tace auntie tun dazu nashirya fa, dr hafsa tace sorry sai danayi ma babyn neighbor din mu allura aydarh tace eyyerh kafin ta bata hanya suka shiga parlor dr hafsa ta dinga bin rabiah da kallo kafin tace rabiah ,rabiah ta kalli dr hafsa kafin tace na'am ina wuni dr hafsa tace lafiya bilki ma ta gaisheta ta amsa ranta fal mamakin abunda yakawo rabiah gidan aydarh tace mutafi? Dr hafsa ta gyada kai kafin Aydarh ta koma bedroom ta dauko hijab din tabude wardrobe ta fiddo da 5k din da malik ya saka mata,Still basu tafi ba suna gani aydarh ta fito rabiah ta mike bilki ma haka rabiah tace sai anjima idan munyi waya da yayah malik din na fada masa nazo, dr hafsa najinta tayi shiru aydarh ma haka kafin tace sai anjima suka fita, suna fita bilki tace wai Allah billahi kawata banyi tunani aie ta kai haka ba rabiah tace hmm nima sai naga Wallahi kaman ta kara wani abu bilki tace ko ciki gareta?rabiah tace nima shi nake tunani kiji structure dinta Kamar cikin ta kamar bata sa masa abinci amma ji kugu tafiyan nan maybe ba da biyu takeyin ta Wallahi bilki tace bawani da biyu haka take ajin ta har yayi yawa ma wallahi ahh. Dr hafsa tace tau muna ta shiri baki tambayi yallabai ba, aydarh ta zaro ido tace ah'ah fa,dr hafsa takalleta tace aa fa mi? tayi kasa da kai tace zai hana ne,dr hafsa tayi murmushi tace ohhni aydarh kullun ke kaman yarinya idan yahana ai sai a hakura amma kin taba ganin inda mata tafita ba da izinin mijinta ba? Aydarh tayi shiru kafin dr hafsa ta fito wayarta daga cikin handbag dinta tace bara nakira maki shi sai ki tambaye sa, dialing number malik tayi har ya kusa katsewa kafin yadaga batayi magana ba ta mikawa aydarh wayar, sallama yayi aydarh ta amsa yana jin itace yanemi guri yazauna yayi shiru yana jiran tayi magana itama shiru tayi kafin takama gefen hijab dinta tana wasa da shi kafin tace ina wuni voice dinta very slow and innocent yace lafiya lau,tayi shiru kafin yace talk,ta tura baki kaman irin yana gabanta tace henna "jin abunda tace yasa

shi maimaitawa dan ba wai yagane bane yace henna? Sai sannan ta gyada kai tayi kasa da murya gabanta na faduwa kar yace bazata je ba kaman waccan ranan tace salon zamuje nida auntie daga nan ayi manah lalle takarasa maganan kamar mai shirin kukan murmushi yayi kafin ya girgiza kai yace tau ba auntie ta mikawa dr hafsa wayan da tun dazu take kallon ikon Allah wannan shagwaba har ina su yan gayu masu kudi komai nasu daban ne,wayan ta karba tayi sallama kafin ta gaishe bata ji abunda yace ma dr hafsa ba kafin tace aa yallabai abarshi wallahi babu damuwa,sai kuma tayi shiru tace tau shknn Allah ya amfana,sai datayi dialing acct digits dinta kafin ta tura masa,ta kalli aydarh tace cewa yayi na tura masa acct number yasaka kudin salon din Aydarh tayi shiru kafin tace to 10k yasa dr ibrahim yatura masu saboda shi bai da acct number yanzu suna shigowa dr hafsa tace masha Allah ya tura 10k aydarh tace to mutafi kafin kuma ta mikawa dr hafsa kudin hannunta tace gashi ai nasa 15k ma bazai isa ba dr hafsa tawara ido tace kai ai 3k ma ya isa aydarh da mamaki tace 3k kuma? dr hafsa tace aaa ai mu daku ba daya bane mu na mu babu tsada kai ta girgiza kai batasan lokacin da tace 35k ne henna kadan a nails sai salon hakane bill din,dr hafsa tayi murmushi tace ina gani a ig aydarh ai ba daya bane da namu aydarh tayi shiru kafin su fita sai da suka rufe kofan part din kafin suka fita,sai dasuka shiga keke kafin dr hafsa tace daman kinsan rabiah ne? Aydarh ta girgiza kai kafin tace sister dr ibraheem ne right?dr hafsa ta gyada kai kafin tace mi yakawo ta? Aydarh tabude hannu alaman batasani ba shiru dr hafsa tayi kafin tace datace idan sunyi waya da yallabai zatace masa sun zo shi ya aiko su? Aydarh tace I didn’t even know kawai ganin su nayi sun shigo, dr hafsa tace basu da hankali yaran nan at all bansan abunda ke damun su ba, aydarh dai tayi shiru har bakin babban plaza mai keken yayi Parking suka sauka dr hafsa ta biyasa kudin kafin suka wuce cikin plaza suka shiga wani irin faduwa.

Wuri suka samu bayan Sadyyyy tayi welcoming dinsu cike da mutunci,tight friend din dr hafsa ce shagon babba ne mai kyau akwai komai a shagon, sadyy tayi murmushi kafin tace kawata ina aka samu balarabiya ne?dr hafsa ta girgiza kai tace gata nan dai kina gani she is my sister sadyyy tace Allah sarki kafin ta kalli aydarh da fara’a a fuskanta tace sannu fa aydarh ta mayar mata da murmushin tace sannu “dr hafsa takalli sadyyy tace jaa da baki zaayi mata lallan ni black kawai nakeso sadyyy tace tau shknn salon fa? Dr hafsa tace shima za’ayi afara yin lallan shi keda wahala,cikin few minutes aka hada komai kafin aka fara zanawa aydarh hadaddan flower a kafa, mai azaban kyau simple style ana farawa dr hafsa tafara warware mata calaban there are experts shiyasa ba awani wahala ba aka gama jan

yayi kyau sosai sai daya fara sha kafin sadyyy ta dinga bin rings din hannu aydarh da kallo aydarh na lura da ita batace komai badai dr hafsa na janta da fira sama sama, kafin sadyy tace ki cire zoben sai ayi black din aydarh ta gyada kai kafin tasa hannu tafara cire rings tana gama cirewa ta hadda duk three din ta mikawa dr hafsa karba tayi tasaka cikin handbag dinta kafin tace cigaba da labarin datakeyi, sadyyy tayi murmushi tace kawata ban taba wa wani lalle yayi kyaun haka ba Wallahi dr hafsa tace dan Allah fa masha Allah aydarh dai murmushi kawai take,sadyyy tasaki baki tana kallon dr hafsa bayan tagama warware ma aydarh calaban gently tasa hannu ta shafa gashin aydarh kafin tayi kasa da murya tace Allahumma bareek" yanzu nan wai gashin nan salon yake bukata? Dr hafsa tace haka yake wannan gashi sai ki dinga ganinsa kamar a gyare kullun " sadyy tace amma baki jima dayin salon ba right? Aydarh ta girgiza kai kafin tace yajima,sadyyy dai tayi shiru tana kallon ikon Allah, tun shigowar su taso tagane aydarh sai dai tayi shiru tarasa ina ta taba ganinta, can takalli dr hafsa tace kawata kina shiga page din salmerh malami right? Dr hafsa tayi murmushi saboda tama san abunda sadyy zata fadi kafin tace ehh ina shiga sadyyy ta rage murya tace dan Allah ba suna kama da wannan yarinyar datake posting ba dan dai wannan tafi waccan haske da giba yarinya dana nuna maki hillis din nace miki a million kadan ke babu did you remember? Dr hafsa tayi saurin cewa ehhh natuna sadyyy " sadyyy tace Wallahi kaman ita, dr hafsa ta kalli aydarh da kanta ke kasa bata son labarin yayi tsawo saboda ta fahimce labarin kaman irin rauni aydarh ne kar abunda yafaru jiya yafaru yau kar daga wannan labarin su sake taso mata inda yake mata ciwo, ta dinga irin kukan datayi jiya,dr hafsat ace ehhh itace kawata sadyyy tawani gwallo ido tasaki hannun aydarh tace ki rantse da martabar Allah dr hafsa tace ai bama wannan wasan, sadyyy tayi shiru tana mamakin abunda yakawo nan din 'shiru tayi kafin tace Allah sarki "tana kallon aydarh kafin tayi kasa da murya tace ki godewa Allah you are more than fine you are more than beautiful kinfi kyawu kyau , dr hafsa tayi murmushi tace awwww sadyyy kice masha Allah yanzu dai ayi sauri agama lallan Saboda mu koma dawuri let her makes some preparation for her husband a gida "sadyyy tace miji? Is she married dr hafsa ta gyada kai tace sure "sadyy da bakinta yak'I rufuwa saboda murmushi tace masha Allah congratulations dear Allah yabaku zaman lafiya da yara nagari aydarh tace Ameen ahankali Still bata dago kanta ba, sadyyy tace kawata amma bata haihu bako? Dr hafsa tace ehh sadyyy tace daga waje zai dawo mijin saboda na lura kamar itama tafi zama waje, dr hafsa tace aaaa sadyyy batayi shiru ba tasake cewa a yola kuke ba? Aydarh ta gyada mata kai kawai,dr hafsa taga tambayoyin nayin yawa tace ki kira wata cikin su sai tayi mun ni ita kiyi mata kawai,sadyyy tajuya tace

tau shknn bara nakira tunda ke baki ne kawai ba? Dr hafsa tace eh baki kawai sai mun retouch itakuma wash kawai zaa mata sai steaming baki daya sadyyy tace tau shknn,wasu hadaddun leaf sadyyy ta zanawa aydarh a hannu yah rabbil alameen yayi masifan kyau yayi endless kyau masha Allah kadan kadan akayi black henna kasancewan ta fara bakaramin zama lallen yayi hannun ba ga yaji kayan hadi ya kara baki har wani shine shine yake, ledan jan aka bude shima yafara.

Dr ibrahim yace tau ka kira ta sai tabude data koh? Malik yace okay kafin yayi dialing number dr hafsa tana daga tayi sallama ya amsa kafin yayi kasa da murya yace kunna data ki ya kashe wayan wayan tabi da kallo kafin ta kalli aydarh sai tajawo ta kunna data kafin taga number dr ibrahim na kiranta vedio call accepting tayi tana mamaki vedio call kuma dr ibrahim , Malik tagani zaune kan katifan Wallahi zatin shi kyau kwarjini nutsuwa da kamala har a cikin waya masun bayana ba a fili kawai ba da sauri ta mika aydarh da aka cire ma lalle hannu daya wayar karba tayi tana ma dr hafsa alama dawaye murya can kasa dr hafsa tayi murmushi kafin tace yallabai “bin screen din wayan tayi da kallo shima ita yake kallo ganin yarda aka gyara mata gashi lumshi ido yayi kafin ya bude yana tasbihi wani irin kyau yaga an kara mata,kanta kasa kafin murya can kasa tace ina wuni sir? Bai amsa mata bas ai cewa yayi angama ne? Ta girgiza masa kai yayi shiru yana kallon yarda take wani dauke ido wani cute smile yayi yashafa hadaddan kwantatcan bread din yasa cikin ransa yace sturbborn bea very cute very demure “cuddle bug” yasamu kansa dafada ahankali a fili bai ma san yafadi ba itama bataji ba, ahankali yace the hair looks good “ ta dago idonta ahankali tace thanks kafin cike da tsokana yawani hade rai yace what about the henna shi ban gani ba? Yace barsa ma no Need Ramlah ma tace mun zataje lalle naga nata,aydarh ta hade rai kafin tace sai ka kirata ta nuna ma “ malik yace right now ma yace sai anjima ‘aydarh cike da tsiwa tace kar ka kashe fa yace tau mi zanyi maki “kaman zatayi kuka tace ai ni lallan zan nuna ma kooooooooo ,kaman wani witch haka yasaki baki yana kallonta,hannu ta daga ta nuna masa yah rabbi ya furta ahankali yana masifan son lalle amma bai taba ganin lalle mai kyau irin wannan ba kallon ahannu yake ko kiftwa babu kafin ta janye ta mayar da wayar dayan ta daga masa hannu ajiyan zuciya yasauki bai sake magana ba itama tayi shiru shidai sai kallon lallan yake can taji shiru tace are you Still there? Tayi tunanin ma network ne yayi failing kafin malik yace sure anyi a kafan tau? Ta gyada masa kai kafin ta mayarda camera back kafan yasha lalle tun da aka wanke yayi wani irin maroon mai kyau kafan tsaban kyau da tsabtan shi

Kamar ka zuba ice cream ka lashe a kafan flowers ne akayi manya masu azaban kyau tana gama nuna masa ta maido camera gaba kafin fuskan nan ba wasa tace,kuma karka kirata Allah,yace as you wish your majesty “tayi wani smile wanda saura kadan malik yayi loosing cike da yarinta tace Good boy,malik ma yayi murmushi ta dinga kallonsa dan Wallahi yi yayi kamar abba “bata masan tana kallonsa din ba Sai da yace hey kafin tayi saurin dauke idonta tace bye “shima yace bye sturbborn bea tahade rai kaman zatayi kuka tace Wallahi bani ba “malik bai ce komai ba ya kashe kiran “ dr hafsa tayi murmushi tace kinga yarda kikayi kyau kam,je kid uba mirror,aydarh tayi murmushi tace thanks auntie dr hafsa tace don’t mention yallabai yace yayi kyau ba?aydarh ta gyada kai tace erh fa yace yayi kyau sai kuma ta bata rai dr hafsa tasaki baki tana kallonta kafin tace what? Wai fa shi yace zai kirata ta nuna masa taje lalle itama,dr hafsa tace ita wa? Aydarh tace I didn’t even know her name ma self,dr hafsa tace ohh Ramlah wai? Aydarh tace erh ita,dr hafsa ta girgiza kai tace don’t bother your self wasa yake bata ma da Ko number sa idan ma taje lalle ai bazaiyi fice a hannunta ba balle har wani yagani so wasa ma yake ita dai aydarh tayi shiru tana kallon dr hafsa , sadyyy tace hafsa ki wanke naki duk yayi dr hafsa tace tau, yayi kyau masha Allah na dr hafsa ma,sadyyy ta kalli aydarh tace tun kafin goben har an nuna masa ohhni aydarh,aydarh tarufe fuskan ta da hijab tana dariya kasa kasa dr hafsa ta tambayi bill din sadyyy tace aaaa bazata karba ba babu yarda basuyi da ita tace kyauta ne Wallahi dr hafsa tace thanks kawata Allah yabar zumunci sadyyy tace amen “ aydarh tace thank you auntie, sadyyy tayi murmushi tace you are welcome dear “ Amma ki gayawa yallabai na biyo sa bashi idan kika tashi dawowa nima irin wannan dubai perfume din nakeso na jikinki aydarh tayi murmushi ta lura sadyyy na son wasa kafin tace in sha Allah “dr hafsa tace tau wannan kamata yayi kawai kice mata perfume dinta ya hadu miye sunansa sadyyy tace woooo kawata ina ni ina iya siyansa dr hafsa tace kya ji dashi dai,sadyyy takara cewa hilis din nan har yanzu fa kun hanna ayi manah imaginations dinsa, aydarh tace eyyerh daman kaman bashi dayawa kaman only 2print ne kuma code 1 oum tasa akayi, sadyyy tace Allah sarki amma sunyi kyau amma dan Allah mamanki keda campany right aydarh ta gyada kai, sadyyy tace Allah yataimaka nagode sosai ku gaida gida sosai sukayi bankwana har bakin hanya ta rakasu she even thinks ko da mota suka zo sai taga sun samun keke ita dai mamaki yak’I barin rayuwarta.

Kasancewan daurin auran safe yasa su tashi da wuri saboda da an daura zasu wuce, koi na cike da Jama ‘a anata hidima dr ibrahim kau murna kaman zai daka kan baby, malik dai sai kallon ikon Allah yake wajan dr

tace Amen. Sai wajan 5:00pm suka dawo suna dawowa ko shiga ciki malik baiyi ba yace wa dr ibrahim yace ta fito su wuce, hibba ta bata turaran datace kafin ta gaya mata yarda zatayi amfani dasu chops din da bata ci ba, hibba ta zuba mata a Leda kafin tasaka hijab har bakin kofa ta rakota inda malik da dr ibrahim ke tsaye suna jiransu, sallama sukayi malik yasake yiwa hibba godiya aydarh ma haka hibba duk sai taji wani kala kaman kar ta tafi, anan bakin titi suka samu keke,har kofan gida yakawo su malik yabiyasa kudinsa kafin suka shige tana gaba yana baya biye da ita, kofan part din yabude suka shiga bedroom tawuce ta ajiye kayan hannunta pics din dake jiki ba karamin sa ta kunya suke bay au daga labarin dasukayi da hibba sai takara jin girma da nauyin dake kanta na auransa,ya idan yanzu fa shima yace suyi irin wannan rayuwa?da sauri ta girgiza kanta tace bana sonshi shima baya sona to babu abunda ma zai faru dawannan tunani ta tattare su ta jera a wardrobe kafin tawuce toilet flask din ruwan zafin ta bude ta juye a bucket tawuce toilet tayi wanka tareda dauro alwallan magriba, vaseline kawai tashafa sai perfume, tasake gyara parking dinta kafin ta saka inners da gown din atampha, bude kofan tayi yana parlor shima da alama yayi wanka amma bai Chanza kaya ba singlet ce jikinsa sai dogon wandon shadda da karamin towel yana goge suman kanshi da ya wanke wanda tayi kusan na wata macen mai gashi a Nigeria yanda sumansa yake kaman na larabawa kallo daya tayi masa ta dauke ido tashige kitchen dasauri yana kallon duk abunda takeyi bai ce komai basai cigaba da abun yakeyi dayayi , har tashiga kafin ta bude idonta da ta rufe ta kulle kofan dasauri, bata taba ganinsa haka ba, ahankali tace katuwa kai tafada kasa kasa tana harara kofan kitchen din kaman yana jikin kofan, ruwa ta tara a tukunya kafin ta kunna gas, ta daura white rice zatayi kadan sai aci da mai tunda yasiyo yaji tana son shinkafa da mai da yaji sau daya ya tabayi tagani shine zata gwada yau tana daurawa ranar hadda wake,bude ledan da taga wake tayi ,tasa cup din data gani ciki ta auna half kafin ta tsince sa tass duk da babu wani tsinta a ciki,wankewa tayi ta zuba kafin ta mayarda tukunya ta rufe,gently take takowa cikin parlor yana zaune kan carpet ya chanza kaya zuwa black shirt sai black jeans, zama tayi can nesa dashi kafin ta saukan da kanta kasa tana wasa da gefen carpet din kallonta yayi yanda inner cap dinta yaja baya bakaramin kyau yayi mata ba, shiru yayi baice komai bay ana sauraron ta, can dai tace “ kasiyo salad din da cucumber”sai tayi shiru kallonta yake ko dauke ido babu can yayi kasa da murya kafin yace mi za’ayi dashi? Tace white rice and beans zan dafa shiru yayi bai ce komai ba itama bata sake magana ba,ta tashi ta koma kitchen, kusan 20mins sai gashi yashigo kitchen din hannunsa rike da bakin leda kwara biyu ya ajiye ya fita,ledan ta bude salad ne sai tomotoes da cucumber da green pepper dayan ledan ta bude

taga five eggs sai gasasshan kifi babba kwara daya, Fido su tayi daga ledan kafin ta wanke shinkafan da ta sa a ruba ta zuba a tukunya salt tasaka sai ajino moto kaman yanda taga yayi ranan, one hour thirty minutes yadauke ta kafin tagama abinci lokacin har ya tafi sallan magrib daki tawuce itama tayi sallarh kafin tadawo kitchen ta gyara shi tass kaman baayi girki ciki ba, knocking akayi tasan shi ne ta bude, parlor ya zauna ta wuce kitchen,yarda yake kallon abinci kaman yau ne first time dayafara ganin irin sa, can yace kinci abinci ta girgiza masa kai tace ah'ah sai mundawo "ya ajiye spoon din hannunsa yace ina zamuje?sai sannan tace ohh auntie ce bata da lapia zamuje dubata hadda ita nayi girkin ma shidai malik bai ce komai ba yacigaba da cin abincin sa ,har sai daya kusa gamawa kafin ta wuce gida,bayan yagama ya kwashe yakai kitchen kafin yawanke bakinsa ya wuce masallaci, tunda tagama sallarh ta fito da warmer nan parlor tana jiran shigowan sa sallama yayi ta amsa kafin ta mike tace muje ? Malik yace aaa.

Tace ah"ah fa kace tafada tana kallonsa,can yayi kasa da murya yace eh aaaa babu inda zamuje kaman zata kuka tace to ai sai natafi ni daya "yace tau shknn sai kindawo har ta dauki warmer tanufi hanyan kofa kafin yasa hannu ya jawota ta dawo baya kaman zata fashe da kuka tace masa "miye haka kikeyi wai? Bai ce komai bay ace miyasa baki tambaye ni tun jiya bas ai yau? Tace ai namanta ne kuma aie shiyasa nace naje ni kawai tunda kai baza kaje ba , malik baice komai ba yasake ta ya dauki warmer din, yayi gaba tana ganin yafita tayi saurin biyo sa rufe kofan yayi suka jera tare suna tafiya, dasauri ta iske su kofan gidan duk irin warnings din shi baya shigan ta tunda ta biyo su Aydarh ke lura da ita shima ya ganta amma sukayi tafiyan su,har sun kusa gidan inna kafin tace yallabai tsayawa malik yayi kafin ya juyu yana kallonta,cike da kilbibi tace ina wuni? Ya aiki malik yace Alhamdulilah ykk?ai yau Ramlah kaman zata mutu tsaban dadi wai malik ne ke ya tambayarta ya take,tawani shagwabe masa kafin tace not fine "yace eyyerh mike damunki? Yah rabbil alameen Aydarh juyawa tayi kawai ta cigaba da tafiya " bata tsaya sauraron su ba malik nagani ta juya daman saboda gabanta ne yayi haka shima ya bi bayanta saboda bazai iya cigaba da magana da Ramlah ba yau ma sa'a taci kawai akwai abunda yake so yayi ne yasa shi magana da ita,anan zauran inna ya tarar da ita alaman bata shiga ciki ba jiransa take hade rai yayi zai wuce ta sa hannu ta jawo ya dawo kafin ta bata rai ta hau saman wani dan dakali dake nan zauran yanda tsawon ta zai kamo nashi duk da ta hau din bai kamo ba amma ahakan tasa hannu ta kama kunnan sa ta wani ja,ba zafi yaji ba amma sai dayayi yar kara bata saki kunnan ba tace idan ita bata da hankali tasake ma magana a waje " tasaki kunna kafin tayi wucewan ta ciki ya kusa 5mins nan a tsaye yana

maimaita magana “har bai so ta saki kunnan ba shafa kansa yayi yarasa miyasa yarinyan nan bata tsoronsa ba, wani zuciya tace itama ke tsoronka amma sturbborness dinta bai barin ta dinga jin shakkar ka,yanda maza da mata ke shakkansa ke tsoron sa a gida daya shigo kowa zai nutsu haka ma mutanan waje ko a kanon ma sosai mutane ke girmama sa saboda kwarjini dayake musu amma ita aydarh rashin kunya sai wace ta manta ke bata yi masa (kaji karya😂😂) binta yayi cikin gidan inna na zaune tsakan gida sai faman wanke zogale take,malik ya duga kusa da ita ya ajiye warmer kafin yace innana ni kadai “inna ta washe baki tace audu ashe hadda kai nayi tunani ita ce kawai ya girgiza kai yace waya na tsaya amsawa,inna tace oho ‘malik yace ina wuni inna ya gida?ya mai jiki kuma? Inna tace ah lafiya lau yakuke? Malik yace alhamdulilah inna ta rage murya tace nidai baa haka dani Wallahi malik yace tau mi yafaru? Inna tace ban sa fa tana ciwonta ba sai dai naji takira shi saurayin nata likita ne shima ai na baka labarin sa ko? Malik yace ki gaya mun wannan wanda yake da mata ko? Inna tace eh shi,can babba asibiti yake aiki ai malik yace oh oh Allah sarki,sai fa kawai naji ance tazo can asibitin kar taje tasu wai ayi maidical chakof, malik yace a ina zaayi mata medical checkups din? Inna tace can babbar asibiti fa malik yace tau ai hakan yafi kila ba malaria bace kawai maybe ma hadda stress na wajan aiki inna dai tayi shiru bata sake magana ba ta cigaba da wankin zogalenta malik yace suna parlor?inna ta gyada kai yace tau bara nashiga na dubata warmer yasake dauka yashiga parlor dr hafsa na kwance kan three siter sai aydarh dake zaune kan one sallama yayi ya ajiye warmer dr hafsa ta tashi zaune kallo daya zakayi mata kasan bata da lafiya duk da taji sauki amma tadan fada, gaishe sa tayi ya amsa yana yi mata ya jiki ta amsa nan kujeran da aydarh take ya zauna duk one siter yasan bazata ishe su ba amma neman rigima yasa shi zama,dr hafsa na gani ta janye ido “ Aydarh kam wani kallo tayi masa kaman zatayi kuka tana nuna mashi direction din dr hafsa kaman ma bai gani ba yasa hannunsa ta cikin hijab dinta yana kama wrist dinta yarike gam,Wallahi kaman zatayi fitsari saboda zafin dataji har sai datayi kwalla amma ta daure,duk abunda yake dr hafsa na kallo ta fuske tana godiyan abinci bata iya amsa taba saboda kunyar datake ji kaman zata nutse a wurin dr hafsa ta mike tace bara, na juye daman dazu nagama ce ma inna tayi mana ta dinga fada wai dambu za tayi malik da kaman bai san miyayi ba yace, sannu dr kinsan halin yan kayanmu ai,dr hafsa na murmushi tafita mamakinsa ya cikata,a rai take fadin “maza fa basu da kunya daman wannan yarinya yarda take ai tabani dashi ko da kau cikin mutane ne, dr hafsa na fita tasa hannu tana kokarin ciro hannunsa dake hijab dinta hawaye nabin cheeks dinta tace what’s all this sir? Malik yaware ido yace what? Wani abu akayi ne? Still hannunsa na a hijab dinta

yana shafa bayanta,tace ka cire idan auntie tayi tunanin wani abu fa? Yace tau hala ita auntie batasan ni mijinki bane? Aydarh tace amma aie babu kyau , yace minene babu kyau kuma? Tace abunda kakeyi din, yace eyyerh na daina tau yafada yana fito da hannunsa daga hijab dinta tace to ka Chanza wuri yace right now ma yamike yafita daga dakin baki daya yana komawa wajan inna, dr hafsa tadawo aydarh tak'I daga ido ta kalleta dr hafsa ta girgiza kai tana murmushi kafin tace kwantar da hankalinki babysis su fa maza babu ruwansu ki daina damuwa ma,sai sannan aydarh tasa hannu ta goge hawayenta tass kafin tace auntie kiyi masa magana "dr hafsa tawaro ido tace maganan mi? Aydarh tana wasa da hannunta tace matan nan kullun sai tayi masa magana hadda ma abinci tayi masa dr hafsa na kallon aydarh ko dauke ido babu yarda take magana cike da yarinta zaka san bawai kishi bane aaaaa kawai tsantsar shagwaba ne bata saba sharing abu da mutane ba tun asali, komai nata nata ita daya " shiyasa bata son yana magana da Ramlah, dr hafsa tace kiyi hakuri idan naji sauki sai nagaya maki abunda zaayi, bani ce zanyi masa magana ba, ke ce zakiyi masa kinji koh?aydarh ta gyada kai tace na fa yi masa auntie amma bayaji har fa tambayanta yakeyi ya take?tafada tana bude ido tareda turo baki dr hafsa ta kwashe da dariya, tace tofa,aydarh tabata fuska tace shine kike dariya auntie?dr hafsa tace ai ke ce da ban dariya kinsan miyasa bai daina ba? aydarh ta girgiza kai dr hafsa tace kiji yanda kike masa magana in a childish manner kinsan idan kina masa warning haka har wani dadi yakeji,Aydarh tace Wallahi ranan har abinci na hana sa sai daya bani tausayi kawai nabasa kuma shima sai dayace nabasa saboda umminsa, dr hafsa duk da bakaramin dariya abun yabata ba amma ta daure tace kai haba? Aydarh tace Wallahi,dr hafsa tace daga yau kar nasake jin kin hanasa abincin the worst part ma ki hanasa jikinki kinji Aseeya? Gabanta yawani irin fadi saboda statement din dr hafsa na karshe,batace komai ba ta sunkuyar da kanta kasa, dr hafsa tace kinga last time har sai daya kwana asibiti duk laifin da zai maki karki na hana kanki kinji Ko aydarh idan bahaka ma malikun rahama zasuyi fushi dake,and abinci ma ki dinga basa kinji babysis? Aydarh duk da Hankalin ta yatashi ta daure tace "to"dr hafsa tace promise me bazaki sake ba Aydarh da kaman zata fashe da kuka can cikin throat tace I promise "dr hafsa tayi murmushi tace yauwa yar albarka Allah yabaku zaman lafiya yakawo cutes twins masu kama da ku,aydarh dai tayi shiru tana sauraron yanda gabanta ke faduwa har sai wajan ten suka tafi time din inna tagama kwada zogalan ta sawa malik a warmer suka tafi dashi.

Tace sai fa nayi contacting world health organization,malik yace tau ko na ma baki aron wayana ki kira can din yanzu? Aydarh tace you thinks am

kidding you ba? Malik yace no Aydarh tace to Wallahi dana kirasu nayi karanka kayimun allura while kai ba likita ba ba nurse bas ai sun ji miyasa,malik yace kai haba hala tunda nayi miki alluran baki cigaba da tafiya ba? Aydarh tawara ido tace kusan ten days fa kenan jira nayi ayi two weeks idan naji wani abu to,malik dai kamar yayi dariya he likes how she behaves he likes every bits of her manners,yarda take magana is killing him deeper, yana son yar muryan nan nata,kadan kadan take magana kuma cikin ruwan sanyi, tace tsaya miyasa kayi mun allura ma?sai yanzu ta tuna kenan yasamu kansa da tambayar kansa,kafin yace sa'a kawai na gwada aydarh tawara ido tana sake gyara zamanta kan katifan tace, this is really bad sir 'malik ohh haba ni ai bansani ba,aydarh ta marairaici fuska,tace what did you study please malik yadauke idonsa daga kallonta yace computer science, tace kuma shine kayi mun? Yace ayi nayi tunanin kowa fa zai iya yin allura shiyasa am sorry yafada yana kama kunnan sa ita dai aydarh bata ce komai ba tayi shiru,amma sam bataji dadin alluran bad uk da babu zafi Ko kadan har ta mance ma sai yau ta tuno kuma batasan yafita waje yau din a tunaninta zai iya haduwa da Ramlah, kuma bata son haka mikewa yayi ya bude wardrobe dinsa yafito da credential dinsa ya daura mata kan laps dinta bude envelope din tayi kafin ta dinga takadan da kallo ko dauke ido babu kusan ten minutes tashiga shock kafin ta bude ido tana kallonsa tace this result belongs to who? Malik yace hala baki da ido ? Sake kallo paper tayi hoton sa ne da kuma sunansa,batasan time din tace first class a wannan uni din?kuma medicine fa?tafada duk mamaki ya cika ta,ya kwashe credential dinsa ya mayar kafin yadawo yace yanzu kinga sai ki kira yan world health organization din ko ? Aydarh dai har yanzu mamaki yaki barinta first class fa a wannan university,can tace tau miyasa baka aiki while gashi nan you are a qualified doctor fa sir yace no am not tace you are practitioner a legally licensed physician surgeon,duly registered and practsing within the scope of your license pursuant to the laws of the country fa sir right now you deserves to be working in a medical field kasan a Nigeria baku dayawa masu irin wannan qualifications din,kallonta yake ko kiftawa babu kafin yace sure ASSEIYARH amma ai ban samu aikin ba,mamaki take tana kallonsa tace why,ya girgiza kai yace nothing tace this unavailable I could remember a school dinmu akwai wani mai irin haka lecturer ne amma right yana working a babban asibiti a can USA malik yayi murmushi yana shafa kansa yace, ai shi yanada hanya ne aydarh tayi shiru tana kallonsa ganin duk tashiga mamaki yasa malik cewa ehen ke fa? Ko can world health organization din kike aiki,yarda yayi maganan kawai taji dariya wani cute dariya take daya sa shi kasa dauke ido kanta kafin tace ai ni ban gama ba yace kai haba why dandanan idonta ya kawo tears tace kai

kaja ai,malik yace nikuma ASSEIYARH? Tace erh,yace how tace saura two days na koma hutu shine kazo akayi manah aure tafada kukan na kwace mata kallonta yake ko dauke ido babu , tace and this is my final year,malik yace stop crying tells talk ina ne school din?tace Cyprus university of technology,malik ya jinjina kai yace mi kike studying?tace pharmacy and technicials Malik yayi shiru bai ce komai ba amma yarasa ma wani tunani zaiyi kukanta take yayi shiru bai ce mata komai ba amma bakaramin tausayi ta bashi ba can yace am sorry lil sis I didn't wished things to come this way but I promise you will be come a qualified technicians aydarh da hawaye still a idonta take kallonsa hannunsa yasa yayi wiping mata hawayen kafin yamikar da ita yabude toilet kafin ya kunna tap yafito yace wash your face and pray let's prepared lunch yafada yana nufar hanyar fita masallaci yawuce kasancewan lokacin azahar ne.wajan mai cefane ya tsaya yasiya nama da kayan miya tunanin conversation dinsu yakasa barin kansa bai taba jin tausayin kansa ba irin yau a yau ne yayi mata kallon su aysha a yau ne yasan akwai babban nauyin ta akansa a yau ne yasan zuciyansa tayi karya a baya amma mi DA SO KAMANE da ba zai.

Da babu shi tsakanin nida ke ! Wani iri yaji dasauri yayi hanyar gida domin baya ma son maganan sam, lokacin daya shiga Ramlah na nan bakin kofan tana jiran dawowan sa yana shigo tayi maza ta tashi tace barka da dawo yallabai "babu yabo ba fallasa yace yawwa yafada yana wuce ta bin sa tayi da kallo har yashige ciki kafin ta dauke idonta heart dinta nawani masifan melting, knocking yayi tazo ta bude masa " ledan hannunsa ya mika mata ta karba kafin yace muje sai muyi white rice da stew ga salad nan batace komai tayi gaba ya bit abaya kitchen din kayan miyan yafara gyarawa ita kuma ta daura ruwan farin shinkafan, can yace ko asaka wake ne? Ta girgiza kai tace ah'ah basai ansa ba zan yanka green pepper a ciki kuma yakare ma aie,malik yace eh namanta dashi kikayi ma dr hafsa girki jiya "tabude ido tace kai baka ci ba ko? Yarda tayi magana yasa shi yin smile yace tau ai nasan ita kikayi wa bani ba,tace da banda kai ai bazan baka ba 'yayi murmushi yace abunda girkin ma sai ahankali daurewa kawai fa nake ruwan dake hannunta a cikin cup zata kara cikin tukunya ta sa left hand dinta tadeba ta watsa masa kadan a kai da fuska,dasauri ya mike baki bude yake kallonta kafin tawani hade rai tace kasan I can cooks more than you "yayi kasa da murya yace naki wasa ne yarinya wanda jiya ma dakyar na iya cin wannan abinci dakika girka, kuma dakika watsa mun ruwa zan rama ne ai! Batace masa komai ba ta juya salad din tafito daga leda mai kyau green shar da tomotoes din manya a robber ta juye kafin ta kuna pampoo tana wankewa duk wani motsi datake yana lura da ita ta gefen ido he didn't

know why idan suna tare baya son dauke ido kanta har yau yakasa gani abu daya wanda tayi lacking tanada komai idan akace komai ana nufi komai da komai kasan yashafa kafin ya mike yace am done with this wash it, karba tayi ta wanke zufa kadan a kan goshinta da hancinta, kallonta yakeyi yanda takeyi da fuska irin aiki yasha maka kan nan yace she is more than cute and she is more than finest,she is an angel tana gamawa ta mika masa robber kaman wani yaronta tace blende it,hannu yasa kafin yace right now ma'am , cikin few seconds yayi blending din sama-sama yana gama wa ya kashe ya dauraye blender, ta mika masa salad din tace ka yanka wannan shima kallonta yake ganin yanzu tazama kaman ita ke koya masa girkin ma da kau sai abunda yace a kitchen din, hannu yasa ya karba itakuma tacigaba da bare cubes, kaman daga sama yaji tace "ita wannan bata schooling or? Malik yace wacece,aydarh tawani bude shoulder tace I can't even remember name,yace tau idan kin tuna you can ask daga haka yayi shiru kusan five minutes babu wanda yasake magana cikinsu, tace wadda apartment dinsu ke farkon shigowa farh,tun dazu yagane wace take nufin he just pretend kafin yace oh oh babe? Tace wace haka? Yace ita wace kika manta sunan nata, tace Ramlah ne babe? Ta fada cike da mamaki "malik yace eh ita fa, tace miye ma sunan state din nan? Malik yace kano tace ehen Kano duk fadin kanon nan karasa waye babe dinka ko what did you even use to called her before ewwa gurl , sai ita are you for real? Wannan tayi kama da mace ma first? Duk dayaji dariya tazo masa amma ya daure yace "yes" Aydarh tace "this is serious " yace kinga danayi kudi sai muje can adamawa a daura manah aure da ita, aydarh ta dinga binsa da kallo kafin tace to Wallahi ummi bazata yarda ba, yayi kasa da murya yace saboda ina auranki ke bazata yarda bako ? Aydarh tawani bude shoulder tace babu ruwanta da wannan can't you see how local and disrespectful she is?she is mannerless she didn't deserves to be a ladie at all,malik yayi shiru bai ce komai ba yacigaba da yanka salad dinshi,can even your sisters will not allowed you to do suchs, malik yayi dariya kafin yace tau so ina ruwansu?ai nin e yayansu duk abunda nayi wajan su daidai ne,Aydarh tace komai fa kace?ya gyada kai yace sure tace sunyi kokarin kam,can tace what is their names? Yace aysha,halime sannan yace maryama autarh "yana fadin autarh ya girgiza kai yayi tare yace she is very sturbborn but you are sturbborn more than her,Aydarh tace nine sturbborn? Yace aaaa ai ke you are more than sturbborn I didn't even know what to call you ma,Aydarh ta hade rai tace kaima ai daka ke daga mana shoulder,kai din ma ai you are more than sturbborn tunda nace kaidaina kula wannan matan,ka ki " yayi murmushi kafin yace how olds are you now? Tace nima bansani ba yashafa kansa yace gayamun kaman bazata ce komai ba tace 22 yace ohh kinga maryam autarh

ma ta fiki , tace ni din yace eh kinga autan gidanmu ma ta girmeki, tace kai shekaranka nawa?yace 35 aydarh ta ware ido tace 15 years ke tsakanin mu? Malik yace ehhh time din da aka haifeki,I finished my junior secondary school, kuma duk da haka sai da na zama babba kafin, nashiga school, Aydarh batace komai ba ta cigaba da abunda takeyi,dandanan suk agama hadaddan white rice da stew din da salad din malik yayi gwanin sha'awa sai da suka gyara kitchen din, kafin yawuce parlor ta fito da abinci tayi serving din sa,itama ta zuba kadan sai salad din da ta zuba sosai kallon abinci yayi bai ce komai bay asa serving spoon yabude warmer farin shinkafan ya kara mata, ta dinga binsa da kallo kafin tace nin ace zan ci dayawa 'yahade rai yace ni nace kuma dole sai kin cinye, kaman zatayi kuka tayi kasa da murya tace amma sir ka duba yayi yawwa fa, malik yace I know just it you can finished it all bana son rashin cin abincin nan, tace so kake nima nazama katuwa kaman kai yabude ido yace daman ni kato ne ai ban sani ba, taware ido tace hala baka duba mirror ne ma? Yace aaa bana dubawa amma indai na kaiki na yarda ni kato ne, tace Wallahi ni am not fat kowa ma yasani aie, malik yace kema bakya kallon mirror, aydarh na kallonsa tace ina kallo manah, yace dubi nan king ani gashi babba yafada yana nuna direction din boobs din ganin inda yake nunawa tayi maza tayi kasa da kanta kafin ta dauki plate din abincin ta mike kaman zata tashi sama ta wuce bedroom har tafara hawaye, malik yabita da kallo har tashige kafin ya girgiza kai yacigaba da cin abincin sa.

Yace tau shi malamin ne yace ba daidai bane tace ah'ah shi fa bahaka yace ba cewa yayi nakara daga yarda yabani din waye ya koyamun malik yace sai kika ce waye tau?tayi shiru tana wasa da nails dinta tace cewa nayi kaine yace so nake ki maimaita mun yarda kikace masa tace cewa nayi yayarh na ya koyamun shine yace bani da aure ne?nace ah'ah,malik yace kinyi shiru ki cigaba, tace ce masa fa nayi kaine yace nine wa? Tayi kasa da murya tace mijina malik yayi wani cute smile yana shafa sajansa yace tau ai kinyi kokari Sosai tace Dan Allah fa ?ya girgiza kai yace sure tace nagode kaga gobe Sunday akwai kuma wani littafin zamu bayar goben yace tau bara nadawo masallaci sai muyi tayi shiru kafin tace yau baza kaje wajan kallon kwallon ba? Yace aaaaa shima dr ibrahim din mura yakeyi bazai je ba aydarh tace eyyerh har ya kusa fita kafin tace sir yajuyo yace ma ta rage murya tace yaushe zamuje wajan auntie hibban?malik yace can din mi akeyi? Ta girgiza kai tace babu kawai I wanted to see her,malik yace barana is there turn now ai mune mu kaje last kibari idan sun zo kinganta,batace komai ba ta juya tafita shima yawuce masallaci jin har an tayarda da sallarh, itama daki ta

wuce tayi sallarh anan saman prayer mat take bata tashi ba har yadawo,littafin ta dauko suka fara karatun, basu jima suna yi ba, ta haddace ya zauna akanta har mamaki yakeyi idan yana koya mata abun sharp sharp take rikewa, murmushi yayi yace sake yi naji,babu wani mistake ta sake biya karatun dayayi mata kafin yace that’s my gurl ki cigaba da yi har time din dazakiyi bacci zanje na kalli ball din online a waya yanzu tace alright yace sai da safe yace sleep like a new born baby,wani cute smile tayi tace I will, kofan ya rufe ya fita. dasafe ma ruwan tea kawai suk asha sai irish zuwa yanzu tayi noticing baya zuwa aiki tana so ta tambayesa amma bata san abunda zatace masa ba,har bakin gate yarakata yau a kafa sukaje duk da bawani nisa sosai amma sai sannu yake mata yasan bata taba tafiya irin haka ba da kafa, a bakin gate din suka tsaya baya barin tayi late shiyasa time din dasuka iso lokacin sauran students ke ta zuwa “kallonshi take da farin idonta dayasha kajal dake cikin nikkab kafin tace sir wajan aiki zakaje,ya girgiza kai yace no tace tau miyasa? Yace ai mutunmin yayi tafiya batace komai ba tayi shiru kafin yace idan antashi kaman jiya sai nazo mudawo tace alright, har zai tafi sai gasu maman noor da maman baffa,jiya yafara ganin su din da haka bai wani gane su ba hade baki sukayi wajan gaishe sa,ba yabo ba fallasa yace lafiya “yafada yana ce mata sai nadawo ayi karatu yafada yana mata waving hannu shima tayi masa su maman noor baki bude suke kallon su kaman zasu hadiye su tsaban kyau da haduwan dasuka yi tareda da Aydarh su ka shiga class din sit din datafara zama ranar daaka kawo ta shine har yanzu yama zama permanent sit dinta ita kawai ke zama front sit din , maman noor ta zauna a sit dinsu tana kallon maman baffa tace Wallahi fa lamarin yafara firgitani maman baffa tace mi kawata? Maman noor tac eke mutanan nan fa ba kananan masu kudi bane Wallahi Maman baffa ta sauke ajiyan zuciya tace gashi duk irin bugun cikin da zamuyi ma yarinyarta can bata bamu amsa “ ni fa abun nan na daure mun kai kiji haduwan mijinta fa Kamar irin bai saba da rana ba kullun rayuwarsa cikin a,c yake kuma sau dayawa a keke fa zuwa balle nace ko yanada mota Wallahi bashi da mota,maman baffa tace ai shine kawata kodai tun tabayin kudi suka talauce ne? Maman noor tace aaaaa gaskia ke kam baki da id oki duba fa har yanzu skin dinsu na nuna alaman kudi da hutu bugu da kari wani irin nutsuwa kamewa da kuma aji, ki dubi fa flat shoe din datake sakawa na islamiya ma ta mayarda su naga kullun dasu take zuwa kunsan 38k fa suke, kuma ma a kanon nan bazaki samesa ba sai dai kiyi order lagos kuma ki sake bata kudin shipping ga kudin shipping yafi na products din,’maman baffa tace eh fa kawata yanzu ta miye abun yi maman noor tace Allah kabashe maman baffa tace Ameen Ameen, sun dai kasa dauke ido kanta sai faman kallonta suke ,itace ta farko wajan bayarda da

hadda,malamin yace kinyi kokari malama Aseeya a sake dagawe ALLAH YAYI albarka tace Ameen , line by line aka bi har yagama karba kafin ya koya saboda lokacin tashi daya gabato Kamar kullun ma yau tun anan ta iya larabcin hausan shine ke fassara mata shi.

Yau ma kaman kullun tun kafin lokacin tashi yayi yakara so anan office din headmaster yazauna har sha biyun yakarasa,bakin gate ya koma ya tsaya kasan wani bishiya yana jiran ta,tare da su maman noor suka fito sai faman labarin da ba kai ba kugu suke hadda cewa ai zasu zo gidanta ita dai aydarh batace komai bat ace Allah yakawo ku lafiya can ta hangosa kanshi kasa yana taba wayarsa,ahankali tace masu maman noor sai anjima “maman baffa ta washe baki tace yar gata ai shi can na hango ohhni bazai ma iya bari ki koma da kanki ba tsaban soyayya, maman noor tace kedai bari kawata amma ki jira nan da anfara yara duk sai abun yaja ba,ita dai batace musu komai batayi gaba tana amsa bankwanan dasuke mata sai kuma next week, tana karasowa gabansa ta dauke nikkab din duk tayi sweat a forehead handkerchief yafido daga aljihunsa yana goge mata kadan kadan tareda hura mata iskan bakin sa,lumshe ido tayi sosai take jin kunya saboda har yanzu baa karasa watsewa ba a bakin gate din dasauran few students wanda cikin su hadda su Maman noor waenda daman ladan su anan suke zubar da rabi da quarter saboda sai an tsaya gulma kafin a tafiya,yarda ta lumshe idon lashes dinta “kaman irin an kara sun kwanta sosai yarda shape din idonta yake yana tafiya da imaninsa kusan 3mins suna ahaka kafin ya dauke,itama ta bude ido tana sukunyan da kanta kasa, keke ya tarar musu sai dasuka tsaya yasiya few ingredients din dabasu dashi kafin suka wuce gida, a kofan part dinsu suka tarar da rabiah zaune hannunta rike da warmer tasha wani shadda duk yaji ruwa ga ubansu dauri da calaban attach blue da green tayi kaman irin karuwan nan,tana taunar chewing gum “ Aydarh ta tsaya tareda kare mata kallo,ledan dake hannunta ta mika masa “kaman wani yaronta haka yasa hannu ya karba, cikin wani irin tone, tace you are stupid and you most be stupid ma,I thinks I have passed this to you time without numbers you should start out of him, and you refused ta dawo daidai side dinta tana kallonta cike da raini kaman taka abun kyama tace , idan kina neman sa kibari yafita kar na kara ganin waennan kafan naki a apartment din nan “Ramlah ta dankaro wani uban zagi ta maka wa Aydarh,duk zagin da hausan yayi girma amma ba karamin ciwo abun yayi mata “cikin wani Irin voice kaman Asad (na cikin auran ajiya) ya kira sunanta ranshi yayi masifan baci ba Ramlah ba hatta Aydarh sai da gabanta yawani fadi ganin yarda cikin few seconds yakoma haka kaman lion, idonsa har wani wuta wuta yake alaman ran maza ya baci (Nagode mijin

ASSEIYERH) yace how dare you! Do you know who is she ?kinsan abunda kikayi yanzu kam,idan baki bar gurinan ba I can remove out the stupidity out of your head “Wallahi Ramlah har kyammar take ta gudu ta kwashe warmer dinta ta fice ya kalli aydarh kafin yasa hannu zai riko nata hannu ta kwashe tayi baya tareda fashewa dawani kuka cike da shagwaba, har wani Jan lumfashi take alaman ranta ya baci, kaman zai yi hauka haka yakara matsowa kusa da ita tasake zillewa,ahaka Allah yabashi daman ya cafko ta yariketa gam kafin yasa key yabude kofan suka shiga ya rufe anan ya ajiye abubuwan hannunsa still kukan take wanda yake jin sa har cikin ransa, bag dinta yasa hannu yacire kafin yakarasa cire nikkab din, hannunsa yasa ya kwashe hijab din, yau batasa hula bas ai hadddan gashin kanta nan tayi parking can keya tare mashi wani style a ribbon, camisole din uniform din ce jikinta sai black lace foam bra dake jikinta wuyan ba babba babe shiyasa baka iya hango bra din said ai hannunta ,ta shoulder dinta kama ta yayi suka zauna, Still kuka take tak’I yarda su hadda ido,shi bai masan abunda zai ce mata ba can yace kiyi shiru bana son kuka, batayi shiru ba ta cigaba,yasake cewa kije kiyi wanka ki fito muyi girki nan ma batace komai ba shima shiru yayi yana kallonta can yace mi kike so kuma?sai sannnan tayi magana kaman wata yarinya tace to ni sai karama mun “yarda tayi maganan yasa shi jikin zaiyi loosing control daf ya daurata kan laps dinsa yace mi zan rama maki? Ta tasake fashe masa dawani kukan tace hala bakaji ta zageni ba? Malik da hannunsa ke kan shoulder din bayan yagama jin ta yace shknn abunda kike so? Ta gyada masa kai yace tau shknn anjima idan nafita sai na rama maki,tayi sauri rike hannunsa dayake mata tafiya dashi a shoulder tace saidai mutafi tare ka rama mun gabana yace mata tau shknn yanzu tashi kije kiyi wanka tace to”har tamike zata tashi daman she is not comfortable zaman datake a laps dinsa ,yayi sauri yadawo da ita bayanta ya dage chest dinsa tayi yar kara duk da shi yakamata yaji zafi,tana wani zaro ido take kallonsa hannunshi yasa yana kokarin sauke mata rigan ta sama gabanta ya yanke yafadi tana wani irin kyamar take hanashi ga magana malamin su da kuma auntie hafsa na mata yawo a brain da kums ears dinta, kyamar take kaman mai jin sanyi shikam yayi alkawarin sai yasake kallo yau din nan, gently yake sauke hannun camisole din dake nan kaman na vest, kaman mai tsoro yake saukewan har yagama ta kulle idonta gam tana sauraron ikon Allah, duk yabude yake kallo ko dauke ido babu,kaman zai hadiye ta saboda kallo, har yana iya jin yarda gabanta ke faduwa,dasauri dasauri,cike da dauriya da karfin hali ta tashi ta banka daki da gudu ko bag din da hijab bata tsaya dauka ba, tana shiga tasa key tasake fashewa da kuka kaman wace aka daka, kusan 10mins tana nan tana kuka,kafin can tayi gathering courage din ta mike tashiga toilet din sai

datayi wanka fess kafin ta dauro alwalla kasancewan azahar tayi, saidai ta shirya kafin ta saka hijab ta tayarda sallarh time din data gama ta bude kofa ahankali tasan bai dawo daga masallaci ba dasauri ta wuce parlor ta dauko bag din da hijab ta gudu ta dawo bedroom ta rufe.

Hibba ta dinga kallonta kafin tace shi yayah malik din bazaki yi masa magana ya baki ki rani ba?aydarh tace ah’ah fa ai daman yace mun Doctor yace zaku zo, hibba tace nima dayayi fixing ranar ji nayi kaman na jawo ta Wallahi ganin nayi Wednesday din nan taki zuwa, aydarh tayi murmushi tace sai gashi tazo, Aydarh tamike zata shiga kitchen hibba ta bita da kallo tace amarya amarya “Aydarh tawara ido kafin ta juyu tana kallon hibba tace ai ke ce amaryan bani ba ,hibba tace aaaa har yanzu fa naga kina wani glowing kalan na amare,kuma idan nace ciki ne kice bahaka ba, aydarh tayi murmushi tace ah’ah fa Allah ai muje ance bahaka bane,tafada tare da yin saurin shigewa kitchen,hibba ta girgiza kai ita har mamakin Aydarh ma take wannan wani irin kunya ne har haka,bakaramin kyau bubu gown din jikin Aydarh tayi ma hibba bad uk da ansaka mata itama sai colors din ba daya ba,hibba tace daman yazaayi ka dinga hadda kanka da ita Allah natuba,kafin kuma ta cigaba da bin parlor da kallo tana mamaki yarda akayi ba furnitures girgiza kai tayi wani zuciya nace mata ke ina ruwanki, aydarh ta fito hannunta rike da tray ta jera da abinci a sama,gaban hibba ta ajiye hibba ta dinga bin tray din da kallo fried rice sai coslow sai fruits da akayi slices kanana an zuba madaran ruwa kuma ba fruits salad bane, hibba tayi murmushi tace wannan irin lunch sannu da kokari aydarh ta koma kitchen ta fito da plate din ruwa ta ajiye kafin ta zauna tace auntie hibba kici manah,hibba na murmushi tace yanzu kuwa, hibba tafara cin abinci yayi dadi sosai tana ci kadan kadan suna labari, sai da ta kusa cinyewa kafin ta ture tafara shan fruits din,can hibba tace daga masallacin fa basu dawo ba, aydarh tace erh maybe ko sunje wani wuri ne hibba ta gyada kai tace ai kwara su barmu muyi fira wani class nashiga abun baa cewa komai Aydarh tace kai haba?mi ake koya a ciki? Hibba tace bara dai kigani tafada tana unlocking wayanta tashiga Whatsapp, aydarh ta dinga bin wayan da kallo normal iPhone X dashi auntie rufaidarh ke amfani har aydarh na mata dariya wai ai bawaya bane, rufaidarh nace mata Erh ba komai da ita dake iphone 15 din da ita dake iPhone X din duk dai ai sunansu iPhone, hibba ta dinga nuna ma aydarh lectures din group din duk kunya ma wani abun ke bata ita dai tama kasa kallo da kyau itakam hibba sai faman zuba sharhi take tace kinga wannan Allah yau ki ruda yayah malik dashi zaki gani,nifa jiya Doctor hadda su kukansa da kyar nasamu muka fito saboda yace yau ba fita Aydarh ta sukunyan da kanta, tana wasa da yatsun hannunta, hibba tace

tau ai nan fa kullun sai an chanza salo kala kala kullun da style din daake koya manah Wallahi,Aydarh tace waii hibba tace wai kau kin tambayesa abunda ke tsakaninsu da yarinyar nan rabiah kau? Aydarh ta girgiza kai tace ah’ah “hibba taware ido tace dan Allah wai?aydarh ta gyada kai tace mantawa ma fa nayi amma zan tambayesa yau hibba tace kwara dai tun wuri mu sani saboda ba hankali ned asu ba kawatan ma miye sunanta bilki naga tana wani shigewa Doctor tau ni daga shi har ita baraga musu zanyi ba domin bazan iya sharing likitana da kowa ba “Aydarh tayi dariya tace ah’ah fa auntie hibba kishin yayi yawa, tau ita wacce kika fada din sonsa take ko miye? Hibba tace bandai sani ba tunda shi dai daga amsa gaisuwa baya kara ko kallonta kawai dai ita naga duk wani take taken ta ,Aydarh tace I didn’t know exactly what wrongs with others girls head,you should be a girl with mind a lady with class and a woman with attitude manah,hibba tace Wallahi kau kedae bari, ke dakika cika mace ke kika san wannan su ai basu sani ba,Aydarh tayi shiru kafin tace su suka sani aie,hibba tace Wallahi.dr ibrahim yayi shiru har malik yakara kafin yace kana nufin ita bata sonka komai? Malik ya girgiza kai yace I didn’t know what’s in her mind amma nidai san tunda akayi manah aure bata taba cewa tana sona ba kuma bata taba cewa bata sona kawa isai naga kaman soyayyyan yan uwanta take mun, kawai dr ibrahim yace tau ya akayi aka hada ku auran?auran hadi kenan komai? Malik ya girgiza kai baya son yafada wa wani sirrin su yace aaaaaa ni nasamu ummina da maganan ita kuma tagayawa abban mu shi kuma yace ayi manah aure kawai, dr ibrahim yace ita da aka gaya mata batace komai ba kuma? Malik ya bude hannu yace bata ce ba, dr ibrahim yace ko kuka ko wani abu irin alaman ta bata sonka,malik yace tayi kuka dai amma nafi tunanin na rabuwa da gidan e , dr ibrahim yace tau dakaje mata da bukatan mu’amulan aure ta yarda?malik ya gyada kai baya son ya nunawa dr ibrahim din ba abunda ya shiga tsakanin su, dr ibrahim yace kace idan taga kuna magana da Ramlah take ko wa tana fushi malik ya gyada kai yace eh dr ibrahim yayi murmushi yace tau ga sauki nan malik yace kaman ya?dr ibrahim yace kayi amfani da Ramlah wajan gano tana sonka malik yahade rai yace ban fa gane ba, dr ibrahim yace kayi kokari ko yayane kana nunawa ramla soyayyya ka nuna soyayya kuke kai da ita har waya ku dinga yi ko a gabanta ma ka dinga nuna zaka aure Ramlah ya dinga yabonta kana nuna irin yarda take sonka, cikin few weeks zaka fahimce abunda nake nufi and you will Appreciate my idea malik yayi shiru kafin can yace kana ganin wannan hanya zaiyi aiki kam? Dr ibrahim ya gyada kai yace in sha Allah just try and see malik yashafa kanshi yace tau shknn but I deep inside bana son naga fushinta fa dr ibrahim yace nasani kawai ka daure a na yan weeks ne kawai malik yace tau shknn mu wuce yanzu gidan mu ci

abinci sai mu fita ai sai dare zaku koma ba? Dr ibrahim yace eh gidan suka wuce anan parlor suka zauna aydarh tayi serving dinsu abinci kafin aka cigaba da fira ita dai Aydarh batace komai sai dan smile datake sai kuma Erh ko ah’ah ko uhm can malik ya kalleta yace hajiya abinci fa? Tace naci hibba tace aaa fa auntie aydarh baki ci ba fa, malik bai ce komai ba ya zuba abinci a plate ya tura mata gabanta yace eat batace komai ba tayi kasa da kai ta dauki spoon din tafara ci kadan kadan rabi taci ta ajiye ya dago yana kallonta kafin yace finished it all kaman zatayi kuka tace na koshi basake magana ba yasaka mata fruits din ya mika mata yace wannan kam sai kin shanye shi tass, su dr ibrahim dai sai kallon ikon Allah suke.

Suke abinci take ci duk a takure saboda bakaramin yawa yayi mata ba dr ibrahim yace wannan ma har kasa ta kware ai,malik yashafa kansa yayi shiru bai ce komai ba, hibba tace ohh Doctor,komai sai kayi magana fada tana dariya giransa ya dage mata yace ai dole yasa yarinya gaba da kallo ai sai ta kware ma wannan, aydarh tawani langaban da kai tana kallonsa kafin murya can ciki tace nakoshi fa bai ce komai ba yasa hannu ya dauki plate din yahade dana su wanda suk agama ya kai kitchen warmer ta dauka da bowl din ta bi bayansa,tana shiga ta ajiye kafin tace fita zakayi sir?yace Erh ko mu zauna ta girgiza kai tace ah’ah fa har kwara ku fita yace daman mu ma bamu ce zamu zauna ba ‘har yayi hanyan fita ta jawo sa yana kallonta ko kiftawa babu yace mi kuma? Tana hade rai tace to kaganta?yabude ido yace wa? Tace ita wannan din ya girgiza kai yace aaa ban ganta ba,munyi waya dai tace mun zataje lalle,Aydarh tace lalle fa kace ohh har digits dinka ma ne da ita yace eh mana yarinyar da zan aura yazaayi tarasa digits dina Aydarh ta tabe baki tace Allah ya kyauta kam,yace Ameen yafita ta kusan five minutes kafin ta bi bayansa dr ibrahim har yadawo kusa da hibbansa yana nuna mata abun a waya malik nafitowa ta dan bada distance tsakaninsu,malik dai yazauna inda ya tashi can aydarh tafito,malik yamike yana zuba hannunsa a pocket yace ma dr ibrahim ai sai kayi mata sallama love wins mu tafita koh,dr ibrahim yace ai sallaman nake mata ka fito, malik yakalli aydarh kafin yace anything before I go? Ta girgiza kai ba kallesa ba tana kallon wani direction daban,murmushi yayi kafin yace amarya mu mun fita hibba tace Allah yatsare ga amanar Doctor nan banda kallon mata please duk macen da ta kallesa kayi making sure yayah malik ya dinga istigifari kenan har ku dawo, malik yayi murmushi yace alright madam “ angama in sha Allah,dr ibrahim yabude baki har sai data gama kafin yarufe yace ai ni duk duniya bayan ke da iya bana ma sauran kallon mata kin sani ai, hibba tayi wani murmushi tace yes my Doctor ,dr ibrahim yakalli aydarh yace madam ke bazaki bani amanan ba?Aydarh ta girgiza kai murya can

kasa ta kalli malik tace “Aji tsoron Allah “ malik mamakinta yakashe sa yasan inda magananta ya dosa “baice komai ba yafita dr ibrahim yabi bayansa yana masa dariya ,hibba tace amma kin bani dariya wai aji tsoron Allah duk kishine haka? Aydarh ta sukunyan da kanta bata ce komai ba.suna fita dr ibrahim yace kai mi kafada mata yanzu? Malik yace cewa nayi wajan lalle zan tarar da yarinya shine ta bata rai fa,dr ibrahim yayi murmushi yace ahankali ahankali komai zai daidaita in sha Allah yauwa maganar aikin har yanzu shiru wai? Malik yace tau yace nabashi time amma har yanzu bawani feedback dr ibrahim yasauke ajiyan zuciya yace Allah yabamu mafita malik yace dr ibrahim yace tunda muke tare yallabai baka taba bani labarin course din dakayi ba,malik yayi murmushi kafin yace ranka dade ai kaine baka tambaya ba so I even thinks you didn’t want to know,dr ibrahim yace kawai dai zancan ne bai zo bas ai yanzu,malik yasauke ajiyan zuciya kafin yafara ba dr ibrahim labarin schooling dinsa tunda yafara dr ibrahim ke kallonsa har sai dayakarasa kafin ya mike yayi saluting dinsa yace due to all respect sir I saluted you,for your field and I saluted for your result yace da dan karfi and I saluted you for remark yallabai kafin ya ba malik side hug sukayi hand shake dr ibrahim yakasa dauke idonsa kan malik mamakinsa na neman kashe sa,yayi wannan babban course din amma ya tsallake yazo yana aikin gini ba karamin tausayin malik din yaji a yau ba ,har wani irin girman malik din yaaji yakaru a ransa cikin da respect dr ibrahim yace yallabai amma da irin wannan result din kake haka? A kasan nan kasan baku da yawa kam? Anfiye tafiya can waje ayi shi kuma asamu aiki can nan Nigeria munyi lacking irin wannan field din can kwananki anguwarmu akwai wani babban likita a can cairo nasamu labarin yazo yana karban credential din mutane duk masu degree a medicine kaman mu,mun kai amma saidai ba abunda yake bukata ke nan ba, yanzu gashi Allah yakawo amma malik ya koma yanzu fa gashi bansan hanyar da zaa same sa ba, malik dake kallon dr ibrahim ko kiftawa babu yace kaga ibrahim zauna dr ibrahim yazauna kusa da malik still idonsa na kanshi yace ka kwantar da hankalinka this my seventh year of graduating, babu aiki kasan anan sai idaan kasan wani,wani yasanka kafin kasamu offer lets keep praying buddy in sha Allah komai zai wuce dr ibrahim yace hakane yallabai amma sai idan babban macuce za ka kai wannan takardun naka yak’I daukan ka aiki, kafi karfin aiki a clinic yallabai da sai nabi duk hanyan da zan bi wajan ganin nayi ma Doctor magana “malik ya girgiza kai yace don’t mind ibrahim komai zai wuce yeah,dr ibrahim yace sure “ malik yace kasan miye babban abunda ke damuna? Dr ibrahim ya girgiza kai yace karatun yarinyar nan ban taba jin tausayin kaina ba sai yanzu ibrahim ashe akwai ranar da nauyin wani zai hau kaina dole dole “dr ibrahim ya dinga kallonsa kafin yace mi karatun

nata yayi malik yace,nayi alkawarin sai ta karasa karatun ta in sha Allah kullun saka nake da warwara amma har yanzu I have no way out ibrahim,dr ibrahim yayi shiru kafin yace mi take karanta ita din? Malik yace pharmacy and technicals dr ibrahim yace eyyerh ina ga akanon nan ma akwai university da akeyin sa? Malik yace ni kai ina tunani course din baiyi yawa haka ba, bako ina aike yinsa ba dr ibrahim yace kwananki muna labari da Doctor yake gayamun zasuje polytechnic can katsina za'ayi introducing course din I thinks can anayi amma diploma ne, malik yayi shiru yace ibrahim idan so samu ne nafi son tayi degree ko ta karasa can inda tafara dr ibrahim yace in sha Allah yallabai da wannan karatun naka you will faithful all your ambitions and you will remember my words malik yayi murmushi bai ce komai ba tunani kala kala ransa "he wish he could see his family ko sau dayane a wannan halin lumshe idonsa yayi kafin yabude ya tsinci kananun dutsi,yana jefawa kusa da ruwan dasuke, dr ibrahim yana kallonsa tausayin sa har yayi masa yawa he wished zaiyi iya yin wani abu amma in sha Allah sai yasan yarda yayi yasamu labarin Doctor usama,can malik ya jefa last stone din dake hannunsa ya kalli dr ibrahim yace ibrahim dr ina zan samu guitar please dr ibrahim yaware ido yace jita jita dai wacce nasani malik yashafa kansa Still idonsa kan dr ibrahim yace eh ita dai a ina zan samu dr ibrahim yace kai kam mi zakayi dashi ko kana waka ?malik ya girgiza kai yace aaaa waka kuma,ko waka daya ma na masu waka ban iya ba balle ni nayi kawai dai I likes playing guitar ne dr ibrahim yace tau tashi muje wajan saeed he is one of my friends nasan yana waka kuma yana business irin haka so definitely nasan zamu samu a wajansa bama sai kasiya ba kawai zan karbar maka saboda yanzu nasan yayi tsada ma ,malik yayi shiru kafin yace muje tau a keke? Dr ibrahim ya ce babu nisa daga nan zuwa studio dinsa so we can treak by our foots malik yace "okay" daga haka suka wuce,cikin few minutes suka karaso babban studio dialing number sa dr ibrahim yayi yace yana bakin studio dinsa ,guy ne dogo bakin yayi styling hair dinsa irin na yan wankan nan welcoming dinsu yayi tareda yi musu iso suka shiga ciki sai da suka gaisa sosai kafin dr ibrahim yayi masa bayanin abunda yakawo su saeed yayi murmushi yace aikam akwai kasan baa rasa nono a riga wani haddadan karamin guitar saeed ya dauko yamikawa, malik karba yayi yana binsa da kallo kusan irin nasa na gida, sai dasuka sha fira kafin malik yasake godiya suka wuce, dr ibrahim ya kalli malik yace to yallabai ai sai kayi playing naji ko,malik yayi murmushi kafin yafara playing jitan kadan kadan ahankali,kidan mai siring dadi babu wani kara sai sound din mai kwantar da hankali ,kusan 10 mins yana playing kafin dr ibrahim yace ya isa haka ai nayi tunanin irin fa nasu yan wankan hausan nan ne ashen aka na yan gayu ne wannan ai kace mutun yayi bacci ma kawai malik

yayi murmushi yace kaga magrib yayi mu tsaya masallaci muyi sallarh kafin mu je gidan sai ku wuce ai yau kam sun sha fira,na ASSEIYARH ai tana sakewa da hibba yanda bata fa da sabo ko kadan amma naga ita sun saba dr ibrahim yayi murmushi yace ai wifey magana ba kaya ba a wajan malik yace ai ta kyauta, sallan sukayi kafin su wuce gida suna shigowa ana dawowa da nepa wanda basu ma cika dauke shi ba,sunan parlor zaune da alaman sallarh suk agama ,shigowa sukayi aydarh tasake gaishe su hibba ma tana yi musu barka da dawowa “dr ibrahim yace tau kin taso mu tafi haka nan ko na barki nan ne sai zuwa jibi? Hibba ta hade rai tace aaa sati zanyi anan katafi kace ma iyana ina gaisheta malik yayi murmushi yace tau ka tafi tace ta na nan dr ibrahim yayi shiru yana kallonsu kafin ya kalli aydarh yace kina fa jinsu ko?aydarh ta gyada kai tace erh please ta zauna bana son ta tafi nima dr ibrahim yarike baki yace tau badani ba kar a makan ta mun mata kwara natafi da abuna gaskia bazan bar ta ba, hibba tayi dare kafin ta kalli aydarh datayi da fuska kaman zatayi kuka tace kinga sorry in sha Allah ai zan sake dawowa sai anjima,aydarh tace thank you auntie hibba we really appreciate,hibba tace don’t mention auntie aydarh Allah yabar zumunci sai nazo ankarasa koya mun fried rice aydarh tayi murmushi tana boye fuskanta a hijab har bakin kofan compound din suka rakasu,kafin su dawo suna shigowa parlor malik ya kalleta yana dan yin kalan tausayi yace hajiya zan sha shayi “tawani hade rai tace a can ba kasha ba?malik ya ware ido yace ina? Tayi masa banza shidai kallonta yake ko kiftawa babu yace wai ina? Aydarh tasake bata rai tace can wajan gurl din taka dafada cike da tsiwa malik yayi murmushi yasha bread dinsa kafin yayi kasa da murya yace nasha fa kawai yanzu so nake nakara sha, kuma ma duk ta gaji bana son bata wahala ne yasa nace idan nadawo sai ke kiyi mun sharp sharp yafada yana danne dariyansa ganin yarda take kallonsa,tace to baza kasha shanyin ba yarinyar data kawo kifi,duk koi na yadauki odor,ba fish din kawai ba har ita babe din naka bad odor take fitanwa kindly inform her about unique perfumes please akwai marar sa tsada daidai na local champions irin ta, amma there are unique,ba kalan nata masu bada very bad scent,malik da tunda tafara magana yayi mutuwan tsaye yana kallonta kaman t.v idan baayi wasa ba zai hadiye yarinyar nan duk a huta she is killing him duk wani bits dinta ji yake yana tafiya da imaninsa he can lie or deny anything,he likes every bits of her, he can deny it he loves how beautiful she is “ she is real definition of beautie , tana gama maganan tayi shiru ganin kaman ma bai ji ta ba yasata cewa kafin ayi isha a gama kawuce mosque fa sai lokacin yadawo hayacinsa yabi ta da kallo ta juya har yakai bakin kofa kuma yadawo yace shayin dan Allah batace komai ba tayi shigewan ta daki ,masallaci yawuce har yanzu yakasa daina tunanin yanda take magana cike da tsiwa

ahankali ya furta yah rabbil alameen mike shirin faruwa dani ni kama yasamu kansa da tambayar kansa, sai wajan nine yashigo bai tsaya koi na ba yawuce bedroom din zaune take a katifa tana karatu tanajin sallamansa ta amsa tacigaba da abunda takeyi bata ko dago ba zama yayi kan katifan kusa da ita yana kallon littafin datake dubawa, littafin ta rufe kafin ta dago tace yau kace babu ball but you stay long a waje ‘’malik yace ai nashigo gida aydarh tace amma ai baka parlor yace ohh ai ba parlor bai na can tareda da Ramlah aydarh ta dauke kanta batace komai ba tana sake bude book dinta,yace ina shanyin tayi masa banza ganin kaman idan ya cigaba da mata zatayi masa kuka yasa shin yin shiru kafin yace ina shanyin ? Batace komai ba tayi shiru kaman bazata ce komai ba can tace ina nagaya maka kaje tayi maka shayi kuma tunda baka jin maganata duk ranar danaga umminka sai na gayan mata ,malik yaware ido jin abunda tace yace kai haba?mi zaki ce mata tau?tawani hade rai tace ai tace tabakani amana right?malik ya gyada kai yace ehh amma bai kowa yasan ban ci amanan bak oh ?aydarh ta girgiza kai tace zance mata baka jin maganata idan nace kada kay isai kayi kuma babu ma ruwanka dani ka fita am sleepy,tafada tareda zamewa zata da kwanta yayi maza yajawo ta jikin yace yau sai na maki proving nine mijinki yau sai kinsan you are not longer a child kema macen aure ne dawani irin speed take kallonsa chest dinta na over racing saboda yarda taga yayi.

Ganin yarda yarike ta din, yace sai kin gayamun,miyasa kika ce “Aji tsoron Allah !gabanta yafadi tawaro ido tace ni nace haka? Ya girgiza kai yace aaaaaa ni nace,tayi wani iri da fuska tace eyyerh ni fa haka kawai nace kuma ba ma sake tuna ma nayi ba?malik yayi shiru yana kallonta yace mikika sake tuna mun? Yafada ya saasssuta rikon dayayi mata ba komai fa “yace ohh naji tsoron Allah kar naci amanan ki naje wajan Ramlah ko?tayi kasa da kanta batace komai ba,malik yace magana fa nake dake tace Erh “yace tau miyasa idan naje yazama rashin tsoron Allah? Tace ai ba matarka bace malik yace amma ai budurwata ce ko? Tayi shiru tana sauraron sa Still kanta nakasa tak’I dagowa ta kallesa , yace kinsa yarda nake sonta kuwa itama take sona kam? Aydarh tayi saurin rufe masa baki da duk hannunta biyun tace ban sani ba and I did want to know,kuma ni dan Allah ma sai dasafe bacci zanyi kafin ta dauke hannunta daga bakinsa yace kwanta tau nima anan din zan kwana yafada ya nuna mata gefenta tawani ware ido tace Allah bazaka kwana anan ba “malik yayi murmushi yashafa kansa yace akwai rana yana fadin haka yafita yabar ta da kallonsa baki bude har yafita,yana fita tamike tasaka wa kofan key kafin ta kwashe books dinta ta mayar jikka tadawo ta zauna kan katifan, tayi tagumi “tunda suka baro gida

sai yanzu take tunanin karatun ta, ganin tunani na neman zautar da ita kawai yasa ta zame ta kwanta tana sauraron bugun zuciyanta,miyasa tayi saurin sabo dashi sabon da bayan abba da salmerh babu wanda take iya zama suyi fira har tayi dariya sai shi wani zuciya tace mata ai dole tunda yanzu baki da kowa sai shi ,tau idan dagaske yake fa idan yayi kudin zai je ayi musu auran d ita fa? Tawani tabe baki tace tau sai mi sai araba auran tunda daman ai bakwa son juna,kowa sai ya koma gidansu kawai lokacin su abba duk sun bar fushin amma kuma ai ko an raba zaki cigaba da ganinsa tunda yanzu you are families! Maida hulanta tayi kafin ta dauko pillow tayi hugging kafin ta yafa duvet ta cure waje daya har bacci yayi gaba da ita. As usual bayan sun gama gyaran gida suka daura breakfast shayi kawai suka dafa yasiyo musu bread sai eggs dasukayi frying kwana biyun nan malik duk yaji sa wani kala kaman baya bata abincin daya Kamata aljihunsa yafara yin kasa ga har yanzu bai sai mu aikin ba daman 10k ne dashi sai yahada da 20k din da Allh musa yabasa making 30k dashi ne yasiyan musu kayan abinci those days Ko fruits din ma baya wani siyan musu dayawa na kudi kadan yake siya he is just managing the situation kafin yasamu wani aikin, kamar ko yaushe shayin rabin cup ta zuba sai madaran kadan sugar kam baa magana tana son sugar sosai bournvita ma haka kallonta yake ko kiftawa babu yarda take motsa tea spoon dagani kasan hankalinta ba wajan yake ba , yace what is wrong ko bakya son shayin ne?ta girgiza kai tace ah’ah yace tau tunanin miki ke? Tace babu komai yayi shiru kafin yace tau yi break din ki ya atare zamuyi wanka to kawai tace masa ta cigaba da shan shanyin haka nan babu bread shima kallacinsa yake can takarasa sha shanyin ta sa fork tayi cutting egg din kadan takai baki sai da taci kusan rabi kafin ta ajiye zata tashi bako dago bay ace come back here and finished it all waza ki bar mawa? Kamar bazata dawo din bas ai kuma ta dawo don tasan yanzu sai yace zai dauke ta itama wannan tabatan dayake na mugun daga mata hankali ganin take har yanzun fa babu kyau kawai dai suna fada ne wannan ai mugun iskanci ne ba kaman wani lectures da tagani a wayan hibba,zama tayi Ahankali take cin kwan sai daya dauke ta kusan 25mins tana cikin waina daya na kwai time din har yagama ya kwashe nasa kayan yakai kitchen yadawo yazauna yana taba wayarsa kawai, ganin tana daukan lokaci har kwan ma yayi sanyi yace idan bakiyi sauri ba zan dura miki abun nan,aikam kaman jira take tayi saurin cinye last cut din kafin ta goge lips dinta da tissue dake nan gefen su a parlor, kafin tamike takawai plate da fork din sai cup da bread din kitchen tana shiga ta hada danasa danata ta wanke tass kafin tasa karamin towel ta sake goge sink din da ruwa yabata kafin ta fita bedroom ta wuce tana fito da kayan dirty ta duk da ba su dayawa ana daga suma kamshi kawai ke tashi (lemme use this opportunity

please and please kuyiwa mahammada rasulilahi S.A.W ko baku da kudin perfume ku din shafa alimun na naira hamsin ya isa yana tsane zufa please, damsel zata baku labari saura kadan tayi barin dan cikinta a wani event damu kaje jiya tsaban an gigita da odor) yana ganin tashiga bedroom yatashi shima ya bita yadinga binta da kallo watau taji yace zasuyi wanki tsaban miskilanci ne yasa tayi masa banza baice komai ba ya dauke kai ya bude inda nashi suke, yacigaba da fitowa dasu, har sai daya gama time din itama tagama, toilet din ta yawuce yadauko buckets sai soap wanda can suke ajiyewa daman can gida yasaba wanki da fizz shiyasa ma dasuka zo nan shi yake siyowa (shima fizz baya da tsada a taimaka yan uwa Wallahi har wanka ana yi dashi shima yana taimakawa wajan yaye odor) kanshi yadaga yana kallon very clean and attractive brassiere dinta dake wanke kal tayi hanging dinsu a nan toilet din murmushi yayi shafa kansa kafin yasa hannu ya jawo su ya dauki bucket din da soap din yafita, yana fitowa ta lura da abunda ke hannunsa ai dawani irin speed takarasa gabansa ta sa hannu ta figze kaman zatayi kuka ta mayarda su bayan ta “malik yabude ido alaman bai ma gane abunda take nufi ba yace ko wanki nace miki zaayi ba? Tayi masa banza yace ko bazaa wanke su ba su? Sai sannan da muryanta har yayi na kuka tace ai dai kasan a wanke su ko,malik yabude hannu yace aaaaa relax hajia kar kiyi mun kuka a ina nasan kin wanke su nayi tunani ai bakima iya wanki ba shiyasa nadauko sai mun wanke,har kwalla ya kawo idonta tayi gaba zata mayarda su toilet din tayi hanging tace daga yau karka sake taba mun,yace Alright booby girl!! Ai har kusan faduwa tayi jin abunda yace aikam da mugun gudu ta kwasa ta shige toilet tana shiga ta fashe da kuka kaman irin sai daya sharara mata mari,ya lura wannan yarinya tafisa fitina rigima gareta da shegen shagwaba sai ka rantse kace she is 15 wani yarinyar ma yar 15 tafita wayyo bazaka tabawa cewa tayi ashirin da biyu ba,kawai dan Allah yayi ta hakane and she deserves to even do more than this duk wani gata na gidan duniyan nan babu wanda bata gani bah, girgiza kansa yayi kafin yadauki veil dinta yakai a nose dinsa lumshe ido yayi yana jin wani irin precious air na bi ta koi na a dakin he is mad akan kamshin nan nata yana son kamshinta fatar take ke very warm gawani natural scent mai yin kaman tana using da rose yana sa shi jin wani iri duk sanda suka samu kusance da juna “ tunda take kukanta yana jinta taki shiru kuma taki fitowa ita kunyar ta daya dayace mata booby girl,bakaramin kunya yasata ba,ganin taki fitowa yasa shi yin knocking tana jinsa tayi masa banza ta dinga zubawa kofan harara kaman irin shine a tsaye wajan,can yace open the door, nan ma tayi shiru kafin yace tau ai shknn bara naje sai ita Ramlah ta tayani tunda ke bazaki fito ba tanaji abunda yace tayi saurin bude kofa, tana kallonsa da fuskanta dahar tayi ja tace Wallahi bara ta taba kayana ba balle

naka ma, idan bahaka ba I will beat her blue and black Allah, malik yayi murmushi yace tau kiyi hakuri yanzu mu tafi can ventilation sai muyi wankin ko? Aydarh ta gyada masa kai shi yadauki kayan dukka ita ta dauki musu bucket da soap, nata aka farawa da ya wanke sai yasa mata yayi tunani bata iya bas ai gashi yaga tana yi , har suka kusa gama nata babu mai magana cikin su amma there looks good kallo daya zakayi musu ka kasa dauke ido can yayi kasa da murya yace ashe kin iya wankin?ta dago tana kallonsa kafin tace erh yace kinyi kokari tayi murmushi kallonta yake ko kiftawa babu yace bana son asaka hakuri amma your own looks cute tayi murmushi tace thank you hakurin gwal din yasake kalla wanda yazauna mata dass a jerin white teeths dinsan sai shine shine yake sau dayawa idan tayi dariya yana so yayi magana shiru kawai yake can dai suka karasa nata ya kwasa ya wuce can bayan part dinsu zai shanya shanya su yayi kafin yadawo yana dawowan yace tau kiji ki huta sai na karasa nawa ko? Ta girgiza tana wasa da foam din dake cikin bucket dinta tace ah’ah zanyi “yayi shiru kafin yace okay wankin suka cigaba dayi babu wanda ke magana a cikinsu kowa da abunda yake ransa sallama akayi suka amsa dr hafsa ce tsaye suna hada ido tayi murmushi tace yau wankin kauna ake tau sannunku malik na murmushi ya amsa gaisuwan datake masa kafin Aydarh tace welcome auntie ina kwana? Dr hafsa tace lafiya alhamdulilah ya gida? aydarh tace lapia lau “kafin ta mike tana wanke hannunta tace ki shigo Auntie dr hafsa tace aaa kawai tunda mun gaisa bara na wuce ai aiki kuke, malik yace no sai fa kin shiga ai mun kusa gama ku shiga kawai nakarasa aydarh ta bude kofan babu yanda dr hafsa zata iya haka tashiga anan parlor suka zauna Aydarh nasake tambayan dr hafsa ya jikinta ina inna? Dr hafsat ace naji sauki sosai Aydarh ina na nan lafiya tama tafi kasuwa maybe yau ma ku ganta saboda naji tana cewa yau bazata kwana bata shigo ba “kwana biyu bata ga audu ba kila ke kika hanasa zuwa Aydarh tabude ido sosai kafin tace ah’ah auntie Wallahi bani bace,banma san yadaina zuwa ba tayi hakuri “dr hafsa tace ahtau idan tazo dai sai kuyi mata bayanin komai kenan Aydarh ta mike tana cewa Allah yakawo ta lapia shiga tayi kitchen ta fito hannunta rike da plate sai pure water biyu akai ta ajiye gaban dr hafsa,dr hafsa nayi mata sannu ta dauki ruwa daya tafasa tana sha,.hibba tayi shiru kafin tace tau yanzu wa zakayi wa maganan kasan yarda zaka samu shi Doctor? Dr ibrahim yayi shiru kafin yace akwai wani yaron gidansa abokina na ne munyi dinki shago daya kafin yasamu aiki a gidansa nikuma nakoma clinic duk karshan wata yake zuwa kano saboda Doctor usaman yasa mar masa aiki a can wani babban private hospital a lagos in sha Allah idan yazo komai yake nan nayi tunani abunyi,hibba ta gyada kai tace nan da kwana sha daya kenan? Dr ibrahim ya gyada kai tace tau Allah yakaimu lafiya asa

munada rabo baki daya dr ibrahim yace Ameen wifey “kafin yawani marairaice fuska yace massage please,batace komai ba domin tasan abunda yake nufi hannunsa kawai takama suka tashi, anan bedroom suka zauna kan gado hibba ta cigaba dayin ta mijinta, kafin kuma suyi tafiya can.bilki ta dinga kallon rabiah ko dauke ido babu batace komai ba rabiah tace kiji wani iskanci niga banza sai surutu nake kinyi mun shiru bilki tace aaaaa wai ai jirana nake kigama tunda na lura kaman kin fara samun damuwa a kwalwa,rabiah tayi wani zagi tace ban ma gane ba mikike nufi ne?bilki tace rabiah banda mu bamu san ciwon kanmu ba kawa isai muje mu kama masa mata mu daka tsabar ke baki da kugu ke kanki dakikayi maganar kinji abun ya hau daidai fisabillahi?rabiah tayi shiru tana kallonta,kafin bilki tacigaba dacewa yoo ko shi bai ce manah komai yayah ibrahim bazai ya hallaka mu ba har lahira “balle wannan bawan Allah da idan kika yana kallon matar sa kamar ya afka mata jikin jamaa ke kalan jikinta ma yayi maki kama da jikin da ake duka?tau idan baki da lissafi ni inda shi babu ruwana kawai kibari mu samu kudi sai a koma wajan malam muga abunda Allah zaiyi,rabiah dai tayi shiru amma bakin ciki kamar ya kasheta so tayi suje su chanza mata kama ko kila ko sau dayane ya kalli ita rabiah da idonsa ko sau dayane tunda duk wani magani data karbo baya aiki har kudinta ma yakare yanzu haka so take tahada su koma amma abun ya faskara shiyasa take ganin shine mafita hakan.

Bilki tace tau Wallahi babu ruwana a wannan hau din idan kingani a lahira fa kaine akai wooo ni shegiya kina ganin mutane jiki duk Hutu bakisan daga inda suke ba, kice zaki haye musu billahi babu ruwana, rabiah dai tayi shiru tana sauraron bilki har tayi shiru kafin tace tau ni Wallahi wayata zan siyar na koma wajan madawaki asan abun yi, bilki tace tau shknn ai yafi dai kafin ta mike tana daukar mayafinta tace rakani wajan anty hibba mu gaisa nawuce gida babah tace kar najima rabiah ta mike tace mutafi Allah yasa yayan bai nan kinsa sa mayyanta ne Wallahi ko da yaushe ya baibaye da ita Wallahi bilki tayi dariya tace halinsa guda da abokin nasa kenan rabiah tace uhm Allah ya kyauta bilki Tace Ameen , Sallama suka hibba ta amsa musu shiga sukayi tana nan zaune parlor tana kallo tana ganin su tayi murmushi tace sannunku da zuwa bilki tace yauwa anty ina wuni? Hibba tace lafiya lau ya gida? Bilki tawashe baki tace lafiya lau, rabiah ma tagaishe ta amsa kafin ta mike ta shiga kitchen zata kawo musu ruwa bilki ta kalli rabiah tace ashe matar nan da kyaunta har kiba ma tayi nagani rabiah dai ta tabe baki tac eke kullun sai kin gama yabon mutane ina dalili kam tafada tana tsaki ruwa ta kawo musu sai chin chin batayi girki bat ace su zauna ta daura ko indomie bilki tace aaaa sauri take idan tadawo zata ci wata rana hibbah tace

Allah yakaimu ruwan suk asha da chin chin sama sama sukayi fira domin hibba sam bata son rawan kan yaran, har bakin kofa ta rako su sukayi sallama ta koma ciki. Kallonsa take har yagama kafin tace to ka kwanta Allah zanyi fa nace maka, malik dai sai kallonta yake kafin yace nace miki ciwon kan kadan ne saboda nashiga rana ne,tayi shiru bace masa komai ba ya mike,yace muje kitchen din suka shiga yayi mata blending, kayan miyan duk da daurewa kawai yake ji yake kaman zaiyi fever tana lura da yarda yake ta ciza lips dinsa ,can tace ka fita zan karasa ya girgiza kai kawai yacigaba da abunda yakeyi, bata sake magana bai ta ta cigaba da yanka vegetables din, kasa daurewa yayi kawai yamike yafice daga kitchen din nan parlor ya dawo ya kwanta kan carpet kansa na wani irin sarawa rufe idonsa kawai yayi yana sauraron yarda yake kyarma,kaman kar ta fita sai kuma ta wanke hannunta ahankali tasa karamin towel ta tsane hannu " fitowa tayi yana kallonsa ko dauke ido babu karasawa tayi kusa dashi kafin ta kai hannu ta a neck dinsa temperature dinsa yayi high sosai dasauri ta dauke hannunta gabanta nafaduwa kafin tace,jikin yayi zafi sir daman baka da lapia? Girgiza kai yayi bai iya ce mata komai ba mikewa tayi ta nufi bedroom very clean duvet dinta ,ta dauko masa tadawo ta yafa masa, har kai ta rufe masa tama rasa mi zatace masa can tace sannu, tazuba masa ido kawai hankalinta bakaramin tashi yayi ba,tana tunani ko ta kira dr ibrahim can tace sir ka kira Doctor manah hannu yasa cike da dauriya yabude duvet din yace kije ki karasa girkin zan kira sa bata tashi ba kuma bata daina kallonsa ba, can dai ta mike ta koma kitchen din ta cigaba da girkin amma hankalinta na wajansa, sharp sharp takarasa ta fito tasame sa,zuwa yanzu ya daina zufan sai ajiyan zuciya dake saukewa kadan kadan alaman yayi bacci bude duvet din tayi ganin he is sweating yasata bude duvet din baki daya bedroom takoma ta dauko tissue tadawo parlor gently ta matsa kusa dashi ta warwari tissue din tana goge masa goshin dan bude idonsa yayi yakalleta kafin yarufe ahankali , sai da ta goge masa tass kafin ta koma bedroom din wanka tashiga few minutes tadauka a cikin toilet din kafin tafito vaseline kawai tashafa sai perfume tasaka kaya ta dawo nan Parlor ta zauna can karshan carpet daga ka ganta kasan bata da nutsuwa, ganin kaman yana dan motsi yasata matsawa kusa dashi jin alaman ta kusa dashi ,yabude duvet dinta ahankali yace kingama?ta gyada masa kai yace kinci? Ta girgiza masa kai bai ce komai ba yadauko kansa dake ciwo sosai kaman zai fadi ya daura a laps dinta Wallahi malik ji yayi kaman an daura sa a aljannan duniya wani irin ajiyan zuciya yasauke nutsuwa na baibaye jikinsa, ganin yarda yayi din yasata jin gabanta yafadi duk ta rude jin ya kwantar da kansa a cinyan ta yakure kan wajan cikin kaman zai mai kan a cikinta,ahankali yace miyasa baki ci ba?muryanta na rawa kaman zatayi

kuka Tace nakoshi bai ce komai ba ya lumshe idonsa shiru cikinsu babu wanda yasake magana kusan 20mins suna ahaka kafin ahankali yamike taga ya nufi toilet yana shiga tamike itama ta wuce bedroom alwalla tayi itama ta kabara sallan la’asar ,bai ji masallaci ba saboda bazai iya ba anan gida yayi sallarnshi nan kana bun sallan ya zauna bai tashi bah, tana fito tagansa zaune bata ce masa komai ba ta dauke ido ta shiga kitchen warmer ta dauko da plates sai spoon da serving spoon ta ajiye nan gefen sa kafin takoma ta dauko ruwa pure water a kan plate shidai bai ce komai bas ai faman kallonta yake ko kiftawa babu,bude warmer tayi serving dinsa abincin kadan badayawa ba ta tura masa gabansa abincin ya kala kafin yasa spoon baya son ya nuna mata bazai iya ci ba, Ahankali yake cin abincin ita dai bata zuba bas ai kallon wuri daya take girgiza kai yayi kafin ya ture abincin yana kallonta murya can kasa yace mata bazaki ci abinci ba ta girgiza kai tace zan ci yace tau sa k ici yafada yana mika mata spoon tareda tura plate din dake gabansa tsakiya,spoon din tasa tafara ci kafin shima yasa atare suka cid uk da bai dayawa amma babu wanda yakara cikin su ruwan ya sha kafin ya mike zai kwashe kayan dasauri ta girgiza masa kai kafin tace kabar shi zan kai kitchen “bai ce komai ba yakoma ya zauna ta kwashe kayan tass tana dawowa yace kije kisaka hijab tace to “ daki takoma ta dako well iron hijab dinta ash tasaka perfume tafito tasame sa, tsaye yana jiranta bakin kofa kallonsa tayi kafin tace ina zamu je? Yace clinic batasake magana ba har ya kulle kofan suka fita anan bakin hanya suka samu keke yafada masa inada zai kai su kafin suka shiga .Dr ibrahim dake kallon malik yace tun yaushe? Malik yayi shiru kafin yace tun jiya nake jin ciwon kai kadan kadan so I didn’t take it that serious nayi tunanin dan nashiga rana ne tau sai yau natashi da fever dr ibrahim yace sannu “malik ya amsa aydarh dai na zaune tana sauraron su dr ibrahim yamike yace tau muje sai nayi maka allura yallabai malik ya mike suka fita ita dai anan office din dr ibrahim ta zauna ta tunanin ko dr hafsa tazo bata sani bad ai “kaman dr hafsat asan abunda take tunani sai gashi ta turo kofan office din tashigo bakinta dauke da sallama aydarh ta amsa mata dr hafsa na ganin Aydarh tawashe baki tana welcoming dinta kafin tace badai ke ce ba lafiya ba?aydarh ta girgiza kai tace ah’ah dr hafsaa tace ko yallabai?aydarh ta gyada mata kai dr hafsa na ajiye fili din hannunta tace asha kam subhanallah? Mike damunsa aydarh tayi kasa da kai tace fever “ dr hafsa tace subhanallah Allah yasawwake fita sukayi ne?aydarh tace erh sunje injection room dr hafsa tace eyyerh Allah yabasa lafiya Aydarh tace Ameen auntie,dr hafsa tace tau mu tafi can office dina kafin su gama koh?aydarh tace “ office din dr hafsa suka wuce, dr hafsa ta kalli aydarh tace Wallahi zazzabin nan ake ta fama Allah dai yasawwake aydarh tace eyyerh Ameen dr hafsa tace ai saboda weather nan

ne Wallahi mutane duk ba lafiya mutun daya daya ne basuyi ba Allah Aydarh tace Allah yabasu lapia Dr hafsa tayi shiru kafin tace yauwa Allah yakawoki yau sai anyi kam,aydarh tadago kai kafin tace me fa? Dr hafsat ace yar rainin wayo ai duk sai wani fuzewa kike bakya son p-test din nikam ban yarda ba fa har yau kinsan akwai cikin da bayasa laulayin ke fa kullun naga wani sake fresh kike idan ba ciki ba Aydarh mi ke gareki kiji fa skin dinki kaman kina wanka da milk wannan uban glow datake haka ji fa yarda komai na fuskanki yasake wani extraordinarie kyau hakanan " ji fa boobs dinki tabarakallah ko ta cikin hijab gwanin burgewa shikam yallabai ya iya kiwo Allah yakara bada zaman lafiya,takarasa maganan tana yar dariya tare da dauko wata karaman container tana mikawa aydarh,ita dai aydarh kanta nakasa bakaramin kunya da mamaki take jib a duk time din da dr hafsa zatayi mata maganan ciki har kaman tayi kuka take ji, dr hafsa tace kinga karba ki shiga nan toilet kiyi fitsari ko kadan ne sai ki kawo mun 'Aydarh da kaman zata fashe da kuka muryanta cike da shagwaba tace bafa naji auntie Allah kuma ni bani da komai ki ma tambaye sa tafada har kwalla yakawo idonta dr hafsa ta rike baki tace ahhhh lalle Aydarh natambayesa shi sani zaiyi ne ki jimun yarinya "shi ai daya shagwaba ki yazo nan yasame n isai ku shiga toilet din yasa kiyi fitsarin ayi awon dan ban yarda dake ba "Aydarh dai ta dukar da kanta tana jan fingers dinta hawaye na bin cheeks dinta ta turo bakin irin shagwababun rich kids din nan, dr hafsa nagama wayan datake sai ga malik yashigo rike da ledan clinic din ahannunsa ciki maganin da dr ibrahim yabasa ne yadawo office din bai ganta ba yakoma wajan dr ibrahim,dr ibrahim yace yaduba office din dr hafsa yasan suna tare yaga yar gidanta ce,sallama yayi dr hafsa ta amsa tana gaishe sa amsawa yayi tana tambayansa ya jiki, yace Alhamdulilah Doctor ya aikin? Tace alhamdulilah yace Allah ya taimaka tace Ameen kafin tayi murmushi tace ina nan nida yar gidana ni fa yallabai nakasa hakura da zancan cikin nan nakasa yarda Allah ka dubeta fa,malik yadaga kai yana kallon aydarh datayi kasa da kanta yayi murmushi kafin yashafa sajansa yace koh Doctor?dr hafsa ta gyada kai tace sosai ma kau yallabai ga abu nan nabata nace tashiga tayi fitsari taki shiga nace idan kazo ai kasa ta tayi sai na gwada,murmushi yayi kafin yasa hannu yakarbi roban ya mike mata yayi kasa da murya yace just do what she said kinji hajia "yanda yayi mata maganan kaman yanda abbanta ke mata magana idan yana lallashinta, tadago suka hada ido hawaye suka sake zubu mata tana kallonsa ta makale kai a kafada ganin yarda tayi yasan halin yan kayansa bafa yin zatayi bay asa shi sakeyin kasa da murya yakai bakinsa daidai kunnanta yarda ita kawai zataji yace kije kiyi idan tayi test din ayi shikenan zata yarda bazata sake takura ki ba kinji cuddle bug 'sunan dayakira ta nakarshe yasata saurin dagowa tana dubansa ko dauke ido babu

kaman bashi yayi maganan ba yafiddo wayansa a pocket yana dubawa ya basar, dauke idonta tayi ita dai dr hafsa na ta kallonsu bakaramin yi mata kyau sukayi ba a haka,bata sake cewa komai ba ta dauki roban walking very slowly tashiga toilet din dake very clean kaman ba na asibiti ba.kusan 1hour sai ga dr hafsa tashigo da result din a hannu ta mikawa malik tace yallabai yanzu kaga na fita a kokwanto your baby is still free Allah yakawo masu albarka tau,malik yayi murmushi yace Ameen Ameen likita nagode, dr hafsa takalli Aydarh tace tau shagwabban audun inna hankalinki ya kwanta ba ciki amma very soon Allah zai kama ki,aydarh tayi dariya tana rufe fuska shidai malik murmushi kawai yake, can yamike yace yamma nayi dr bara mu wuce gida sai kin taso “dr hafsa tayi murmushi tace tau nagode yau ansha wuni a clinic,malik Yace gaskia “dr hafsa ta tako wata karamin shopping bag cike da candies ta mikawa Aydarh tace tau gasu iloka da gullisuwa mai tsoron ciki aydarh tasa hannun takarba tana dariya tace ah’ah fa Auntie bana tsoro,malik yace kai dr hadda wahala kuma tau angode Allah yasaka,dr hafsa na murmushi tace babu komai yallabai nima nagode, har bakin clinic suka rakasu ita da dr ibrahim suka hau keke suka wuce. Sai da ta chanza masa bedsheet kafin ya kwanta tana kallonsa tace ko zaka koma bedroom din?ya girgiza kai yace aaaa ai kin chanza bedsheet din zan kwanta anan din tace to sai dasafe, malik yace Allah yakaimu sarkin rowa “da sauri ta juyu tace waye mai rowan tafada tana bata fuska, yace wanda zaa bawa candies tahana mijinta, aydarh tawara ido tace lah kasan nafa manta dashi tace bara nakawo ni fa ban taba shan su ba yace kai haba? yafada yana mamaki kaman irin tafadi wani babban abu tace Allah kuwa,can ta fito da ledan ta zauna kusa dashi tabude tana ta kallon tuwan madara da iloka sai gullisuwa da medulla manya masu kyau sosai kwara daya ta mika masa he forgets when last da sha wannan abun murmushi yayi yasa hannu yakarba itama irinshi ta dauka tana sha taji wani mugun dadi dasauri tajuyu tana kallonsa tace kaji dadinsa kau ya gyada kai yana bude Ido sosai yace yayi dadi sosai tace ka iya yinsa ya girgiza kai yace aaaa saidai su aysha tace eyyerh su sun iya?yace Sosai kina son ki koya ne ta gyada kai yace tau mu sha sauran muje,tace ba fa dayawa zan baka ba.

Yace tau naga dai tare aka bamu ko? Tace kuma da aka bam uba tare bane dai muna atare zaka ce sir ‘yace tau shknn ki sha candies a daran ma idan ina so zuwa dasafe zakiga ankawo mun su nan “taware ido tace wazai kawo makai ta Auntie zaka wa magana?yace wacece kuma auntie,tace ita dr hafsa din malik ya girgiza kai irin he is very serious din nan yace ni dake da budurwa kuma matan dazan aura har sai nemi abu wajan wani,aydarh tayi shiru dai tana kallonsa tana jiran yakarasa yace ita gurl zanwa magana cikin

daran nan gobe tun eight zaki gansu anan,ta tabe baki kafin ta kallesa tace kai haba har sai ankai eight aie nayi tunani da subhi zata kawo maka “ya danne dariyan dake cin sa yace lafiya lau ma zata kawo da asuban ya dauko wayan yayi kaman zai yi dialing ya kirata aydarh ta kafe sa da ido tace yanzu fa sai kace zaka kirata din?yahade rai yace tau dawasa nake da? Aydarh tace Allah bazaka kirata ba,yace saboda mi? yafada yana wara ido tace miyasa ma zata kawo ma abu bayan ummi tace kowa amana ni,yace bangane ba tayi kaman zatayi kuka tace Allah kasani nidai karka kirata ka kira ita auntie hafsa kace ta koyamun kuma ma ai ni wasa nake tare zamu ci wannan din ma I can’t finished it kasani ma,yayi murmushi yana shafa kansa yace tau ai abun hannu wace ta damu dani zanci tayi shiru tana kallonsa dan ba wai ta fahimce abunda yake nufi bane ganin hakan yasa shi chanza magana yace tau zanyi wa dr magana idan nasamu time tayi shiru kafin tace to zaka kirata din?yace dr? Tace ah’ah ita waccan din yace ohh wai gurl nafasa kiranta yanzu sai dasafe zamuyi waya tace mun zan rakata cocktail din wed din kawanta, aydarh na kallonsa ko dauke ido babu tace cocktail fa kace?yace eh shi tace uhm yace miye a cocktail din?ta mike tsaye tace you are sick you are going no way kuma Allah yakaimu goben tazo tagani ta fada tana dauka cup daya na gullisuwa da tuwan madara da iloka sai medulla ta bar masa sauran biyun murmushi yayi yashafa kansa yana kallonta har ta shige daki kafin ya gyara zamansa,tunanin kala kala aransa zuwa yanzu baya jin fever ko wani ciwon kai kawai rashin kwarin jiki ne kuma shi yayi prescribing drugs din da kansa bai dauko pain reliever saboda baya son shan sa,iloka daya kawai yasake ci kafin yarube cups din dasuke cikin sosai ,ya kwanta ahankali yana rufe idonsa scent din jikinta har yakama bedsheet din da pillowcase din data Chanza masa wani irin sanyi ke bin jikinsa da haka wani irin bacci mai dadi yayi gaba dashi wanda he can’t even recalled when last yayi baccin shine bai farka ba har asuba,kiran sallan farko ya tayarda shi daga hadaddan baccin daya dauke sa yatashi dauke da addua a baki toilet yawuce yayi alwalla kafin yashiga ya tarar da har ta tashi har cikin ransa bakaramin appreciating islamiyan nan yayi ba cikin kwanakin nan data fara zuwa bakaramin sauyi tasamu ba daga kan sallarh gaisuwa da kuma kananunun abubuwa na addini wanda bata sani ba ranar ya zauna yana kallonta tana sallarh cikin nutsuwa ba kaman da da kaman ana mata dole ba.sai da gari yayi haske yadawo bedroom din ya tura yatarar da ita nan kan prayer mat tana bacci Ko hijab din bata cire ba, riganta ta kwashe daga kasan kafanta har kusan gwiwa ya dinga bi very cute legs dinta da kallo wanda tun lallen da aka musu da dr hafsa sai yanzu yafara alama fita bakaramin kyau yayi ba daya fara gogewan har karasa ma lokacin dayafi kyau da sanda akayi sa da yanzu zama yayi gefan katifa his

eyes still on her,sai kallonta yake ko dauke ido babu kusan 20mins kafin yaga alama zata farka har tafara motsi, mikewa yayi ahankali yafita ya rufe mata kofan a ranshi yake tasbihi da kuma godiyan Allah daya hallice sa ya hallice iyayansu shi da ASSEIYARH dakuma ita,dakuma godiya da kaddaran data hadasu waje daya shima yana dawo nan parlor yasake kwance ko 5mins baayi bas ai ga bacci yadauke sa babu wanda ya farka cikinsu sai wajan nine, kaman an tashe su a tare suka farka ,tamike ta dinga bin inda ta kwanta din da kallo kafin tacire kawai ta fada toilet wanka tayi tass kafin ta fito kaman jewel sai shine take kullun kaman angel din kara kyau ke kara mata kyau ita kam wai? Vaseline tashafa sai powder da kajal yau hadda lips kafin ta shafa perfume as usually kamshinta is very amazing, riga tasaka bayan tasaka inners ta kara perfume,kafin ta gyara katifan ta kauda komai na dakin duk da babu wani dirty ahankali tabude kofa ta dawo parlor kallo daya tayiwa shimfidarsa taga baya nan sai karan ruwa a toilet mopper tadago da tsintsiya tawuce bedroom sai data share tayi mopping kafin ta fesa freshener , tafito da kayan shara ta mayar dasu,Still bai fito ba ta dinga bin wurin da kallo wai ko zataga idan Ramlah takawo masa candies din (😂) amma babu alaman wani abu tun cups biyun jiyane har yanzu a wurin gyara shimdar tayi tasan kwanciya zaiyi kafin ta dauko tsintsiya ta duka tafara shara karan bude kofan yasata kallon direction din toilet kafin kuma tayi saurin janye ido tacigaba da shara ahankali yafito yana goge suman sa da karamin towel sai singlet da wando shadda a jikinsa,ko dagowa batayi ba balle ta kallesa,murya can ciki tace Good morning yace morning kafin gently tace how was health?ya gyada kai yace Alhamdulilah daga haka taja bakinta tayi shiru shi kuma yawuce can bedroom din yashirya bai fito har tagama moping takara gudun fan din dun yayi saurin bushewa can sai gashi yafito sanye da wani jallabiya black mai kyau yana wannan kamshin nasa mai dadi,zama yayi kan shimfidar tasa yana kallonta kafin yace breakfast fa?tace yanzu zan daura ruwan shayi yace tau daga haka tawuce kitchen shikuma ya dauko guitar shi yana playing kidan kadan kadan sound din ba karfi ko kadan sai dan karan dadi ,tana kitchen ta dinga jin sound din guitar kasa hakura tayi har sa da ta bude kofan kitchen din taga daga ina ne tana budewa tagansa zaune kansa kasa yanata playing guitar kallonsa tayi mamakinsa ya ciketa daman tasa ce tun jiya daya shigo da ita taso tayi masa magana na waye sai kuma tayi shiru batace komai ba ,kallonsa tayi almost 5mins shi bai ma sani ba kansa kasa sai playing abunsa yakeyi, komawa tayi kitchen din sound din yayi mata dadi sosai shayin ta sauke kafin ta juye a flask ta dauko cups biyu da spoon sai bread da kayan shayin babu kwai yakare Irish ma haka kuma taga bai siyo ba maybe bashi da kudi tafada a zuciyanta tana daga kafadan alaman she didn’t care bude kofan tayi ta kai

parlor kan carpet ta ajiye kafin ta koma kitchen din takarasa gyara inda ta bata,tafito lokacin ya ajiye guitar ya hau kan carpet din yana hada musu shayin hada mata yayi daidai yanda yasan tana iya sha kafin ya hada nasa shima,zama tayi ahankali tana kallonsa shima ita yake kallo batace komai ba ta dinga bin shayin da kallo mamaki take wai har yasan iyakan abunda take iya ci,shayin ta dauka tana juya tea spoon din dake ciki tunda tafara yake kallon hannunta rings dinta masu dan banza kudi da kyau,(dan diamond ba wasa ba hajiya kinga diamond kinga English gold karki wasa idan kinada shi siyi kiyi gayu yayata □□) sunyi ma hannun kyau kaman dan hannu akayi rings din, can yayi ajiyan zuciya yace ko sai ya huce zaki sha?ta girgiza kai tace ah’ah aie babu zafi yace oya drink kuma kina hadawa da bread din yau! kai kawai ta gyada masa kafin tafara kurban shayin tana cin bread din kadan kadan bata wani ci biredin dayawa ba ta ture shayin dai ne ta shanye dukka yana ganin ta bai ce komai ya mike bayan ya gama nasa ya kwashe kayan ya kai kitchen yadawo cup din candies din ya bude ya fiddo iloka wanda shine favorite dinsa yafara chewing itama tashi tayi tawuce bedroom,toilet tashiga ta wanke inners dinta da detergent sai liquid soap din dettol kafin ta wanke toilet din tass tafito sai data kara gudun fan saboda zafin da akeyi garin yau babu hadari sai rana bata da haske sai zafi, hakan yasata zama gefen katifan tabude cup din candies dinta tafara ci kasancewan tana masifan son zaki shiyasa taci ya kusa quarter ma .kallonta yake ko dauke ido babu yace shi malamin ne yace a daina saka nikkab?ta gyada masa ,Kaifin yace ke kawai yace ma wa ko duk students din?tace ah’ah fa mu uku kawai saboda baya jin karan muryan mu sosai sai yace mu daina sakawa maybe shi ke sa bayaji ma,malik yayi shiru kafin can yace hala shi mahaukaci ne bai san duk matan mutane bane a ajin? Ta bude hannu alaman bata sani ba kafin tawara ido tace wai shine mahaukaci? Sir wanda bashi da hankali fa ake cewa mahaukaci ,malik ya gyara zamansa yace eh mahaukaci manah banda bai da hankali matan auran zai ce suwani daina saka nikkab bazaki daina bai dan kuma yasake magana ki gamun ta gyada tayi shiru yace amma bakya jin yunwa?tace yunwa kuma? Ka manta munyi lunch ya girgiza kai yace ai indomie ce kawai mu ci Ko fruits yau ba a sha ba tayi shiru tana wasa da hannunta bata ce komai ba ,yace tau dinner fa naga kusan 5:30yanzu yafada yana kunna hasken wayarsa, ta girgiza kai tace zan sha sauran candies din akwai dayawa,sai kuma ta kallesa tace kai sa nadafa maka shape pasta shi akwai yayi murmushi yace aaaa anima zan sha candies din yafada yana yin kalan voice dinta tayi smile kawai bata ce masa komai ba, ya mike yace tau ni bara naje naga time din datace yayi natafiya cocktail din,dasauri ta kallesa ou bai mance ba kenan itama ta mike “tana hade rai tace ina zaka?yashafa kansa kamshinta na gigitar mar tunani

kaman zai jawota yasa ciki, bai so yayi spoiling mood din ba sosai yake jin dadin fira da ita duk wani shirme kaji sa bakinta komai nata na yarinta take shikam wannan akwai aiki Sosai a gabansa ,yace tare zamu fita da gurl yafada irin kaman dagasken nan har wani gyara sanyin p-caps dinsa yake wanda ta bi suman kansa ta fito baya kaman dan balarabe, tace baka san baka da lapia ba? Wallahi saura kadan yayi dariya ya danne, yace nasani manah amma ai kinsan inada zanje din is very important kar na batawa yarinyar can rai kinga ita duk abunda nakeso tamun, tawani hade fuska ta gyara tsayuwanta tace mi take maka? Yace abubuwa dayawa manah ,tace ohhni bana yi maka kenan? Tafada kaman zata saka kuka har kwalla yakawo idonsa yace aaaaa ni bah aka nake nufi ba ita ai soyayyya muke ke kuma ai kanwata ce ko kinga ba same relationship muke ba kowa danasa opposition din aydarh dai sai kallonsa dake da mamaki tace to ita miye hadinta dakai ina n ice kawai kasani nima kai kawai nasani kadai na saka ta a rayuwanmu mu ne kawai a rayuwanmu mu biyu, tace wai minene din shi din ma take maka yace kibari mu dawo zan gaya maki yafada yana nufan hanya kofa dawai irin speed tariga sa isa tayi sauri tasakawa kofan key tacire ta boye key din a bayanta,binta yayi da kallo ganin abunda tayi ouu bazai fitan ba kenan hade rai yayi sosai yace ki bani key din duk da yarda yayi din sai da gabanta yafadi don ba dan kadan take tsoronsa ba,Amma ta daure itama tahade ran cike da tsiwa tace Allah fa bazaka fita ba yace kee “tace bazaka fita ba koma miye,yayi shiru kafin yace kibani key lokaci na wucewa kar tagaji da jirana,aydarh tace said ai ta mutu da jiranka tunda ita batasan ciwon kanta ba zata dinga bin namiji bashi ya bita ba, malik yace bani key din tace Allah sir kayakuri ni fa bazan bayar ba bara ka fita ba kaji ma,yayi shiru kafin yace ke zan fa balla ki ko ki bani,aikau sai ga hawaye sha a fuskan ta,cike dawani irin yarinta da zallan gayu, tace erh daman zaka balla nin manah tunda abba yace baya sona don kaga an maka aure dani shine zaka dinga mun komai don kaga bani da wanda nasani a nan sai kai shiyasa kake mun abunda kake so to Allah bazaka fita bas ai dai ka kasheni din “ malik yayi shiru yana kallonta zuciyarsa har harbawa take yarda take maganan sai yaji duk wani lissafinsa ya kwance wannan yarinyan bai ma san yarda zaiyi da ita ba daurewa kawai yake amma da tuni ya barar da shawaran dr ibrahim saboda baya son wannan rigiman da koke koken,sa shi suke yana loosing, daurewa yayi yace idan kingama kibani key din bana shirme fa jiranki nake cike da masifa tayi masa tsiwa tace to Allah baran baka ba , bai ce komai bay asa hannu zai kwace key din ai dasauri ta jefasa cikin riga ganin abunda datayi ne yasa shi yin kasa da kasa yana wani killer smile kafin ya dago yace kibani key din tace ai nace baran baka kuma bazai ka fita ba yayi shiru kafin yasa hannu yamaida hannunta baya yarike su da

hannu daya yasaka ta cikin jikinsa, gabanta yafadi ganin abunda yayi hankalinta ya tashi tace miye haka miye haka kakeyi sir kasake ni manah ka rabu dani,ni Malik bai ce komai yakarasa matsawa jin bango sosai, kafin yasaka hannu.

Yarda ta firgita har sai da numfashin ta ya dauke na wucin gadin she never except this bata taba tunanin zaiyi kokarin cewa zai dauka ba yarda yake zage zip din kaman yana hadawa da fizgan numfashin ta, rufe idonta tayi gam ta riga tagama sallamawa,shi kansa malik bai san abunda yahau kansa ba , sai da yabude zip din tass white soft boobs dinta suka bayana cikin red lace foam bra tayi tighting dinta sosai dan tayi mata kadan daga sama, iyakar ta rabi bata rufe rabi ba hannunsa na kyamar idonsa na kan wurin ko kiftawa babu yasa hannu kawai ya dauke key din kafin ya janye ta daga gabansa ai kaman jira take dawani irin gudu ya ruga bedroom wani irin kuka na kwace mata dayasa shi jin har kansa ya sara,key din yasaka jikin kofan ya bude, anan ventilation din ya tsaya yafidda p-cap dinsa yadafe kansa yana sauke wani irin ajiyan zuciya yakai 10mins nan tsaye idonan a jajir ga can dai yayi kokarin sai saita kansa kafin ahankali yabude kofan parlor yashiga yadinga bin parlor da kallo kaman irin yau yafara shigowa din nan, zama yayi nan kan carpet kafin ya maida idonsa kan kofan bedroom din sound din yarda tafashe da kuka nasake playing a kunnansa, tashi kawai yayi yanufi bedroom din yana Allah Allah bata rufe ba, aikam yana burdawa yayi saa a bude, yarda tade kanta da gwiwa kawai sai yaji hankalinsa ya tashi walking majestically ya karasa kusa da ita har yanzu kukan take, ahankali ya hau kan katifan yasa hannu zai dago kanta taki dagowa daman yasan bazata dago ba,sai kawai yasa hannun ya dauko ta kaman wata yar yarinya ya daura ta saman kafansa,yayi placing kanta a chest dinsa,cike da lallashi yake shafa bayanta, kafin voice dinsa very slow and calm yace ya isa haka,bana son yawwan kuka shiit, kiyi shiru “bayan ma banje can din ba nafasa zuwa nace mata “sai sannan ta dago kanta fuskanta har yayi zufa tsaban kuka,tace ni bashi ya dameni ba tafada tana sake rushewa da wani kukan kaman irin daya dago ai ya falla mata marin nan “kallonta yake ko dauke ido babu yace tau miya dameki? Sai sannan ta zame jikinta daga kanshi tadawo kasa ta sukunyan da kanta “tace bayan kullun sai ka dinga ganina tafada wani kukan sakarci nasake kwace mata,malik yayi shiru duk da ya fahimce abunda take nufi,can yace tau hajia ba dole na dinga ganinki ba kullun har wani irin zabura tayi tadago idonta da duk kukan datayi babu wani alaman ja sai da hancinta da fuskanta duk tayi zufa ganin yarda tayi dinne yasa shi daga kafada yace eh mana ai dole na dinga ganinki tunda a gida daya muke rayuwa ke bakya ganina kullun? Aydarh dai kanta nakasa

ganin shi bai ma fahimce ta ba da farko tayi tunanin ya fahimta,bata sake cewa komai ba ta cigaba da kukanta yace ohh bazakiyi shirun ba wai? Still kukanta,take hade rai yayi fuskanshi ba alaman wasa yace wai ba magana nake da ke yafada cikin fada fada aikam kamar ance tasake fashewa da kuka haka takara volume din daya fi na dazu subhanallah wannan yarinyar zata zautasa, ya dinga kallonta kafin yace idan baki rufe ma mutane baki ba sai na taka ki a dakin nan ai kaman andauke ruwa haka tayi shiru sai saukan ajiyan zuciya kawai, Still idonsa a kanta yace Allah yasa naji kin sake kukan tunda ke bakya tausayin kanki, bayan kinsan idan kina kukan rashin lafiya kike, kamar ba babba ba wai wasu yaran ma basa abunda kikeyi, Allah yasa na kara jin bakinki kiga yarda zanyi dake, yarda yake mata fadan kamar irin yana yiwa dan yaro “mikewa yayi sai kuma yayi kasa da murya yace kije toilet ki wanke fuskan ki sameni a parlor kina ji? Kanta a kasa ta gyada mashi kai, yafita sai data kara kusan 5mins kafin ta shiga toilet din ta wanke fuskanta hadda soap tasa towel ta goge kafin ta fito riga ta chanza da kaman kar tafita parlor sai kuma ta mike ta dau hijab dinta ahankali take tafiya kaman bata son taka tiles din har ta karaso parlor yana zaune kan carpet itama bisa ta zauna amma can nesa dashi ta sukunyan dakanta, yakasa cire ido kanta a jikinta taji yana kallonta sukunyan da kan tasake yi tana sauraron jin abunda zai ce mata shiru shiru bai ce komai ba har aka kira magrib tashi yayi ya nufi hanyar toilet bayansa ta bi da kallo har yashige kafin ta mike itama tashiga bedroom tana shiga ta wuce toilet tayi alwalla tafito time din har an fara sallarh hijab tasaka ta kabbara . Kitchen ya ajiye kafin ya shiga bedroom din bayan ta gama sallan isha’I ta dauko books dinta zatayi assignment wanda yanzu sai tayi take nuna masa idan inada ba daidai bane sai ya gyara mata ,kallon books din yake ko dauke ido babu can dai yakasa hakuri yace “who writes this for you? Ta dago kai taware ido tace ba kowa “yayi shiru kafin yace ke kika rubuta? Ta gyada masa kai yayi murmushi yace your handwriting is the best “tayi wani cute smile tace kaima sir naka yanada kyau sosai yashafa kansa yace really? Tace sure yace tau idan kingama ki fito muyi dinner tace dinner kuma girki kayi ne? Ya girgiza kai yace taya zanyi girki matan gida batasani ba it’s something special kawai ki fito zaki gani tace to “ ten minutes later sai gata ta fito ta cire hijab din tasaka hula a kai ,ahankali tazauna kafin ya tura mata plate din awara a gabanta ta dinga bin awaran da sauce a gefe sai cabbage da carrots suma anyi slicing din su in a very attractive way, ta kalli plate din ta kallesa kafin tace wa yayi? Cike da tsokana yace Ramlah,ta dinga kallonsa kafin ta mike tace to babu wanda zai ci abun nan kam, yayi kasa da murya yana ware ido yace why? Tace ai nace ta daina kawo abu nan gidan wani ma yace muna son abincin dazata girka ta kawo ne? Malik yace

aaaaa ita fa kawai don nine tayi nikuma naga ba zan iya ci baki ci bane that is why nace kifito muci,Still idonta kansa tace to wai miye very special anan ina irin abunda ake siyarwa a kofan gidan nan ne shine special? Kafin cike tsiwa tace maybe ita shi take siyarwa yasa takawo maka “malik yayi murmushi yace bai burgeki ba kiji fa yanda komai ke very neat a nan, aydarh tace hala ni girkin nawa is very untidy? Ya girgiza kai yace haram ban fada ba tace to ka mayar gobe zanyi maka yace kai haba kin iya ne ?ta hade rai ta girgiza kai tace ah’ah zaka koyamun ne yace tau ni waya ce na iya?tace to sai auntie ta koya manah amma dai babu wanda zai ci wannan ka bayar ko ka mayar mata bama so “yayi dariya yace aaaaa gaskia ni zan ci kema dole kice tace To Allah babu wanda zai ci a cikinmu, ganin dai dagaske ta yarda Ramlah ta bayar kuma yaga reacting dinta,yana murmushi yace kinga relax zauna Doctor yakawo yace hibba tayi tace akawo manah “tabata fuska kaman zatayi kuka tace shine kuma zaka ce ita tabada? Yace sorry zauna dai let’s chop ta zauna kafin ta hade rai tana turo baki tace ni to kadaina jana gaskia,yace nadaina muci, tace to ina naka naga nan plate dayane “yace fork biyu kuma ba ,batace komai bay ace tare zamuci ai ,kafin yayi shiru yasa hannu suka fara ci yayi dadi sosai kusan five taci kafin ta mike ya bi ta da kallo yace what? Tace nakoshi ruwa zan kawo yace ni zan cinye duk wannan c’mon dawo nan hajiya ‘kananan kwalla tafara tace Allah nakoshi ganin zatayi masa kuka yasa shi yin shiru yaciba da cin awaransa,kitchen din ta shiga ta dauko masa ruwa,ta ajiye ta koma gefe tana shan nata” kafin ta ajiye ta jawo roban candies din dake nan ajiye nasa yana ganinta yayi shiru bai ce komai ba budewa tayi tana sha,ina ma yanda take son zaki haka take son abinci ‘sturbborn bea kawai “ganin takai kusan na five duk da girman abun yasa shi dago kai yace ‘ko kin manta bai fi five days ba,taware ido tace miye bai fi five days bay ace shi cramps din dakike dagawa mutane hankali kaman zaki mutu, dasauri tayi kasa da kai tana ajiye roban kaman zata ruga,yace ohh ashe ke ke jama kanki kina shan zaki baki san shi ke saki wahala ba?tayi shiru batace komai bad ai tana sauraron sa amma da akwai space da sai ta nutse anan din, tsaban kunyan dataji, yayi shiru ya cigaba da abunda yake a waya, kaman bashi yayi maganan ba, ta turo baki kafin a ranta tace “ko ma ina ruwansa ya akaiyi yasan saura kwana nawa tayi mp? Bata da mai bata amsa kuma bazata iya tambayar sa ba kawai sai taja bakinta tayi shiru.Tayi shiru kafin tace ai baka gogeshi bay ace kai haba ai mantawa ma nayi,anjima zan goge ai sai jibi school din ko?ta gyada kai kafin tace exams zaa fara ma,yace yaushe tayi shiru sai kuma can tace wai nan da two weeks “yace au uba jarabawan zakuyi ba kenan tace miyasa?yace ai naji kince wai tace to nan da two weeks zamu fara yace Allah yakaimu,tayi shiru kafin yace bara na fita na amsa waya,tabi sa da

kallo tace to yace da Ramlah zanyi waya tace vedio call ko audio tambayar tabasa mamaki yace miya kika tambaya ?tace ah’ah kawaii na so nasani idan vedio call ne sai nace ka rufe camera cus ban san yarda zata fito a vc ba takarasa tana tabe baki,malik was very speechless yarda take zaro magana Wallahi bakaramin mamakinta yake ci ba , idan tayi maganan bazaka taba tunanin ita tafada ba,malik yashafa kansa yace waya gaya maki?tajuyu tana kallonsa tace ka san dai ai she is more than ugly right? Malik yahade rai yace gurl din ce ugly kodai baki gane wacce nake nufi ba? Aydarh tace indai wannan abun ce a bazata taba kyau a camera vc ba,matar da afili ma she no fine inaga a vc, ita din kaman ba mace ba,yace ya isa haka ki daina kusheta amma duk container Africa ban taba ganin mai kyau ta ba har a Europe’s countries din ma “ai dasauri aydarh tadago tace ai kam taje can kasan cage zasuyi mata,anemi central zoom a hadda ta da giraffes dan there even resembles each other, duk yarda yaso kar yayi dariya sai dayayi,ta dinga kallonsa ko kiftawa babu ganin yarda yake dariya kafin ya tsaya da dariyan ya riko hannunta yace matan da zan auran kike gayawa haka ta turo baki tana turesa tace erh en ai I didn’t lie komai nata nafada yace tau ai babu kyau haka tace to bazan sake ba kaima karka sake mata magana yace ,miyasa tau tace kawai bana so yace minene bakya “so? Tayi shiru batace komai ba ya sake matsawa towards her har suna gogan juna, kafin yasa hannu ya jawota ta hau jikinsa,yace idan baki fada mun ba,bazan daina mata magana ba,tace nidai kawai yace ke dai kawai mi? Tace bana sonta yayi murmushi ganin yarda ta tura kanta a kirjinsa ,Yace tau miyasa bakya sonta dan bata da kyau? Tace nidai ah’ah yace tau ni ki fito kina damuna,tayi saurin dagowa sai lokacin ma ta kalli abunda tayi din ta juyan da kai ya dinga kallonta ko kiftawa babu kafin yayi murmushi yace tau anjima mu shirya muje gaishe da inna, tace to “.

Inna tace waye kuma haka? Malik da ya zauna gefen inna yace shi ibrahim din ne baki sani ba? Inna tace tau dole aka ce kowane kwashe kwashe sai na san shi? Dr hafsa na jinta tayi shiru batace komai basai danna wayanta take, Aydarh dai abun inna mamaki yake bata da dariya ma,Malik yace kuma fa har auransa kika je kwana biyu ma kikayi a can, inna tayi mitsi mitsi da ido tace tau gaskia namanta sa,malik yayi murmushi yace tunda kin manta sa ai shknn sai na mayar masa da sakon,inna tace sako yabaka daman? Malik ya jinjina kai yace eh tace shi ibrahin din nidai daman nasan Wallahi iya ce tahana sa zuwa waje na tunda yayi aure bai zo ba balle yakawo mun matar nagani daman ai ba tsoron Allah gareta ba,dayake ba lami bace, uwarta Allah yajiqanta, Malik yace kingane sa yanzu kenan?tace nagane sa miya baka ka kawo man?malik yace ai sakon magana ne, inna ta bude baki tana

suka fito wanda hakorin gold dinta na makka yakara musu kyau sai shine shine yake “ shima murmushi yayi kadan kafin ya dauke su tabarakallah yafada bayan yagama “ita dai tashi tayi tana karban wayan tace zakayi editing?ya girgiza kai yace no nafi son su ahaka (kunsan maza da rashin son editing 😂) batace komai ba tafita daga photos din “ tashiga contacts dinsa “ kafin tayi searching sunan Ramlah shidai malik sai kallonta yake hannunta dake operating wayan na mugun tafiya da imaninsa aikam sai ga sunan Ramlah yayi appearing haka nan yakarbi number ta bai taba kiranta ba tun lokacin plan dinsu da dr ibrahim yasamu number ta ‘dago kai tayi ta kallesa kafin tayi blocking number tayi deleting bai ce komai bas ai karamin murmushi dayake yi “tadinga kallon contact dinsa bata sake ganin wani number na mace ba kuma bayan inna da dr hafsa “ yace tunda kinga babu ai sai ki ajiye ba? Ta kashe wayan tana ajiye ta gefenta “ta kamo hannunsa kafin tace ehen tell me what the congratulations is for? Yayi shiru kafin yace mata nasamu aiki ta bude ido kafin tayi murmushi tace woaw are you for real? Yace mata yes wife tabata fuska tace shine zaka gayawa kowa ni bazaka gayamun ba ka kyauta kenan sir?ya girgiza kai kafin ya rike kannunansa yace pardon me ma “I just wanted to surprise you tace surprise kuma?tace kasan kullun idan nayi sallarh tun bayan dana ga result dinka sai nayi maka addua yayi murmushi yace adduan ki kuma ta karbo ASSEIYARH “ tun bayan aurena nadake nake ta haduwa da abubuwan alkhairi wanda adaa ban same su ba “tayi shiru dai tana kallonsa kafin yahade forehead dinsu long long noses dinsu na haduwa dana juna “yace it’s our destiny to be in one place ASSEIYARH it’s our destiny to be husband and wife ASSEIYARH nasan bakya sona ko yanzu muka koma yola zaki barni yafada kaman mai shirrin yin kuka “ Still goshinsu a hade yace nasan kinyi kokari zama a inda baki taba tunanin zakiyi rayuwa ba “ ASSEIYARH promise me please ko bayan mun koma gida you will continue seeing me as your own biological brother tunda bakiyi accepting auranmu ba “har cikin brain dinta take jin maganarsa tone din yake maganan bakaramin ratsa ta yayi ba shiru yayi taji lema na sauka a fuskanta tana dagowa taga kuka yake “sai taji wani irin rauni da tashin hankali at same time “ bata son ganin wani na kuka balle shi wanda a yanzu duk duniya bata dakowa bayan shi ahankali tasaka gefen veil dinta tana goge masa hawayan sa itama kaman zatayi kuka batasan dalilin kukansa ba amma har cikin ranta taji yanzu bata son rabuwa dashi bata taba zama so free tayi magana dawani a rayuwanta ba kaman shi bayan oum rufaidarh babu wanda yasan wani abu da yashafeta sai shi “yasan dariyanta yasan kukanta yasan jikinta yasan adadin cin abincin ta yasan adadin shan ruwanta yasan adadin kwananki mp dinta alluran dayake mata har yafi na dr khaleel ma bata taba jin ta damu wani a rayuwarta ba

kaman shi hakanan kawai she cares about him “ganin duk tazama so disturb da maganganun sa da kuma hawayan sa yasa shi yin murmushi yajawo ta jikinsa tayi lamo shima lamo din yayi kowa na sauraron bugun zuciyar dayan “,Dr ibrahim yace kinga muje dare nayi hibba tace tau kar mu katse musu soyayyya kuma, dr ibrahim yace rabu dasu sun karasa a gida “ tura kofan yayi aydarh tayi kokarin tashi daga jikin malik amma yaki bata dama ahankali malik ya daga idonsa yana kallon hibba da dr ibrahim kafin yace mu wuce right?dr ibrahim yayi murmushi yace ehhh sai a karasa soyayyan a gida kama hannunta yayi yasata a jikinsa sosai har kofan gidan dr ibrahim yakawo su kafin suyi sallama “kofan part din ya bude suka shiga fitan su kaman wani wutan soyayyan Aydarh aka kara masa ita kuma wani irin tausayin sa taji “duk motsin dayayi sai ta bisa da ido duk yana lura da ita “lokacin da ta fito daga wanka baya bedroom din vaseline din tashafa sama sama kafin tasaka wata gown marar nauyi tashafa perfume sama sama hula tasaka kafin ta kwanta kan gadon tana rufe har kanta da duvet “ ahankali yaturo kofan dakin yashigo kashe hasken yayi kafin walking very slow yakarasa kan katifan kusa da ita yakwanta kafin yajawo ta jikinsa yasauke wani ajiyan zuciya “itama lamo tayi a jikinsa tana jin wani irin nutsuwa duk lokacin datake jikinsa ko da kau tana jin tsoro sai taji kaman she is safe “ shiru shiru tana jiran taji ko zaiyi mata wani abu sai kuma yaji shiru,har bacci ya dauke ta shima baccin ya daukesa zuciyarsa na tayi mata azalzala dafin sonta na mamaye masa zuciya. Yace ko zaki je gidan dr ibrahim din? dasauri ta gyada masa kai yace tau je ki shirya ina jiranki kan carpet din yazauna itakuma tawuce bedroom din da sauri “can sai gata tafito tasaka doguwan riga tayafa veil akanta yama kasa dauke ido a kanta wallahi shidai sai kallonta,yamike yace go back and put on your hijab cuddle bug langwabar da kai tayi kaman zatayi kuka tace pleaseeeeeeeeeee muje ahaka lumshe ido yayi yana girgiza kai yace zan tafi nabarki fa “turo baki tayi kafin ta juya tasaka hijab din hadda nikkab ma ta dauko gani yayi ma Wallahi tafi yin kyau da hijabin “batace komai ta mika masa nikkab din tana turo baki murmushi yayi aranshi yace na tabo rigima fa nikkab din ya daura mata kafin yayi kissing goshinta yakama hannunta “suka fita rufe kofan yayi kafin suka fita bakin kofan gidan zasu samu keke “wani irin bacce ranta yayi ganin Ramlah she forgets when last da ta ganta kawai hannu malik kawai takama sukayi gaba kafin ma Ramlah takaraso “ganin tajasa yasa sa dinga kallonta har sukayi nisa kafin yace naga dai acan muke samun keke yau ko dai ance miki babu keke a can?aydarh ta hade rai duk da a cikin nikkab ne sai daya lura kafin tace ai wannan yarinya nasan data karaso sai tayi maka magana nikuma bana son Allah, malik ya dinga rike dariyar sa amma sai data fito kafin yace kinga yi hakuri nifa babu ruwana da ita ke kadai ce

kanwata kawai kinji?ta dinga kallonsa kafin dai takasa hakura tace kuma ni kadai ce matarka “baki bude yake kallonta shi mamakin kishinta yake ya lura akan kishi zata iya komai, murmushi yayi ransa yace Allah nagode maka zanyi amfani da wannan hanyar ganin yanata murmushi tace the smile is for? Ya girgiza kai yace no finest batace komai ba har suka samu keke “malik yafada masa inda zasuje suka shiga “yakalleta yace ke da wakike kama? Oum ko abba?tawara ido tace both of them yayi murmushi yace bangane ba kaman ya both of them fa? Tace to ni ai bansan ma da wanda nake kama ba “yace nidai da abby na nake kama tace ai kasa kallonsa nayi to bazan ce ga kaman sa ba yayi murmushi kafin ya riko hannunta yasa ana shi yacigaba da kallon titi “can tadago tace ehen aiki wani kala sir?yace as a medical doctor tace congratulations sir all your hard work has finally paid off am so excited for you! Ya jinjina kansa yace thank you my priority “tayi murmushi tana dage nikkab tace did you just said am your priority?ya girgiza kansa yace sure batace komai ta maida nikkab dinta tana murmushi, kofan gidan su dr ibrahim din aka ajiye su yabiya mai keken kudinsa “ suka wuce cikin zauran gidan suka ci karo da rabiah “ai yau ko damar gaishe da malik aydarh bata ,bata taja hannunsa suka wuce sai da suka shiga bangaran iya suka gaisa tayi masa murna kafin suka wuce bangaran dr ibrahim din “hibba ba karamin murna tayi ba ganin aydarh batayi tunanin tare zasu zo ba dayake dr ibrahim din ma already yashirya malik yake jira suje duba plot din ko zama basu yi dr ibrahim da malik suka wuce addua hibba tayi musu har sun fita kafin malik yadawo yarada ma aydarh yace karki ga bana nan ki kince bazaki ci abincin ba kinjini? Ta gyada masa kai tana murmushi sai kuma yace be a good girl “yayi mata waving hannu ita dai hibba sai kallonsu take “yana fita hibba tace ohni auntie aydarh wannan tsaban so har ina?aydarh tace kai auntie tafada tana cire nikkab dinta hibba ta dinga kallonta tace Wallahi auntie aydarh da sirrin dakike boye mun kan wannan glow din naki kodai wani lotion kike amfani dashi ko kuma yallabai yayi ajiya “Aydarh tayi dariya tace ba wata fa ajiyan dayayi auntie hibba yace bama yanzu ba nikuma I support my husband “hibba ta rike bacci tace ahh yayi masoya watau har yanzu ba a gama cin amarcin ba kenan tau Allah dai yasa adawo daga Washington ba a zo manah da triplets ba “Aydarh dai tayi dariya duk da bata fahimce maganar hibba ba tace “yace am still a baby fa tafada tana rufe ido hibba tace kid ai ce shi zai fara shanye milk din kafin babies din aydarh tayi saurin rufe fuskan ta da hijab tana dariya “kafin tace auntie kenan a da fa nafi haka Hibba tace wai lokacin da kina budurwa? Aydarh ta gyada kai tace wai shi yallabai soyayya kuke ko haka kawai aka hada ku “Aydarh tayi shiru bata son fada mata abunda yafaru gani take wannan sirrinsu ne “can tace shine fa yace yana sona kawai akayi manah

aure Hibba tace Wallahi yayi daidai Allah yakara bada zaman lafiya yakawo cutest masu kama daku aydarh tayi kasa da kanta “Hibba tace kwana biyun nan daurewa kawai nake amma sai na dinga tashin zuciya shima ya lura kawai dai sai nace masa ba komai, aydarh tace eyyerh auntie ko fever ne?ki fada masa sai yayi miki test ba “Hibba ta girgiza kai tace kema dai auntie aydarh ina tunanin kawai har nayi gamo “ Aydarh tayi shiru tace like?don bata fahimta bah ibba tace ina jin kaman inda ciki ne.

Aydarh tace congratulations auntie Allah yasauke ki lapia “Hibba tayi murmushi tace Ameen Ameen aydarh banda tabbaci sai dai anyi test din aydarh tace to auntie idan yadawo sai ki gaya masa ayi test din,Hibba tace in sha Allah ya islamiyan?aydarh tace Alhamdulilah muna ta fama fa exams zamu fara next week “hibba tace Allah yataimaka kila ma daga wannan week din bazaki sake zuwa ba idan kun tafi aydarh tace ana karatu Sosai amma kin sami auntie?hibba ta girgiza kai aydarh tace classmates din nawa sai ahankula kullun komai nasu a fade komai na gidansu sai sunyi sharing a islamiya kuma which is not good at all “hibba ta jinjina kai tace kinsan wasu matan kaman basu da hankali ko mi ma zance “ace baki da sirri komai na gidan ki sai kin gayawa kowa sai kowa yasani “ aydarh tace shine fa auntie “Hibba tace Allah yasa su gane aydarh tace Ameen kafin ta mike tace auntie bara nayi sallarh hibba tace tau shknn shiga nima banyi sallan ba aydarh tace ina ma da alwalla fa hibba tace tau shigo bedroom din “ Aydarh ta girgiza kai tace kibani prayer mat zanyi anan kawai hibba tace tau shknn abun salla takawo mata kafin ta wuce bedroom din ita sai datayi alwalla kafin tayi sallan “har ta fito aydarh na zaune kan prayer mat zama hibba tayi kan kujera tana kallon aydarh tace auntie aydarh ko muyi wainan flour shi nake son ci? Aydarh ta gyada kai tace tau shknn auntie hibba tace tau yallabai yana ci ne? Aydarh ta girgiza kai tace erh yana ci amma ba sosai ba gaskia ranan auntie hafsa ta yi manah amma bai ci ko biyu ba nidai kam ina so sosai, hibba tace dr kam na so Sosai ko sai ki girka masa ko jallof din macaroni? Aydarh tace ah’ah auntie kawai ayi wainan idan mukaje gida nayi masa girkin “hibba tace aaaaa aydarh kar nasake ji kar ki sake barin mijinki yawuce lokacin cin abinci bai ci ba saidai idan baya nan yanzu kinsan sai sun kwaso yunwa ga rana kafin su dawo kuma har sai kunje gida kafin kiyi masa girki?aydarh dai tayi shiru tana wasa da rings din hannunta bata ce komai ba Hibba tace muje sai kiyi greating kayan miyan akwai vegetables ma hadda kifi sai ki saka masa “Aydarh dai tace thank you auntie kitchen din suka shiga Hibba ta ba aydarh duk wani ingredients din da zata masa girkin “ kafin ta cigaba da harkan wainan flour ta “Hibba dai takasa dauke idonta daga kallon aydarh ganin yarda take girkin komai tsaf komai cikin

kwanciyan hankali, sunayi suna fira aydarh dai sai kokarin rike numfashin ta take saboda kamshin wainan flour dake damun ta “can dai tafara jin numfashin ta na seizing ta dai daure tayi shiru hibba kam sam bata ma lura da abunda aydarh keyi ba labari kawai take bata cikin kwanciyan hankali duk da aydarh bata amsata tacigaba da labarin daman tasan haka aydarh keyi “ can dai tafara tari ahankali ahankali hibba tace sannu auntie aydarh mura neba?aydarh ta girgiza kai tana cigaba da tarin ta hibba tamike ganin yarda aydarh ta rike chest tana tari non stop ga zufa dayafara keto mata dasauri takashe camping gas din datake suyan wainan flour daman takusa gamawa,karasawa tayi kusa da Aydarh tana tambayar lafiya ko sarkewa tayi cike da karfin hali aydarh ta girgiza kai idonta yayi ja tana jan numfashin ta dakyar “har tama kasa breathing din da kyau hibba data gama rudewa tace aydarh ko dai kinada asthma??????da kyar aydarh ta gyada mata kai aikau dasauri hibba takama ta suka shiga parlor banda inalilahi waina illahil rajiun babu abunda hibba ke fada sai jera ma aydarh sannu take tama rasa yarda zatayi ita Wallahi ganin yarda aydarh ke fighting da numfashin ta yasa hankalin hibba karasa tashi kama aydarh tayi tana kara gudun fanka kafin ta sake ta duk ta rude tana dage curtains din parlor da wani irin speed tashiga daki tayi dialing number dr ibrahim bugu daya ya dauke “yawani langwabar da murya yace did you just started missing me roohi?a rude tace dr kuyi sauri ku dawo Wallahi banyi tunanin aydarh is asthmatic patient ba kaurin wainan flour yasa asthma tashi dan girman Allah ku dawo “kashe wayan tayi ta koma parlor tacigaba da jera ma aydarh sannu Wallahi iyakan tashin hankali Hibba ahankalin ta yatashi bata masan taya zata taimaka mata ba kafin su iso duk ta gigice “ addua tacigaba da tofa mata “ .wallahi malik gani yake mai keken baya sauri du kinda hankalinsa yayi dubu yatashi dr ibrahim ke ta basa karfin gwiwa yayi hakuri ba abunda zai faru da ita amma ina bayaji sai ruwan masifa yake zubawa mai keken “shidai bawan Allah sai iyakan bakin kokarinsa yake daga mai keken har dr ibrahim sun masa uzuri saboda ganin duk yarda ya gigice “sunata basa magana “ ai suna isa kofan gidan dr ibrahim ko jiran mai keken ya tsaya bai yi ba ya dire “cike da sarfafa yake tafiya daga kansa kaga cikaken karfafan namiji mai ji da karfi gashin kansa har kwantowa yakeyi “sallama yayi yashiga aydarh na rungumai jikin hibba duk ta gama galabaita, tana ganinsa “kwalla yasauka idonta ai hannu yasa kawai yayi sama da ita kafin hibba ta mike ta zira mata hijab dinta “kaman baby haka ya fita da ita rike hannu dr ibrahim da bai sallami mai keken ba yabasa hanya shiga da ita rike a hannunsa duk ya rude ya gigice dr ibrahim yashiga gaban keken ,mai keken ya tayar suka wuce clinic”dr ibrahim yakira hibba yace ta rufo gida tasamu keke ya kawota clinic kafin kashe wayan “ Wallahi malik kaman ma ba dr ba don yakasa yin

komai ma kallonta yake kawai har suka isa clinic din yafito da ita 2k dr ibrahim yafito ya mikawa mai keken yayi masa godiya da adduan Allah yabata lafiya dr ibrahim ya amsa masa kafin ya rufawa malik baya ,emergency room din malik yashiga ya kwantar da aydarh kan gado hawayen dake fita a idonta da yanda take fighting da breath dinta yasa jin wani irin rauni kawa isai hawaye sharrr Wallahi dr ibrahim kasa boye mamakinsa yayi malik kuma kuka?ganin malik bai ma da niyyar yin komai don dr ibrahim ya fahimce malik yamance waye shi yasa kiran nr saratu dake nan reception dr hafsa bata kai da zuwa ba,bai ce wa malik Komai yabarsa nan rike da hannuta yayi kasa da kansa itama ta rike hannunsa sosai kaman zaa kwace mata shi, dasauri dr ibrahim da taimakon nr saratu sukayi kokarin daidaita numfashin aydarh cikin few minutes sukayi mata allura cikin abunda bai fi ten minutes bacci ya dauketa ahankali tafara ajiyan zuciya a wahale kadan kadan sai lokacin malik da idonsa yayi jawur ya dago kai,yana kallonta ko dauke ido babu hannunsa yasa yagoge mata hawayen dake nan a fuskan ta kafin shima yadago hannunta yarike yadinga goge hawayen fuskan sa da hannunta “ sai kallonta yake wani irin kyau tayi masa mai daukan hankali lashes dinta sun tattare wuri daya wanda ruwan hawaye ya jikasu, dr ibrahim daya shigo dakin ya kalli malik yace katashi muje masallaci in sha Allah she will be alright yallabai ai kasani dai malik kaman bazai tashi ba dan kona second daya baiyi missing kallon fuskanta ba ahankali yasaki hannunta kafin yasaka Hijab dinta ya rufe mata jikinta dr ibrahim dai sai kallonsa yake, ahankali yake bin bayan dr ibrahim duk yayi wani kala a bakin kofan clinic suka hadu da hibba dauke da basket din Abinci gaishe su tayi kafin fuskanta cike da damuwa ta tambaye su ya jikinta dr ibrahim ne ya amsa mata da sauki kafin ya nuna mata dakin yace tana ciki ta samu bacci hibba tace musu tau kafin da sauri ta nufi hanyar dakin dr ibrahim yabi ta baya yana karban basket din hannunta shidai malik yayi shiru ya lumshe ido,sai da yakai mata basket din kafin yadawo ya tarar da malik nan inda yabar sa suka wuce masallacin magrib,hibba na shiga ta zauna kan plastic chair din dake dakin tayi shiru Wallahi duk tadamu sai taga kaman ita tasaka ta cikin wannan halin gani take kaman ita taja mata duk wahalan,basu suka dawo bas ai da aka gama Isha’I ,hibba nayi musu sannu da zuwa dr ibrahim kawai ya amsata yana tambayar ta ya mai jikin ta farka?hibba ta girgiza kai tace aaaaa bata farka ba fa bacci kawai take dr ibrahim yace tau masha Allah Allah yakara lafiya Hibba tace Ameen kafin tace bara nasaka muku abincin dr ibrahim yace bara muje office nan kar motsin mu ya tayar da ita, yakalli malik yace yallabai muje office “sai sannan malik yadago ya girgiza kai yace kuje ibrahim zan zauna da ita zanci abincin anjima in sha Allah dr ibrahim yayi shiru yace tau shknn yallabai

Allah yabata lafiya, malik yace Ameen hibba ma addua tayi masa kafin ta dauki warmer wainan flour da plate sai rubber yaji tabar dayan warmer shape pasta dasauran plates din tabi bayan dr ibrahim bayan fitarsu malik ya kwantar da kansa bisa gadon ya lumshe ido ,har wajan ten bata farka ba lokacin har dr hafsa ta iso “dr ibrahim yayi masa sallama yace zasu tafi in sha Allah gobe daga masallacin asuba zai shigo ya sallamesu ya mikawa malik sauran drip da alluran ta na daran tunda in sha Allah da angama dosage din suke nan hibba ta kalli malik kafin tace am sorry yallabai bada gangan nayi ba,malik yayi murmushi yace ba komai amarya mungode sosai Allah yasaka da alkhairi hibba tace babu komai yallabai Wallahi duk anzama daya.

Sai wajan karfe sha biyun dare aydarh tafara bude ido ahankali kanta yayi mata masifan nauyi “ahankali tasauke idonta kansa hannunsa rike da hannunta dake da karin ruwa,ya kifar da kansa kan gadon hannunta ta dago wanda babu karin ruwa ta taba fuskan sa da sauri ya dago kansa “kana ganinsa kasan bai da kwanciyan hankali dasauri yakara rike hannunta yana jera mata sannu ita dai ganin duk ya gigice yasa ta dinga kallonsa da idonta dasukayi laushi kallo daya zakayi mata kasan ta wahala a yau din nan “ahankali tabude baki tace zanyi fitsari tafada tana kallon drip din dake sa mata mikewa yayi dasauri yakama hannunta “kaman mai tsoro ji mata ciwo ahankali ya cire mata drip din kafin yasa hannu ya dakata jikinta babu karfi ko guda, ya dinga jera mata sannu kafin yasa hannu ya dauke ta daf yayi hanyar toilet da ita toilet din dake wanke very neat “ya daura ta kan sit kafin ya dage mata riga zai taimaka mata “dasauri ta rike masa hannu tana girgiza kai kafin ahankali tace zanyi ka fita, malik bai ce komai ba ya juya yafita yana jiranta bakin toilet din bayan tagama tace naga ahankali dasauri yashiga toilet din ya daukota kaman yarda yashiga da ita ya kwantar da ita kan gado kaman wanda zai ajiye kwai “ita dai takasa daina kallonshi “drip din ya mayar mata tadan runtse ido kadan alaman taji zafi a rude yashafa kanta yace sorry jewel it will not you anymore cuddle bug sannu kinji ita tausai ma yabata ganin duk yayi wani kala batace komai bat asa hannunta kan nashi kafin tamaida idonta tarufe tana sauke numfashin kadan kadan “ ahankali malik yace mi zaki ci?ta girgiza masa kai tace babu,malik yayi shiru kafin yace bara nakira hafsa ta zauna dake akwai wani eatery anan kusa sai nasiyo maki ko irish ba?ta girgiza kai kuma tace nakoshi zan sha ruwa Malik da kaman zaiyi kuka bai ce komai ba ya dauko ruwan dake cikin basket din da hibba ta kawo masa sai lokacin ma ya tuna da abincin yasan ma bazata iya ci ba shima bazai ci tunda ya huce bottle water ya dauko mata kafin ya koma sai daya tayar da ita zaune yasata ajikinsa,kafin yafara

bata ruwan kusan rabin roban tasha kafin ta kwantar da kanta a chest dinsa tayi lamo tana sauraron bugun zuciyansa shima shiru yayi yana patting bayanta “ tari tayi kadan tasake mayar da kanta ta kwanta sannu yayi mata ahankali kuma yayi placing hannunsa a kirjinta kusan ten minutes suna ahaka har bacci ma yafara daukanta ahankali akayi knocking malik yace yes “still bai saketa ba kuma bai dauke hannunsa daga kirjinta bai ta kuma bata ma da energy tashin duk data so hakan dr hafsa tayi sallama tashigo tana maidan kofan ta rufe “ta dauke kanta har takaraso kusa da gadon kafin ta kalli aydarh data sake rufe idonta ala dole bacci take dr hafsa kuma tasan kunya ce aydarh keji ita har mamakin kunyar yarinyar nan take “ tayi murmushi kadan tace naga ta samu bacci ma? Malik ya gyada mata kai kawai duk da yasan aydarh ba bacci take ba kafin yace yauwa dr ki zauna please zanje eatery din nan baya nasamu mata abincin bana tunanin tun breakfast tasake cin komai ba dr hafsa tace tau shknn yallabai sai kadawo naga kusan pass 12 yanzu ko zaa samu?malik yace erh nasan zaa samu in sha Allah dr hafsa tace tau sai kadawo malik ya mike ahankali ya daura kanta bisa pillow kafin yamike ya fice,bayan fitan malik dr hafsa tace sannu aydarh aydarh dai tayi shiru ala dole bacci take dr hafsa tayi murmushi tana girgiza kai bata ce komai ba ta cigaba da zama anan “ can ta bude ido jin kaman tana sake jin kishirwa “kafin tace auntie zan ruwa dasauri dr hafsa tamiko mata sauran ruwan da malik yabata yanzu tasha kafin ta zauna tana jinginar da kanta da kan gadon dr hafsa tace bara dai nasaka maki pillow ai karfan ba dadi aydarh ta tace to “pillow tasaka mata kafin tasake yi mata sannu ta amsa Still taki bari su hada ido ganin hakan yasa dr hafsa ta rabuwa da ita tadawo tayi zamanta “ahankali malik yaturo kofan yashigo hannunsa rike da ledoji dr hafsa ta amsa mashi sallama kafin ta mike tace sannu da zuwa yallabai kasamu kenan?malik yace ehh dr suna nan ya jikin nata?dr hafsa takalli aydarh dake kallonsu tace ah dasauki alhamdulilah “malik yace nagode dr yafada yana mika mata leda daya daga cikin ledojin hannunsa dr hafsa tayi sauri cewa aaaa fa nagode yallabai kabarsa malik yace no naki ne ai “Dr hafsa tasa hannu ta karba kafin tasake masa godiya ta fice “tana rufu kofan ahankali yake tafiya har yakarasa gaban gadon ya ajiye ledojin kan drugs drawer,yace mata sannu kai kawai ta gyada masa tana binsa da ido juyawa yayi yadauko plate daya cikin basket din sai dayashiga toilet din dauraye sa duk da bawani amfani akayi dashi ba kafin ya fito yazuba mata lafiyayan chips din daya ji ketchup ansuya kwai baba sai pepper chicken kadan agefe dayan ledan kuma fruits ne aciki ahankali ya mika da ita kaman dazu haka yasake sakata ajikinsa “ yashafa kanta yace kadan zaki ci sai nayi miki allura “kinga dasafe zamu wuce gida kwara ki ji sauki baki daya jibi Saturday islamiya right?ahankali ta gyada masa kafin

yadauko chips din yafara bata ta bude baki yanda take chewing ahankali ahankali bakaramin shaawa tabashi bah akan yasa sa shagala da kallonta “ba laifi taci Sosai don ko kazan taci kusan two pieces kananu” kafin ta dauke kanta ruwa yabude yakai bakinta tasha kafin yace ki Kara abincin ko kadan ta girgiza masa kai yace please cuddle bug har kwalla yafara taruwa a idonta “tace amai zanyi idan nasake ci kuma yana bani wahala “ai dasauri malik ya ajiye chips din yana dauko wani plate yarufe sa “ita dai sai kallonsa take yadauko injections din da sauran kwara biyu kuma waje daya zaa hade yahade kafin ya matso kusa da ita gabanta dai sai faduwa yake kaman tace bata so duk bashi da zafin allura ko dan amma tsoron alluran take ji, ahankali yazo kusa da ita kafin yasa hannu yadage riganta ai take white soft laps dinta suka bayana dake nan very soft and creamy har wani dan banza glow glow suke har saida zuciyansa ta motsa dasauri ya dauke kai jin yana neman loosing “ita dai ta kankame pillow tarufe idonta da bugun karfi gabanta tana faduwa “kadan yasa hannu ya janya black pant din jikinta yayi mata alluran “yazare syringe yasa hannu yana luliya wajan har sai dayafara luliya mata kafin tabude ido sai sannan tasan yayi mata Amma ko kadan bata ji zafi ba,tun tana sauraron yacire hannunsa amma sai taji shiru daga luliyan wa yacigaba da shafa wajan wanda take jin tsikan jikinta nawani iri “ ya dinga sauke ajiyan zuciya yana zagaye hannunsa gabanta kau ya yanke yafadi cikin karfin hali tasa hannu tarike nasa ahankali ta tashi zaune tana kallonsa shima ita yake kallo da idonshi dayayi wani iri, Tace kaci abincin kai?ya girgiza mata kai still his eyes on her tace to kaci ai kaima tun breakfast baka sake cin komai bay ace mata zanci tace ban yarda ba carry the food I will feed you “dasauri yakalleta kafin yace really?ta gyada kai tana wani cute smile tace sure abincin yadaura kan laps dinta yana kallonta cheeks dinsa ta tallafa looking so cute tafara bashi abincin “aikam sai lokacin yasan yana jin yunwar feeding dinsa take shikuma sai kallonta yake ko dan kiftawa babu fuskan ta sharr looking so pale and sick “ har ya kusa cinyewa kafin ahankali ta bude bottle water takafa masa baki tana basa tass ya shanye ruwa tass ya cinye abincin kafin tayi murmushi tace daman you are hungry sir “malik yayi murmushi kafin yadauke plate din yasaka a basket din yashiga toilet yadauro alwalla kafin yacire rigansa daga shi sai singlet yasa hannu yayi switching din hasken dakin ita dai sai kallonsa take “gadon ya hauro yasata jikinsa kafin yagyara mata hulan kanta yasaka duvet ya rufe su shigewa jikinsa tayi sosai ya cigaba dashafa bayanta ahaka har bacci ya dauketa rungume dashi shima baccin ya daukesa “kiran sallarh farko yafarkan dashi bakinsa dauke da addua ya bude ido yana kallonta ko dauke ido babu bacci take very peaceful a jikinsa ahankali ya zareta daga jikinsa Still bata farka ba, yawuce toilet alwalla yayi kafin yafito ya shimfida

prayer mat din da dr hafsa takawo masu ya tayarda salla motsin sa ya tayarda ita tayi lamo kan gadon tana kallonsa har ya idar da sallan kafin yayi azkar yataso yadawo gaban gadon da niyyar tayar da ita yaga har ta farka ma" bai ce mata komai ba yataimaka mata tayi alwalla ta fito anan kan carpet din tayi sallarh kafin ahankali cikin voice dinta dake very calm and sweet tace ina kwana? Yace lafiya lau cuddle bug ya jikin?ta gyada masa kai ahankali tace dasauki yace da sauki sosai ta gyada masa kai yace tau Allah yasawwake yabaki lafiya tace Ameen "tayi shiru shima bai sake cewa komai ba "dr hafsa tayi knocking tashigo,ta gaishe da malik kafin ta amsa gaisuwan da aydarh ke mata cike da fara"a dr hafsa tace how your body? aydarh tace so much better auntie "dr hafsa tace tau masha Allah Allah yakara afuwa " zuwa anjima nasan dr Ibrahim zai shigo ko rufe baki batayi basai ga dr Ibrahim din yaturo kofan yashigo da sallama malik da dr hafsa suka ams asa dr hafsa tace dan halak kenan yanzu fa muke chanza ka,dr Ibrahim yashafa kansa yace Allah dai yasa ba gulmana ake ba?malik yace ai sai abunda dr hafsa kawai ta manta ke bata fada kanka ba,dr hafsa tarufe baki tace lah kai yallabai aydarh dai tayi murmushi tana kallon malik tayi masa hararan wasa dasauri yawara hannunsa alaman ba ruwansa "fa yasa hannu yana kama bakinsa aydarh tace Doctor babu fa abunda auntie tace kashigo dr Ibrahim yace nasani ai kinsan maybe shi yafadi ma wani abun dr Ibrahim yafada yana dariya "kafin yaba malik hannu suka gaisa yana tambayarsa ya mai jikin?malik yace alhamdulilah dasauki jiki ya warware " yafada yana kallon aydarh,dr hafsa ta gaishe sa ya amsa yana mata sannu da aiki kafin aydarh ma tagaishe say ace ya jikin amarya?aydarh tace dasauki alhamdulilah kanta a kasa "dr Ibrahim yace ai idan gari ma yakarasa wayewa sai ku tafi gida yallabai,malik ya gyada kai yace tau in sha Allah kafin malik yace ka koma manah Ibrahim babu komai Wallahi kabaro amarya ita kadai "dr Ibrahim yace ai kwara nazo naga ya jikin tunda jiya dakyar aka samu ka daina kuka duk ka daga manah hankali malik yayi shiru kafin yace ehh ai babu komai tunda dai kuka kawai nayi dr hafsa tayi murmushi tace ohhni yallabai kuka fa? Dr Ibrahim yace kuka fa nake gaya miki na sosai din nan " aydarh dai tayi kasa da kanta jin ance yayi kuka jiya sai tayi murmushi kadan " dr Ibrahim yace idan kun wuce zan kawo roohin gida idan garin yakarasa wayewa malik yace tau shknn abokina Allah yasaka yabar zumunci dr Ibrahim yace Ameen Ameen har bakin clinic malik yarakasa kafin yadawo, itama dr hafsa office ta koma tana hada kayanta tana jiran zuwan nr saratu itama tawuce gida. Wajan 7:00am suka shigo gidan tun kofan gida sukayi sallama da dr hafsa malik yasake mata godiya " bedroom ta wuce ta kwanta kan katifan tana maida ajiyan zuciya tana lumshe ido, kitchen yashiga yadaura mata ruwan wanka kafin yadawo

parlor yazauna kan carpet kusan15 mins kafin yakoma yadauko bucket yahada mata ruwan wanka “yamatsa kusa da ita murya cike da lallashi yace tashi sai kiyi wanka kafin nan nadafa miki shayi sai ki sha ki sha magani ki kwanta “Aydarh ta gyada masa kai kafin yajuya yafita ita kuma ta tashi tawuce toilet din wankan tayi tass, kafin tafito daure da towel tasaka hijab ta rakube kan katifan sai data goge jikinta tafara shafa vaseline din kafin tagama pant kawai tasaka tashafa perfume kafin tasaka plain gown marar nauyi ash tasaka hula “daidai lokacin yashigo da cup rike hannunsa wanda yahada mata shayin yashigo yana kallonta ko dauke ido babu kaman zai hadiyeta tsaban kyaun daya gani tayi masa cup din yamika mata yace sha sai ki sha magani sannu “karba tayi ta rufe ido tafara shan shayin har kusan rabi kafin ta ajiye ganin tasha har kusan rabi yasa shi balla mata maganin ya mika mata sai data ya mutsa fuska kafin ta karbi maganin ta rufe ido gam ta sha kafin ta ajiye cup din “ahankali yakalleta yace sannu ta gyada masa kai kawai tayi shiru ta zame tana kwantawa lumshe ido tayi yasa hannu yana rufe mata jikinta da duvet din kafin yashafa kanta yayi mata da addua ya kwashe cups din yafita sai daya gyara kitchen da parlor ya wanke kayan da baa wanke ba kafin ya juya ruwan yashiga toilet yayi wankansa tass kafin yafito kofan bedroom din yabude without making any sound yashiga vaseline yadauko da comb sai perfume da jallabiyan dazai sake kafin yafito parlor ya chanza kayansa yashafa man yasaka perfume din kafin yayi combing kansa “yawuce kitchen din tea yahada yadauki sauran bread din yadawo parlor yayi sha kafin yamayar kitchen yadawo ya kwanta nan kan Carpet din bayan few seconds bacci ya daukesa.

Sai wajan ten ya farka shima vibrating din wayansa ya tayar dashi dauke da addua yabude bakinsa “ ahankali ya tashi zaune yana duba wayan dr ibrahim n eke kiransa har ta kusa katsewa ya dauka yakara a kunne “cikin voice dinsa da alaman yanzu ya farka daga bacci ya amsawa dr ibrahim sallaman dayake masa,daga can dr ibrahim yayi murmushi yace easy yallabai bazaa iya mata hakuri ba malik daya fahimce abunda dr ibrahim yake nufi yayi murmushi kawai yana shafa kansa,yace kaji dashi dr ibrahim yace tau daman dan nagaya maka basai kunyi lunch ba ga hibba na nayi hadda ku wajan twelve in sha Allah zamu shigo “ ai kasamu kiran dr usama ba?malik yace nayi receiving message dinsa dai so I told him bata da lafiya dr ibrahim yace Allah sarki idan nazo sai muje mu same sa bayan la’asar haka malik yayi shiru kafin yace tau shknn Allah yakaimu daga sukayi sallama ya katse wayar “sai daya shiga toilet ya wanke fuskan shi kafin walking very majestic yanufi hanyan bedroom din ahankali ya bude kofan a tunaninsa bacci take sai yaganta zaune a kan katifan “ta lumshe idonta

kallonta yayi kusan 2mins kafin ya maida kofan dakin ya rufe “ yayi sallama sai sannan ta amsa masa tana bude ido ta zuba mashi idon tana kallonsa ko dauke ido babu shima hakan ita yake kallo har ya karaso ya zauna kusa da it akan katifan yasa hannu yana kama hannunta ahankali tace “bacci kayi? Gyada mata kai yace kin tashi lafiya ya jikin? Tace lapia lau “so much better yace tau sannu tace yauwa kafin yayi shiru can yace why didn’t you tell her bakya son smoke?aydarh tayi shiru tana komawa ta kwantar da kanta kan pillow ahankali ta rufe idonta shidai kallonta kawai yake “tace naga last time damukayi da auntie gidan inna bai mun koma ba shiyasa, yace ai can akwai iska ko ba tsakan gida kukayi sa ba kuma akan murhun gawaye?ta gyada masa kai yace nan a kitchen ne right kan camping gas right?ta gyada masa kai baice komai ba yayi shiru kafin yasa hannu ya rike hannunta tadan bude ido taga kallonta yake ta mayar ta rufe ahankali ya cigaba da murza hannunta cikin nasa, yana cigaba da kallonta ko dan kiftawa babu,daga kanta har zuwa chest dinta wanda sai yanzu ya lura ma babu bra gasu nan very bounce and balloon yah Allah “ahankali yace why didn’t you put on brassiere?dasauri ta bude ido ta kallesa kafin ta dauke kai tana turo baki tace aie chest dina is still aching me yace ohk” kafin yace mi zaki ci yanzu kinga shayi kawai kika sha dr ibrahim yace we shouldn’t prepare anything for lunch matansa zatayi “Aydarh tace eyyerh ai dabasuyi ba ,sai kai kayi tunda ance you cry all over yesterday, malik yayi murmushi yace waya gaya miki tace ina jiya gabana Doctor yake fadawa auntie “malik yayi shiru “Aydarh tace Doctors fa basa kuka “yace ni I didn’t even know what makes me to cry cuddle bug,aydarh ta gyada kai tace to daga yau karka sake kuka kaji boyyie?malik ya gyada mata kai yana murmushi baice komai ba ahankali ya kwantar da kansa gefen cikinta,hannu tasaka tana shafa masa suman kanshi dake very black and soft, shiru dukkan su sukayi babu mai magana cikinsu kowa da abunda yake tunanin a ransa “Allah ya nuna mashi ranar dazai mayar da ASSEIYARH tashi Allah ya nuna mashi ranar dazata haifa masa yara kyawawa kaman ta Allah yanuna masa ranar dazai koma cikin ahalinsa Allah yanuna masa ranar dazai dauki dawaniyyar kowa na ahalinsa “Idan Allah duk yacika masa wannan burin kuma Allah yasa mahaifinta yabar auransu yasan zai mayi wuya “ malik yamike ahankali yana dafa kanshi idan yana tunowa da haka ji yake kaman ana kona masa zuciya kaman ana daura masa garwashi a zuciya baisan lokacin da dafin sonta yashigar mashi zuciya ba “idan akwai ciwon dazai kassara rayuwarsa tau ciwon rabuwa da ita ne wanda baya ma fata ko na seconds gudu “yarda ya tsara suna Washington da two months zai dauketa su koma adamawa su nemi yafiyar iyayansu su fara sabon rayuwa “ abu daya yake ganin zaiyi wanda dakyar abban yara basu kuma in sha Allah bazai chanza komai ba sai

ya koya mata soyayyar shi da har abada bazai goge ba zai koya mata sonshi irin son nan da baa son ko jin kalman rabuwa sake maida kansa yayi bisa gefen cikinta yana saukan da ajiyan zuciya ita dai aydarh mamakinsa kawai take sau tari tana ganin damuwa a fuskanshi gakuma yawwan tunanin,batace komai ba ta kama hannunsa tayi masa alaman daya kwanta Sosai kwanciya yayi gefenta tasaka duvet tarufe sa “ kallonta kawai yake yana kara jin wutan sonta nasake ruruwa a ransa daman ance shi SO BA KAMA bane jawota yayi jikinsa kirjinsa dana ta suka hadu wuri daya ita tarasa gane kanta yanzu duk lokacin dazai tabata bata iya hanasa kaman ma wani so take yataba tan “shiru tayi tana sauraron yarda yake kokarin placing hannunshi a fatan boobs dinta kanshi yashigar a neck dinta yasaka hannunshi ta saman riganta yana shafa boobs dinta tayi lamo duk tsoron data ke ji amman takasa hanashi “ ganin dai bai da niyyar bari ita kuma bata iya hanasa yasata sakar masa jikinta baki daya “babu inda bai kissing yashafa ba daga kan flat tummy dinta zuwa fuska “ bashi yabarta bas ai wajan 11:30shima baya yatashi bane aaa yana manne jikinta wasu irin pleasures na rantsa sa,ita dai tayi shiru jikinsa har yanzu kuma hannunsa na riganta baya son dauke hannun ko na one seconds shi fa bai taba tunani how sweet boobs is bas ai kanta ko a school duk daya karata ya karanta textbooks kala kala kuma yanada lalura amma ko sau daya bai taba imagining ba ,she has the best boobs ever “ big balloons boobs dake bouncing cikin hannunsa nasa shi jin yana aljannar duniya yau da batayi kokarin hanasa yin komai bas ai yaji kansa nawani irin girma “ ahankali yazare hannunsa ya mike yashiga toilet dinta wanka yayi yafito dagashi sai boxers Ko singlet babu sai karamin towel dayake goge kansa six packs dinsa ga gashi daya kwanta kaman jikin larabawa farine bana wasa ba har ja ja yake ga tsawo “bai da giba amma ko ina na jikinsa a murde yake irinsu ne idan suka dake ka kake shiga uku “bazata ma iya juran kallonsa ahaka ba kunya take ji yayi babba dayawa “yasata yin saurin rufe idonta, shi bai masan tanayi ba goge jikinsa kawai yake kafin yaje gaban wardrobe ya dauki vaseline ya zauna yana shafawa “ jallabiya kawai yasaka yana fesa perfume ko combing gashinsa baiyi ba yabarsa ahaka “kallo daya yayi mata yasan ba bacci take ba rufe idonta kawai tayi girgiza kai yayi kafin yace na siyo miki apples ? Dasauri ta girgiza kai Wallahi bata son yafita ita bata taba ganin namiji mai kyau ba kaman abbanta dashi “idan akaga abbanta aka gansa sai ka rantse da Allah shine babansa “ yace tau mikike so ne?tace babu komai idan auntie hibban tazo sai naci ai bana jin yunwa ma gyada kai yayi yace tau “ kitchen yashiga ya daura ruwan zafi kafin yadawo bedroom din ya zauna kan carpet babu wanda yayi wa wani magana cikinsu kusan 10mins kafin ya tashi ya koma kitchen din bucket yadauka ya juyu mata

ruwan zafin yakai mata toilet din bedroom din “ ahankali yace tashi sai kiyi wanka lokacin sallarh ma ya kusa tace to mikewa tayi ya dinga bin waist dinta da kallo ko kiftawa babu har tashige bayin kafin ya dauke idonsa bedsheet din ya gyara kafin ya koma kitchen yadauko tsintsiya da mopper,sai da yashare dakin yayi mopping sharp sharp.malik yabude musu kofan suka gaisa yana basu hanyar wucewa “basket din hannun dr ibrahim ya ajiye kafin su sake gaisawa hibba na tambayar ya mai jiki malik yace bara nakirata nasan batasan kunzo ba “hibba tace jikin dasauki dai koh malik yace eh amarya bana fada mata kunzo malik yafada ya mikewa yanufi hanyar bedroom din yana shiga ya tarar ta kokarin daure gashinta bayan tasaka gown din atamphar sai kamshi mai dadi ke fita daga jikinta “karasawa yayi kusa da ita tamika masa ribbon din tana tura masa baki kaman zata fashe da kuka murmushi yayi ya karbi ribbon din ya mata parking kaman yanda yake mata kafin yadauki hulan yasaka mata yace tau fito amma kisaka hijab gasu dr ibrahim nan ta kallesa kafin tace hijab kuma sir?bayan nasaka hula malik yanuna mata boobs dinta dake showing daga sama yace ahaka shi ibrahim din zai ganki?dasauri ta dauke kanta ta bude wardrobe din tafito da well ironed hijab dinta tasaka tare suka fito yana gaba tana binsa a baya “murmushi tayi takarasa kan carpet din ta zauna kusa da hibba “kafin tace ina wuni Doctor “dr ibrahim yace lafiya lau madam ya jikinki kuma? Aydarh tace dasauki Alhamdulilah “ kafin ta kalli hibba tace welcome auntie hibba ina wuni?ya gida hibba da murmushi tace thank you patient lafiya lau alhamdulilah y karfin jikin aydarh tace dasauki sosai auntie hibba “hibba tace banji dadi ba aydarh dasai Ki gayamun you are asthmatic patient amma kikayi shiru fisabillahi?aydarh ta kalli malik da tun dazu ita yake kallo ko kiftawa babu kafin tayi murmushi tace ba komai fa auntie hibba banyi tunanin smoked din zai yi har haka amma ai naji sauki “ malik yace babu komai fa amarya duk kin damu babu komai shidai dr ibrahim murmushi kawai yake bai ce komai ba,kiran sallarh akayi yasa malik mikewa yana kallon dr ibrahim yace tau muje masallaci “dr ibrahim yace Alright idan muka dawo sai muyi lunch mu wuce kawai “kafin ya kalli Aydarh yace karki alwalla da cold water akwai warm water a flask there are not hot basai kin sirka ba hun “kanta akasa tace ohk “hibba tace sai kun dawo suka amsa suna ficewa “ hibba tace ina ma da alwalla bara nayi sallarh anan kawai aydarh tace to “auntie bara na dauko miki prayer mat,hibba tace tau shknn abun sallarh ta shimfida mata kafin itama ta koma bedroom ta kabbara sallan “ .ko da suka dawo daga salla suna nan zaune a parlor suna fira ganin sun shigo yasa hibba yin shiru daga abunda take fadawa aydarh “ hibba tace sannunku da zuwa dr ibrahim yace yauwa wife “a zuba manah abincin muna sauri malik na shafa kansa ya kalli dr ibrahim

yace sarki mai abincin everything food anything food everytime food aydarh takalli malik jin abunda yake fada kaman shi din ma bahaka yake ba “ ahankali tace what about you sir “hibba tayi murmushi tace yauwa rama manah dasauri dr ibrahim yace kiji shi fa idan muka fita har Allah Allah yake yadawo sai kiji yana cewa nasan yanzu ASSEIYARH ta karasa girki Doctor muyi sauri please malik na dariya yakalli malik yace you should fear Allah mr man “dr ibrahim yace ita kanta matar taka ai tasani baka da hakuri indai bangaran abincin ne “malik yayi shiru sai kallon aydarh yake datake masa dariya kasa kasa “kasancewan hibba hadda plates da serving spoon ta sako “yasa tafara serving malik da dr ibrahim din a plate daya vegetable white rice ce sai stew da kaza a ciki sai coslow a cikin jug din kuma blue sparkling ne sai lemon kadan data yanka a ciki “ a cups ta zuba musu mock tail din kafin ta saka musu ita aydarh “Aydarh ta mike tace muje bedroom auntie sai mu ci ba?hibba tace aaaa kawai mu zauna anan malik yadago yazuba mata ido yace promise me idan kunje can you will eat?aydarh ta langwabar da kafin tagyada masa kai kawai malik yace amarya kuje can din please taci abincin hibba tayi murmushi tace in sha Allah yallabai aydarh ta rike musu plate din abincin ita kuma hibba ta rike two cups din suka shiga bedroom din ansaki curtains din ga kamshin freshener da perfumes dinsu dakin gwanin dadi Hibba ta ajiye tana kallon aydarh da tazauna kan carpet kafin itama ta zauna tace wai auntie aydarh duk kamshin ne haka wani irin turaran wuta ne wannan please?aydarh tayi murmushi tace nikam ban sani ba shidai yadawo dashi ranar ban ma san inda yasiyo sa bas ai dai ko na tambayar miki shi tafada tana mikewa hibba tace aaaa kibari kin tambayesa ba yanzu bak i zauna muci abincin yanzu “da kadan kadan suke ci suna fira sai gashi aydarh kam ta ci abincin ba laifi duk da ta riga hibba fidda hannunta “kafin ta dauki cup din tace woaw auntie fave dina ne fa mock tail din nan hibba taware ido tace kai haba??aydarh ta gyada kai tace Allah auntie zaki koya mun ma please?hibba ta gyada kai tace ehh mi zai hana zan koya miki manah tace to ngd sosai “shima mock tail din duk kiran fave dinta ne bata wani sha dayawa ba ta ajiye “malik yayi knocking kafin ahankali yayi sallama yashigo ya kalleta kafin yamika mata drugs dinta da bottle water tayi wani iri da fuska kaman zata fashe da kuka shikam yakasa dauke ido daga kanta sai kallonta yake hibba tamike rike da plate din da kuma cup din datasha mock tail din tace bara naje parlor fita tayi tabarsu tana rufu musu kofan zama yayi kusa da ita yana.

Tace erh yawuce yace tau sannu “ tace yauwa yace numfashin yadawo daidai ne?ta gyada masa kai,ahankali yace tau take care zamuje can gidan dr usama ta kallesa batace komai ba tayi shiru yace sai mun dawo “kafin ya

mike ahankali ta rage murya tace Allah ya tsare “yace Ameen Ameen yafada yana mata waving hannu itama hannu ta masa waving ya fice anan parlor ya tarar dr ibrahim da hibba zaune sun hada kai yana nuna mata abu a waya “malik yace tau mutafi dr,dr ibrahim yace Alright kafin yakalli hibba yace sai mun dawo tace Allah yatsare ya bada sa”a yace Ameen juyawa sukayi suka fita,aydarh tafito da cup din mock tail din wanda Still akwai a ciki ta karaso ta zauna kusa da hibba,hibba tace sannu auntie aydarh “Aydarh tayi murmushi tace yauwa auntie ngd “hibba tace babu komai wai ya chanza Ramlah?aydarh ta wara ido tace har kinsa ma natuna ta ai nagoge digits dinta a wayansa , Hibba tace ahh yauwa kinyi daidai shima yallabai dai ai yasan wannan yarinyar is not his type neman dalili ne kawai fa irin na maza “Aydarh tace ai saura kadan yasa mun bp saboda ita gashi nifa bana sonta batayi mun ba sam auntie bana son mutun most especially mace ma mai rawan kai shi kansa duk da baya magana auntie hafsa sai da tace mun ranar yayi mata fada, Hibba tace bafa sonta yake ba amfani kawai yake da ita against you aydarh!aydarh ta gyara zama she is little bit confused tace against me kuma?like?hibba tace aydarh kenan shi fa namiji a kullun so yake ki mayar dashi tamkar yaro karami so yake ki dinga ririta shi kaman dan goye shiyasa nace miki auntie aydarh wannan halin naki na miskilanci yayi yauwa na tabatta akwai abunda yayi lacking a wajanki yasa shi yin amfani da Ramlah ba wai don yana sonta ba billahi ni nagaya miki wannan ki nutsu tsaf kawata kiyi tunani “Aydarh tayi shiru tama rasa kalan tunanin daza tayi maganar hibban ma duk ya kwance mata kai bata masan mi zatace ba kuma tayi shiru dai tana sauraron hibba har tagama kafin tace shi fa auntie hibba baya son magana idan kinga yayi magana Sosai dawani to inna mace sai nifa don ko auntie hafsa sai yanzu yafara saki suna magana “ hibba tace tau kingani ba yanzu saura kwana nawa ku tafi can?aydarh tace ina kuma?hibba tace can wajan aikin nasa aydarh tawara hannu tace I didn’t know fa “hibba tace tau magani nake so a turo manah dashi daga can nijer “duk da aydarh bama sai kin sha wani abun dazai kara miki wani abu ba daga body structure har gyaran skin duk wani kyau dakuma haduwa da mace ke bukata kina dasu aydarh, Aydarh tayi shiru tana sukunyan da kanta kasa hibba tace babu abunda kika nema kika rasa kin hada komai aydarh ki kwantar da hankalinki ki cire duk wani sauran kunyar dake tsakanin ku ki daina masa kallon yayarh or something like that “babu wani abu dayayi saura yanzu ya riga daya yamayar dake tashi babu inda hannunsa bai kai ba a jikinki babu wani sauran wurin dabaki gani ba a jikinsa tau kunya tami kuma bacin ki dinga cutarsa Wallahi kunyar nan cutar su take kwara ma ki cire kunyarki ki ajiyeta gefe nifa idan Doctor na nan daidai da daya bana sakawa ahaka nake zama shima yayi zaman sa ahaka aydarh dai tasake yin

kasa da kanta tana wasa da rings din hannunta hibba tayi shiru tana ta sauraron hibba ji take kaman zata nutse tsaban kunya “ hibba tayi shiru aydarh ma dai bata son maganar hakanan dasauri don karma hibba ta taso maganan tace wai anyi test din auntie? Hibba ta gyada kai tace ehhh four weeks fa kenan aydarh tayi murmushi tace woaw can’t to see the babe Masha Allah Allah yaraba lapia hibba tace Ameen kafin tace Allah yakawo muku naku kuma auntie aydarh “Aydarh dai tayi shiru batace komai ba, can tace wai kuma auntie badagaske bane yawan ciwon da ake cewa if you are pregnant kanayi? Hibba ta girgiza kai kafin tayi yar dariya tace ai kinga kuwa da kalan yarda yakeyi “wasu fa har sai sun kwanta asibiti tsaban laulayi “ Aydarh tawara ido tace kai haba?hibba tace Wallahi kuwa nidai kawai abun yazo mun dasauki amma duk da haka fa duk dare sai nasha fever kuma ko kadan bana son Doctor yamatsa daga kusa dani “ Aydarh tace eyyerh auntie sorry,hibba tace duk na rame ba?aydarh ta gyada kai tace kin rame kadan kuma kinyi haske sosai masha Allah “hibba tayi murmushi tace haka Doctor ma yafada amma kinsan mi aydarh ta girgiza kai tace ki kokari dai kafin ku dawo kuyi manah tsaraban twins “ masu kama daku aydarh tayi murmushi tayi kasa da kanta “batace komai ba tace kinga bara natashi ina son naje mu gaisa da inna fa “Aydarh tace eyyerh kuma ban tambayesa ba da mun tafi tare “hibba ta girgiza kai tace no keda baki da lafiya ki bari kawai zanje I will not stay long ai aydarh ta gyada kai tace tau sai kin dawo hibba ta mike tana yafa veil din abayanta “ fita tayi aydarh kuma ta mike ta wuce bedroom din toilet tashiga duk da jikinta babu kwari haka tasaka detergent a bucket ta wanke masa singlets dinsa da cire da boxers “ kafin ta shanya ta fito ta dawo parlor ta wanke masa toilet dinsa tasake gyara parlor ta shiga kitchen din ta wanke kayan dasuka bata, da sallama hibba tashiga gidan inna “inna dake bakin kofa sai aikin gurzar tiles din bakin pampoo take tana ta sababi “ta amsa ma hibba sallamanta datayi mata tace wacece kuma wannan?hibba tayi murmushi kafin ta durkusa har kasa tace sannu inna ina wuni ya gida ya iyali?inna ta washe baki tace ahh lahiya lau alhamdulilah saidai ban gane bah ibba tace hibba ce matan ibrahim “inna tace Allah yayi kenan dan bakin halin yabarki kin zo gaishe ni kenan?hibba tayi murmushi kafin inna tace maraba shigo amarya parlor suka shiga inna ta kawo mata ruwa kafin tace ina shi ibrahin din? Hibba tace yaje wajan aiki amma idan yadawo zai shigo in sha Allah inna tayi kasa da murya tace shi fa baya da kaunar Allah a lissafin rayuwarsa karya bawani abu bace wajan nasa bafa zuwa zaiyi ba Wallahi kawai tunda dai ke Allah yasa baki da muguwar zuciya Allah yayi miki albarka “ Hibba tace Ameen kafin tace inna hafsa fa? Inna tayi mitsi mitsi da ido tace wacece kuma hafsa? Allah na tuba mi yahadani da ita yarinyar da sai data kare mun

Tana shiga gidan sukayi clashing da Ramlah saukan da kanta kasa kawai tayi ta cigaba da tafiya Ramlah dawani irin gudu tazo tasha gabanta aydarh ta dakata kafin ta dago tana mata wani irin wawan kallo sai tadauke kai zata wuce Ramlah tasaka hannu ta fizgo aydarh har sai da veil dinta ya zame aydarh da ranta yayi masifan baci ganin yanda Ramlah tasa hannu a jikinta “still bata iya jin zata bude baki tayi ma wannan kazamiyar magana “Ramlah ta washe dawani banzar dariya irin full karuwan nan tace yau gaki gani ke daya “batare da ogan naki ba wanda kike wa mutane iskanci da dagin kai saboda shi” kin dauka kyau gayu aji ko surar jiki ko kuma kyaun fatar da duk ke gareki shi zai saka wata takasa shiga rayuwar mijin naki? Tau Wallahi ganin dama ke bamu yi ba wawiya shashasha “yau zanyi maki bugun dazai kasa gane kamanin ki sai na lalata wannan tsadadiyar abayar jikin naki sai na lalata wannan cikaken kyau da fuskar ki dashi “Aydarh dake mata wani irin wulakantacan kallo from head to toe “ganin bazata iya cigaba da yin shiru ba yasata cewa “as a married women I will never fight with a prostitute like you very low level lady like you ,you are nothing but a trash just allow me to past before I show you bake kawai ne mad ba “Ramlah tayi wata dariya tace oh haba wannan turanci naki ai ko daga British Columbia sai haka “ Aydarh tayi gaba Ramlah ta dinga binta “ har bakin kofan part dinsu kafin ta fizgo aydarh har sai da buga kanta da bangon wurin tabata wani irin lafiyayan mari har sai da jini ya fito kadan ta gefen cute lips dinta nakasa “malik dake parlor yagama girki da duk wani gyaran gida duk da sunyi dasafe sai daya sake gyarawa yanzu after he finished cooking,wanka yafito ya shirya lokacin sallarh la”asar ne daidai ya buda kofan zai fito Ramlah tasake daga hannu zata sake wankawa aydarh second slap “ai billahi ji yayi duniyan nayi masa upset down jiyayi ana hajijiya ana juyasa whatttttt?matarsa ta rike haka zata mara his ASSEIYARH his cuddle bug his everything “dawani irin bala’In speed kaman wani asad (lion)kamar wani wanda zai tashi sama fuskarshi kaman hadari “yasa hannu ya fizgo aydarh da ganinsa yasata fashewa dawani irin dan mahaukacin kuka “malik kam jin kukan aydarh yasa jin zuciyarsa kaman tana barazanar fitowa kaman tana barazanar fashewa “ wani irin wawan fizgar Ramlah yayi ya wurgo ta kasa kafin ya kwance belt din jikinsa ya dinga jibgarka ta kaman jakka ya dinga sa kafa yana harbata billahi yanda yake bugun Ramlah kaman irin yan sanda na bugun rikaken criminal din nan “yah rabbil alameen yanda yake bugun Ramlah kaman daga sama aka aiko sa yin hakan kaman aikin daya zo yi duniyar nan kenan “sai da aydarh taga yana neman halaka Ramlah domin yayi loosing temper ta lura bai san ma abunda yakeyi ba “gashi Ramlah ma har ta suma ma,domin tun tana ihu har ta sume “gidan babu kowa sai Ramlah daman sun fita,barka sai lokacin su maman

Ramlah suka shigo gidan suka tarar da abunda ke faruwa wani irin kara uwar Ramlah tafasa,kaman mahaukaciya ta rugu tayo kansu tana jijiga Ramlah ‘aydarh da wani irin tsorata dashi ahankali tasa hannu tajasa suka shiga daki “idonsa kaman zaiyi aman wuta yajawo ta jikinsa yabada wani warm hug “kaman zai hadiye ta cikin jikinsa ahankali yasa hannu yadinga shafa bayanta kafin muryanshi na rawa “yace am sorry mamanarh kiyi hakuri it’s my fault kiyi hakuri dan Allah can’t protect you am very sorry yanda yake ta zuba mata words din he his sorry kaman ya haukaci ahankali ya zare daga jikinsa ta rike hannunsa kafin tace it’s not your fault nayi hakuri amma dukan dakayi mata yayi yawa sir “ajiyan zuciya ya sauke yace yayi yawa?yawa I wished I kill her!!dasauri aydarh tasa hannu tana rufe masa baki ta girgiza kai tace it’s very bad for you to beat a lady ba a dukan mata malik yazare hannuta daga bakinsa yace ita kuma ta dage ki?aydarh tayi shiru kafin ta kwantar da kanta a chest dinsa tana sauraron yanda zuciyansa ke bugawa kusan 5mins malik yaji kafansa har tayi masa wani nauyi ahankali yacireta a jikinsa “kafin yasa hannu yakamata suka shiga bedroom ruwa yahada mata a bucket kafin yafito da very clean towel ya dawo bedroom din tana zaune kan katifa yasa yatsan sa yana shafa inda bakinta yadan fashe kadan ga alaman jini a wurin kasancewan ta fara yasa wurin ya nuna girgiza kai yayi kafin ya mika mata towel din yace refresh and pray kinji ta gyada masa kai “yace ki shiga nima bara nayi sallarh yana tunanin a rayuwansa bai taba missing profer time din sallah ba sai yau kabbara salla yayi har yagama Still yakasa tashi daga kan prayer mat din kansa nayi masa wani irin azaban ciwo “hannu Ramlah daya gani fuskanta yanasa jin dana sanin Ramlah a rayuwarsa whattttt bazai kyale yarinya ba billahi sai tayi dana sanin maran masa mata datayi,aydarh ta fito daga ita sai white towel din sai kamshin shower gel take ga kamshin lallan data ke tashi kadan kadan “tunda tafito yake bin white long legs dinta da kallo da very creamy yah rabbil alameen cinyanta ya hadu yashafa kansa yakasa dauke ido daga kanta, kasa tayi da kanta ahankali kafin ta wuce wurin wardrobe ta bude tafito da white plain gown maran nauyi ta ciro bra da pant ta juya ta koma toilet sakawa tayi kafin ta dauro alwalla tafito shidai sai kallonta yake tasake bude wardrobe din tafito da hijab ta fesa perfume ‘kafin tazo gefen sa ta kabbara salla kan katifan yakoma ya zauna sai bin kafan ta da kallo yake lallan kaman an daura ba zanawa akayi ba saboda tsaban kyaun dayayi she is real definition of fine “komai nata mai kyau ne lallan yahau kafan ya zauna daram ya rabbi wai Allah “sallan takarasa kafin ta juyo ta kallesa ahankali tace ina wuni?gyada mata kai kawai yayi kafin yasa hannu yajawo ta ya daura ta bisa laps dinsa yacire abayan jikinta ya rike hannunta yana kallon lallan kafin yasa baki yayi kissing both hands din

yace yayi kyau kaman mai shi masha Allah tayi murmushi tana dago kafan shima yasaka hannu yakarba yana shafawa kafin yayi kasa dakai zaiyi kissing kafa tace nooo sirrrrrr kafane fa malik yace what ever ya dinga sakar ma kafan kissies kaman zai cinye kafafun ita dai sai kallonsa take tana murmushi can ya dauko yace kitson fa?ta warware ribbon dinta na duku masa da kanta “Yah rabbil arsh “har hannunsa rawa yake kafin yakai yayi placing yana shafa kitson yama kasa magana saboda bai son words din dazaiyi using ba wajan ce mata kitson yayi kyau ,lumshe ido yayi yabude yana kallon yarda aka tsara kitson ga kamshin gashin na nema zauta masa kai “ahankali ya dago kanta yana kallon cikin idonta duk taki kallonsa saboda nauyi da girmansa datake gani duk lokacin dasuka samu eye contact yace akwai zafi?ta girgiza masa kai yasake daura hannunsa gefen bakinta tayi yar kara yayi saurin janyewa yace sorry kinji yi hakuri “muje kici abinci sai muje chemist nasiyo equipment nayi miki dressing ta gyada masa kai kawai tunda suka zo garin nan bayan ranar dayafada mata yasamu aiki sai yau take jin wani irin farin ciki ganin yanda yayi don waccan yarinyar ta mare ta daga gani deep inside he his hurt.Yanda yake treating dinta kaman princess domin abincin ma tana ci yana mata sannu murmushi kawai tayi bayan yagama saka mata hijab yace ko dai na dauke ki?ta girgiza kai tace noo zan tafi dakaina yace ohk ma “hannunta yagama ya rufe gidan suka fito, yana gaba tana baya har suka zo daidai part dinsu Ramlah tana kwance kan tabarma duk tasha bandage da plasta a fuska da hannu ga farida tsaye akansu sai bala’I take wai ayi karar su maman Ramlah tace karar su ta gidan ubanwa? Har kofan sasshen su ta iske su tabugar mai mata nakai karar su bayan bayan a gabanki caji opis din su kace duk ranar data sake tadawowa akan kas din fada sai su mikata gidan yari? Farida tayi shiru tace tau ai shknn Allah yakara mata daman ina ita ina waccan bawan Allahn fisabillahi mudai Allahu yataimake mu ya hakura Wallahi kinsan masu illimi yanzu zaiyi karar ku yace kun dakar masa mata maman Ramlah tawara ido tace billahilazi da babu ruwana tattara matsiyaciya zanyi namika musu ita tunda bata da kirki yar iska shegiya “Ramlah dake jinsu tass bakinta a kumburi takasa magana hawaye kam sun kasa tsayawa “tunda suke fadace fadacan su da maza da mata har dai yan sanda sun daketa amma billahi bata taba shan irin wannan dukan ba a rayuwarta, maman Ramlah nagani “ malik da aydarh ta zabura ta mike ta bi bayansa tace yallabai kayi ma darajar ma’aiki kayi hakuri banda mu ba banda halin mu Wallahi yarinta ce da shegen taurin kai kayi ma Allah ka hakura yallabai billahi bugun dakayi mata kayi man daidai yallabai kayi hakuri har kasa maman Ramlah ta duka tana kallon aydarh tace hajiya kice yayi hakuri dan girman manzon Allah kiyi hakuri aydarh ta gyadawa maman Ramlah kai kawai batace Komai don

bakaramin tausayi taba bata ba “malik dai bai ce komai ba yakama hannun aydarh suka fita daga gidan suna fita takallesa tace sir ‘yace what tace kayi hakuri yawuce aie shknn ni na hakura “yace are you sure ta gyada masa kai yace Allah yayi miki albarka tace Ameen suka cigaba da tafiya basu wani jima ba a chemist din suka siya abunda zasu siya hadda maganin ciwon kai ya siyan mata wai ala dole saboda kitson yasan yayi zafi gida suka koma ya goge mata ciwon tasha magani ta kwanta kan katifa shikuma yana zaune suna waya da dr usama “shiru yayi yana sauraron bayanin da dr usama ke masa har yagama kafin yace it’s alright sir Allah yasaka da alkhairi daga can dr usama yace Ameen son “malik yayi murmushi yana shafa kansa yace Allah yakawo mata tagari dr usama yayi murmushi manya yace kaji ka ko mata kuma?wannan na bar muku ni na hakura malik Yace nooo uncle cike da tsokana yace I will find one cute hajiya for you dr usama da har sun saba da malik irin sabon nan bana wasa ba ma yace I will catch you son naga dai nazama abokinka yanzu, dr usama yace so bayan magrib zai kawo muku visa everything is ready anan dakuma can gobe 4:pm ne tafiyan naku Allah ya tsare yakai ku lapia malik yace Ameen yah rabbi uncle I appreciate Allah yabani ikon saka maka da alkhairi dr usama yace Ameen kafin ya kashe wayan “yana kallon aydarh da itama shi take kallo yace kin huta?ta gyada masa kai yace Alright muji na karbo dink isai mukara siyan abunda bamu siya ba takallesa kafin tawara ido tace miye ne shi abunda bamu siya ba? yace rigan sanyi da kayan sanyi ko babu sanyin a can? Aydarh ta gyada masa kai tace akwai sanyi sanyin ma yace kingani ba shirya muje tace hijab kawai zan saka yace ohk “ ta mike ta bude wardrobe tafito da jalab brown tasaka tafesa perfume kitson nan ba dan karamin haske da kyau ya Kara mata ba kaman kasace ta ka gudu, keke suka shiga suka sauka shagon daya bada dinkin nasa angama ya karba ya karasa biyan kudin suka fito boutique suka shiga dake kusa da shagon dasuka karbi dinki Expensive kayan sanyi yasiyan musu kusan kala biyar kala daya na mata masa sai kuma tayi musu choosing different colors riguna kawai masu hula kusan 300k na kayan sanyin kawai yabiya suka wuce tace muje gidan Doctor auntie hibba tace zata bani sako malik ya girgiza kai yace no yace mun zasu zo da dadare basai mun je ba, aydarh tace Alright yace ko muyi order perfect cake?ta girgiza masa kai tace no baza mu ci basai dai muje mu siya grilled meat da pepperonis pizza “yayi murmushi yaja dogon hancinta yace when it comes grilled meat you can eat for Africa amma abincin bazaki ci bak o ?tayi murmushi tanayin kasa da kai yace Alright bara mu samu keke amma takeaways zamuyi baza mu ci a can ba,aydarh ta gyada masa kai kafin tace ohk”keke suka shiga sai eatery lafiyayan takeaway yayi musu pizza har zai karbi kwara biyu tace daya ya isa biya yayi kafin suka wuce gida.masallaci

yawuce saboda ankira sallarh “itama kitchen takai takeaways din kafin tashiga dasauran kayan bedroom tawuce toilet tayi alwalla tafito ta kabbara sallarh “ tareda su dr ibrahim suka shigo bayan yafito sallarh yahada su, anan parlor hibba da dr ibrahim suka zauna shikuma yace bara yashiga yayi mata magana “tana zaune kan abun salla yashigo da sallama ta amsa masa yace kifito gasu Doctor tace ohk “kafin ta mike ta bi bayansa Sai da kashe da dr ibrahim kafin suka gaisa da hibba, fira suka fara kafin aka kira salla suka wuce masallaci suma su aydarh salla sukayi kafin hibba tace billahi wannan lallan ban masan ta inda zan fara cewa yayi kyau ba aydarh tayi dariya tace shima haka yace hibba tace ai dole Wallahi muga kitson tanuna mata kitson hibba tace barakallah abun har baa cewa komai “can hibba takalli aydarh tace miyasa mike a baki naga kaman yadan gurje “aydarh tayi shiru kafin tayi ma hibba narrating komai daya faru ‘hibba ta ajiye ajiyan zuciya tace ubangiji Allah ya biyasa yana nuna mata cewa nata iskanci karami ne yoo Allah natuba yallabai ko tsofin criminals yarike yama wannan dukan sai sunji balle ita data zo angama iskanci duniya Allah natuba aydarh tayi murmushi kawai tace “muje mu shirya dinner kafin su shigo hibba tace Wallahi alhamdulilah nikam ko kamshin abinci bana so balle na ci sa shima yaci abinci sauri zamuyi mu koma yarinyar kanwar iya zamuyi wa barka “malik yakalli dr ibrahim yace nama manta da box ma fa yanzu sai mu fita musiya kawai.

Dr ibrahim yace sai ka dauketa yanzu kuje ku siyo malik yace ehh ba kafin yace in sha Allah dasafe zan shigo muyi bankwana da iya inna ma sai zuwa gobe zan shiga muyi sallama in sha Allah malik yace Allahu yasha tau daga haka suka shiga gidan dr ibrahim yakalli hibba yace sannu ta gyada masa kai kawai “yace tau tashi mu tafi dare nayi malik yace aa ibrahim kabari muyi dinner manah sai ku wuce dr ibrahim yace Allah mungode zanmu biya tayi wa cousin sis dina barka kuma kaga yanayin jikinta malik ya gyada kai “hibba ta kalli aydarh tace tau muje sai na baki sakon daga haka suka shiga bedroom din “hibba tace dan girman Allah aydarh ki daure ki ding asha saboda kalan wahalan da aka sha kafin kayan nan su karaso daga can nijer din “Aydarh ta gyada kai tace in sha Allah hibba tace promise don bawai yarda nayi dake ba ,aydarh tace Allah I promise zan dinga sha hibba tace tau shknn aydarh tace thank you auntie Allah yasauke ki lapia hibba tayi murmushi tace Ameen aydarh kuma Allah yakawo muku masu Albarka aydarh batace komai ba tayi shiru daga bakin kofa sukaji ana knocking malik yace ki dauko takalmin ki sai mu fita tareda su kawai mu karbo sako aydarh tace ohk”kafin ta bude wardrobe tasaka ledan da hibba ta bata “suka fito tare rufe gidansu kayi a bakin hanya suka samu keke hibba tayiwa

aydarh waving hannu tace sai mun hadu a airport mu zamu raka ku aydarh tace to auntie “kasancewan anan bakin hanyar ke da babban shagon boxes da textiles wani haddan box yasiya masu kwara uku sunyi kyau bana wasa ba yabiya kudin suka wuce gida this time a keke suka dawo,shi ya dauke kaff box ukun suka shiga gida bedroom yakai su kafin yakalleta yayi kasa da murya yace ko hakanan akayi takeaway din baza’a ci abincin ba?tayi murmushi tace acici “kawai tayi gaba ya bita da ido har ta shige kitchen din kafin ya zauna parlor murmushi dai yaki barin fuskan sa yadinga bin parlor da kallo hadda daga kai sama “he will surely missed this house he will surely miss kano bai taba tunanin sake samun wani farincikin ba tun bayan tahowar su daga adamawa bas ai gashi abubuwan dasuka faru dashi na alkhairi a kano ko dawasa baitaba ko da dreaming hakan ba “sai gashi cikin abunda bai fi one year rayuwarsa ta juya yashafa kansa yayi yana tunanin plan dinsa dakuma rayuwarsa a Washington lumshe ido yayi ya bude yace Alhamdulilah “ahankali ta bude kofan kitchen din tafito hannunta rike da plate din data zuba grilled meat din sai dayan kuma da spoons da fork da kuma cups dasauri ya taso yarage mata wasu kayan hannun nata kafin ya ajiye kan carpet itama nan ta ajiye kafin ta juya kitchen din yabi bayanta a tare suka karasa fiddo pizza da drink suka zauna “ya kalleta yace kinyi kyau tawara ido tana kallon jikinta tun rigan data saka dazu ne white sai kanta ma abude babu ko hula kitson nan kaman an zana ya rabbil alameen “murmushi kawai tayi kafin tafara mashi cutting naman hannunta yakama suka yi cutting a tare kafin yafara feeding dinsu tana masa fira kadan kadan “shi dai yashagala kallonta kawai yana bada naman shi ko ci ma bayayi can ta lura ahankali ta taba sa tace what’s wrong? Ya girgiza kai yace babu komai gashi yacigaba da bata naman can dai ta dauka shima ta kai masa baki Wallahi hadda hannunta ya hada “tayi yar kara duk da gangan ya ciza din kadan “ ta tura masa baki tace shine zaka hada da hannu na dazu daman budurwa ka ta dagan nidai nagaji both the girlfriend and the boyfriend are against me “malik yayi shiru yace sorry cuddle bug dawasa fa nayi aydarh dai ki kallansa “ahankali yajawo ta yace ni dai ki cigaba dabani am hungry fa “ sai sannan tace to idan kasake cizawa bazan sake baka bay ace yeah naji “ahaka ta dinga feeding dinsa har yakarasa grilled meat din kafin yajawo pizza shima sun ci kusan rabi kafin ahankali ta mike tace sir cikina zai fashe malik yayi murmushi yace ai naga kinyi kokari ma yau kin ci abincin dayawa tayi yar dariya tace so nake na fika kiba ai “malik yawara ido yace kai haba?ta gyada masa kai yace tau zo ki ga wani abu tace me? yace kedai ki zo kawai “ahankali yasa hannu yajata jikinsa “ya lumshe ido yana placing hannunsa a cikinta yana shafawa tayi lamo tana sauraron sa can yacigaba da zarce hannun har kan maranta dasauri ta rike masa hannu

tana girgiza masa kai tace stop “yayi shiru duk jikinsa ya mace kawai yadaga ta suka wuce bedroom “kan katifan ya ajiyeta kaman wata yar baby kafin ya kwanta a jikinta duk da bai sakar mata nauyi bas ai datayi yar kara “daran sai da malik ya gama ruda aydarh kafin ya rabo da ita kuka ta dinga masa kaman zaa zare mata rai “duk bawai ko yayi attempting disvirgin dinta ba “a jikinta dai ne kawa isai wurin daya manta ke bai taba bak o yayi wasa dashi “ko daya dawo daga sallan asuba tana cure kan prayer mat still carrying ya matsa kusa da ita yazare hijab din jikinta yasata a jikinsa yacigaba da Patting bayanta har dai yaga tasaki jiki dashi ahankali yamike yace bara nashirya manah kayan box saboda zamuje bankwana dasu iya da inna aydarh ta gyada masa kai kafin ta mike ahankali tace I will help you yayi murmushi yace Alright darl “ kayan suka jera a box kowa danashi karamin ne ya rage malik yayi kasa da murya yace tau ko mu hade inners din cikinsa kawai aydarh tace nawa dana ka?yace ehh tayi shiru kafin tace to “kaf brassiere dinta da pants yahade cikin box din sai yasaka boxers dinsa da singlet da few kayan dasuka rage “kafin yazage zip din yamikar da both the three akwatin “yakalle yace ko zaki koma bacci ta girgiza masa kai yace tau sauran kayan can su buckets dawani kayan kitchen kawai sai nasaka a fitan ma inna dashi tabayar kawai “Aydarh ta gyada masa kai yace ko muyi warming sauran naman can?tace to “sai dasuka gyara koi na na gidan suka mikar da duk abunda suka tarar nan kafin suka hade nasu waje daya da niyyar idan gari yakara haske malik yasa a fitan dasu a kai gidan inna “kaman yanda yafada warming nama sukayi kawai tahada musu tea suka yi breakfast wanka tashiga shima yashiga toilet din nan parlor.Bayan sun gama shiryawa already anfitan da kayan zuwa gidan inna yakalleta yace mu fara zuwa wajan iya muyi bankwana ba kafin mu dawo nan tace ohk “ sunyi kyau bana wasa ba farar shadda yasaka sabuwa dal Tabarakallah murmushi tayi kadan tana rage murya tace kayi kyau sosai kaman wani ango “shima murmushi yayi yace ai kin fi ni yin kyau pretty “tawara masa ido tace dagaske ya gyada mata kai taja cheeks dinsa tace mutafi kaga har twelve yanzu “Da murmushi iya ta tarbe su “rabiah na nan zaune sai fama kallon malik take kaman zata hadiye sa Wallahi aydarh don dai kawai wajan iya suka zo amma dasai tasa sun bar wajan saboda kallon da rabiah ke masa daurewa kawai tayi tana dai sauraron nasihar da iya keyi musu amma bawai tana fahimta ba kawai she is eager su tafi ji take kaman ta rufesa rabiah tabar ganinsa “ iya tace Allah yayi muku albarka abdoolmalik a rike gaskia in sha Allah zakuyi nasara a rayuwa ka rike yar uwarka “ka rike matarka Allah yabaku zaman lafiya “ malik yayi kasa da kai yace Ameen Ameen iya mungode Allah saka da alkhairi iya tayi murmushi tace Ameen abdool “kafin aydarh ma tayi kasa da kai tace angode iya Allah yakara girma “iya tace

Ameen asiya Allah yamuku albarka a cigaba da biyayya asiya a cigaba da hakuri “Aydarh ta gyada kanta kawai malik yamike yace rabi’atu dasauri rabiah ta dago kanta tace naam yaya yace ki tura mun acct number ki zan Saka ma iya sako “Aydarh takallesa ohh tana number tasa kenan “ma dahar zai ce ta tura masa mikewa tayi ahankali itama kafin tace iya bara nashiga wajan auntie Hibba inna tace anya kam basa nan sunje can asibiti tare ko wani test zaayi mata amma ai naji suna cewa tare zaku tafi can filin jirgin malik ya gyada kai yace ehh iya “yanayin aydarh yakalla dasauri yace “ohh namanta samun yafada yana mika mata wayarsa aydarh tasa hannu ta karbi wayan kafin tamikawa rabiah acct number ta rubuta kafin tamika mata wayan karba yayi nan take yayi mata transfer 100k kafin yasaka wayan ajihu ya sukunyan da kansa yace iya zamu tafi ubangiji yasaka muku da alkhairi Allah yabar zumunci ana haka rabiah tace iya yayah ya tura dubu dari iya “iya tace kai haba abdool hadda wani wahala haka Allah yayi muku albarka “malik yace Ameen Ameen har kofa gida iya suka rakasu tare da rabiah “bayan iya takoma saboda hadda dan kukanta sabo “malik ma duk sai yaji wani kala aydarh ma haka “rabiah ta saukar da kanta tace “dan Allah kiyi hakuri da duk abunda nayi muku Wallahi ba laifi nabane shidai malik ko kallonta baiyi ba aydarh ta girgiza kai tace babu komai rabiah,rabiah tace nagode Allah yasaka da alkhairi “Allah yakara baku zaman lafiya aydarh tayi murmushi tace Ameen kafin sukayi sallama rabiah ma ta koma sukuma suka shiga keke sai dasuka yi salla saboda har kusan 1:30kafin suka wuce gidan inna “suna shiga tana zaune kan tabarma “ansha dinkin lace sabo fill ga samira datayi ma malik kwadon zogale a gabanta kusa da ita yazauna aydarh ta ta zauna daga dayan side din inna suna zama inna takama harbar zane tafashe da kuka cikinsu babu wanda ya iya mata magana sai da tayi mai isar ta kafin ta tsagaita tace “yanzu shknn shi daman sabo haka yake “inalilahi waina illahil rajiun shknn yanzu audu tafiya zakayi kabarni wayyo Allahna “malik yayi murmushi aydarh kam juyawa tayi tana dariya saboda bakaramin dariya inna tabata ba tama yi tunanin wani abun akayi mata “malik yace tau waya gaya miki bazan dawo ba?inna tasaki baki tace yoo kodai ni yar iskace ai bazan taba yarda zaka dawo ba wanene wanda zai bar kasar nan yace kuma zai dawo shknn masifa ta sauka dan wajan audu kawai nake samun rahama yanzu shknn anbar ni da wannan tsohuwar macan ta kasheni da bakin ciki sai ta sake fashewa da kuka “malik yace kinga kiyi hakuri ni dana son kina zuwa babu abunda zai hana nasa ayi miki visa mutafi tare!aydarh tace yanzu ma za’a iya miki inna sai kema kizo kawai “inna tayi shiru tana kallonsu kafin tace ashe dai ba tinugu kawai aka dauka marar kan gado ba a kasar nan ba haddani “malik cannot even hold it but to laugh itama dai aydarh murmushi kawai tayi malik yace kings ke

kinfiye rigima “ai naga missing dina zakiyi shiyasa matana tace miki haka yanzu dai tsaya ki daina wannan kukan ina zogalan innaa tayi kasa da murya tace kaga da nima ina da wayar zamanin na da sai kaga ta ita ina tura maka kwadon zogalan nan babu wani bata lokaci amma can dai babu inda zaka sami zogala billahi basu ma sanshi ba idan ma sun sanshi said ai araba ma namun jije “malik yace aikam dai yace ai ankawo miki kayan ko? inna tace eh Wallahi sun kawo yanzu duk wata kazamar mace a anguwar nan na cireta a rabon kayan lokacin dana dinga basu fatarwa suyi tsabtar ai basuyi ba don haka yanzu lokacin ramawa ne yayi su san nima baa bazan nake zaune ba “yan gayun layin kawai zan raraba ma kayan kitchen dinnan malik ya gyada kai yace gaskia dai inna tace gaskia manah ai dauda ba kyau “yace ina dr hafsa?inna tayi mitsi mitsi da ido yace wacece kuma dafta hafsa “Aydarh tace mai nan gidan tafada tana dariya kasa kasa “inna taji ta sarai yasa ta kalli malik tace tau akwai waenda basu da tsoron Allah dayawa a rayuwar nan tau ita hafsa din yaushe ta siya gida ba ‘asani ba aydarh tace to ai nan gidan ta ne malik yaga lokaci na wucewa ya mike yace tau ki kai atm dinki wurin mai pos na tura maki sako inna tace Allahu akbar audu wayyo Allah malik yayi murmushi kawai yaja hannu aydarh suka wuce bai tsaya jin inna ba da niyyar idan dr ibrahim din sun zo yashigo atafi airport din tare da inna. Yarda yake kallonta sai yaga kaman bata taba masa irin wannan kyau ba zaune take kusa da hibba da dr hafsa sai inna dake gefe tana faman tsuke fuska wai kar arainata ayi tunanin wannan ne zuwanta farko a airport tun kafin four din takarasa dr ibrahim daya aro motan abokinsa yazo daukan su hadda inna da dr hafsa.

Dr ibrahim daya lura da irin kallon dayake ma aydarh don details ma yake nuna masa a waya amma hankalinsa baya wajan sam “dr ibrahim yayi gyaran murya kafin yayi kasa da murya yace tau idan dai har kayi hakuri dakun isa can aiki kawai zai dinga fiddaka babu wani baki daza su dinga distracting dinka “malik yayi murmushi yana shafa kansa yace kai dai kasani “hibba tace duk kinyi wani kala auntie aydarh “sai lokacin dr hafsat ace ai dole ne ni kaina duk wani kala nake ji Allah hibba tayi murmushi tace shin sabo shi daman haka yake inna dai najin su batace komai sai dai bin jama “ar dake kai kawo kowa na hadaddar tafiya saura 10mins jirgin su ya tashi,Hibba tayi kasa da murya yanda inna bazata ji su batace auntie ki taimaka mun wurin begging yarinyar nan wajan shan kayan nan Wallahi karki so kiga uban wahala da aka sha kafin a kawo su dr hafsa tace tau ai shine ni kaina da karbo mata wasu perfumes idan ma tayi wasa su dai matan can ba kaman namu ba aydarh kanta nakasa tana fidgeting fingers dinta tana dai jinsu duk kunya ma suke bata bakaman da dr hafsa nayi mata

bayanin maganin “ dr ibrahim ya taho ‘gabansu malik na can yana making call “ dr ibrahim yakalli inna yace hajajju ta tsuke baki yace tau ko dai duk wannan fushin so kike a je dake komai?fada naji inna tayi banza ta kyalesa “yayi murmushi kafin yace tau idan kun gama bankwana lokacin tashin flight din yayi Hibba tace mun gama bara ta taho “ya juya ya koma wajan malik dr hafsa tayi hugging aydarh kafin tace Allah yakai ku lafiya aydarh Allah yabaku zaman lafiya da yara masu albarka I will surely missing you little sister “Aydarh da idonta ya cika da kwalla tace I will miss you too big sis I appreciate all your gooddoings on me Allah yabaki miji nagari “dr hafsa tashare guntun hawayan ta tace Ameen baby girl banda miskilanci a cigaba da biyayya yeah ? Tafada tana murmushi ga hawaye “Aydarh ta juya kafin tayi hugging hibba tace maman baby Allah yaraba ku da baby lapia nagode sosai Allah yasaka miki da alkhairi thanks for correcting my wrongdoings “hibba tayi murmushi ahankali tace aydarh I will surely missed you nima nagode da alkhairan ki gareni Allah yakai ku lafiya yasa ki zo manah da cikin yan hudu dariya sukayi innaa dake gefe tace yau naga buhun masifa shidai matukin jirgin ba dan iska bane dazai zauna zaman jiran ku gaba wannan abubuwan daidai nan malik ya karaso sukayi sallama dasu dr hafsa da hibba kafin ya riko innaa yana kallonta yama rasa abunda zai fada mata kawai yace zan saka hafsa ta siyo miki wayan babba sai mu dinga vedio call hakan yayi maki ko inna ta aza kuka tace Allah ga jikana nan Allah katsare shi ka kareshi ka daukaka man shi karaba shi da sharrin masu turanci Ameen yah rabbil izzati “malik yace Ameen kakata aydarh dai duk kaman an watsa mata ruwan zafi tayi wani kala “proper sallama malik da dr ibrahim sukayi malik yace buddy only god will reward you “dr ibrahim da zuciyansa ta kare kaman zaiyi kuka Wallahi yadai daure kawai suka daga musu hannu “basu suka bar airport ba har sai da flight dinsu ya tashi “duk da this is his first time na hawan flight ko kadan bai nuna wani attitude bako reacting na nuna shi bako ne a flight “lokacin da jirgin su ya tashi ya rufe idonsa kawai yana karantu adduan godiya ga Allah dakuma tasbihi ga fiyayyan halitta Annabi Muhammad (s.A.W) wani irin rahama ke bin duk wani kofofin jijiya na jikinsa wani irin ajiyan zuciya yasauke “wani irin sanyi na mamaye masa zuciya “kamshinta jikinta na supporting breath dinsa yanda ta shige jikinsa kaman zata koma cikin jikinsa “duk tayi wani kala Wallahi wani irin kewan su dr hafsa take ji duk da baaje ko ‘ina ba tunani ne kala kala a ranta “ahankali yasa hannu kaman mai tsoro ya kama nata hannu batare dayayi mata magana ba itama bata ce masa komai ba tayi shiru “tana sauke ajiyan zuciya kadan kadan shknn yanzu a rayuwa bata da kowa sai shi shknn yanzu a rayuwarta daga ita sai shi miye makoman rayuwansu ita shi “tasan Wallahi bazata iya rabuwa dashi ba kuma ita kodai don batasan so bas ai

taji bata sonsa ko kadan amma ko na wuni daya bata son tag abaya kusa dashi his presences makes her heart to feel better kawai tana jin kaman shine wani babban support dinta a rayuwa “babu abunda take tsoro irin ranar dazai nuna he wants her “inalilahi waina illahil rajiun she cannot bear ita ma “bata masan yarda zatayi ba “shi fa tasan ba sonta yake ba idan ta yarda dashi fa shknn kuma zai je ya auro wacce yake so itama shknn rayuwanta yagama batasan lokacin da ta rufe ido da karfi ba har sai daya lura saboda yi tayi kaman ta tsorota yah rabbil alameen “his heart beats for her love “basan taya zai fara fada mata ba saboda har yanzu ya lura bawai tana fahimtan rayuwa sosai ba “shiru yayi kafin ahankali ya zareta daga jikinsa yana kallonta ko kiftawa babu yace what?ta gyada masa kai kafin tace I want to drink water yace ohk”hannu yasa ya bude bottle water da aka basu kafin yamika mata kadan tasha kafin ta mika masa bottle din ya rufe ya maida ya ajiye yana sake sakata jikinsa ko ten minutes baa kara ba bacci yayi gaba da ita “ kasancewan batayi wani isasashan bacci “yasa bai ta ta farka ba har sai da flight dinsu yayi landing a Washington Dulles international airport “passengers din jirgin suka fara sauka,hannu yasaka yashafa fuskan ta ahankali kafin yace wake up cuddle bug mun sauka “ahankali take bude idonta har takarasa budewa tass kafin tayi wani very cute smile tace ni fa ba bacci nayi ba malik dake kallonta ko dauke ido babu yace yeah I know ba bacci kike ba mu tafi hannunta ya kama “suka dinga sauka daga stairs din jirgin “yana sauko ya sauke wani irin ajiyan zuciya kafin yaja numfashin ya fuzgar da iska da karfi “takura jikinta tayi saboda sanyi daya dake ta mantawa ma tayi bata rike rigan sanyi a hannu ba shima malik bai yi tunanin sanyi yakai haka ba hannu yasa yana kamata kafin yarage murya yace miyasa baki gayamun sanyin yayi reaching haka ba “tayi shiru kafin tace nayi tunanin kasani malik yace how will I know ni da ban taba zuwa ba?tayi shiru kafin tace nasan ma bai wuce 18 degrees ba bawani sanyi ke Akwai sosai ba “malik yawara ido yace kai haba yanzu nan yafada yana jinjina kai ana haka sai gawani baturan mutun yasha jacket yarufe har kansa da hula “malik yakalle sa ganin dashi yake magana cike da girmamawa “mutanan ya gaishe da malik malik ya amsa sa kafin mutunmin ya kwashe luggage’s dinsu malik yasaka a booth already dr usama ya fada ma malik idan suka sauka zaa zo daukan su back seat yabude musu suka shiga “kafin ya tada motan yahau titi “shidai malik sai bin garin yake da kallo ko a dream bai taba tunanin zuwa wani kasa ba sai gashi a reality aydarh ta kwantar da kanta a shoulder dinsa tayi shiru “har suka isa wani hadaddan anguwa mai shegen kyau ga manya buildings roads kau kaman a cartoon tsaban haduwa “Aydarh na kallon malik tace lah sir kasan me?malik ya girgiza kai shima yana murmushi aydarh tace nan fa anguwan abba ke

sauka hadani da oum fa malik yawara ido yace kai haba tace Wallahi fa yace tau miye sunan anguwan?aydarh tace chelan county anguwan yana kyau sosai akwai playground for water lovers yace one tace akwai thrill riders yace two tace and akwai culture seekers yace woaw kice mun zo babban anguwa aydarh ta gyada masa kai bakin wani gida driver yayi parking karami ne sai dai trees kaman irin wurin siyar da professional flowers “flowers neb asu azaban kyau da haduwa gidan fine die I swear whattttt “ shi malik ma dai sai yazama dan kallo fito musu yayi dakayan yasaka wani card kawai jikin kofan ta bude “sai da malik yayi addua kafin yayi stepping cikin gidan itama aydarh haka “karamin parlor mai dauke dawasu mad English cushion masu dan azaban kyau English room ne babu hayaniya ko kadan sai kyau dagani komai sabo ne “ wani hadaddan sofa sai study table gaban sofa “ room and parlor ne sai kitchen both the bedroom and the parlor contains toilet wurin yayi kyau bana wasa bedroom din suka shiga wanda driver yashigo musu kayan wani Turkish bed ne da wardrobe sai mudubi dawani karamin bag rag da shoe rag kala daya komai white zalla suma sabbi ne “ card din mutunmi yamika wa malik kafin ahankali malik yace thank you “ mutunmin yace you are always welcome Doctor “har yayi gaba malik yabisa baya kafin ya tambayesa miye sunan sa mutunmin yace mr joe malik ya gyada kai kawai kafin yamika masa wani sabon sim pack kwara biyu nakasa kafin yace masa yanzu zaa kawo musu abinci zuwa dasafe kuma sai yazo ya daukesa su siyo duk wani abu da babu a store din malik yace it’s alright sallama sukayi kafin mr joe ya juya malik yasa nan parlor yayi folding hannunsa a chest yana bin parlor da kallo komai na gidan yayi masa kyau “wucewa yayi bedroom din yasa meta tsaye tana jiran yashigo ya dinga kallonta kafin tace ina kasaka mun towel ban gan sa ba malik yace eyyerh sai dai kiyi amfani danawa tace naka kuma why nawa fa? yace ai na mantu sa ne aydarh tayi shiru kafin tace to ina sabon da muka siyo karamin box din yabude yafito mata da sabon towel fill maroon “karba tayi kafin ta juya tashiga toilet din komai akwai hadda heater tabude pampoo taji ruwan zafi yazo fitowa tayi Still da towel din hannunta ta dauki shower gel sai sponge dinta da brush sai maclean kafin tabude daya ta dauki hijab takoma shidai kallonta kawai yakeyi har ta shige toilet din kusan 20mins sai gata yafito sai faman kamshin shower gel take kallonta yake from head to toe non stop saboda yanda ruwa ke bin kafanta lallan kafan har wani kashe masa ido yake yanda red din yayi wani kala mai daukan hankali ahankali yabi ta bayanta yashiga toilet din shima wanka yayi ya dauro alwalla kafin ya fito har tagama shafa cream dinta tasaka inners tana shafa perfume sai datagama shafawa kafin ta tuno na wajan dr hafsa ahankali tace bazan manta ba next kayan sanyin ta ciro riga da wando nata

wanda suke da kala daya nata light blue shikuma dark blue sakawa tayi kafin ta bude jikkan dataga yasaka pray mat tasaka hijab dinta bayan ta fesa masa perfume ta kabbara sallan datayi missing a flight shima sharp sharp yashirya cikin exactly kayan sanyin dake jikinta yah Allah yayi wani irin kyau bana wasa ba,hadda combing hair dinsa yayi 'Yayi kyau kaman wani dan balarabe, perfume yasaka he forgets when last ya duba kansa a Mirror sai yau yayi haske yayi kiba yagani murmushi kawai yayi kafin ya dauki dayan abun sallama ya koma parlor yakabbara "kusan ten minutes daya karasa sallan yaji karan door bell mikewa yayi yaje yabude yaga wani mutun da kayan restaurant a jikinsa ga leda shima mai dauke da rubutun sunan restaurant din ya mikawa malik karba malik yayi kafin yayi masa godiya kitchen din yashiga nan ma babu wani hayani kayan amfani ne the kitchen decoration is very attractive and unique kitchen utensil da equipment din kusan duk na campany daya ne komai na gida is more than perfect for him ajiye ledan yayi yawuce bedroom din da sallama ta amsa kafin ta dinga kallonsa tayi kasa da murya tace naga da ini nafara saka kayan yashafa kayansa yace tau n isai akace kar nasaka ina ke kikayi manah choosing ma? tayi shiru kafin yace fito muce abinci tace masa ohk "atare suka dawo kitchen din duk komai na plates da spoons din are very clean sai data dauraye kafin tayi serving dinsu curry rice sai fresh grapes juice da wani karamin bottle water kwara two "parlor suka dawo ahankali suka fara cin abincin kaman irin ansan daidai cikin sun nan tass suka cinye duk da malik taste din abinci ya chanza masa amma bawani sosai bah aka yaci aydarh kam ta saba ma da kalan abinci plate din ta wanke sai spoons din da cups kafin tadawo parlor tasame sa "zaune yana duba abu a wayarsa kusa dashi ta zauna kafin ahankali ta daura kanta a shoulder dinsa tana kallon abun yakeyi wayan can tace "nasan asibitin yace serious?ta gyada masa kai yace kin taba zuwa tace erh yace baki da lafiya net ace Erh inads Doctor dake dubani "yace eyyerh.

Yace ranar Monday in sha Allah zan fara shiga "Aydarh ta gyada kai tace jibi kenan right?malik yace ehh tace Allah yakaimu lapia am so happy for you sir Allah yasa albarka "malik yayi murmushi yana shafa kanta yace Ameen yah rabbil alameen mamanarh Allah yasaka miki da gidan aljanna aydarh tayi wani cutest smile tace Ameen "ahankali ya dagota 'yace kinyi fushi?tawara ido tace for?yace maganan school fa"ta girgiza kai tayi kasa da kanta tace no babu komai I agreed with your command Allah yasa hakan yafi zama alkhairi "malik ya dinga kallonta ko kiftawa babu,kafin ya mikar da ita yace muje mu kwanta dawuri tace Alright rike da ita suka shiga bedroom din bayan yayi switching duk kayan wutan dake parlor ya jawo

kitchen din haske ya rage na parlor yarage bedside lamp kawai ta kwantawa tayi yasa ta jikinsa kafin yarufe su da duvet “ kasancewan sun gaji yasa bayan yashafa musu addua ba jimawa bacci yayi gaba da ita scent din jikinta yafi komai firgita shi jikinsa nawani masifan reacting kaman ana jona masa lantarki duk da sanyin dake akwai a dakin sai faman zufa ke keto masa “yah Allah yafada kafin ahankali yazare ta daga jikinsa yana faman kallonta mikewa yayi yacire rigan jikinsa already babu singlet box dinsa yabude yafito da drug dinsa yakoma kitchen ya dauki bottle water yasha maganin “ya kusa 50mins anan kan kujera a parlor jikinsa bai sauya basai ma kara vibrating yake “duk adduan data zo bakinsa yakeyi “can yaji kaman yafara lafawa yamike walking very slow yatura kofan bedroom din yashiga bacci take very tight bacci take very peaceful kallonta yayi for few seconds kafin “yawuce toilet alwalla ya dauro kafin ya dauki rigansa yamayar “ya shimfida prayer mat ya kabbara salla har sai wajan asuba yana nafila “kafin yasallame ya mike ya nufi gadon shafa cheeks dinta yayi tadan turo baki kafin gentle ta bude idonta dake much white tabarakallah ‘murmushi tayi masa ya daure ya mayar mata kafin ahankali yace wake up its time for fajr “Aydarh ta lumshe ido kafin tayi adduan tashi daga bacci ta mike yabita da kallo har tashiga toilet kafin ya janye idonsa ya girgiza kai ya tayarda sallarh bayan tafito daga toilet “tajawo hijab dinta,itama ta shimfida prayer mat ta kabbara salla shi yaja su bayan sun gama ta biya masa karatun ta bacci a idonsa bana wasa bah akan yasa shi mikewa ya haye gadon ita dai bata tashi ba kallonsa kawai tayi kafin ta kwanta kan sallaya tana rufe ido “karan door bell ta tayar dashi kusan sau uku tana ringing kafin ya tashi yasauko daga kan gadon ya dinga kallonta ta cure kanta cikin hijab tana bacci kaman wata baby “ga kafanta tadan leko kadan “ yana bin lallan da kallo “fita yayi ya bude yaga wani waiter daga the same restaurant din da aka kawo musu dinner jiya “waiter yamika wa malik cike da girmamawa yace here it’s your breakfast sir “malik ya gyada kai yace thank you kafin ya juya ya rufe kofan kitchen yakai ya ajiye yana jin kansa na wani irin nauyi yana masa ciwo “sallama yayi Still tana bacci ya duka yakama hannunta kafin yakira sunanta ta bude ido “mikewa tayi ahankali tace Good morning my Doctor yayi murmushi yace morning my girl yau kuma sunan dana samu kenan?ta gyada masa kai tana turo baki yace wake up munyi ranan bacci,tace Alright mikewa yayi yawuce toilet wanka yayi tass kafin ya dauro bathrobe yafito ga karamin towel a kansa kasa kallonsa tayi ta mike ta zare hijab din jikinta still taki yarda ta kalli ko da direction dinsa duk kuma yana lura da ita “bai ce komai ba ya dauko vaseline dinsa data saka ya chanza yana shafawa toilet tashiga itama tayi wanka lokacin da tafito,har yasa kaya wani blue T shirt ne mai zanan black sai black jeans yasaka p-cap yayi kyau

kaman wani dan gayun kasan waje bata san lokacin datace you looks perfect murmushi yayi bata yace ki shirya ki fito lets have breakfast “tace ohk “ fita yayi tahau shiryawa “abaya tasaka baby pink yah arrahamar rahimin yah rabbil alameen “warabul ka’aba tafi kyawu kyau tayi musulmin kyau da hadu yah rabbi how the gown suits her kaman campany don ita yayi abayan veil din ta yafa kafin ta dauko perfumes din da dr hafsa ta bata ta dinga kallon yar kwalbar kamshin na ne zautar da ita lumshe ido tayi ta bude kafin tafesa perfume din ko”ina na jikinta tafito kamshinta yayi sallama dago kai yayi ya dinga kallonta kaman zai cinyeta kasa tayi da kanta kafin ahankali tace gani “bai ce komai ba yamike ya wuce kitchen din ta bi bayansa tare suka shiga kitchen din kafin suka juye light food din sai coffee suka juye a mug, tare suka fito da kayan anan parlor suka zauna kan sofa babu wanda ke magana a cikinsu suka hau breakfast din. Bayan sun gama vedio call dasu dr ibrahim ta kallesa tayi shiru kafin tace auntie hibba tana wahala sir “malik ya gyada kai kafin yayi kasa da murya yace cikin ne yazo mata ahaka wasu kam har sai yazama babba zaka gane “tawara ido tana kallonsa kafin tace really?yace mata sure tayi shiru tayi lamo a jikinsa,can wayansa yayi kara yana dubawa yaga dr usama ne cike da girmamawa yadaga suka gaisa kafin dr usama yafada masa content din dazai fada masa sukayi sallama Still tana jikinsa kaman yan mage her boobs is taking him up yanda suke gogan gefan sa nasa sa jin wani yarrr”can tace masa kan yadaina ciwo ya girgiza mata kai kafin yace saura kadan but is still aching me “Aydarh tayi shiru kafin tace masa sorry yace jeki cikin karamin box din nan daga cikin karamin zip dinsa zaki ga paracetamol carry it for me tamike tace ohk “yanda ass dinta kew ani shaking cikin abayan yake ta bi da kallo,shiga tayi ta bude akwatin ta zage zip din daya fada “kafin hannunta yakai kan drug din daya ke sha takai kusan five minutes tana juya maganin a hannunta mamaki take tasan drugs sosai saboda abunda take karanta kenan tasan amfanin magani “shiru tayi tana mayar da maganin kafin ta dauki paracetamol din day ace kawai tafita kitchen ta shiga ta zuba masa ruwa a wani hadadaddan glass cup “tafito ta mika masa kafin ta ciran masa magani kwara biyu ta mika masa tadai kasa kallon fuskan sa karba yayi yace thanks cuddle bug ta gyada masa kai kawai yazame ya kwanta nan kan kujeran “ yana rufe idonsa, mikewa tayi walking very adorable tashige bedroom din ta zauna kan gado tana rufe idonta ahankali tasamu kanta da tambayar,miya keyi da maganin is he sick?tadinga maimaita sunan magani da amfanin sa kafin ta zame ta kwanta kan gadon da tunani kala kala a ranta “ can bayan sun karasa salla isha”I ta waiwayo ta kallesa ahankali tace ya jikin?ya gyada mata kai kafin yace so much better Alhamdulilah “tace Allah yabada lapia mai amfani yace Ameen Ameen,mikewa yayi yace

change ga mr joe can a waje yana jiranmu ‘ta kallesa kafin tace waye haka yace driver tace oh tace ina zamuje?yace provision zamu siyo aydarh tayi shiru kafin tace no I will stay kaje kawai “yace tau what of idan na bace nida bansan koina ba, aydarh tace ai tare dashi zaku tafi so bazaka bacce bay ace no tashi kawai ki sake kaya mu tafi “mikewa tayi ta bude wardrobe inda tajera kayanta dayan side din ku ta jera masa nasa “rigan sanyi ta dauka kawai tana cire hijab din ta daura kan abayan ta kafin tayi rolling da veil dinta tasaka perfume shidai already yafito parlor yana jiran ta fito “bayan ta fito ya kalleta yace wait tabi sa da kallo yakoma bedroom din ita kuma ta zauna kan sofa tana facing kofan bedroom din kalan rigan sanyin ta yasaka yana murmushi kafin yafito tana kallonsa batace komai ba har suka fita daga gidan malik ya rufe kaman yanda mr joe yanuna masa,kafin suka shiga back seat din daya bude musu malik nata kallon anguwar aydarh tayi kasa da muryar sa kafin tayi magana da hausa tace ni bana son gasa Allah malik yawara ido yace minene gasa?tace kana saka kalan kayana Allah kadaina yace wai saboda yan matan turawa su san ni mijin aure ne kema matar aure ce kar asamu matsala ace wata ta soni aydarh ta zuba masa wani harara tace basai ka dinga fita kai daya ba,balle ma har su ganka yayi murmushi yana shafa sajan sa yace I like this your perfume tace dan Allah ya gyada kai yana kama hannunta yana kallo lalle kaman yasa hannu a baki yaci,can yakalleta yace why baa yiwa maza this henna kallonsa tayi tana wara ido kafin tayi dariya har sai da yaji sound din dariya white clean teeth dinta tass suka bayana wanda hakorin gold dinta na makka yakara masa kyau “shagala yayi da kallonta har sai data hura masa ido kafin yadawo “tace to muje sai na siya lallan nayi maka yace kin iya ne?ta gyada masa kai yace kai haba ta turo baki kafin tace oh baka yarda ba yadaga hannunsa sama dasauri ya girgiza kai yace noooooo na yarda hajiya tace good boy “bakin wani katon super market mr joe yayi parking building din wurin yayi kyau har yagaji billahi bude motar sukayi suka fita a tare,mr joe yamika wa card din fidda kudi da dr usama yasaka ayi masa na can kasar kafin ya zauna a motar shidai yarike hannunta duk da baisan ta inda zasu bi ba amma he is acting well babu wani kauyanci saboda tsaban illimi dake zaune a kansa “cikin super market din suka shiga babu inda aydarh bata sani ba a wurin “still suna rike da hannun juna ta dinga jansa suna siyayyan su shidai binta yake tana daukan duk wani abun amfani daya dace, ganin bata wani dauka dayawa bay asa doubling abubuwan data dauka tana laftawa a basket din sai data cigaba da kallonsa har yagama kafin ya tura basket din tana biye dasu “wajan luxury Expensive chocolate suka je “unique chocolate ta dinga daukowa tana sa su a karamin basket din da ta dauka malik yace keda bakya shan chocolate?sai sannan ta juyo tadan kallesa tace wannan is not

same da wannan malik yagyada ka kawai yana kallonta har tagama kafin yace shknn abunda kike so?tagyada kai kafin dasauri tace nooo I want sanitary pads malik yace ohk “shima kusan pack gudu dayan mata kafin yayi payment ya mika card din kafin aka cire akayi packaging kayan a leda kafin aka ba wani ya dauka musu har a mota “.bayan sun gama shirya kayan a kitchen komai yayi daidai a kitchen din, tafito ta samesa zaune yana research bedroom tawuce tayi shirin baccinta ta kwanta, shima bai jima ba yazo ya kwanta ,alhamdulilah yayi bacci yau kasancewan yasha magani bayan sun gama sallarh asuba “Aydarh komawa tayi ta kwanta,malik kau kasa ko da baccin yayi ma yarasa miyasa yake jin wani kala yau din nan kasancewan yau ne first dinsa a aiki sai yake jin kansa wani kala ganin dai yakasa baccin gashi 7 tayi kawai ya mike yashiga toilet yayi wanka kafin ya fito ahankali ya tayar da ita yace je ki kiyi wanka kar muyi late ahankali tashiga toilet din tayi wanka tass tafito tana shiryawa yana kitchen tea kawai yayi making musu jiya sun siyo slices bread, lokacin daya shigo dakin har sarkewa yayi wajan kallonta Allahumma bareek tabarakallah masha Allah yah rabbi!!she is damn cute her body is a necessary she has the finest body structure in the world her skin is very cool and creamy har wani shining skin dinta keyi yah malikul muliki “is this how beauriiiii she is Ahhhhh whatttttttttttttt.. yaseen tafi kyauwu kyau tafi hadewa haduwa “English gown tasaka dark blue sai belt din daure rigan takawo chiffon veil shima dark blue tasaka sai wani karamin necklace da dan kunnanta silver mai kyau ga kuma bracelet hannunta shima na sarkan mai dan azaban kyau fuskanta hadda powder ga kajal da massacara,sai red lips data saka kadan yayi kaman nude ma Allah “ yabi kafan ta da kallon hills ne masu uban su kyau wanda dakanshi yayi mata choosing a boutique din dasuka siyo, sunyi tsini mai kyau ga lallan kafan daya sake ma takalmin kyau Wallahi yarda tayi kyau har fizgansa take “ahankali tace masa shall we?gyada mata kai yayi kaman dan yaro kafin ta tashi kamshinta na fita ahankali yana shiga hancinsa “ kusa da inda yake tsaye ta karaso tace muje yayi kasa da murya yace nope bazaki fita ahaka ba “Aydarh jin abunda yace yasata langwabar da kai tana turo bakinsa tace pleaseeeeeeeeeeee sir billahil azim kaman tayi masa wani magic yazama kaman sakarai “yace ohk “tayi murmushi kafin takama hannunsa suka wuce parlor sharp sharp suka karasa breakfast din ta mike tana gyara masa suit din jikinsa murmushi can kasa tace handsome Doctor I wish you all the best for your first sir,malik yace thank you cuddle bug “ mr joe na waje yana jiransu kafin suka fito daidai zasu shiga mota karan notification yashigo wayan text sms din dr ibrahim yashigo a wayansa yana wishing dinsa all the best for the work “ malik yayi murmushi kafin yayi replying message din the journey was silent kafin “ mr joe yayi parking

baki wani katon apple store malik ya tambayesa kafin cike da girmamawa yafada masa sako dr usama yace a karbo masa “ fita mr joe yayi yashiga apple store din already anyi masa packaging latest 16pro sai kuma normal 16”da wani Expensive MacBook mai dan azaban kyau.

da haka Allah yaso babu dadi sam “ummi tamike ta warwari tissue tasharewa aydarh hawayen ta tass tasake gyara mata pillow ta kwanta “kan prayer mat ummi ta koma ta zauna tana fara lazami sai ga Sallaman hajajju tashigo ga leda kasassan kaza a hannunta tana shigo tanemi wuri ta zauna kan plastic chair “tana kallon ummi tace shi audul din tafiya yayi ne asiya? ummi tace eh hajiya hajajju tace uhm nan dakika ganni daga wajan uban yan biyun ramda muke ummi da mamaki take kallon hajajju tace wai hajiya kina nufin wajan senator ? Hajajju tace can fa hajajju tayi kasa da murya tace Wallahi nasa naga wani katon mutun ashe yarone wannan ai karshan shi 38 Wallahi gashi dan dogo bafullatanin asali ga naira ta zauna hajajju tace bakaramin tausai suka bani bai ta dashi karki so kikaga yarda take sonshi shima yana sonta amma gaskia dai sonta yafi nashi duk ajin ramda har kasa ta dauka ta gaishe sa billahi tau badai ruwana amma ko ma mi nake shiryawa dakomai yatafi nomal duk zan miki bayani saboda Allah yarinyar nan ramda na dauketa kaman diyar dana haifa jin take nake har cikin raina shiyasa zanyi duk yanda zanyi na share mata hawaye daga nan tayi shiru ta hau bude leda kazarta wanda ex husband din dr raudarh yabata bundle guda na 50k dr raudarh kuma ta tsaya ta siyan mata kazan a hanya ummi dai sai bin hajajju take da kallo don ba dan karamin mamakin ta tayi ba ummi tace tau Allah ya kyauta “hajajju tamike ta dauko plat tasaka 6 pieces na kazan ta mikawa ummi tace gashi kiba matar danki tunda shi yamaida kanshi wani kala yaro ga shegen kudi amma bazai iya rike siyan kaza biyar kullun ba dafa yanzu an sallami matar Wallahi gashi yau har saura kwana biyar su juya can kasar idan Allah yataimaka naji zan iya zuwa nace masa na amince da binsu can garin kaman yanda yaroke ni “ummi dai tayi shiru amma tasan yaushe malik ma yayi wannan maganar mikewa tayi takarasa kusa da aydarh tace ta tashi ko zata ci nama aydarh tace bazata ci bai dan tayi overfeed amai zatayi ummi ta lura bata son abinci bata son matsa mata ne kawai yasa ta rabu da ita tadawo kusa da hajajju wanda hajajjun ta koma kan bargon datake kwanciya tacire mayafinta sai faman cin kazar take babu sauki a lamarin ummi tamikowa hajajju tace gashi hajiya kinji tace ta koshi hajajju tabi plat din da kallo tace tau aie shknn ke sai k ici wannan din daman wannan idan tayi saura audul nayi niyyar na aje mawa bawan sai wahala yake yakasa zaune yakasa tsaye amma ko abincin kirki baya ci kuma babu wanda yadamu da haka tsabagen rashin tsoron Allah ummi tadaiyi shiru just 3 pieces taci na kazan ta ture hajajju na lura da ita taci mai isar ta ta rage pieces daya tahade da wanda ummi ta ajiye ta kulewa malik a leda “toilet tashiga ta wanke bakinta kafin tadawo ta kwanta ummi tarage hasken dakin saboda aydarh har hajajju ta kwanta tayi maza ta tashi tace kinjini da rashin kan gado wai yanzu tafara takawa ba laifi?ummi

tace eh hajajju tace ai kamata yayi a sallamemu haka nan atai gida kuma ayi case tunda baa asibiti zamu watse ba jinyar fyade ahtau “ummi dai tayi shiru ta kwanta “hajajju tagama surutan ta kwanta aydarh duk najin su don yanzu andaina mata alluran bacci kuma kaman jikinta najiran dare yay isai tafara jinta sam babu dadi ga tunani kala kala aranta babu abunda ke mata kai kawo akai irin maganar data gaya masa a dazu ji take kaman wani abu na damunta “sam kuma sai taji sunan linda datakira masa a dazu wani irin kishi nadawo mata yanda yatashi yafita daga dakin dazu idonsa yayi ja sosai kaman wanda zaiyi kuka da alama maganan ta yayi masa ciwo sosai rufe idonta tayi trying hard to sleep. Oum ta durkusa har kasa tahade hannunta both two din tayi wani irin kyau cikin grand super datasaka ash anyi mata riga da zani ga bangles na gwal da zobe sai earrings da necklace shima duk dai set ne da da bangles din dayan hannunta da apple watch mai tsada abba dake kallonta ko kiftawa babu yace what is all this wife saboda mi eh? miyasa kike son nayi abunda bana so eh?nagaya miki yaron nan sai yasakar mun yarinyar miye na damun kanki koma miye yawuce aie kuma kusantar mun yarinya dayayi da kansa my only problem will be if he impregnates her kuma shima sai an zubar don baby bazata zauna dashi ba anymore sai yasakarmun ya am I cleared yafada yajuya kawai zai fita oum ta mike tabi bayansa kafin yafita tayi saurin shan gabansa ta rufe kofan dakin tasaka key ta kamosa da karfi tawani kalan fashe da kuka tana hade bakinsu Wallah isai da zuciyansa tayi wani kalan harbawa zarah know his weak point miyasa zata dinga zubar da hawayen ta bayan tasan is the most worst abun dayayi hating in his whole life miyasa zatayi masa abunda tasan zai hakuri duk girman laifin da akayi masa cire bakinta tayi daga nasa ta cigaba da masa kuka while placing her head on his board chest “har yana jin damshin hawayenta kasancewan babu riga a jikinsa kasa daurewa yayi kawai yaja ta yazaunar da ita kan gado taki yin shiru sai faman jan kukan take ransa na baci da this kukanta “rungumeta yayi so tight a jikinta muryan shi can ciki yace shshsh u know I hate your tears kinsan bana son kukanki kiyi shiru and tell me abunda kike so “sai dakara kukan na almost 4mins kafin tayi shiru tana jan majina tana faman saukan da ajiyan zuciya ya cigaba da patting bayanta “ahankali tace nikawai karka raba su they love each other habeeby how will you feel idan sheik yace sai kasakeni (babanta)eh habeeby?how will you feel dasauri abba yarufe mata baki yace bazai taba cewa ba and karki sake cewa haka zaki saka zuciyana ta buga “oum tace shima Abdoolmalik haka yake ji yah umri haka yaji shima yaron!abba yayi shiru baice komai ba amma maganar da tayi dinnan duk sai yaji zuciyan sa tayi weak tayi sanyi “ganin tafara samun kansa yasa tamike rike dashi suka shiga bathroom din ta tayi masa wanka kaman wani yaron ta shiryasa yau

abinci ma ita tayi feeding dinsu shidai abba sai wani kamewa yake ala dole bai son yabada wani fuska “wunin ranar haka sukayi sa duk da taga akwai alaman nasara amma bai ce mata eh ko aa ba tadai cigaba da lallashinsa “,yau baki daya malik keeping kansa busy yay isai da yatabbatar angama komai na gidan daya siyawa abba harta da security’s an zuba a gidan already yasiya cars a ajiye a gidan ko daya nunawa abby tasa kasa magana yayi yace yabari idan an sallamo su ummi daga asibiti zasuyi komai a tare nagani gidan damotocin banki yaje tun safe sai yanzu yasamu daman ma abby upgrading acct dinsa 2B yasaka masa kafin yawuce can campany steels din wanda tun yana Washington suke contacting juna damasu campany a ranar yagama komai campany baki daya ya koma na abby bai gayawa abbyn ba don ko takardar dasai saka hannun bai basa bay ace sai ana gobe zai koma su maryam ma duk yafara musu processing school halime dake son base itama ta online yafara nema mata admission throughout yau yayi keeping kansa busy ko tunanin maganganunta baya son yayi sam yayi avoiding asibitin yau “duk dahaka tunaninta yana nan makale aransa “Abby yace sannu malik “malik yace yauwa abby nayu tunanin kafita yace aaa yanzu nadawo daga kai ma yan asibiti sako maryam nacan asibiti malik yace su aysha fa? Abby yace sunje gaisuwa maman kawarsu ta rasu “malik yace eyyerh abby yace kaje kayi wanka sai kaci abinci kafin ayi magrib idan kaje asibitin sai kadawo mun da maryam malik yace tau abby yafada yana wucewa dakinsa na gidan.Sai daya tsaya yasiyan musu fruits da few favorite abunda take ci “yayi gaba wani babban eatery yamata takeaway na grilled chicken yawuce asibitin yana shiga asibitin sai ga kiran dr ibrahim bayan sun gaisa yake tambayar su flight din karfe nawa ne dr ibrahim yafada masa malik yace Allah yakaimu ya kashe wayan yana maidawa cikin aljihun wandon jeans dinsa yashiga dakin da sallama ya zare shade din idonsa tare da cire p-cap dinsa maryam na zaune kusa da aydarh dayau ta chanza gown din asibiti tasaka abaya purple plain mai touches white mai kyau sai purple inner cap tadan zame daga gaban goshinta gashi luf luf tayi kyau bana wasa ba ga rahamar ciwo “daurewa yayi yadauke ido daga kallonta yakaraso yana gaishe dasu oum da rufaidarh da ummi sai hajajju dake zaune tana shan tea da bread da daran nan fa “hajajju tace duk ahankalinmu ya tashi da kyar nasamu ina dan shan wannan ruwan shayin da guntun biredi munyi tunanin guduwa kayi kabar manah da ita da lura nasa cutar kayi niyyar yi ta maza shidai bai ce mata komai ba yakarasa yana ajiye kayan hannunsa hajajju ta washe baki tace dan albarka kenan malan audul daftan turawa “maryam tace ina wuni yayah kadawo malik yace lafiya autah ya jikin auntie dinki?maryam na murmushi tace Alhamdulilah yayah gata nan yanzu ma muka dawo daga exercise “kafan yayi sauki aydarh na jinsu ta

juyar dakai ahankali tace good evening malik najinta bai amsa ba yayi mata shiru yana daga tsaye yabude ledan sabbin drugs din da aka bata yau ya duba oum tamike takalli rufaidarh kafin rufaidarh tace yayah muje waje mu danyi magana ummi tace tau shknn muje rufaidarh “ fita sukayi hajajju ta bisu da ido tana cigaba da bude ledan fruits din daya kawo malik yaja plastic chair gaban gadon ya zauna yana kallon maryam kafin yace autah nr din nan datace nayi mata hotspot sai kirana take kuma gaskia nima tayimun maryam tayi shiru don bata gane ba amma sai tabi shi.

Tabi sa da ido can dai tagane abunda yake nufi daman ko da can they can pretend ita dashi shiyasa she is his favorite sister “tawani wara ido kai kace gaske tace kai haba yayah daman nasan da biyu tace kayi mata hotspot kuma daga hotspot shine hadda karban digits dinka ita kam a gaishe ta malik irin da gasken nan anyi haka yayi da fuska yace maybe ta lura banda mata kinga before 5 days din yacika sai a fara processing nema mun auranta mu wuce kawai Maryam ta jinjina kai tace tau yayah kai kana sonta ne?malik yayi yar dariya yace why not?baki ganta bane?ai the lady is hotter billahi aydarh har ji tayi kwalla na neman zubo mata har ta mance rabon datayi kalan wannan tashin mikewa tayi dasauri don ita tama wani mance dawani stitches a jikinta duk suka bita da ido hajajju tana shan kankana itama dai aydarh take kallo baki bude “data wuce tagabanshi saura kadan ya shide whatttttttt wani kalan kamshi daya daki hancinsa mai tafiya da imani ga kalan abayan yahau jikinta her well shaped kaman ansake fidda shi ko miye ma zai ce hajajju tace “kodai fitsari ya matse ta yarinyar da ko tafiyar kirki bata iyawa amma kaga kalan tashin da tayi “gaban ummi ne take zuba lanbo son ranta kadai audul an cuce ka anbaka maka jabu yarinya sai dan banza kyau da shagwaba ta dinga sukunyan dakai kaman tsohuwar munafuka ahtau nidai ba ruwana bara nayi shiru naga bani hajara aka cuta ba bakina alaikum babu ruwana aydarh ko tsayawa jin maganar hajajju batayi ba tashige toilet tayi banging door din garam sai sannan malik yadauke idonsa yarufewa maryam ido guda itama tayi masa sukayi shaking hannu sai kuma maryam tayi wani kala da fuska tace Allah yayah nidai ba ruwana kawai karka jamun ma auntie aydarh taji haushina kaga fa kaman tayi fushi duk da ciwon kafan ta daure ta tashi fa “malik yayi murmushi yace no lily ai taimako kikayi babu abunda zatace allow her I will handle the rest case in sha Allah maryam tasake kasa da murya duk yanda hajajju ta iya amma takasa jin abunda suke fada sai faman shan fruits dinta take duk zatayi lokacin su daga uwayan har yaran dasuka dauke ta kamar wata yar iska ana ta magana bata “tace kai yanzu yayah is there any lady in this dunia data rage kuma kasota after auntie aydarh? Malik yayi shiru baya

magana suchs da sisters dinsa ita kanta maryam din kasa rikewa tayi har sai datayi maganar saboda yana son ko da firanta ne a dinga yi masa yayi dan jim kadan kafin yace why do you say suchs Lily?maryam tasake matsowa da kujeranta kusa dashi tace yayah see how beaurie she is “ga ta Wallahi yar gayu yayah and she is very nice babu ruwanta Allah yayah kaji fa yanda take kunya da respecting din ummi and abby “yayah kai kam ka taba jin mai magana kalan nata yah rabbi yayah do you see how prettier she is when she smile “malik dake kallon maryam ko dauke ido babu don mamakin maryam din ma yake yace tau ko dai matarki ce ba matata ba da duk bazan ga wannan abun ba ya mike yace dana samu wata zanyi aure maryam ta tabe fuska tace dan Allah yayah aaa Wallahi babu wacce zaka samu kaman ta nidai kaje kabata hakuri kace wasa ma fa kake Malik yace Alright jirani yanzu ki shirya mu wuce gida yafada yana nufar hanyar bathroom din “hajajju tabisa da ido kafin ta juyo tana kallon maryam tace tau ko dai bai lura wannan yarinyar tashiga ba maryam tayi kasa da murya tace kedai ki bude naman mu ci babu ruwanmu hajajju tawashe baki tace Wallahi “cikin wall din toilet din yaganta tsaye tayi wani kalan kicin kicin da fuska kaman zata fashe da kuka yakarasa har kusa da ita bayan ya rufe toilet din hadda key idon har yakawo ruwa bata so tayi magana ba saboda tana iya fashewa da kuka ahaka ta daure dai tawani sake hade rai shikam Wallahi yakasa janye idonsa kanta bai san irin son dayake ma aydarh ba shidai yason idan zuciyarsa ta buga sanadin sonta ne “tace miyasa zaka shigo mun toilet while kasan ina ciki tafada cike da tsiwa “malik yayi shiru kaman bada shi take magana ba tasake masa wani kallo tace why do you follow me here?ai baka da mata ba kaje kana gaya musu baka da mata har kana yiwa wata connecting hotspot and kana sharing digits dinka kai ga wanda baka da mata that means I should report you to the police tunda babu aure tsakanin mu kayi sexing dina ohh I mean kayi raping dina tunda is against my wish’s ai kasa ni in all this pain kasan kalan wahala dake akwai a wannan stitches din kasan irin wahalan danake sha I didn’t even thinks I can continue surviving da wannan kalan abunda kayi mun “ mark this Abdoolmalik sai kasake ni banayi auran anymore daman bana sonka kai dakake sona that is your business not mine am I cleared??tafada dan karfi tawuce trying very hard not to cry ga yanda take tafiya dasauri na mata zafi amma ahaka ta daure yama kasa ko da motsi balle yayi attempting hanata fita ficewa tayi daga toilet din tabar shi nan a tsaye kaman status yana ta kallon inda ta wuce ko dauke ido babu “Maryam ke gefen hajajju tana sauraron bayanin da hajajju keyi wa baba a waya sai kallonta take ji duk bayanin babu kai balle kugu she is just talking mean less “ Aydarh tayi avoiding hadda ido dasu tawuce ta side din gadon ta zauna tana kwantar da

kanta in between her laps zugin data daina ji kwana biyu shine yadawo mata ita kam yau ko mi zai faru bazata sake kwana asibitin nan ba sam batajin dadin rayuwanta she need to rest bata taba shiga kalan wannan halin ba a rayuwarta sai yanzu da malik ya shiga rayuwarta she prepared lonely a yanzu idan aka raba auran abba ya yafe mata zata koma can Cyprus takarasa karatunta za tadawo ma a fresh bazata sake dawo wa Nigeria ba kuma saboda bataga dalilin haka ban “Maryam dai sai kallonta take bayan hajajju tagama waya tamike tana dauka tissue ta goge hannunta tace bara kiga naje wajan ramda nasan yanzu tashigo kwara azo a sallamar masa mata tun kafin yakara aikata wani mugun abun kuma duk aji kunya kwara su tattara su tafi ta lura yarinyar itama ta warke tunda har wata irin tafiya take musu tana juya mazaune ita ummi dake ta gadin aida gashi nan har sun san su fa kewaye ita da miji dayake babu tsoron Allah a ransu ita kuma bata tausan kanta ko gama warkewa batayi ba har hajajju tafita bai fito ba hajajju na fita maryam tamike gently takara so gaban gadon ta zauna gefen aydarh ta dafa ta dagowa tayi idonta yayi ja sosai tasakar wa Maryam murmushi “maryam ma ta mayar mata kafin tace auntie wai miyasa kike fushi da yayah am so sorry to ask aydarh tawara ido tace noo maryam tayi shiru tace koma miye kiyi hakuri ki yafe masa dan Allah,aydarh tayi murmushi wanda iyakar sa lips tace ohk yah mariam maryam tayi murmushi itama kafin tace mi zan zuba miki ko fruits din zaki far asha ?aydarh ta girgiza kai tace ah’ah na koshi maryam tace kullun bakya cin abinci ke kin koshi aydarh dai batace komai sai dan murmushi take amma Wallahi yau malik yayi masifan bata mata rai ashe kenan ita ba matarshi bace har zai bude baki yace ta lura baida mata tunda haka yace kuma haka yazaba zata nuna masa itama bata da miji “kuma cutar dayayi mata yayi ma rayuwarta Allah ya isa ba yafe mishi bak aran bude kofan sukaji ko dagowa batayi ba balle yama sa ran zata kallesa fuskan sa babu alaman wasa yakoma asalin malik dinsa yakalli Maryam yace pack your things and wait outside ganin yanayinsa yasa maryam ko musu batayi masa ba tasaka hijab dinta kowani sallaman kirki batayi wa aydarh ba tafice daga dakin sai daya matso kusa da ita gab kaman wanda zai fado kanta still kanta nakasa ko motsi batayi ba his voice sounds very serious yace I will show you nine babba and nine mijin har tadago zata gaya masa magana taga ya juya walking very majestic har wani bouncing yake ga tabarakallah kaman ma kara tsawo da kwari yayi bayansa tabi da harara yana fita tafashe da kuka tana wargo pillows din gadon kasa Wallahi tsaban bakin cikin sa data sha yau sai taji ma babu inda ke mata ciwo so take kawai asallameta ta wuce gida let her feel herself tana son tazama alone “ummi tace da dai anduba itama yarinyar fatima tunda shi zaman aure baa dole so kawai ku qyale mun yarinya tunda tace batayin

auran kuma “inaga kwara a rabu da ita kawai zai fi oum takalli rufaidarh kafin tace auntie asiya yarinta ce fa kuma dan dai tana kan dokin zuciya ayi hakuri kawai tunda abban yasauko idan kwanankin hutunsa sun kare yadauke matarsa kawai su tafi ummi ta girgiza kai tace inaga abar maganar nan kawai tafada tanayin gaba daga oum har rufaidarh bayanta suka bi da kallo kafin oum tasauke wani ajiyan zuciya underneath her breath tace uktiee kinga wani sabon abun kuma yanzu ita auntie asiya babu yanda zaayi tabar bayan aydarh duk dana son itama she is not happy with decisions dinnan she is just trying to be okay amma babu komai zanyi magana da yah ibrahim din dashi kansa Abdoolmalik din rufaidarh ta jinjina kai tace gaskia dai uktiee ina ga shi zaifi amma maganar raba aure babu cus aydarh tasamu mijin one in trillion kaf naija kai kaf dunia nan uktiee shine kawai irin mijin da idan aka ba baby baa cuceta ba shine perfect combo dinta oum ta girgiza kai tace in sha Allah uktiee komai zai zo karshe tirka tirkar da akasha nakusa 22 years da yarda Allah cikin kwana biyu komai zai wuce rufaidarh tace Allah shi yarda uktiee “oum tace Ameen suma juyawa sukayi suka bi bayanta,a bakin kofan dakin ummi taga Maryam tsaye kafin ma tayi mata magana sai ga malik yafito yana kallon ummi,ahankali Yace ummi sai dasafe tace Allah yabamu alkhairi “tana shiga dakin takarasa gaban gadon dasauri har sai da gabanta yafadi a rude take tambayar aydarh abunda yasameta “tace baby jikin ne?aydarh ta girgiza kai tace shi Abdool din yayi miki wani abun?nan ma ta girgiza kai ummi tazauna tace inalilahi waina illahil rajiun baby kagaya mun miya faru kinji aydarh tashare hawayen ta murya very slow irin na shagwababin rich kids dinnan tace ummi nagaji da zama anan ayi discharging dinmu please ummi tayi shiru kafin tace are you sure is the only problem baby? Aydarh ta gyada kai tace erh “ummi tace wipe off your tears kinji baby in sha Allah yanzu zan saka a sallame mu shiknn aydarh tagyada kai kaman yar baby ummi tayi murmushi daga oum har rufaidarh suna tsaye jikin kofa suna kallon ikon Allah” ummi na juyowa suka hada ido dasu kowa yayi murmushi oum tace tau bara mu zauna idan yanzu zaayi discharging din naku sai muyi dropping dinku gida basai kun tado yayan ba mijin ma naga yatafi aie yanzu ummi tace da kau mungode bara naje wajan dr nasan hajiya nacan ma oum tace hajajju ikon Allah na lura ai tana ji da dr din ummi tace ahhh bana wasa ba fa sosai take ji da ita “zama sukayi ummi tafita rufaidarh na kallon aydarh tace kina jina?aydarh ta gyada kai tace maganar kice a raba aure kar naji kar nagani ko dawasa baby girl kowa dakika gani yana son yayi aure ni kaina against my wish nake zama haka babu aure amma ko yanzu miji yazo aurena zanyi “babu wanda ke son yayi aure yafito ball eke yar yarinya dake kuma mijinki loves you beyond imagination haka ma both his mother father and his sisters duk suna sonki

kuma dan uwanki ne he is your elder brother tau kiyi hakuri ki koma ita kanta mamarsa bata son ace tayi rashin aldaci ne amma Wallahi duk wani son dazatayi miki saboda yaronta ne hope I made my self very cleared ita dai aydarh tayi shiru batace komai ba rufaidarh tace idan kuka je can gidansu tunda yanzu dare ne gobe kisaka adawo dake gida ki cigaba da zama kafin ku koma akwai mai gyaran dana ke and kizo ko saboda Abbanki “oum najin bayanin da rufaidarh duk kewa aydarh tayi shiru kaman bata wurin don itama hakan yayi mata “Dr raudarh tagama duk wasu rubuce rubucen da zatayi tamikawa ummi kafin tace ta cigaba da sit bath din har jikinta yazama daidai daidai kar ayi wasa aunt please ummi tace in sha Allahu dr “sauran magungunan dasuka dace dr raudarh tayi prescribing tace aje can pharmacy a karba “ummi tayiwa dr raudarh godiya kaf bill din malik yayi settling sai ma ciko da zaa basu ,Bayan ummi ta dawo daga pharmacy hannunta rike da ledan sauran maganin ta shigo dakin cleaners din asibitin suka kwashe masu kayan su suka saka a booth din motar oum tafiddo sabon kudi daga jikkanta tabasu har wajan mota dr raudarh tayi musu rakiya aydarh na jikin ummi suka shiga motar rufaidarh tashiga gaba sai oum ta zauna gefen aydarh suna jiran hajajju dasuke sallama da dr raudarh ita dai dr kaman zatayi kuka saboda tafiyan hajajjun “ hajajju tace kinga karki damu goben dai kizo gidan kaman yanda nace miki in sha Allah babu abunda zai gagara kinji ni? Dr tagyada kai tace tau shknn hajiya Allah yatsare har hajajju tayi gaba sai kuma tadawo tace shin ramda kodai telan nan dan iska ne duk mutanan adamawa basu sani ba daga dan modiredin dinki shine zaka kwashe kusan kwana biyu kana abu guda gakuma uwar kudinsa an damka masa hannu tau ko dai baida tsoron Allah nufinsa ya handame kayan ganewa ce bamuyi ba?dr raudarh tayi murmushi tace in sha Allah zan taho miki dasu gobe hajajju tace tau Allah yakaimu lafiya bara mu tai gida kuma a cigaba da fafatawa .Bayan sun sauke su babu yanda ummi batayi dasu oum ba su shiga oum tace aaaa zasu dawo in sha Allah dare yayi yanzu daman hajajju ko dawasa batayi niyyar su shiga ba wucewa sukayi ummi suka shiga gidan kasancewan akwai nepa koi na gidan tarr ga anshare shit ass babu ko alaman dirty.

Ummi tace ko zaki sake yin wanka baby amma fa akwai sanyi sosai “Aydarh ta girgiza kai tace ah’ah ummi yayi hakan ma ummi tace tau shknn yau dai ba custard zaki sha ba abinci zaki ci kaman kowa aydarh tayi kasa da kai tayi dan murmushi ahankali tace “to”ummi tafito tsakan gidan ko’Ina da hasken glob tadaga curtain din dakinsu aysha duk suna kwance banda halime dake cleansing white soft face dinta dake nan keta glowing ummi takalleta kafin tadauke ido tana kallon maryam dake ta latsa wayan aydarh

snap kau sai wanda ta manta ga 16 pro mas a hannunta ummi takarasa shigowa tac eke wai bazaki bar mata waya ta huta ba?maryam ta tashi zaune tace yayah ma fa yace kafin ya tafi duk zai siya manah wayan nan halime tace ummi kin kau san yayah har yasiyan mun form din base duk ta online yaketa mun processing komai billahi “ummi tayi shiru don mamaki ne yakamata batace komai bat ace ku kashe wuta kafin ku kwanta aysha tamike zaune tace ummi ko zaa girka mata wani abu ummi tace ba white rice da stew kukayi ba?aysha tace ehh shine mukayi ummi tace salad ne komi?aysha tace yakare saidai akwai fresh a fresh hadda lemon ma shima fa yayah bai ci Komai bas ai faman bakin rai yake Wallahi idonsa yayi bala’In ja ummi tajuya tana fadin Allah yakyauta kitchen tashiga saida tafara warming hadaddan stew din data sha kaza kaca kaca a ciki kamshin is simple amazing Wallahi kaman mi “kafin tafito da fresh lettuce din tahau yankawa bayan tagama tayi slicing din cucumber da tomotoes sai lemon data matsa kadan a ciki ya warware “kadan tazuba shinkafan daidai yanda tasan aydarh zata ci kafin tazuba stew din akai kusan ma duk pieces din kaza ne ta saka enough salad a sama wani plate tasake dauka tazuba shinkafan kafin shima tazuba stew din da salad din tasa another plate tayi covering dinsa kafin tadauki spoon tadaura kan Abincin data zubawa aydarh takoma dakin kwance take ta lumshe idonta looking very pale and sick kaman yanda take dai a asibiti alaman har yanzu bata zama fully recovered ba daman sai ahankali karasawa tayi gabanta ta ajiye plate din kan dan bedside din gadon kafin takira sunan aydarh “Aydarh tabude ido tana tashi zaune ahankali wanda halinta ne yin komai ahankali sai da ummi ta tabbatar tazauna very comfortable a gadon kafin tadaura mata pillow a laps dinta tadauki plate din ta aza kan pillow tace eat kinji baby bara nayi making juice ina zuwa kinji “yanda ummi ke treating dinta kaman wata yar little jewel abun nasa ta kunya da jin dadi “har ummi tafita aydarh nasatan kallonta maganganun rufaidarh ke mata yawo akai that means idan tace bazatayi auran ba kuma da malik kenan ummi bazata cigaba da sonta ba shknn kuma babu ita babu su “ji tayi wani kala duk babu dadi kawai tasa hannu tadauki spoon din tana juyasa a cikin abincin duk da ya burgeta kuma tanajin yunwa tana so taci amma sai taji abinci duk yafitan mata akai Wallahi,ummi nafita tayi knocking dakin malik takai kusan 5mins kafin yabude dakin don baisan ummin bace bai masan sun dawo ba yana ganin ummi yace ummi wani abu zaki dauka ai da kin kira sai nakawo miki ummi ta girgiza kai tace kazo daki kasame ni tana fadin haka tawuce kitchen abincin data rufe da plate tasa spoon tafito dashi tashige dakinta tana shiga ta ajiyesa gefen gadon tazauna tana facing aydarh ganin tafara cakular abincin ummi tace common dota sai kinji abincin nan tass rashin cin abinci

ke sa har yanzu babu kwari a jikinki ga strong antibiotics kin asha ki daure kici abinci aydarh tace “to”dasallama yashigo dakin idonsa kanta yakalleta for few seconds kafin ya janye ido yazo yazauna gefen ummi yakasance sun saka ummi tsakiyansu Wallahi ko dago kai batayi ba balle takallesa abinci gabanta kawai ta cigaba da turawa duk da ba directly yake kallonta ba amma yana lura da duk abunda takeyi “ummi batace masa ci kanka ba ta dauko plate din abinci tabasa ahankali tace finshed it all bana son naga saura “malik yakarba duk da baya jin cin abincin amma babu musu shima yahau ci sai abun yazama kaman gasa kowa cikinsu sai faman cin white rice din yake ummi dake lura dasu both tarasa miyasa take jin kalan wannan pleasures duk lokacin data gansu tare yah rabbil alameen bazata iya zama mai son kai ba amma wannan hukunci na aydarh tafi kowa bakin ciki dashi idan auran nan yarabu ciwon zuciyar dazatayi a yanzu sai yafi nada she is just managing her situation she is just trying to be okay will she is not! mikewa tayi babu wanda tayiwa magana cikinsu tawuce kitchen bottle water data gani cikin fridge shine tadauko kwara biyu duk basu dawani sanyin kirki har ummi tafita tadawo babu wanda yayi wa dan uwansa magana ummi nashigowa tafara mikawa aydarh ruwan gently tasa hannu ta karba kafin tace thank you ummi “ummi tayi murmushi kafin tamikawa malik shima karba yayi ahankali shima yace nagode mama “ummi tasake komawa tsakiyansu tazauna sai da aydarh tacinye abincin tass kafin tabude ruwan zata far asha ummi ta tsayar da ita cike da kulawa da bata drugs dinta yanda dr raudarh tayi mata bayani duk yanda takai darashin son magani idan shi ko ummi suka bata tarasa dalilin dayasa take karba Malik sai satan kallonsu yake yana mamakin yanda yau take shan drugs ko bata fuska babu “juyawa yayi kawai yana facing wall after tagama shan drugs din ahankali ta kwantar da kanta a shoulder ummi don bacci takeji bana wasa ba “ takai kusan two minutes ahaka kafin yajuyo yana ganin yanda tayi Wallahi bakaramin dadi yaji ba ganin yanda ummi da aydarh ke masifan son juna kaman irin uwa da da dinnan “sunyi kyau ahaka he cannot hold it but to smile yayi murmushi kadan kafin shima ya kwantar da kansa a kafadan ummin “ummi batayi tunani ba kawai sai jin kansa a shoulder dinta tayi abun har yaso yabata dariya aydarh na lura dashi bata tashi ba kuma batace komai ba ummi ma tayi shiru tana sauraron kai kawon da zuciyanta ke mata Allahu akbar wai yau itace a zaune tareda malik dinta dakuma matarsa which favor of Almighty can she deny Allahu akbar “kusan twenty minutes suna ahaka ummi bata gaji bak o da tagajin zata iya daurewa bazata so su tashi ba a kafadan alaman saukan numfashin aydarh taji ahankali ahankali ya sauya bacci yadauketa kenan baayi good 10mins ba shima hakan sai ga baccin yadauke sa ahankali tadaga both hannunta tayi placing a cheeks din

murya can kasa don batason su tashi tace Allah yayi muku albarka ubangiji yanuna isar sa da ikonsa akan wannan aure naku Ameen Ameen! Almost 40 minutes tunda suka kwantar da kansa kan both shoulders dinta tama rasa wa zata tayar a cikinsu saboda tasan both of them needs her suna son su ji dimin jikinta ko datayi rantsuwa bazatayi kaffara ba rabon su da kalan wannan baccin har sun manta tunda tana daurewa kar tayi bacci amma wannan peace of mind din data samu yasata jin wani kalan bacci ga her body is very cool yah Allah " itamaa ummin Wallahi ahakan tayi baccin duk suna ahaka.Kiran sallarh asuba da akayi ya tashesu daga wannan baccin takuran dasukayi malik yadinga bin wurin da kallo wai ahaka suka kwana dasauri yamike daga jikin ummi kafin yasa hannu ya kama aydarh kaman yana daukan kwai ya shimfida da it akan gadon "cike da kulawa da nuna damu yace sorry ummi mun gajiyar dake what about your shoulder sorry ummi "ummi tadaure tamike tsaye takallesa tace go and prayed tafada tana shigewa bayi "ahankali yamike yakarasa kusa da aydarh yamatsar da fuskansa cikin tasa yayi mata peck a forward "kafin yajuya yafice.Ummi tace kinyi shiru kuma baby "Aydarh tasake yin kasa kai tana wasa da yatsun hannunta murya very soft and cool tace "daman ummi ina son naje gidane,ummi tayi murmushi tace gida kuma baby?aydarh da duk nauyi da kunya sun isheta ta gyadawa ummi kai ummi tayi dan murmushi tace tau ba laifi baby bara mijin naki yashigo sai kishirya yayi dropping dinki "aydarh tace nagode sosai har ummi zata fita aydarh tace ummi zan dawo aie ummi tayi murmushi tace tau shknn girl Allah yasa bara nadawo sai nahada miki box dinki ba?aydarh tace ah'ah zan hada ummi "ummi tace keda har yanzu jikinki babu kwari bara nasa Maryam tazo sai tahada miki hakan yayi aydarh tayi murmushi tanayin kasa da kai kafin tace "Erh"ahankali,Bayan har wayan takusa tsinkewa kafin dr ibrahim yadaga malik yace bakace mun 10 ba? Dr ibrahim yace ai ba ten nace zamu sauka ba cewa nayi 10 zamu tashi "malik yace Allah sarki, Allah yakawo ku lafiya yah inna fa?dr ibrahim yace ai kawaii idan mun karaso kwa hadu duk a zauna lapia, malik yayi murmushi yace da abunda take tsarawa kenan dr ibrahim yace inna ce fa sallama sukayi kasancewan su dr ibrahim na airport " sallama yayi yashiga anan tsakan yaga ummi "tana faman gyara shanyar dake kan igiya " malik yayi mata sannu da gida ta amsa masa kai tace kashirya yanzu sai ka mayar da baby can gidan Habib malik yashafa kansa yace ai ummi tare zamuje daku har abby ma nacan ummi tadanyi jim kafin tace.

Ummi tace mi akeyi a can din malik yace gaskia nima bansani ba yadai bani car key yace nataho tare daku ummi tace tau shknn tana fadan haka tawuce dakinsu aysha tana dage curtain din taga sun shirya aysha ce kawai tarage

itama kuma perfume take fesawa da mamaki ummi ke kallonsa ouu sun ma san da fitar kenan batace musu komai ba ta sauke curtain din tajuya dakinta “ta dinga bin aydarh da kallo Sosai bakin abayan yayi mata kyau tayi kyau bana wasa ba her beauty of skin is beyond imagination har wani creamy creamy take fadawan datayi kadan shima yakara mata kyau kayan fuskanta kaman irin an zana su,tana cikin rolling veil dinta bayan tayi zipping box dinta da maryam tasake arranging kayan ciki duk perfumes din yawancin su ta kyautarwa su maryam dasu duk da sai dakyar tasamu suka amsa har sai da suka ga tayi fushi kafin “ummi tace sannu baby “Aydarh tayi kasa da kai tace yauwa “ ummi tace ashe ma abbyn dinku nacan gidan yace duk muje baki daya “ Aydarh tace “to” ummi tabude wardrobe dinta tafito da gogagan hijab kalan cotton lace din jikinta mai onion color “ahankali ummi ta matso tasauke box din aydarh kasa kafin ta kwallawa halime kira tazo ta fitar dashi cikin mota “Aydarh ce karshen fitowa kafin ummi duk da ranan bawani zafi bane da ita amma sai data sa hannu takare data fito “malik dake zaune driver sit sai binta yake da ido ko kiftawa babu “har takaraso tana tafiya kaman bata son taka kasa kuma har yanzu bataji tadawo daidai ba don zafin stiches din har yanzu akwai “har tabude back sit zata shiga sai ga ummi takarasa rufe gida tafito tace baby dawo front sit mu sai mu zauna baya babu musu tadawo duk da bata so hakan bako kadan tana zama ta rufe ido “tunda suka hau hanya babu mai magana sai maryam da halime wanda ummi data gaji da hayaniyar su tace suyi mata shiru “,Ummi dai batace komai ganin anbude dayan gate din gidan dake kusa dagidan su aydarh wanda har yaso yafisa kyau da haduwa duk yanda gidansu aydarh yakai ga kyau da haduwa don ginin gidan yayi kaman irin white house din nan amma wannan yafisa haduwa security’s ne kwara hudu tsaye bakin gate din aydarh ma bata kawo komai a ranta bad uk tunaninta ko abba yasiya gidan suka dawo nan Parking yar 406 din abby yayi cikin jerin motocin dake parke a Parking lots din “abby najin karan motan yafito daga cikin mad palace parlor din wanda fadan irin dukiyan daaka zuba kaca kaca wurin hada parlor wani sabon aiki ne billahi “ko da suka fifito su aysha komawa sukayi kauyawa banda aydarh da ummi dake ta rikewa “Aydarh dai ganin gidan bazai girgiza ta ba don tasha zuwa wanda yafisa ma kawai dai tana son gidan don ta taba shigowa ma ada da abba yayi niyyar siyansa kuma yafasa ummi ta hango abby natahowa yana karasowa yana binsu da kallo da bayan daya aydarh ta sukunyan da kai tana gaishesa yaamsa ta dauke da fara’a kafin yamaida dubansa ga ummi yabude mata hannunsa muryansa nan na manya mutane kamilalu yace welcomes to your new home fullani na!wallahi ummi was little bit confused don bata gane abunda abbyn ke nufi ba tadai sake gyara tsayuwanta tana kallonsa matsowa yayi yana murmushi yakama

hannunta ta dinga binsa babu musu “ har suka shiga cikin gidan tunda take a rayuwa bata taba tunanin akwai rana irin wannan dazai zo rayuwanta bak o kadan wasu kalan hawaye taji masu dimi na fitowa daga idonta kallon malik take dake tsaye kusa da kofan babban parlor yaki shigowa both halime aysha da maryam sun kasa yin komai saboda murna itama aydarh ba dan karamin dadi taji ba bakaramin burgeta malik din yayi ba a yau kallo daya yayi wa ummi yadauke ido sai yatako ahankali har yazo kusa da ummin yasa hannu yana goge hawayen fuskanta dayakasa tsayawa “su aysha na kallonsu suma duk hawayen dadi ya balle musu da gudu suka karaso kusa dasu wani irin warm hug suka ba ummi malik na tsaye shima sai yaji tausan mamanshi da sisters dinsa aydarh ma bakaramin tausai suka bata ba Wallahi har cikin ranta taji tana son su kuma tana son zama dasu duk irin gata data samu tayi lacking all this dasukeyi bata da kowa bayan oum da abba da rufaidarh wanda sometimes sai tayi six months bata gansu ba itama gently tamike takarasa kusa dasu ga tears a fuskan ta tayi joining dinsu malik naganin haka yafara murmushi da hawaye atare yahade su yayi hugging dinsu shidai abby nadaga gefe yana dariya mai hade da kuka juyawa yayi yafita daga parlor “Wallahi the moment is such a unforgettable memories whatttttt kowaye kai dole this family ya burgeka atare suka dinga zagayawa gidan har sun gaji kuma basu gama ba “at last dai ummi tace su dawo bakomai ba saboda yanayin aydarh nan parlor suka dawo suka zauna bai iya seconds batare da ya kalleta ba sau baadadi suke hada ido sai dai Tamaka masa harara yayi murmushi kawai don dariya ma take basa “karan door bell sukaji malik ne yabude sai ga oum da rufaidarh atare hade da maids dasuka riko difference warmers and jug na abinci kala kala dasukayi musu “kusan shigen riga daya suka saka aydarh da ummi rufaidarh kam yau dogon rigan swiss lace tasaka mai masifan kyau da tsada tayi musulmin kyau “bayan duk sun gaisa oum tayi congratulating ummi da abby haddasu aysha ma likewise rufaidarh “oum tayiwa malik godiya da addua kunya ma tahana sa amsawa “ A dining dake nan suka shirya abincin gwanin burgewa atare suka ci hadda abby malik dake kusa da sit din aydarh sam she is not comfortable duk taji wani kala ga dan rashin kunya irin nasa ta cikin plate dinta yake deban salad bata dai ce masa komai ba amma kunyarsu ummi take ji abunda yakeyi din kuma kowa na kallo bayan sun gama cin abinci ummi suka zagaya tare dasu rufaidarh da oum ko’ina na gidan sosai sukayi addua suka sa albarka kafin suyi sallama su ce zasu dawo zuwa dare in sha Allah ummi taso abar aydarh anan tunda sun zo kusa amma tasan itama oum na bukatar yarinyarta kusa da ita malik ne yadauke box din aydarh da kafa suka shige gida rabon datayi tafiya haka har ta manta tun Washington sai yau dasuka zagaya sabon gidan dayayi wata anguwan gashi daga gate

din gidansu zuwa main entrance din akwai tafiya Sosai oum da rufaidarh nagaba sai ita abayansu sai shi daga can baya yana lura da tafiyan ta sai faman zuwa waist dinta ido yake kaman zai cinyeta suna shiga parlor babu wanda tayiwa magana tayi hanyar stairs zuwa dakinta wanda har ta gagara tashiga she forgets when last data ga dakin she badly missed the room yah Allahu tana shiga taga dakin kaman yanda yake very tidy and neat ga scent dinta har yanzu a dakin Komai nata na nan a yarda yake pictures dinta dake cikin frames an jera su a wall din dakin sunyi kyau bana wasa ba yawancin pictures dinma duk a kasan wajene wasu a school wasu a café sai wanda suke ita da oum da abba a can gidan su na USA sai kuma wanda take ita da rufaidarh a uk wanda asibiti aka kaita can ganin wani Doctor kan case din asthma Wallahi aydarh is super natural in all aspects yarinyar tahadu ya rahaman tanada kyau tahadu ta iya gayu the way she talks na fizgan hankalin da namiji yarinya is hundred percent akomai kawai rashin son mutane da talakawa ya cuceta wanda rashin gwada matan daakayi ne hakan dakuma laifin abba akan cutar da rayuwanta na rashin islamiya shi yayi causing komai amma yanzu Alhamdulilah shigowan malik into her life changes her bayan oum ta godewa Allah seconds mutun da zata godewa in her entire life shine malik saboda haka aka aurawa aydarh shi kuma Alhamdulilah yayi abunda oum ke so har da ma kari “Alhamdulilah yanzu buri dayane ya rage na oum neman hanyar da yan uwa biyun zasu shirya su dawo kaman daa kuma cikin ikon Allah an biyo hanyar hakan Alhamdulilah “abunda aydarh batasani ba shine oum da kanta ke shigowa ta gyara dakin nata bawata yar aiki ba bakaramin namijin kokari tayi ba wajan sadaukar da farin cikinta saboda gyaruwan farin cikin nata saboda aydarh farin cikinta ce kuma tasan ko da bayan ranta aydarh tasamu uwa,uba,miji,wa,kanni,dakuma aboki domin malik deserves aydarh aydarh deserves malik ba cuta ba cutarwa cikinsu kowa yasamu daidai da class dinsa dan duk wacce malik zai aura will be local champion idan akayi comparing dinta dashi “haka zalika itama aydarh!! Oum takallesa tace son idan kahau stairs dakin dake kallonka na farko shine nata ka kai mata box din acan bara nasa a hada maka juice fresh one “malik yace Alhamdulilah oum sauri nake zan dawo zuwa anjima na gaishe da abba oum tace aa fa son kajira yanzu ma sai ku gaisa dashi abban naku malik yashafa kansa kafin yace tau mom “wucewa yayi kaman yanda oum tagaya masa dakin nan yashiga gently yasa hannu yabude kofan dakin yashiga “scent din daya dakar masa hanci yasa shi dakatawa yayi shiru abakin kofan kafin yakarasa shigowa dakin yayi kyau irin kyaun nan na azaba “tayi kwance kan gadon ta rufe har fuskanta da duvet baby pink mai kyau daka ga bargon kasan ansaka kudi wurin siyan sa ajiye box din yayi yakai 10mins yana kallon

pictures dinta na frames din murmushi yayi kafin yamatsa kusa da gadon tunda yashigo taji ajikinta shine tadai ki tashi ahankali yasa hannu yana yaye duvet din tabude ido tana bata fuska tayi masa wani kallo kafin ta janye ido zama yayi kusa da ita yana kallonta kaman zai cinyeta ita kuma taki koda kallonsa “muryansa can kasa yace tashi let’s talk kinji “Wallahi batayi niyyar tashi ba amma da tone din dayayi maganar batasan yaakai ba kawai tamike “yasa hannu yana kama nata hannun dukkansu wani shock sukaji “amma bai saki hannun ba ya cigaba da murza shi ahankali ahankali yace “cuddle bug” kadan tadago white clean round eyes dinta dasuka sha kajal ga lashes din kaman takara tsaban kyau “yayi wani kala da fuska, is heart is melting billahi zuciyansa na narkewa kaman yasata a jikinsa and tell her sorry “ ahankali yace bazaki iya yafemun ba for my mistake?waya gaya miki I didn’t feel your pain?ciwon ajikinki yake amma nike jinsa deep inside my heart baby girl! Kinsan how sleepless nights I have all this days ganin nasaki in suchs situation ahankali yasauka kasa yayi kneeling kaman zaiyi mata kuka yahade both hannunsa yace am critically sorry babysis Kiyi hakuri and pardon me I promise you not to repeat this again am so sorry kiyi hakuri kinji ni?aydarh dai kanta na gefe tajuya masa baya babu abunda take bayan hawaye ita fa bayan wannan abunda yayi mata ba abunda ke dawo mata a rai irin tunuwa da yanda tasamesa shi da linda datayi hakan na matukar masifan bata mata rai yana mata ciwo irin mugun mikin nan mai zafi “ tashi tayi daga kan gadon tayi hanyar toilet dasauri ya sha gaban yariketa as if his life depends on her yana sauke wani irin ajiyan zuciya “cikin wall ya jinginar da ita yabita yana hade bakinsu yakai 5mins yana kissing dinta duk yanda jikinta ke vibrating amma batayi kissing dinsa back bas ai share tears dinta take faman yi “ahankali ganin yasaki jikinsa tazare bakinta “tana sake fashewa dawani kukan “muryar ta har sarkewa take “ tace did you know how I feel sir? Kasan how hurts am I sir? Ganinka da ita in suchs conditions yasani naji nayi fail, I hate myself I hate the country tasake fashewa dawani kuka har tana shidewa tace and kace am not your wife!!!bayan you disvirgin me kuma kadawo kace am not your wife is this how you hate me is this how ka tsaneni ka lallata mun rayuwa and yanzu kadawo kace am not your kasa ta zube kan gwiwanta tana rufe fuskanta da hannu tana wani kalan kuka marar sauti daga gani kasan she is hurt shima dukawa yayi Wallahi bakaramin tausanta yaji ba ji yayi yatsani kansa kan furcin dayayi “Wallahi Allah bai san maganar zaiyi mata ciwo har haka ba jawota yayi yasata a jikinsa yadinga shafa bayanta tana kuka har tagaji kukan yalafa “hannu yasa yashare mata hawayen “yace shssh bana son kukan nan kinji am lying karya nayi duk duniya bayan ke I have no other girl to call a wife “you are the only girl I have here and after “kece kawai

matata my only sturbborn wife “ my only little princess my jewel “ta dinga sauke ajiyan zuciya kaman tayi race tayi lamo jikinsa Wallahi bata san miyasa ba amma ji tayi she feel at peace “a jikinsa tunda ta kwanta asibiti bata taba jin nutsuwa ba kaman yanzu “ahh”Ahankali yace mata I LOVE YOU!wallahi dagowa tayi dasauri tana kallonsa “kalman tazo mata suddenly “yana sonta fa yace! Gyada mata kai yayi alaman yess yace yes I LOVE YOUUUUUUUUUUUU WIFE FROM THE FIRST DAY THAT I SAW YOU NAJI INA SONKI I LOVE YOU FROM NOW TILL MYLAST BREATH I LOVE YOU IN THIS DUNIA AND I WILL ALSO LOVE YOU IN HEREAFTER!! HEREAFTER!!HEREAFTER sai daya ya maimaita hereafter kusan sau uku kwalla nabin idonsa “saukan kukansa taji a wuyanta dasauri ta mike tana kallonsa Wallahi ganinsa yana kuka yasata jin wani kala a zuciyarta batace masa komai ba don a yanzu bata san mi zata fada din ba batasan exactly moods din datake ciki ba Wallahi ‘daurewa tayi ta mike tabarsa nan tashige toilet tarufe kofan ta jingina ta rufe bakinta tawani kalan fashewa da kuka “harda shesheka “yakara kusa 15mins a dakin kafin yadaidai ta kansa ya mike yafice bakaramin dadi yaji ba ganin babu kowa a parlor yayi saurin barin gidan yafada sabon gidansu yana shiga duk suna parlor yakarasa yazauna kusa da abby,ahankali abby yace na yanke shawara zan ba yaron amini na waccan gidan kyauta halak malak yazauna shida iyalansa kayan ciki kuma zan kyautar dasu duk wani abun bukata zuwa anjima zanje dakaina nakawo su nan din malij yace badamuwa abby hakan ma yay isai a gyara masa can din in sha Allah,abby yace masha Allah Allah yasaka maka da alkhairi “ malik yace Ameen abby yakalli su maryam yace ku shirya tonight zamu fita ku siya abubuwan maryam tace thank you brose aysha tace Allah yasaka da alkhairi yayah halime tace “we are very proud of you my love “ummi dai batayi magana ba sai can tace maryam kuje ciki zamuyi magana da yayanku tashi sukayi da gudu maryam da halime ke hawan stairs din already kowa ya zabi daki don babu abunda ya bambamta a furnitures din komai iri daya ne dukka su ukun “sai parts din abby nashi daban ummi ma haka.ummi tayi shiru bayan tagama fadin yarda sukayi da aydarh kan cewa bazata koma ba Wallahi kaman ansa guduma an dakki zuciyansa haka yaji duk girman ac ac din dake akwai a parlor har zufa tafara keto masa “duk suna lura dashi daga abby har ummin tashi yayi without saying a word kawai yafita “har yafice daga parlor cikin babu wanda yadauke ido kansa kallonsa suke cike da tausai bayan yakarasa ficewa ummi tace anya abby yaron nan zai iya yin hakuri kuwa?abby yace in sha Allah babu maganar rabuwa a auran nan munyi waya da baba tace mun zata shigo zuwa anjima tareda hajajju in sha Allah ita takwarar taki zata hakura kila sabani yashiga tsakaninsu shiyasa tafadi hakan! Ummi tayi shiru kafin tace Allah ya kyauta

abby yace Ameen “kan booth din farin GLK abby ya zauna “tunda yafito babu abunda yake bayan furzar da iska da sha kansa da karfi “zuciyarsa sai faman bugawa take dasauri sai addua yake tasamun sauki wajan ubangijinsa “wayarsa ce tafara ringing kaman kar yaduba sai kuma yafiddota daga cikin aljihunsa “yaduba yaga dr ibrahim ne slicing yayi ya dauka yakara a kunnasa bayan ya amsa sallaman da malik din.

Motan dayake sama yasauka yashiga cikin gidan Still ummi da abby su nan parlor suna magana “bayanin waenda zasu zo malik yayi musu aikam kar ku so kuga murna wajan ummi da abby,Abby yamike yace yanzu zaka dauko su daga airport din?malik yace eh abby yace tau masha Allah bismillah muje “kafin yakalli ummi yace ki kira su mamana duk akwai komai abun bukata a can kitchen din a daura girki ai kamata yayi kafada tunda wuri saboda a shirya “ malik da duk bai cikin mood mai kyau amma zuwan su dr ibrahim din yadan saukaka masa zuciya “ yace hakan ma lafiya lau zan yo musu take away a hanya ummi ta girgiza kai tace zaa komai anan din “ yace tau yafada yana juyawa “abby ya rufa masa baya,babu abunda abby yakeyi a motan bayan ba malik baki yana kwantar masa da hankali abby is wise enough Wallahi shawara yake ba yaronsa cike da hikima can malik yace “itama fa abby kawai kishi ne nidai gaskia kayi confront din abban nata abarmun matana bazan sake ta ba koma mi zai faru abby yajuyan da kansa yayi da murmushi watau malik dinsa ne yazama marar kunya har haka kan mace “bai ga laifinsa ba shi so aie gaskia ne “ suna shiga airport din babu wani wahala suka hadu dasu “wani irin murmushi malik yayi kawai yaje ya rungume dr ibrahim shima cike da jin dadi yayi hugging abokinsa back ita dai dr hafsa sai faman murmushi take ganin yanda malik ya chanza yazama wani babban mutun yafito asalin balaraban sa sak jikinsa yasake wani murdewa “inna kau dake gefe tasha uban mayafinta ga handbag dinta mai kyau yau dai hadda glasses “ abby dake cike da farin cikin ganinsu saboda duk duniya baida kaman su abunda sukayi masa a rayuwa bashi da bakin magana durkusawa yayi har kasa ya gaishe da inna cike da murna inna ta amsa sa tana fadin ai dagani ma ba tambaya wannan uban audu ne barakallah ga fuskar nan “ abby yayi hugging dr ibrahim yana shafa kansa yace welcome son “sosai dr ibrahim yace dadin haka anan airport din suka fara gagaisawa abby yace suje gida duk sunfi sakewa a can “ anan parlor suka shigo security’s suka kawo musu box dinsu ciki “ummi tace marhaban lalle sannunku sannunku sannunku da hanya “inna dai takasa rufe bakinta Allah ne yataimake ta takama yaran nan ta rike da ace cutarsu sukayi suka musu mugun abu da duk yanzu anyi can gidan yari dasu kaman yanda abby yayi itama ummi har kasa ta duka ta gaishe da inna tana musu sannu da

neman mun ciwon kaiii “tace nidai yanzu ina dilki zamuyi magana anjima yanzu bazanyi magana dakai ba bye my heart is always beating for your love “dr usama yayi murmushi yace same dear!ta kashe wayan..malik yayi shiru bayan yagama jin complain dinta “yace miya sa baki fadamun ba tun safe tashare hawayenta tace ai sai nayi niyya kuma namanta ya dinga kallonta ko kiftawa babu tadan fada sai wani uban haske datayi har yanzu bata saba dashi ba kwata kwata tafi jin dadin lokacin dasuke a kano saboda babu abunda ke shiga tsakanin su a lokacin yanzu kam ya matsa mata “Daurewa kawai take amma Wallahi tagaji da this sex gashi kwana biyun nan duk bata jin dadi ma “ahankali yamike yace tashi tau mutafi tadago tace ina yace asibiti sai nayi miki proper checkup a can “ta girgiza kai tace nidai kawai ka siyo mun magana kaji “yace tau hajiya “yazauna gefenta ya dan karya wuya kafin yayi kasa da murya yace eyyerh mamana mi zan samu ta maka masa wani harara tace Allah sir babu ni am tired ma yau din nan “yayi shiru kafin yace tau yallabiya “tamike tabar masa parlor baki daya ma “ tana shiga bedroom din tahau kan gado ta kwanta bai ma dauke ta ko 5 mins ba kaman yar yarinyar “yana shigowa bedroom din yayi tsaye yana kallonta ya lura cikin week din nan tacika yawan bacci ga masifa kaman tana jiransa “girgiza kaii yayi yamatso gently yasa duvet yarufe ta kafin yashafa mata addua yafita daga dakin kitchen yashiga yakwashe few plates din dasuka bata ya wanke ya goge kitchen din kafin yadawo parlor nan ma tagyara sa yasake arranging pillows kafin yasaka fresher yana daidaita room heater parlor kwanan sanyi yakaro sosai shiyasa yake tunanin ko hakan ke saka ta bacci ko kuma gajiya ne don shi kansa yasan yana takura wa yarinyar nan a rana zaya nemi sex wurin sau uku fa kuma baya yi kadan yazama satisfied sai yadau lokaci shiyasa duk tafada shikam ya isa isa yayi wani kiba ga skin dinsa data goga masa kyau a fata “lumshe ido yayi yana murmushi Wallahi yana son aydarh “ bedroom din yadawo daman yasan bata farka ba without making any sound yabude wardrobe yafito dawani blue yard mai kyau yasaka ‘ preparations din tafiya Nigeria suke shiyasa duk tayi musu parking kayansu a box,wajanta yazo ya daukar dakai yayi kissing lips dinta da forehead ya shaki kamshinta na kusan five minutes kafin yamike yadauki wayansa yayi mata sending message “Am out girlie and promise you will feed me if am back “yatura mata yafice ‘ Rufaidarh tace ina jinki fa baby aydarh ta fashe da kuka rufaidarh tace inalilahi waina illahil rajiun ke lafiya miya faru wani abun akayi miki komai?duk ta gigice tana jiran jin abunda aydarh zata fada gwanin ban tausai tace Allah mom nidai am tired Nigeria zan dawo ina kokari amma abun yawuce tunanina nidai nagaji “rufaidarh tace wai ke kam dan ubanki yakike so nayi ne kin ki kimun bayani kina kuka kince zaki dawo Nigeria tau wai bazakiyi bayani bane eh? Aydarh ta tsaya

da kukanta tace babu komai indai ya kasheni ai zaya dawo kuma da death body na “rufaidarh tayi wani shekeke tana sauraron aydarh “rufaidarh tace kina jina mun fi son haka ma kinji ko idan yakashe ki ma ko bakomai ance a gidan mijinki kika mutu mutuniyar banza kawai marar kirki “Aydarh dai tayi shiru duk da maganar tayi mata ciwo saboda sam batasan wanda zatayi wa karar malik yadaina ba tayi tunanin rufaidarh zata bi bayanta sai taji itama bata bi ba gashi bata son masa musu yayi mata ta karfi amma ita kam jarabar sa tayi mata yawa “har fargaba take ji idan ta tuna zaya dawo ko kuma taji shigowansa “ ga tausayin dayake bata son dayake yi mata yayi yawa idan tace zata barsa batayi masa adalci ba don Allah kawai yasan irin hali dazaya shiga don irin son kashe kan dayake mata har yayi yawa “ ga tsoron sa datake ko tayi niyyan tayi masa masifa bazata iya ba “har yanzu gata nan dai batasan tana son sa ko bata son sa ba kullun abun nayi mata yawo a rai gawani bakin kishinsa datake ji ko ranar daakayi wani conference a wajan aikinsu baki daya hana sa tayi tashi ko nan da can suna tare saboda da mata ‘ “karan motan mr joe taji tasan shine yadawo tamike ahankali tawuce bedroom tashiga toilet tawanke fuskanta tass ta karamin towel ta tsane fuskan “ tafito gaban mirror ta tsaya tabude face cream dinta tashafa a fuskan kafin tasa kajal a ido kaman batayi kuka ba idonta haka yayi “ ya danna door bell tazo tabude masa yayi murmushi yace Assalam alaikum “ta amsa masa ahankali yasata jikinsa yayi hugging dinta very tight har sai datagaji ta zare shi daga jikinta takama hannunsa suka wuce bedroom “sai dayayi wanka kafin yafito ya chanza kayan data ajiye masa yadawo parlor a kitchen ya isketa tana slicing fruit cikin bowl ‘ yana shiga yasa hannu yadauki slice apple daya yana shay ace gobe zamu tashi in sha Allah da yamma ne flight din ta gyada masa kai kafin yace nawa zakiyi bawa mom gudunmuwa? Tayi shiru kafin tace to”yayah 5m yayi malik yawara ido yace ehh kaman yayi kinga ni sai nahada danawa yacika 15m kenan ta gyada masa kai tace Allah yasaka da Alkhairi yayi cute smile yana jan long pointed nose dinta yayi kalan muryanta yace hun “tayi murmushi yasa hannu yajawota tayi facing dinsa yahada ta da well kafin yasa hannu yaja zip dinta kasa batayi mamaki ba don bay au yafara having dinta ko’ina na gidan ba dauke kanta tayi gabanta ya yanke yafadi kawai yasa hannu cikin bra dinta yana yawo da hannun wurin jikinta very warm kaman tana running temperature tsayan da hannunsa yayi daga yawon da yakeyi dashi yakama fuskan ta yana kallonta yace are you sick dear?tayi raurau da ido tace masa yes “malik yace yah Allah yakama hannunta suka fita daga kitchen din yazaunar daita kan sofa nan parlor kafin shima yazauna yajawota jikinsa yace since when tun na shekaran jiyan nan? Naji miki ciwo ne when sex my love? Kiyi hakuri Wallahi ban sani ba mamana “ mikike ji

yanzu? Duk ya daga hankalinsa Wallahi shiyasa yake bata tausayi ‘tayi kasa da murya tace nagaji yace dami kika gaji girlie? Tace can you allow me for even today only?dasauri yagyada kai yace yes love ki dinga fada mun kinji kidaina cutan kanki you know ina sonki aydarh and I respect any of your decisions bazan zama someone very selfish ba har haka kinjini kiyi hakuri ‘ta gyada masa yace tashi nashirya ki lets go to hospital yanzu bana son musu kuma “ta gyada masa kai gwanin ban tausan haka yadinga sauri hijab kawai yadauko mata sai rigan sanyi ita kuma mutuniyar ganin yanata rawan kafa yasa duk tasake shashabewa “ko mr joe bai kira ba yakama matarsa suka samu rickshaw yakai su har asibitin su malik din “baiyi tunanin mata any test ba shima dai kaman ba dr ba kuma ita tahanasa ma saboda tsoro take kaman zaa mata wani injections “ har yahada allura zayayi mata tasa masa kuka shikuma mijin tace din ya biye ta last lasts dai babu wani serious treatment dayayi mata magani kawai tayarda ta karba suka zauna office tayi lamo jikinsa shikam yana ta faman lallashi.

Tamike takama hannunsa tace ka tashi fa mutafi nace malik ya girgiza kai this girl will never allow him to rest yanzu a cikin daran nan takeson su fita siyan fries yau kuma?yarinyar dawani lokacin sai yabata mata rai take cin abinci ganin yaki ya tashi yasa tafashe masa da kuka hadda hawaye whattttt baki a bude yake binta da kallo kaman yaga t.v ganin kukan gaske yakeyi yasa shi mikewa dasauri yana kamota yace shshshsh sorry fave Ai duk bai haka baa bun minene na kuka muje muje Ai duk fa inda yake a fadin Washington dinnan sai ansiyo shine ‘ta tura masa baki tace tau muje wardrobe yabude yaciro musu rigan sanyi da jacket ita hadda hijab ma looking very cute ita dashi din yakama hannunta suka fita daga gidan ya rufe “garin kaman da rana ga haske manyan fitilu masu kyau a ko’ina ga mutane kowa na harkan gabansa dakafa suka dinga takawa tana jansa da surutu shidai sai faman kallonta yake yana murmushi ‘can tace tau wai yayah dazu kacemun uncle yace muyi ma mom magana tanada gaskia fa malik yawara ido kafin yace shima yanada gaskia fa kawai magana zamuyi mata first thing gobe in sha Allah muna isa Nigeria tagyada kai tace Allah yakaimu lapia yace Ameen ‘kafin yace kinga idan mukaje Nigeria part dinmu na nan cikin gidan abby “Aydarh tasaki hannunsa kafin ta tsaya da tafiyan tace kana nufin kenan ba a gida zan zauna ba zan bika gidanku kaman dai wanda bata da kunya?nidai Wallahi ah’ah malik yayi shiru yace Wallahi fa kikace hajiya tabude ido kafin tabata fuska tace Allah nidai zan huta ne shiyasa ma kaga am eager mutafi dan murmushi yayi bata da wayau sam kinga har tafada masa abun yasa take murna har tausai take basa yanzu bata iya masa gardama gashi kuma yana matsa mata kugunta yasake

wani irin fitowa likewise her boobs fatanta kuma anyi *3 kan daa ‘saboda yawan sex har idonta yafada ma tazama wani very weak “ tayi tagama amma bazaiyi hakuri ba fa bazai ma iya ba wannan sam sam ‘bakin wani babban café suka tsaya suna shiga taja masa kujera yazauna ita tawuce can tamusu order hot coffee sai fries din tace amata takeaway ‘kaman yanda tafadi haka akayi tafito dakudi ta biya har yafiddo wallet dinsa yafito dakudi saboda yana ganin komai dake dainda yake zaune yaga tayi payment yazauna karasowa datayi dana shi mug din rike a hannu ‘ tana zuwa yamike yasa hannu yakarba kafin tajuya itama ta karbi mug din nata daga hannun waitress din “ zama tayi tafara sipping coffee ahankali yace ina nawa fries din “takallesa kafin tayi murmushi tace kaji mun sir naga kayi rakiya and tsaban how sweet able am I nasiyan maka coffee fries din kuma nawane “ gashi nan ma anyi mun packaging sai naje gida ‘malik yayi murmushi yana girgiza kai bai ce komai ba sai dasuka gama kafin yace yanzu sai ki rakani mall din dake gefe nan nima tace ohk” suna shiga yaje yasiyan musu few things ba don babu ba no yaga yakusa karewa ne, wani babban teddy bea tagani purple jikinsa mai kyau sosai ta tsaya ta dauka “yakalleta ya girgiza kai yace tau nace a dauki teddy ne daga rakiya kuma sai ki dauki abu? Baki ma ga how sweet able am I ba dana siyan miki hair spray dinnan da soaps ? ta bata rai watau ramawa zaiyi kenan ta juyan dakai kaman yar marainiya tace eyyerh sir tau ka aramun ka biya idan yaso muna zuwa gida I will pay yace promised dasauri ta gyada kai yace muje tau “kudin suka biya this time taxi suka samu zuwa gida saboda dare yayi sosai “ .ya dinga kallonta ko kiftawa babu ganin tayi kwance a kasa duk sanyin dake akwai gently ya durkusa kusa da ita yace miya faru mamana baki da lafiya ne?ta tashi zaune tana girgiza masa kai tace no kawai bana jin dadi ne yace subhanallah tashi sai kiyi wanka idan kika shirya zan baki magani tagyada masa kai “bayan sun shirya tsaf yabata magani sai faman lallaba ta yakeyi taki bari kuma yace bata da lapia yabarta ahaka “mr joe daya zo yataimaka wa malik wurin kai luggage dinsu booth, duk tayi wani kala shidai sai faman binta da kallo yake wannan karon ma kaman last time tunda suka tashi take bacci sau biyu tana farkawa shima ruwa kawai take tambaya sai takoma “da yamma sosai sukayi landing ummi da abby kawai suka samu taran su a AirPort din “Aydarh na ganin ummi ta shige jikinta itama ummin yarda take mata kaman kwai sawani faman lallaba ta take shidai malik kaman baa san shi ba “ babu yanda ummi batayi ba aydarh tazauna wajanta abby yace aaa itama gida zata wuce ta huta kuma tunda gidansu ake biki su shirya sosai shidai malik sai faman bakin rai yake “Aydarh na lura dashi ko datace masa sai dasafe bai amsa ta ba ‘bata damu ba tasa kai tayi ficewanta “ .Oum tace uktiee anya kwanciyan yarinyar nan baiyi yawa bakam?rufaidarh me kika

gani?oum ta girgiza kai tace naga Ai tunda tazo gidan nan baki daya bata dawani kuzari tun datayi isha fa take kwance rufaidarh ta girgiza kai tace kiji uktiee dawani zance keda kinsan daman haka take miye na damun kanki? Kawai dai Allah yasa lafiya shima mijin ko zama baiyi ba daya zo gaishe mu oum tace kinsan gajiya gashi kuma dan ango da amarya kuma abokin ango busy yake rufaidarh tayi murmushi tace wai abokin ango " oum tace ehen " na riga dana tura 20m din na home décordar din yanzu ina ga babu saurin wani kuma rufaidarh tabude ido tace kai uktiee saidai da kika siya waccan din lah ila " har na 20m na daki uku 90m kenan oum tayi murmushi tace kedai Allah yasa alkhairi yabaku zaman lafiya rufaidarh tashare hawayen takama hannu oum tace Ameen yah Allah " uktiee nagode sosai Allah yasaka muku da alkhairi bani da bakin muku godiya ' oum tagirgiza kai kawai tamike tace bara natashi naje wajan baban amarya nasan yashigo zuwa yanzu rufaidarh tayi dariya tace ai mijinki yanzu na koma kakarsa , oum tace ki rabu dashi mutun nan kawai " oum na mikewa sai ga sallama malik yasha white jallabiya yayi kyau bana wasa bam asha Allah yakaraso yazauna kan carpet kansa kasa ya gaishe su cike da Fara'a suka amsa shi oum tasake masa ya gajiyar hanya yace Alhamdulilah daya daga cikin maids din dake kitchen din downstairs din takira tasa takawo wa malik ruwa yace Alhamdulilah ' rufaidarh tace ka karasa son "tana dakinta malik yashafa kansa yace ohk'kafin yamike yana nufan hanya stairs din "yana shiga dakin yahango ta kwance kan gado duk tabaza pillows tarufe har kanta da duvet 'yakarasa ahankali yajanye duvet din yana kallonta hannu yakai yataba ta yaji jikinta rau dawani kalan mugun zafi ' dasauri ya janye hannunsa kafin ya kira sunanta gently tabude idonta tana kallonsa yakama ta tashi zaune yace sannu mamana baki da lafiya fa " ta girgiza masa kai tace noo nagaji ne yace tashi muje asibiti ta girgiza masa kai tace ah'ah zan sha magani yayi shiru kawai bai ce komai bat ace zan sha tea 'yace ina ke da kayan tea din ko naje gidan ummi nayi miki ta girgiza kai tanuna masa wani drawer dake bedside tace akwai a can ga cup nan sai flasks din nan akwai ruwan zafi a ciki yace ohk ma "cikin few seconds yahada mata tea din yazo yasaka ta a jikinsa yafara feeding dinta tea din saidai tayi rabi kafin ta ture jikinta har yanzu dazafi yataba kanta yace yana ciwo?ta girgiza masa kai yace ohk" magani yabata ya duba babu bottle water a dakin yace ta daure tasha da tea din takarba,yace dasafe in sha Allah zamuje asibiti ta gyada masa kai tace Allah yakaimu lapia yace Ameen mi zaki iya ci yanzu ta girgiza kasa kai tace na koshi "banga addah ba bata nan ne? Yace sunje kano ita da inna iya ke bata ji dadi ba sukaje dubata "Aydarh tace eyyerh Allah yabata lapia yace Ameen takallesa tace zaka tafi yanzu ne sir ya gyada kai yace eh daman nashigo ne kawai naduba ki ta

jinjina masa kai yace sai dasafe make sure you prayed before sleeping tace in sha Allah yamata waving hannu kafin yafice “Dasafe ma tun bayan datayi salla kasa tashi tayi daga kan prayer mat anan ta kwanta “ jin shiru har kusan 11 yasa oum tashi ta shiga dakin aydarh a kwance taganta kasa idonta a rufe takarasa gabanta tana tabata taji wani irin zafi jikinta hankalinta yatashi tasa hannu ta tasheta ahankali take bude ido har takarasa bude shi tarrr suka hada ido da oum kokarin tashi tayi amma takasa sai cija lips dinta take oum data fahimce haka ta taimaka mata ta tashi kan gado ta daurata kafin tazauna tana tambayanta lafiyan ta aydarh ta girgiza kai ahankali tace fever da ciwon kai nake tafada sai ga hawaye “ oum tace sorry ki daure kiyi wanka sai kisha tea kafin ki sha magani sorry bara nahada miki ruwan tafada cike da so toilet din oum tashiga tahada mata warm water kafin tazuba bath perfumes tafito toilet takawo mata ta daura kafin tashiga wanka sharp sharp oum tagyara shimfidan gadon kafin tabude box dinta tafito mata da wani plain abaya mai brown mai kyau sai brassiere da pant da undie black ‘sai black inner cap “ fita tayi daga dakin tahadu mata shayin tana sauka kasa nan dinning taga rufaidarh zaune tasha riga da zani na wani super wax ash and blue tayi daurin zara buhari gashin nan yasha gyara kamaan dai oum “rufaidarh tasha kwalliya kaman dai yanda amare keyi a week din auransu “ tana ganin oum tace kinga yanzu nake cewa bara naje dakin baby naduba wai lafiya ashe kin rigani “oum tace Wallahi fa uktiee nima naga bata fito ba naje dakin nasameta she is sick Wallahi rufaidarh tace subhanallah mike damunta tafada tana ajiye mug din hannunta tamike tsaye oum tace tau fever dai ce tacemun nace tayi wanka sai takarya tasha magani rufaidarh tace tau shknn uktiee ki hada mata tea din bara naje dakin nata “ oum tace tau “ lokacin da rufaidarh tashiga tafito wanka tana daure da towel ta kwanta bata da karfin shafa cream ko kadan jikinta is very weak kaman wacce aka zare wa lakka “ rufaidarh takaraso tace subhanallah baby abun yakai haka wai sannu Allah yasawwake takaraso tajanye duvet din kafin ta dauke cream din tashafa mata ta taimaka mata tasaka kayan tasa mata hula sai ga oum tashigo da cup din tea sai dayan hannunta da bowl wanda French taste vegetable fry eggs ne a ciki “ takaraso ta ajiye mata tana mata sannu sai faman kallonta takeyi “rufaidarh ta karba tamatso kusa da ita takai shayin bakin kurba daya tayi ta dauki kai ganin bata so ne yasa rufaidarh dauka fork din dake cikin bowl din ta debo kwan tana kai mata baki ai kaman tana jira sai ga yunkurin amai yataho aikam ta dinga kwara shi duk dabawani abinci kirki a ciki hankalinsu oum bakaramin tashi yayi ba ganin yanda take kwara amai kaman zata fitar da kaf kayan cikinta dasauri rufaidarh tarike ta sai faman jera mata sannu suke ‘ga damuwa a fuskan su “sai datagama rufaidarh takamata ta wannke

mata ta chanza kai kaya “oum tace tau uktiee yazamuyi da wannan case din asibiti zamu tafi ko nayiwa abba magana rufaidarh tace kin manta yau asubancin tafiya abuja yayi ba?kawai mijin zamu kira oum tace tau shknn ki kirasa “ tana daukan wayar aydarh zata kirasa sai ga kiran ummi yashigo wayan dauka tayi “bayan sun gaisa ummi tace kira nayi mu gaisa da ita nasan bacci gajiya take naji ya jikinta jiya damuka rabu tacemun kanta nadan mata ciwo “rufaidarh tace Wallahi fa yayah yanzu haka ma Abdoolmalik din zan kira yazo mutafi asibiti jikin nata yayi kasa kware Wallahi yanzu haka amai tagama ummi tace inalilahi waina illahil rajiun subhanallah amai kuma ai gashi nan zaune yana kallaci bara mu taho yanzu nan tafadi hakan tana kashe wayan hijab dinta ta warware tasaka yace ummi minene yafaru tace tashi muje jikin baby ne yayi kasa rufaidarh tace amai kawai take ya ajiye slice daya na bread din hannunsa yamike yace amai kuma ummi ? Ummi tace c’mon malam katashi mutafi zaka tsaya kana tambayana “ tashi yayi ummi nagaba yana baya ji yake kaman yabi ta katanga ya dira tsaban yanda yakagu yaje “direct dakin aydarh sukaje sama sama suka gaisa ummi takara so tarike aydarh tace sannu baby “ mike miki ciwo yanzu aydarh da duk ta galabaita tsaban aman datayi girgiza kai tayi shidai malik na baya tea din ummi ta dauka tana lallabata ko zata sha tana kai shi bakinta sai ga amai ‘ ta dinga kwara shi zuwa yanzu ko yatsan ta bata iya dagawa ta jigata hankalinsu duk yatashi malik ya matso yana kokarin ganin yanda zai taimaka mata duk ya rude Wallahi “ rufaidarh tace Ko first aid dinka zaka dako sai kayi treating dinta oum tace eh Abdoolmalik ka nutsu manah “ummi tace babu wani magana home treatment muje asibiti kawai oum tace ai shima dr ne yayah ummi tace nidai ban yarda ba koma miye muje asibiti hankalina zai fi kwanciya malik yace zan dubata ummi anan ma “ ummi tadaga masa tsawa tace zaka dauka mun yarinyar ko kuwa “karasawa yayi yasaka ma aydarh hijab dinta yadauke ta kaman paper idonta na arufe domin nauyi suke mata su kansu idon ta wahala bana wasa ba Wallahi, ko makiyanta bata fatan yasha wahalan irin aman datayi yanzu nan “daki oum da rufaidarh suka wuce kowa ya dauko mayafi da handbag suka wuce cikin mota rufaidarh malik ne yayi driving dinsu zuwa asibitin dr ramda suna isa tafara sheka amai wannan karon babu abunda yafito sai wani yellow abu tsaban babu komai a cikinta rushing dinta akayi to emergency dr ramda bata kasan ita da tsohon mijinta da hajajju tashiga tafita a maida auransu suka tafi USA kai yan biyun su asibiti har yanzu basu dawo ba tun waccan lokacin “ nr Asma’u tayi komai suka bata treatment din gaggawa “tayi kasa dayawa “drips suka daura mata da allura kafin akayi tests din duk dazaayi.kusan 1 hr 30mins suna receiption zaune har yanzu nurses din basu fito ba zuwa yanzu abby da hajajju sai baba kulu sun iso “

nr Asma’u ce tafito sai faman murmushi take “takaraso wurinsu malik da ummi ne suka mike suna nufar ta sai rufaidarh nr Asmau tayi murmushi tace shalelen family kenan wannan gata haka yanzu wa zan fara bawa sakon? Abby yace kinga diyata ki fadi kawai amma yazaayi akawo patient kuma kifito kina murmushi kice zaki bada sako ummi tace eh nurse ki fadaman ko ma miye hajajju tace baiwar Allah nan duk fameli ne idan ba so kike duk mu taru zuciyar mu ta buga bak i fadi manah yaron nan kadan ya rage yafasa manah makoki anan “tunda dai ba hakuri ne dashi bakan wannan balarabiyar yarinyar nr asmau tayi murmushi tace to congratulations Doctor ka kusa zama baba matanka nada ciki har na sati biyar.

Malik yawara ido yasa hannu yarufe bakinsa kafin yace are you serious nurse dagaske kike abunda kika fada? Ummi tayi kasa sujjudah tayi abby yabi bayanta saida sukayi adduao’I kafin suka mike shikam malik kasa rufe bakinsa yayi hannu yasa cikin aljihun sa ya fito da car key din dake ciki yamikawa nurse Asmau tasa hannu takarba tana murmushi “kafin yace thank you nurse “ I really appreciate you news and you should contact me to collect your gift wannan na duba mun mata ne !nr Asma’u tace nagode kwarai dagaske ranka dade ubangiji Allah yaraba su lapia duk su baba sukace Ameen fadin irin farincikin dake fuskan kowa cikinsu wani babban aiki ne amma sunyi murna bana wasa ba abby yafito da bundles na 1k 1k kwara biyar yabawa nr Asmau yace mungode sosai diyata “ummi tace yajikinta sister wannan ta jika suke bata diyata ba nr Asmau tace Alhamdulilah hajiya bacci take yanzu saboda jikinta dayayi kasa dayawa anjima kadan zaku iya duba ta “malik baima jira ko karasawa tayi ba yanufi hanyar dakin duk suka bishi da ido suna kallo abby ya girgiza kai yana murmushi yaron duk yawani susuce kan yarinyar “ oum dai tunda aka fara zancan kanta ke kasa batasan iya kan adadin yanda zata fasilta farin cikin datake ciki ba wai aydarnta n eke da ciki baby ke da ciki Allahu akbar she wished abba is here to witness this Alhamdulilah Alhamdulilah Alhamdulilah “rufaidarh tace mun bani jamaa ku duba mun yaro ance bazaa shiga ba yanzu yashige “hajajju tace yoo muna ganin abu ganin idon mu anan kedai mau Allah ya kashe yabaki don ba kyauta garesa ba nan dakike gani na kakarsa ce ni amma banda kujerar makkah sai gida kawai daya siyan mun yabude mun akawun yamaka kudi a ciki shine iyakan abunda nasan yahadani dashi kekam kin ji dadi abby dai ya girgiza kai watau duk hidiman nan dayayi bata gani “ dayake kowa murna yake babu wanda yabi ta kan hajajju duk suka zauna ana mamakin malik “ oum tamike tsaban kara takalli ummi tace tau yayah Allah yabata lapia ni zan wuce gida akwai sauran wasu

abubuwan damu karasa ba hidima nata matsowa rufaidarh tasaki baki tana kallonta haka ma hajajju “ Abby yace no fatima ai da kinyi hakuri ta farka idan suka bari muka ganta sai ki wuce oum tayi kasa da kai tace ah’ah yayah ga auntie nan ai Allah yabata lapia “ta karbi key din hannun rufaidarh tace zatayi driving da kanta hajajju tace ke kam dai anyi marar lafiyar kai fatiee yoo wannan ai rashin wayewa ne jamaa kit saya kiduba yarinyarki mutun ya dankara mata ciki tana ta wahala anzo da ita asibiti rai ahannu Allah don ni isowa ta nan nayi tunanin zan ga kuna fasa makoki ma ashe abun duk bana arziki bane “ oum dai tayi musu sallama tawuce baba ta girgiza kai tayi murmushi tace Allah sarki fatima Allah yasaka maki alkhairi da duk mata zasu zama kamanta da anji dadi ubangiji Allah yayi muku albarka Allah yacigaba da hada kanku Allah kuma ya aurar da sauran ummi tace Ameen yah Allah mama “Abby yace bara nakira nababa na fada masa ankusa manah mata ko aboki rufaidarh tace yakamata kam yana can abuja abby yagyada kai yace ni nakai sa airport da asuban nan yace zaije yayi signing wani contract ‘’rufaidarh tace ehh hakane baba tace Allah yataimaka yabada sa’a abby yafito da wayansa yayi dialing number abba bai shiga ba “Yana zuwa dakin yatura kofan ahankali yashiga “ yamaida yarufe ya jinginar da kansa jikin kofan “ yana mata wani kalan kallo kallo mai cike da so soyayya kauna shauk’I burgewa dakuma tausai “ All praise been to Allah ‘ hakika bashi da bakin yiwa Allah godiya he cannot pretends or deny anything amma Allah yayi masa kyauta dakari Allah yamasa ni’ima da rahama a rayuwa cikin abunda bai fi shekara daya ba Allah ya chanza masa rayuwa Allah ya aiko masa da ita cikin rayuwarsa tazama haske da salama a rohi da rayuwarsa! Ta zaman masa abun Alfahari “inda yace bazai mata so irin son mutuwa ba yayi karya idan yace bazai mata gata irin na nunawa a duniya ba ya cuce rayuwarsa “ bayan ummi da abby bazai taba hada kaunar daya ke mata dawani abun ba a rayuwarsa yana mata so irin son dake daure jijiyoyin jiki “ kwance take kan gadon ansaka mata karin ruwa sai yanzu yake lura da wani extra haske da glowing din data kara komai na fuskanta kaman an dai zana “ saidai tafada tayi rama murmushi yayi kadan abubuwa dayawa nadawo masa a kai game da ita “komai nata na burgesa tun farkon haduwar su “ karasawa yayi yaja kujera yazauna ahankali yana kallonta ko kiftawa babu ga murmushi kwance a kyakyawar fuskan shi sajan sa ya cika sosai yakarawa farin fatan sa kyau da haiba “ kaman tana ido biyu yanda yake wani dage gira irin na bad boys tunani kawai yake yanda zasu kasance da ita idan tafarka tasan tanada ciki yah Allahu yasan akwai daru tsakanin su koma miye zai iya handling matansa ko ba komai yasan tana shakkarsa “ hannu yasa yana rike hannunta mai karin ruwa har yanzu akwai zafi amma ba kaman na dazu ba ‘ahankali yafara tofa mata addua kafin yakai hannu

yayi placing daidai kasan maranta yaji tayi tauri mamaki yake yana kara jinjina ikon Allah yanda Allah yaboye abunsa “ko kadan bai taba tunanin yarinyar nan nada ciki ba “ ko kadan alama bai nuna masa yasan ita kuma bata sani ba duk sai yanzu yake recalling abubuwan da duk zaya nuna masa alaman hakan amma bai gane ba “ hakika Allah shi ke yarda yaso a lokacin daya so Alhamdulilah, ya dinga yawo da hannunsa a cikin ta dan motsa bakinta tayi hankali yalura so take ta tashi yayi murmushi yana dauke hannunsa a cikin ya dinga kallonta dai. Ba ita ta farka basai bayan daakayi azahar cikinsu babu wanda yatafi har abby tun oum data tafi babu wanda yakara tafiya lokacin suka shigo kowa ya dubata da jiki ita dai sai binsu take da ido Allah kawai yasan halin wahalar da ta shiga yau sai ita “ tasha wahala ba wahalar wasa ba bakinta yayi mata nauyi ma bazata iya jin zatayi magana ba ummi ta lallaba ta sukaje toilet tayi mata alwalla suka fito ta taimaka mata tayi salla nr Asmau ce tashigo tasake dubata ta rubuta wasu drugs din kafin tace asamu ko da tea ne a gwada bata ko zaya zauna a cikinta yunwa babu dadi ba kaman ita da yanzu ba ita daya bace “ abby yace rufaidarh ta taso sai ta karban mata shayin a gida tunda tafarka shi zaya koma campany “baba ta tashi tace bara ta bisu “har zasu fita abby ya juyo yace kai malam bazaka koma gida bai dan yaso sai ka dawo tunda aie ba kwana zatayi anan ba right?babu kunya malik yace aaaa yallabai ina nan hajajju tayi mitsi mitsi da ido tace nan fa zaya zauna ya dinga gadin matar yasan yana sonta yake bata wahalar dazaa dinga kwantar da ita gadon asibiti gashi kaza wannan bazai iya zuwa ya siya yakawo ba Allah dai yasawwake nidai kingani nan babu ruwana “ fita sukayi yarage daga ummi sai malik da hajajju “ummi takalli aydarh datayi shiru idonta a rufe amma ba bacci take bas ai faman sauke numfashin wahala take kana kallonta kaga marar lafiya “ ummi tace sannu baby “Aydarh tasamu ahankali ta gyada mata kai malik sai faman kallonta yake ko kiftawa babu hajajju tayi gyaran murya tace yanzu fa idan ba wasa bas ai kiga yarinyar nan tayi gadon uwarta “wajan wahalar kwaikwai kaiiiiii sam kwaikwai ba kyau “ haka uwarta ke wahala har tsawon wata shidda “Wallahi Allah dai yaraba su lapia amma sam laulayi mugun abune bashi da kyau “kaf aydarh najin hajajju amma bata ma fahimta da kyau kan abunda take magana taji tana cewa Allah yaraba su lapia tau hankalin ta da tunanin ta duk bai kai nan ba wahalar datake sha a yanzu kawai ya isheta ‘ Babu bata lokaci rufaidarh nashiga gida ko wajan oum bata karasa ba tasaka maids su hada lafiyayar lunch dakuma ruwan tea tafada musu abubuwan dazasu saka wajan dafawar wanda tasan favorites din aydarh ne “tana shiga parts din oum ta isketa parlor waya take da alama kuma cikin maaikatan mall dinta ne dake can lagos saboda maganar kayan datayi order suke a gefenta ta zauna har

takarasa wayan tana zarewa a kunne ta waiwayo tana kallon rufaidarh tace amarya “ya jikin babyn ne?rufaidarh tayi murmushi tace alhamdulilah fa ta farka yanzun ma dawowa nayi namata tea nakoma “oum tace eyyerh Allah yaraba lapia rufaidarh tace Ameen yah Allah yo uktiee wannan miji yanata rawar kafa badole kunya tasa mu bar masa mata ba don ma maman tashi daidai take dashi cikinsu har karasa ma wanda yafi kula da baby saidai fa na zama yar kallo Wallahi “oum tayi murmushi tace shiyasa na taho ni babu dalilin zamana tunda yanda zasuyi mata ni ba lallai hakan zanyi mata ba “ rufaidarh ta gyada kai tace Alhamdulilah fa uktiee baby kam Allah yabata nidai fatana daya kada Allah yasa ke ta biyo da mun bani Wallahi Saboda da alama itama laulayin nan baya zuwan mata dasauki Allah dai ya inganta oum tace tau Ameen yah rabbil alameen amma dai baby dawannan rakin nata da lanbon ta da baaji dadi ba “rufaidarh tamike tace bara na watsa ruwa ina mukullin motana ina ganin daga kasa zan wuce basai nadawo nan bas ai dai mun dawo kawai oum tasa hannu tana miko mata tace tau shknn Allah yatsare sai kun dawo din rufaidarh tace yauwa kin fadawa babanta ne? Oum ta girgiza kai tace no idan yadawo yaji kawai mun daiyi waya yanzu dashi “ rufaidarh tayi yar dariya tace lallai kam kinada aiki yayansa baban mijin kina fitowa yadaga waya ya doka masa call don ma bai same sa ba oum tarike baki tace wai wai abun nasu sai su din rufaidarh tace gaskia dai “ dakin ta wuce bayan tasha maganin ta kaza ne daya dahu luguf mai mata gyaran jiki tabata wanka tashiga tayi amfani da magungunan wankan tafito wani kalan kamshi mai sanyin dadi na fitowa daga jikinta sharp sharp tashirya tasaka dogon rigan swiss lace orange and black tayi kyau sosai har kiba ta kara tsaban gyara datake sha har sunka mata baskets din cikin mota tashiga tawuce asibitin “sai wajan bayan Isha”I aka sallame su bayan an tura mata musu wani magani “suna shiga gida tace rufaidarh takama ta wanka take son yi har yanzu bata san tanada ciki ba malik na nan makale dakyar aka samu rufaidarh ta lallabesa yawuce gida shima sai da aydarh tayi masa magana ta ido “yanayi wanka Ko abinci bai tsaya yaci ba ya saka wani hadaddan cotton yard sky blue anyi masa dinki kafta kana kallon yard din kasan tsaban kudi aka saka wajan siyan sa “ parlor ya tarar dasu aydarh ta kwantar da kanta a laps din rufaidarh tasaka white sleeping dress sai katuwan rigan sanyi da safa sai hulan sanyi a kanta tayi shiru idonta a rufe “ sai oum dake gefe tana juya mata tea yahuce tasha ga drugs din a leda nan kasa “sallama yayi rufaidarh da oum suka amsa shi gently yakarasa cikin parlor yazauna nan kasan carpet yayi kasa da kai kafin duk ya gaishe su “ suka amsa shi da fara’a rufaidarh tace son amma Ko abinci baka tsaya ci ba nasani kayi saurin dawowa baice komai ba yadai shafa kansa yana murmushi oum tace yakarasa can dining sai akawo masa dinner yayi mai

jikin dasauki Alhamdulilah ma “rufaidarh tace gaskia sosai rashin cin abincinne damuwa aman daman kuma sai ahankali malik yadago kai yasace kallonta kafin yace mom tasake aman ne yanzu rufaidarh takalli aydarh ta jinjina kai tace ehh Wallahi tayi yanzu ba dadewa kafin mu dawo parlor yace ohk “ yamike yace zanje nadawo mom “ rufaidarh ta gyada masa kai tace ohk son sai kadawo “ahankali tabude idon bakinta yamata nauyi don juya ma take gani tace masa zan ci fries “juyowa yayi dasauri yace tau fries kawai? Ta gyada masa kai his reaction only will explore what’s in his mind “zaka ga iya adadin so da damuwan dayayi da ita Wallahi bakaramin dadi oum ke jiba”dasaurin sa yafice daga parlor “rufaidarh takalli oum tace wai uktiee wani magnet ne ko kuma wani magic ne a jikin mu dake jan maza zuwa garemu kowa ba son wasa yake manah ba kiji fa yanda yaron nan ke son baby “oum tayi murmushi tace daga kabilan ne kaf familyn mu ko acan sudan din ai kinga yarda maza keyi manah son kashe kaii kiji yanda Doctor ke miki wannan son sau daya fa yazo yaganki amma ki duba kigani “rufaidarh tayi murmushi tace kedai uktiee kawai mu cigaba da addua da biyayya shine kawai zamu saka musu da kalan wannan son oum tace hakane “kafin oum tayi kasa da muryanta ahankali tace girlie kidaure ki sha ko kadan in sha Allah you will not throw up kinji “Aydarh tabude ido ta marairai ce fuska idonta yakawo ruwa ta girgiza kai batace komai rufaidarh tace ke kau baby girl ki daure ki sha ko kadan “kina jina? Aydarh tace bazan iya ba mom “ oum tace dan Allah babe kinji ko?rufaidarh tace barta uktiee in sha Allah idan mijin yakawo fries din nasan zata karba in sha Allahu “ oum da duk bataji dadi ba tace tau shknn Allah yasa. Sake second attempt this time kawai jikinsa tafada tasakar masa wani marayan kuka “har cikin ransa yaji kukan yasa hannu yana shafa bayanta yace shshsh ya isa haka nadaina bazaki sha bak o ?ta gyada masa kai yace ohk ya isa haka “ yace taso tau ta makale kanta yace tau fadamun mi zaki ci “cikin wani kalan slow voice tace masa na koshi yace aaaa fa mamana baki da lafiya kuma kice you won’t eat anya kam? Tace amai zanyi nidai kabani magani nadai aman kawai “I promise to eat indai nadaina aman yace tau shknn “yace saidai ko allura tunda shima magani kinki karba ta girgiza masa kai da sauri tace ah’ah bana so kawai kabani maganin zan daure nasha yace Alright amma fa kinga dana fita allura ce nasiyo na throw up din bara nasake fita sai nasiyo tace to nidai katafi da ni “yayi murmushi yalura yau kuma bata son yana tashi shikam idan haka laulayin yazo da yaronsa ya biyasa yace ohk love bara nasaka miki hijab ta gyada kai tace and karka sake using this perfume of yours kaji yayana “ kaiiiiiiiiiiii Wallahi malik wani mugun dadi yakeji yanda take masa with due respect dear in sha Allah yanzu ma sai nayi sauri na chanza kayan nadawo ta gyada kai tace and bana son wannan hulan

sanyi shima ka cire kasaka p-cap yafi maka kyau yace ohk dear Amma kinga akwai sanyi dadaran nan tafasa masa wani shagwababan kuka tana tashi daga jikinsa jikinta babu kwari sam duk tayi wani da kala dasauri yakamota yace in sha Allah cuddle bug natafi na chanzo kayan ko mufita tare eh? Ta gyada masa kai hijab dinta yadauka yasaka mata yagyara mata hulan sanyin kanta “sai tayi kaman yar baby “yasa hannu yakamata ta mike tsaye yasata a jikinsa suna tafiya har suka karasa stairs yace I should back you mama? Tawara masa ido tace noob aka gani akwai maids a gidan gasu oum idan suka gani fa yace ai sun san baki da lafiya babu wanda ma zaya gani ‘tayi shiru kawai yaduka kusan one minute yana sauraron yaji tahau amma shiru ahankali yace calm dear “daurewa tayi tahau amma duk a tsorace take “ luckily har suka fita parking space kafin suka ga yan aiki babu wanda yadamu dasu ahaka yashiga da ita har part din sa “tana ganin yana kokarin cire kaya tayi saurin sa hannu tarufe fuskan ta “murmushi kawai yayi yakarasa saka kayan har zai fesa perfume din dasauri tace sir ajiyewa yayi yace ok ok ma am sorry wani yadauka shima kadan yasaka kafin yadauki mukullin mota yana kamata suka fita front sit yabude mata tashiga shima ya zagaya ya shiga yatayar da motar suka fita da anguwan resting kanta tayi a sit din motar yakalleta kafin yasaka hannu yakamo nata hannu tabude ido jikinta zafi sosai yanzu kuma “bude ido tayi suka hada ido yayi mata murmushi yace sannu “ta gyada masa kai kafin tace what’s wrong with me sir fever nake nasan is not asthma kuma ni is very hard nayi amai amma ko damuka dawo asibitin after all the treatments sai danayi wani “ yayi shiru yana tunanin yafada mata ko kyaleta wani yayi maganar gabanta? Ahankali wani zuciya yace better inform her yourself “ sake kama hannunta yayi kafin gently yayi parking murmushi kwance a fuskanshi yawara ido yace just guess what? Ta bata fuska tace am not good in guessing fa yace amma promised me zaki bani gift idan nafada maki kaman wata yar yarinya tace Allah zan baka akwai wani watch nagansa a ig will order it for you Wallahi nayi alkawari yayi murmushi yace ohk mrs Abdool nayarda tace oya be fast and tell me yace ohk dear congratulations you will soon give birth to Malik’s copy in sha Allah “you are pregnant baby girl nayi miki ciki.

Wani kalan kallo tayi masa kafin ta girgiza masa kai dawani kalan tone tace wait wait sir bangane ba what did you just say nine ke da ciki kana nufin am pregnant did I even hear it well ko kunne na ne ya ji hakan???? Tana kallonsa kaman idonta zai fito gaban na wani irin bugawa “ shidai Malik sai kallonta yake daman yasan sai anyi hakan “kanta tasa in between her laps ta fashe masa da kuka “ mai sauti shidai mamaki tama basa baiyi tunanin abun zai kai ga kuka ba don ma yasan ita kuka bawani babban aiki bane a

wurinta “ hannu yasa gently yafara caressing head dinta “ ta dago tana kallonsa tace but you promised me ba yanzu zanyi ciki ba shiyasa nace maka kamun allura ko pills kace mun ai baka bi hanyar da zakayi mun ciki ba nine nace maka am ready to give birth nine nace maka zan iya haihu for now?yayah miyasa baka tausai? Zakayi sexing dinna babu ko kula da am tired or not “ ina hakuri kawaii na daurewa ne ba don bana shan wahala ba “nace duk na amince da hakan amma don Allah kada nayi ciki “ shine kayi mun inalilahi waina illahil rajiun da wanne zanji nabani “ tasake rushe masa da kuka Wallahi kallonta yake ko kiftawa babu kaman idonsa zai fado tsaban yanda yake kallonta “ yarinyar nan mi take nufi ne hannunsa yasa ya murza goshin sa kafin yakamo hannunta ta fizge tana cizgar kuka kaman wacce aka daka “tace ahaka zan cigaba da yin this sickness haka kasan wahalan danasha daga jiya har zuwa yau “ bana son cin komai bana son abinci jikina fever bana jin dadin komai “ kashe motan yayi da yake a kunne “ kanta ya dago yawarware tissue daga cikin tissue box din mota ya goge mata hawayen ta tass “ har ga Allah bai ji zafin words dinta basai ma tausayi data basa batasan duk kalan wannan abun is necessary for woman’s ba “ shiru tayi tana ta saukan da ajiyan zuciya irin wanda yayi kuka mai mugun ciwon nan “muryar sa can kasa cike da lallashi da so dakuma tsananin tausayinta dayaji “ yace mamana taki dagowa yace ki ja numfashi tayi yanda yace “yace ki fesar still tasakeyi “ kafin yace am critical sorry mama “banyi niyyar saka ki kuka ba kuma this is not my fault dear Allah ne yayi manah kyauta babu yanda zaayi “kamata yayi kiyi murna sai ki godewa Allah akan kyautar dayayi miki “Manzon Allah SAW yace kuyi aure ku hayayyafa don nayi alfahari da gobe a gobe kiyamah “ did you want us to push this rahama girl?tayi shiru yajuyo yana facing dinta Sosai yasa hannu biyu yana rike both hands dinta yace see madam “ Ai you know my field right? Ta gyada masa kai yace you know who am I and you trust my qualification you trust my occupation right?ta jinjina masa kai while wiping off her tears da gefen hijab dinta yace babyn na kaiwa months din haihuwar sa zan cire miki shi in sha Allah you will not go through the painful of labour kuma wama yafada miki haihuwan da wahala?ta girgiza kai tace ai nasani kuma naji ana fada “ yace tau ke ai babyn Doctor ce bazan tabari ki wahala ba duk da ba wai ta yarda dashi ba amma ta ce you promised?ya gyada mata yakai yana smile tayi shiru dai tana kuka silently yajawota yana shafa bayanta kukan nan datayi har takara wa kanta zazzabi Wallahi yana son aydarh shi yana tausayinta he values his wife “daya nada hali yanda zayayi da bai bar laulayi yasata wahala ba “ amma he promised himself koda zaiyi loosing aikinsa ya yarda kawai don ya zauna ya kula da matansa bazai kara zuwa ko nan da can ba wurinta zai dinga zama ya kula da abunsa “idan ma

takama hutu zai dauka har sai cikin yayi kwari “ ta dago a firgice yayi saurin rike ta tasake marairaice fuska tafasa masa wani sabon kukan runtse ido yayi ya ciza gefen lips dinsa da mugun karfi kaman zaya fasa su “kafin ahankali kaman wanda zaiyi kuka yace minene cuddle bug? Tace sir who will feed the baby ma? Har yasu tabashi dariya dai ya daure kawai yayi pointing boobs dinta yace gashinan ke mana ta girgiza masa kai dasauri tace no ah’ah gaskia nine zan dinga fita dashi daga riga in public ina bayar wa kunya nake Wallahi bazan iya ba “ whatttttttt malik yayi murmushi yace kina ji ba ni ma bazan bari a dinga fito da this pretty balloons din nawab a mutane na gani this place is only made for me darl “dasauri tasa hijab tana rufe idonta duk da halim datake ciki sai da taji kunya “ahankali tace bad “ yayi murmushi kafin yaje daidai kunnanta yace this nono is for me na ni babansa ne shikuma zan mu basa formula how do you see the deal?yafada yawani dariya tadago ta maka masa harara tace kai bazaka sake mun wayau ka sha ba “ ya marairaice fuska kaman gaske yace tau ba zan sake cin abinci ba ma “tace wannan kuma ruwanka “ ya kunna motar tace ina zakaje bance na hakura ba fa I will thinks about it “ yace okay favorite in sha Allah zakiyi tunani mai kyau ba pity the innocence creature please “and pity his father don Allah ASSEIYARH har cikin ranta taji maganar sa yakai mata har kasan zuciya “ batace masa komai ba tayi kasa da kanta don kan ma ciwo yake mata ga tashin zuciyan datake ji “koi na na joints dinta amsawa suke “ tayar da motar yayi yahau titi yana shara gudu “bakin wani hadaddan cold stone yayi parking baya son tasha sanyi amma for only today zaya mata abunda take so just to makes her happy aji tausan su shida dan unborn dinsa “kadan yace zaki shiga ciki ko nasiya miki fav dinki ta gyada masa kai kawai fita yayi ya kulleta a motan ta bi bayansa da kallo taki dauke ido is damn hot yayi tsayi dayawa gashi wani murdade “zubinsa irin ma lafiyayun maza masu ji da kudi gayu illimi haduwa dakuma karfi “ ita bata taba ganin hadaddan namiji ba kaman duk kau a Nigeria zata iya ilga kasan dabata je bako don bata damuwa da mutane bane shiyasa bata lura yanada wani irin nutsuwa ta daukan hankali “he is hundred percent “tama rasa kawai abunda take ji akansa “ lumshe idonta tayi ta kwanta da kanta jikin sit din “bai wani jima Sosai a ciki ba yafito hannunsa rike da paper bags kwara biyu sai wani leda mai sunan wajan yakaro sa yabude motan yashigo gently tabude idonta yace sannu ta jinjina masa kai cike da lallashi yace zaki sha yanzu ko muyi sauri mu karasa gida? Ta girgiza kai kafin tace zan sha dasauri yahau bude ledan ya fito da classic popsicle na yan gayun nan favours kala da iri yasan tafi son anything choco shiyass ya warware mata choco delight yayi bismillah yana kai mata a baki yana adduar Allahu yasa ko shine kawai yazauna a cikinta bai so tasha kayan sanyi ba amma babu yanda zayayi ne “

bude bakinta tayi tafara licking yamata dadi sosai bakin tissue yaciro da dayan hannu ya tara kasa kafin ya cigaba da bata tana sha murmushi yayi ganin tana sha “can ta janye bakin tana kallonsa yace minene?ta girgiza kai tace ya isa yace ki kara ko kadan sai ga hawaye tace sanyi nake ji ya gyada kai yasa tissue yagyara mata idan yayi stain kadan a gefen bakinta da hijab dinta yasauke glass yana fitar da tissue din kafin ya maida ya rufe ‘pop din yamayar cikin leda kafin ya tayar da motar baki daya hankalinsa na kanta yarasa mi zai siya tace ya zauna mata “ tafiya yayi har wani babban Cakestries “ yayi parking tabude idonta tace mi zaka siya?yace da cake zan karbo miki ko zaki iya ci cuddle bug batace masa komai ba yafita “ yatarar da hadda grilled meat and chicken ma a wurin siya yayi both two din kafin yace abasa sponge cake yasan bata cin wani cake apart from sponge Ko redvelvet ma da matar ta dauko masa girgiza kai yayi yace ta barsa banda shi kudin ya biya yafito yanzu ma da uban ledoji a hannunsa “ this time bai tambayi shawaran ta ba kawai yabude “ yafara mika mata grilled chicken din bata ji wani tashin zuciya ba yakarbi yanka dayan daya kai mata baki “ tana taunawa kadan kadan shikam sai addua yake Allah yasa ta zauna aikam har pieces uku ta karba ai kam yaji dadi bana wasa ba ya bude sponge cake din shima taci ba laifi duk cikin mota kaman abun bala’I bottle water yabude yakai mata tasha kusan rabi yayi murmushi yace tau sannu yan matana “tayi masa wani harara tace nine yanmata ai am not longer yanmata yarinyar dake da ciki yanzu shknn ummi dakowa yasan muna yi “tasa hannun tana goge hawaye yawara ido yace subhanallah kinga namanta ma inalilahi waina illahil rajiun yanzu shknn duk kowa yasan kina zuwa wurina wayyo Allah wani kalan juyowa tayi tana gyara zama cike da tsoro ta kamo hannunsa tace sun san am pregnant? Ta gyada mata kai tarufe fuskanta ta fashe da kuka tace shknn am done nabani na shiga uku wayyo Allah na inalilahi waina illahil rajiun “ yace ina da shawara ta gyada masa kai yace mu boye kanmu kar su dinga ganin mu tace to ina ?yace can gidan abby a part dina sai mu dinga kwanan mu can tayi shiru kafin tace to babu wanda zai san ina kwana wajanka again idan kuma kasake cewa zakayi fa tunda kawai you will never be patience “malik trying very hard not to laugh yace tau ai shknn ni daman taimakon ki zanyi amma dai ai da kunya ace har kin iya zuwa wajan miji kuna kwanciya wai fa hadda ciki duka takai masa a kirji tace duk bakai kaja ba “ kullun abu daya kullun abu daya wayyo Allah “ yace yanzu dai jikinki akwai fever mu tsaya pharmarcy zan Chanza miki drugs yakamata fever nan yasauka by now “tace ina jin tashin zuciya da ciwon kai am all my body is aching me yace duk zai bari in sha Allah ta gyada masa kai sam bataji dadi sanin da su ummi sukayi ba amma yazatayi “idan ma oum ko mom sun tambayeta zatace ita bata sani ba “ yace

zaki kara cake din tagirgiza kai tace zan cii dan munje gida “yace ohk wife ta juya kai ta cigaba da kallon titi kawai ji tayi kaman abunda taci yanzu zai dawo mata ta dafe cikinta “ta rike hannunsa ahankali tace ka tsaya dakarfi daka Breakerr yayi dasauri tabude kofan mota ta dinga kwara amai babu sausautawa kaman zata fitar da duk kayan cikinta “ dasauri yafito daga mota yadauki ruwa Wallahi bakaramin tausayi tabasa ba da alama cikin bai zo mata dawasa ba baiwar Allah bakinta yawanke mata kawai ta rushe masa da kuka zagayowa yayi caressing her head sai kuka take masa jikinta yakara zafi kaman wuta dakyar ya lallabata tayi shiru “ ya tayar da mota sai pharmarcy da kansa ya zagaya har can ciki ya dauko drip da drugs hadda na tsayar da aman ya Chanza mata injections yabiya yafito “ tayi lamo kan kujera sai hawaye take ji yayi duk wani kala yakamo hannunta yace kinga is okay kinji darling kiyi hakuri zaki daina in sha Allah batace masa komai ba.Suna karasawa gida suka tarar da ummi da oum sai rufaidarh Alhamdulilah yace aransa tunda babu hajajju by now ma yasan she slept “ hannunsa a nata ga maids da wannan uban siyayyan dayayi mata bata ci ba jiri take gani da daukan zaiyi taki kaman tasan suna parlor kasa “suna shigowa ummi ta mike dasauri “ tace subhanallah jikin ne haba malan taya zaka fita da ita in suchs condition kaima kaman ba likita ba fisabillahi rufaidarh tace son dana ga kun fita nayi tunanin ta warware oum tace tunda dai sun dawo yanzu ai shknn kamshi kifi taji kaman ana soya shi taji wani kala kaman zata suma aikam sai ga amai karfinta yakare baki daya babu wani abu a cikinta banda ruwa “Wallahi oum juyan da kanta tay isai ga hawaye bazata so ace ita aydarh ta biyo ba wannan na daya daga cikin dalilin abba na hana oum haihuwa saboda wahalan datake sha bana wasa ba gashi data samu ciki sai ya zube aydarh ce kawai cikinta ya tsaya amma duk sai da aka fitar ma oum rai daga rayuwa “ kitchen kawai tashige batare da ta juyo ba ummi duk ta rude ganin yanda yarinyar ke faman kwara amai kaman zata mutu “malik kau yakama matar sa yarike yanata faman mata sannu “rufaidarh tace bara na kamata muje sama sai a wanke jikin “ummi tace aaa yadauke tunda kila bazata iya tafiyar ba,tun kafin ummi tayi shiru yadauke ta yayi hanyar dakin ta da ita duk suka bishi baya babu wanda ma yalura da cewa oum bata nan toilet yashiga da ita yacire mata kayan jikinta yasa towel da ruwan zafi ya goge mata jikin nata tama kasa ko da kukan Allah “ fitowa yayi duk suna zaune yawuce closet dinta yafito mata dawani kayan yakoma yasaka mata yafito da ita kan gado ya kwantar da ita “ kafin yakoma kasa dasauri ya kwaso maganin sai binsa suke da kallo rufaidarh tayi dan murmushi tana kallon ummi tace bawan Allah yabani tausai ummi tace hankalinsa duk ya tashi daman shi can baya son ganin rashin lafiya balle har irin wannan duk sai ya rikice kaman ba likita ba “rufaidarh tace

tagirgiza masa kai yace tau gobe dasafe in sha Allah dr faisal zai mata introducing kansa nasan ma bazatayi rejecting bay ace bazai koma Lagos bas ai ansaka biki aydarh tace that’s nice Alhamdulilah am so happy for her “ amma da dakace wai uncle din uncle usama sai naji babu dadi yace ai dakika ce no kinga ban sake tayar da maganar bat ace better of you yace kinaji gobe kika saka kala wannan perfume din a daki zani rufe ki bazaki fito wunin ba tace kayi hakuri zan gyara yace shknn yanzu zan sa atashi dare yayi tace ohk yace and tonight din tayi saurin dauke kanta tana murmushi yace na yafe miki har agama hidima amma duk zaki biya tawara ido tace yes zaka sha mamaki yace ahan ahhhh yamike atare suka jera tanufi inda oum take suka gaisa da wasu baki shikuma yaje yasanar lokacin tashi yayi “kasancewan gobe wuni ne da budar kai dazzy da alijita har gobe su zasuyi performing yasa suka sauka a hotel Alhamdulilah kamu ya tashi lafiya kudi ned ai ankashe su har basan adadi ba. Rana bata karya saidai uwar diya taji kunya a yau aka shaida daurin auran Usama Ali kusa da Rufaidarh Abdulfatah bin arab “auran daya samu halatar manya manya masu kudi damasu mulkin sarauta da siyasa na kasa kasa ko da kanin babansu rufaidarh yazo yace yabawa abba wakilcin daurin auran shikuma abba yace yabawa abby abby yazama wakilin rufaidarh Alhamdulilah andaura aure kan sadaki naira million daya da sisin gold dari biyar wanda aladar familyn su ce ahaka fadin irin farincikin da oum tashiga a yau wani babban aiki ne kana ganinta kasan she is happy yauma kaman jiya sun shaa makeup dan dai yau fabric dinsu kala dayane dinkin ma kala dayane banda hibba kawai da akayi ma boubou saboda ciki “kaman jiya yau ma straight gown ce akayi ma aydarh fabric din yaci kudinsa yayi kyau irin sosai dinnan sukayi kyau masha Allah wasu mad low fast ne kafan aydarh black sunyi kyau sosai sunyi ma kafar kyau flat ne sosai daidai veil dinsu kala dayane bayan andawo daurin aure a parlor dr usama yashigo dasu malik akayi pictures din daurin aure kala lace daya oum da rufaidarh suka saka lace nakusa 1.something million sunyi kyau bana wasa ba rufaidarh daice duk tayi wani sukuku dr usama yakamata akayi pictures kafin gaban kowa yayi pricing dinta in dollars and ponds ya biya fuskan ta wanda ban masan adadin nawa bane “da oum tazo akayi musu hoto tare da rufaidarh da dr usama rufaidarh fashewa tayi da kuka tana rike oum Wallahi daurewa kawai take amma itama kukan take son yi amma bata son rufaidarh taga tana kuka ummi ta lallaba rufaidarh aka gyara mata kwalliya su Doctor usaman dasu abby da duk mazan aka wuce wajan reception wanda governor yahada reception din da kansa “ malik sai daya tsaya akayi musu couples picture da aydarh sunyi kyau Allahumma bareek flash vedio photographer yasaka su maryam suyi mashi yayi masu malik din hoto abayanta yasa yasa hannunsa daya a waist

dinta itama ta daura nata a nasa “ yasa kansa a neck dinta din kafin tasa hannunta daya a cheeks dinsa Barakallah style din yayi kyau sosai su ummi da oum da rufaidarh duk wucewa sukayi aka bar yanmata kawai na photon wani kuma yasata a jikinsa kaman zaya maidata a jikinsa Wallahi kaman ango da amarya yanda sukayi kyau a hoton saida aka gama tass kafin malik yace dr hafsa tazo zaiyi magana da ita aydarh tabiyo sa in brief yayi mata bayanin komai batace komai tace duk abunda yayi daidai ne aydarh tace kinyarda auntie? Dr hafsa tagyada kai kawai malik yayi murmushi kafin yafita yakira dr faisal yace yasami hafsa din a parlor kasa “ nan babu kowa duk ana compound din gidan ana wuni,Aydarh tace jiya da kana son abincin ai magana kayi mun shine yau zaka yiwa rabiah magana tasamu muku abinci kai da nr yasir shine zaka cemun crush dinsa ce Allah sai ka fadamun abunda ke tsakanin ka da ita tafada tana fashe masa dawani shagwababan kuka yadafe kansa yana gyara babbar rigarsa “ yace Wallahi Allah cuddle bug shine kawai abunda yasa ki yarda manah “dazai shigo dakin yaga maryam kuma suna tare da rabiah lokacin dayayi mata maganar zaya ja ma kansa wajan gyarawa wani wasa shi zaya lalata nasa bai da wani solution bayan yakira maryam tabada shaida hanyar kofa yanufa takallesa tace ohh fita zakayi kenan? Yace wayyo Allah Wallahi yasan masu karamin ciki da rigima ga masifa da sai yace yaje yayi yanda take masifan nan fita yayi luckly yaga maryam a wajan halime namata hoto da waya har basu gajiya da hoto yace lilyy come here maryam tace ohk yayah bayansa ta bi suka shiga dakin aydarh na gefen gado inda yabarta fuskar nan dinki Ko murmushi babu maryam tace gani yayah malik yace kifadawa auntie maganar danayi da rabiah.

Aydarh tayi masa wani kallo Wallahi apart from su maryam bata son taga yana magana da duk wata macce on this earth ‘maryam ta tsaya gefen malik dake nan tsaye kusa da sofa yayi kaman wani marar gaskia babban rigansa ma ya jirkiceta ‘maryam tace muna tare da ita ne dazu kace mata takawo muku abinci a can kofan gida nurse yasir naso zaiyi magana da ita Allah auntie ki yarda shine kawai abunda yafaru yanzu haka ma rabiah suna tare dashi nurse yasir din “Aydarh tayi kasa da kai don Wallahi kunya ma taji bata so yakira maryam din ba kar suga kaman ta raina musu dan uwa zaiyi magana taki yarda kawai dai she cannot control her heart saboda kishi “ aydarh tace erh yah mariam shima yayi niyyan kiranki ne amma ba ma maganan danayi ba kenan maryam tayi murmushi tace bara natafi malik yagyada kaii maryam tajuya ta fita yadawo kusa da aydarh yakamo hannunta tasa hannu tana kama kunnansa bawai zafi yaji ba amma sai dayayi yar kara dasauri tasaki tace shine zaka kira yah mariam duk don

kowa yace bana yarda dakai yace aie kece kaman kishi yasa kin iya masifa Allah “ tajawo sa tasaka kansa a kirjinta yayi wani ajiyan zuciya yanka wuyan rigan yayi kyau ga diamond necklace dan karami black a wuyanta kalan fabric din black ne sai silver kadan ajiki “ hannu yasa yana wasa da sarkan kamshin fatan ta nayi mashi irin fresh strawberry dinnan ga fatan har milky milky take “ har tacikin riganta yake sa hannu sa tasaman boobs din tana jinsa batace masa komai ba saima wayanta da dauka tashiga chart din aysha ganin pictures da vedios din daakayi musu yau har anyi editing dinsu budewa tayi tafara scrolling tana kallo shima kallo yake still kansa kwance a boobs dinta wani slide ne wanda style din yafi mata kyau murmushi tayi tace kaganka kaman gaske you fine “malik yatashi zaune yace keeee “nine ma kaman gaske am fine tau ni yanzu abunda zan fada ma shine bazan yafewa camera din nan ba saboda ta mayar dani wani kala wasu kuma anyi musu kyau tayi dariya tace jealously kawai kafito fili kace kaga hot cake ka like mata ‘Ni fa daina magana zanyi da mutane saboda haduwan mijina malik yayi murmushi Allahu yaja long pointed nose dinta yace you are funny ‘tayi murmushi ahankali yarufe idonsa har cikin zuciyarsa yaji murmushin yace nima zan saka hakorin makka “tace lahhhhh baya ma maza kyau Allah yace tau ke yaakayi yamiki kyau ta tada kansa daga kan boobs dinta tace oh ni mazane kenan?yayi shiru yana murmushi tace karka sake kwanta mun anan tau dasauri yakama hannunta yana dariya yace ai duk duniya a wajena kowa namiji ne apart from you tayi murmushi tana juya masa eyes yasaki baki yana kallonta tace to bara dai kasa hakori bayace in sha Allah aie zamuje umra bah this umrah dazaayi tayi shiru kafin tace to yace kingani I have never been there before idan mukaje wannan karon is my first time tace eyyerh Allah sarki yace bara natafi kafin ibrahim yaje yadinga spreading news nataho wajanki nabarsu da hidima aydarh tayi murmushi tace Alright kaje tare suka fito daga dakin suka fita compound din gidan anata hidima biki akayi mai sunan biki biki na nunawa a duniya bikin da naira tayi magana wajan yin shi ance ansha an zubda kudi Alhamdulilah saidai muce Allah yaba amarya da ango zaman lapia Ameen “ ummi dake kallon aydarh tace sannu baby aydarh tayi kasa da kai tace Alhamdulilah baba tace ai bata da lanbo ma nalura da tanada shi kam bikin nan da yanzu ta fice Hayyacinta laulayi ba sauki Allah yasawwake ummi tace Ameen Ameen ummi tace bara naje gida can ma akwai baki daga kuma hajajju sai inna acan suke nasu wuni baba tace tau mi yahana su zama bayan angama kidin ummi tayi yar dariya tace Wallahi bansani ba baba “mariam tashigo parlor da waya kare a kunnata halime take kira yayansu yace dr umar ke son yayi magana da ita janye wayar tayi tana tambayar aydarh ina halimen??aysha tace aie zaa tambaya ina tare kuka fita daga

compound maryam tace aaaa Wallahi tare sukaje da auntie hafsa nida rabiah muka fita aydarh tace ko zaki duba dakin mom maybe sunje can tare naji tana neman wiper zata goge kwalliyanta Maryam tace bara naduba ummi tayi yar dariya tace Allah sarki uktiee ita fa baki daya yau a sukuku take tunda akace an daura auran nan dazu ma da oum namata manni ina ganin tana kuka aydarh dai tayi murmushi ahankali tamike tace bara naje wajan mom din ummi tagyada kai itama tana mikewa tace bara tace tunda dai baki sun fara ragewa itama ta sallami nata baba tamike tace bara ta bita aysha ta cigaba da zama a parlor dawaya ahannunta nata duba posting din bloggers a ig na bikin nasu sunyi trending bana wasa ba saboda biki ne akayi na manya “ bata goge makeup dinta bai ta sai kallabinta daya ja baya kadan gashinta yafito maids nata gyaran parlor dayake babu mutane vip kawai aka ajiye awurin kuma dayawansu sun tafi oum ko ganuwa batayi yau saboda hidima abby da abba duk suna can tare da manya manya kasar da wasu cikin su duk sai gobe flight dinsu zaaya tashi ‘ sallama akayi aysha ta amsa gently yakaraso cikin parlor yazauna kan sofa kanta tadago tana ganinsa tagane sa shine mc din jiya wanda already tasan shi matsayin tight din malik a school dauke kai tayi ahankali tace ina wuni ya aiki ya gajiya dazzy yayi murmushi yace Alhamdulilah kyau!tawara ido cike da miskilanci tace kyau kuma dazzy ya jinjina kai yace pretty sure tasa hannu tana rufe fuskanta yace kece kawai baki wanke kwalliyar ba why? Tace zan wanke anjima am tired for now yace daman kinada alwalla ba?ko lafiya lau akeyin alwalla dashi?tayi kasa da kai bata salla shiyasa ma bata goge kwalliyar ba shiru tayi tana dan murmushi yakama goshin saa yace sorry little I talks much right tagirgiza kai yace first of all sai kinyi hakuri dani yeah?saboda I talks much gaskia shiyasa ma nake mc and ke kuma you are not use to talk ta daiyi shiru dazzy yace without wasting much of time kinsani kinsan who am I ,kuma kafin nazo wajanki sai dana tambayi izini wajan abokina which is your biological brother ya isa dake a komai and his friend kaman yanda kika sani “Ayshatourh nib a yaro bane kema kanki nasan ba yarinya bace bantaba soyayya ba cus ban samu type dina baduk wacce kika ganmu tare ita tace tana sona bani nace mata ba aysha dai ta kallesa yace “kafin nazo yayan yafadamun bakya soyayya da kowa kuma babu wanda akayi ma alkawarin aurenki ta gyada masa kai yace tau Alhamdulilah ayshatourh idan kina sona nayi miki ina sonki da aure dasauri tayi kasa dai tana jin wani kala Wallahi ba don alkunya na musulunci ba da hausa fulani da sai tayi murmushi agabanshi mikewa tayi tahaye upstairs dagudu Wallahi bin bayanta yayi da kallo yana girgiza kai with smile on his face “ daki na farko tashige tana jingina jikin kofan ta dafe kirjinta tana sauke ajiyan zuciya kwalla yaciko idonta ga dariya a fuskanta whatttttttt itace ake ma zancan

aure ahankali tace Alhamdulilah Alhamdulilah Allah na gode maka tarufe ido sai ga hawaye Wallahi batasan iyakar farincikin datake ciki ba ayanzu ita wa zata fada mawa ummi?dasauri ta girgiza kai tace kaiii no ina jin kunya wata zuciya tace ga halime da maryam ne ‘daga karshe dai kawai yankewa tayi zata fadawa Aydarh kusan ten minutes kafin tafito daga dakin ai kawai dakin aydarh tawuce babu kowa sai maryam da dr hafsa data dawo daga wurin dr faisal yanzu tunda suka shirya na wunin take wurinsa data dawo sai kuma yasake kiranta har dai tagaji gashi fa bawani labari suke bas ai labarin aiki sai kuma maganar baya so ya koma Lagos sai anyi engaged dinsu dr hafsa na kwance don tagaji Wallahi bata cika saka hills ba amma tunda aka fara bikin nan dasu suke wuni a kafan su kuma duk aikin oum ne dole sai anyi gayu aysha na shigo maryam tadinga kallonta ganin kaman she is happy tasan halin addar tasu idan tana farinciki dole sai kagani saboda haka nature dinta yake kaman batada walwala shiyasa farat daya ake fahimtar farincikinta maryam ta tashi zaune tace addah tells me mike faruwa ne dan Allah naga kaman you are happy aysha tace gulma kawai dr hafsa ta tashi zaune tac eke Sholly dan Allah fada mana minene aysha ta zauna tana yin kasa da kaii tace uhm dr hafsa tace wai uhm da miye bana son wannan abun fa maryam dake very eager taji minene tace kaii addah kiyi magana pleaseeeeeeeeee aysha tace zan fada fa dr hafsa tace tau ki fada manah aysha tace auntie faa? Maryam tace tana wurin mom fr ko na kirata ayi a gabanta aysha ta gyada kai dagudu maryam tafice bayan tasaka slippers din aydarh dake nan kofan dakin already tace hills din kafanta “ dakin rufaidarh tawuce sai datayi knocking aydarh tace come in shiga tayi aydarh tagoge nata makeup din ta warware kallabin rufaidarh ma ta chanza kayanta zuwa wani vilisco sky blue da pink riga da zane “ babu ko mai a fuskanta tayi fauuu barakallah idonta yayi ja alaman kuka tayi aydarh ta kwantar da kanta jikinta maryam ta gaishe da rufaidarh ta amsa tace sannunku maryam maryam tace sannu mom Aydarh tace yes yah mariam kina nema na?maryam tagyada kai tace ehhh dan Allah rufaidarh tace tau kuje can dakin aydarh tace tau mom zan dawo rufaidarh tagyada kai tace tohm baby son ma yaje yakawo uncle dinku yanzu zasu zo tare aydarh tace ohk ina oum fa ? Rufaidarh tace taje raka matan senate president airport nasan yanzu zata dawo akwai mutane har yanzu ba?’maryam tace ehh mom akwai sosai amma a guest side rufaidarh tace ohk ‘aydarh tace promise me bara kiyi kuka ba please tafada tana marairaicewa rufaidarh ta gyada kai fita sukayi tare dakin aydarh suka shiga ahankali aydarh tazauna Wallahi idan kana da ciki duk jikinka wani kala yake komawa “yanzu duk bata jin dadi Wallahi “tace Allah yasa lapia dai auntie miya faru dr hafsa tace ahtau shi nake tunani nima yanzu tace wai sai kinzo tafada aydarh tace please

addah we are all ears shaaaaa aysha tadago tana murmushi tace it’s dazzy maryam tace yah dazzy yayi mine dr hafsa tace waye dazzy din aydarh tace kaman wannan mc din abokin sir right maryam ta jinjina kaiii tace eh eh shine dai aydarh tace miyayi ne wai aysha tarufe fuska tace yacemun yana sona maryam tayi wani ihu aydarh tayi murmushi dr hafsa tace ohhhhhhh is the year for us Allahumma bareek Alhamdulilah yah rabbi maryam tayi hugging aysha daidai halime da Rabiah sun shigo dr hafsa tafada abunda ke faruwa kowa sai murna yake cikin su aydarh tayi musu murna Wallahi taji dadi yanzu maryam kawai yarage a single kowa is token yanzu masha Allah hibba na can gidan tagaji tana wajan ummi “ dr hafsa tace duk rana daya zaayi yanzu kila aydarh tayi murmushi tamike tace mune manya so sai yanda mukayi deciding tafada tana murmushi maryam tace yes my auntie kice ma yayah don Allah next month ayi aydarh tayi dariya tace in sha Allah “.Dr usama na kallon malik yace gobe in sha Allah komai sha biyu zamu wuce in sha Allah malik yace Allah yakaimu lapia dr usama yace ko zakayi dropping dr flex a new embar yace yanada guest a can idan kadawo sai mu tafi in sha Allah malik yace Alright uncle kayi masa magana sai muwuce dr usama ya jinjina kai yace sannu son ubangiji yasaka maka da alkhairi yayi maka albarka malik yashafa kansa yace Ameen uncle Allah yabaku zaman lafiya da mom yakawo manah yan kanni next year dr usama yagyara glasses din sa yana murmushi yace maybe am your granpa yanzu tunda kamun aure aie dole malik yayi murmushi yace noooooo sorry buddy wasa nake dr usama yace nima aie murmushi dr usama yayi yabashi side hug ‘dr flex sukayi sallama da malik bayan ya ajiyesa ‘yajuya dawani irin speed yake driving din a titi babu kowa kan titin kasancewan hanya baa cika shige da fice ba “gudu yake sosai bana wasa ba ko kadan trailer batayi horn bas ai shawo corner kawai tayi malik the thing cames to him out of a sudden inalilahi waina illahil rajiun wani irin banka trailer tayiwa motansa “kyyyyyyyyyyyyyyyyy kake ji subhanallah dawani irin sauri mai motan ya taka birki salati kawai yake ganin abunda yafaru glass din gaban motan malik yayi wani kalan damage “hankalinsa yayi tashi saboda ko dawasa bazai kawo ma ransa na cikin motar zai rayu ba bude motan yayi ganin kan malik yama langabe gefe ga jini a goshin sa “ya bata farin shadda shi hulan kansa yacire har cikin suman kanshi jini ne rudewa mutunmin yayi gani balaraban mutun a suchs condition ga motar tashi kana gani kaga kudi Wallahi rasa yanda zayayi yayi Wallahi ganin irin abunda yayi ma mai kudin nan baidawo cikin hayacin sa ba sai dayaji ringing din Expensive Iphone din malik di dasauri yadauka dr usama n eke kiran mutunmin yace mai wayan yayi hadari yanzu haka mun nufi federal medical center dashi Wallahi dr usama bai tsaya ma karasa maganar ba ya kashe wayar duk su dr ibrahim dasu abby na wurin suka

tambayesa miya faru ganin duk ya gigice yafada musu Wallahi duk sun rude abby ne yayi karfin halin cewa su tafi asibitin mota biyu suka cika suka nufi asibitin, daidai sun karaso daidai ankawo malik basu sha wahala ba suka hadu aka shiga da malik accidents and emergency kowa na asibitin hankalinsu yadawo kan classy mutanan dasuka gani abba ne a rude yake magana da doctors ayi duk abunda yadace idan bazai yiyu ba abasu shi su fita daga kasar yanzu dr ibrahim da dr faisal kasa hakuri suka saida suka shiga dakin da aka kai malik sukace zasu taimaka gani suke kaman doctors din nan basu ma san abunda sukeyi ba " shidai dr usama yazama kaman wani status tunda yayi shiru yakasa motsi babu abunda ke mashi reversing a brain irin hadarin matarsa da dansa idan abunda yafaru dasu yafaru da malik zai iya hadan zuciya ya mutu,tun dazu take jin duk wani kala Wallahi lafiya lafiya fa suke zaune amma yanzu ji take gabanta na faduwa kaman wani abu na shirin faruwa da ita har sai da Hibba ta lura tayi mata magana tace babu komai tana ganin gajiya ne kawai ' baba dake parlor tayi shiru bayan tagama waya da abby batasan ta inda zata fara fada musu this bad news ba inalilahi waina illahil rajiun kawai take repeating a mind dinta ga inna da hajajju sai zuba suke kaman kanya labari kuma marar kai marar kugu " baba tamike ganin kaman zai fi sauki tafadawa oum kan ummi dakin oum tanufa oum naganinta tace ahh baba ai da kunsaka ankira ni sannu ya gajiya baba tayi murmushin karfin hali tace Alhamdulilah fatima "cikin hikima baba tayi ma oum narrating komai Wallahi oum zama tayi tabas tadafe kaiii Hankalinta yayi mugun tashi kaman dai yanda ummi zatayi a ganin baban ma oum sai tafi ummi din tadauka abun zai fi zuwa dasauki Wallahi oum komai kwance mata yayi tafita ta kwatsa maganar "ummi kaman daga sama taji zancan "lokacin su aydarh na daki rabiah tashigan musu da maganar kwata kwata aydarh bata gane ba don bata maji da kyau ba dr hafsa tayi mata alamar datayi shiru 'inna da hajajju suka dinga ruri "dakyar aka samu baba da rufaidarh suka tsawata ma kukan duk suka a firgican suke ummi dai tayi shiru tana kallon wuri daya saboda a tunanin ta ma yarasu aka rufe musu daman tunda yamma take jin kirjinta na bugawa Wallahi ashe da dalili "baba tace su fito suje asibitin hajajju sai ihu take tana sun bani sun shiga uku " gatan su yakare 'oum tasa dr hafsa tariko mata aydarh suna zuwa parlor aydarh dai sai bin kowa take da kallo ganin hajajju da inna na kuka yasa gabanta yin wani mumunar faduwa har sai data rufe ido tana inalilahi waina illahil rajiun " sai lokacin ummi tamike su maryam dai saboda aydarh baa san reacting din dazatayi bay asa suka rike kukansu amma kana kallon kowa zaka gansa so disturb karfin hali kawai ummi keyi tana daurewa amma Wallahi ji take kaman zata zube "cikin dabara ummi tafita da aydarh drivers duk sun matso da motan ummi da

shiga da aydarh mota so take ta tambaya amma tama ji bakinta yayi nauyi “oum da rufaidarh sai baba suka shiga mota daya da aydarh da ummi hajajju da inna dasu aysha a dayan mota sai addua suke hibba tace yah rabbi make it easy for him yarinyar can na iya yin miscarriage tsaban shock dan Allah daman gida aka barta halime tace nima banga dalilin tahowa da ita ba Wallahi aysha tace haba dan Allah Wallahi komai yafaru da ita anja mata ne dr hafsa tace dole ne a tafi da ita Allah dai ya kyauta yabashi lafiya maryam tace ai kwara ma da akasaka matan can su biyu dayar motar Wallahi duk su zasu rudata “ suna isa asibitin aydarh dai sai faman kallon su take ummi tasake riketa suka shiga ciki “ abby ne ya tari su hajajju yace asibiti ne baa hayaniya aydarh rike hannun ummi sosai tana jiran ganin abunda ke faru bude kofan emergency akayi Doctors zagaye da gadon daaka turo malik “fashewa maryam da halime sukayi da kuka aydarh takasa bude idonta da kyau balle tayi masa kallo na biyu wani irin juya ke debanta kaman ana juyata!dakyar tace what is wrong kowa yayi shiru babu wanda ya amsata daga voice dinta kawai ya isa yasa kaji tausanyinta dakarfi tace someone should answer me here ‘abby yayi karfin halin cewa kiji daughter ki kwantar da hankalinki ganin babu wanda yayi mata bayani ga oxygen datagani ansa masa anrufe jikinsa banda fuskar sa kaman gawa wani irin jiri ya debeta tayanki jiki tafadi ummi ta zabura duk aka yo kanta jinin ne ke bin white leg dinta.

Wani kalan neman wuri oum tayi ta zuba ma sarautar Allah ido sai lokacin ummi tasamu daman fashewa dawani irin kuka a rude abba yanufi reception din yakira nurses doctors din dasuka turo malik tuni sun wuce dashi x-ray room “rufaidarh da dr hafsa suka kama aydarh suka daura kan wheelchair “ aysha kam kama ummi tayi itama tana fashewa da kukan already su maryam daman kuka suke rabiah na taya su hibba dai ibrahim kama ta yayi ya zaunar da ita saboda lura da yanayin ta Wallahi abby sai dayayi regretting fadawa baba da yasan haka zasu zo tafaru amma lokacin dayakirata irin yanayin nan yashiga na karasa makama da abun yi baki daya lokacin he is not himself kara kawai yake da alkunya Wallahi cikin gaggawa nurses din suka shiga da ita labour room ummi tabi zata shiga suka dakatar da ita suka shige tunda suka zo ta lura da yanda yayi kaman andasa shi a wurin kaman hankalinsa baya jikinsa ma Wallahi rufaidarh baki daya tausayin kansu taji ita da dr usaman idan wani abu yafaru da malik ko abun dake cikin aydarh har kullun zasu ga ta sanadin su abunda yasata fashewa dawani kalan kuka wanda yasa dr usama kaman anyi hitting brain dinsa yadawo daga shock din daya tafi kaman wani wanda yazare yamike tsaye dawani kalan speed yanufeta kamata yayi suka zauna yakama hannunta fim

baice mata ba “Wallahi kowa a cikinsu kana kallon sa zaka ga asalin tashin hankalin dayake ciki kwata kwata babu nutsuwa tareda su mutane sai kallonsu ake kaman t.v wasu nayi musu adduan Allah yaba wanda suka kawo lafiya wasu kuma fargabar ma tunkaro wajan su suke ganin manya mutane haka gasu kaman larabawa “ahankali iya ta mike takarasa kusa da ummi ta dafa kafadanta tace kiyi hakuri hajiya asiya dole kina cikin wani hali amma kuka baya maganin komai ke uwace addua zaayi masu Allah yabasu lafiya in sha Allah babu abu marar kyau wanda zai faru muyi musu addua maryam halime aysha ke rabiah ya isa haka ku daina magana kuka shi marar lafiya addua yake bukata ba kuka ba baba ta gyada kai tace kwarai dagaske inna tace shknn tamu takare mu kuma ya Allah ka dauki ranmu kabar audu Allah kana gani kana ji yaron mutun ne hadda rabi ubangiji Allah yabashi lafiya hajajju Allah yatai maki yarinya can da abunda ke cikinta tadafe kai tace wehuwehu dazu muna cikin murna yanzu kuma anyi manah yankan kauna baba tace ayi addua dai dan Allah kafin takarasa wajan oum tajawo ta tasa ta jikinta ta rage murya tana mata nasihar taba zuciyarta hakuri duk abunda Allah yayi shine mai kyau oum ta gyada kai daman bawai kuka take a fili ba no kukan zuci take mai ciwo “kusan 40mins tunda suka shiga da ita labour room din babu abunda aka ce musu sunyi shiru zuwa yanzu kowa da abunda yake ransa dr ibrahim da dr faisal suna can tare da doctors din kan malik wanda bayan ciwon dayaji a goshi babu wani wuri daya ji ciwo shiyasa har yanzu suna cikin dubasa x ray akaje ayi masa saboda kaman yaji ciwo a hannu dakuma baya sai numfashin sa dake tafiya yana fizga shiyasa aka masa fixing oxygen har yanzu bai san abunda akeyi akansa ba mutumin nan mai trailer tunda su abba suka karaso Wallahi gani yake kaman yagama yawo yabanke yaron masu kudi har haka shikam bai san iyakar hukuncin dazaa masa ba kila ma suce daga nan ayi prison dashi ganin babu sark isai Allah yadinga istigifari yasamu yafice daga asibitin dasauri car key din malik ya ajiye motar yayi damage buh yana tashi dashi ma suka zo asibitin “ can sai ga wata nurse tafito rasa ma wanda yafara tashi cikinsu za kayi wani irin zabura suka kaman zasu cinye ta ganin hakan yasa tayi dan murmushi tana girgiza kaii abby yayi karfin halin cewa lafiya take ita da abunda ke cikinta ba? Wallahi ummi ji tayi har zuciyarta zata fito saboda rashin sanin abunda zaa ce yafaru da cikin nurse din tace where is her husband dr usama yamike yadaka mata wani tsawa yace what the hell are you doing “what’s your business with her husband? Can’t you talk ma’am ganin yanda yake magana with so much anger idonsa kaman zaiyi aman wuta yazare medicated glasses dinshi ahankali rufaidarh tasa hannu tarike hannunsa tana girgiza mashi kai shiru yayi kawai dazzy shima da nurse din tabashi haushi yayi magana sounding so pissed up yace kinga

malama kimana magana ki fada manah ya jikinta wani mijin bayan waccan dake kwance yayi hadari duk waenda ke nan bazaki fada ma halin da take ciki bas ai mijinta kinsan abunda kike kam do you know your job anya “dr hafsa tace kiji malama idan baza ki fadamana ba zan shiga what nonsense is this familyn patient nason sanin halin datake ciki kina mana zancan miji bayan gashi a kwance ba lafiya “Wallahi duk maganar nan babu abun fada amma dayake kowa ranshi babu dadi shine zaa sauke kan nurse din ta fahimce su tayi musu uzuri hajajju tayi mitsi mitsi da ido tace ko dai bata da isasassar lahiya ne wannan kiyi manah kin kama baki kin rufe daman su nas din nan babu abunda suka sani ran oum yasake bace kasa magana kawai tayi don bakin haushi ya isheta ma billahi “ nurse din tagyara tsayuwanta tace kuyi hakuri dan Allah ku kwantar da hankalinku in sha Allah he will fine and itama Alhamdulilah cikin bai fita ba yananan kawai ta tsorata ne and mahaifanta bashi da kwari so bed rest muka bata saboda ko yaushe wani abu zai iya faru marar dadi wanda baa fata yanzu mu maida ta postnatal ward anjima kadan zata koma amenity jikinta Alhamdulilah kaman a tare oum da ummi suka sauke wani irin ajiyan zuciya har kana iya ji rufaidarh ma Zama tayi tana fadin Alhamdulilah abby ya jinjina kai yayi ma nurse din godiya kafin shima yazauna din har yanzu tsugunne bata kare musu ba har sai sunji halin da malik din yake kasa hakuri dr usama yayi yajuya yana nufar hanyar x ray room din dasuka nufa da malik abba yaga yanayin sa kawai yasa shi jawo hannunsa yace am sorry Doctor ka kwantar da hankali idan ma abun yafi karfin su zasu fada kuma nan there’re good in sha Allah zasuyi komai abby yace in sha Allah ummi tace tau ni yanzu dan Allah arakani wajan babyn baba tace kiyi hakuri ta huta din kaman yanda nurse din tafada ummi ta girgiza kai tace dan Allah baba kuyi hakuri ba wai gardama zanyi daku ba amma dan Allah ataimaka abarni naje na dubata “ baba ta gyada kai dr hafsa takama hannu ummi suka tafi bakin kofan wajan ga cleaner dake tsaye wajan tana hana shiga wai ba time din shiga bane ana medication ga wasu bayin Allah tsaye anyi ma yar uwarsu cs tahana su shiga su ganta kuma ta farka sai wulakanci take musu “daga dr hafsa har ummi babu wanda ya bi takanta ba dr hafsa tawani hade rai tabude kofan gently suka shige itama cleaner ko yunkurin hana su batayi ba domin taga bama wurin da zata attitude din nasu na cleaners bane “ domin wata fuskar tafi gaban mari (Allah kayi manah arziki □□) suna shiga tana can building din karshe dassuri ummi takarasa wajan da aydarh take an yafa mata zanin asibiti ga karin ruwa ana mata ta dan yamutse fuska bacci kawai take ummi ta zauna gefen gadon ahankali takama hannu aydarh wanda babu cannula kallonta take ko kiftawa babu cike da tausai a cikin malik ma ta taba haka bakaramin wahala tasha ba ahankali ummi tarufe ido tace ubangiji Allah

yaba mijinki lafiya yabaki lafiya yarabaki da abunda kika dauka lafiya Allah yayi muku albarka tasa hannu tashare hawayenta dr hafsa tace Ameen kafin itama kwalla cike a idonta tace dan Allah ummi kukan ya isa haka kuyi hakuri in sha Allah duk zasuji sauki ummi ta gyada kai shiru sukayi daga ita har dr hafsa din fuskan su cike da jimami ga sauran patients duk a kwance wasu ga babies nan a gefensu waenda suka haihu akayi ma cs kenan .sai da suka hada result din duk wasu tests da aka ma malik din kafin sukayi ma su abby bayani “Wallahi tunda abun yafaru basu dan samu peace of mind basai yanzu da aka fada musu halin dayake ciki dr usama ya gyara tsayuwar sa kafin yace bayan frakcer da injury daya samu a kai babu wani abu bayan nan?dr din yace yes sir sai kuma chest hit daya samu wanda Alhamdulilah shi babu wani matsala right now ma he is breathing normal “ dr usama ya gyada kai kafin yakalli dr faisal da dr ibrahim yace well done sons “abby yace tau Alhamdulilah duk sai kowa hankalinsa ya nutsu tunda ba wani babban abu bane yafaru dashi din abba yace aaaa yayah ciwo dai ciwo ne saidai fatan Allah yabashi lafiya oum ta jinjina kai sai yanzu ta dawo hayacinta dr usama yamaida glasses dinsa yana kallon dr ibrahim yace can we cheaks on him Doctor?dr ibrahim ya jinjina kai yace sure sir dr usama yakalli abby yace muje amma dan Allah ku hakura da kukan nan haka nan zamu shiga wurinsa baya son hayaniya kuyi hakuri dan Allah baki daya suka shiga amenity room ne sun cika sa faa su dr umar dasu nurse yasir ma a waje suka tsaya saboda babu wurin daza su tsaya a dakin addua sukayi masa abby yace duk su fita fita sukayi banda abba dakuma dr usama su suna nan aka barsu tare dashi abby yaduba agogon hannunsa ganin karfe 12 saura yace yakamata suje gida sai abar wanda zai kwana wurinshi da kuma wurin aydarh “dr faisal da dr ibrahim aka bari babu yanda rufaidarh batayi ba ummi ta tafi gida zasu zauna ita da dr hafsa wurin aydarh cewa tayi aaaa bazaayi rashin hankalin nan ba amarya ce ita abby yace kwarai dagaske da ummi da dr hafsa aka bari sauran suka tafi maryam har yanzu taki daina hawaye “ dazzy ne da dr umar suka dawo suka kawo yan asibitin duk wani abunda zaa bukata kafin su koma “su ummi na zaune sun kasa sun tsare ita da dr hafsa tsakanin dakin da malik yake kwance da inda aydarh take ummi tayi zarya yakai sau goma bayan tafiyar su abba takasa zama duk yanda dr ibrahim yace ta hakura ta zauna amma inaaaaa bata jiba kuma daga aydarh har malik din babu wanda ya farka “wajan karfe daya da rabi nadare aydarh tafara bude idonta ahankali ahankali kanta ciwo yake ga idon sun mata nauyi celling din dakin tabi dakallo kafin ahankali tarufe idonta tana recalling yanayin dataga malik kafin tayi fainting wani kalan zabura tayi oh my goodness ‘ta tashi zaune dasauri ummi tarungume ta aydarh tafashe dawani irin kuka wanda dole kabata tausayi kira take ummi where

is he?ina sir yake you should answer me please miyafaru dashi miya samesa inalilahi waina illahil rajiun nabani nashiga uku ku taimaka kuce masa kar yayi ciwo he should pity me Wallahi ba wasa nake masa ba I love him dagaske am done nabani kwalla suka cika ma ummi ido tasa aydarh sosai a jikinta aydarh kam sai kuka take kaman ranta zaya fita gashi bata da karfi gawani irin zafi datake ji a maranta “ummi tafara patting bayanta tace ya isa haka baby ya isa kiyi hakuri baki da lafiya fa kidaina wannan kukan stop shaking yourself har haka baby baki da lafiya kina bukatar hutu aydarh tasake fashewa da kuka tace a fadamun miyasamesa dan Allah auntie dasauri dr hafsa takama hannun aydarh tace ki nutsu first idan baki nutsu ba babu wanda zai fada miki dasauri tabar jikin ummi tafizge cannula hannunta ummi tarufe ido ganin abunda aydarh tayi Wallahi ji tayi har cikin ranta ita kawai tasan halin datake ciki gawannan ciwon ga tashin hankali dasauri tasa hannu tana share hawayenta tace to na nutsu Wallahi nayi shiru nadai ki fadamun dr hafsat ace he has an accident but not that much serious yadan samu injury a kansa kawai yanzu haka ma bai jima da fita daga dakin nan ba yazo kina bacci tau shima yagaji hidiman nan gashi anyi masa allurar bacci ya kwanta “kema ki kwantar da hankalinki ki huta idan Allah yakaimu gobe sai kiduba sa nama san shi zai fara zuwa duba ki in sha Allah aydarh tasake fashewa da kuka tace why not now auntie dan Allah nidai a kaini na duba shi he is all what I have shima nasan he wanted to see me Ina so nafada masa kar yasake ciwo bana so ‘ dr hafsa tace yanzu fa nafada miki yace ki huta shima zaiyi bacci dasafe kwa hadu sai yafi ma tunda yanzu anyi masa allura idan kuma bakya son yayi baccin ya warke shknn aie ki tashi muje ta girgiza kai tana goge hawayenta tace no nahakura auntie kar yace banji maganar sa ba ai dasafen zai shigo koh?dr hafsa ta gyada kai tace yes in sha Allah baki daya aydarh tamanta da ummi dake wajan baki daya hankalinta da kanta da zuciyarta suna kan malik dr hafsa ta lallaba ta mayar mata da cannula “kafin ummi ta kwantar da ita ta rufa mata new expensive duvets din da rufaidarh tadako kala daya kwara biyu tabasu dazzy suka kawo ita kasancewan alluran baccin da akayi mata bai saketa ba yasata komawa baccin ‘ ummi tayi murmushi tana goge hawayen ta tace Allah yacigaba da baku zaman lafiya dr hafsa tace Ameen Ameen ummi “ ta bangaran malik kuma bakaramin hutawa daman ake bukatar yayi ba shiyasa har yanzu bai farka bas ai ajiyan zuciya yake saukewa ahankali ahankali dr faisal yakalli dr ibrahim yace Allah mai yarda yaso yanzu yanzu idan yaga dama sai yadauki ranka baki daya Allah yasa mucika da kyau da imani kaduba fa kwata kwata da fitarsa da faruwar hakan bai fi 30mins ba ,dr ibrahim yace Ameen Ameen kafin ya maida dubansa akan malik din yana kallonsa ya tausaya mashi ba tausan wasa

bayana daukar malik kaman uwa dayauba daya suka hada bawai abokantaka ba “ CMD dakansa yashigo dakin yanzu yaduba Komai kafin yarubuta wani magani yabasu “yace dasafe a siyo su sake duba daurin da akayi mashi ganin komai yayi Alhamdulilah.

Kiran sallan farko yasaka sa motsa hannunsa kadan kan idon dr ibrahim ahankali yabude manya manya idonsa dasukayi ja sosai yafara tari ciki ciki dasauri dr ibrahim yamike yakarasa gaban gadon ganin idonsa a bude yasa shi yamishi murmushi yace sannu yallabai “malik ya jinjina kai cike da karfin hali tsaf yasan abunda yafaru dashi domin karan keyyyyyyyyyyyy din nan nadawo masa a kunne duba drip din dr ibrahim yayi ganin yama kare yasa shi cire masa ‘ganin lokacin salla ma yayi kokarin tashi zaune yake dr ibrahim yace hold on yallabai relax first malik ya kwanta yadaina attempting tashi sai kallon hannunsa dake nade yake ga uban bandage kuma kai “ dr faisal yabude idonsa don bacci ne ya dauke sa daga zaunan dayake a kujera yamike zaune yace Alhamdulilah Doctor ka farka malik ya jinjina kai kafin dr faisal yace how are you feeling now?ahankali ya motsa bakinsa yace Alhamdulilah atare suka hada baki wurin fadin Masha Allah dr faisal yace Allah yatashi kafadunka “malik ya gyada kai alaman Ameen ‘knocking sukaji a bakin kofa malik yazuba kofan ido magana yake son yamusu amma kwata kwata wahala take mashi definitely yasan ummi tashiga wani hali lokacin da taji bashida lafiya tau what about his wife duk suna ina?dr faisal ne yabude ganin ummi tsaye bakin kofa da alama kwata kwata batayi bacci ba shigowa tayi dr faisal yarufe suka dinga jera mata sannu dr ibrahim yace ummi da ankai ki gida su yaran sai su zauna tunda jikinsu Alhamdulilah dasauki ummi tayi murmushin karfin hali tace babu komai yan albarka kafin takarasa gaban gadon ta zauna very close to him hannu tadaura tarike hannunsa marar ciwo tayi shiru addua take tofa masa kusan 15 mins kafin tabude baki tace ya jikinsa dr ibrahim yace ah jiki Alhamdulilah ummi dasauki sosai ummi tamaida kallonta ga malik tace ya jikinka yayi murmushin dayayi masa kyau sosai yace Alhamdulilah ummi ummi tace Allah yamaka albarka yace Ameen dr ibrahim naso ya jikin aydarh so baya son yayi magana malik ya fahimce abunda yafaru da ita “ ummi ta mike tace ibrahim ku shiga dashi ayi masa alwalla kuje masallaci zan dawo yanzu dr faisal yamike yana bude mata kofa Yace in sha Allah “fita tayi takoma dakin da aka mayar da aydarh domin ummi cewa tayi baza su kwana wurin ba saboda ita yarinyar “ amenity aka mayar dasu lokacin da tashiga aydarh tafarka dr hafsa ta jinginar da pillow ta mata relaxing kanta sama idon a rufe ta daura hannunta a cikinta while her eyes are close, ummi tace sannu hafsa ‘dr hafsa dake kan pray mat tace yauwa sannunku ummi idan sun zo

anjima sai a mayar dake gida ki huta “ummi tace lafiya lau anan din ma hafsa, takarasa kusa da aydarh tace sannu baby aydarh tabude idonta tayi kasa da kai ahankali tace dasauki ummi muryanta can kasa irin na wanda dai yashiga wahalar ciwo “ummi tace Allah yasawwake toilet ummi ta wuce tayi alwalla tazo ta tayar da salla. Kaman kwai haka ta dinga treating aydarh saboda bed rest ko da zataje toilet dr hafsa ta kaita har suka fito lokacin gari yafara haske sai ga nurse din tashigo hannunta rike da bp box “gaisawa sukayi da su ummi tanayi masu ya mai jiki suka amsa ta karasawa tayi kusa da aydarh sai kallonta take ko dauke ido babu ai yarinyar nan ce da mijinta dasuka dinga trending inda yayi mata waka wajan kamu sai yanzu ma tagane su aie jiya hadda amaryar sake shiga hankalinta tayi ganin su a asibitin ta sake kallon aydarh wacce idonta ke rufe tace sannu ya jikinki aydarh tabude idonta kadan tana jinjina kai tace fine ‘nurse din tace Allah yabaki lafiya aydarh ta jinjina kaii “bp dinta ta auna kafin ta waiwayo takalli ummi tace dan Allah idan gari ya waye a samar mata tea mai zafi tasha ummi tace Alright anan ma ankawo kettle da kayan shayin let me makes it for her yanzu ‘nurse din ta jinjina kai tace tau hakan ma yayi aranta take mamakin komai na masu kudi yan bako is different Allahu akbar! Dasauri ummi tamike ta bude bottle water tasake dauraye kettle din kafin tazuba bottle biyu a ciki ta jona kettle din strawberry lipton tasaka sai liquid ginger dake cikin wani classy rubber na campany “ few seconds sukayi cup din daaka kawo ummi ta dauraye kafin tazuba ruwan zafin a ciki tarufe saboda yadan sha kadan brush din aydarh tadauko dasu dr umar suka kawo ta saka Tooth cleaner sama takama ta dr hafsa tace dan Allah ummi kibari zan kaita please ummi ta gyada kai tana murmushi kadan dr hafsa takama aydarh gently suka karasa bayin tayi mata brush din suka fito sai sannu suke mata zata kwanta ummi tace daure baby ki zauna sai ki sha shayin ki gasa cikinki “ Aydarh tace ah’ah ummi nakoshi tafada ahankali kwalla cike a idonta ummi ta girgiza kai tace aaaaa baby daure ki sha mai ciki baya zama da yunwa kaman kaman ke yanzu a stage din dakike kai we all have to be very careful kinji baby aydarh tayi kasa dakai ahankali tace to”Ummi da kanta tayi feeding aydarh shayin dakyar aka samu tasha half cup shima tanayi tana goge hawayenta “ummi takama hannunta tace sannu baby kukan nan ya isa haka kidaina kukan bana so aydarh tashare sauran hawayen tace in sha Allah “ knocking akayi dr hafsa tabude dr faisal ne tsaye yasa hannu a aljihu kansa kasa kaman wani marar gaskia Allah “ kasa tayi da kanta ahankali tace ina kwana yace ya mai jiki tace Alhamdulilah tafada tana bashi hanya yashigo yasake gaishe da ummi kafin yama. Aydarh ya jiki tace Alhamdulilah dr faisal yashafa kansa kafin yace ummi Ko Doctor zata raka tane wajan shi? Ummi tayi shiru kafin tace tau faisal juyawa yayi

ya tafi hijab dr hafsa tasaka mata “ ummi tace abi hankali baby don’t rush hafsa ki nuna mata tafiyan dan Allah dr hafsa tace in sha Allahu ummi duk zan mata bayani ita dai aydarh kanta akasa ‘dr hafsa takama ta gently suka fita dakin da malik yake hafsa tayi knocking dr ibrahim yabude suka shiga ciki yana zaune ga mug a dayan hannunsa tunda tashigo yake kallonta ko kiftawa babu itama shi take kallo ahankali dr hafsa takaraso da ita kusa dashi ta zaunan da ita gefen gadon dr ibrahim yace bara mu basu wuri dr hafsa ta gyada kai “ fita sukayi dr faisal yarufu musu kofan suna fita aydarh ta matsa kusa dashi tafashe da kuka mug din hannunsa ya ajiye yasa hannu yakamo ta jikinsa yasaka ta “ya kwantar da kanta a board chest dinsa yace shshshsh ya isa stop crying tadago tace miyasa zakayi ciwo dasauri yasa hannu yarufe mata baki yace karki sabu baby girl kinga am fine ta girgiza kai tace you are not fine sir kaga ga bandage a kanka ga shi a hannunka “yace duk babu zafi kiyi shiru bakida lafiya ne naga hafsa ta kamaki are you sick? Tace dana kanka ne in suchs condition shine nayi fainting “ malik yayi shiru wani irin tausayinta yaji gabansa yafadi tayi fainting da karamin ciki inalilahi waina illahil rajiun zuciyarsa ta tsinke shi mijine kuma uban ne baya son yabar bad think din dayake zuciyarsa yayi tasiri muryarsa na shaking yace mamana tadago ido ahankali yace what about the baby aydarh tarufe ido tace ummi tace sun bani bed rest sauke ajiyan zuciya yayi Alhamdulilah hakan na nufin cikin na nan! Yace are you feeling pain har yanzu? Tagyada kai tace amma nidai bana son kana ciwo dan Allah yace in sha Allah I promise you I will be fine yafada yana murmushi ahankali tace I LOVE YOU MINE TILL DEATH!wallahi idan tafada haka jiyake anyi masa wani irin zabura a zuciyarsa yace I LOVE YOU TOO EVE CWRY kadan tace shine ka tambayi your baby bandani aransa yace sarkin kishi kenan ! Yace kiyi hakuri tau ai duk dayane you all are my babies you know ai tace uhm yace bana son rigima baby kinga am sick kema haka zaki kara mun ciwo ne? tagirgiza kai dasauri yace tau stop it idan bahaka ba ummi prison zatayi reporting dina ace an baki bed rest kumaa dasauri tarufe masa baki tace stop it yayi murmushi tayi lamo a kirjinsa “wajan 8 daidai su aysha suka zo da breakfast abby ne yace dan Allah ayi hakuri adaina cika asibitin saboda hankalin mutane duk kansu yake dawowa kuma kasancewan abba is very popular bazaa barsu su huta ba bakin mutane ya isa koda suka je kai breakfast kawai sukayi suka juyo gida dr usama ne sai rufaidarh kawai aka bari “ still kuma waenda suka kwana jiya na nan Tunda aka daura auran su jiya babu wani magana sosai daya shiga tsakanin su yanzun ma fitowa rufaidarh tayi zata shiga dakin da aydarh take zata dauki spoon “ dr usama na nan tsaye a reception yana making call yana ganinta yayi murmushi tasaka farin abaya dal mai flower gold jiki lallan hannuta yasake duhu ga

bangles na zinari da rings dasukayi ma hannun kyau bata saka inner cap ba tayi rolling veil din hijab din “tana zuwa tayi kasa da kai zata wuce sa dasauri yasa hannu yajawota tafirgeta Don batayi tunani ba sam ‘ kama hannunta yayi yashige da ita wani office da aka shimfida carpet da alama ma manya staffs ke hutawa a wajan the place is very quiet and clean hadda kamshin gbc “ yarufu kofan tabude ido tana kallonsa a rude tace minene haka zan kai spoon fa uncle tafada tana marairaicewa “ yace I just wanted to congratulates you andaura aure Allah yasa alkhairi yakawo yara nagari rufaidarh ta mishi wani kala da ido tace awwww thank you and same to you dear yace anyway baza mu tafi yanxu ba in sha Allah sai after anyi discharging dinsu daga asibiti rufaidarh tayi kasa da kai tace Allah yakaimu lafiya yace Ameen yace kinyi kyau tarufe fuska tace thank you yace you’re always welcome my darh tace can I go? Ya girgiza kai yace ai bamu gaisa ba tace bayan na gaishe ka ka manta yace is this how to greet your husband? Tayi kasa da kaii tana turo baki tace tau ai ni ban san yanda zanyi bayace oya yafada yana bude mata hannu alaman tayi hugging dinsa “ tace oh no yace sai fa kinyi tagirgiza masa kai tace no please sir not now dan Allah likita yace wannan umarni ne from your husband batada wani way out but to hugs him gently ta shiga jikinsa Allahu akbar tunda Allah ya halicce ta this is the first time da wani da namiji ya rungumeta wani irin pleasure taji tunda cikin brain dinta har kafanta tasauke ajiyan zuciya murmushi yayi shima dr usama har ya manta when last dayayi hugging mace tun kafin matarsa ta rasu “ sai yau ji tayi kafanta yakasa daukanta yalura da hakan yasa shi kamata suka zauna bisa carpet din gently yayi grabbing lips dinta yafara mata wani french kiss ji tayi kaman zatayi mi Allahu! Wallahi kaman wata yar yarinya tafashe masa da kuka “ganin yafara shafo boobs din a rude yasake ta shi kansa bai san abunda yazo kansa ba she cannot control his urge kanta yayi mistake cus here is not the right time to do suchs kukan take yace shshsh am sorry princess kiyi hakuri kinji tagyada mashi kai yafito da wani clean handkerchief yashare mata kukan yace kiyi shiru kinji bazan sake ba “ta girgiza masa kai tace kayi hakuri please ka yafemun tahada both her two hands alaman yayi hakuri ya girgiza kai yace no love kin fi ni gaskia yakama hannunta suka fita dakin da aydarh take suka shiga itace kawai wurin tana bacc isai ummi dake toilet tana wanke ma aydarh kayan data cire dr usama yaduba yanayin saukan drip din da breath dinta kafin yakalli rufaidarh yace zaki dauki abu ne? Tace eh yace dauka naraka ki spoon din tadauka sai bottle water suka fita “.YACE ai kene kawai yakamata ki ganni bas uba tayi kasa da kai tace to “yace zaki iya kamani?ta gyada mai kai yamika mata hannunsa tarike da taimakon ta duk dabawani karfin kirki bane da ita ta kamasa “tasa hannunsa a shoulder dinsa suka shiga toilet din

“ ta zaunar dashi kan sit “ kafin ta tara ruwan zafi a bucket shidai sai kallonta yake gani yake kaman bai kyauta ba itama fa bata da lafiya daurewa kawai take shikuma baya son yayi loosing wannan moment din “ sai binta yake da kallo yace bayan tagama tayi kasa dakai kafin tasa hannu ahankali tadauki towel tafara goge masa jiki har cikin ransa yake jin dadi banda saka mata albarka babu abunda yakeyi a ransa tagama tadauki brush dinsa tayi masa brush bata lura ba tadan shafi hannunsa mai ciwon yace ashhhhh dasauri tajuyo tana bude ido duk tarude tace nataba maka kaji zafi am so sorry sir ban lura ba kayi hakuri dazafi I should call the doctors? Malik yayi murmushi yace relax madam “ babu wani zafi kuma haka zaki kira Doctors din su ganni?tayi kasa da kai kunya takamata bayan tagama takama sa suka koma dakin kan gadon ya zauna yana kallonta ganin ta yamutsa fuska “ yace kin gaji sannu cuddle bug ta girgiza mashi kai “ rezoner leafer tasha fasa kasancewan bashida karfi kamshin sa tashafa masa vaseline gently take treating dinsa kaman wani baby tahada masa tea kafin tasaka masa chips and egg ahankali tafara feeding dinsa shidai sai kallonta yake tass yasha tea din dankalin kuma bai ci dayawa ba “ drugs dinsa tabasa “ ahankali yace Allah miki albarka matana! Tayi murmushi tace Ameen mijina “yace I love you tarufe fuska tace har bazan iya counting sau nawa kafada ba yau “yace I cannot get enough of saying it tace you try bude kofan akayi ummi ta shigo duk da malik baida lafiya kuma har cikin ranta taji dadin yanda aydarh keyi mashi amma ita ma fa bata da lafiya ummi ta kallesa tace hala babu wanda yafada maka yarinyar nan na on bed rest kake saka ta wannan aikin malik yayi shiru aydarh tayi kasa da kai ummi tace su su ibrahim din miye amfanin su inda ace lafiya lau take wannan ita ke da hakki amma bata da lafiya ta kanta take ita shknn a aikinka zata kare? Babana?malik dai yayi shiru ummi tace baby hafsa batayi miki bayani ba? aydarh tayi kasa da kai tace tamun ummi ta hade rai tace kuma shine bakya tausan kanki baki san naki rashin lafiya yafi nashi ba baby?aydarh dai ba tace komai ba ummi tace taho muje ki huta ga su baba can zasu dubaki malik yashafa kai yace ummiiiiiiiiiiii ummi tace ummi miye kasan bana son rashin adalci abdool kabarmun yarinya ta huta kana jina idan kana son wani abu bara su ibrahim su shigo ina can ina jinya ashe ita tana nan tana jinyar ka kuma kai kaman ba Doctor ba idan cikin ke baka so kafada kawa isai mu sani yau zan saka ayi discharging dinta muje gida tahuta kai sai ka warke anan din yace ummi nima yau zamu tafi kinga hannun ne kawa isai ciwon a goshi shima bawani ciwo bane ummi tace oh yanzu kasan haka kenan ita da kake langwabewa kana tayar mata da hankali baka fada mata ba wani ciwo bane kenan ?kanta kasa tana.

Idan kasamu maman miji kaman ummi you are very lucky idan watace kan danta said ai duk wahalar dazaki ki sha she didn't bother care amma yanzu ita kaman ko yaushe bayan matan dan nata take ❤ kuma gaskia ne ciwon malik dana aydarh ba daya bane ita nata barazanar rai ake shikam Alhamdulilah tunda an gano bawani ciwo yaji sosai banda karyar a hannu

Littafin mu nata bankwana

musu magana daman bana following kowa a matan takallesa ya gyada mata mariam ce tayi knocking glass din side din aydarh bude mata tayi tamiko mata wayan da handbag din sai warmer pepper chicken tace gashi inji ummi aydarh ta marairaice fuska tace wai dagaske inji ummi mariam ta kwashe da dariya tace wallahi har nasamu nadauki hand bag din da wayar “nafito compound sai ga ummi tafito ta hanyar kitchen din baya ko magana bata mun bat ace gashi nakawo nace kun kyauta malik yace saka a back sit bude motar mariam tayi tasaka tamusu waving hannu “malik yatayar da mota yaja suka tafi tunda suka hau hanya tayi shiru batasake magana ba “tunanin ummi kawai take duk kunya yakamata pass eleven yanzu ya tsaya yasiyan musu fruit yayi parking bakin mall suka shiga tare yau kaman yazare yadinga kwasan mata perfumes kala da iri duk fa abunda zai siyan mata tanada shi amma babu yarda ta iya sai data barshi ya siya chocolate yadaukan ta yan kadan baya son tasha zagi “yau soyayya sabuwa as usually tare sukayi gyaran gidan da girki. Ita ta taya shi hada files din wajan aiki bayan magrib yana shigowa daga masallaci tana nan zaune parking taci ubansu wani Egypt abaya red anyi mashi kwalliya da black lace wallahi abayan yayi kyau anshafa powder da kajal ga red lipgloss daya ma dan bakin kyau “ tayi kyau kaman kasace ta ka gudu anyi parking long hair dinta can kasa yasha gyara babu hula ma akanta “sai wasu fashionate earrings da necklace black sai stone din ciki red foreign necklace ake magana kalan na turawa tayi wani kalan azaban kyau tabarakallah ga wani kamshi dake fita daga jikinta yana shigowa ta amsa masa sallama idonsa kanta yazauna kusa da ita yakasa dauke ido kasa tayi dakai tace muje kaci abinci kaman wani yaro tagama hannunsa sukayi dining ita taja masa kujera ya zauna kafin tayi serving dinsa shape pasta suka dafa sai vegetable stew da kayan ciki “ da fresh juice din pineapple din dasukayi ansaka ice cubes kadan yayi sanyi daidai daidai cikin wani hadaddan glass jug mai kyau “ita tayi feeding dinsu har suka gama kafin ya tashi yadauko mata maganinta tasha isha’I aka kira yamike zuwa masallaci yace taje tayi sallarh tayi rolling veil dinta su abby zasuje dasu oum suma bankwana “tace masa to ‘tace yayah zamuje abujan? Yagyada mata kai yace I have already booked a flight for us tomorrow morning in sha Allah daga abujan zamu bi flight to Washington “ta gyada masa kai “ masallaci yawuce itama ta haye sama don yi Sallarh ta shirya.

Yau dai oum cire kunya tayi tsaf tafada wa aydarh yanda zatayi idan cikin yakarasa tsofa “dakuma yanda zata kula da kanta da yanda zatayi idan tafara jin alama nakuda “ rufaidarh kam tahada mata kaf wani maganin data karbo musu ita da aydarh daga sudan “ummi ma bata magunguna “

bankwana sukayi dasu abba dasu baba su hajjaju da inna kam antafi kano a jirgi yau lokacin dasuka je gida dare yayi karasa hada kayan su tayi suka kwanta “sai da ya tabbatar da koina is safe yabar ma mai gadin enough kudi a wurinsa driver gidan abby yakaisu airport saboda yadawo da motar gida har makullin motar yabarwa “ mai gadin wai ko zaiyi amfani da motar in case of emergency ko rashin lafiya haka tunda yanada mata harda yara biyu “ flight din safe suka bi zuwa abuja. A gidan amarya dr hafsa dr faisal tun safe yake bada hakuri da ban baki amma inaa ko fuska bata sakar mashi “sam batayi tunanin abun yakai haka ba at that time tayi tunanin kashe ta kawai yake so yayi ne “shidai sai bi yake ana mai bori “ su rabiah kam da nr yasir kusan halinsu daya duk yan rawar kai ne sai zuba show dinsu suke atare har anfara couples picture a parlor da a motar ana posting su ga newly wedded “ haka doctors da nurses maza da mata suka dinga zuwa amma ina said ai gidansu rabiah da nr yasir suke shiga dr faisal yaki bude gidansa saboda halin dayaga princess din ciki wallahi raki gareta ko dan she is too classy aji ake masa da alama “A abuja kam yan uwan dazzy duk sun zo yawancin su age mates ne da aysha masu mugun kirki sai nan nan suke da da aysha kowa cikin su sai bakin kokarin shi yake da ita shi dazzy bai angwance ba “aysharsa is on mp “ , gidansu yayi kyau ita da halime bana wasa ba furnitures din su duk kala daya “ ne su hudun “ Halime kam daga ita sai dr umar familyn shi na jalingo halime tayi kokari sosai da sosai kaman dai rabiah wallahi wani irin so dr umar ke mata da bawani Sosai take son sa ba amma daga jiya zuwa yau yasamu wani special position in her heart tana son mijinta “wurin 12:00pm daidai flight dinsu yayi landing a airport cab yasamar musu yakai su da kayansu hotel yace bazasu kwana gidan sirikai bai ta dai aydarh ko ma ina zasu kwana bata dam uba burinta yacika tunda dai anzo abuja itama mariam tana school jiya tadawo “ sai dasukayi wanka suka huta malik yamusu order abinci shi yaci ita kadan ma tacit ace masa amai takeji haka yasa said ai black tea tasha kawai “ gidan halime zasu fara zuwa dr umar din ne yazo yadauki su daga hotel din sukayi hugging juna da malik yaji dadin zuwansu wallahi Sosai da sosai aie halime naganin aydarh tayi wani uban tsalle tayi hugging dinta har sai da malik yamata tsawa kafin aydarh dai sai murmushi take itama she is very happy wallahi data ga halime din kwana biyu kawa isai taga halime ta chanza mata tana lura da tafiyan halime wallahi sai ta tuna time din ta itama har tausai halime ta bata amma da alama ita bata wahala ba kaman ita ko dayake her husband is different “abubuwa kala da iri halime tacigaba da kawo musu aydarh ta lura daga halime har dr umar halinsu guda duk comedians ne “dayan parlor suka koma aka aydarh da malik wannan wai su ci abinci “ malik yakalli aydarh yace kin sa mun zo gidan amarya koh?tayi wani kala da

ido tazo kusa dashi tace kai aie baka ma bari anyi hakan bas ai kawai aka ganni da ciki “malik yasa hannu yarufe bakinsa yace lahhh subhanallah karki mun sharri nidai “ina kinkai one year kina kada mun ass da nan yayi pointing boobs dinta dasauri tajawo sa hannu tarufe masa baki tace wai miye haka a gidan mutane “yace nayi shiru tace is better dai “tace kuma saura karka daina ka cigaba wata rana zaka fada wurin dazaka saka duk muji kunya yace aie nadaina ma tace to ka ci abinci “nan ma kadan kadan taci chops din shima haka sun kai 3hrs a gidan duk da malik bai so haka ba amma matanshi naso shiyasa suka jima bundle biyu yaba halime na 1k dasuka tashi tafiya tarasa mi zata bama aydarh tabude cikin akwatin ta tafito da grand super mai kyau purple and maroon da mayafinta sabbi dal tasaka ma aydarh a paper bag mai kyau “tabata dakyar da karba shima sai da umar yahada malik da Allah kafin yasa hannu yakarba kaman dazu yanzu ma dr umar ne yakai su har gidan dazzy aysha dabatayi expecting dins uba wallahi hada malik din da aydarh tayi baki daya tayi hugging maalik yabubuga bayan aysha dazzy da malik kam bawani surukunta “ suka kama juna kaman dai yanda suka saba “ a parlor dazzy da malik sai dr umar suka zauna aysha takawo musu abinci hadda drinks komai mai kyau na yan gayu irin na gidan amarya “aydarh na dakin aysha “aysha tashigo tazauna tace wallahi banyi tunanin zaku zo ba aydarh tayi murmushi tace yace mu zo muyi muku bankwana aysha tace wallahi naji dadi bana wasa ba yaushe zaku tafi? Aydarh tace gobe in sha Allah aysha tace Allah yakaimu sai yaushe kenan idan kuka tafi? Aydarh ta cigaba dawasa da yatsun hannunta tace uhm yace sai suna aysha tace kai haba wai nufin sh isai bayan kin haihu auntie aydarh?aydarh tagyada mata aysha wai ai dayake nan da 3 to 4 months ne koh Allah yakaimu lafiya “aydarh tace Ameen “ aysha tace yauwa auntie aydarh daman ina so inyi tambaya so ban san wanda zan tambaya ba dazan kiraki waya sai gashi ma kinzo “Aydarh tace ayya “aysha tace kinga auntie aydarh yanzu mp nake aydarh dai tayi shiru tana sauraron aysha “aysha tace tau idan nagama ni zan fada masa ne?ba ma wannan bas hi wannan maganin ya zanyi amfani dashi su halime duk sun sha dayake ba mp suke ba ni oum tace nabari sai nagama nasha ya zanyi kenan wallahi tunda aysha tafara magana aydarh taji wani kala kunyar ayshar take ji amma yata iya itama mom ta koya mata yanda ake using dashi without having eye contact da aysha tamata bayani in brief duk da aysha ta fahimta amma sai dataji mamakin aydarh tau miye na kunya ahhh wannan yarinyar aysha ta kwashe ta mayar duk aydarh tayi shiru saboda kunya “aysha tace auntie ke gyaran ma mi zakiyi fisabillahi “ wannan ko saboda jikinki wallahi yayah bai damuwa dawani gyara aydarh dai tayi dan murmushi ta lura aysha so take dole sai anyi maganar “ aydarh tayi kasa da murya tace kwara dai agyara

addarh aysha tayi dan dariya tace balle naki mijin nadaban ne “ mikewa aydarh tayi tace naji ana kiran magrib ina toilet aysha ta girgiza kai har toilet ta raka aydarh tanuna mata kafin ta shiga tayi alwalla,sun fito parlor tareda aysha sai ga sun dawo sallarh bankwana sukayi malik yabama aysha kudi kaman yanda yaba halime har bakin gate suka musu rakiya kafin dr umar yakai su har can hotel din sukayi sallama yayi godiya yawuce gida

FOUR MONTHS LATER.

Ya dinga kallonta ko dauke ido babu “sai tura basket din take duk lokacin da zasu zo siyayyan kayan babies shi ke zaba koi ya zaba ma batayi ba har wanda ba na babies din ma ba dauka take duk abunda zasu siya “unisex yake siya kuma sai yasiya na mace danamiji daban kayan babies din dasuka siya kaman dai malik baya son kudin sa yanda kuka san zaya bude wani dankareran babies wears a Washington “zuwa yanzu aydarh dai tafara ganin dagaske ake don sun gama siyan komai gashi yanzu kusan kullun idan zasu waya ko vedio call da ummi lallashi ne da kwantar mata da hankali take watan haihuwan ta yakama harta week din da EDD dinta zai cika sun shiga yanzu ma suna zaune a gida yana aiki a system yaga tayi lamo tashige cikin sofa sai kallon wuri daya take baya son yaga tana wannan tunanin duk ta riga ta tsorata da haihuwar ne wallahi mugun tausan ta yake shi duk tunanin shi da lokacin haihuwar yayi kawai suje ya mata aiki afitar da babies din subul da baka yayi yafada wa ummi ta dinga masa fada tace kar ya kuskura a mata c.s cire yaran yabari tahaihu da kanta duk tausayin datake basa kenan “gently yarufe system din yakama hannunta ta kallesa ya girgiza mata kai yace what’s wrong mamana ta girgiza masa kai yace a ina kike Jin ciwo tagirgiza masa kai yace kin gaji ne?sai ga hawaye sharrr shiru yayi “yacigaba da murza mata hannu yace minene tasa right dinta ta goge hawayen “ kallonta yake kaman yacinye ta tasake wani kiba wallahi tayi daya da rabin da kana ganin cikin kasan ya isa haihuwa “ tayi wani haske duk tazama wani shiru shiru yanzu sai yayi five minutes yana magana daga erh sai uhm idan yamatsa mata ma tasa mai kuka haka ake zaman yanzu shi ke duk wani gyaran gida da wankin toilet but har yanzu maganar wankin singlet boxers ko yatafi wajan aiki idan yahanata sai tayi girki ma ita keyi tana da karfin hali sosai wallahi dakyar yasamu CEO dinsu ya yarda yadauki hutu saboda yanayinta yanzu bata iya bin sa wajan aikin bata ma son zuwa ita gani take kawai watan mutuwar ne ya kusa tsayawa “yanda cikin yayi girma har daga mata hankali yake wani babban mall suka je ita dashi a wani dan karamin yanke outside Washington shima aiki aka tura sa suka tafi tare a can mall din suka siya maternity gown kala kala sunyi kawai take sakawa

basa ta takura ta “daidai bra duk kunyar ta yanzu bata sakawa “ko motsi tayi sai ya tambayeta tausan kanta take ga kuma tausan mijinta “sakata yayi ta shirya suka fita rasa inda zasuje yayi shiyasa suka je babies wears din duk da daki guda ne a gidan banda kayan jarirai da gadon su hatta keke dai malik yasiya (lastest faazaaa 😂kenan yah hanif din jewel) kyau tayi masa yanzu din datake tura basket din sai yashiga yafara mata vedio har takara so kusa dashi tasa hannu tacire face mask din fuskarta yayi murmushi yace sannu tagyada mai kyau bottle water dake hannunsa yabude yakamata suka zauna ya bata kadan tasha ta marairaice fuska tace am tired jellybean am hungry ma self jellybean “yayi wani kala fuska yace oh sorry yakai hannunsa kan cikinta kallonsa tayi kafin tayi placing nata very soft and beautiful hannun a nasa yace hey pikins kudaina sakamun pina cola saurin jin yunwa fa gashi kuna gajiyar mun da mata “she can’t hold it but to smile tayi masa flashing wani hadaddan smile tace dan Allah muje gida naci abinci ya gyada kai dasauri shi yatura basket din yakai ya biya aka kai masa har cikin taxi kafin yadawo yakamata suka fice daga wurin suna isa gida a parlor tazauna tacire veil dinta kanta calaba ne kwara four tasa ribbon tayi parking dinsa kasan keya “ shi yamata calaban da kansa irin dai nasu kitson maza “kitchen yashiga dasauri sauri yahada mata oat yakawo mata yakoma yayi slices din apple da grape yakawo mata “cikin nan da ya tsofa duk sai ya mayar da ita wata acici haka cikin dare zata tashe sa wai zata ci abinci dasaurin sa zai fito yakawo mata shiyasa baya yarda ma yazauna gidan babu wani abu dazata ci emergence “sai data cinye komai tass anan parlor ta kwanta sai bacci tsayawa yayi akanta ya kama waist dinsa yana murmushi ya girgiza kai kayan dasuka siyo ya dauka yashige dakin dasu kafin yadawo idan tana bacci baya tashin ta har yasaba ma da daukarta duk kiban datayi ga ciki amma bama yajin nauyin ta don bawai tayi nauyin bane daf yadauki abunsa kaman baby yana kallon da wani kalan smile a fuskanshi irin murmushin nan na shauki kalan murmushi nan na zallan so irin murmushi girmamawa da tausayi “a duk seconds na numfashinsa kara masa son aydarh ake duk wani movements dinsa na rana son take karowa a ransa da ma jikinsa kaman wanda yadauki babyn dabaa so yafarka haka yakeyi kaman wanda yadauki egg haka yakaita bedroom dinsu ya kwantar da ita gently yasa duvet yarufe ta yaja hancinta dakaman an kara masa tsawo da kyau kafin yafita so yake yayi sauri yakarasa aikin dayake a system kafin ta tashi baccin “yana dawowa yaga ana kiransa audio call dayake a parlor yabar wayan yana dubawa yaga ummi ce dasauri yadauka sai dasuka gaisa da damuwa take tambayar aydarh yace tana bacci yace ummi tasauke ajiyan zuciya tace har yanzu Abdool nakudar shiru?malik yayi dan murmushi yace ku kwantar da hankalin ku ummi daga ita har babies din duk suna cikin

koshin lafiya ko jiya munje asibiti kuma da kaina na dubata ummi tayi shiru kafin tace Alhamdulilah tau ko kila mai yin nakudar baki dayace shidai malik murmushi kawai yayi duk tadamu ummi wallahi tasake cewa Abdool nidai idan bazaka kawo ta ba koni nazoo ne dan Allah “malik yace hajiya ummiiiii ummi tace Abdool yace ki kwantar da hankalinki babu komai fa in sha Allah kibari tana sauka zaku taho kidaina daga hankalinki in sha Allah zata sauka lafiya ummi tasauke ajiyan zuciya tace tau ubangiji Allah yasa a kula dan Allah malik ka kula karamar yarinya ce babu abunda tasani kasamu doctor ko ma nurse babbar mace haka wacce ta jima a aikin dan Allah ta dinga kula da ita kaga babu wani babba malik yagyada kai yace in sha Allah ummi “ummi tace Allah yayi muku albarka Allah yaraba su lafiya Allah yamuku albarka malik na murmushi yace Ameen maman aydarh nagode sai yanzu ummi tayi murmushi tace kaji dashi aie ja’iri kawai “kashe wayan ummi tayi shi ummi har tausayi take bashi son datake ma aydarh ma baya boyuwa “abba ne yafado masa a rai sam bashi da kara game da aydarh ita kam oum wallahi kaman ba diyar ta ba ko waya takira saidai a gaisa sama sama ko datazo Washington din batawani bari sun had uba kayan datasiyo na babies tunda turkey aiko musu tayi dashi bata zo ba kuma bata bari sun zo ba shikam abba duk karshen wata indai yana landon sai yazo “ girgiza kai yayi ya cigaba da aikinsa.

A nigeria kam yau dr hafsa kwana ta biyu gidan ummi miscarriage tayi kuma jini ya balle mata dr faisal din baida family a lagos duk suna kano “gashi wajan aiki shine md na asibitin su asibitin nasu itama aka mata transfer take aiki ga office dinta gana nashi a wurin aiki ma abun yafaru “ daman tunda ta tashi ranar take masa complain din maranta na ciwo cikin daman karami ne two months ko laulayi batayi sai bar shi akan bara ya tsaya daga yin sex dasukeyi maybe hadda shi yake ja mata ciwon maran duba da yanda baiyi kwari ba ahaka ta daure har sukaje wajan aikin daidai zai shiga office dinta ga files din patient ahannunsa yakai tayi signing duk da shine oga amma duk wani abunda zai sa ta dinga wahala shi keyi “daya shigo office din yaga ba kowa kuma shidai bai ganta waje ba “ah ko tana toilet ne aie bai ma karasa tunanin ba yaji wani kara da salati dawani kalan speed yafada toilet din yaganta kwance cikin jini rufe idonsa yayi ya hau salati yakasa yin komai ma ga jini tana fitarwa sosai ganin bai da niyyar kamata duk yarude yasa tafasa kara tace waii yah faisallllllllll baka gani cikin masifa tayi magana taja sunan shi sai lokacin fa yadauke ta yayi labour room datayi kasa yin komai yay isai dai aka kira wata babbar nurse ita ta taimaka ta gyarata still jini yaki tsayawa sunyi iya kokarin su saidai yarage duk dr faisal yayi wani firi firi dakyar nr yasir yasamu yakai sa gida yayi

wanka atare da rabiah sukaje tashiga gidan dr faisal din ta kwaso ma dr hafsa duk abunda zata bukata ga gida ga gida suke cikin doctors housings din “ sune kawai dangin juna da rabiah da dr hafsa din rabiah ce tsaye kan dr hafsa din wanda ita har yanzu amarci suke sha ba ciki da ita da aysha daman da halime da dr hafsa ne masu cikin Allah dana shi ikon kuma ga na hafsa ya zube har dare dr hafsa her condition is critical rabiah ce takira gida ta sanar dasu duk hankalin kowa yatashi inna data dinga kuka wiwi wiwi a cikin daran tad’aga ma abby hankali sai ankai ta lagos taga halin da marainiyar Allah take ciki diyar amana ce yau hajajju har tafi inna kamewa ita ta lallashi innar tadinga bata baki su iya ma dasu hibba duk rabiah ce tafada oum takalli ummi tace yanzu kodai konice naga zan iya samun flight ko zuwa asuba ne sai naje lagos din tunda babu wani babba acan ummi tayi shiru tace wannan shawara ce oum su amma ko bari zaayi muga abunda hali yabada ko zuwa gobe ne in sha Allah idan ba sauki wanda baa fata sai mu tafi baki daya Abby yagyada kai yace wannan gaskiyane oum su mubari zuwa goben in sha Allah yatashi yakoma kusa da inna yazauna yace hakuri zakuyi hajiya in sha Allah zata ji sauki manya likitoci ne acan din damuna nan damuna can duk dayane ko munje babu abunda zamu iya yi kuyi hakuri dan Allah ai ta addua kukan da ifaceifacan bashi da amfani adduar tafi bukata inna tayi shiru tasa gefen mayafinta tana goge hawayenta hajajju na taya ta hajajju takalli oum tace itama tagoge hawayenta tace ki kiramun mijin aida ki sanar dasu halin damuke ciki shima habibu ki kirasa ki fada masa da jafa’in damuka tashi yau wannan masifa dami tayi kama anata murna yarinya tasamu rabo amma matsafan legas sun cinye ciki baba tace uhm-uhm subhanallahi wai ku dan Allah miya har yanzu kaman baku da lissafi watau kenan Allahn daya basu bai karban abunsa sai tsafi kenan anya anya kam hajajju tayi mitsi mitsi da ido tace aaa yaya abunda hwa nasani na fada kaf wurin nan kaf familin nan duk wanda yayi magana baki ga bakinsa basai ni abby yadafe kai yace kunga kunga duk ayi hakuri hajiya wannan ba lokacin kace nace bane lokacin jimami ne hajajju ta tsuke baki takama bakinta tayi shiru tace tau bara muyi shiru kafin a canza manah magana ta kalli inna tayi mata alaman datayi shiru abby yakalli oum yace kinga fatima maganar ki fadawa malik abarshi kar a dagawa ita asiyar hankalin tunda ga halin datake ciki itama ummi tayi saurin gyada kai tace wannan gaskiya ne malam ubangiji Allah yabata lafiya duk suka ce Ameen “acan lagos kuma ba ita ta farka bas ai wurin 1:30am na dare rabiah ce zaune kusa da ita a dayan side din sai dr faisal din dake zaune kusa da kanta rike da hannunta wanda babu cannula yazuba mata idonsa dayayi yaushi don wallahi kuka yayi whatttt yanda yake son hafsa yanda yake valuing likitar shi inaaaa dole yashiga wani hali gashi wallahi dole kaji tausan ta taji wuya “babu yanda

nurse yasir baiyi dashi ba yayi hakuri su tafi gida yana bukatar hutu idan yaso yadawo da asuba amma inaa dr faisal kiyawa yayi yace babu inda zaije babu yanda aka iya haka abarsa “fuskanta gefen dayake take kallo ahankali take bude idonta har tabude sa kansa yana ganin haka yayi maza yamike yana murmushi yace sannu hafsa sannu boo ta gyada masa kai bakin ta yayi nauyi “rabiah tace Alhamdulilah sannu auntie ya jikin dr hafsa ta gyada kai rabiah tace Allah yabaki lafiya dr hafsa ta jinjina kai awani kalan hankali da muryanta dayayi kasa da yawa tace yafita?dr faisal yakama hannunta daya yakai lips dinsa bisa yagyada mata kai gently talumshe ido tabude tasake cewa kamani naje bayi dasauri yamike yabi ahankali yazare mata cannula daman jini ne ake kara mata ya kusa karewa ma daukarta yayi bai bari tayi tafiya bai ta dai rabiah daga yar jinya yar kallo tazama shi mata komai yasake shirya ta pad ma tayi kadan sai da aka hadda hada pampers tass ya wanke kayan data bata yadauko ta yadawo yazaunar da itakan gadon ruwan Lipton rabiah tahada mata dakyar take sha kafin aka zuba Pepper meat a bowl mai zafi shima dakyar yasamu tasha yabata magani ta kwanta “kwanan su biyu asibiti oum da ummi suka zo hadda inna ummi tace kwara ta taho da ita idan ta warware sai yazo su taho tare don wallahi tasha wahala “har fadawa tayi bana wasa ba amma da bayan biki first ziyaran dasuka kawo dr hafsa duk tafi su cikan daki tayi wani irin masifan kyau daman abu ga mai kyau “ kwana su daya suka taho da ita ummi c eke kula da ita a kwana biyun nan har taji sauki amma ummi tace sai tayi sati arana kam dr faisal sai yakira sau goma vedio call kam ba magana abun nashi ba sauki ahhh wani lokaci ma bata dauka saboda kunyar ummi “ummi duk nasane dasu haka su baba “inna kasa hakuri tay isai datayi magana da aysha da halime hadda mariam yan makaranta shiryowa sukayi suka zo dubata dasu hibba da junior dinta sai iya hadda dr ibrahim suka dubata duk kwanan su daya suka koma wani irin kula dr hafsa ke samu wajan ummi har tamayarda jikinta ita kanta ji tayi takara wani son ummi din yanda take kula da ita wallahi kaman ita ta haifeta “Halime tayi sa’a babu laulayi babu komai Allah ne yataimake ta ga aure ga ciki ga hidiman school shiyasa ma cikin bai bata wahala “ranar da aka san anada cikin waiiiii aie cikin daran wanda can Washington safiya ce sai data kira aydarh tafada mata wallahi ita aydarh kunya mataji malik na zaune sai data kashe wayar ya kalleta yace kingani bas ai ke sarkin kunya ki dinga wasu boye boye ta tura masa baki cike da tsiwa tace erh din anyi din “ina har dadi ma kake ji kana cemun shy bea malik yace kee wa din ni a ina da dai sturbborn bea ne wannan nasan nafada aikam kaman tana jira tafashe masa da kuka ba hawaye tace ohh nine ma sturbborn bea bayan this sturbborn bead aka hadani dasu har ni kake kira sturbborn bea? Yayi murmushi yace aie rama mun suke tayi masa banza tacigaba da cin fries din

gabanta “.Wani kalan ciwo da bayanta yakeyi tun tana daurewa har tafasa kuka bai nan yafita yasiyo mata hot chocolate datace tana so a cafe din kusa dasu “ wani kalan sharp pain wanda bata taba experiencing ba taji for the second time in her life daga ranar daya karbi virgin dinta sai yau take jin wani azaba kuma a bayanta da kuma maranta kan sofa take zaune amma inaa sai da ta lallaba tasamu tasauko kasa kan carpet tahade kanta da sofa ta fashe dawani irin kuka “ciwon karuwa yake ga tana jin cikin kaman yana sauka ma wayyo Allah wani kalan zufa take duk uban sanyi dake akwai a kasar zufa take kaman ana zuba mata ruwan azaba haka take ji yanda tarike rigan dake jikinta kaman zata yaga shi ruwa taji mai gumi yana bi mata kafa tana dubawa taga jini ne zuwa yanzu azaban datake ji yafi gaban tayi kuka ashe kuka ma rahama ne ashe kuka ma sauki ne tagama ba ranta ko ya dawo a yanzu said ai dead body dinta yanda dai take ji a yanzu sake tahowa jinin yayi kaiiiii bata iyawa wani kalan dogon suma tayi aie masifan yayi yawa Allah “ Yasan tashi namata wahala shiyasa ko doorbell din ma bai danna ba yayi using unlocks card yabude yashigo wani hadaddan jacket ne a jikinsa brown malik yasake zama wani kato yasake kyau kana kallonsa kasan akwai kudi da hutu a wurin kyau idan yahadu da naira maza sake hadewa suke bakaman masu kyau da kirar kyau kaman malik shigowa yayi yamaida kofan yarufe ga ledan café a hannunsa yace Assalam alaikum “shiru bata amsa ba yakarasa yaganta kwance kan carpet ga uban jini gata kaman ba rai sakin ledan hannunsa yayi da zuciyarsa tawani buga da uban karfi sai jiri yayi kokarin kwasar shi yaye hulan jacket din yayi daga kansa yayo kanta yazube kan kafarsa the forget who’s he a situation dinnan he is lose and even traumatized daga kansa yayi sama wasu kalan hawaye suka zubo yace yah Allah karka daura mun jarabawar da tafi karfina yah Allah karka daura mun kaddara dakasan ba zan iya dauka ba yah Allah kaji tausayina yah Allah kasani kasan zuciyata kasan wacece ita a wajena yah Allah karka dauki nata ran kabar nawa yah Allah ka datse numfashinmu a lokaci daya kusan this is really sad kukan namiji babba babu kyau this touch my heart!duk tunaninsa fa mutuwa tayi saboda babu wurin dake motsi a jikinta wani irin dauriya da juriya yaji Allah yadaura masa hannunsa na masifan rawa da jikinsa baki daya yakai daidai hancinta wallahi baya hayacinsa bai masan abunda yake ba shiyasa yakasa fahimta dube dube yafara yi ga hijab dinta nan kan prayer mat din datayi sallarh daga zaune a parlor hijab din yasaka mata yadauke ta daf yafita da ita ranga ranga hannunsa ikon Allah kawai yafitar dashi bakin titin don ko gani da kyau bayayi baya ganin gabansa “tafiya kawai yakeyi “dasauri wani mai taxi ya tsaya ganin shi rike data mai taxi yayi saurin fitowa da kansa ya bude wa malik kofa yashiga rike da ita dakyar ya iya hada sunan asibitin su yafada

“har cikin compound din babbar asibitin mai taxi yashiga ana ganin malik ne hatta da security duk sukayu caaaaa rushing aka dinga yi hankalin kowa na asibitin sai daya tashi dakyar doctors mata suka karbeta daga hannunsa kunsan turawa yaki sakinta balle atura ta a gadon dasuka turo sun lura ma he is totally lost bai san abunda yakeyi ba “ labour room suka shiga da ita jinin datake fitarwa is too much “sai lokacin yafara fahimtar abunda ke faru kaman wani zararre haka yafada labour room din sunan kanta bakin rai bakin fama iyakar kokarin su suke kanta “jikinta baya receiving treatment at all tayi kasa dayawa bafa jimawa tayi ba tana labour zuwan lokaci daya yayi mata tayi wani kalan jigata bata da ko karfin daga yatsanta bata dashi balle wani pushing sai yarfe zufa suke su kansu nata labour yabasu mamaki suna cikin haka suka gansa kanta yayu yawani riketa kusan halin turawa doctors din mata suka kama shi kaii yau dai malik yazama kaman dan yaro dakyar suka fitar dashi daga labour room din CEO da kansa yakama shi yakaisa office dinsa malik yayi shiru akasa ma yanzu yahada kansa da gwiwa “acan labour room din babu yanda basuyi ba karshe ma sai jijiga da aydarh tafara “CEO yashiga daya dakin dake office din zai hadawa malik coffee this time around malik da gudu yafice daga office din duk ana ganinsa yayi hanyar labour room din yana kuka da karfi dr jay yayo kansa dasauri yana rikesa (subhanallah □□) duk iyakan taimakon dazasu mata sunyi amma takasa Dr mac ce tahada epidural injection da oxytocin wuri daya that’s hardly ahade su wuri daya but babu yanda zasuyi the girl condition is critical tayi kasa da yawaa ga jini dake zuba pitocin dinoprostone suka saka mata a harshe bleeding dinta ke yayi yawa dr nairobi tace lets try this dr mac messages her uterus and press her abdomen let’s see if she can makes dr mac tacire face mask din tace but this is a very simple method doctor I didn’t think this can work in this her condition let’s proceed on a emergency surgery we didn’t have much of time if not probably we can loose the babies or the mother! Dr nairobi tafita dasauri tace this is very serious “ gani tayi duk anyi tsaye a receiption duk an zagaye malik dake zaune a kasa anata basa baki “ zuwa tayi takama hannun CEO tafada masa abunda ke faru binta yayi zuwa office dinsa malik dake kallon su yamike yabi bayansu”.

CEO yace I didn’t thinks this can cause a problem doctor try as much as you can to save her life and babies life too, Tace what about MD ?CEO yace I will handle him you all should proceed on the girl am coming fita yayi dakansa yakarasa wajan da malik din ke zaune “ yahade kansa da bango yayi shiru CEO yanemi wuri kusa da malik yazauna yazare glasses dinsa yafara magana sai yaga malik din yamike tsaye yanufi hanyar fita daga

wurin baice masa komai ba yabar sa har yakarasa ficewa baki daya “dr nairobi tasake komawa labor room din wani kalan jijiga aydarh tayi tausake wani ajiyan zuciya kaman wanda aka zare ma raii “ tadaina jijigan datake yi “ kama hannunta dr mac ganin kaman aydarh ba a sume take ba tarige hannun dr mac din sosai kaman zata karyata dr mac tace push mrs MD push “kasa motsi aydarh tayi tunda tazo duniya bata taba shiga cikin irin wannan halin ba sai yau wallahi lallai haihuwa kanwar ciwon aljali ne “ still dinoprostone a harshenta saboda bleeding numfashinta yafara sama sama dasauri dr nairobi tace asthmatic attack dr mac ta gyada mata kaii “ oxygen tamata fixing bata cire pitocin din ba dake bakinta “ ahankali tabude idonta bata masan wurin datake ba “ idonta yayi wani kalan jaa kaman garwashi gawani irin hawaye dake zuba ta gefen idonta kokarin cire oxygen din tafara dr nairobi ta rike hannunta tsananin azaba yasake tafizge sai data cire shi wallahi bakinta da jikinta na rawa dakyar tace ya.ya..h sam basa jin abunda take fada muryanta yayi kasa dayawa basa fahimtar abunda tafada dr mac takai kunnata satin bakinta tace saa taji tasake fadin my.hu.s..band “ dr mac tamayar mata da oxygen din ta cire nose mask dinta tace she is calling her husband dr nairobi tace I thinks we should MD maybe he can help let her hold his hand I wished they can makes it together ‘dr mac tagyada kai tafice daga labor room din fita tayi daga labor room din tafita wurin da tabar malik din zaune taga baya nan dasauri taje nurses cabinet ta tambaya sai ga CEO yashigo hannunsa rike dana malik din karasawa tayi wurin su tafada ma CEO malik yabiyo ta “yau malik zama yayi kaman yaro baya fahimtar abubuwa shiyasa dr mac ta kama hannun malik din yadinga binta zarai zarai har cikin labor din suka shiga ansamu improvements yanzu din saboda kan baby har yataho dr Nairobi sai hada zufa take tana kira ma aydarh push iyakar bakin kokarinta take amma takasa “ yana shigowa labor din yahango ta kwance a gadon sun saka blue yard sun rufa mata kanta babu kallabi hulan tazametadaman tuni suka cire mata hijab din daya saka mata wallahi jini yake gani duk ya bata farin floor din kaman an yanka mutun “sai faman juya kanta take ga oxygen din yana zamewa nurse din dake cikin su na maida mata dasauri yakarasa inda take dan flash fuskan shi tayi mata tabude idonta tana kallonsa shima ita yake kallo wasu hawaye masu zafi suka sauko mashi tariga da ta tsorata da haihuwar tun farkon cikin take jin tsoron wannan ranar ashe haka zata kasance ita kadai “ke hango ma kanta ashe inalilahi waina illahil rajiun hannunta dake da uban cannula kusan biyu ta dinga mika masa “ dasauri yarike hannun hawaye kawai yake itama tana lura da kukan dayake ta rufe idonta kamm wani kalan yunkura tayi tayi wani nishi “jini yawani irin zubo mata yana ganin yanda kirjinta ke dagawa yana sama da kasa “hannunsa both two din yakai

yarike ta kaman zaa kwace masa ita babu irin addua dabai tofa mata ba awurin afili ma yakeyi muryar sa na rawa alaman kuka “yace mamana push you can do it try it “ASSEIYERH try again you are brave enough I know am waiting for you pina cola am here for you try mamana tryyyyyyyyyy my baby ya wani fashe da kuka yafada da karfi wallahi sai yabaka tausayi “motsi tayi da kafanta har cikin brain dinta take jin maganarsa tawani irin rikesa tasa kanta a chest dinsa dakarfi tayi numfashi sai ga kukan baby Alhamdulilah!! Hannu dr nairobi tasa tajawo sa baby boy ne tabarakallah masha Allah “murmushi duk sukayi banda malik dashi binsu kawai yake da kallo aydarh ta rikesa wani kalan gammmmm “ sake wani second attempt tay isai ga kukan baby girl Allahu akbar “maida numfashi tayi duk ta sankare jikinsa “ kafin tayi motsi da kafa sai gawani baby boy din Allahu akbarrr wallahi malik sakinta yayi yazube kasa gabas yadaidaita yayi sujjud sai dayayi kusan ten minutes yana ahaka kirari da godiya yake ma Allah Allahu akbar Allah mai kyauta da kari “Alhamdulilah Alhamdulilah Alhamdulilah Allah mai yarda yaso hakika dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah ubangiji sammai da kassai Ubangiji mai kyau da kari!wani lakwas aydarh tayi takoma kan gadon tasume “ dr nairobi ce ta gyara su sai lokacin ma malik yatuna da babu kayan kowani abu dasuka dauka “dasauri yafita daga labor room din yafita compound din asibitin dube dube yafara sai ga doctor linda tafito hannunta rike da key din motar ta zata fita tana ganin malik tawani tsaya tace hey handsome “ malik mai dago ba yacigaba da abunda yakeyi a waya message yama abby sai kuma posting dayaji yayi duk wani social media platform “matsowa tayi yayi gaba har yafice security duk sukayo Kansa ana tambayarsa ya jikinta yakasa rufe bakinsa fada musu kawai yake an sauka kusan turawa dai har yakarasa fita dr linda tashiga motar ta tabisa baya gabansa tasha motar wallahi babu yanda zaiyi ne sauri yake kawai yasa yashiga motar takai sa gida yadauko kaya surutu take masa da rawan kai shidai ba uhm uhmm harkar gabansa kawai yake aydarh sa ta sauka his baby gave birth to triplets his love of his life gave birth to 3 babies Allahu akbar shi ko damuwa da kallonsu bayi bai dan yadaukar musu kaya koma miye sai ayi “suna zuwa gidan yacigaba da lodu kaya sai da yacika back sit din motar kafin yashiga ta mayar dashi asibiti nurses suka taya shi shigar da kayan sun goge babies din an nade su cikin wani white clean cotton yard “ana kawo kayan suka hau saka musu daman malik kaman yasani duk abunda zai siya na mace da namiji ne sai unisex kaya ne masu dan burauban kyau da tsada “ shirya su akayi yah Allahu kuzo kuga kyau tabarakallah masha Allah kafin kace mi babies bar din yacika kowa kallon babies din yake daga doctors din har nurses abun mamaki ne wajan su turawa “duk da ba a dauka saidai cikin gadon da kowanen su yake suke kallon su gift kam

kaman suna jira shidai malik dr mac yabar masu yakoma wajan matar shi “ shi yagyara abunsa this time ya saka mata hospital gown saboda bleeding din datake she is still unconscious “dakin hutu aka kaita “babu mai shiga sai sh isai doctors din dake dubata “sai daya tabbatar dasauki jikin nata har tasamu bacci ma kafin yawuce babies bar din wallahi murmushi yakamayi daya shiga ancika dakin da gifts kala kala ga yaransa dake cikin gadon jarirai uku a jere sai dr mac dake tsaye a dakin yana shigowa tayi murmushi tamiko masa hannu shima yamika tace congratulations Doctor yayi murmushi yace thank you dr mac I really appreciate your efforts tagirgiza kai tace it’s our duty to do suchs “fita tayi gently yakarasa gaban first bed din yana murmushi ga tears of pleasure na saukar masa hannu yasa yazuge zip din net din gadon yana kallon babyn daaka shirya cikin wasu mad kayan sanyi na ficharm dake nan Washington blue ne whatttt kallon yaran yake ko kiftawa babu his baby don try tayi kokari yaron babba ne sosai barakallah farinsa har kashe ido yake duk da ansaka masa hula amma bakin gashin yaron har a fuska sai ka rantse yayi 4 months yanda yacika gadon babu abunda yafi basa mamaki sai wani irin kama dayaga yanayi da babyn Allahu akbar ahankali yasa hannu yaciro babyn daga cikin gadon wani irin sanyi yaji ya ratsa mai zuciya hakika jini jini ne “ kaman yaron najira yasa masa kuka wani kalan dariya malik yayi yafara jijiga sa “ ai kaman jira dayan babyn yake shima ya tsala ihu kallon dayan gadon yayi wallahi dariya yayi har all white clean teeth dinsa suka fito ahh what girgiza kai yayi yana shafa bayan baby yace shshsh tau ya isa kunga momma is still sick karkuyi rigima yes angles?innya dinsu suka cigaba malik kaman gasken nan yabata fuska kafin yayi murmushi yace ahh zamu fara koh baku san waye momma bako you should better learn how to be patience beanies kun san what is beanies that tight cap faa mai kamewa dinnan kar kuyi rigima su fa basu san yanayi ba kukan su suke “ murmushi yayi gently yakai bakinsa satin kunnan yaron dake hannunsa yayi masa kiran sallarh kafin yayi murmushi yace Allah ka raya manah Muhammad Adam “ahankali ya mayar dashi cikin gadon ya kwantar dashi ahankali yace sorry adam kuna jin yunwa baa? Karasawa yayi nakusa dashi yaja dan hancinsa aikam yasake fashewa dakuka kaiii there are very identical aiee kamansu yayi yawa they have to indicate between the two of them dole yamusu shaida ahh “ sunyi kama dayawa kuma wallahi duk kaman shine gasu duk sun yi girma barakallah kaman bayau suka zo duniya bamasha Allahu a shoulder dinsa yasaka sa yayi yawo dashi a dakin “ adam yayi shiru “shima babyn na hannunsa hakan sai kokari yake yasaka hannunsa a baki amma ya kasa dagani yunwa yakeji Malik yayi murmushi he cannot believed that he is the father of 3 yanzu Alhamdulilah shima na hannun nasa kiran sallarh yayi masa yashafa kansa yace Allah yarayaka

habib naff (abba aka ma namesake kenan masha Allah “ ajiye naff yayi yakarasa wurin budurwar “tabarakallah Allahumma bareek shiru yayi yana mata wani kalan kallo “ hannu yasa yagoge hawayen da yataho masa aydarh tayi kokari tayi jarumta kuma ubangiji Allah kasakawa yarinyar nan da mafificin alkhairi Allah yabasa iko da damar saka mata da alkhairi yarinyar dake kwance cikin baby bed din a kaman ummi babu abunda yarinyar tabari wannan soyayya tsakanin Aydarh da ummi har sai data haihu mai kamanta kenan Allahu akbar “ wani irin son yarinyar yaji a ransa kaman dai yanda yaji a sauran yan mazan hannunsa narawa yaciro ta a gadon daga ta yayi aikam tabude ido tarr wani smile yayi ahh “sauran fa basu bude bas ai ita kiran sallarh yamata kafin yazauna rike da ita a hannu yasake gyaraa mata showel dinta yakama hannunta kaman tasan abunda akayi tasake kallon sa kurrr yayi murmushi yakai lips dinsa a forehead dinta yabata pecky a goshi yace Allah yarayamun mamana Allah yamiki albarka ASSEIYERH sultana “(kaka asiya mama asiya diya asiya that’s nice)itama mayarda ita yayi cikin gadon cikin kayan dayazo dasu hadda zam zam da dabino ajwa tundaga makka yasiyo shi saboda kalan wannan ranar fito dasu yayi kafin yadauko sabbin feeder bottle dinsu sai daya yabude yagoge dawani clean cloth kafin yasaka dabinon a baki yamurza yabi each feeder yasaka yadauki zamzam din shima yazuba kaman wata mace yabi yarufe daya bayan daya yadinga ciro su a gadon yana basu bayin Allah yunwa suke ji har mamaki yayi yanda suka karbaaa wai wai “ tun ahannunsa naff yayi bacci ya mayarda shi cikin gadon yafito da sulty tana hannunsa wayansa yayi kara vedio call ne abby ke kiransa murmushi yayi yasake yagyara ta a jikinsa yadauki kiran “what a beautiful family masha Allah su abby ne da ummi da inna da baba da hajajju da dr hafsa sai oum duk sun cika screen din kowa naso yaga babies din oum ce can karshe tana kara “ duk a fuskan kowa wani kala shimfidadan farin ciki ne da murna yanda yanayin su ya nuna kaman waenda akama bushara da gidan aljanna “abby yayi murmushi yace gidanku Abdool nine nazama abokin wasanka watau kwara dayane kenan shine zaka cemun kwara uku ne koh? Malik bai ce komai ba yana dai ta murmushi yamike rike da sulty a hannu yajuyan da camera yanuna masa handsome babies din dake cikin cute babies bed suna bacci duk sun cika kayan sanyin da gadon tabarakallah “wani kalan hawayen murna suka fito daga idon ummi mantaawa fa tayi dawasu sirikai ko wasu yara a wajan tarungume abby tafashe da kuka “abby ma rungume matarshi back yayi yana shafa bayanta yana murmushi shima ga kwalla ta cika masa ido amma cewa yake kinga kukan miye hakan tau ya isa manah kukan namiye? Oum tamike tafice daga parking dakin baba ke kusa da ita tashiga ta kalli gabas tayi sujjud addua tayi sosai kafin tashiga kiran abba fada masa tayi ta fadawa rufaidarh

“ aie rufaidarh na kashe wayar tafada ma dr usama yashiga booking mata flight to Washington “a daran nan “hada kayanta tahau yi wallahi dr usama burgeshi tayi yanda duk ta rude ance aydarh tasauka takasa zaune takasa tsaye bakinta bai rufuwa kafin kace kwabo “ yan booking flight to Washington sun karo su aysha da halime hadda mariam jirgin asuba zasu bi tareda rabiah zasu tafi itama flight zata bi zuwa abuja cikin daran nan sai su hadu su tafi baki daya ummi da hibba ma duk gobe zasu tafi su oum da baba da inna da hajajju da iya sai ran daran suna ita oum ma dai cewa tayi bazataje bas ai daga baya taje taga baby abba kam daga can turkey zai wuce dakyar oum tasamu ta lallaba shit ace yayi hakuri yabari suje tare later “ “. Tasake kallonsa still batace komai ba don bata jin zata iya magana ma sam sai faman binsa dai take da ido ancire mata oxygen din har yanzu ana kara mata jini tayi yaushi tayi kasa dayawa dakin datake baa barin ana shiga daga dr din dake treating dinta sai shi “sake rike hannunta yayi kafin yasa hannu yagoge mata hawayen gefen idonta dake ta zuba duba yanda jinin yake dropping yayi lafiya lau kafin yashafa kanta “ yakai lips dinsa a forehead dinta yadaura mata kissing har zuwa lips dinta “ talumshe idonta “ tana jinsa bata iya komai don wallahi jikinta kaman ba nata ba har yanzu bata gama regaining from unconscious ba “duniyar ma upside down take mata wani juuuuu take jin in all over her body “yagyara mata bargon datake rufe dashi “ta glass din door din yahango tahowar dr mac tana shigowa tagansa zaune tajuya tace bara takoma wajan triplets har ya gagara ummi ta iso wallahi “yasan zata tsaya da yaran shikuma yazo yabama matan full care din datake bukata ta wahala iya wahala haihuwan ba zo mata da wasa ba kuma nakudar yara uku banan bace tamayi kokari tsakanin shi da ita sai fatan gamawa lafiya Allah ne sila itace silar zamuwar shi wani abu a rayuwa tayi masa komai na duniya “dan yamutsa fuska tayi dasauri yakalleta “idonta a rufe sai kwalla kawai dake zuba ta gefen ido yana gangarawa “ya wanke hatta da rigan data bata wajan haihuwa da hulan da kayanshi da komai na jinin da zaa wanke shi wanke sa sai data sha ledan jini five Alhamdulilah zuwa yanzu jikinta dasauki har angama saka mata jinin drips ne kawai yarage “shi yagoge mata jiki da asuba tasamu tear sosai bazata iya wani zaman kirki ba kawai yabarshi idan mom ko ummi suka iso sai su zaunar da ita suyi mata proper wankan jego “jikinta yagoge mata yasaka mata riga tea yahada mata mai kauri yasakata a jikinsa yana bata dakyar yasamu tasha ko half cup baiyi ba ya kwantar da ita “ alluran bacci aka mata saboda tasamu hutu sosai aie yarinyar tayi kokari ma “ajiyan zuciya yasauke da baccin yadauke ta rabon shi da bacci tun safiyar jiya a zaune ya kwana rabi wajanta rabi wajan yan uku shi da dr mac rigima garesu bana wasa ba kamar ma adam yaji labari duk yafi su kuka sai cin socks din

hannunsa yake da alama yunwa yakeji dashi a shoulder malik ya kwana a zaune naff da sulty sun fi sa sauki sake basu ruwan zamzam din yayi da ajwa bayan anyi musu wanka an shirya su “ yaran sunyi kyauu ahhh kaman yaran arabs pictures yayi musu dr nairobi taba da shawaran yasiyo musu formular kafin maman tasu taji sauki ko kuma akai su su sha nono kaii bazai iya ba mugun tausayinta yake dakuma su kansu yaran yana tausan su basu ci komai ba tunda suka zo duniya dakin datake yashiga yaga she is still sleeping tsayawa yayi akanta yana kallonta she looks very pale and sick duk tayi wani kala idon yayi kumburi duk da arufe yake ga bakinta ya bushe “yagirgiza kai yasa yatsan right hand dinsa yashafa lips din nata kafin yagyara mata duvet yafita “taxi yasamu takai shi babies foodie “ yasiyan musu formular kala da kala masu kyau na new born babies yadawo asibitin tareda dr nairobi suka zo gida ita tahada musu ta cika musu three feeders suka koma “da naff da sulty kaman sun san madara dasauri dasauri suka karba bayin Allah har subaka tausayi wani kala malik yaji daya ga suna haka kaman bai kyauta bas ai dayabari suka ji yunwa har haka “ babu yanda baayi ba adam ko yafara karba sai yasaki ya tsala kuka “duk hankalin malik yatashi sake fita yayi yaje da kanshi ya hada dayan flavour”yadawo so sau biyu bai karba yasa kuka malik yarasa yanda zaiyi yadaukesa yace dr nairobi ta zauna bara yaje yakai sa wajan dr jaz ko baida lafiya babu irin dubawar da dr jaz bai masa ba lafiyarsa lau ana haka sai ga kiran wayan rufaidarh ya duba yaga number tane na kasar ta zo kenan ‘dagawa yayi tace yafada mata wurin dasuke har tashiga taxi fada mata yayi takashe wayan sake komawa yayi ya gwada basa madara ko zai karba amma ina bai karba ba kiransa tayi tace yafito tazo dr Nairobi ta karbi adam daga hannunsa su naff da sulty kam bacci suke abinsu sun sha wankan su da abinci sai bacci yana fita yahango mom tsaye tasha jacket black tayi rolling black tissue veil ga uban black shade sai trolley kwara daya da handbag dinta gefenta tayi kyau mom ga cikinta yafito sosai da alama girman ciki gareta karasowa yayi da fara’a suka gaisa yadauki trolley tarike handbag din tana masa congrates shiga sukayi tace ni narasa ma wanda na kagara nagani matanka dai tayi hakuri kishiyuyina na kagara nagani malik yayi murmushi yashafa kansa yace babu komai mom da dai tsohuwan zuma ake magani mom tayi dariya tace tau am eager to see them all muje ina ned akin malik yace dayake ba wuri daya suke bai ta tana can vip postnatal har yanzu she is on rest suma suna nan babies bar mom tace ashaa kam haihuwan yazo mata da damuwane?malik yace Alhamdulilah dasauki rufaidarh tayi shiru tace muje naganta malik yace no mom tasamu bacci kuma basu cika barin ana zuwa wurin ba kindai san halin su nan rufaidarh tagyada kai tace Allah yaraya man su Allah yabata da lafiya muje nagansu shi yayi gaba tana binsa abaya

har yanzu adam a hannu dr nairobi sai kukanshi yake sauran kauu na bacci dasauri rufaidarh ta ajiye handbag dinta tasa hannu takarbesa tahau jijiga sa “ ko yayi shiru sai ma sake tsala ihu yake yana kuka cike dawani kalan kauna rufaidarh ke jijigashi dakyar aka samu yayi shiru tasauke ajiyan zuciya dr nairobi tamata sannu rufaidarh tayi murmushi tamata godiya “daya bayan daya tabi tana kallon yaran bakinta yaki rufuwa tsaban yanda suke da mugun sha’awa da adam da naff duk abunka bazaka iya bambamta su ba “ lil ummi kuma lips dinta kaman an musu jam baki gashi kau har kusan gira masha Allah cigaba da jijiga adam tayi har aka samu shima yayi bacci yunwa yakeji banda ruwan zamzam da ajwa babu abunda yakarba “rufaidarh tace ahh son mi zai saka bazaa basa nono ba?ko bata da ruwan non oita uwar? Malik yayi shiru sai kuma can yace baa gwada ba “rufaidarh tawara ido tace yau ga shirmen banza ban gane baa gwada ba baa gwada ba kamar? Shine daman aka fara bawa yara madara har shi wannan bazai karba ba bayan ga abincin su can jikin mahaifiyar su “malik yayi tsaye yana sauraronta yace mom bata da lafiya ne rufaidarh tace malan baby bacci take ko idonta biyu?yace dazu dana fita bacci take tace tau yanzu nasan tafarka muje ka rakani na kai shi yasha nono “malik yagyada kai. Su ummi da hibba sun riga su aysha isowa malik yasaka dr joe yaje airport yadauko su lokacin dasuka shigo asibiti yana can dakin aydarh jikinta yayi sauki har tazauna ma amma rabi da rabi tazauna a jikinsa yana bata oat “dasukaje da mom hanasu shigowa akayi shiyasa baa bama adam nonon ba kuma anyi saa yayi shiru itama ummi babu yarda baayi da ita ba tazauna bat ace afara kaita wajan aydarh dr mac ce tamata iso aydarh naganin ummi taji wani kuka yataho mata.

Ummi tayi murmushi ganin yanda aydarh tayi dasauri takaraso wajan gadon’’ aydarh tamiko mata hannu rike hannun aydarh tayi kaman tana jira tafashe da kuka “ummi na murmushi tace ya isa ya isa haka baby sannu sannu “ malik yashafa Kansa yasaki aydarh yatashi ummi tazauna wurin daya tashi aydarh tashige jikin ummin taboye kanta sai kuka take ahankali ahankali don bawani karfin kirki bane da ita “ummi tacigaba da shafa bayanta tace sannu sannu baby Allah yaraya Allah yabaki lafiya kinyi kokari baby “ aydarh tayi shiru sai sauke ajiyan zuciya take ummi taciro ta daga jikinta “ta daura kanta a kafanta tace Allah yaraya manah triplet “triplet kuma “kallon malik aydarh tayi ahankali suka hada ido yayi saurin janyen idonsa itama haka ita fa bata ma tambayi abunda tahaifa ba baki daya kwata kwata bata kaii 2 hours dafara gane abubuwa ba “ cikin ranta ta maimaita kalman triplet yaran har kwara uku ne or? Ummi tace kukan ya isa haka ki karasa shan shanyin ahankali aydarh tagyada kai muryan ta can

kasa irin na masu ciwo dinnan “tace nakoshi ummi tace aaaaa “ baby sai fa kin daure hakuri zakiyi ki sha ko bakinki babu dadi kinga bazakiyi saurin warwarewa ba bakya cin abinci shan magani da cin abinci yazama dole yanzu saboda ruwan nono ki kuma samu karfin jikinki kinji baby aydarh tayi kasa da kaii akwai saura kenan nono kuma yanzu fa sai taba yaron nono ba chap aikam daman sunyi da shi yayan formular zaa dinga bawa babyn ita dai ba nononta ba kwara ma yafada musu “dakyar ummi tasamu aydarh takarasa karban shayin “malik na zaune kan kujera yana kallonsa banda murmushi babu abunda malik keyi son da ummi take ma aydarh na daban ne wani kalan so take mata irin na uwa da diya “kwantar da ita tayi ta kalli malik tace ruwan zafi fa? Malik yace akwai a heater cikin toilet din ummi tace jeka can inda su hibba suke kace nace tabude karamin akwatina akwai kayan wankan dana zo dasu sai ka kawo mun “ malik yace tau fita yayi yaja dakin ummi tashiga bayin ruwan masu zafi daidai ayi wanka jego toilet din kaman baa taba amfani dashi ba da alama sabon building ne wurin babu wanda yataba shiga aydarh is the first person daaka fara kwantar da a dakin cikin bathtub ummi ta tara ruwan tafito daidai yashigo dakin rike dawani leda daakayi well packaging yamika ma ummi da hannu biyu “karba tayi tacire veil dinta ta ajiye tashiga toilet din kayan wankan tasaka ciki “dan jim tafito tace kayanta faa?malik yace duk suna can babies bar ummi tajuya tace naga da sabon towel nan jeka ka dauko kayan nata da pads yace tau ummi “tashi yayi yatafi ummi tamatsa kusa da gadon tace yi ahankali ki daure baby ki gwada tashi zaune mu gani aydarh ta lumshe ido ta gyada kaii kokarin tashi tafara ta cije baki ta dai daure din ta tashi zaune ummi tayi murmushi tace masha Allah yauwaa sannu baby ummi tace ko har tashi ma zaki iya?aydarh tagyada kai ummi tace Alhamdulilah tashi tau “kokarin tashin tafari y isai gashi tashi tsaye but kafanta nadan rawa narashin karfin jiki da taimakon ummi suka karasa toilet din “ummi taware sai data tabbatar tama aydarh pure wanka jego tazauna cikin ruwa ta gasa ta kafin tadaura mata towel suka fito duk da this is not the first time da ummi tamata wanka amma takasa hada ido da ummin tsaban kunya yana daya daga cikin abunda kesaka ummi jin kara son aydarh kunyar yarinyar nutsuwan ta dakuma kawaici sun taimaka sosai wajan daura ma ummi son aydarh fiye da yanda take son iyayan ta data haifa da cikinta kan gadon tazauna har malik yakawo kayan nata da uban pads kusan five bags ga pants kusan six sai inner cap hadda socks da sweater da perfume da cream dinta “ ummi taimaka mata tashafa cream din kafin tahada mata pad kwara biyu tasaka mata tabata pant din tasaka rigan dayakawo mata tasaka tasa hulan da sweater ummi ta duka tasaka mata socks din zata kwanta ummi tace tadaure tayi exercise ko dakin ta zagaya”so take tace ina babien

tagansa amma kunya take ji hakan nan taji tana son ta gansa “ yayah yace mata kama yake dashi har yagama duk labaran sa dazun nan jin sa kawai take bata da bakin mayar masa “ shigowa dakin yayi hannunsa rike da leda har kwara biyu friuts ne kala da kala sai dayan ledan kuma abincin wani restaurants ne yasiyo suna dishes na all country yasamu mata pepper meat sai grilled meat sabon gashi “ ajiyewa yayi yakalli ummi yace sannun ummi ummi tace yauwa mom dinku fa? Malik yace suna can babies bar din yace aie ko ita da hibban ne sun tafi gida junior fa mura yake dasunyi wanka sun huta “ malik yace kwarai dagaske suma yaran zaa iya tafiya dasu gida tunda they are all fine ummi tace tau Alhamdulilah ita baby fa? Malik yace zuwa dare in sha Allah zamu iya tafi sai nakarasa mata sauran medications din a gida ummi tagyada kai tace tau ba damuwa maganar suna fa kun yanke shawaran suna ne yayi kasa dakai yana shafa suman sa yace eh ummi ansa musu suna ummi nakallonsa tace waya samu su?yayi murmushi yace nine ummi “ummi tayi smile tace inyee ita maman yaran fa?tare kukayi shawaran ko gaban kanka kayi Abdool? Aydarh najin abunda ummi tafada tanemi wuri tazauna kan kujeran dake kusa da ita tayi kasa dakai tana wasa da yatsun hannunta “ wai wasu yara itafa wannan kiran yaran yaran daake nasa ta jin wani kala wai yara har nawa kodai kwara ukun ne? Malik ya girgiza kai yace aie bata da damuwa ummi “ummi tayi shiru kafin ta gyada kai tace mika aka saka musu “malik yarage murya yace babban Muhamad adam sai tabiyun sunanku ne ummi sultana sai karamin shine abba naff ummi tayi wani kalan murmushi tace Allahu akbar ubangiji Allah yama su albarka Allah yaraya su Allah yasa su biyo masu halin Allah yasa duniya tayi alfahari dasu Allah yamuku albarka Allah yaba mamansu lafiyan shayarwa da kuma ikon tarbiyantar dasu Allahumma bareek malik na murmushi yace Ameen Ameen mamaarh Allah yasaka muku da alkhairi Aydarh tasakeyin kasa da kai tace Ameen “ amma lissafin yayi yanzu duk ya kwance mata tunani wallahi bakinta yayi nauyi sai yane take jin haushin wannan bakan masifan kunyan nata datakasa yin tambayar dake ranta in Ummi’s presents bakinta fal zuciyanta fal tambaya amma bakinta yakasa buduwa yayi su “ tayi shiru tana kallon kasa ummi takalli malik tace bude mata abincin tafara ci bara naje wajan mom dinku “har ummi tamike sai kuma ta tsaya tace wai ita baby taga yaran ankawo su wajanta ne? Malik ya girgiza kai ummi tace yau ga shirmen banza tau kan wani dalilin? Malik yace ummi aie baki daya datashinta da zuwanku babu tazara daman niyyana sai tafarka kafin ummi tace tau aie shknnn yanzu taci abinci sai tasha magani bara naje sai nazo dasu malik yajinjina kai ummi takalli Aydarh tayi kasa da muryanta cike da lallashi tace kidaure kici abinci kinji namesake sai ki sha magani sannu ahankali ahankali jikin zai karasa warwarewa ko dakika gan isai daaka sha

wannan wahalar kafin yazo duniya said ai nawani yafi nawani “bakaman ke kinyi namijin kokarin nakudar da har uku “still kan Aydarh nakasa bata dago ba “ ficewa ummi tayi dasauri tadago takalli malik tayi raurau da ido yadage mata gira yace what?mike miki ciwo? Tace yanzu har kwara three ne yayah “ malik yatashi yamatso kusa da ita yajinjina mata kaii yace yes cuddle bug this is suchs a blessed Alhamdulilah Alhamdulilah Alhamdulilah mungode ma Allah dawannan kyautar daya manah mamana “a lokaci daya a rana daya yara dayday har kwara three this is very amazing Allah yamiki albarka nagode sosai Allah yasaka da alkhairi “tasa bayan hannunta mai cannula tagoge hawayen dake zubo mata ta jinjina masa kai muryanta narawa alaman zatayi kuka tace masa to yayah waye zai dinga basu nono? yanda tayi maganar har yaso yayi dariya ita da zuciya daya tafada wallahi yasani “daurewa yayi baiyi bay ace ke ai kinyi mai wuyar tunda kin haifa madara zamu cigaba dabasu tagyada mai kai dasauri kaman irin yan yaran nan daake so amma wayau “tayi kasa da murya tace daman aie kafada to yanzu ma kasake maimaitawa ko kasiyo formular ma? Malik yagyada kai yace erh tun ma jiya fa nasiyo har sun far asha but adam is not responding to the milk “Aydarh tayi shiru tace wanne cikinsu? Yace wanda kika fara haifa har bata so ta tuna wani kalan yankewa gabanta yake fadi tsaban yanda bata son tunawar daga ita sai Allahn daya halicce ta kawai suka san iyakar matukar masifan wahalan azabar datasha tasha wahalar da baki daya tayi tunanin fitar da rai daga rayuwa tasa mutuwa zatayi at that stage she even pray for her death da wahalan datasha “ ahankali tace why?malik yawara ido yabude hannu yace wallahi bandai sani ba kuma anduba sa he is fine amma ina ganin ko baya son madara sai natural breast milk “Aydarh tadan kallesa tadauke ido “ bude mata grilled meat din yayi yasan she will like it more than the pepper meat “ already anyi sliced din apple din da peach sai strawberry yamiko gabanta ahankali take ci kaman bata son ci sai dayayi kaman yanda ummi tace taci taci sosai tasha fruits din da maganin ta “ rufaidarh ce tafara yo gaba rike da naff a hannunta daaka musu wanka anchanza musu kayan zuwa wani baby set white da abun daukar dakomai off white ne “sai sulty dake hannun hibba tagoya junior abaya dake bacci ummi ce karshen shigowa rike da adam wanda yanzu ma dakyar tasamu yayi shiru “Aydarh tadinga binsu da kallo dasauri hibba tamikawa malik sulty taje taba Aydarh hug tace masha Allah Alhamdulilah sissa congratulations Allah yaraya manah triplet Alllah yabaki lafiya dakuma lafiyar shayarwa kinyi kokari gaskiya masha Allah Aydarh tayi murmushi tace yasu iya?where is my baby hibba tace wannan sarkin rigiman yayi bacci Aydarh tace erh zaman flight aie babu dadi “ ki kawosa hibba tace no aji da yan kannansa first bakaman sarkin kuka bawan Allah “rufaidarh tayi

murmushi tace sannu baby Aydarh tace mom kinzo rufaidarh ta jinjina kai tace dolene aie baby “ sannu Aydarh tayi kasa da kai “ tace yauwa “ummi ta matso tace fara karban wannan bawan Allahn dan baby duk yafi matsowa dan Allah afara bashi muga in sha Allah zaya karba Aydarh data fahimce abunda ummi ke nufi dasauri ta kalli malik suka hada ido kasa yayi da kansa shi bai masan yanda zaiyi ba shifa wasa yakeyi all ce matan dayake ba ita zata shayar da yaran ba “kallonsa take ta yi kaman zatayi kuka so take yayi magana amma taga baida alaman yi don yama dauke kansa yamayar kan yarsa “ummi na kallonta bata gane abunda Aydarh ke nufi ba taga dai tana ta kallon malik kwalla yacika mata ido daura mata yaron tayi a cinya sai lokacin takalli yaron daya bude dan bakinsa ya tsala kuka “ whatttt aie malik tagani sak a fuskan yaron so take tasake kallonsa amma bara ubansa yayi shorting wannan case din first ummi taga Aydarh ko motsi batayi ba balle takama yaron taciro nono tabasa tace basa yasha manah baby kukan nasa yayi yawa kuma duk yunwar ke cinsa nasani “ dan motsi tayi da hannunta sai kuma tasauke kanta tana satar kallon yaron “tagefen ido “ idan ma maganar tayi feeding din yarone bazata iya ciro nono gaban su ba tabashi ai wallahi kunya takeji ita fa ansata tsaka mai wuya rufaidarh tagyara rikon naff a hannunta tace yau ga iskanci kewai ko bakiga yaron nan kukan dayake ba baby? Ummi tace ayi mata ahankali mom “mom tace ba maganar ahankali bane ummi ita komai sai tayi yarinta tau dan ubanta kar tabashi yasha tabarsa ya sike “malik dai kansa nakasa ummi takalli hibba tace daughter kije ki can dakin ki dauko mun feeders dinsu mom kawo mijin nawa kema kije ki huta mom talura ummi so take su fita bata son fadan dake ma Aydarh tamika mata naff din tace tau aie shknnn sai tayi “daga haka mom da hibba suka juya ummi tasamu ta lallaba Aydarh da hawaye yarr yafara mata zarya a kuncin ko fito da nonon wallahi bata iya ba baa tsoron miji yataba ko yasha sai dan bawan Allah dabai san abunda ke cikin duniyar ba “duk ummi ta taimaka mata ga uban hawaye ga yal banzar kunya har aka samu aka fito da right tit dinta “ ummi tanuna mata yanda zatayi tanayi yaron kaman yana jira yawani kama dasauri “dasauri tace ouchhhhh sai ga uban hawaye don wallahi wani kalan zafi taji a nipple din “haka ya dinga sha tana hawaye malik tashi yayi yakwantar da sulty gefen naff da ummi ta kwantar kan gado sadaf sadaf yafice daga dakin kaman wani munafuki Aydarh tafakaici idon ummi tabanka ma bayansa harara har yawuce daman damuwan adam bai wuce na yunwa ba kuma bai ya son formula saidai nono sai ummi tasa ta chanza masa har yasaki da kansa Aydarh tasauke ajiyan zuciya tana lumshe ido ga hawaye share share “ummi takarbe sa tashafa bayan sa da ko 2 mins baayi ba yayi bacci ummi taje ta kwantar dashi “ kusa da sauran wani kalan kyau suka mata sun burgeta

sosai a kwancan wai duka yaranta ne ita ta haifesu dagaske “duk zasu dinga cema mama itama she is now a mother?waiii kaiii she cannot believes this ita din nan with 22 ko 23 ma ne yanzu she gave birth to triplets oh wow “su naff ma duk sai dasuka sha kaman zatayi hauka don haushi yanda ummi tasa ta feeding dinsu sukuma sai sha suke as if there lives depends on it (yoo it depends of it manah) .A ranar akayi sallama basu kwana ba suna karasawa gida sai ga mr joe yakawo su halime da malik yace yaje yadauko su suna shigowa suka rikita gidan da ihu da murna sai daukan yaran su wallahi duk suna ta murna sai jin dadi ake anata tabata yan uku masha Allah malik ma yaki fita dashi aketa zaman jegon ummi ce tsaye kan Aydarh komai ita kema ta , Jego mai kyau da tsafta Aydarh tayi kafin ranar kwana bakwai ta isa isa tazama wata iri har kashe ido take fatanta yayi fresh yasake daura haske kan nata tayi fari tass barakallah tayi kiba sosai masha Allah “ yau daran suna yau su iya zasu iso taron suna “har sun iso suna ciki yanda aka shiri kaman baa wata kasar ba kaman a nigeria sai hidima suke.

Tun daga ran da aka haife su har yau idan zaa basu nono sai an shafa fama bata yarda tabada nono gaban kowa har kwara ummi itama tsayawa take don ta tabbatar ta basu din malik kam bawan Allah indai har zaayi feeding dinsu yana kusa sai ansace kallonsa an watsa masa harara “kwata kwata bata son raino ba iyaka a bata yaran tabasu nono a karbe har kwara adam ana barin shi wurinta duk yafi sauran yawan shan nono ga rigima yacika kuka kwata kwata idan dare yaraba zai tashi yadasa da ita da ummi sai triplet suke kwana a daki daya dayan dakin su mom da hibba dasu mariam ke kwana malik ya kwana a parlor yau dasu iya suka iso sai wurin kwanciyar yayi karanci yafara processing samar musu gidan inda yafi nan mom tahana sa tace su da zasu koma gobe in sha Allah ummi ce kawai zaa bari kar yakashe wannan uban kudin “ ko da rufaidarh tayi maganar ama mai lalle booking flight daga sudan Aydarh kwabe fuska tayi tace bata so rufaidarh tasaki baki tana kallonta tace hala kin taba ganin inda akayi mai jego babu lalle ran suna?aydarh ta girgiza kaii aysha tace kiyi hakuri manah auntie basai tazo tayi miki ba Aydarh tayi shiru batace komai ba malik dake can sofa yayi kaman baya jinsu yana dadana waya yadago gently suka hada ido yawani kashe mata ido ta danna mai harara shi dinnan ma bai san haushinsa takeji bane kawai yana cin arzikin su ummi batace masa komai ba gashi kila ma hutu ya dauka wajan aiki don baya fita fa idan ma yafita baya cika one hour yake dawowa ba kunya zai tsatsalaka yadauki yaransa “yanzu din ma naff ne a hannunsa shi aka fara gamawa wanka sauran na can wurin ummi ana musu mariam ce mai taya ta rikesu idan angama ko hibba ko mom ke shirya su “ yace mom ku duba ga kudin flight din nan rufaidarh

takalli wayanta aikam ga alert nan tace haba son dandai kudin flight zan biya baice komai ba yayi murmushi yatashi da naff a hannu yawuce daki yace mamana bismillah kaman bashi yayi maganar ba yashige daki kallon bayansa ta danyi bata tashi ba “ rufaidarh tayi shiru tana kallonta taga iyakar gudun ruwanta ahankali tamike tana tafiya kadan kadan wanda tunda ta haihu haka take tafiya da zama ahankali dan ma ummi tsaye take kanta wajan sit bath shiyasa take jin wurin ahankali ahankali yana warwarewa kanta a kasa wai kunya tabude dakin tashiga yana tsaye da naff a shoulder yana jijiga sa tasamu wuri ta zauna kan gadon “ tace gani “yace aie naganki tayi kasa da kai yamika mata naff dake dan korafi yace feeds him first Aydarh tasace kallonsa taga fuskan nan babu wasa ta turo baki gently tafito da tit din yazauna kusa da ita yaron na kamawa ta dan cija lips “ malik yace maganar suna tunda aka saka musu suna baki ce komai bak o baiyi ba dasauri ta girgiza kai tace yayi yayah Allah yayi musu albarka yayi murmushi yace Ameen maman adam “Aydarh tasa hannu tarufe fuska tace lallai kam maman adam tarage murya tace kuma haka mutane zasu cigaba da fadamun? Malik ya jinjina kaii yace eh manah tazare naff tana mayarda nononta tace nidai Allah yayah ah’ah am shy ma self yar karama dani bana so malik yarage murya yace tunda mijinki yamiki ciki kuma kin haihu aie shknnn yanzu kema daidai kike dakowace mace “ tace umm yace kiyi magana manah tace ita oum bazata zo?yadan shafa giransa yace Allah sarki oum “kara take duk waennan mutane basu isa bas ai tazo zata zo definitely but sai after kowa yakoma “Aydarh tace sir kanajin hajiya bay ace wa wai hajajju tace erh ita dai fa kasan sometimes inna bata shiga abunda bai shafeta ba da dai kan auntie hafsa ne wannan malik yace nasani ita hajiyar mi ta maki Aydarh tace wai fa irin su huta dinnan sai nadauki hijab nasaka naje na gaishe su nayi musu ya hanya shine fa take cewa hala har nakoma wajanka nayi wani cikin shine nake fama da hijab ita dai ba ruwanta bazata gantale a hanyar zuwa wannan kasar ba suna “ baba ce ma tayi mata magana kuma ummi da iya duk suna dakin malik yayi dariya yace don’t worried about her kinsan halinta aie suma sun sani rabu da it ani rabon da ko dan kiss dinnan ma shiga tsakanin mu tun ran daran dazaa haifa su damsel ‘tace sulty ne damsel din?yace dawa tace ni manah yamata wani kala da ido yace oh really?tadaure fuska tace pretty sure yace tau madallah “tace kaga idan zaka karbi yaronka ko fita better idan kuma kuna nan ni bara nafita bazaka jamun abun magana ba ace wani abu ni ban son suchs maganganin su inna dan Allah yace babu inda zakije tace dan Allah fa yayah yace yaron nan bai gama sha ba kimayar dashi tamarairaice fuska tace ayyah sir kaga sauran dole nabasu kuma zafi nakeji gashi dana masu zanna tajin yunwa yunwa “kaman mi “ malik yace shiyasa naga ummi bata cika

two hours bata maki something to eat bat ace nidai yanzu kadauka yaronka ku fita “yace Allah ko kibasa kona ciro nabasa “ Aydarh takallesa tadauke ido bata ciro din ba hannun yasa yarike ta ya kwantar da naff a laps dinta yasa hannu cikin riganta yafito da boobyn kallonsa take yana kokarin saita naff wurin taki taimaka masa sai ma dauke kai datayi mariam tayi knocking malik yace yes tayi tunanin zai bari ko ummi ce bai bari ba mariam ta turo tayi sallama “kallo daya tayi musu tawani kalan kasa da kaii “Aydarh tashiga shock ganin har mariam tashigo bai bari ba kwalla taji yazo mata dasauri mariam ta ajiye yaron ta kama gabanta tana fita tashige inda tabar halime da rabiah sauran duk suna parlor halime hutawa take rabiah kuma na waya da mijin ta “ rufe kofan tayi halime tabude ido kadan tace haba haba mariam don nahuta nazo nan see how you just bang the as if wani ya kora ki mariam tamatso tace yoo koroni akayi manah rabiah tace aie tsiyar ki kenan bakya magana kasa tsaye tace yanzu naje nakaiwa auntie Aydarh adam daaka gama masa wanka na tarar da yayah dakansa yaciro yana bawa naff halime tayi tsaki tace shine mi tau?rabiah tace bar banza tau wanda shi yayi cikin karewar yafito mata da nono yaba yaro “mariam tabude baki tace tau aie shknnn badamuwa “ ficewa tayi duk suka cigaba da abunda sukeyi wannan tacigaba da wayanta halime takoma tarufe idonta.Dr ibrahim da dr faisal da dr umar sai nr yasir da dazzy yau suka iso cikin daran nan hotel suka kama hadda “ malik acan zasu kwana “ bayan sun zo sun ga babies da matan su duk an gaisa triplet sun sha gifts bana wasa ba wurin kowa na familyn abby yabude musu share a account na kaf companies dinsa da sunan aydarh dakomai dakomai nata “godiya sukayi ma abby yana murmushi dayake vedio call ne yace sai ga uwargida da amarya sunyi anko din suna? Aydarh tayi kasa da kai tana murmushi ta jinjina kai yace gashi kuma naga kaman su sosai masha Allah malik yace saima a fili abby abby yace masha Allah nima in sha Allah bayan suna zan shigo sai mu taho tare da umminku ko zaka barta tabiyo sune Aydarh ta dan sace kallon malik ya girgiza kai dasauri yace aaaa abby daman tasan zaayi hakan shiyasa bata masa ma ranta ba “ Dr hafsa kusan kullun sai takira vedio call sau hudu tana ganin Aydarh da triplets dinta daga ita sai oum akabari har yanzu yanayin jikinta ummi tace tazauna “kafin masu tafi sai dayazo yaganta “yakawo mata wani set din boxes din da latest expensive atampha’s laceses dakuma dubai abayas har motar sai da ya chanza mata hadda car key din yasaka cikin box din motar na can lagos kaman zatayi masa kuka itama zataje yace aaaa tayi hakuri idan ma Aydarh bata zo ba tana jin sauki shi da kansa zaya kaita Washington din sannan fa kudi ya tura mata a account duk nunawa oum “oum tamasa godiya suka tafi ita har tarasa tsakanin ummi da oum wanda yafi kirki kowa yayi bakin kokarinsa da iyawar sa akanta “ . Mai

lallan ta iso Aydarh ce first wacce aka fara mawa kalan dai waccan wanda take musu “yau hadda baki maakayi kadan kadan zo kaga kyau dan Allah kunshin yabi skin din yayi luf yayi wani kalan kyau ga gyaran kai anyi an kwance calaban dayayi mata sai tafito zallar asalin mai jegon ta tayi wani fresh kyau masha Allah “kullun sai ummi da malik sun tofe yaran da addua saboda bakin mutane nonon Aydarh nada kyau sun sake zama lukutaye “duk anma kowa lallen cikin su aysha” washe gari dasafe suka hau shirin suna wanda iyakar su ne sukayi sunan su sai few wanda malik yasani a garin suka zo da matan su suna yayi dadi don parlor kusan cika yayi da gifts din Aydarh da triplets kowa dayazo cikin turawannan sai dayayi musu presenting gifts “ Aydarh tayi kyau kyau irin kyau dinnan mai suna kyau wani kalan arna cotton lace tasaka coffee sai golden jikinsa hijab boubou aka mata da straight skirt dr nairobi tazo tare da yarinyar ta “ itama tama Aydarh makeup kwalliya aka mata kalan na turawa “ masha Allah tabarakallah kayan jikin yan uku abun kallo ned asu da maman su da babansu bazaka taba so ka dauke ido daga kallon su ba kowa yayi kyau duk sunji kudi “ kudi da hutu ya zauna masha Allah anyi pictures anci ansha saidai muce ubangiji Allah yaraya manah triplet yamusu albarka “ har dare mutane basu gama tafiya ba suma yan nigeria gobe zasu dau hanya wasu sai jibi rufaidarh ma yau dr usamanta ya iso acan nigeria akama yaran yanka abby cewa yayi bai yarda da dabbobin nan kasar ba shima kuma malik ya goyi da bayan hakan “company da abba keyi a jordan dakuma canada dasunan triplet aka budeshi saboda yace yabasu shi halak malak yasaka ma company komai duk wani profits dama komai yaware a account ana zuba musu “ malik bai san dawani baki zaiyi amfani dashi ba wajan godewa family din nasa ba amma yaga so yaga kauna said ai yace Alhamdulilah don wata kyautar ma tafi gaban nagode saidai na tuba “ yarage sune kawai inna tace azo abude kyaututukan bata fahimce abunda suke nufi ba dabasu ce abude ba mariam da rabiah suka dinga bude mata inna har tagaji dagani tace ya isa haka abarshi zuwa safe sai a karasa “ yau yan abuja suka koma banda mariam dasunyi hutun school tace tana nan sai tare da ummi zata koma idan anyi fourthy barinta sukayi da dr faisal da nurse yasir sai rabiah flight din dazai sauka lagos suka bi “ dr ibrahim ne yatafi dasu inna da baba da iya da hajjaju sai matarsa da dansa dr usama da rufaidarh kam sai gobe daman akwai meeting din dayake dashi anan kasar din gidan yarage daga mom sai ummi da Mariam “yau adam wuni yayi kuka ga ummi tasha magani ta kwanta low bp take hadda stress kuma tana kokari wallahi gashi lokacin tafiyansu rufaidarh yayi daga mariam sai Aydarh yarage duk sun rasa yanda zasuyi dashi wallah isai kuka yake mariam ta goya naff sultana kuma baccinta take baiwar Allah sarkin hakuri

yana hannun Aydarh yarda yarudata ma babu wani kunyar mariam taciro nono tabasa yaki kamawa sai wani kalan tsala kuka yake duk ta rude itama wallahi tsaban batasan abun yi ba tafashe da kuka sai hankalin mariam yakarasa tashi tace minene auntie wai miyasame?aydarh na kuka tace ban sani ba yah mariam kinga fa nabasa bai karba ni bansan yarda zan masa ba mariam tace ki cigaba da gwadawa ko naje nataso ummi dasauri Aydarh ta girgiza kai tace dan Allah allow her to rest mariam tace tau ki kira babanshi dasauri tahau dube duben wayanta tadauka tayi dialing number shi bugu biyu yadauka yace yummy mummy “still tana kuka tace yayah adam is crying baya karban nono na jijigasa yaki shiru yah mariam ta karbesa har yanzu yakiyin shiru “malik yace wait ki saurara ki basa nono tace wai yayah idan ban basa ba zance na basa yayah bai karba ba fa yace ki chanza masa dayan kaman tafasa ihu tace na chanza masa faaa “ yace ina ummi fa Aydarh tace tasha magani ta kwanta yace ko bashida lafiya ne? Aydarh tace bansani ba tayi maganar very pissed off wallahi ba don dokansa bane bata kashe waya ba saidai shi yakashe daya kashe wallahi “ tsaban yanda tambayarsa ke bata haushi bayan tasan ko by mistake ta karya masa doka tasan sauran zare wayanta tayi akunnata ta matsa kusa da adam da wayan malik najin kukan adam din “yakashe wayan dasauri yafito daga asibitin “motar yashiga wanda CEO yaba triplet ita as gift dashi yazo asibitin “ dawani kalan speed yahau titi yakama hanyar gida “ yana isa ko Parking din kirki bai tsaya ba “ yabude motar yashige gidan “ a parlor ya tarar dasu hadda ummi dataji kukan nashi yayi yawa karbansa yayi daga hannun ummi “Yana duba sa arude yakalli Aydarh yace dauko hijab dinki mu tafi asibiti “yakalli ummi yace muna zuwa bedroom takoma tadauko hijab dinta da wayanta da handbag dinta hadda dan goyensa da feeder tafito har yafita ummi tarakata tashiga motar kafin tadawo ta dauki naff mariam tagoya sultana “ dake bacci ummi tazauna tace Allah yasa dai lafiyansa lau mariam tace Ameen ummi bawan Allah bakiga fa bak o nono baya karba “ ummi tace miyasa kuka kasa tashina tace itace tace sai nabarki kin huta “ ummi tace wallahi dayake baccin yayi nauyi banjiba sai da abun yayi tsananin ummi tace kuma kiji ban bisu ba mariam tace ahh ummi kwara dakika bar su sukaje “ in sha Allah bawani damuwa bane kila ma rigimansa ne ‘ummi tace Allah yasa tafada tamike tana shigewa daki da naff tagoyasa. Office din Dr jazz suka yi direct shi ya daukesa Aydarh a baya”dasauri dr jazz yakarbesa daga hannun malik yace what is wrong doctor is he alright malik yasauke ajiyan zuciya yace I didn’t know what exactly is the problem dr jazz yakalli Aydarh yace what is wrong with him mrs MD Aydarh tagirgiza kai tace he is crying since morning “ and he is ruining temperature “ dr jazz yakalli malik yace am coming fita yayi da adam a hannu malik yace kuma

